Darusa Na Yau Da Kullum Daga Taskokin Ilimi

Wallafar:

Ibrahim bin Muhammad bin Humaid

Da

Abdurrahmad bin Abdallah Ash-Sharif

Bugawa:

Daru Adalus Alkhadra Lin-nashri Wat-tauzi

Daru Adlasil-Khadra: Gidan buga littattafai da rarrabawa 1446AH.
Mawallafi: Ibrahim bin Muhammad bin Humaid
Da
Abdurrahman bin Abdullah As-Sharif
Sunan littafi: Darussan Yau Da Kullum Daga Taskokin Ilimi
Riyad, 1446AH.
623 p. : 24 cm - (Darussan Yau Da Kullum Daga Taskokin Ilimi)
Lambar ajiya: 1446/5983
ISBN: 978-603-8469-15-6

Abin lura:

- Ba a yarda a buga ɓangaren ƙasa tare da katin ƙamus ba.
- Ɗakin karatu na Ƙasa na Sarki Fahd yana fatan a aiwatar da abin da ya zo a tsarin ajiya bisa tsayi iri ɗaya, saboda haka, akwai buƙatar a buga ɓangare na sama da irin wannan girma a bayan shafin taken cikin littafi na cikin littafin, haka kuma dole a sake buga lambar ISBN a ɓangaren ƙasa na bangon littafin ta gefen hagu.
- Kuma dole ne a miƙa kwafi biyu na littafin zuwa Ɗakin karatu na Ƙasa na Sarki Fahd nan da nan bayan kamala buguwa, tare da wani kwafi a faifan CD.

((Gabatarwa))

Da sunan Allah Mai rahama Mai Jinƙai

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga mafificin Annabawa da Manzanni, Annabinmu Muhammadu, da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

Bayan haka; Muhinmancin ilimin shari'a ba abu ba ne mai ɓuya, a halin koya da koyarwa da nema da kuma bayarwa; haƙiƙa nassoshi na shari'a sun bibiyi juna wajen bayanin falalarsa da tasirinsa da falalar koyar da shi da yaɗa shi, da isar da shi ga mutane ta hanyoyi da sababba mabanbanta, saboda abin da ke cikin hakan na tasiri mai girma wajen tsarkake rayuka da inganta aƙidojinsu da gyara ibadunsu, da dasa ɗabi'u ingantattu a cikin zukatansu da ladubban tarbiyya a ayyukansu.

Kuma daga cikin waɗannan hanyoyi da sababba a dunƙule, akwai jiyar da karatun littattafai masu amfani a kunnuwansu, a cikin masallatai da gidaje da makamantan haka cikin wajejen da ake taruwa.

Haƙiƙa Allah Ya sauƙaƙe mana fara tattara wani littafi dake ɗauke da wannan manufa, wanda zai kasance mai tattaro manyan abubuwa na farko-farko da suka shafi ilmomi guda shida na shari'a, masu taƙaitattun bayani, masu mabanbantan maudu'i, wanda aka jera shi a bisa tsarin kwanakin mako, yana ɗauke da mako hamsin da biyu, sai wannan littafi ya fito da dacewar Allah da taimakonsa, wanda aka sa masa suna:

(Darusa Na Yau Da Kullum Daga Taskokin Ilimi)

Domin ya kasance abin tattaunawar musulmi mafi kusa a lokacin keɓewarsa, da liman a masallacinsa, da iyalai a gidajensu, da abokai a lokacin haɗuwarsu.

Kuma jerin darusan littafin za su kasance ne kamar haka:

Ranar Lahadi: Darasi cikin Tafsiri.

Ranar Litinin: Darasi cikin Hadisi.

Ranar Talata: Darasi cikin Aƙida.

Ranar Laraba: Darasi cikin Fiƙihu.

Ranar Alhamis: Darasi cikin Sirar Annabi.

Ranar Asabar: Darasi cikin tarihin sahabbai.

Kuma ba mu sanya wa ranar Jumu'a maudu’i ba, saboda taƙaituwa da hudubar Juma’a.

Kuma domin cika fa’idar littafin da tabbatar da darusansa, an sanya wa kowane mako tambayoyi da amsoshinsu waɗanda suke ɗauke da dukkan darusansu, domin mai karatu ya yi bitan abin da ya koya, ya kuma yi gasa da iyalansa da abokan zamansa; kuma haƙiƙa malamai sun ambaci cewa lallai gasa a cikin ilimi da jefo tambayoyi a cikin mas’alolinsa, yana daga cikin mafi muhinmancin hanyoyin samun ilimi da tara shi.

Sannan saboda sauƙaƙa abin da wannan littafi ya ƙunsa, da kusanto da shi, da yawaita hanyoyin isar da shi, an taskance dukkan darusansa a cikin sauti (Audio), sai ya fito cikin gajerun sauti na saurare (Audio) guda (312), kuma an ɗaura su a kan manhajojin (YouTube, da Telegram, da kuma SoundClaud), kuma an sanya cod na isa ga waɗannan sautuka a farkon kowane mako.

Allah mai karamci muke roƙo da ya sa an yi wannan littafi ne domin neman yardarsa, kuma ya amfanar da shi; lallai shi Allah Mai jin ne kuma Mai amsa addu’o’i.

Domin tuntuɓa ko ba da shawara; sai a yi magana da mu ta manhajar WhatsApp a wannan lamba:

0504162913

MAKO NA FARKO

LAHADI : DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL FATIHA

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ١ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ ٣ مَٰلِكِ يَوۡمِ ٱلدِّينِ ٤ إِيَّاكَ نَعۡبُدُ وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ ٥ ٱهۡدِنَا ٱلصِّرَٰطَ ٱلۡمُسۡتَقِيمَ ٦ صِرَٰطَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمۡتَ عَلَيۡهِمۡ غَيۡرِ ٱلۡمَغۡضُوبِ عَلَيۡهِمۡ وَلَا ٱلضَّآلِّينَ ٧﴾

❖ Fassara:

1. Dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talika.

2. Mai rahama Mai jinkai.

3. Mamallakin ranar sakamako.

4. Gare Ka kaɗai muke bauta kuma gare Ka kaɗai muke neman taikamako.

5. Ka shiryar da mu tafarki madaidaici.

6. Tafarkin waɗanda Ka yi ni'ima a gare su, ba tafarkin waɗanda Ka yi fushi da su ba, ba kuma na ɓatattu ba.

❖ Falalar Surar:

An karɓo daga Abu Sa'id ɗan Almu'alla (RA) ya ce : Lallai Manzon Allah (SAW) ya ce : (Tabbas zan sanar da kai wata sura, ita ce mafi girman sura a cikin Alƙur'ani, kafin ka fita daga wannan masallaci), sannan ya riƙe hannuna, yayin da na ga yana ƙoƙarin fita, sai na ce masa: Ashe ba ka ce: (Lallai haƙiƙa zan sanar da kai wata sura mafi girma a cikin Alƙur'ani ba?), sai ya ce: («Alhamdu lillahi Rabbil

alamin», ita ce ayoyi bakwai mafi maimaituwa da Alƙur'ani mai girma wanda aka ba ni).[1]

❖ Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:

Tabbatar da tsantsar bauta ga Allah Maɗaukakin sarki.

❖ Bakin kalmomi:

بسم الله	Bismillahi	Ina fara karatuna da neman taimako da sunan Allah
الرحمن	Arrahman	Wanda rahamarsa ta yalwaci dukkan halittunsa
الرحيم	Arrahim	Mai jinƙan muminai
رب العالمين	Rabbil-alamin	Mai raino ga dukkan halittu da ni'imarsa.
إياك نستعين	Iyyaka nasta'in	Muna keɓance ka da neman taimako, wanda shi ne dogaro ga Allah Maɗaukaki cikin abin da ke janyo amfani ko tunkuɗe cutarwa.
الصراط المستقيم	Assiraɗal mustaƙim	Hanya fayyacacciya wacce babu karkata a cikinta, mai sadar da bawa zuwa ga Allah da aljannarsa.
غير المغضوب	Gairil magdubi alaihim	Waɗanda suka san gaskiya kuma suka bar ta kamar Yahudawa da wasunsu.
الضالين	Addalliin	Waɗanda suka bar gaskiya saboda jahilci da ɓata kamar Nasara da wasunsu.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

Suratul-Fatiha sura ce da ta sauka a Makka, ayoyinta guda bakwai ne, ta fara da godiya ga Allah da yabo a gare shi, sannan ta ambaci wani sashi na siffofinsa masu girma, Shi ne Ubangijin kowane abu, Shi ne mai rahama Wanda ya siffantu da sakakkiyar rahama, wacce

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4474).

ta yalwaci kowane abu, Mai jin ƙai, Wanda Ya keɓance wanda Ya ga dama da tausayinsa, kuma Shi ne Wanda ke da mulkin ranar da za a saka wa mutane da ayyukansu na alherinsu ko na sharrinsu, sannan surar tana tabbatar da kaɗaitawar muminai ga Ubangijinsu, Shi kaɗai suke bauta wa kuma suke tsarkake bauta gare Shi, kuma a wajenshi Shi kaɗai suke neman taimako, kuma shiriyarsa kaɗai suke nema, kuma game da hanyoyin ɓata su masu neman tsari ne.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Surar ta fara da sunan Allah, kuma a cikin hakan akwai fadakarwa ga musulmi da riƙa fara dukkan wani aiki ko magana da sunan Allah, don neman taimako da dace.

2. Daga cikin shiriyar Alƙur’ani mai girma da nusarwarsa a cikin addu'a, akwai farawa da girmama Allah da yabo a gare Shi, sannan gabatar da abin da bawa ke nema.

3. Wajibcin gode wa Allah Maɗaukakin Sarki ta hanyar yabo da harshe da ɗa’a da gaɓɓai, da kuma tabbatarwa a zuciya.

4. Wajibi ne a kan musulmi ya kebance Allah Shi kaɗai da bauta da neman taimako, domin Shi ne Ubangiji Mafi cancantar a bauta masa ba waninsa ba.

5. Muhinmancin musulmi ya kira Mahallicinsa a kan ya shiryar da shi zuwa ga gaskiya kuma ya taimake shi don ya tabbata a kanta, kuma ya nisantar da shi daga fitintinu, ya kare shi daga hanyoyinsu.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR RUKUNAN MUSULUNCI

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Wani baƙauye ya zo wajen Manzon Allah (SAW), ya ce: Ka nuna mini aikin da idan na aikata shi zan shiga aljanna. Ya ce: (Ka bauta wa Allah kada ka yi tarayya da Shi a cikin bauta, kuma ka tsayar da salla, ka bayar da zakka ta farilla, ka azimci watan Ramadan), sai ya ce: Na rantse da Wanda raina ke hannunsa, ba zan ƙara a kan wannan ba. Yayin da ya juya baya, sai Annabi (SAW) ya ce: (Duk wanda zai masa dadi ya kalli mutum ɗan aljanna, to ya kalli wannan mutumin).[1]

❖ Sharhi:

A cikin Wannan hadisin, Annabi (SAW) yana ba da labarin cewa wanda ya aiwatar da farillan Allah, kuma ya nisanci haninsa, to haƙiƙa ya siffantu da siffar Musulunci da imani, kuma ya tabbata daga cikin masu tsoron Allah masu rabauta, kuma ya cancanci shiga aljanna da kuɓuta daga wuta.

Kuma abu na farko mafi cancanta shi ne abin da Annabi (SAW) ya ambata a karon fari, shi ne kaɗaita Allah da bauta, domin shi ne sharaɗi na farko wajen karɓar ayyuka da ingancin dukkan bauta, kuma da shi ne bawa yake shiga Musulunci, idan babu shi zai dawwama a cikin kafirci, sannan sai ya biyo bayansa da ambaton rukunnan Musulunci da manyan ibadodinsa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Falalar komawa zuwa ga ma'abota ilimi da tambayar su.

2. Lallai kaɗaita Allah wajen bauta shi ne farkon abin da ake farawa da shi wurin kira zuwa ga Musulunci.

[1]. Bukhari (1397) da Muslim (6) ne suka rawaito shi.

3. Muhinmancin rukunan musulunci guda biyar, kuma lallai su ne tushen ibadu da musulmi ke neman kusanci zuwa ga Ubangijinsa da su, kuma addininsa ba zai cika ba har sai ya zo da su.

4. Lallai duk wanda ya cika waɗannan rukunnan guda biyar, to aljanna ta tabbata a gare shi.

TALATA: DARASI CIKIN AƙIDA

BAYYANAR KARKACEWA A CIKIN AƙIDAR MUTUNE.

Allah Ya halicci ran mutum kuma Ya sanya sa a kan ɗabi'a ta Musulunci, yana mai tabbatar da kaɗaita Allah, yana mai son sa, yana bauta masa kuma ba ya haɗa Shi da wani a wajen bauta, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: ((Ka tsayar da fuskarka ga addini mai kauce wa ɓarna. Shi ne asalin halittar da Allah Ya halicci mutane a kanta. Babu wami canji ga halittar Allah)),[1] kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wani abin haihuwa face an haife shi ne a kan tsarin Musulunci, sai dai iyayensa su mayar da shi bayahude ko banasare ko bamaguje).[2]

Asali game da ɗan'adam shi ne Tauhidi, kuma addininsu shi ne Musulunci tun daga zamanin Annabi Adam (AS), da waɗanda suka zo bayansa daga zuriyarsa zamani mai tsawo, ita shirka kutse ce da shige a ckinsa, kamar yanda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Mutane ba su kasance ba face al'umma guda ɗaya, daga baya sai suka samu saɓani)).[3]

Kuma farkon abin da ya faru na saɓani da karkacewa a cikin aƙida ya kasance ne a cikin mutanen Annabi Nuhu; Ibnu Abbas (RA) ya ce: "A tsakanin Adam da Nuhu (AS) akwai ƙarni goma, kuma dukkansu a kan Musulunci suke",[4] Nuhu (AS) ya kasance shi ne farkon Manzo, kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((lallai Mun yi wahayi a gare ka, kamar yanda Muka yi wahayi zuwa ga Annabi Nuhu da Annabawa a bayansa)),[5] kuma Maɗaukaki Ya ce ((Mutane sun kasance al'umma guda ɗaya, (sai suka samu saɓani), sai Allah Ya aiko da Annabawa suna masu bishara da gargaɗi)).[6] Saboda

---

1. (Arrum: 30).
2. Bukhari (1357) da Muslim (2658) ne suka rawaito shi.
3. (Yunus: 19).
4. (Hakim ne ya rawaito shi (3654).
5. (Annisa'I: 163).
6. (Albaƙara: 213).

haka, sababin aiko manzani shi ne samun saɓani a kan addini ingantacce da kuma kauce wa asalin tsarin halittar ɗan’adam.

Dalilin karkacewar mutanen Annabi Nuhu shi ne: wuce gona da iri a haƙƙin bayin Allah na ƙwarai, lokacin da waɗannan bayin Allah suka rasu, sai shaiɗan ya yi wahayi zuwa ga mutanensu da su kafa mutummutuminsu a wuraren zamansu kuma su ambace su da sunayensu, sai suka aikata hakan, amma ba su bauta musu ba, har sai da waɗannan suka shuɗe, aka manta ilimi, sai aka bauta musu.[1]

Haka kuma an samu karkacewa a cikin larabawa; haƙiƙa sun kasance farkon al'amari suna kan addinin Annabi Ibrahim (AS), har sai da Amru ɗan Luhai Alkhuza'i ya zo ya canza addinin Annabi Ibrahim (AS), kuma ya kawo gumaka zuwa ƙasar larabawa, sai aka bauta musu koma bayan Allah, kuma shirka ta yaɗu har zuwa lokacin da Allah Ya aiko Annabinmu Muhammad (SAW), sai ya kira mutane zuwa ga Tauhidi da komawa zuwa ga tafarkin Annabi Ibrahim, sai aƙidar tauhidi ta dawo tsaftatacciya gangariya, sai kuma ƙarnoni mafifita suka kasance a kan tafarkinsa daga farkon wannan al'umma da waɗanda suka bi sawunsu.

Sannan kuma sai jahilci ya fara siɗaɗowa tsakanin gamagarin musulmai, shirka ta yaɗu cikin ƙarnonin baya-bayan nan, a cikin irin yanayin da ta yaɗu a farkon al'amari cikin mutanen Annabi Nuhu (AS), ta hanyar girmama waliyyai da bayin Allah na ƙwarai, da da'awar nuna soyayya a gare su, da gina wurin bauta a kan ƙaburburansu, tare da riƙe su a matsayin gumaka da ake bauta musu koma bayan Allah, ta hanyar addu'a da neman agaji da yanka da bakance, kuma suka kira shirkarsu da suna tawassuli da mutane nagari, sun manta wannan shi ne abin da mushirikan farko suke riyawa a inda suke cewa ((Ba ma bauta musu face sai don su kusantar da mu kusa da Allah)).[2]

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4920).
[2]. (Azzumar: 3).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

TSARKI

Addinin Musulunci addini ne mai girma, yana ɗauke da tsarin shari'a cikakke, kuma ya ƙunshi mafi kyawun ladubba da mafi karamcin ɗabi'u, kuma ya game dukkan abin da zai amfani mutum da maslaharsa, bai bar wani abu ba wanda mutane ke buƙata a addininsu da duniyarsu face ya bayyana shi, daga cikin haka akwai hukunce-hukuncen tsarki, saboda tsarki shi ne mabuɗin salla kuma mafi ƙarfin sharuddanta; don haka ne za a fara gabatar da magana a kansa kafin magana a kan salla.

Hakan ba komi ba ne face dalili a kan girman salla, ta yadda shiga cikinta ba ya inganta sai da tsarki guda biyu: Tsarki na ma'ana (tsarkin zuciya), na Tauhidi da tsarkake bauta ga Allah, da kuma tsarki na zahiri daga kari (hadasi) da ƙazanta, domin ya shirya don ganawa da Mahaliccinsa cikin kyakkyawan yanayi, kuma cikin mafi cikar girmamawa da darajawa ga Ubangijin talikai.

Jiki mai tsafta, da zuciya mai tsarki, da tufafi mai tsafta, da wuri mai tsarki, daga nan ne tsarki yake zama rabin imani, kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya ce: (Tsarki rabin imani ne, kuma faɗin "Alhamdu lillahi" yana cika ma'auni).[1]

❖ Ma' anar tsarki:

Tsarki: shi ne ɗauke kari (hadasi) da gusar da najasa.

Abin da kuma ake nufi da ɗauke kari (hadasi): shi ne gushewarsa ta hanyar alwala idan ya kasance hadasi ne ƙarami, idan kuma babba ne ta hanyar wanka, idan kuma aka gagara samun ruwa, sai a yi taimama a maimakonsu.

Ita kuma gushewar najasa tana nufin tsaftace jiki da tufafi da mahallin salla daga gare ta.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (223).

❖ Da wane abu ne tsarki ke samuwa?

Abin da aka shar'anta a wurin tsarkin alwala da wanka shi ne amfani da ruwa, ba a yin tsarki da wani abu mai ruwa-ruwa koma bayan tsantsan ruwa, kamar irinsu tsumi, da man fetur, da lemon kwalba da abin da ya yi kama da su, saboda faɗin Allah Maɗaukakin Sarki ((Idan ba ku sami ruwa ba, to ku yi taimama da turɓaya mai tsarki)),[1] da a ce tsarki na samuwa da wani abu mai ruwa-ruwa koma bayan tsantsan ruwa da an mayar da tsarki zuwa gare shi idan aka rasa ruwa, da kuma ba a mayar da shi zuwa ga turɓaya ba.

[1]. (Alma'ida: 6).

ALHAMIS : DARASI CIKIN SIRA

SUNAN ANNABI (SAW) DA HAIHUWARSA

❖ Sunansa da nasabarsa (SAW):

Shi ne : Muhammadu ɗan Abdullahi ɗan Abdul-Muɗɗallib ɗan Hashim ɗan Abdu-Manaf ɗan Ƙusai ɗan Kilab ɗan Murra ɗan ka'ab ɗan Lu'ayyi ɗan Galib ɗan Fihir ɗan Malik ɗan Nadr ɗan Kinana ɗan Khuzaima ɗan Mudrika ɗan Ilyas ɗan Mudar ɗan Nizar ɗan Ma'addi ɗan Adnan, daga zuriyar Ismail ɗan Ibrahim (AS).

Yana dangantuwa (SAW) zuwa ga dangin gidan ‘ya’yan Hashim, mafi asalin gida a ƙabilar Ƙuraishawa, Manzon Allah shi ne mai mafi ɗaukaka da darajar dangantaka, mai mafi darajar ƙabila da dangi, mai mafi daraja da tsarkin gida; Manzon (SAW) ya ce: (Lallai Allah Ya zaɓi Kinana daga 'ya’yan Ismail, kuma Ya zaɓi Ƙuraish daga Kinana, kuma Ya zaɓi 'ya’yan Hashim daga Ƙuraishawa, kuma Ya zaɓe ni daga 'ya’yan Hashim).[1]

❖ Mahaifiyarsa:

Ita ce Amina 'yar Wahab ɗan Abdu-Manaf, Mahaifin Manzon Allah Ya aure ta yana ɗan shekara ashirin da huɗu, sannan ya bar Makka zuwa ƙasar Sham don kasuwanci, sai ya rasu a Madina a hanyarsa ta dawowa.

❖ Haihuwarsa:

An haifi Manzon Allah (SAW) a Makka, ranar Litinin, a cikin watan Rabi'ul Auwal, a shekarar giwa, wanda ya yi daidai da shekara ta 571 Miladiyya, bayan rasuwar mahaifinsa Abdullahi da wasu watanni, sai kakansa Abdul-Muɗɗalib ya sanya masa suna (Muhammad). Ya tabbata a hadisi cewa: (Lallai mahaifiyar Manzon Allah (SAW) lokacin da ta haife shi ta ce ta ga kamar wani haske

[1]. Muslim ne ya rawaito (2276).

ya fita daga gare ta har sai da ya haska gidajen sarautar ƙasar Sham).[1]

[1]. Ahmad ne ya rawaito shi (16700).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABUBAKAR SIDDIK (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Abdullahi ɗan Abu Ƙuhafa Attaimi Alƙurashi, dangantakarsa tana saduwa da ta Annabinmu Muhammad (SAW) a kaka na shida, wato “Murra ɗan Ka'ab”.

An haife shi a Makka bayan shekarar giwa da shekara biyu da wata shida.

❖ Tarihinsa da falalarsa:

Ya kasance (RA) mai farin launi, mai siririn jiki da ƙauri mara kauri, mai kwarmin ido, ya kasance daga cikin mafi gudun duniya da tsoron Allah a cikin mutane, mai karamci da yawan kyauta, yana ciyar da dukiyarsa duka domin addinin Allah.

Abubakar Siddik ya fara rayuwarsa a cikin Musulunci da kira zuwa ga Allah, ya kira mutanensa da abokansa, kuma adadi mai yawa sun shiga Musulunci a hannunsa, daga cikinsu akwai, Zubairu ɗan Awwam, da Usman ɗan Affan, da Ɗalha ɗan Ubaidullahi, da Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas, da Abdurrahman ɗan Auf.

Haka kuma an san shi da taimakon masu rauni da mabuƙata, haƙiƙa ya 'yanta Bilal ɗan Rabahi, da Amir ɗan Fuhaira da Ummu Ubais da Zinnira da sauransu.

Ya yi yaƙi tare Manzon Allah (SAW) dukkan yaƙoƙi, kuma ya keɓantu da wasu keɓantattun siffofi, ta yadda ya kasance wazirin Manzon Allah (SAW) kuma abokin shawararsa, abokin rakiyarsa lokacin hijira, kuma Manzon Allah (SAW) ya gabatar da shi limancin salla a lokacin rashin lafiyarsa da ya rasu a ckinsa.

Kuma an yi masa inkiya da laƙabobi masu yawa, daga cikinsu akwai:

Assiddiƙ: Saboda yawan gasgatawarshi ga Manzon Allah (SAW), kuma Manzon Allah (SAW) ne ya yi masa laƙabi da shi a kan dutsen Uhud; lokaci da ya kasance tare da Abubakar, Umar ɗan Khaɗɗab, da Usman ɗan Affan, sai dutsen ya girgiza da su, sai Annabi (SAW) ya ce: (Ka tabbata ya kai Uhud, domin a samanka akwai Annabi da Siddiƙi da shahidai guda biyu).[1]

Kuma bayan aukuwar Isra'i, an jarrabi dayawa daga cikin mutane, sai wasu mutane suka zo wurin Abubakar don su ji zancensa, sai ya ce: (Lallai idan ya faɗi hakan, to haƙiƙa ya yi gaskiya; Lallai ni ina gasgata shi a kan abin da ya fi haka nisa, ina gaskata shi a kan labarin da ke zuwa masa daga sama).[2]

Kuma Manzon Allah (SAW) ya yi masa laƙabi da "**Atiƙ**", wato (‘yantacce daga wuta), lokacin da ya ce masa: (Lallai kai ne 'yantaccen Allah daga wuta).[3]

Ana ce masa "**Sahib**" wato aboki; Allah Maɗaukakin Sarki ne Ya yi masa wannan laƙabi a inda yake cewa: ((Lokacin da yake ce wa abokinsa, kada ka yi baƙin ciki, lallai Allah Yana tare da mu)).[4]

Haka kuma daga cikin laƙubansa akwai "**Al’atƙa**", wato mafi tsoron Allah, kuma shi ma wannan laƙabi Allah Maɗaukakin Sarki ne da kansa Ya kira shi da shi a cikin faɗinsa: ((Kuma mafi tsoron Allah zai nisance ta)).[5]

Bayan rasuwar Manzon Allah (SAW), Abubakar (RA) ya jiɓinci al'amarin halifanci ta hanyar mubaya'a da aka masa a ƙarƙashin Rumfar Banu Sa’ida, kuma ya kasance a matsayin halifan musulmai na tsawon shekara biyu da wata uku, ya fara da yaƙan waɗanda suka yi ridda, sai ya aika runduna goma sha ɗaya zuwa dukkan birane da ke yankin larabawa a cikin wannan ɗan ƙanƙanin lokaci, sannan

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (3675).
[2]. Dala’ilun nubuwa na Baihaƙi (2/361).
[3]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3679).
[4]. (Attauba: 40).
[5]. (Allail: 17).

bayan haka sai ya tura wata rundunar domin buɗe ƙasar Sham da Iraƙi, kuma a lokacin halifancinsa ya tattara Alƙur'ani dukkansa a cikin littafi ɗaya.

❖ Rasuwarsa:

Abubakar (RA) ya rasu a daren Talata, ranar ashirin da biyu ga watan Jumada Akhira, a shekara ta sha uku bayan hijira, bayan ya yi rashin lafiya, kuma an binne shi a kusa da Manzon Allah (SAW) a ɗakin A'isha, sai ya kasance tare da abokinsa kamar yanda ya kasance tare da shi a duniya, Allah Ya saka masa da alheri a kan ƙoƙarinsa ga al'ummar musulmai, Ya kuma ƙara masa yarda.

Auna fahimtarka a darusan mako na 1 -			**Amsa ta ƙwarai**
Darasin Tafsiri	Tambaya: Su wane ne (Almagdubi alaihim)?		**A**
	a. Waɗanda suka san gaskiya kuma suka yi watsi da ita, kamar yahudawa da ire-irensu	b. Waɗanda suka yi watsi da gaskiya saboda jahilci, kamar kiristoci.	c. Mulhidai masu ƙaryata samuwar Allah.
Darasin Hadisi	Tambaya: Mene ne farkon abin da ake fara kira zuwa ga Allah da shi:		**B**
	a. Kyakkyawan hali.	b. Kaɗaita Allah da bauta.	c. Salla.
Darasin Aƙida	Tambaya: Farkon karkacewa daga barin aƙida ya faru ne a cikin mutanen:		**B**
	a. Annabi Luɗu	b. Annabi Nuhu.	c. Annabi Hudu
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Tsarkin kari (hadasi) ya kasu zuwa:		**C**
	a. Na asali da wanda ba na asali ba	b. Sabo da tsoho.	c. Babba da ƙarami.
Darasin Sira	Tambaya: Annabi (SAW) yana dangantuwa zuwa ga mafi asalin gidajen ƙabilar Ƙuraishawa, su ne:		**A**
	a. Banul-Abbas.	b. Banu Hashim.	c. Banu Umayya.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin Laƙuban Abubakar (RA) akwai:		**C**
	a. Alkarim.	b. Assafir.	c. Al’atiƙ.

MAKO NA BIYU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-IKHLAS

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
قُلۡ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ۝١ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ۝٢ لَمۡ يَلِدۡ وَلَمۡ يُولَدۡ ۝٣ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدُۢ ۝٤﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai rahama, Mai jin ƙai

1. Ka ce: Shi ne Allah Ɗaya.

2. Allah Abin nufa da ɓuƙatu.

3. Bai Haifa ba, kuma ba a haife Shi ba.

4. Kuma babu wani da ya kasance kini a gare Shi.

❖ Falalar surar:

- An karɓo daga Abu Darda’ (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Yanzu ɗayanku zai gagara karanta ɗaya bisa ukun Alƙur’ani a cikin dare), sai suka ce: Ya ya za a yi ya iya karantarwa?! Ya ce: (“Ƙul huwallahu Ahad” yana daidai da ɗaya bisa ukun Alƙur’ani).[1]
- An karɓo daga Abdullahi ɗan Khubaib (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Karanta “Ƙul huwallahu Ahad” da Ƙula’uzai biyun nan sau uku da yammaci da safiya, ya isar maka daga dukkan wani abu).[2]

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (811).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3575).

❖ Sababin saukarta:

Malamai sun ambata game da sababin saukar wannan surar cewa lallai mushirikai sun ce wa Annabi (SAW): Ka ambato mana nasabar Ubangijinka? Sai Allah Ya saukar da wannan surar.[1]

❖ Sakon da surar ke ƙunshe da shi:

Kaɗaituwar Allah da cancantar kaɗaituwa da bauta da kamala, da kuma tsarkakuwarsa daga ɗa da uba da tamka.

❖ Bakin kalmomi:

الصمد	Assamad	Shugaba, wanda yake da kamala a shugabancinsa da wadatarsa, kuma wanda ake nufa don neman biyan buƙatu.
كفوا	Kufuwan	Tamka, tsara, ko kini.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

Suratul-Ikhlasi tana daga cikin surori da suka sauka a Makka, kuma tana da falala mai girma; saboda haƙiƙa an tambayi Annabi (SAW) wata rana game da Ubangijinsa Mai girma da buwaya, sai aka umurce shi a wannan sura da ya ba da amsa da cewa lallai Ubangijinsa Shi ne Allah, Mai kaɗaituwa da cancantar bauta, wanda yake Ɗaya Tilo a zatinsa da siffofinsa da ayyukansa, wanda ya haɗa sifofi na kamala, Shugaba da ake nufata a kodayaushe don neman biyan buƙatu, wanda ya wadato daga dukkan halittunsa, kuma dukkan halittunsa suke da buƙatuwa zuwa gare Shi, ba Shi da tamka, ko kini, ko kuma uba ko ɗa, don haka bauta ba ta dace da kowa ba sai Shi, kuma bauta ba za ta inganta ba sai gare Shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Sanin Allah Maɗaukaki da sunayensa da siffofinsa.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3364).

2. Tabbatar da siffofin kamala ga Allah Maɗaukaki, kamar kaɗaituwa da wadata.

3. Kore siffofin tawaya daga Allah Maɗaukaki; kamar danganta ɗa gare Shi, ko tsara, ko makamanci.

4. Lallai halittun sama da ƙasa gaba ɗayansu masu buƙatuwa ne zuwa ga Allah Maɗaukaki maƙurar buƙata, suna tambayarsa buƙatunsu, kuma suna komawa gare Shi cikin damuwowinsu.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WAJIBCIN IMANI DA FALALAR TSAYUWA A KANSA

An karɓo daga Sufiyanu ɗan Abdullahi Assaƙafi (RA) ya ce: Na ce: Ya Manzon Allah, Ka sanar da ni wata magana a Musulunci, wacce ba zan tambayi kowa koma bayanka game da ita ba. Sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ka ce: Na yi imani da Allah, sannan ka tsaya ƙyam a kai).[1]

❖ Sharhi:

Safiyanu (RA) ya nemi Annabi (SAW) da ya yi masa wasiya wacce take tattare da alheri, mai kaiwa zuwa ga tsira, sai ya umurce shi da al'amura guda biyu:

Al'amari na farko: Shi ne imani da Allah, wanda yake ƙunshe da abin da ya wajaba a ƙudurta shi na ginshiƙan imani da rukunansa, da abin da ke biye da haka na ayyukan zukata, da miƙa wuya ga Allah, da jayuwa zuwa gare shi, da ayyuka nagartattu.

Al'amari na biyu: Shi ne dawwama a kan haka, da tabbatuwa a kanshi har zuwa mutuwa.

Waɗanna al'amura guda biyu su ne ginshiƙan tsira da rabauta; kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai waɗanda suka yi imani, sannan suka tsaya a kansa, to babu tsoro a gare su, kuma ba za su yi baƙin ciki ba () Waɗannan su ne 'yan aljanna, suna masu dawwama a cikinta sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa)).[2]

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Wannan hadisin yana daga cikin dunƙulallun kalmomin Annabi (SAW), saboda lallai wannan jumlar ta: (Ka ce: Na yi imani da

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (38).
[2]. (Al-Ahƙaf: 13-14).

Allah, sannan ka tsaya a kai ƙyam), ta tattara dukkan mas'alolin addini, ta ɓangaren aƙida da shari'a.

2. Wajibcin sanin haƙiƙanin imani, wanda a wajen Ahlussuna wal-jama'a shi ne: Gaskatawa da zuciya, da furuci da harshe, da kuma aiki da gaɓoɓi da gangarjiki, yana ƙaruwa da ayyukan ɗa'a, kuma yana raguwa da ayyukan saɓo.

3. Falalar daidaituwa da tabbatuwa a kan addini, da kuma cewa lallai sakamakon hakan shi ne aljanna.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

TAƘAITACCEN TUNANI GAME DA RAYUWA

Taƙaitaccen tunani game da rayuwa: Shi ne tunanin mutum ya zama mai taƙaituwa ne a kan daɗaɗe-daɗaɗen duniya, kuma aikinsa ya zama ya taƙaita ne a kan nemanta; saboda haka, lahira ba ta da wani matsayi a wajensa, kuma bai damu da sha'aninta ba! Haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya yi alƙawarin narko ga wanda tunaninsa ya taƙaitu a kan jin daɗinta, sai Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai waɗanda ba sa tsammanin gamuwa da Mu, suka kuma yarda da rayuwar duniya, kuma suka nutsu da ita, da kuma waɗanda suke gafala daga ayoyinmu () Waɗannan makomarsu wuta ce saboda abin da suka kasance suna aikatawa)).[1] Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Waɗanda suke nufin rayuwar duniya da ƙawace-ƙawacenta, to za Mu ba su cikakken sakamakon ayyukansu a cikinta, kuma ba za a tauye musu komai ba () Waɗannan su ne waɗanda ba su da komai a lahira sai wuta; kuma abin da suka aikata a cikinta (duniyar) ya rushe, kuma abin da suke aikatawa ya lallace)).[2] Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Wannan alƙawarin Allah ne; Allah kuwa ba Ya saɓa alƙawarinsa, sai dai kuma yawancin mutane ba su san hakan ba () Suna sanin abin da yake sarari na rayuwar duniya ne, alhali kuwa su gafalallu ne game da lahira)).[3]

Su, duk da kasancewarsu ma'abota ƙwarewa game da duniya da nemanta, amma kuma jahilai ne ba su cancanci a siffanta su da ilimi ba; saboda lallai ilimin nasu bai wuce zahirin rayuwar duniya ba, kuma tunaninsu zuwa gare ta bai wuce irin tunanin dabbobi ba, bari dai, su sun ma fi dabbobin ɓata daga hanya, Allah Maɗaukaki Sarki Ya ce: ((Ko kuwa kana tsammanin cewa yawancinsu suna ji ne (na fahimta) ko suna hankalta? Ai su ba wasu ba ne illa kamar dabbobi;

---

[1]. (Yunus: 7-8).
[2]. (Hudu: 15-16).
[3]. (Arrum: 6-7).

a’a su ne ma suka fi (dabbobi) ɓacewa daga hanya)).[1] Saboda su sun ba da ƙarfinsu da lokutansu ga abin da ba ya wanzuwa gare su, kuma su ma ba za su wanzu gare shi ba, kuma ba su yi aiki don makomarsu wanda yake jiransu ba, kuma babu makawa sai sun koma; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Yanzu kuna tsammanin cewa Mun halicce ku ne don wargi, kuma lallai ku ba za ku komo zuwa gare Mu ba)).[2]

Amma ingantaccen tunani game da duniya shi ne: Mutum ya ɗauki abin da ke cikin wannan rayuwa na dukiya da ƙarfi da ‘ya’ya da lokaci a matsayin hanya ce da za ta taimaka masa wajen aikata kyawawan ayyuka masu wanzuwa; domin duniya hanya ce da kuma gada da ake ƙetare su don zuwa lahira, kuma masukwana ne da ake tsere a cikinsa zuwa ga ayyukan alheri, kuma daga gare ta ake samun guzurin zuwa aljanna, kuma a cikinta gonar lahira take, kuma mafi alherin rayuwa da ‘yan aljanna za su samu, to suna samunsa ne sakamakon ƙoƙari da suka yi a duniya na salla da azumi da ciyarwa; domin lallai Allah Maɗaukaki Yana ce wa ‘yan aljanna: ((Ku ci ku sha kuna masu farin ciki saboda abin da kuka gabatar a kwanakinku da suka shuɗe na (duniya)).[3] A wannan duniya ana gwada gaskiyar bawa a kan neman lahira, kuma ana jarraba ƙoƙarinsa na nemanta; kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai Mu Mun sanya abin da yake bayan ƙasa ya zama ado a gare ta, don kuma Mu jarrabe su, wane ne daga cikinsu ya fi kyakkyawan aiki)).[4]

---

[1]. (Alfurƙan: 44).
[2]. (Almuminun: 115).
[3]. (Alhaaƙƙah: 24).
[4]. (Alkahaf: 7).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

HUKUNCE-HUKUNCEN RUWA

❖ Rabe-raben ruwa:

Dukkan ruwa da ke ban ƙasa ya kasu kashi biyu:

❋ **Ruwa mai tsarkakarwa:** Wanda ake iya yin tsarki da shi, da ruwa mai najasa wanda ba a tsarki da shi.

Shi ruwa mai tsarkakarwa: shi ne mai tsarki a zatinsa kuma mai tsakakar da waninsa, shi ne wanda yake kan siffarsa ta asali, wacce Allah Ya halicce shi a kanta, daga sama ya sauko kamar ruwan sama da narkakken ƙankara da raɓa, ko ko mai gudana a ƙasa, kamar ruwan ƙoramu, da maramarai, da rijiyoyi, da tekuna.

Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma Mun saukar da ruwa mai tsarkakarwa daga sama)).[1]

Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce game da ruwan kogi: (Ruwansa mai tsarkakarwa ne, kuma mataccen abin cikinsa halal ne).[2]

❋ **Amma ka ga ruwa mai najasa**: Shi ne wanda ɗaya daga cikin siffofinsa guda ukun nan suka canja (warinsa, ko ɗanɗanonsa, ko launinsa), da wata najasa da ta faɗa a cikinsa.

Wannan nau’i na ruwa ba ya halatta a yi amfani da shi wurin ɗauke kari (hadasi) ko gusar da najasa; saboda shi ƙazanta ne mai cutarwa, yana lalata jiki, kuma ba ya tsarkake shi.

Cikin abin da ya gabatar; za a gane cewa lallai asali game da ruwa shi ne cewa an halicce shi ne mai tsarkakarwa, kuma ba a hukunta cewa mai najasa ne sai dai idan ya canza da najasa a bisa tabbas.

---

[1]. (Alfurƙan: 48).

[2]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (83), da Tirmizi (69).

❖ Hukuncin ruwan da najasa ta faɗa a cikinsa, amma bai canja ba:

Idan najasa ta faɗa cikin ruwa, amma babu ɗaya daga cikin siffofinsa guda uku da ya canza; to lallai shi ba zai zama mai najasa ba; saboda yana nan a bisa asalin siffarsa wacce aka halicce shi a kanta; dalili a kan haka kuwa shi ne faɗin Manzon Allah (SAW): (Lallai ruwa mai tsarkakarwa ne, babu wani abu da yake mayar da shi mai najasa),[1] da kuma faɗinsa (SAW): (Idan ruwa yawansa ya kai manyan tulu biyu, to ba ya ɗaukan najasa).[2]

❖ Hukuncin ruwan da wani abu mai tsarki ya faɗa a cikinsa:

Ruwa ba ya cutuwa idan wani abu mai tsarki ya faɗa a cikinsa ko kuma ya cakuɗu da shi; kamar ganyen bishiya, ko sabulu, ko ganyen magarya, ko makamancin haka, ko da kuwa ya sauya shi sauyawa ɗan kaɗan, matsawar cewa lallai bai rinjayi ruwan ba, kuma bai canza masu sunansa zuwa sunan wani abu mai ruwa-ruwa ba; to shi mai tsarkakarwa ne, yana shiga cikin sunan ruwa; kuma haƙiƙa ya tabbata daga Annabi (SAW) cewa lallai ya yi umurni da ayi amfani da magarya da kafur wajen wanke gawa).[3]

---

[1]. Ahmad ne ya rawaito shi (3/15), da Abu Dawuda (61).
[2]. Ahmad ne ya rawaito shi (2/27), da Abu Dawuda (63).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (1253), da Muslim (939).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

SHAYAR DA SHI DA TASOWARSHI

❖ Shayar da shi:

Yana daga cikin al'adun manyan larabawa ba da jariransu ga masu shayarwa cikin mutanen ƙauye; don su koyi fasahar yare da harshe a wajensu, su kuma kuɓuta daga cututtuka da annoba, sai Aminatu mahaifiyar Annabi (SAW) ta so aikata haka, sai ta jira zuwan mata masu shayarwa daga Banu Sa'ad, don ta ba da ɗanta ga ɗaya daga cikinsu, yayin da suka zo sai ya zama daga cikinsu akwai wata mai shayarwa da ake kira: (Halimatus-Sadiya), sai ta karɓe shi, sai ya zama albarka a gare ta da kuma gidanta, sai ya zauna a wajenta har sai da ya kai shekara huɗu, a wannan lokacin mala'ika Jibrilu (AS) ya tsaga ƙirjinsa, sai ya fitar da zuciyarsa, sai ya wanke shi ya kuma tsarkake shi daga rabon shedan.[1]

❖ Rasuwar mahaifiyarsa:

Annabi (SAW) ya dawo daga ƙauyen Banu Sa'ad zuwa ga mahaifiyarsa Aminatu a Makka, to bayan shuɗewar shekaru biyu sai mahaifiyarsa ta fita tare da shi zuwa Madina don ta ziyarci kawunnnensa, sai ta kamu da rashin lafiya a kan hanyarta ta dawowa, sai ta rasu a wani waje da ake kira (Abwa'i), a lokacin Annabi (SAW) yana ɗan shekara shida, sai ya zama maraya mara uba da uwa a wannan lokacin.

❖ Rainonsa a wajen kakansa:

Kakansa Abdulmuɗɗalib ya cigaba da renon sa bayan rasuwar mahaifiyarsa, amma wannan reno bai ɗauki lokaci mai tsawo ba; saboda kakan nasa shi ma ya rasu bayan shekara biyu da rasuwar mahaifiyarsa!

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (162).

❖ Rainonsa a wajen baffansa:

Abdulmuɗɗalib ya kasance yana sane da abin da ɗansa Abu Ɗalib yake da shi na siffofi masu daraja, a yayin da ya ga alamar cewa mutuwarsa ta kusa, sai ya yi masa wasici da renon jikansa, sai Abu ɗalib ya reni ɗan ɗan'uwansa mafi kyawun reno, duk da cewa shi mai ƙarancin dukiya ne, mai kuma tarin iyalai, ya kasance yana son sa so mai tsanani, kuma yana gabatar da shi a kan 'ya'yansa wajen abinci da abin sha, sai Annabi (SAW) ya zama albarka a gare su, har aka kai matakin da idan iyalan Abu Ɗalib suka ci abinci ba sa ƙoshi saboda yawansu, amma idan Annabi (SAW) ya ci tare da su, sai su ƙoshi, sai Abu Ɗalib ya ce: Lallai kai yaro ne mai albarka.[1]

[1]. Dala'ilun nubuwwa na Baihaƙi (2/20).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

UMAR ƊAN KHAƊƊAB (RA)

❖ Sunansa da haifuwarsa:

Shi ne Umar ɗan Khaɗɗab ɗan Nufailu ɗan Abdul'uzza ɗan Riyah, ana masa alkunya da "Abu Hafs", nasabarsa tana haɗuwa da Annabi (SAW) a kaka na tara, wato "Ka'abu ɗan Lu'ayyu ɗan Galib".

An haife shi a Makka, bayan shekarar giwa da shekaru goma sha uku.

❖ Tarihinsa da falalarsa:

Umar (RA) ya kasance mai ƙaƙƙarfan jiki da ginin halitta, yana siffantuwa da jarumtaka da gwarzantaka, a fuskarsa akwai wani jaja-jaja da yake ƙaruwa idan ya fusata.

Ana masa laƙabi da "**Alfaruƙ**" saboda Allah ya rabe tsakanin ƙarya da gaskiya da shi.

Kuma haƙiƙa Allah Ya taimaki Musulunci da shi, don amsa addu'ar Annabinsa (SAW): (Ya Allah Ka ɗaukaka Musulunci ta hanyar mafi soyuwan ɗaya daga cikin mutane biyun nan masu suna Umar a gare Ka),[1] sai ya musulunta yana ɗan shekara ashirin da shida a wannan lokacin, sai Musuluncinsa ya zama ƙarfi ga musulmai; Ibnu Mas'ud (RA) yana cewa: "Musuluncin Umar ya kasance buɗi, hijirarsa kuma nasara, shugabancinsa rahama, ina rantsuwa da Allah ba ma iya yin salla a wajen ɗakin Ka'aba a fili har sai da Umar ya musulunta, ya yaƙe su har sai da suka ƙyale mu mu yi salla".[2]

Umar (RA) ya halarci dukkan yaƙoƙi tare da Annabi (SAW), kuma bayan Abubakar (RA) ya rasu sai ya karɓi shugabanci, sai ya zama shi ne halifa na biyu a cikin halifofi shiryayyu, ya kasance a lokacin

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (3675).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (3675).

halifancinsa mai adalci a tsakanin musulmi, mai tausayin masu rauni da miskinai, mai yawan kyauta da ciyarwa ga mabuƙata, mai tsananin tsantseni da gudun duniya a karan kanshi, har ma sahabbai na tausaya masa saboda kaushin rayuwarsa da ƙarancin dukiyarsa.

Shi ne farkon wanda ya kafa "Baital-malin" musulmi, kuma farkon wanda ya kawo tsarin shugabanci, kuma ya kawo tsarin soja, ya kuma kawo kalandar musulunci ta hijira.

A lokacin halifancinsa aka buɗe mafi yawan ƙasashen Musulunci; kamar Dimashƙa, da sauran garuruwan Sham, da Iraƙi, da Misira, da Libiya.

❖ Rasuwarsa:

Ya yi shahada a ranar Laraba 26 ga watan Zulhijja, shekara ta 23 bayan hijira, bayan dowawarsa daga hajji, a lokacin da yake yi wa mutane sallar asuba, sai Abu Lu'lu'atal-majusi ya caka masa wata wuƙa mai kaifi biyu, wanda aka shafe ta da guba, ya caka masa ita har sau shida, sai aka ɗauke shi zuwa gidansa alhali jini na zubowa daga wajen ciwon nashi.

Kuma yayin da ya ga alamar kusantowar ajalinsa sai ya ce wa ɗansa Abdullahi: "Ka je wurin A'isha ka roƙe ta ta ba da izinin a binne ni tare da Manzon Allah (SAW) da Abubakar,[1] sai ta ba da izini, sai Umar ya ƙara kwana bayan haka, sannan ya rasu, sai Suhaibu ya jagoranci yin salla a gare shi tare da mutane, sai aka binne shi a kusa da Annabi (SAW) da abokinsa.

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (1392).

Auna fahimtarka a darusan mako na 2 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Me ake nufi da (Assamad)?		A
	a. Shugaba wanda shugabancinsa da wadatarsa suka cika, wanda kuma ake nufatar sa don neman biyan buƙatu.	b. Masanin manyan al'amura da ɓoyayyunsu.	c. Ma'abocin ɓoyayyen tausasawa.
Darasin Hadisi	Tambaya: Asalin tsira da rabauta a duniya da lahira shi ne:		C
	a. Wadata da daraja.	b. Ƙoƙari da himma.	c. Imani da Allah da tabbatuwa a kai har mutuwa.
Darasin Aƙida	Tambaya: Taƙaitaccen tunani game da duniya shi ne:		B
	a. Bawa ya haɗa tsakanin aiki don duniya da shiri wa lahira a rayuwarsa.	b. Tunanin mutum ya zama ya taƙaita ne a kan daɗaɗe-daɗaɗen duniya, kuma aikinsa ya taƙaita a kan nemanta.	c. Ya damu da lamarinsa a farko.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Idan najasa ta faɗi a cikin ruwa, amma ba ta sauya siffofinsa uku ba, to wannan ruwan:		B
	a. Mai najasa ne.	b. Ba mai najasa ba ne.	c. Za a yi aiki da shi don larura.
Darasin Sira	Tambaya: Daga cikin waɗanda suka raini Annabi (SAW) a yarintarsa akwai:		C
	a. Baffansa Abbas.	b. Baffansa Hamza.	c. Baffansa Abu Ɗalib.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Umar ɗan Khaɗɗab (RA) ya musulunta yana da shekaru:		C
	a. 20.	b. 24.	c. 26.

MAKO NA UKU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-FALAƘI

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلۡفَلَقِ ۝١ مِن شَرِّ مَا خَلَقَ ۝٢ وَمِن شَرِّ غَاسِقٍ إِذَا وَقَبَ ۝٣ وَمِن شَرِّ ٱلنَّفَّٰثَٰتِ فِي ٱلۡعُقَدِ ۝٤ وَمِن شَرِّ حَاسِدٍ إِذَا حَسَدَ ۝٥﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai rahama, Mai jin ƙai.

1. Ka ce: “Ina neman tsari da Ubangijin asuba.

2. “Daga sharrin abin da Ya halitta.

3. “Da kuma sharrin dare idan ya lulluɓe da duhu.

4. “Da kuma sharrin mata masu tofi a cikin ƙulle-ƙulle.

5. “Da kuma sharrin mai hassada yayin da ya yi hassadar”.

❖ Falalarta:

Annabi (SAW) ya ce: (An saukar mun da wasu ayoyi a wannan daren, ban taɓa ganin kamarsu ba: ((Ƙul a’uzu bi Rabbil-falaƙ)), da ((Ƙul a’uzu bi Rabbin-nas)).[1]

❖ Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:

Kwaɗaitarwa a kan neman tsarin Allah daga sharrori.

❖ Baƙin kalmomi:

أعوذ	A’uzu	Ina neman mafaka da tsari.
الفلق	Alfalaƙ	Asubahi.
غاسق	Gasiƙin	Dare mai tsananin duhu.
إذا وقب	Iza waƙaba	Idan duhusa ya shigo ya ratsa.

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (813).

النفاثات في العقد	Annaffasati fil-uƙadi	Mata masu sihiri, waɗanda suke tofi ba tare da yawu ba a cikin ƙullin zare da manufar sihiri.
حاسد	Hasidin	Shi ne wanda ke burin gushewar ni'ima daga waninsa.

❖ Ma'anar surar a dunƙule:

Suratul-falaƙi tana daga cikin surori da suka sauka a Makka, kuma ɗaya ce daga cikin surorin neman tsari, ta zo ne don ta nusar da bayi izuwa ga haƙiƙanin fakewa zuwa ga Allah Mai buwaya da ɗaukaka, ta hanyar neman tsarinsa daga sharrori da bala'o'i, sai ta ƙunshi neman tsari daga sharrori huɗu:

Na farko: Sharrin kowane ma'abocin sharri cikin dukkan halittu.

Na biyu: Sharrin abin da ke faruwa a cikin dare daga dabbobi da ɓarayi da shedanu.

Na uku: Sharrin mata masihirta masu tofi a cikin ƙulle-ƙulle.

Na huɗu: Sharrin mai hasada idan ya yi hasadar.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Wajibcin kaɗaita Allah Maɗaukaki da neman mafaka da tsari; Shi ne kaɗai Mai ikon a kan kiyaye bawa.

2. Shiryarwa zuwa ga hanya mai amfani don neman kariya daga sihiri da hasada da sauran sharrori; kuma wannan hanyar ita ce: Zikirori da hanyoyin neman tsari na shari'a.

3. Harancin sihiri, da kafircin wanda yake yin sa ko yake gaskata shi.

4. An keɓance hasada da neman tsari, saboda lallai ita ce mafi cutarwar masifu, kuma ita ce asalin ƙiyayya tsakanin aljanu da mutane, da kuma mutane a tsakaninsu.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WAJIBCIN KIYAYE HARSHE DA HANNU

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amr (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Musulmin gaske shi ne wanda musulmai suka kuɓuta daga harshensa da hannunsa, mai hijira na haƙiƙa kuma shi ne wanda ya ƙaurace wa abin da Allah Ya yi hani a kansa**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito.[1]

❖ Sharhi:

Annabi (SAW) ya bayyana cewa lallai Musuluncin mutum ba ya cika har sai ya so wa musulmai abin da yake so wa kansa, kuma hakan ba zai samu ba sai idan sun kuɓuta daga sharrin harshensa; don haka ba zai zage su ba, ba zai la'ance su ba, ba zai ci namansu ba, kuma ba zai yi kowane irin nau'i daga cikin nau'ukan sharri da ɓarna a gare su ba, haka kuma idan suka kuɓuta daga sharrin hannunsa; saboda haka, ba zai ƙetare iyaka a kansu ta hanyar duka ko cutarwa ba, kuma ba zai karɓi dukiyoyinsu ba a bisa gaskiya ba.

Kuma ya bayyana cewa mafi falala cikin masu hijira shi ne wanda ya ƙaurace wa zunubai da saɓo; ita wannan ƙauracewar farilla ce ta tilas a kan kowane mutum, kuma ita take ne na cikar Musuluncinsa, da gaskiyar amsawarsa ga Ubangijinsa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Wajibcin kiyaye harshe da hannu daga cutar da musulmai.

2. Annabi (SAW) ya keɓance harshe da hannu ne saboda yawan kurakuransu da cutarwarsu, domin mafi yawan sharrori suna aukuwa ne daga gare su.

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (10), da Muslim (40).

3. Annabi (SAW) ya gabatar da harshe ne saboda cutarwa da shi ya fi yawa kuma ya fi sauƙi, kuma ciwonsa ya fi tsanani, kuma tasirinsa yana shafan rayayyu da matattu.

4. Wajibcin yaƙar zuciya a kan barin abubuwan da aka haramta da ƙaurace musu.

5. Lallai mafi falalar musulmi shi ne wanda ya ba da haƙƙoƙin Allah Maɗaukaki Sarki da haƙƙoƙin musulmai.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

ABUBUWAN DA ADDININ MUSULUNCI YA KEƁANTA DA SU

Addinin Musulunci: Shi ne addinin da Allah Ya aiko da Annabinsa Muhammadu (SAW) da shi, kuma Ya cika shi ga bayinsa, kuma Ya cika musu ni'ima da shi, kuma Ya yarda da shi a matsayin addini gare su; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((A yau Na cika muku addininku, kuma Na cika muku ni'imata, kuma Na yardar muku Musulunci ya zamo shi ne addininku)).[1]

Addinin Musulunci: Shi ne addinin duniya gaba ɗaya, wanda Allah Maɗaukaki Ya farlanta wa dukkan mutane su riƙe a matsayin addininsu, sai Ya ce – a inda Yake magana da Manzonsa (SAW) -: ((Ka ce: "Ya ku mutane, lallai ni Mazon Allah ne zuwa gare ku gaba ɗaya, wanda Yake da mallakar sammai da ƙasa, babu abin bautawa da gaskiya sai Shi; Shi ne Yake rayawa, kuma Shi Yake kashewa; don haka ku yi imani da Allah da Manzonsa Annabi Ummiyyi, wanda Yake imani da Allah da kalmominsa, kuma ku bi shi don ku zama shiryayyu")).[2] Kuma Annabi (SAW) ya faɗi a hadisi cewa: (Ina rantsuwa da wanda raina ke hannunsa, babu wani cikin wannan al'umma da zai ji labarina, bayahude ne, ko banasare, sannan ya mutu ba tare da ya yi imani da abin da aka aiko ni da shi ba; face ya kasance cikin 'yan wuta).[3]

Addinin Musulunci: Shi ne addinin ingantacce wanda Allah ba Ya karɓar wani addini koma bayansa daga kowa; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai addini a wajen Allah shi ne Musulunci)),[4] kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma duk wanda ya biɗi wani addini ba

---

1. (Azzumar: 3).
2. (Al-A'araf: 158).
3. Muslim ne ya rawaito shi (384).
4. (Suratu Alu-Imran: 19).

Musulunci ba, to ba za a karɓa daga gare shi ba, kuma a ranar lahira yana cikin hasararru)).[1]

Addinin Musulunci: Shi ne addinin gaskiya wanda Allah Ya yi alƙawrin kare shi da taimakonsa; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Shi ne Wanda Ya aiko Manzonsa da shiriya da addinin gaskiya, don ya ɗaura shi a kan dukkan addinai ko da mushirikai ba sa so)).[2]

Addinin Musulunci: Shi ne cikakken addini, wanda ya ƙunshi dukkan alheri da nagarta a aƙidarsa da shari'arsa; domin shi yana umurni da kaɗaita Allah, kuma yana hani daga shirka, yana umurni da gaskiya, kuma yana hani a kan ƙarya, yana umurni da adalci, kuma yana hani a kan zalunci, yana umurni da amana, kuma yana hani a kan ha'inci, yana umurni da cika alƙawari, kuma yana hani a kan yaudara, haka kuma yana umurni da biyayya ga iyaye, kuma yana hani a kan saɓa musu, yana umurni da sada zumunci, kuma yana hani a kan yanke zumunci, sannan yana umurni da kyautata maƙwabtaka, kuma yana hani a kan munana maƙwabtaka; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai Allah Yana umurmni da adalci, da kyautatawa, da ba wa makusanta taimako, kuma Yana hani a kan alfasha da mummunan laifi da zalunci, Yana muku wa'azi don ku wa'aztu)).[3]

[1]. (Suratu Alu-Imran: 85).
[2]. (Attauba: 33).
[3]. (Annahal: 90).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

LADUBBAN BIYAN BUƘATA

Addininmu addini ne na tsarki, da tsafta, da ladabi, da kunya; ya shar'anta ladubba na shari'a ga biyan buƙata, waɗanda mutum wanda Allah Ya karrama shi yake banbanta da su daga dabbobi, daga cikin waɗannan laduba akwai abubuwa masu zuwa:

❖ Abin da aka sunnanta yin shi wajen shiga bayan gida:

1. An sunnanta gabatar da ƙafar hagu a lokacin shiga bayan gida, da faɗin: "Bismillahi, Allahumma inni a'uzu bika minal-khubsi wal-khaba'isi", idan kuma a sarari ne sai ya faɗa a lokacin da zai zauna don biyan buƙata; dalili a kan haka kuwa shi ne cewa lallai Annabi (SAW) ya kasance idan zai shiga bayan gida yana cewa: (Allahumma inni a'uzu bika minal-khubsi wal-khaba'isi),[1] kuma ya zo a wani hadisi daban cewa, Annabi (SAW) ya ce: (Shamaki da ke tsakanin aljanu da al'aurar mutane shi ne idan mutum zai shiga bayan gida ya ce: "Bismillahi".[2]

2. An sunanta gabatar da ƙafar dama lokacin fita daga bayan gida, da kuma faɗin: "Gufranaka"; ya zo a hadisi cewa: (Ya kasance idan ya fita daga bayan gida yana cewa: "Gufranaka"[3], kuma ƙa'ida ita ce: Dama ana aiki da ita ne cikin abin da akwai girmamawa da kyawu a cikinsa, hagu kuma ana aiki da shi ne wajen gusar da ƙazanta da makamantanta.

3. An sunnanta wa mutum idan ya kasance a sahara, to ya tafi waje mai nisa ya kuma suturta kansa da katanga, ko bishiya, ko makamancisu; ya zo a hadisi cewa: (Lallai Annabi (SAW) ya

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (142), da Muslim (375).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito shi (606).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (148), da Muslim (266).

kasance idan ya tashi biyan buƙata sai ya yi tafiya mai nisa har sai ya je wajen da ba wanda yake ganinsa).[1]

❖ Tsarki da ruwa da kuma tsarki da hoge:

Yana wajaba a kan musulmi bayan ya gama biyan buƙatarsa, ya tsaftata kuma ya tsarkaka daga ɓurɓushin abin da ya fito daga gare shi, ta hanyar amfani da ruwa ko dutse, kuma yin sakaci a cikin hakan haramun ne, domin haƙiƙa Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ku tsarkaka daga fitsari, domin lallai mafi yawan azabar kabari daga rashin tsarkaka daga fitsari ne)[2].

- Kalmar "**Istinja'u**": Tana nufin: Gusar da ɓurɓushin abin da ya fito ta hanyar amfani da ruwa.
- Kalmar "**Istijmari**" kuma: Tana nufin: Gusar da gurbin abin da ya fito, da wani abu da ba ruwa ba, kamar dutse, ɗan kyalle, da makamantansu.

Kuma tsarkin dutse kaɗai yana wadatarwa, ta hanyar amfani da dutse da makamancinsa ko da kuwa akwai ruwa, Annabi (SAW)ya ce (Idan ɗayanku ya tafi zuwa bayangida, to ya yi tsarki da duwatsu guda uku, domin sun isar masa)[3], amma amfani da ruwa ya fi, kuma haɗa amfani da su biyun ya fi matuƙa wajen cika.

***Kuma tsarki da dutse yana da hukunce hukunce a shari'a, daga cikin su akwai:**

1- Ƙasa da shafa uku ba ya wadatarwa a tsarkin hoge, sannan idan ukun bai isa ba, sai ya yi ta shafa har sai wurin ya tsarkaka.

---

[1]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (2).
[2]. Ƙurɗubi ne ya rawaito shi (1/128).
[3]. Ahmad (2/108), da Daraƙuɗni (144) ne suka rawaito shi.

2- An sunnanta yin tsarkin dutse a kan mara (witiri), kamar uku ko biyar.

3- Lallai ya haramta a yi tsarki da kashin dabbobi ko ƙashi ko abinci, ko wani abu mai daraja, kamar takardar da akwai sunan Allah a kanta, da makamancin haka.

A cikin hadisin Salman (RA) ya ce: "Manzon Allah (SAW)ya hana mu yin tsarki da hannun dama, ko tsarki da ƙasa da dutse uku, ko tsarki da kashin dabbobi ko kashi"[1].

[1] Muslim (262).

ALHAMIS: DARASIN SIRA SAMARTAKAR ANNABI (SAW)

Annabi (SAW) ya yi aikin kiwon tumaki a samatarsa, domin ya rage wa baffansa Abu Ɗalib nauyin kashe kuɗi a kansa, kuma a lokacin da ya kai shekara goma sha biyu, baffansa ya fita da shi zuwa ƙasar Sham don yin kasuwanci, saboda kulawa da jin ƙai gare shi; domin rasa wanda zai kula da shi idan ya bar shi. A wannan tafiya kuwa ya sami ƙwarewa game da halin mutane da hanyoyin kasuwanci, kuma haƙiƙa baffansa ya ga alamomi a tare da shi a cikin wannan tafiya, waɗanda suka sa baffansa ya ƙara kula da shi da tsare shi, domin ya ci gaba da kasancewa cikin kariya, daga cikin alamomin akwai yadda gajimare yake masa inuwa, da kuma yadda bishiya ke karkatar da inuwarta gare shi, da kuma bisharar da Bahira ya yi a kansa, da umartarsa da cewa ya dawo gida da shi, domin kada yahudawa su gan shi su cutar da shi.[1]

Yayin da ya kai shekara goma sha biyar, ya halarci yaƙin Fijar, kuma ya yi tarayya da wasu baffanninsa a wasu daga cikin kwanakin yaƙin, domin kare wurare masu tsarki.

Sannan a lokacin da yake ɗan shekara ashirin, ya halarci yarjejeniyar Fudul, wadda manyan Ƙuraishawa suka haɗu suka yi alkawarin cewa za su taimaki duk wanda aka zalunta a Makka, kuma su mayar masa haƙƙinsa. Annabi (SAW) ya ce: (Haƙiƙa na halarci yarjejeniyar da aka yi a gidan Abdullah ibn Jud'an, da a ce an kira ni zuwa gare ta a lokacin Musulunci, da na amsa. Sun yi alkawari cewa za su mayar da haƙƙoƙin da aka tauye ga masu su, kuma kada wani azzalumi ya ci zarafin wanda aka zalunta)[2].

[1] Tizmizi (3620) ne ya rawaito shi.
[2] Baihaƙi (6366), da Ibnu Hisham (1/133) ne suka rawaito shi.

Kuma haƙiƙa Allah ya yi wa Annabinsa (SAW) kyakkyawar tarbiyya, ya kuma halicce shi bisa siffofi na kamala; domin haƙiƙa ya kasance mafi kyawun halitta a tsakanin takwarorinsa, kuma mafi kyawun hali, mafi kaifin hankali daga cikinsu, mafi gaskiya a magana, kuma mafi kiyaye amana, har sai da aka masa laƙabi da “Al’amin”, wato (Amintacce).

Kuma Allah Ya kare shi daga munanan ɗabi’u, bai taɓa bautar gumaka ba, bai taɓa shan giya ba, bai kuma taɓa aikata abin da zai zubar da mutunci ko ya rage masa darajan ba.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

USMAN ƊAN AFFAN (RA)

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne Usman ɗan Affan ɗan Abil As ɗan Umayya, wanda nasabarsa ta haɗu da ta Annabi (SAW) a kakansu na uku "Abdu Manaf". An haife shi a garin Ɗa'if bayan shekarar giwaye da shekara shida.

❖ Rayuwarsa da matsayinsa:

Usman (RA) ya kasance kyakkyawa ne, ba gajere ba, ba dogo ba, mai laushin fata, mai yawan gemu, mai yawan gashi. Yana daga cikin mutane mafi kunya, Annabi (SAW) ya ce game da shi: (Shin ba zan ji kunyar wanda mala'iku ke jin kunyarsa ba?)[1].

An masa laƙabi da "Zunnurain" ma'ana: (Ma'abocin haske biyu) saboda ya auri 'ya'yan Annabi (SAW) guda biyu: Ruƙayya da Ummu Kulsum.

Kuma ya kasance (RA) daga cikin masu yawan ibada, kuma mafiya yawan rawaito hadisai, kuma mafiya yawan karatun Alƙur'ani.

Kuma ya kasance yana cewa: "Da zukatanmu sun tsarkaka, da ba su ƙoshi da jin maganar Allah ba."[2]

Usman (RA) ya kasance daga cikin Sahabbai 'yan kasuwa, ya sadaukar da dukiyarsa wajen kyauta da bayarwa a tafarkin Allah. Yayin da Annabi (SAW) ya zo Madina, ya tarar da ruwan sha mai daɗi ya yi ƙaranci, sai Annabi (SAW) ya ce: (Wa zai sayi rijiyar

[1] Ahmad (26466) ne ya rawaito shi.
[2] Albidaya wannihaya (7/214).

Ruma, ya amfana da shi tare da sauran Musulmai, sai Allah ya saka masa da wanda ya fi shi alheri a Aljanna)[1].

Sai Usman (RA) ya sayi rijiyar daga wajen wani Bayahude da dirhami dubu ashirin, ya sanya ta don matalauta da mawadata da matafiya.

Bayan Annabi (SAW) ya gina masallacinsa, kuma masallacin ya yi wa mutane ƙanƙanta, sai Annabi (SAW) ya ce: (Wa zai saya filin gidan wane, sai ya ƙara shi cikin masallaci, sai Allah ya saka mishi da wanda ya fi shi alhaeri a Aljanna."[2] Sai Usman ya saye ta daga dukiyarsa da dirhami dubu ashirin da biyar.

Kuma a yaƙin Tabuka, Usman ya shirya rundunar "Jaishul-Usrah", inda ya samar da raƙuma dubu ɗaya da dawaki dari, ya kuma shirya su matuƙar shiri, ba tare da an rasa ko da dabaibayi ko linzami ba, sai ya zo wurin Manzon Allah (SAW) da dinari dubu goma, ya ajiye su a gabansa, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk abin da Usman ya yi daga yau ba zai cutar da shi ba)[3].

Usman ɗan Affan (RA) ya karɓi mulki bayan Umar (RA), sai ya kasance halifa na uku cikin halifofi shiryayyu, kuma ya gudanar da manyan ayyuka a lokacin mulkinsa, cikin su akwai ayyuka kamar haka:

- Ya tattara Alƙur'ani a cikin littafi guda, kuma ya yi kwafi huɗu daga gare shi, kuma ya rarraba su zuwa birane, ya kuma yi umarni da a ƙona dukkan wani Alƙur'ani koma bayan waɗannan.
- Ya faɗaɗa Masallatai biyu masu alfarma, kuma ya sake gina su da duwatsu.

[1]. Tizmizi (2703) ne ya rawaito shi.
[2]. Tizmizi (2703) ne ya rawaito shi.
[3]. Tirmizi (3701) ne ya rawaito shi.

- Ya kammala yaƙe-yaƙen faɗaɗa daular Musulunci da aka fara a zamanin Umar ɗan Khaɗɗab, har aka buɗe birnin Iskandariyya, da Afirka da Ƙuburus, kuma a zamaninsa daular Musulunci ta faɗaɗa a gabas da yamma.

❖ Rasuwarsa:

A ranar Juma'a, 18 ga watan Zul-Hijja, shekara ta 35 bayan hijira, wasu 'yan tawaye sun kai hari gidan Usman karkashin jagorancin bayahude Abdullah ɗan Saba', sai suka afka wa mutum huɗu daga samarin Ƙuraishawa yayin da suke kare shi, kuma ya kasance ya ji ajalinsa ya gabato, sai ya 'yanta bayi ashirin, ya kuma ce: " Lallai na ga Manzon Allah (SAW) jiya a mafarki, na kuma ga Abubakar da Umar, sai suka ce mini: (Ka yi haƙuri, domin lallai za ka sha ruwa tare da mu a dare mai zuwa)." sai ya buɗe Alƙur'ani yana karantawa, sai aka kashe shi alhali Alƙur'ani yana gabansa[1].

Kuma an binne shi a maƙabartar Baƙi'u, yana da shekara tamanin da biyu 82.

[1]. Siyaru A'laminnubala (1/204).

Auna fahimtarka a darusan mako na 3 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Hanyar kariya daga sihiri da hassada ita ce:		C
	a. Kula da ƙarfin jiki.	b. Barin hulɗa da mutane.	c. Zikiri da addu'o'in neman tsari da suka zo a shari'a.
Darasin Hadisi	Tambaya: Muhajiri na gaske shi ne:		A
	a. Wanda ya ƙaurace wa abin da Allah ya hana.	b. Wanda ya bar garinsa don neman abin da zai rayu da shi.	c. Wanda ya bar garinsa ya zauna a Makka ko Madina.
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin siffofin addinin Musulunci akwai cewa shi ne:		B
	a. Addinin da Allah Ya wajabta wa Larabawa kawai.	b. Addinin da Allah Ya wajabta wa mutane gaba ɗaya.	Addinin da Allah Ya wajabta wa mala'iku makusanta.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: An haramta yin tsarki da:		C
	a. Taɓo.	b. Dutse.	c. Abinci.
Darasin Sira	Tambaya: Yayin da Annabi (SAW) yake da shekaru ashirin ya halarci:		B
	a. Yarjejeniyar Fudul.	b. Yaƙin Fijar.	c. Sake gina Ka'aba.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin ayyukan da Usman (RA) ya yi akwai:		C
	a. Aika rundunar Usama.	b. Rubuta littafi.	c. Haɗa Alƙur'ani a wuri ɗaya.

MAKO NA HUDU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUN-NAS

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قُلۡ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ۝١ مَلِكِ ٱلنَّاسِ ۝٢ إِلَٰهِ ٱلنَّاسِ ۝٣ مِن شَرِّ ٱلۡوَسۡوَاسِ ٱلۡخَنَّاسِ ۝٤

ٱلَّذِي يُوَسۡوِسُ فِي صُدُورِ ٱلنَّاسِ ۝٥ مِنَ ٱلۡجِنَّةِ وَٱلنَّاسِ ۝٦﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: “Ina neman tsari da Ubangijin mutane.

2. “Sarkin mutane.

3. “Abin bautar mutane.

4. “Daga sharrin mai sa wasuwasi, mai noƙewa.

5. “Wanda yake yin wasuwasi a cikin ƙirazan mutane.

6. “Daga aljannu da na mutane.”

❖ Saƙon da surar ke ɗauke da shi:

Ƙwaɗaitarwa game da neman tsarin Allah daga sharrin shaiɗan da wasiwasin da yake sanyawa.

❖ Baƙin kalmomi:

أعوذ	**A’uzu**	Ina neman tsari
برب الناس	**Birabbin Nas**	Mai tarbiyantar da su, kuma Mahaliccinsu, Mai jujjuya halinsu.

إله الناس	**Ilahin Nas**	Abin bautarsu bisa cancanta.
الوسواس	**Alwaswasi**	Shaiɗan wanda yake jefa shakkunsa da ƙarairayinsa a cikin zuciya yayin gafala.
الخناس	**Alkhannas**	Wanda yake ɓuya kuma yake gudu yayin Ambaton Allah.
من الجنة والناس	**Minal jinnati wannas**	Mai sanya wasiwasi ya kan kasance mutum ko aljan.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

Suratun Nas na cikin surorin Makka, kuma ita ɗaya ce daga cikin surorin neman tsari guda biyu, kuma a cikinta ne Allah Maɗaukaki ya yi umarni da neman tsarin Ubangijin mutane kuma mahaliccinsu, daga sharrin shaiɗan wanda yake sanya wasiswasi a cikin zukatan mutane da ɓoyayyar muryar da ba a ji, sai ya jefa musu shubuhohi da tsoro da zargi marasa tushe, kuma yana ƙawata mummuna kuma yana munanta kyakkyawa, wannan kuwa yana faruwa ne idan mutum ya gafala daga ambaton Allah Maɗaukaki.

Kuma kamar yadda shaiɗan mai saka wasiwasi yake kasancewa daga cikin aljannu, haka nan yana iya kasancewa daga cikin mutane, yana aiki wajen ƙawata sharri, da kira zuwa gare shi, da jefa shubuhohi masu ɓatarwa da kalmomi marasa kyau.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Lallai Allah Maɗaukaki Shi ne Ubangiji na gaskiya, wanda ya wadatu daga halittu, Mai cikakken mulki da dukkan iko, da zartaccen hukunci a cikin halittunsa da umarninsa da hukuncinsa, yadda Ya so kuma lokacin da Ya so.

2. Bayanin maganin wasiwasi da tunani marasa kyau, ta hanyar yawaita ambaton Allah da neman tsari daga shaiɗan.

3. Wajabcin neman tsarin Allah kaɗai daga duk abin da mutum yake tsoro.

4. Hatsarin abokin banza, domin yana cutar da mutum kuma yana ɓatar da shi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI DAGA CIKIN ƊABI'UN MUNAFURCI

An karɓo daga Abdullah ɗan Amr (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Akwai wasu abubuwa guda huɗu da idan aka same su tare da mutum, to ya zama cikakken munafuki, kuma duk wanda aka samu ɗaya daga cikinsu a tare da shi, to yana da wata siffa ta munafunci har sai ya bari: Idan zai yi magana sai ya yi ƙarya, idan kuma ya yi alƙawari sai ya karya, idan kuma aka aminta da shi sai ya ci amana, idan zai yi husuma sai ya wuce gona da iri**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi[1].

❖ Sharhi:

Munafunci shi ne: mutum ya bayyana saɓanin abin da yake ɓoye a zuciyarsa, kuma ya kasu kashi biyu: munafunci na zuciya da munafunci na aiki.

- **Munafuncin na zuciya:** Shi ne mutum ya ɓoye kafirci a zuciyarsa amma ya nuna Musulunci a fili, kuma mai irin wannan nau'i kafiri ne mai dawwama a cikin wuta.

- **Munafunci na aiki:** Shi kuma yana nufin ayyukan da aka siffanta su da munafunci, waɗanda suke daga cikin halayen munafukai, amma ba ya cire imani daga zuciya, kuma wannan nau'in yana daga cikin manya zunubbai, amma ba ya fitar da mutum daga Musulunci.

A cikin wannan hadisin, Annabi (SAW) yana gargaɗi game da wasu daga cikin halayen munafunci na aiki, kuma su guda huɗu ne, duk wanda suka tattaru a tare da shi, to ya zama cikakken munafuki,

[1] Bukahari (2459), da Muslim (58) ne suka rawaito shi.

kuma duk wanda yake da ɗaya daga cikinsu, to yana da siffar munafunci har sai ya daina.

Na farko: Ya kasance ya shahara da cin amana tsakanin mutane.
Na biyu: Ya kasance ya shahara da ƙarya a cikin magana.

Na uku: Idan ya yi alkawari da wani, yana cin amanarsa, kuma baya cika alkawarinsa.

Na huɗu: Yin fajirci yayin husuma, kuma ma'anar fajirci a nan ita ce: ya kauce wa gaskiya da gangan, domin ya mai da gaskiya ta koma ƙarya, ƙarya kuma ta koma gaskiya.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Lallai munafunci na aiki yana da siffofi masu yawa, kuma waɗanda aka ambata a cikin wannan hadisin su ne mafiya shahara kuma mafiya cutarwa.

2. Tsawatawa a kan cin amana, sawa'un a cikin aiki, ko dukiyoyi, ko haƙƙoki, ko sirrika, da makamantansu.

3. Hatsarin yin ƙarya a cikin magana, da kuma cewa yana daga cikin siffofin munafukai.

4. Gargadi game da karya alƙawura, wanda ya haɗa alkawuran da ke tsakanin bawa da Ubangijinsa, da kuma alkawuran da ke tsakanin bawa da sauran mutane.

5. Haramcin yin fajirci yayin husuma.

6. Wajabcin guje wa munafunci da ma'abotansa.

7. Cewa mutum na tattara siffofin alheri da siffofin sharri, da siffofin imani da siffofin munafunci.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA
MATSAYIN ILIMIN AƘIDA

Ilimin aƙida shi ne mafi daraja kuma mafi girma cikin ilimomi, kuma wannan matsayi nasa ya kasance ne saboda abubuwa da dama:

1. Lallai darajar ilimi tana da alaƙa da abin da ake koyo, kuma abin da ake koya a cikin ilimin aƙida shi ne sanin Allah Maɗaukaki da sunayensa da siffofinsa da ayyukansa, da abin da ya dace da shi da abin da ya wajaba a tsarkake shi daga gare shi, kuma wannan shi ne mafi girman abin da ake koya, kuma shi ne mafi muhimmanci abin da ya kamata a nema.

2. Lallai darajar ilimi tana kasancewa ne gwargwadon buƙatuwar mutane gare shi, kuma babu wani ilimi da mutane suka fi buƙatuwa zuwa gare shi fiye da ilimin aƙida, domin duk lokacin da sanin bawa ga Ubangijinsa ya zama ingantacce kuma cikakke, sai ya ƙara sa shi girmama Ubangijinsa, da bin dokokinsa da shari'arsa, kuma hakan zai fi sanya shi yin shiri don lahira.

3. Lallai ilimin aƙida shi ne sababi mafi girma na samun rayuwa mai daɗi, domin aƙida tana sadar da mumini da Ubangijinsa, kuna tana sa ya san Ubangijinsa, sai ya rayu cikin kwanciyar hankali, ba tare da damuwa ko tashin hankali ba, ko ruɗani a tunani, ko karkacewa a zuciya, domin ya yarda da Ubangijinsa a matsayin Mahalicci, Mai tsara al'amura, Mai hukunci, Mai tsara dokoki, kuma Shi kaɗai ne abin bauta, wanda ake masa ɗa'a, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Waɗanda suka yi imani, kuma ba su garwaya

imaninsu da zalunci ba, waɗannan su suke da aminci, kuma su ne shiryayyu))[1].

4. Lallai ana auna darajar ilimi ne da girman amfaninsa da haɗarin rashinsa, kuma ingantacciyar aƙida ita ce ginshiƙin tsira a lahira, kuma ita ce sharaɗin karɓar duk wani aiki na alheri, shirka kuma ita ce sababin lalacewar ayyuka da dawwamar da mutum cikin wuta, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Lallai Allah ba Ya gafarta a yi shirka da Shi, amma Yana gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda Ya ga dama. Kuma duk wanda ya yi shirka da Allah, to haƙiƙa ya ƙirƙiri wani gagarumin laifi))[2].

5. Lallai ingantacciyar aƙida tana ‘yantar da bawa daga dogaro da halittu da aiki domin su, wannan it ace izza ta gaskiya da ɗaukaka ta haƙiƙa, saboda haka, bawa ba zai zama bawa ba sai na Allah, kuma ba ya fatan samun rabauta sai daga gare shi, kuma ba ya tsoron kowa sai shi, kuma wannan shi ne cikakken rabauta.

[1] [Suratul An‘am: 82].

[2] [Suratun Nisa’i: 11]

LARABA: DARASIN FIƙIHU
ABUBUWAN DA AKA HARAMTA A YAYIN BIYAN BUƘATA DA ABUBUWAN DA AKE ƘI

❖ Abubuwan da suka haramta yayin shiga bayan gida:

1. Haramun ne mutum ya fuskanci alƙibla ko ya juya mata baya, yayin biyan buƙata wurin da yake fili ne, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan kuka je za ku biya buƙuta, to kada ku fuskanci alƙibla, kuma kada ku juya bayanku gare ta, sai dai ku juya gabas ko yamma)[1], Amma idan yana cikin gini ne, babu laifi, saboda abin da Abdullah ɗan Umar (RA) ya faɗi cewa: "An hana yin hakan ne kawai a fili, amma idan akwai abin da yake tsakaninka da alƙibla, to babu laifi"[2], Amma abin da ya fi shi ne a guji yin hakan ko da kuwa a cikin gini ne.

2. Haramun ne karanta Alƙur'ani a bayan gida, ko shiga da shi, domin shi magana ce mafi daraja, kuma karanta shi ko shiga da shi irin wannan wuri nau'i ne na wulaƙantawa.

3. Haramun ne mutum ya riƙe al'aurarsa da hannunsa na dama yayin yin fitsari, ko ya yi tsarki da shi, domin Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan ɗayanku zai yi fitsari, to kada ya riƙe al'aurarsa da hannun damansa, kuma kada ya yi tsarki da hannunsa na dama)[3].

4. Haramun ne yin fitsari a cikin ruwan da ba ya gudana, kamar tafkuna, da ƙananan kwazazzaɓai, da wuraren wanka, saboda yana gurɓata su kuma yana lalata tsaftarsu, ya zo a cikin hadisi cewa:

---

[1]. Bukhari (144) da Muslim (264) ne suka rawaito shi.
[2]. Abu Dawuda (14), da Tirmizi (14) ne suka rawaito shi.
[3]. Bukhari (154) da Muslim (267) ne suka rawaito shi.

“Manzon Allah (SAW) ya hana yin fitsari a cikin ruwan da baya gudana”[1].

5. Haramun ne mutum ya biya buƙatarsa a kan hanya, ko a cikin inuwa, ko a wuraren jama’a, ko ƙarƙashin itaciya mai ‘ya’ya, da makamantan haka. Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ku kiyaye abubuwa guda biyu da ke jawo la’ana.” Suka ce: Mene ne waɗannan abubuwa biyu, ya Manzon Allah? Ya ce: “Mutumin da yake biyan buƙatarsa a kan hanyar mutane ko a inuwarsu.”[2]

❖ Abubuwan da suke makaruhi ne yayin biyan buƙata:

1. Makaruhi ne mutum ya bayyana al’aurarsa a wurin da yake fili kafin ya kusanci ƙasa, ya zo a cikin hadisi cewa: “Manzon Allah (SAW), idan yana son yin bayan gida, baya ɗaga tufafinsa sai ya kusanci ƙasa.”[3]

2. Makaruhi ne yin magana yayin biyan buƙata, domin an ruwaito cewa wani mutum ya wuce kusa da Annabi (SAW) yayin da yake yin fitsari, sai ya yi masa sallama, amma bai amsa masa ba[4].

3. Makaruhi ne yin fitsari a cikin rami ko wani wuri da ya tsage. Ya zo cikin hadisi cewa: “Annabi (SAW) ya hana yin fitsari a cikin rami.”[5]

4. Makaruhi ne shiga bayan gida da wani abu da ke ɗauke da ambaton Allah, sai dai idan akwai buƙatar hakan, ya zo cikin hadisi cewa: “Manzon Allah (SAW) idan zai shiga bayan gida yana cire

[1]. Bukhari (239), da Muslim (281) ne suka rawaito shi.
[2]. Muslim (269) ne ya rawaito shi.
[3]. Muslim (11) ne ya rawaito.
[4]. Muslim (370) ne ya rawaito shi.
[5]. Abu Dawuda (29) da Nasa’i (24) ne suka rawaito shi.

zoben sa.”[1] Amma idan akwai buƙata kamar shiga da takardun kuɗi waɗanda idan aka bar su a waje za a iya sacewa ko ko amanta da su, to babu laifi.

[1] Abu Dawuda (19) da Tirmizi (1746) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASIN SIRA AUREN ANNABI (SAW)

Yayin da Annabinmu (SAW) ya shahara da gaskiya da amana a tsakanin mutanensa, sai Khadija ‘yar Khuwailid (RA) ma’abociya ɗaukaka da dukiya, ta yi masa tayin yin kasuwanci da dukiyarta zuwa Sham, sai Annabi (SAW) ya amince, sai ya tafi tare da ayarin ‘yan kasuwa daga Makka zuwa Sham, tare da rakiyan Maisara bawan Khadija, sai Annabi (SAW) ya sami riba mai yawa.

Kuma yayin da ayarin ya dawo, sai Maisara ya faɗa wa shugabarsa abubuwan da ya gani daga kyawawan halayen Annabi (SAW) da gaskiyarsa, sai hakan ya burge ta sosai, sai Khadija ta masa tayin aurenta.

Sai Annabi (SAW) ya aure ta, a lokacin tana da shekaru arba’in, shi kuma yana da shekaru ashirin da biyar, sai ta kasance matarsa ta farko, kuma wacce ya fi so a cikin matayensa.

Ta rayu tare da shi cikin farin ciki, ta ƙarfafe shi kuma ta taimake shi, kuma bai auri wata ba sai bayan rasuwarta bayan shekaru ashirin da biyar da aurensu.

Khadija (RA) ce ta haifa wa Annabi (SAW)’ya’yansa maza da mata, su ne: Alƙasim — wanda da shi ake yi wa Annabi alkunya — da Abdullahi, kuma sun rasu tun suna ƙanana; sannan Ruƙayya, Zainab, Umm Kulsum, da Faɗima, ban da Ibrahim, shi mahaifiyarsa ita ce Mariya Alƙibtiyya.

ASABAR: DARASIN RAYUWAR SAHABBAI

ALIYU ƊAN ABU ƊALIB (RA)

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne Abul Hasan Aliyu ɗan Abu Ɗalib ɗan Abdulmuɗɗalib Alhashimi Alƙurashi, ɗan baffan Manzon Allah (SAW) kuma surukinsa.

An haife shi a Makka shekaru goma kafin Manzanci, kuma lokacin da aka aiko Annabi yana ƙarami, shi ne na farko da ya karɓi Musulunci daga cikin yara.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Aliyu (RA) ya kasance mai kyakkyawar fuska, mai tsananin baƙar ƙwayar ido, jarumi mayaƙi, ya siffantu da jarumta, ya halarci dukkan yaƙoƙin Manzon Allah (SAW).

Daga cikin manyan ayyukansa (RA): akwai cewa shi ne ya sadaukar da kansa don Manzon Allah (SAW) a daren hijira, inda ya kwanta madadin Annabi domin mushirikai su zaci cewa Annabi (SAW) bai fita ba.

Kuma daga cikin manyan ayyukansa akwai cewa yana daga cikin masu rubuta wahayi, kuma Annabi (SAW) ya aminta da shi, kuma yayin da Annabi (SAW) ya rasu, Aliyu (RA) yana daga cikin waɗanda suka yi masa wanka, kuma yayin da ya kalli Annabi, sai ya ce: “Mahaifina fansa a gare ka! Ka kasance mai tsarki a rayuwarka da bayan mutuwarka”[1].

[1]. Ibnu Maja (1297) ne ya rawaito shi.

Kuma Aliyu (RA) yana daga cikin sahabbai mafiya ilimin Alƙur'ani da ilimominsa, an ruwaito daga gare shi yana cewa: "Ku tambaye ni game da Littafin Allah, domin babu wata aya face na san ko da da daddare ko da rana aka saukar da ita, ko a kan tudu ko kuma a saman dutse"[1].

Tabi'i Masruq ɗan al-Ajda' ya ce: "Ilimi yana tiƙewa zuwa mutane uku: Malamin Madina, malamin Sham, da malamin Iraƙi. Malamin Madina shi ne Aliyu ɗan Abu Ɗalib, malamin Kufa kuma shi ne Abdullahi ɗan Mas'ud, malamin Sham kuma shi ne Abu Darda'"[2].

Aliyu (RA) ya karɓi halifanci bayan Usman (RA), ya kasance halifa na huɗu ga musulmai, ya yi umarni da kula da harkokin kasuwanni, kuma ya tilasta wa 'yan kasuwa bin dokokin shari'a.

An san shi da tawali'u, da gudun duniya, da himma wajen neman lahira, wani lokaci Ashtar ɗan Ƙais ya shiga wajensa, sai ya same shi yana tsaye yana salla da daddare, sai ya ce masa: "Ya Amirul Muminina, kana yin azumi da rana, kana kuma yin salla daddare, ga kuma gajiya tsakanin dare da rana". Sai Aliyu (RA) ya ce: "Tafiyar zuwa lahira tana da nisa, don haka akwai buƙatar rage ta da daddare"[3]

❖ Rasuwarsa:

Aliyu (RA) ya rasu a daren 21 ga watan Ramadan shekara ta 40 bayan hijira, bayan Ibn Muljam ya sare shi da takobi mai guba a kansa, yayin da yake jagorantar musulmai a sallar Asuba a masallacin Kufa, Ya rayu bayan haka kwanaki uku, sannan ya rasu

[1]. Tarikhu Dimashƙ (42/398).
[2]. Tarikhu Dimashƙ (42/410).
[3]. Majmu'u rasa'il Ibn Rajab (4/421).

(RA), yana da shekaru 63, kuma ya yi halifanci tsawon shekara biyar.

Auna fahimtarka a darusan mako na 4			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Menene ma'anar "Alkhannas"?		A
	a. Wanda yake ɓuya kuma yake gudu idan an ambaci Allah.	b. Wanda yake jefa shakku da ƙarairayi a zukuta idan suka gafala.	c. Wanda yake lalata wa masallata sallarsu.
Darasin Hadisi	Tambaya: Mene ne hukuncin munafunci na aiki "Nifaƙ Amali"?		A
	a. Yana daga cikin manyan zunubai.	b. Babbar shirka ne.	c. Ƙaramar shirka ne.
Darasin Aƙida	Tambaya: Ilimin Aƙida shi ne mafi daraja kuma mafi girma daga cikin ilimomi, saboda:		B
	a. Alaƙarsa da ibadodi na gangan-jiki.	b. Alaƙarsa da Allah Maɗaukaki.	c. Zurfin mas'alolinsa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Hukuncin magana yayin biyan buƙata:		C
	a. Makaruhi ne.	b. Halal ne.	c. Haramun ne.
Darasin Sira	Tambaya: Khadijah (RA) ita ce ta haifi dukkan 'ya'yan Manzon Allah (SAW) maza da mata, banda:		C
	a. Faɗimatuz-Zahra.	b. Alƙasim.	c. Ibrihim.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Aliyu (RA) ya siffantu da:		A
	a. Jarumta da gwarzantaka.	b. Yawan tafiya.	c. Tsawon tafiya da kasala.

MAKO NA BIYAR

LAHADI: DARASIN TAFSIRI

SURATUL-KAFIRUN

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡكَٰفِرُونَ ١ لَآ أَعۡبُدُ مَا تَعۡبُدُونَ ٢ وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ ٣ وَلَآ أَنَا
عَابِدٞ مَّا عَبَدتُّمۡ ٤ وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ ٥ لَكُمۡ دِينُكُمۡ وَلِيَ دِينِ ٦﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Ka ce: “Ya ku waɗannan kafirai.

2. “Ba zan bauta wa abin da kuke bauta wa ba.

3. “Ku kuma ba masu bautar abin da nake bauta wa ba ne.

4. “Ni kuma ba mai bauta wa abin da kuke bauta wa ba ne.

5. “Ku ma ba za ku bauta wa abin da nake bauta wa ba.

6. “Addininku na gare ku, ni ma kuma addinina na gare ni.”

❖ Sababin Saukar Surar:

Surar ta sauka domin martani ga shawarar wasu daga cikin mushrikai da suka nemi Annabi (SAW) da ya bauta wa ababen bautansu tare da su na tsawon shekara ɗaya, kuma suma su bauta wa Ubangijinsa tare da su na tsawon shekara ɗaya, domin sulhu tsakaninsu da shi, da kawo ƙarshen husumomi a tunaninsu![1]

[1]. Tafsirin Ɗabari (23/703).

❖ Falalar Surar :

- An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar Allah YA ƙara musu yarda ya ce : Manzon Allah (SAW) ya ce: (Surar «Ƙul ya ayyuhal kafirun » tana daidai da ɗaya bisa huɗun Alƙur'ani)[1].
- An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (RA) ya ce : «Ba zan iya ƙirga sau nawa na ji Manzon Allah (SAW) yana karanta 'Ƙul ya ayyuhal kafiru' da 'Ƙul huwallahu Ahad' a raka'o'i biyu na bayan sallar magriba da na kafin sallar asubahi ba »[2].

❖ Saƙon da surar take ɗauke da shi:

Barranta daga kafirci da ma'abotanta.

❖ Baƙin kalmomi:

لا أعبد ما تعبدون	**La a'budu ma ta'budun**	A yanzu ba zan bauta wa abin da kuke bauta wa ba.
ولا أنا عابد ما عبدتم	**Wa la ana abidun ma abattum**	Kuma har a nan gaba ba zan bauta wa abin da kuke bauta wa ba.
لكم دينكم	**Lakum dinukum**	Ku riƙe shirkarku da kafircinku.
ولي دين	**Wa liya din**	Zan riƙe ikhlasi na da tauhidi na.

❖ Ma'anar surar a dunƙule:

Suratul Kafirun na daga cikin surorin Makka, ta zo domin kiran mutane zuwa tsantsanta ibada da tauhidi, da barranta daga shirka da bata. A cikinta Allah Yana umurtar Manzonsa (SAW), da ya katse tsammanin kafirai cewa zai bar kira zuwa gaskiya ko ya bi

[1] Tirmizi ne ya rawaito shi (2893).
[2] Tirmizi ne ya rawaito shi (431).

addininsu. Shi kuwa yana nan tsaye a kan bauta wa Allah wanda babu abin bauta wa bisa cancanta sai Shi, amma su kuma suna nan suna bautar gumakansu marasa amfani, su suna da addininsu wanda suka kwaikwayi kakanninsu a cikinsa, kuma shi yana da addininsa wanda Allah Ya yardar masa.

❖ **Abubuwan da za mu koya daga surar:**

1. Tabbatar da Kaɗaita Allah cikin bautarsa, da tabbatar da bauta gare Shi, Shi kaɗai, tare da barin bautar gumaka.

2. Tabbatar da bambanci tsakanin ma’abota imani da ma’abota shirka, da barranta daga gare su da shirkatsu.

3. Lallai duk wanda bai kaɗaita Allah shi kaɗai da ibada ba, kuma bai amince da Musulunci a matsayin addininsa ba, to kafiri ne.

LITININ: DARASIN CIKIN HADISI

KWADAITARWA GAME DA LIZIMTAR TSORON ALLAH MADAUKAKIN SARKI

An karɓo daga Abu Zarri Algifari (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: “Ka ji tsoron Allah a duk inda kake, ka bi bayan mummunan aiki da kyakkyawa sai ya goge shi, kuma ka mu’amalanci mutane da kyakkyawar ɗabi’a.”[1]

❖ Sharhi:

Wannan hadisi ne mai girma, wanda a cikinsa Manzon Allah (SAW) ya tattara abin da ya zama tilas ga mumini na haƙƙin Allah da haƙƙin bayin Allah.

Haƙƙin Allah: Shi ne bawa ya ji tsoronsa matuƙar tsoronsa, ta hanyar tsoron fushinsa da azabarsa, ta hanyar yin abin da ya wajabta, da barin abin da ya haramta, kuma duba da cewa sakaci zai iya faruwa a cikin wannan tsoron nasa, sai Annabi (SAW) ya yi umarni da abin da zai tunkuɗe sakacin kuma ya goge shi, shi ne bin bayan mummunan aiki da kyakkyawa, kamar sadaka, da istigfari, da tuba ta gaskiya, da komawa ga Allah, domin goge wannan zunubi da kawar da tasirinsa daga zuciya.

Haƙƙin mutane: Shi ne kyautata musu ta hanyar kyakkyawan hali, da kyautata mu’amala, da tattausan magana, da sakin fuska, da haƙuri, da juriya, da kawar da abin cutarwa, da yafe wa wanda ya munanta.

[1] Ahmad (21441), da Tirmizi (1987) ne suka rawaito shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Wajincin tabbatar da tsoron Allah, kuma shi ne wasiyyar Allah ga waɗanda suka gabata da waɗanda suka zo daga baya, kuma ita ce wasiyyar Manzon Allah (SAW) ga al'ummarsa.

2. Ma'anar taƙawa: Ita ce ka sanya katanga tsakaninka da azabar Allah ta hanyar aikata abin da Allah ya wajabta da barin abin da ya haramta.

3. Lallai aikata kyakkyawan aiki bayan mummuna yana zama sanadiyyar gafarta mummunar.

4. Kwaɗaitarwa game da kyakkyawar mu'amala da mutane, kamar yadda Allah Ya ce: ((Ku faɗa wa mutane kyakkyawan magana)).[1]

[1]. [Al-Baqara: 83].

TALATA: DARASIN AƘIDA

AMFANIN INGANTACCIYAR AƘIDA

Amfanin Aƙida: shi ne kyawawan sakamako da ake samu daga bin aƙida ta gaskiya.

Su kuwa suna da yawa, daga cikinsu akwai:

Na farko: Tsarkake niyya da ibada ga Allah Maɗaukaki; domin duk wanda aƙidarsa ta gyaru, kuma ya san Ubangijinsa da kyau, zai girmama shi, kuma ya ji tsoransa, ya kuma tsantsanta aikinsa saboda Shi.

Na biyu: Cikar son bawa ga Ubangijinsa Allah Maɗaukaki, da girmama shi bisa kyawawan sunayensa da sifofinsa maɗaukaka.

Na uku: Jajircewa cikin al'amura, ta yadda mumini ba zai bari wata dama ta aikin alheri ta wuce ba face ya yi amfani da ita, cikin fatan samun lada daga Allah; kuma ba zai kusanci wurin zunubi ba, saboda tsoron azabar Allah.

Na huɗu: Lallai mumini yana samun sauƙin yin ibada, kuma yana samun sauƙin guje wa bin son zuciyarsa; domin daga cikin jigon aƙidarsa akwai tsoron Allah da yarda da tashin kiyama da sakamako bisa ayyuka.

Na biyar: Allah Maɗaukaki yana gafarta zunubai ta dalilin tauhidi, yana kuma shafe kura-kurai da shi; kamar yadda ya- zo a hadisin Ƙudusi: (Ya kai ɗan'adam, idan da za ka zo mini da zunuban da suka cika ƙasa, sannan ka haɗu da ni ba tare da ka yi mini shirka ba, to da na zo maka da gafara kwatankwacinsu".[1]

[1]. Tirmizi (3540) ne ya rawaito shi.

Na shida: Lallai tauhidi shi ne babban sababi da Allah ke shigar da mutum Aljanna saboda shi, kuma yana hana shiga wuta. Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya shaida cewa babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah Shi kaɗai, ba Shi da abokin tarayya, kuma Annabi Muhammadu bawansa ne kuma Manzonsa, kuma Annabi Isa bawan Allah ne kuma Manzonsa, kuma kalmarsa ce da ya jefa ta ga Maryama, kuma ruhi ne daga gare shi, kuma Aljanna gaskiya ce, wuta ma gaskiya ce, to Allah zai shigar da shi Aljanna bisa abin da ya aikata na ayyuka).[1]

Na bakwai: Lallai gyaruwar aƙida ita ce sababi mafi girma na shimfiɗa ni'imomi da alherai, da kawar da masifu da damuwa a duniya da lahira, Allah Madaukaki Ya ce: ((Kuma in da a ce mutanen alƙaryu sun yi imani kuma sun tsare dokokin Allah, to lallai da Mun buɗe musu albarkatu daga sama da kuma ƙasa)).[2]

Na takwas: Lallai ingantacciyar akida tana rage wa bawa tsanani da ƙunci, kuma tana sauƙaƙa masa ciwo da jarabawa, tana kuma sanyaya masa zuciya lokacin masifu, sai ya karɓe su da buɗaɗɗiyar zuciya, cikin nutsuwa, da yarda da ƙaddarar Allah; saboda saninsa ga hikimar Ubangijinsa da tausayinsa, da fahimtarsa ga haƙiƙanin duniya da makomarta.

[1]. Bukhari (3252) da Muslim (28) ne suka rawaito shi.
[2]. [Al-A'raf: 96].

LARABA: DARSI CIKIN FIƘIHU

SUNNONIN FIƊIRA

Sunnonin fiɗira: Wasu ayyuka ne kyawawa da addininmu madaidaici ya zo da su, saboda abin da ke cikinsu na ado da tsafta da kyan gani, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Abubuwa guda biyar na daga cikin tsaftar ɗan'adam, su ne: aske gashin al'aura, da kaciya, da aske gashin baki, da cire gashin hamata, da yanke farce)[1].

Kuma an kira su da wannan suna ne, domin mai aikata su yana siffantuwa da wani tsari da Allah ya halicci mutane a kansa, kuma ya so mu shi, domin su kasance a mafi kyawun yanayi da kuma mafi cikarsa, haka kuma su ne sunnar da ta gabata, wadda Allah ya zaɓa wa annabawa, kuma dukan shari'o'i suka haɗu a kanta.

***Ga cikakken bayani a kansu kamar haka:**

1. **Aske gashin al'aura:** Shi ne cire gashin da ke kewaye da al'aura, an kira shi da suna "istihdaɗ" ne saboda amfani da ƙarfe wajen aske shi, kuma cikin cire shi akwai kyau da tsafta, kuma ba laifi a cire shi ta hanyar amfani da wasu kayan cire gashi na zamani.

2. **Kaciya:** Wajiba ce ga maza, kuma sunna ce ga mata, abin da ya fi shi ne yin ta lokacin ƙuruciya domin ya fi warkewa da wuri, kuma don yaro ya tashi cikin cikakkiyar kamala. Hikimomin da ke cikin kaciya su ne:

- Ita sunna ce ta Annabin Allah Ibrahim (AS), da kuma zurriyyarsa masu tauhidi.

[1]. Bukhari (5889), da Muslim (257) ne suka rawaito su.

- Tana kawo tsafta da tsarkakewa daga taruwar najasa.

- Tana daidaita sha'awa, domin idan ta yi yawa tana mayar da mutum kamar dabba, idan kuma aka rasa ta tana mayar da mutum tamkar sandararrun abubuwa.

3. **Aske gashin baki da rage shi:** Ingantattun hadisai sun zo suna umarni da aske gashin baki da rage shi, da kuma barin gemu da cika shi, domin abin da ke cikin haka na kyawu, kamannin na mazantaka, da saɓawa kafirai, da guje wa kamanceceniya da mata, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ku aske gashin baki, kuma ku bar gemu, ku saba wa Majusawa).[1] kuma ya ce: (Ku saɓa wa mushrikai, ku bar gemu, ku rage gashin baki).[2]

4. **Yanke akaifa (farce):** Yanke akaifa yana ƙawata su, kuma yana cire datti da ke taruwa a ƙarƙashinsu, kuma yana nisantar da mutum daga kamanceceniya namun daji masu farauta.

5. **Cire gashin hamata:** Ana cire gashin hamata ta hanyar cizge shi, ko aske shi, ko ta wata hanya daban; domin hakan yana kawo tsafta, da kawar da wari.

Akwai wasu halaye biyar ƙari a kan waɗannan guda biyar, su ne: goge baki, shakar ruwa cikin hanci, kurkurar baki, yin tsarki da ruwa, da wanke lungunan yatsun hannu, waɗanda datti ke tattaruwa a cikinsu, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Abubuwa goma na daga cikin tsafta, su ne: aske gashin baki, da barin gemu, da amfani da siwaki, da shakar ruwa, da yanke faratu, da wanke lungunan yatsu,

[1]. Muslim (260) ne ya rawaito shi.
[2]. Bukhari (5892), da Muslim (258) ne suka rawaito shi.

da cire gashin hamata, da aske gashin al’aura, da yin tsarki da ruwa)[1].

[1]. Muslim (261) ne ya rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA
LABARIN ABIN DA YA FARU GAME DA DUTSEN HAJARUL ASWAD

Yayin da Annabi (SAW) ya kai shekaru talatin da biyar — wato shekaru biyar kafin a aiko shi annabta — ƙabilar Ƙuraishawa ta sake gina Ka'aba, saboda rushewar da ta samu daga ambaliyar ruwa da ta shafi Makka a lokacin.

Sai suka raba aikin ginin tsakanin ƙabilu, kowace ƙabila ta ɗauki wani ɓangare daga cikin bangarorin Ka'aba, kuma suka fara gina Ka'aba da duwatsun da ke cikin kwari.

Yayin da suka gama gina ta, kowace ƙabila ta so ta sami darajar saka Dutse Mai Tsarki (Hajarul Aswad) a wurinsa, sai rikici ya taso tsakaninsu, har ya zama saura kaɗan su yi yaƙi, Sai Abu Umayya bin Mugira Almakhzumi ya ba su shawara cewa su amince cewa duk wanda ya fara shigowa ta ƙofar Masallaci Mai alfarma, to shi ne zai zama mai yanke hukunci tsakaninsu. Sai suka yarda da wannan ra'ayi, suka jira farkon wanda zai shigo, sai ga Manzon Allah (SAW), da suka gan shi, sai suka yi ihu da farin ciki suka ce: Ga amintacce! Mun yarda shi ne zai yi mana hukunci!

Sai suka ba shi labari, sai Annabi (SAW) ya umarce su da su kawo masa wata riga, sai suka kawo, sai ya sa Dutse Mai Tsarki a tsakiyarta, sannan ya umarci manyan ƙabilu su riƙe gefen rigar, su ɗaga tare har zuwa wurin da za a sa Dutsen, da suka kai wurin, sai Annabi (SAW) ya ɗauki Dutsen da hannunsa mai albarka, ya sanya shi a wurinsa[1].

Da haka Annabi (SAW) ya katse wutar fitinar, kuma hikimarsa da kaifin hankalinsa suka bayyana.

---

[1]. Albidaya wan Nihaya (2/300).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI ABDURRAHMAN ƊAN AUF (RA)

❖ Sunan sa da haihuwarsa:

Shi ne Abdurrahman ɗan Auf, ɗan Abdi Auf, ɗan Haris, ɗan Zuhra ɗan Kilab, nasabarsa tana haɗuwa da ta Manzon Allah (SAW) ta ɓargaren Kilab ɗan Murra.

An haifi Abdurrahman ɗan Auf (RA) a Makka bayan shekarar giwaye da kusan shekaru goma, kuma sunansa kafin zuwan Musulunci shi ne “Abdu Amr”, yayin da ya musulunta Annabi (SAW) ya canza masa suna zuwa “Abdurrahman”[1], kuma alkunyansa ita ce Abu Muhammad.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Abdurrahman ɗan Auf (RA) yana daga cikin farkon waɗanda suka shiga Musulunci, kuma shi ɗaya ne daga cikin mutum takwas na farko da suka yi imani, haka kuma, yana daga cikin sahabbai goma da aka yi musu Bushara da shiga Aljanna, kuma yana daga cikin farkon waɗanda suka yi hijira sau biyu.

Ya kasance (RA) mai kamun kai, mai yawan kyauta, mai yawan bayarwa saboda Allah, mai tawali’u da kuma gudun duniya. Yakan yi tafiya tsakanin bayinsa, amma saboda tawali’unsa da saukin halinsa ba a bambance shi da su.

Haka kuma ya kasance ɗan kasuwa mai basira, masanin hanyoyin kasuwanci, daga cikin labarinsa a fannin kasuwanci akwai cewa lokacin da ya isa Madina, Annabi (SAW) ya haɗa ‘yan’uwantaka tsakaninsa da Sa’ad ɗan Rabi’ Al’anṣari, sai Sa’ad ɗan Rabi’ ya yi

[1]. Ɗabarani (253) ne ya rawaito shi.

masa tayin rabon dukiyarsa, sai ya ƙi, kuma ya ce: “Ku nuna min kasuwa”, sai ya fara kasuwanci, yana saye da sayarwa, har ya samu riba kuma dukiyarsa ta haɓaka.[1]

Abdurrahman ɗan Auf (RA) ya halarci yaƙin Badar, da bai’atur-Riḍwan, da sauran yaƙe-yaƙe, kuma Annabi (SAW) ya yi salla a bayansa a lokacin yaƙin Tabuk.[2]

Ya janye kansa daga neman halifanci lokacin majalisar shura, bayan kashe Umar (RA).

Yana daga cikin masu kyautata wa matan Manzon Allah (SAW) bayan wafatin Manzon Allah (SAW), yana taimaka musu da dukiya da kulawa.

Yayin da mutuwa ta zo masa, ya yi wasiyya ga kowane mutum daga cikin mutanen Badar ɗari cewa a ba su dinari ɗari hudu-hudu, haka kuma ya yi wasiyya ga kowace daga cikin matan Manzon Allah (SAW) da dukiya mai yawa[3].

❖ Rasuwarsa:

Abdurrahman ɗan Auf (RA) ya rasu a shekara ta 32 bayan hijira, yana da shekaru 75 a lokacin, Usman bin Affan (RA) ne ya yi sallace shi, kuma an binne shi a maƙabartar Baƙi’u.

[1]. Bukhari (5072) ne ya rawaito shi.
[2]. Bukhari (4421) da Muslim (274) ne suka rawaito.
[3]. Albidaya wab Nihaya (10/255).

Auna fahimtarka a darusan mako na 5 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Daga cikin falalar Suratul Kafirun akwai cewa:		B
	a. Tana daidai da kashi uku cikin ɗari na Alƙur'ani.	b. Tana daidai da kashi ɗaya bisa hudu na Alƙur'ani.	c. Ta yi daidai da rabin Alƙur'ani.
Darasin Hadisi	Tambaya: Mene ne haƙiƙanin tsoron Allah?		A
	a. Shi ne ka sanya shinge tsakanin ka da azabar Allah, ta hanyar aikata abin da Allah Ya wajabta da barin abin da Ya hana.	b. Barin duniya da jindaɗinta.	c. Ƙarancin magana da yawaita shiru.
Darasin Aƙida	Tambaya: Mene ne sababi mafi girma da Allah yake shigar da bayi Aljanna ta dalilinsa?		A
	a. Tauhidi.	b. Salla.	c. Sadaka.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin sunnonin fiɗira akwai:		C
	a. Sanya turare	b. ƙunshi.	c. Kaciya.
Darasin Sira	Tambaya: Al'amarin Hajarul Aswad ya faru alhalin Annabi (SAW) yana da shekaru:		B
	a. 30.	b. 35.	c. 40.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin falalar Abdurrahman ɗan Auf (RA) akwai:		C
	a. Shirya rundunar Jaishul Usra	b. Tattara AlKur'ani wuri guda.	c. Annabi (SAW)ya yi masa salla bayansa.

MAKO NA SHIDA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUN-NASR

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا جَآءَ نَصۡرُ ٱللَّهِ وَٱلۡفَتۡحُ ١ وَرَأَيۡتَ ٱلنَّاسَ يَدۡخُلُونَ فِي دِينِ ٱللَّهِ أَفۡوَاجٗا ٢ فَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ

رَبِّكَ وَٱسۡتَغۡفِرۡهُۚ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابَۢا ٣﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Idan nasarar Allah ta zo da kuma buɗe (Makka).

2. Ka kuma ga mutane suna shiga addinin Allah ƙungiya-ƙungiya.

3. To ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka, ka kuma nemi gafararsa. Lalle Shi Ya kasance Mai karɓar tuba ne.

❖ Saƙon da surar take ɗauke da shi:

Bushara ga Annabi (SAW) da samun nasara da kuma cikar manzanta.

❖ Baƙin kalmomi:

الفتح	**Alfath**	Buɗe Makka, kuma ya kasance a shakara ta takwas bayan hijira.
أفواجا	**Afwaja**	Jama'a masu yawa, jama'a bayan jama'a.
فسبح بحمد ربك	**Fasabbih**	Tasbihi shi ne: Tsarkake Allah daga dukkan abin da bai dace da shi ba. Kuma ya yi umarni da a haɗa tasbihi da

		hamdala, ma’ana yaba masa da cikar kamalarsa.
توابا	**Tawwaba**	Yana karɓar tuba daga wanda ya tuba kuma ya koma gare shi.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

Suratun Naṣr na daga cikin surorin Madina, akwai bushara da umarni ga Manzon Allah (SAW) a cikinta:

- **Busharar ita ce:** Nasarar da Allah zai ba shi (SAW), da buɗe Makka, da shigar mutane cikin addinin Allah jama’a-jama’a.

- **Umurnin kuwa shi ne:** Ya gode wa Ubangijinsa bisa wannan ni’ima, ya yi tasbihi tare da yabonsa, ya kuma nemi gafararsa; domin samun nasara alama ce ta kusantowar ajalinsa (SAW), da kuma ƙarewar aikinsa da aka aiko shi da shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Cika alkawarin da Allah ya yi wa Annabinsa (SAW).

2. Wajabcin gode wa Allah Maɗaukaki yayin tabbatuwar ni’ima, da harshe, ta hanyar yabon sa tsarki ya tabbata a gare shi, da kuma amfani da gaɓɓai ta hanyar yi masa ɗa’a, da barin saɓa masa, da kuma zuciya ta hanyar sanin cewa ni’imar daga gare Shi take, ba saboda cancantar bawa ba.

3. Wajabcin yin tawali’u da danganta falala zuwa ga Allah Maɗaukaki.

4. Kwaɗaitarwa game da yawan ambaton Allah Maɗaukaki, da tasbihi, da yabonsa, da tahlili.

5. Kwaɗaitarwa game da yawan neman gafara da tuba zuwa ga Allah Maɗaukaki.

6. Dalilin faɗin: “Subhanakallahumma wa bi hamdika, Allahummaghfir li” yayin ruku’u da sujuda; domin sunna ta tabbatar da hakan.[1]

[1]. Bakhari (4968), da Muslim (484) ne suka rawaito shi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI FALALAR KIRA ZUWA GA SHIRIYA, DA HATSARIN KIRA ZUWA GA ƁATA

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya yi kira zuwa ga shiriya, to yana da lada kwatankwacin ladan waɗanda suka bi shi, ba tare da an rage komai a ladansu ba; kuma duk wanda ya yi kira zuwa ga ɓata, to yana da zunubi kwatankwacin zunubin waɗanda suka bi shi, ba tare da rage komai daga zunubinsu ba).[1]

❖ Sharhi:

Wannan hadisin yana kwaɗaitar da mutane a kan kiran jama'a zuwa ga shiriya da ayyuka na ƙwarai, da kuma yin gargadi daga kiran su zuwa ga ɓata da bidi'a da fajirci, don haka sakamakon wanda ya kira mutane zuwa ga shiriya kuma ya bayyana musu, shi ne ya samu lada kwatankwacin ladansu, ba tare da an rage komai daga ladansu ba. Kuma sakamakon wanda ya yi kira zuwa ga ɓata da saɓo, shi ne ya ɗauki zunubi kwatankwacin zunubin waɗanda suka bi shi, ba tare da an rage komai daga zunubinsu ba.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Falalar kira zuwa ga Allah Maɗaukaki, da yaɗa alheri.

2. Hatsarin kira zuwa ga ɓata da sharri.

3. Kwaɗaitarwa game da yin gaggawa wajen alheri da fara shi, da gargaɗi game da fara aikata sharri don tsoron kada a yi koyi da shi.

4. Wajabcin takatsantsan da masu kira zuwa ga ɓata, daga cikin abokai na banza da makamantansu.

[1] Muslim (2674) ne ya rawaito.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA
SHAIDAWA BABU ABIN BAUTA BISA CANCANTA SAI ALLAH

❖ Matsayin shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah:

Wannan ita ce kalmar shahada, kuma ita ce tushen tsantsanta ibada, kuma ita ce kalmar taƙawa kuma igiya mai ƙarfi, kuma ita ce ginshiƙi na farko daga cikin ginshiƙan Musulunci, wadda take bambanta tsakanin kafirci da imani, kuma ita ce kalma mafi nauyi a ma'auni, bari dai, ita ce mabuɗin aljanna, kuma saboda ita ne Allah Ya aiko da manzanni, kuma ya saukar da littattafai, kuma saboda ita ne ranar ƙiyama za ta tsaya, mutane kuma su rabu gida biyu: Rabautattu da taɓaɓɓu, saboda haka ne ya zama wajibi kowane mumini ya himmatu da ita, kuma ya girmama ta yadda ya kamata.

❖ Ma'anar shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah:

Kamar yadda ya zama wajibi a furta wannan shaidawar da harshe, haka nan ya zama wajibi a fahimci ma'anarta, furuci kawai ba ya wadatarwa ba tare da sanin ma'anarta da tabbatar da it aba.

Ma'anar kalmar (Ashhadu) ita ce: Na tabbatar kuma na yarda, kuma na gaskata.

Ma'anar (ilaha): Abin bauta wanda zukata ke bauta masa, kuma suke ƙaunarsa kuma suke nufinsa da buƙatu.

Saboda haka, ma'anar kalmar (La ilaha illallah) ita ce: Babu abin bauta da ya cancanci bauta sai Allah, kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Wannan kuwa saboda lallai Allah Shi ne (abin bauta) na gaskiya, kuma lallai abin da suke bauta wa wanda ba Shi ba shi na ƙarya ne))[1].

[1]. [Alhajj: 62].

❖ Rukunan shaidawa (babu abin bauta bisa cancanta sai Allah):

Wannan kalma mai girma tana da rukunai guda biyu: Su ne korewa da tabbatarwa.

Korewa tana cikin faɗin: (La ilaha), da wannan za a kore bautar dukkan ababen bauta na ƙarya.

Tabbtarwa kuma tana cikin faɗin: (illallah) wato ana tabbatar da bauta ga Allah Mai girma da ɗaukaka.

Dalilin waɗannan rukunai biyu shi ne faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma ka tuna lokacin da Ibrahimu ya ce da Babansa da mutanensa: “Lallai ni ba ruwana da abin da kuke bautawa () “Sai dai wanda Ya halicce ni, to lalle Shi ne Zai shirye ni.” () Ya kuma sanya ta (kalmar Tauhidi ta zama) kalma ce mai wanzuwa a cikin zuri’arsa don (mutanen Makka) su komo (kan hanya)).[1]

[1]. [Azzukhruf: 26–28].

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

ASUWAKI

❖ Falalar Asuwaki:

Asuwaki yana daga cikin sunnoni da aka ƙarfafa, kuma bayanin falalarsa ya zo a cikin fiye da hadisai ɗari, dukkansu suna kwaɗaitar da yin sa, kuma ya kasance daga cikin shiriyar Manzon Allah (SAW), yana kiyaye yin sa sosai, har ya kusan umartar al'ummarsa ya wajabta musu yinsa, ba don kada a ƙuntata musu ba, sai dai kuma ya sunnanta musu yin sa a dukkan lokuta, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Asuwaki yana tsarkake baki kuma yana yardar da Ubangiji)[1].

❖ Lokutan da yin asuwaki ya fi zama mustahabbi:

1. Yayin alwala, saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Ba don kada in ƙuntata wa al'ummata ba, da na umurce su da yin asuwaki yayin kowace alwala)[2], hakan yana kasancewa yayin kuskurar baki, domin hakan ya fi tsaftace baki.

2. Yayin yin salla ta farilla ko ta nafila, domin an umarce mu mu kasance cikin yanayi na tsabta da cikakken kamala, domin bayyana girman ibada, Manzon Allah (SAW) ya ce: Ba don kada in ƙuntata wa al'ummata ba, da na umurce su da yin asuwaki yayin kowace alwala)[3].

3. Buƙatar yin asuwaki tana ƙarfafa yayin karatun Alƙur'ani, domin tsarkake baki da sanya masa ƙamshi.

4. Yayin tashi daga barci, saboda barci yana haifar da sauyin yanayin baki, kuma asuwaki yana tsaftace shi, ya tabbata daga

---

[1]. Bukhari (1934) ne ya rawaito shi mu'allaƙ.
[2]. Bukhari (1934) ne ya rawaito shi mu'allaƙ.
[3]. Bukhari (887), da Muslim (252) ne suka rawaito shi.

Annabi (SAW) cewa: “Idan ya tashi daga barci yana goge bakinsa da asuwaki)[1], Ma’anar kalmar “yashusu” ita ce: yana goge bakinsa.

5. Buƙatar yin asuwaki tana ƙarfafa yayin shiga masallaci ko gida, saboda hadisin A’isha (RA), lokacin da aka tambaye ta cewa: “Da wane abu ne Manzon Allah (SAW) yake farawa idan ya shiga gidansa? Ta ce: “Da asuwaki”[2].

6. Buƙatar yin asuwaki tana ƙarfafa idan aka yi dogon shiru, ko hakora suka fara rawaya, ko yanayin baki ya canza saboda abinci ko wani abu makamancin haka.

❖ Siffar yin asuwaki:

Sunna ne asuwaki ya kasance da itacen “Arak” ɗanye, ba mai karyewa ba, kuma ba ya raunana baki, saboda wannan shi ne irin asuwakin da Manzon Allah (SAW) yake amfani da shi.

Kuma idan aka yi amfani da buroshi da man goge haƙori saboda tsarkake baki da haƙora, to yin hakan yana shiga cikin ma’anar sunna, amma amfani da itacen Arak ya fi falala, saboda shi ne sunnan Annabi (SAW), kuma yana ɗauke da sinadarai masu amfani, sannan kuma yana da sauƙin samu da araha.

Idan mutum ba shi da abin da zai yi asuwaki da shi, to zai iya yin amfani da yatsansa wajen asuwaki, kamar yadda ya zo a cikin sifar alwalar Annabi (SAW).[3]

---

[1]. Bukhari (245), da Muslim (255) ne suka rawaito shi.
[2]. Muslim (253) ya rawaito shi.
[3]. Ahmad (1/108) ne ya rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA
IBADAR MANZON ALLAH (SAW) A CIKIN KOGO

Yayin da Allah Maɗaukaki ya nufi aika rahamarsa zuwa ga bayinsa, sai ya sanya wa Annabimmu Muhammadu (SAW), son keɓancewa, kuma ya sanya masa ƙin abin da mutanensa ke aikatawa na ayyuka marasa kyau da zunubai.

Kuma wurin da yafi soyuwa ga Annabi domin yin wannan keɓancewar kuwa shi ne kogon Hira, wanda yake a saman dutsen Nur, a gabashin Makka, a gefen hagu ga mai tafiya zuwa Arafa. Wannan kogo yana nesa da tsakiyar Makka, kuma wuri ne da ke ba da nutsuwa daga hayaniyar mutane, yana kuma sa mutum yin tunani da Nazari, idan ka yi dubi zuwa ga wurin, ba za ka ga kome ba sai duwatsu, kai ka ce suna sujada ne don girmama Allah Maɗaukaki, kuma a samansu akwai sarari mai faɗi, mai haske, babu abin da ke tare ganinta har zuwa ƙarshenta.

Saboda haka, Manzon Allah (SAW), yana yin ibada a wannan kogo, kamar yadda masu ibada a zamaninsa suke yi, yana zama a ciki tsawon wasu darare da kwanaki ƙididdigaggu, wani lokacin ma har wata ɗaya, kuma Khadijah (RA), ta kasance masa mafi alherin mai taimako a wannan lamari; ta kasance tana ziyartar sa lokaci zuwa lokaci, musamman ma idan ya daɗe, tana kai masa abinci da ruwa, tana zama kusa da shi ɗan lokaci, sannan ta bar shi yana ibadarsa da tunaninsa.

Manzon Allah (SAW) ya ci gaba da kasancewa a haka har sai da Allah ya saukar masa da wahayi, Ya aika shi zuwa ga halittu gaba ɗaya, yana mai shiryarwa da yi wa mutane albishir da kuma gargaɗi, kuma yana kiran mutane zuwa ga Allah da izninsa, kuma shi haske ne mai haskakawa.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI ƊALHA ƊAN UBAIDULLAHI (RA)

❖ Sunsansa da haihuwarsa:

Shi ne Ɗalha ɗan Ubaidullahi ɗan Usman ɗan Amr ɗan Kaʿab ɗan Saʿad ɗan Taim ɗan Murra.

An haife shi a Makka shekaru goma sha biyar kafin manzanci.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Ɗalha (RA) yana daga cikin farko-farkon waɗanda suka musulunta, kuma yana daga cikin mutum takwas na farko da suka karɓi Musulunci, kuma yana daga cikin mutum goma da aka yi musu busharar aljanna, kuma yana daga cikin mutum shida da Umar ɗan Khaɗɗab ya zaɓa domin su zaɓi khalifa bayan sa.

Annabi (SAW) ya yi masa busharar shahada tun yana raye, inda ya ce: (Wanda yake son ya ga shahidi yana tafiya a doron ƙasa, to ya kalli Ɗalha ɗan Ubaidullahi)[1].

Ya kasance mai yawan kyauta, mai yawan ciyarwa, bai bar wani mabuƙaci daga cikin mutanen Banu Taim ba face ya kula da shi, ya kula da iyalinsa, ya aurar da zawarawa, ya biya bashin masu bashi daga cikinsu.[2]

Wata rana ya sayar da gonarsa a farashin dirhami dubu saba’in, da aka kawo masa kuɗin, sai ya ce: “Lallai mutum wanda waɗannan za su kwana a gidansa bai san abin da zai same shi daga hukuncin Allah ba, lallai ruɗaɗɗe ne”, sai ya kwana alhali ɗan aikensa yana raba su a cikin unguwannin Madina, har ya wayi gari babu dirhami guda da ya rage a wurinsa[3].

---

[1]. Tirmizi (3739) ya rawaito.
[2]. Aɗɗabaƙatul-Kubra (3/166).
[3]. Tarikhuɗ-Ɗabari (4/405).

Ya kasance (RA) jarumi, ya kare Manzon Allah (SAW) a yaƙin Uhud har sai da hannunsa ya shanye, kuma haka ya kasance har zuwa rasuwarsa[1].

A yaƙin Uhud, ya sunkuya wa Annabi (SAW) sai ya hau bayansa, sai Annabi (SAW) ya ce: (Aljanna ta wajaba ga Ɗalha)[2].

Kuma wani lokaci Annabi (SAW) ya karanta faɗin Allah Maɗaukaki: ((Akwai wasu mazaje daga muminai da suka cika abin da suka yi wa Allah alƙawari da shi; akwai daga cikinsu wanda ya haɗu da ajalinsa, akwai kuma daga cikinsu wanda yake sauraron (ajalin); kuma ba su yi kowace irin saɓawa ba game da alƙawarin))[3], sai ya yi nuni ga Ɗalha, ya ce: (Wannan yana daga cikinsu)[4].

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu (RA) a watan Rajab, shekara ta talatin da shida bayan hijira, a lokacin yana ɗan shekara sittin da huɗu, kuma an binne shi a garin Basra.

[1]. Bukhari (3734), ne ya rawaito shi.
[2]. Tirmizi (3738) ne ya rawaito shi.
[3]. [Al'Ahzab: 23].
[4] Hilyatul Auliya'I (270).

Auna fahimtarka a darusan mako na 6 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: A cikin Suratun-Naṣr akwai wata bushara, ita ce:		B
	a. Buɗe Ƙusɗandiniyya.	b. Buɗe garin Makka.	c. Buɗe Masar.
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin ladan wanda ya kira mutane zuwa ga shiriya kuma ya bayyana shi ga mutane akwai:		C
	a. Shiga Aljanna ba tare da hisabi ba.	b. Tsira daga fitinar Dujal.	c. Zai samu lada kamar na waɗanda suka bi da'awarsa.
Darasin Aƙida	Tambaya: Mene ne ma'anar kalmar "La ilaha illallah"?		B
	a. Babu samamme sai Allah.	b. Babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah.	c. Babu wani abin bauta a duniya da ake bauta wa sai Allah.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Mene ne hukuncin amfani da asuwaki?		C
	a. Wijibi ne da yake kan kowa.	b. Wajibi ne da wasu za su iya ɗauke wa wasu.	c. Sunna ce mai karfi.
Darasin Sira	Tambaya: A ina kogon Hira (Garu Hira) yake?		B
	a. A Dutsen Uhud.	b. A dutsen Nur (Janalun-Nur).	c. A Dutsen Ṣafa.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin labaran jarumtar Ɗalha (RA) akwai cewa:		B
	a. Ya kasance yana yaƙi da takuba biyu.	b. Ya kare Annabi (SAW) a Yaƙin Uhud har sai da hannunsa ya shanye.	c. Ya jagoranci buɗe Ƙusɗandiniyya.

MAKO NA BAKWAI

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL MASAD

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

تَبَّتۡ يَدَآ أَبِي لَهَبٖ وَتَبَّ ۝١ مَآ أَغۡنَىٰ عَنۡهُ مَالُهُۥ وَمَا كَسَبَ ۝٢ سَيَصۡلَىٰ نَارٗا ذَاتَ لَهَبٖ ۝٣

وَٱمۡرَأَتُهُۥ حَمَّالَةَ ٱلۡحَطَبِ ۝٤ فِي جِيدِهَا حَبۡلٞ مِّن مَّسَدِۭ ۝٥﴾

❖ **Fassara:**

Da sunan Allah, Mai rahama Mai jin ƙai.

1. Hannayen Abu Lahabi sun halaka, shi ma kuma ya halaka.

2. Dukiyarsa da abin da ya tsuwurwurta ba su amfana masa komai ba.

3. Ba da daɗewa ba zai shiga wuta mai balbali.

4. Da kuma matarsa mai yawan ɗaukar kayan ƙaya.

4. A wuyanta akwai igiyar kaba mai ingantacciyar tukka (a ranar alƙiyama).

❖ **Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:**

Bayanin asarar Abu Lahab da matarsa.

❖ **Sababin saukar surar:**

Yayin da Annabi (SAW) ya kirayi mutanansa, kuma ya ce: (Ni mai gargaɗi ne gare ku game da wata azaba mai tsanani), sai Baffansa Abu lahabi ya tashi ya ce: Tir da kai! Ashe saboda wannan ka tara mu? Sai Allah Ya saukar da waɗannan ayoyin.[1]

[1]. Bukhari (4973) da Muslim (208) suka rawaito shi.

❖ Baƙin kalmomi:

تَبَّتْ	Tabbat	Sun yi hasara kuma sun halaka
وَتَبَّ	Wa tabba	Asara da halaka sun same shi
حَمَّالَةَ ٱلْحَطَبِ	Hammatal haɗab	Tana ɗaukar ƙayar sa'adan, tana jefa shi a kan hanyar Annabi (SAW) don cutarwa gare shi da ƙiyayya
جِيدِهَا	Jidiha	Wuyanta
مِّن مَّسَدٍ	Min masad	Na Wani soso mai tsanani kaushi wanda ake ɗaga shi ga wuta sannan a jefar

❖ Ma'anar surar a dunƙule:

Suratul-Masad tana daga cikin surori gajeru da aka saukar a Makka, kuma ana kiran ta suratut-Tabbat, ta kaɗaita da yin zance a kan maƙiyi daga cikin maƙiyan Allah, da Manzonsa (SAW), wannan shi ne Abu lahab - Abdul'uzzah ɗan Abdulmutallib - baffan Manzon Allah (SAW), wanda ya yi ƙiyayya da Manzon Allah mafi tsananin ƙiyayya, kuma ya yaƙe shi mafi tsananin yaƙi, kuma ya zaburar da mutane a kansa da sauran musulmi, ƙiyayyar bata tsaya kawai a nan ba, bari-dai, sai da takai har ga matarsa " Ummu Jamil" Arwa ‘yar Harb, wacce ta yi ta ƙoƙarin cutar da Manzon Allah (SAW), ta kowace hanya, saboda haka ne Allah Yayi musu alkawarin azaba mai tsanani, kuma ya keɓe matarsa da azaba ta musamman.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Haramcin cutar da muminai da bayin Allah na Ƙwarai.
2. Lallai yanda al'amari yake shi ne, dukiya ko ɗa ko dangantaka ko matsayi ba su da wani amfani matuƙar suna tare da kafirce wa Allah Maɗaukaki.
3. Gaskiyar annabtakarsa (SAW), domin surar ta yi hukunci a kan Abu Lahab da matarsa da shiga wuta, kuma sun rayu bayan wannan hukuncin har tsawon shekara goma a kan kafircinsu, ba su musulunta ba koda a zahiri ne.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR FAHIMTAR ADDINI

An karɓo daga Mu'awiya (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Duk wanda Allah ya so shi da alheri, sai ya fahimtar da shi addini**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito[1].

❖ Sharhi:

Fahimta a cikin addini, shi ne sanin shari'o'in addinin Allah da hukunce-hukuncensa, kuma shi ne ilimin da babu wani ilimi da ya yi kusa da shi wurin falalarsa da darajarsa da girman matsayinsa, domin shi ne gadon annabta wanda ba su bar wani gado ba sai shi.

Saboda haka wannan hadisin yana nuni cewa lallai neman ilimin addini alama ce bayyananniya na rabautar bawa, da kuma nufin alheri da Allah ya yi masa, tayadda ya hore masa haryar sanin Allah Mai girma da buwaya da sanin addininsa da ya saukar, kuma hanya ce ta samun yardarsa a lahira, kuma hadisin yana nuni a kan cewa lallai duk wanda ya kawar da kai game da ilimin addini kuma bai damu da shi ba, to lallai Allah bai nufe shi da waccan alherin ba, tayadda Ya haramta masa sabbuban da ake samun alkhairan ta dalilinsu, kuma ake samun rabauta da su.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Kwaɗaitarwa a kan fahimtar addini, da bayanin falalarsa da matsayinsa.
2. Falalar fahimtar addini ya ƙunshi neman fahimtar kowace irin mas'ala daga cikin mas'alolinsa, a cikin aƙida, ko fiƙihu, ko hadisi, ko waninsu.
3. Falalar fahimtar addini, ya ƙunshi neman fahimta ta hanyoyin da aka same su cikin falalar Allah a wannan zamanin, na yanar gizo da na'urori da shafuka da dandamaloli amintattu waɗanda suke taimakawa a kan haka.

---

[1]. Bukhari (3116), da Muslim (1037) ne suka rawaito shi.

4. Hatsarin barin fahimtar addini, da kuma cewa hakan alama ce da ke nuna cewa Allah ba ya nufin bawansa da alheri.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

SHARUƊAN SHAIDAWA BABU ABIN BAUTA BISA CANCANTA SAI ALLAH

Shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah tana da sharruɗa guda bakwai, dalilai na shari'a sun yi nuni a kansu, don haka wajibi ne ga musulmi ya yi ƙoƙari wurin tabbatar da su, domin kalmar ta kasance mai amfani a gare shi a wurin Ubangijinsa.

Kuma waɗannan sharuɗan su ne kamar haka:

1. **Ilimi**: Shi ne fahimtar ma'anar kalmar, da sanin abin da ta ƙunsa na korewa da tabbatarwa, tayadda zai yi aiki da ita, kuma ya aiwatar da ita cikin rayuwarsa, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (Ka sani lallai babu abin bauta bisa cancanta sai Allah), [1] kuma Allah Ya ce: (Sai dai wanda ya shaida da gaskiya alhalin yana da sani). [2]

2. **Yaƙini**: Ya kasance yana mai yaƙini a yayin furta kalmar, yana mai ƙudurce ma'anarta a cikin zuciyarsa, yana mai ƙudurce ingancin abin da yake faɗi, kuma kishiyar yaƙini shi ne shakka da kokwanto, saboda haka shaidawar ba ta inganta daga mai shakka ko mai kokwanto, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (Lallai muminai kaɗai su ne waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa sannan ba su yi kokwanto ba), [3] kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ina shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, kuma lallai ni Manzon Allah ne, wani bawa ba zai haɗu da Allah da su ba alhali ba ya shakka a cikinsu sannan Allah Ya kange shi daga shiga aljannah).[4]

3. **Karɓa:** Ya karɓa kuma ya yarda da abin da wannan shahada ta ƙunsa, ba tare da ƙyamar hakan ba ko girmankai, Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗa dangane da mushirikai cewa: (Su ne waɗanda suka

---

[1]. Suratu Muhammad: 19
[2]. Suratul Zukhruf: 86
[3]. Suratul Hujurat: 15.
[4]. Muslim (27) ne ya rawaito shi.

kasance idan aka ce musu babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, sai su riƙa girmankai). [1]

4. **Jayuwa**: Shi ne miƙa-wuya da ƙanƙan da kai, da bin dukkan abin da shahadar take nuni a kai, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: (Kuma ku koma zuwa ga Ubangijinku kuma ku miƙa-wuya a gare shi) [2]

5. **Gaskatawa**: Hakan yana nufin ya faɗe ta yana mai gasgata hakan, ta yadda zuciyarsa za ta dace da harshensa, yana mai imani da ita a bayyane da ɓoye, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wanda zai shaida cewa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah kuma lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, yana mai gasgata hakan cikin zuciyarsa, face Allah Ya haramta wuta a gare shi). [3] Idan ya faɗe ta da harshensa ba tare da gasgata hakan da zuciyarsa ba, to shi munafiki ne, ba za ta amfane shi ba, kuma ba za ta tseratar da shi daga wuta ba, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: (Kuma daga cikin mutane akwai Wanda yake cewa mun yi imani da Allah da ranar ƙarshe, Amma su ba masu imani bane. Suna yaudarar Allah da waɗanda suka yi imani, amma ba kowa suke yaudara ba face kawunansu alhali su ba su sani ba).[4]

6. **Ikhlasi**: Shi ne ya nufaci Allah da faɗin ta Shi kaɗai, kada ya faɗe ta a halin riya ko jiyarwa, ko don kwaɗayin wani abu na duniya, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lallai Allah ya haramta wa wuta cin naman wanda ya ce: "La Ilaha Illallah" yana mai neman yardar Allah da hakan). [5]

7. **Soyayya**: Shi ne ya so wannan kalma kuma ya so ma'anarta, kuma ya gabatar da soyayyarta a kan duk wani abin so, haƙiƙa Allah Ya

---

[1]. Suratus Saffat: 35.
[2]. Suratuz Zumar: 54.
[3]. Bukhari (128) da Muslim (32) ne suka rawaito shi.
[4]. Suratul Baƙara: 8-9.
[5]. Bukhari (425) da Muslim (657) ne suka rawaito shi.

siffanta masu imani cewa su ne mafi tsananin mutane wurin son Allah, Allah Ya ce: (Kuma waɗanda suka yi imani su ne masu tsananin soyayya ga Allah). [1]

[1]. Suratul Baƙara: 25.

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

ALWALA

❖ Falalar alwala:

1. Rabauta da soyayar Allah Maɗaukakin Sarki, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: (Lallai Allah Yana son Masu tuba kuma yana son Masu tsarki).[1]

2. Haske da sheƙi a gaɓɓan alwala ranar Alkiyama, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lallai al'ummata za'a kirasu ranar alkiyama suna masu hasken fuska da ƙwabri daga guraben alwala, saboda haka duk wanda yake da ikon tsawaita hasken fuskarsa to lallai ya aikata hakan).[2]

3. Kankare zunubai da ɗaga darajoji, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Shin ba zan yi muku nuni a kan abin da Allah Yake kankare zunubi kuma yake ɗaukaka daraja dashi ba?), Suka ce: gaya mana ya Manzon Allah (SAW), sai ya ce: (Cika alwala a lokutan ƙi), da yawan taku zuwa masallaci, da jiran salla bayan salla, wannan shi ne ribaɗi (zaman dako). [3]

4. Karramawa a cikin aljanna, ta hanyar sanya wa mutum kayan kwalliya da awarwaro a gaɓɓan alwala, Manzon Allah (SAW) ya ce: (kwallaiyar mumini tana kaiwa inda alwalarsa takai). [4]

❖ Hukuncin alwala:

Alwala tana kasancewa mustahabbi a wasu lokuta, kuma wajibi a wasu lokutan, mustahabbi ne ga musulmi ya kasance tsawon lokacinsa a cikin tsarki, kuma wannan shi ne mafi kamalar yanayi, saboda abin da ke cikin hakan na girmama Allah Maɗaukakin Sarki, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu mai kiyaye alwala sai Mumini).[5]

❋ Sai dai mustahabbancin yana ƙara ƙarfi yayin wasu al'amura kamar haka:

---

[1]. Suratul Baƙara: 222.
[2]. Bukhari (136) da Muslim (246) ne suka rawaito shi.
[3]. Muslim (251) ne ya rawaito shi.
[4]. Muslim (250) ne ya rawaito shi.
[5]. Ahmad (22414) ne ya rawaito shi.

1. Lokacin ambaton Allah (zikiri) da kuma karatun AlƘur'ani, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ina ƙin yin ambaton Allah sai cikin tsarki (alwala). [1]
2. Yayin barci, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan ka zo makwancinka to sai ka yi alwala irin alawalarka ta salla). [2]
3. Mustahabbi ne yin alwala ga mai janaba idan zai ci abinci ko zai sha abin sha ko zai yi barci, ko yana nufin komawa ga biyan bukatar iyalinsa, saboda Hadisin A'isha Allah ya ƙara mata yarda cewa: "Manzon Allah (SAW) ya kasance idan yana da janaba, kuma ya yi nufin cin abinci ko barci, sai ya yi alwala irin alwalarsa ta salla,"[3] kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan ɗayanku ya zakke wa iyalansa, sannan ya so ya koma karo na biyu, to ya yi alwala).[4]
4. Mustahabbi ne yin alwala kafin wanka, saboda aikin Manzon Allah (SAW) na yin hakan. [5]

❋ **Kuma wajibi ne ayi alwala saboda waɗannan abubuwa masu zuwa:**

1. Salla: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Allah ba zai karɓi sallar wanda ya yi kari (hadasi) ba har sai ya yi alwala). [6]

2. Ɗawafi: Domin aikin Manzon Allah (saw): "Domin lallai shi ya yi alwala, sannan ya yi ɗawafi." [7]

3. Shafar AlƘur'ani ba tare da shamaki ba, saboda faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: (Ba mai taɓa shi sai masu tsarki).[8]

da kuma faɗinsa (SAW) cewa: (Ba wanda zai taɓa AlƘur'ani sai mai tsarki). [9]

---

[1]. Ibnu Hibban (806) ne ya rawaito shi.
[2]. Bukhari (247) ne ya rawaito shi.
[3]. Muslim (305) ne ya rawaito shi.
[4]. Muslim (308) ne ya rawaito shi.
[5]. Muslim (316) ne ya rawaito shi.
[6]. Muslim (223) ne ya rawaito shi.
[7]. Bukhari (1614) da Muslim (1235) ne suka rawaito shi.
[8]. Suratul Waƙi'a: 79.
[9]. Malik (1/199) da Daruƙuɗiniy (1/121) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

FARKON SAUKAR WAHAYI

Lokacin da Annabinmu (SAW) ya kusa cika shekara arba’in, alamomin wahayi suka fara bayyana a gare shi. Kuma farkon wannan al’amar shi ne mafarki na gaskiya, bai taɓa ganin wani abu ba face ya faru daidai yadda ya gani, kamar hasken safiya, shi kuwa a wannan yanayi yana cigaba da ibadodinsa a kogon hira, da kuma nisantar ɓatar mutanensa da warginsu, Allah Maɗaukakin sarki kuma yana tanadinsa ga wani al'amari mai girma.

A ranar litinin wacce ta dace da ranar ashirin da ɗaya ga Ramadana, sai wayahi ya masa bazata alhali yana cikin kogon, kuma Jibrilu aminci ya tabbata a gare shi ya zo masa, sai ya damƙe shi kuma ya lulluɓe shi har sai da ya kai maƙura, sannan ya sake shi sai ya ce da shi: Yi karatu, ya ce: (Ban iya karatu ba), sai Jibrilu ya maimaita masa har sau biyu, Manzon Allah kuma yana amsa masa da irin abin da ya amsa masa a karon farko, sai Jibrilu ya ce: (Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, Wanda Ya yi halitta () Ya halicci mutum daga gudan jini () Ka yi karatu alhali Ubangijinka Shi ne mafi karamci () Wanda Ya koyar ta (hanyar) alƙalami () Ya koyar da mutum abin da bai sani ba), [1] sai wannan ya kasance farkon saukar wahayi da Allah ya saukar masa.

Sai Annabinmu (SAW) ya dawo gida cikin tsoro, zuciyarsa tana bugawa, ya shiga gida wurin Khadija Allah Ya ƙara mata yarda, yana cewa: (Ku lulluɓe ni! Ku lulluɓe ni!), sai suka lulluɓe shi har lokacin da tsoron ya tafi.

Sannan ya ba wa Khadija labarin abin da ya faru ya ce mata: (Ina jiye wa kaina tsoro), sai Khadija ta ce masa: "Kada ka damu, wallahi Allah ba zai tozarta ka ba har abada! Domin kai kana sada zumunci, kana gaskiya cikin zance, kana ɗaukar nauyi, kana samar da abin da aka rasa, kana girmama baƙi, kuma kana taimakon masu bukata".

---

[1]. Suratul Alaƙ: 1-5.

Sai Khadija ta tafi da shi zuwa wurin ɗan baffanta Waraƙatu ɗan Naufal, wanda ya kasance mai yawan shekaru, masanin littafan ahlulkitab, sai Khadija ta ce masa: "Ya ɗan baffana, ka saurari abin da ɗan ɗan'uwanka ya ce." Sai Annabi (SAW) ya ba shi labarin abin da ya faru, sai Waraƙatu ya ce: "Wannan shi ne mala'ikan da aka saukar wa Annabi Musa, ina ma ace ina matashi, ina ma ace ina raye a lokacin da mutanenka za su kore ka!" sai Manzon Allah ya ce: (Yanzu su ɗin za su kore ni?!) Waraƙatu ya ce: "Eh! ba wanda zai zo da irin abin da ka zo da shi, face an yi adawa da shi, idan na kasance ina raye a wannan lokaci, to lallai zan taimake ka taimako mai ƙarfi."

Amma ba da daɗewa ba, sai Waraƙatu ya rasu.[1]

[1]. Ƙissar tana cikin Bukhari (4953) da Muslim (160).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ZUBAIRU ƊAN AWWAM (RA)

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne: Zubairu ɗan Awwam ɗan Khuwailid ɗan Asad ɗan Abdul'uzza ɗan Ƙusaiyi ɗan Kilab ɗan Murra ɗan Ka'ab, ya haɗa dangi da Manzon Allah (SAW) ta ɓangaren Ƙusaiyi ɗan Kilab.

An haife shi kafin aiko Annabi (SAW) da shekara goma sha bakwai, ya girma a Makka cikin maraici saboda an kashe babansa Awwam a yaƙin alfijar.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Zubairu ya kasance mutum ne fari, dogo marar cikar gemu da saje.

Kuma ya kasance daga cikin farkon waɗanda suka karɓi Musulunci, kuma yana daga cikin farkon waɗanda suka yi hijira zuwa habasha, kuma yana daga cikin waɗanda aka yi musu bushara da aljanna.

Ya musulunta tun yana ƙarami, kuma kawunsa ya kasance yana ɗaure shi a jikin tabarma, sai ya cinna mata wuta yana cewa "ka dawo addinin ka", Zubairu kuma yana cewa: "Ba zan kafurta ba har abada".[1]

Ya yi hijira zuwa Habasha hijira ta farko, amma bai daɗe a cikinta ba, sannan ya yi hijira zuwa Madina, sai aka haifa masa Abdullahi ɗan Zubair, sai ya kasance shi ne farkon wanda aka haifa wa musulmai a Madina.

Manzon Allah (SAW) ya yabe shi, sai ya ce: (kowane Annabi yanada 'yan gani-kashe-ni, kuma ɗan gani-kashenina shi ne

[1]. Ɗabaraniy (239) ne ya rawaito shi.

Zubairu),[1] saboda haka Zubairu shi ne ɗan gani-kasheni na Manzon Allah, kuma shi ne ɗan innar Annabi Safiyya, kuma mijin Asma'u ƴar sayyidina Abubakar wadda ake wa laƙabi da "ma'abociya kyallaye biyu", kuma shi ne farkon wanda ya zare takobinsa a Musulunci.

Ya halarci dukknin yaƙoƙi, kuma shi ne kwamandan ɓangaren dama na runduna a yaƙin badar, kuma yana daga cikin mutane uku da suke riƙe da tutar muhajirai a fatahu Makka, kuma yana daga cikin waɗanda Umar ɗan Khaɗɗab ya aika su zuwa ga Amru ɗan Aas saboda neman ƙarin kayan yaƙi lokacin da aka buɗe ƙasar Masar, kuma ɗaya daga cikin mutum shida da Umar ya naɗa su a kwamitin zaɓan khalifa a bayansa.

An san shi (RA) da yawan ibada da tsantseni, kuma daga cikin wa'azozinsa akwai: "Duk wanda zai iya kasancewa yana da aiki mai kyau ɓoyayye, to ya aikata".[2]

❖ Rasuwarsa.

Ya rasu a watan Rajab shekara ta 36 na hijira a garin Basra, a lokacin yana da shekara 64, sai aka birne shi a can.

[1]. Bukhari (3719) da Muslim (2415) ne ya rawaito shi.
[2]. Littafin Azzuhud (119) na Imamu Ahmad.

Auna fahimtarka a darusan mako na 7 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar "masad"		B
	a. Alhariri mai taushi.	b. Soso mai kaushi.	c. Sarkar ƙarfe.
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin alamomin Allah yana nufin bawa da alheri shi ne ya azurta shi da:		C
	a. Dukiya mai yawa.	b. Matsayi mai girma.	c. Fahimta cikin addini
Darasin Aƙida	Tambaya: Mene ne ma'anar ikhlasi cikin Kalmar shahada?		B
	a. Ta kasance ita ce maganarsa ta ƙarshe a duniya.	b. Ya kasance ya nemi yardar Allah shi kaɗai da furta ta.	c. Ya riƙa faɗin ta bayan kowace salla.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin falalolin alwala akwai:		A
	a. Kankare zunubai.	b. Yawan arziki.	c. Gyaruwar zuri'a.
Darasin Sira	Tambaya: An aiko Annabinmu Muhammadu ɗan Abdullahi a matsayin Annabi kuma Manzo yana da:		B
	a. Shekara 30.	b. Shekara 40.	c. Shekara 50.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Zubairu bin Awwan (RA) ya shahara da cewa shi ne:		B
	a. Mai huɗubar Manzon Allah (SAW).	b. Amintaccen wannan al'ummar.	c. Ɗan gani kashenin Annabi (SAW).

MAKO NA TAKWAS

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATU ƘURAISH

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

لِإِيلَٰفِ قُرَيۡشٍ ١ إِۦلَٰفِهِمۡ رِحۡلَةَ ٱلشِّتَآءِ وَٱلصَّيۡفِ ٢ فَلۡيَعۡبُدُواْ رَبَّ هَٰذَا ٱلۡبَيۡتِ ٣ ٱلَّذِيٓ

أَطۡعَمَهُم مِّن جُوعٖ وَءَامَنَهُم مِّنۡ خَوۡفِۭ ٤﴾

❖ Fassara:

1. Domin sabon da Ƙuraishawa suka yi.

2. Sabonsu na yin safara a lokacin ɗari (zuwa ƙasar Yaman) da lokacin bazara (zuwan ƙasar Sham).

3. To sai su bauta wa Ubangijin wannan Ɗakin.

4. Wanda Ya ciyar da su daga yunwa, Ya kuma amintar da su daga tsoro).

❖ Saƙon da surar take ƙunshe da shi:

Bayanin ni`imar Allah ga ƙuraishawa, da haƙƙin Allah a kansu.

❖ Baƙin kalmomi:

لِإِيلَٰفِ	Li'ifi	Sabo: Daga sabo da abu sabawa, ya saba da shi kuma wahala ta gushe daga gare shi.
رِحۡلَةَ ٱلشِّتَآءِ	Rihlatush shita'i	Zuwa ƙasar Yaman.
وَٱلصَّيۡفِ	Wassaif	Zuwa ƙasar Sham.

❖ Ma`anar ayoyin a dunƙule:

Suratu ƙuraish tana daga cikin surorin da suka sauka a Makka, kuma ana kiran ta da Suratu “Ilafi”, ta zo tana mai nuna baiwar Allah ga

ƙuraishawa da tunatar da su a kan ni`mar Allah gare su, da abin da ya lizimce su game da wannan ni`mar; haƙiƙa an ba su cikakken aminci saboda makwabtakarsu da Masallaci mai alfarma, da yalwar arziki ta hanyar sauƙaƙe musu hanyar kasuwanci zuwa Sham lokacin bazara da Yaman a lokacin hunturu, har suka zamto mafiya wadatar larabawa, tare da cewa suna wani kwari ne wanda ba ya karɓar shuka, kuma zukatansu suka saba da wadɗancan tafiye -tafiye masu aminci masu riba, sai suka zamo musu al'ada da sabo, da ba don wadɗannan ni'imomi guda biyu ba, da ba za su kasance sun samu wurin zama a wannan ƙasa tasu ba, ko kuma su samu wani matsayi a wurin sauran ƙabilu.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Wajibcin tuntuntuni koda yaushe game da ni'imomin Allah Maɗaukaki, da danganta su zuwa gare shi, da taka-tsantsan daga kafircewa da musuntawa.
2. Lallai caccanzuwar yanayi na shekara yana daga cikin ni'imar Allah ga bayinsa, saboda abin da ke cikin shi na abubuwan amfani mabanbanta ga mutane da dabbobi, da shuka.
3. Matsayin ɗakin Allah mai alfarma da girmansa, da alfarmarsa a wurin Allah da wurin mutane.
4. Mahimmancin aminci da kasancewarsa daga cikin mafi girman ni'imomi waɗanda suka zama wajibi a gode wa Allah Maɗaukaki a kansu.
5. Lallai duk wanda ni'imomi biyu suka haɗu a gare shi, ni'imar arziki da aminci, to ƙarin dagewa wurin fuskantar Allah Maɗaukaki, da bauta masa zai ƙarfafa cikin haƙƙinsa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WASIYYOYIN ANNABTA MASU AMFANI

An karɓo daga Abu Huraira (RA), ya ce: “Masoyina (SAW) ya yi min wasiyya da abubuwa guda uku: Azumin kwanaki uku cikin kowani wata, da raka'a biyu lokacin hantsi, da kuma kada na yi barci ba tare da na yi wutiri ba". Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.[1]

❖ Sharhi:

A cikin wannan hadisi akwai wasuyyoyi na annabta guda uku, a kan wasu abubuwa uku mafiya girman nafilan salla da azumi.

Farkon wannan wasiyoyi: Shi ne azumi uku a kowane wata, lallai suna daidai da azumin wata cikakke; domin lallai kyakkyawan aiki ɗaya yana da lada kwatankwacinsa sau goma, sai a samu ladan shekara cikakka sakamakon dogewa a kan su, kuma abin da ya fi falala shi ne ya yi su a ranakun sha uku da sha hudu da sha biyar, kuma yana halasta ayi su a wasu kwanakin.

Wasiyya ta biyu: Sallar walaha, kuma ƙarancinta shi ne raka'a biyu, kuma lokacinta shi ne: daga ɗagawar rana gwargwadon tsinin mashi zuwa kusa da gushewarta, kuma mafi falalar lokacinta shi ne ƙarshenta, lokacin da zafin rana yake ƙuna ga kofaton 'ya'yan raƙuma, kuma aikata ta yana isarwa daga yin wasu ayyuka masu yawa na daga sadaka da zikiri da sauransu, kuma a cikin yin ta akwai nuna godiya ga Allah da kuɓutar gaɓɓai da ɓangarori.

Wasiyya ta uku: Sallar wutiri, kuma shi sunna ce mai ƙarfi, Manzon Allah (SAW) ya kwaɗaitar a kan yin ta kuma ya dawwama yana yin ta a lokacin zaman gida da lokacin tafiya, kuma ƙarancinsa raka'a ɗaya ne, idan mutum ya so zai iya ƙarawa zuwa raka'a uku, ko biyar, ko bakwai, ko tara, ko raka'a goma sha ɗaya, lokacinta shi ne: daga bayan sallar Isha'i zuwa fitowar alfijiri, idan wutiri ya

[1]. Bukhari (1981) da Muslim (721) ne suka rawaito shi.

ƙubuce masa saboda barci ko mantuwa, ana so ya rama shi da rana raka'a biyu.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Ya kamata ga Musulmi ya riƙa sabar wa iyalansa da abokansa da wasiyyoyi masu amfani.
2. Lallai Maganar Annabi (SAW) ga mutum ɗaya cikin al'ummarsa, magana ce da ta shafi dukkan al'umma.
3. Lallai daga cikin ayyukan samun kusanci ga Allah, akwai abin da lada mai girma yake hawa kansa ta hanyar aiki kaɗan.
4. Lallai mustahabbi ne yin witiri kafin barci ga mutumin da ya san cewa ba zai iya tashi ƙarshen dare ba, amma wanda zato ya rinjaya zai iya tashi ƙarshen dare, to ya jinkirta shi zuwa lokacin.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

SHAIDAWA LALLAI ANNABI MUHAMMAD MANZON ALLAH NE

❖ Matsayin shaidawa lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah ne:

"Shaidawa lallai Annabi Muhammad Manzo Allah ne" shi ne rukunin shahada na biyu, ɗayar rukunin shahadar ba ta wadatarwa daga ɗayar, bari-dai, dole su zama an haɗa su tare, wato "ina shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma ina shaidawa Annabi Muhammad Manzon Allah ne", kuma yana daga cikin abin da ya zama dole a san shi, shi ne: Lallai imani da annabtar Annabi Muhammad (SAW) wajibi ne, Musulunci ba ya inganta sai da shi, saboda haka ne ma lokacin da Annabi (SAW) ya aika Mu'azu ɗan Jabal zuwa Yaman domin ya kira su zuwa ga Musulunci, sai ya yi masa wasiyya da faɗinsa cewa: (lallai kai za ka je wurin wasu mutane daga cikin ma'abota littafi, ya kasance farkon abin da za ka kira su zuwa gares hi shi ne: Babu abin bauta bisa cancanta sai Allah kuma Annabi Muhammad Manzon Allah ne). [1]

❖ Ma'anar shaidawa lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah ne:

Kuma ma'anar shaidawa lallai Annabi Muhammad Manzon Allah ne shi ne: Gaskatawa da tabbatarwa na yankar shakku cewa lallai Muhammadu ɗan Abdullahi Manzon Allah ne na gaskiya, Allah Ya keɓance shi da wahayi da Manzanci, kuma ya aika shi zuwa ga mutane da aljanu, saboda kiran su zuwa ga gaskiya da addini, kuma shi ne cika-makin Annabawa babu wani Annabi bayansa, tsira da aminci su tabbata a gare shi, Allah Maɗaukaki ya ce: (Ka ce: Ya ku mutane! Lallai ni Manzon Allah ne zuwa gare ku baki-ɗaya),[2] kuma Allah Maɗaukaki ya ce: (Ya kai wannan Annabi, lallai Mu Mun aiko ka kana mai shaida, kuma mai albishir kuma mai gargaɗi () Kuma

[1]. Bukhari (1425) da Muslim (19) ne suka rawaito shi.
[2]. Suratul A'araf: 158.

mai kira zuwa ga Allah da izininsa, kuma fitila mai haskakawa), [1] kuma Allah Maɗaukaki ya ce: (Annabi) Muhammadu bai kasance uban ɗaya daga cikin mazajenku ba, sai dai (shi) ya kasance Manzon Allah ne kuma cikamakin annabawa).[2]

❖ Abin da shaidawa lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah ne take hukuntawa:

Shaidawa lallai Annabi Muhammadu Manzon Allah tana hukunta abubuwa guda huɗu waɗanda shaidar ba ta inganta sai da su, su ne kamar haka:

1. Yin biyayya gare shi cikin abin da ya ba da umarni.

2. Gaskata shi cikin abin da ya ba da labari.

3. Nisantar abin da ya yi hani a gare shi kuma ya tsoratar.

4. Kuma kada a bauta wa Allah sai da abin da ya shar'anta.

[1]. Suratul Ahzab: 45-46.
[2]. Suratul Ahzab: 30.

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

FARILLAN ALWALA

Farillan alwala: su ne rukunan da suka gina su, kuma alwala ba ta inganta sai da su, kuma su shida ne, Allah Ya ambace su a cikin ayar alwala, yana cewa: (Ya ku waɗanda suka yi imani, idan kun tashi za ku yi salla, to ku wanke fuskokinku da hannayenku zuwa gwiwoyinsu, kuma ku shafi kawunanku, kuma (ku wanke) ƙafafunku zuwa idon sawu). [1]

❋ **Kuma ga cikakken bayani a kansu kamar haka:**

1. Wanke fuska gaba-ɗaya: Daga cikin haka akwai kuskuren baki da shaƙar ruwa a hanci; domin baki da hanci a cikin fuska suke, kuma Annabi (SAW) ya yi kuskuran baki ya shaƙi ruwa a cikin alwalarsa,[2] kuma iyakar tsawon fuska shi ne, daga saman goshi zuwa ƙasar haɓa, kuma faɗinta shi ne daga kunne zuwa kunne.

Kuma gashin gemu yana cikin fuska, saboda haka wajibi a wanke shi koda ya yi tsawo, hanyar wanke shi kuwa itace: idan ya kasance mara cika ne sai a wanke abin da ya bayyana da kuma tsatstsefe cikinsa, hakan wajibi ne, idan kuma ya kasance mai cika ne, tayadda ya zamto ya rufe fatar fuskar, to sai a wanke zahirinsa, sai tsatstsefe ƙarƙashin gashin ya zamto mustahabbi.

2. Wanke hannaye biyu: Daga saman yatsu zuwa gwiwar hannu; domin Manzon Allah (SAW) ya kwarara ruwa bisa gwiwowin hannunsa.[3]

3. Shafar dukkanin Kai tare da kunnuwa sau ɗaya, Kuma shafar wani ɓangare na kai kuma a bar wani ɓangare, ko shafar kai ba tare da kunnuwa ba, ba ya wadatarwa, saboda faɗar Annabi (SAW)

---

[1]. Suratul Ma'ida: 6.
[2]. Muslim (235) ne ya rawaito shi.
[3]. Daruƙuɗuniy (1/83) ne ya rawaito shi.

cewa: (Lallai kunnuwa biyu suna daga cikin Kai),[1] duk yadda ya shafi kansa, to ya wadatar.

Sai dai siffar da tafi, ita ce: Mutum ya sanya hannayensa biyu jiƙaƙku a farkon kansa sai ya kewaya da su zuwa ƙeyarsa, sannan ya dawo da su zuwa wajen da ya fara da shi, sannan ya shigar da yatsunsa manuniya cikin fatun kunnuwansa, sai ya shafi bayan kunnuwansa da babban yatsarsa.

Kuma mace kamar namiji take a cikin hakan, kuma ba za ta yi shafa a kan kitso ko abin da ya sauka na gashin kanta ba (amma ba dukkan malamai ba ne suke da wannan ra'ayi).

4. Wanke ƙafafuwa biyu zuwa idon sawu; saboda Annabi (SAW) ya wanke ƙafarsa har sai da ya kusa ƙwabrinsa.[2]

5. Jerantawa: ta yadda zai wanke fuskarsa da farko, sannan hannayensa, sannan ya shafi kansa, sannan ya wanke ƙafafuwansa; domin Allah Madaukaki ya ambace su a jere, kuma Annabi (SAW) ya yi alwala a jere.[3]

6. Bibiyarsu da juna: Ta yadda ba zai jinkirta wani sashi na alwala a kan sashin da ya zo gabaninsa ba, sai dai ya wanke shi da ya gama da shi ba tare da jinkiri ba; domin haƙiƙa Annabi (SAW) ya kasance yana alwala ne a jere.[4]

❁ **Hikimar da ta sa aka keɓance waɗannan sassa na jiki da yin alwala:**

1. Su ne ɓangaren da ya bayyana a jikin mutum, kuma su ne abubuwan mannewa da jiki da kuma datti suka fi kama su.

2. Kuma su ne gaɓɓai da aka fi amfani dasu wajen aikata zunubai, haƙiƙa Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya yi alwala kuma

[1]. Tirmiziy (37) ne ya rawaito shi.
[2]. Muslim (246) ne ya rawaito shi.
[3]. Muslim (235) ne ya rawaito shi.
[4]. Muslim (235) ne ya rawaito shi.

ya kyautata alwalar, dukkan kura-kurensa za su fita daga jikinsa har sai sun fita daga ƙarƙashin faratunsa).[1]

[1]. Muslim (245) ne ya rawaito shi.

ALHAMIS: DARASIN SIRA

DA'AWA A SIRRANCE

Bayan abin da ya faru da Annabinmu (SAW) a kogon Hira, da bazatan da mala'ika Jibirilu (AS) ya yi masa, sai wahayi ya yanke masa, kuma ya zauna tsawon lokacin da Allah Ya so ba tare da zuwan wahayi ba, sannan wahayi ya sake dawo masa, sai dai wahayin ya zo ne da ɗaura masa nauyin isar da saƙo, da kuma gargaɗi, sai faɗin Allah Maɗaukaki sarki ya sauka cewa: (Ya kai mai lulluɓa () Tashi ka yi gargaɗi () Kuma ka girmama Ubangijinka () Ka kuma tsarkake tufafinka () Ka kuma ƙaurace wa (bautar) gumaka), [1] sai Allah Ya umarce shi a cikin waɗannan ayoyi da yin gargaɗi ga mutanensa daga barin shirka, Kuma ya kira su zuwa ga kaɗaita Allah.

Sai Annabi (SAW) ya ɗaura ɗamara game da kira zuwa ga Allah, kuma ya tsayu a kan addinin Allah mafi cikar tsayuwa, sai ya fara da'awarsa a ɓoye, sai waɗanda Allah Ya haskaka zukatansu ga Musulunci suka amsa, a cikin iyalan gidansa Khadija (RA) ita ce farkon wadda ta amsa masa, haka kuma ɗan riƙonsa Aliyu ɗan Abu Ɗalib (RA) ya amsa masa, yana ɗan shekara goma, kuma a lokacin ya kasance ƙarƙashin kulawar Manzon Allah (SAW), ya dawo da shi wurinsa don taimaka wa baffansa a shekarar fari, Kuma bawansa Zaidu ɗan Harisa (RA) ya musulunta.

Kuma a wajen gidan Annabi (SAW) wanda ya riga kowa shiga musulunci shi ne Abubakar (RA), Kuma daga lokacin da ya musulunta sai ya zamto yana taimakon Manzon Allah (SAW) cikin addinin Allah, kuma ya ƙarfafe shi wurin da'awa, sai Usman ɗan Affan da Ɗalhatu ɗan Ubaidillahi da Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas, da Abdurrahman ɗan Aufi, da Zubairu ɗan Auwam, da Abu Ubaidata Amiru ɗan Jarrahi suka amsa kiran Abubakar, kamar yadda kuma a wannan lokacin ne Ammar ɗan Yasir da Bilal ɗan Rabah da Jafar

[1]. Suratul Muddassir: 1-5.

ɗan Abu ɗalib, da Arƙam ɗan Abu Arƙam, wanda musulmai suka riƙi gidansa a matsayin cibiyar tarukansu.

Kuma haka kira zuwa ga Allah ya cigaba a ɓoye kuma adadin musulmi yana ta ƙaruwa yau da gobe, har zuwa lokacin da Allah Ya umarci Manzonsa (SAW) bayan shekaru uku da ya yi kira zuwa ga addini a fili kuma ya bayyana da'awa.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SA'AD ƊAN ABU WAƘƘAS (RA)

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne: Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas baƙuraishe ɗan ƙabilar Zuhura, kuma babansa "Abu Waƙƙas" shi ne Maliku ɗan Wuhaib ɗan Abdu Manaf ɗan Zuhrata ɗan Kilab.

An haifi Sa’ad a garin Makka kafin aiko Manzon Allah da shekara goma sha huɗu.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Ya musulunta yana ɗan ƙarami, Kuma aka ce shi ne na ukun waɗanda suka musulunta, wasu kuma suka ce shi ne na bakwai, kuma yana daga cikin mutane goma da aka yi musu bushara da aljanna, kuma yana cikin waɗanda suka sammako wurin shiga Musulunci.

Ya halarci dukkanin yaƙoƙi tare da Annabi (SAW), kuma shi ne farkon wanda ya yi harbi da kibiya don ɗaukaka kalmar Allah, Kuma hakan ya faru ne lokacin da ya shiga cikin mayaƙan farko a Musulunci, wanda Manzon Allah (SAW) ya aika domin su tare wani ayari na ƙuraishawa a shekarar ta farko ta hijra.

Annabi (SAW) ya yabe shi da faɗinsa cewa: (Wannan kawuna ne wani ma ya nuna mini kawunsa),[1] saboda Sa’ad ɗan ƙabilar Banu Zuhra ne, kuma mahaifiyar Annabi (SAW) ita ma 'yar ƙabilar Banu Zuhrata ce.

Kuma a ranar yaƙin uhudu Annabi (SAW) ya yi fansa a gare shi da iyayensa, sai ya ce da shi: (Ka yi harbi fansar mahaifina da mahaifiyata gare ka), [2] kuma Annabi (SAW) ya keɓance shi da addu'arsa, ya ce: (Ya Allah ka isar da harbinsa, kuma ka amsa masa

[1]. Tirmiziy (3752) ne ya rawaito shi.
[2]. Bukhari (2905) da Muslim (2411) ne suka rawaito shi.

addu'arsa), [1] sai ya kasance mafi ƙwarewar mutane wurin harbi, kuma mafi kaifin idanu cikinsu.

Umar ɗan Khaɗɗab ya sanya shi a matsayin jagoran rundunar da ya aika domin yaƙar farisa, sai ya rusa su a yaƙin ƙadisiyya, kuma ya buɗe garuruwar kisra a ƙasar Iraƙi.

Kuma Umar ya sanya shi gwamna a Kufa, bayan Sa'ad ya ƙirƙire ta a shekara ta 17 na hijira bisa umarnin Umar, kamar yadda ya kasance cikin mutane shida na kwamitin shura wanda Umar ya zaɓa domin su zaɓi halifa a bayansa.

An san shi da gudun duniya da tsantseni (RA), da kuma guje wa fitintinu, kuma daga cikin wasiyyoyinsa ga ɗansa akwai: "Ya kai ɗana, idan za ka yi salla, to ka kyautata alwala, kuma ka yi sallar da a ganinka ba za ka sake wata salla bayanta ba har abada, ina maka kashedi da kwaɗayi; domin shi talauci ne a halarce, kuma ina kwaɗaitar da kai cire rai daga abu, domin shi wadata ne, kuma kashedinka da dukkan abin da za'a nemi uzuri a kansa na magana ko aiki, ka aikata abin da ya bayyana gare ka. [2]

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu a shekara ta 55 bayan hijira a Aƙiƙ, kuma an binne shi a Madina, kuma shi ne na ƙarshen rasuwa a cikin muhajirai.

[1]. Hakim (3/500) ne ya rawaito shi.
[2]. Littafin Azzuhud (149) na Imamu Ahmad.

Auna fahimtarka a darusan mako na 8			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Zuwa ina tafiyar Ƙuraishawa take kasancewa a lokacin hunturu?		A
	a. Zuwa ƙasar Yaman.	b. Zuwa ƙasar Sham.	c. Zuwa ƙasar Habasha.
Darasin Hadisi	Tambaya: Yaushe ne lokacin sallar walaha yake farawa?		C
	a. Daga bayan sallar asuba.	b. Daga lokacin fitowar rana.	c. Daga lokacin da rana ta ɗaga daidai tsayin mashi.
Darasin Aƙida	Tambaya: Mene ne ma'anar shaidawa lallai Annabi Muhammad Manzon Allah ne?		B
	a. Sanin rayuwarsa daki-daki da abubuwa da suka faru a tarihinsa.	b. Yarda da cewa shi Manzon Allah ne da gaske, Allah ya keɓance shi da wahayi da manzanci.	c. Girmama sahabbansa da mutunta matansa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Farillan alwala guda nawa ne?		C
	a. Su huɗu ne.	b. Su biyar ne.	c. Su shida ne.
Darasin Sira	Tambaya: Shekara nawa kira a ɓoye ya ɗauka?		A
	a. Shekara uku	b. Shekara huɗu.	c. Shekara biyar.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas ya yi fice da cewa shi ne:		A
	a. Farkon wanda ya yi harbi da kibiya don ɗaukaka kalmar Allah.	b. Farkon wanda ya yi mutuwar shahada a Musulunci.	c. Farkon wanda ya fara musulunta daga cikin mutanen Madina.

MAKO NA TARA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-MA'UN

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
أَرَءَيۡتَ ٱلَّذِي يُكَذِّبُ بِٱلدِّينِ ١ فَذَٰلِكَ ٱلَّذِي يَدُعُّ ٱلۡيَتِيمَ ٢ وَلَا يَحُضُّ عَلَىٰ طَعَامِ
ٱلۡمِسۡكِينِ ٣ فَوَيۡلٞ لِّلۡمُصَلِّينَ ٤ ٱلَّذِينَ هُمۡ عَن صَلَاتِهِمۡ سَاهُونَ ٥ ٱلَّذِينَ هُمۡ يُرَآءُونَ ٦
وَيَمۡنَعُونَ ٱلۡمَاعُونَ ٧﴾

❖ Fassara:

1. Shin ka ga wanda yake ƙaryata ranar sakamako?

2. To shi ne wanda yake ingije maraya (daga haƙƙinsa).

3. Ba kuma ya kwaɗaitarwa wajen ciyar da miskini.

4. To tsananin azaba ya tabbata ga masallata.

5. Waɗanda suke masu rafkana su bar sallarsu.

6. Waɗanda su ne suke yin riya.

7. Suke kuma hana kayan taimako.

❖ Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:

Bayanin siffofin masu ƙaryata ranar sakamako, domin bayyana lamarinsu, da zargin ayyukansu, da tsoratarwa daga cututtukansu.

❖ Sababin saukar surar:

Farkonta ya sauka ne a kan Aas ɗan Wa'il Assahmi: ((Shin ka ga wanda yake ƙaryata ranar sakamako? () To shi ne wanda yake ingije maraya (daga haƙƙinsa) () Ba kuma ya kwaɗaitarwa wajen ciyar da miskini)), ragowarta kuma ya sauka a kan Abdullahi ɗan Ubayyi ɗan

Salul munafikin nan, tun daga fadin Allah ((To tsananin azaba ya tabbata ga masallata) har zuwa karshanta.[1]

❖ Bakin kalmomi:

يُكَذِّبُ بِٱلدِّينِ	Yukazzibu biddin	Yana karyata sakamako na ranar alkiyama.
يَدُعُّ ٱلۡيَتِيمَ	Yadu'ul yatim	Yana ingije maraya da rashin tausayi daga hakkinsa.
وَلَا يَحُضُّ	Wala yahuddu	Ba ya kwadaitar da waninsa.
فَوَيۡلٞ	Fawailun	Azaba mai radadi.
سَاهُونَ	Sahun	Ba sa damuwa da ita, suna jinkirtar da ita daga lokacinta, kuma ba sa yin ta daidai.
يُرَآءُونَ	Yura'un	Suna bayyana ayyukansu don mutane su gani.
وَيَمۡنَعُونَ ٱلۡمَاعُونَ	Wa yamna unal-ma'un	Suna kin ba da aron abin da bayar da aronsa ba ya cutarwa, na tukwane da makamantansu.

❖ Ma'anar surar a dunkule:

Suratul-Ma’uun ta zo ne domin ta aibanta dabi’un wadanda suka karyata ranar sakamako da ranar lahira, farkon siffarsa, shi ne lallai shi yana tunkude maraya kuma yana zaluntarsa, don haka ba ya tausaya masa kuma ba ya ba shi hakkinsa, Kuma daga cikin siffofinsa lallai shi ba ya kwadaitar da kansa kuma ba ya kwadaitar da waninsa a kan ciyarda matalauci.

[1]. Littafin Annasik wal Mansuk (205) na Ibn Salama.

Sannan Ubangijinmu ya yi alƙawarin boni ga masallata, waɗanda suke shagala game da salla, sai su riƙa jinkirta ta daga lokacinta, ko kuma su bar ta a wani lokacin ba tare da sun sallace ta ba, kuma waɗannan su ne munafukai, waɗanda suke tsayuwa da ayyukansu domin mutane su gan su, su ne waɗanda suke yanke aiki kyakkyawa ga mutane, ba sa taimakon su da komai na daga abubuwan da ake anfanuwa da su; kamar tukunya da gatari da guga da waninsu!

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Lallai gaskata ranar sakamako yana lizimta bayar da haƙƙoƙin Allah da haƙƙoƙin bayinsa.

2) Falalar karrama maraya, da ciyar da matalauta, da bibiyan buƙatunsu.

3) Wajibcin kiyaye salla, da tsoratarwa daga jinkirta ta daga lokacinta.

4) Wajibcin yin aiki domin Allah, da tsoratarwa a kan yin aiki don a gani ko a ji.

5) Kwaɗaitarwa a kan yaɗa alheri na daga taimkon wani da kuɗi, da kuma ba da aron abin da ya yi saura daga kayan aiki.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

TSORATARWA GAME DA CUTAR DA MUSULMI

An karɓo daga Abu Sirmata (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Duk wanda ya cutar da wani musulmi, to Allah zai cutar da shi, kuma duk wanda ya tsananta wa musulmi, to Allah zai tsananta masa**). [1]

❖ Sharhi:

Wannan hadisin yana nuni a kan ma'anoni guda biyu masu mahimmanci:

Ta farkonsu ita ce: Haramcin cutar da musulmi da shigar da shi cikin tsanani da wahala, a jikinsa ne ko iyalansa, ko dukiyarsa ko ɗansa, kuma lallai duk wanda ya aikata hakan tabbas Allah Maɗaukaki shi ne zai jiɓinci yi masa sakamako da uƙuba.

Daga cikin misalan cutar da musulmi akwai: Yin makirci da yaudara da algus da babakere cikin mu’amala, da ɓoye aibu cikin mu'amala, da cutarwar da abokin hulɗa ga abokin hulɗarsa, maƙobci ga maƙobcinsa, ko miji ga matarsa; kamar ƙuntata mata saboda zalunci don ta fanshi kanta daga gare shi, ko ya mayar da ita kamar ratayayya, ko yi mata kome da nufin cutar da ita, ko ya karkata ga ɗaya daga cikin matansa da makamantan haka.

Ta biyu ita ce: Lallai sakamako yana kasancewa ne daga jinsin aiki na alheri ko sharri; saboda haka, duk wanda ya aikata abin da Allah Yake so, to Allah zai so shi, kuma duk wanda ya aikata abin da Allah ba Ya so, to Allah zai ƙi shi, kuma duk wanda ya sauƙaƙa wa wani musulmi, to Allah zai sauƙaƙa masa a duniya da lahira, kuma duk wanda ya cutar da musulmi, to Allah zai cutar da shi, haka kuma duk wanda ya ƙuntata masa, to shi ma Allah zai ƙuntata masa, da makamantan haka.

---

[1]. Tirmiziy (1940) da Ibnu Maja (2342) ne suka rawaito shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Saboda cikar adalcin Allah da rahamarsa sai cutarwa da ƙuntatawa tsakanin musulmi, kuma ya yi umarni da jinƙai da 'yan’uwantaka.
2. Daga cikin hikimar Allah wacce ake gode masa a kai, akwai sanya sakamako ya kasance daga jinsin aiki, cikin alheri da sharri.
3. Lallai wasu sahen zunubai Allah yana gaggauta yin uƙuba ga ma'abocinsu tun a duniya.
4. Lallai musulmi yana da daraja da alfarma a wurin Ubangijinsa, Allah ba ya yarda a keta su.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

WAJIBCIN SON MANZON ALLAH (SAW) DA GIRMAMA SHI

Farkon mafi girman soyayyar da ta zama wajibi a kan bawa ita ce son Allah, saboda ita ce mafi girman nau'ukan soyayya, Allah Maɗaukaki Ya ce: (Waɗanda suka yi imani sun fi son Allah (fiye da komai),[1] domin shi ne Ubangiji Mahalicci ga dukkan halittunsa, wanda ya hore wa bayi dukkan ni'imomi na bayyane da na ɓoye.

Sannan bayan soyayyar Allah Maɗaukaki, sai soyayyar Manzon Allah Muhammadu (SAW), domin shi ne wanda ya yi kira zuwa ga Allah, kuma ya sanar da mutane Allah, kuma ya isar da shari'arsa, kuma ya bayyana hukunce-hukuncensa, kuma duk abin da ya samu mumini na alheri a duniya da lahira, to haƙiƙa Allah Ya sanya shi ne hannun wannan Manzon, kuma ba wanda zai shiga aljanna har sai ya bi shi, kuma ya yi koyi da sunnarsa (SAW).

Yana da matsayi mai girma wanda Allah ya ba shi (SAW), shi bawan Allah ne kuma Manzonsa, kuma zaɓaɓensa cikin halittunsa, shi ne mafi kamalar manzanni kuma mafificin halittu, kuma cikamakin annabawa, kuma shi ne mafi jin tsoron Allah cikin bayinsa kuma mafi taƙawarsu, Allah Ya aiko shi zuwa ga dukkan mutane da aljanu baki ɗaya, kuma ya wajabta musu ɗa'a gare shi da kuma bin sa, kuma haƙiƙa Allah Ya buɗe masa ƙirjinsa, kuma ya ɗaukaka ambatonsa, kuma ya sanya wulaƙanci da ƙasƙanci ga duk wanda ya saɓa wa umarninsa.

Shi ne ma'abocin matsayi abin godewa, wanda Allah Maɗaukakin sarki ya faɗi game da shi cewa: (Tare da fatan Ubangijinka ya tashe ka a matsayin sha-yabo),[2] shi ne matsayin da Allah zai ba shi domin ya yi ceto ga mutane ranar alƙiyama, domin ya hutar dasu daga tsananin wahalar wannan ranar.

---

[1]. Suratul Baƙara: 165).
[2]. Suratul Isra'i: 79.

Kuma Allah Ya ɗaukaka matsayinsa ta yadda shi da mala'ikunsa suke masa salati, kuma ya umarci bayinsa da su yi masa salati tare da nema masa tsira, sai ya ce: (Lallai Allah da mala'ikunsa suna salati ga Annabi, ya ku waɗanda suka yi imani ku yi salati a gare shi da sallama mai yawa). [1]

Kuma soyayyar Manzon Allah (SAW) wajibi ne, kuma imani ne, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Abubuwa uku duk wanda suka haɗu a kansa, to ya samu zaƙin imani; Allah da Manzonsa su kasance sun fi soyuwa a gare shi sama da waninsu, kuma ya so mutum ba don komai ba sai don Allah, kuma ya ƙyamaci komawa cikin kafirci bayan Allah Ya tsamo shi daga cikinsa, kamar yadda yake ƙyamar a jefa shi cikin wuta), kuma wajibi ne a gabatar da son Annabi a kan son dukkan wani masoyi koma-bayan Allah Maɗaukaki; Manzon Allah (SAW) ya ce: (Imanin ɗayanku ba zai cika ba, har sai na kasance mafi soyuwa a gare shi fiye da ɗansa, da mahaifinsa, da kuma mutane bakiɗaya).[2]

[1]. Suratul Ahzab: 56.
[2]. Bukhari (16) da Muslim (44) ne suka rawaito shi.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SUNNONIN ALWALA

Sunnonin alwala: Su ne ayyukan da ake so a aikata su yayin alwala, kuma a ba da lada ga wanda ya aikata su, kuma wanda ya bar su ba shi da laifi, su ne kamar haka:

1. **Yin bismillah a farkonta;** saboda umarnin Annabi (SAW) da yin ta.[1]
2. **Yin asuwaki**; saboda fadinsa (SAW) cewa: (Ba don kada na tsananta wa al'ummata ba, da na umarce su da yin asuwaki yayin kowace alwala). [2]
3. **Wanke tafukan hannu a farkon alwala sau uku**; saboda aikatawar Annabi (SAW) cikin siffar alwalarsa. [3]
4. **Zurfafawa wurin kurkurar baki da shaƙar ruwa a hanci ga wanda ba ya azumi;** saboda fadin Annabi (SAW) cewa: (Ka zurfafa wurin shaƙar ruwa a hanci, sai dai idan kasance kana azumi).[4]
5. **Cuccuɗawa**; saboda aikatawar Annabi (SAW) "Domin lallai ya kasance idan yana alwala yana cuccuɗa hannayensa".[5]
6. **Tsefe gemu mai cika** har ya kasance ya isar da ruwa ƙarƙashinsa, ya zo a cikin hadisi cewa: "Annabi(SAW) ya kasance yana shigar da ruwa ƙarƙashin haɓarsa, sai ya tsefe gemunsa da shi",[6] kuma tsefewar wajibi ne koda gemun ya kasance babu cika.
7. **Damantawa**: Shi ne gabatar da hannaye da ƙafafuwa na dama kafin hagu; ya zo a cikin hadisi cewa: "Manzon Allah (SAW), ya kasance yana son damantawa gwargwadon iko, cikin tsarkinsa, da sanya takalmansa, da taje kansa, da dukkan sauran al'amuransa".[7]

---

[1]. Ahmad (2/418) da Abu Dawuda (101) suka rawaito shi.
[2]. Bukhari (1934) ne ya rawaito shi.
[3]. Muslim (235) ne ya rawaito shi.
[4]. Abu Dawuda (142) da Nasa'i (87) ne suka ya rawaito shi.
[5]. Ibnu Hibban (1082) da Baihaƙiy (1/196) ne suka rawaito shi.
[6]. Abu Dawuda (145) ne ya rawaito shi.
[7]. Bukhari (426) da Muslim (268) ne suka rawaito shi.

8. **Wankewa sau uku uku** a fuska da hannaye da ƙafafuwa, kuma wajibi shi ne a wanke so ɗaya; ya zo a cikin hadisi cewa: "Lallai Annabi (SAW) ya yi alwala sau ɗaya-ɗaya, kuma ya yi sau biyu-biyu, kuma ya yi sau uku-uku".[1]

9. **Faɗin zikirin da ya tabbata bayan kammala alwalar;** Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wani daga cikinku da zai yi alwala sannan ya cika alwalarsa, sannan ya ce: “Ashahadu an la ilaha ilallahu, wahdahu la sharika lahu, wa ashadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluh”, (Ma’ana: Ina shaidawa babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah, shi kaɗai ba shi da abokin tarayya, kuma Annabi Muhammad bawansa ne kuma Manzonsa), face an buɗe masa ƙofofin aljanna guda takwas ya shiga daga wadda ya so daga cikinsu),[2] kuma Tirmizi ya ƙara da cewa: “Allahummaj-alni minat-tawwabin, waj’alni minal-mutaɗahhirin”, (wato: Ya Allah ka sanya ni daga cikin masu tuba, kuma ka sanya ni daga cikin masu tsarki).[3]

❋ **Munasabar wannan zikirin bayan alwala:**

Lallai yadda lamarin yake shi ne, lokacin da ya kammala da tsarki na zahiri ta hanyar yin alwala, to ya dace ya bi bayansa da tsarki na baɗini ta hanyar kaɗaita Allah tare da tuba, domin idan tsarki biyu suka hadu a gare shi, to bawa ya cancanta da shiga wurin Allah da tsayuwa gabansa, da ganawa da shi.

[1]. Bukhari (157) da Muslim (226) ne suka rawaito shi.
[2]. Muslim (234) ne ya rawaito shi.
[3]. Tirmiziy (55) ne ya rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

DA'AWA A BAYYANE

Annabi (SAW) bai gushe ba yana kira a ɓoye har tsowon shekara uku don guje wa cutarwar mushirikai, bayan haka sai umarni ya zo daga Allah Maɗaukaki da ya yi kira zuwa ga gaskiya, kuma ya bayyana da'awa, sai faɗin Allah ya sauka cewa: (To ka tsage gaskiyar abin da aka umarce ka da shi, ka kuma kawar da kai daga mushirikai),[1] kuma Allah Mai tsarki ya keɓance iyalansa da danginsa makusanta, sai ya ce: (Kuma ka yi gargaɗi ga danginka makusanta). [2]

A nan ne Manzon Allah (SAW) ya fuskanci Banu Hashim da waɗanda suke tare da su daga Banul-Muɗɗalib, sai ya hau kan dutsen Safa ya riƙa kira, har sai da mutane suka tattara zuwa gare shi, sai Annabi (SAW) ya ce: (Shin kuna ganin da zan ba ku labarin cewa lallai wani doki zai fito daga ƙasan wannan dutsen, shin za ku gaskata ni?), sai suka ce ba mu taɓa samun ka da ƙarya ba. Sai ya ce: (To lallai ni mai gargaɗi ne gare ku game da azaba mai raɗaɗi), sai Abu Lahab ya ce: Tir da kai! saboda wannan ne ka tara mu?[3]

Sai Manzon Allah (SAW) ya cigaba da kiran mutane, yana mai haƙuri da neman lada, babu wani mai kangewa da yake kange shi daga haka, kuma ba wani da yake mayar da shi daga gare shi, kuma zargin mai zargi ba ya hana shi kira zuwa ga Allah, yana kira zuwa ga Allah dare da rana, a sirrance da bayyane, yana kiran manya da yara, maza da mata da baƙi da fari.

Sai bayyanawar da shelanta da'awar suka ɓata ran mushirikai, kuma adadin musulmai ya ƙaru, kuma zargin ababen bautar mushirikai da siffanta su da rashin amfanarwa ko cutarwa da yake yi ya fusata su, sai suka bayyana ƙiyayya gare shi, kuma suka bayyana zaginsa da

---

[1]. Suratul Hijiri: 94.
[2]. Suratul Shu'ara'i: 214.
[3]. Bukhari (4973) da Muslim (208) ne suka rawaito shi.

cin mutuncinsa, da kuma fuskantar waɗanda suke tare da shi da cutarwa da azabtarwa da yanke hulɗa.

Sai Allah Ya katange Manzonsa (SAW), kuma ya ba shi kariya ta hanyar baffansa Abu Talib; domin shi yana da daraja kuma ana yi masa biyayya a cikinsu, ba sa iya ƙarfin hali a kan bijiro masa da wani abu dangane da al'amarin Annabi Muhammad (SAW); domin abin da suka sani na tsananin soyayyar da yake masa.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SA'IDU ƊAN ZAIDU (RA)

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne: Sa'idu ɗan Zaidu ɗan Amru ɗan Nufail ɗan Abdul'uzza ɗan Ribah.

An haife shi kafin aiko Annabi da shekara goma sha uku, kuma babansa ya kasance yana kan tauhidi, yana yawo cikin garin Sham yana me neman addinin Annabi Ibrahim amincin Allah ya tabbata a gare shi, yana neman gaskiya, ba ya yin yanka domin gumaka, kuma ba ya cin mushe ko jini, sai dai bai riski Musulunci ba, ya rasu kafin aiko Annabi.[1]

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Ya kasance (RA) cikin waɗanda suka shiga Musulunci a farko, kuma daga cikin Muhajirai na farko, kuma ɗaya daga cikin mutane goma da aka yi musu albishir da aljanna.

Ya halarci yaƙin Badar da kibiyarsa da ladansa, sannan ya halarci sauran yaƙoƙi da suka biyo bayanta.

Kuma ya kasance yana lizimtar Annabi (SAW) mafi tsananin lizimta; Sa'idu ɗan Jubair yana cewa: "Kuma matsayin Abubakar da Umar da Usman da Aliyu da Ɗalhat da Zubairu da Sa'ad da Abdurrahman ɗan Auf da Sa'idu ɗan Zaid, shi ne suna kasancewa a gaban Manzon Allah (SAW) a wurin yaƙi, da kuma bayansa a lokacin salla".[2]

Umar ɗan Khaɗɗab ya auri Atika 'yar uwar Sa'idu ɗan Zaid, kuma shi ma Sa'idu ɗan Zaid ya auri Fatima ƴar Khaɗɗab 'yar'uwar Umar, kuma ya yi hijira tare da ita zuwa Madina, amma bai yi hijira zuwa Habasha ba; ta yadda ya kasanca daga cikin masu darajar Ƙuraishawa da shuwagabanninsu, saboda haka bai fuskanci

[1]. Littafin Siyaru A'alamin Nubala (1/126).
[2]. Littafin Asadulgaba (2/237).

azabtarwa ba kamar yadda waninsa ya fuskanta daga cikin masu rauni.

Sa'idu ɗan Zaidu (RA) ya kasance mai tsoran Allah da tsantseni, mai karɓaɓɓiyar addu'a, daga haka akwai cewa: lallai wata mata ta kai ƙararsa wurin Marwan ɗan Hakam gwamnan Madina; kuma ta ce: Lallai shi ya zalunce ni game da filina. Sai Marwan ɗan Hakam ya aika a kira shi, sai Sa’idu ya ce: "Shin kuna gani ni zan zallunce ta, alhali na ji Manzon Allah (SAW) yana cewa: (Duk wanda ya ɗauki wani sashi na ƙasa bisa zalunci, za’a dunƙule masa ita tun daga ƙasa ta baƙwai?!), ya Allah idan ƙarya take yi, Ka makantar da idanunta, kuma ka kashe ta a filin nata. Ya ce: ba ta mutu ba har sai da ta makance, ya ce: Na gan ta a makance tana bin bango tana cewa: Addu'ar Sa’idu ɗan Zaid ta kama ni, sannan wata rana tana tafiya a cikin filin nata, sai ta faɗa a cikin wani rami ta mutu.[1]

❖ Rasuwarsa:

Sa’idu (RA) ya rasu a Aƙiƙ, shekara ta 51 bayan hijira, yana da shekara saba’in da ɗoriya a lokacin, sai aka ɗauke shi zuwa Madina, kuma a ka binne shi tare da Sahabban Annabi (SAW).

Kuma Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas ne ya yi masa wanka kuma ya sanya masa likkafani, sai Mugira ɗan shu’uba ya yi masa salla, kuma ya binne shi, kuma Abdallah ɗan Umar da Sa’ad ɗan Abu Waƙƙas suka shiga ƙabarinsa, kuma mutanen garin Madina sun yi baƙin ciki mai tsanani game da mutuwarsa.

[1]. Muslim (1610) ne ya rawaito shi.

Auna fahimtarka a darusan mako na 9 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah Maɗaukaki: (Kuma suna hana kayan taimako)?		B
	a. Suna hana zakka ga waɗanda suka cancanta.	b. Suna ƙin ba da aron abin da bayar da aronsa ba ya cutarwa, kamar tukunya.	c. Suna cin gado.
Darasin Hadisi	Tambaya: Faɗin Annabi (SAW) cewa: "Duk wanda ya cutar da musulmi, to Allah zai cutar da shi" dalili ne a kan:		B
	a. Imani yana ƙaruwa kuma yana raguwa.	b. Sakamako yana kasancewa ne daga jinsin aiki.	c. Marabauci shi ne wanda ya ɗauki izina daga waninsa.
Darasin Aƙida	Tambaya: Muna son Annabi (SAW) saboda shi ne:		C
	a. Mafi alherin ƙibilun larabawa.	b. Ya kasance maraya babu uwa babu uba.	c. Wanda ya yi kira zuwa ga Allah, ya sanar da mutane Allah kuma ya isar da shari'arsa kuma ya bayyana hukunce-hukuncensa.
Darasin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin sunnonin alwala akwai:		B
	a. Bibiya.	b. Asuwaki.	c. Shafar dukkanin kai.
Darasin Sira	Tambaya: Wane ne ya yi wannan maganar: (Tir da kai! Saboda wannan ka haɗa mu)?		B
	a. Abu Jahal.	b. Abu Lahab	c. Abu Sufyan.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Sa'idu bin Zaid ya auri:		C
	a. Fatima bint Ƙais	b. Fatima bint Asad.	c. Fatima bintul Khaɗɗaba.

MAKO NA GOMA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-KAUTHAR

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ﴾

﴿إِنَّآ أَعۡطَيۡنَٰكَ ٱلۡكَوۡثَرَ ١ فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنۡحَرۡ ٢ إِنَّ شَانِئَكَ هُوَ ٱلۡأَبۡتَرُ ٣﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.

1. Lallai Mu Mun ba ka tafkin Alkausar.
2. To sai ka yi salla don Ubangijinka, ka kuma soke (abin hadayarka).
3. Lalle mai ƙin ka shi ne mai yankakken alheri.

❖ Saƙon da Surar ta ƙunsa:

Ni'imar da Allah Maɗaukaki Ya yi wa Annabinsa (SAW) ta ba shi alheri mai yawa, da kuma kare shi daga maƙiyansa.

❖ Sababin saukar Surar:

An rawaito cewa lokacin da ɗan Annabi (SAW) Al-Ƙasim, ya rasu, sai Al-As ɗan Wa'il da wasu daga cikin mushrikai suka ce: "Muhammad mai yankakken baya ne, ba shi da magaji, sai Allah Maɗaukaki Ya saukar da wannan Sura dake ɗauke da raddi gare su, kuma don ta ƙarfafi Manzo (SAW), ta kuma yi masa bushara da al'ummarsa da kyautar Al-Kauthar[1].

[1]. Asbabun-Nuzul na Al-Wahidi (466).

❖ Baƙin Kalmomi:

الكوثر	Al-Kauthar	Alheri mai yawa, kuma daga cikinsa akwai ƙoramar Al-Kauthar a Aljanna
وانهر	Wanhar	Ka yanka abar yankarka don Allah Shi kaɗai
شانئك	Shani'aka	Maƙiyinka kuma mai gaba da kai
الأبتر	Al-Abtar	Mai yankakken baya, wanda aka yanke daga dukkan alheri.

Ma'anar Surara a Dunƙule:

Suratul-Kauthar sura ce Makkiyya, kuma ita ce mafi gajartar Surorin Al-ƙur'ani mai girma, a cikinta Allah Maɗaukaki Ya yi wa Manzonsa (SAW) baiwa ta hanyar ba shi alheri mai yawa da ni'imomi masu girma a duniya da lahira, daga cikin wannan alheri akwai wata ƙorama a aljanna da ake kira Al-Kauthar.

Annabi (SAW) yana cewa: (Alkawthar wata ƙorama ce a aljanna, gefunanta zinariya ne, ruwanta kuma yana gudana ne a kan duwatsu na lu'u-lu'u da yaƙuti, ƙamshin ƙasarta kuwa ya fi na almiski, ruwanta kuma ya fi zuma zaƙi, kuma ya fi kankara fari) [1].

Sa'an nan Allah Maɗaukaki Ya umurce shi da ya gode wa Ubangijinsa bisa waɗannan girmamawa da Ya yi masa ta hanyar yawaita salla don neman yardar Allah Shi kaɗai, kuma ya yanka mafi tsadar abin da ya mallaka na dobbi domin neman kusanci ga Allah.

Sa'an nan aka rufe Surar da bushara ga Annabi (SAW) da katse dukkan alheri ga maƙiyinsa, da yanke ambatonsa daga harsunan mutane.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3361).

❖ Abubuwan da za mu koya daga cikin Surar:

1. Matsayin Annabi (SAW) a wurin Ubangijinsa da kariyarsa gare shi da ɗaukaka shi da Ya yi duniya da lahira.
2. Kafircin wanda yake ƙin Annabi (SAW) ko yake ƙin wani abu daga abin da ya zo da shi.
3. Muhimmancin gaggawa wajen godiya bisa ni'imomin Allah, da kuma cewa lallai hakan sababi ne na wanzuwarta da ƙaruwarta.
4. Kwaɗaitarwa game da zubar da jini ta hanyar layya ko hadaya ko suna, domin bauta ga Allah Maɗaukaki.
5. Cewa lallai ɗorewa wajen gabatar da salla da yanka domin Allah, shi ne mafi girman abin da ya kamata bawa ya fuskanci ni'imomi da shi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FIFIKON MUMINI MAI ƙARFI

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Mumini mai ƙarfi ya fi alheri kuma ya fi soyuwa ga Allah fiye da mumini mai rauni, kuma kowanne akwai alheri tare da shi, ka yi kwaɗayin samun abin da zai amfane ka, kuma ka nemi taimakon Allah, kada kuma ka gajiya, kuma idan wani abu ya same ka, kada ka ce: da na sani na aikata kaza da kaza, da kaza da kaza da ya kasance, sai dai, ka ce: Haka Allah Ya ƙaddara, kuma abin da Ya ga dama Ya aikata, domin kalmar "da na sani" tana buɗe aikin shaiɗan**)[1].

❖ Sharhi:

Manzon Allah (SAW) yana ba da labarin cewa muminai suna bambanta a fifiko, da ƙarfin imani, da ƙaunar da Allah Maɗaukaki Yake musu, da kuma yadda suke tsayuwa da addininsa, da kuma cewa lallai su suna bisa matakai ne mabambanta a cikin haka, kamar yadda Allah Ya ce ((Suna da darajoji mabambanta a wurin Allah))[2], da kuma cewa lallai mumini mai ƙarfin imani yana da mafi ɗaukakar waɗannan darajoji da matakai a wurin Allah Maɗaukaki, ba tare da an kore darajar ga mumini mai rauni ba, sai don mumini mai ƙarfi amfaninsa yana wuce kansa ya isa zuwa ga wasu, yayin da shi mumini mai rauni amfaninsa yana taƙaita ne ga kansa kawai.

Sa'an nan Annabi (SAW) ya yi wa al'ummarsa wasiyya da ta tattara fa'idodi masu yawa a cikinta, sai ya umurce su da su dage wajen neman abubuwan da ke da amfani gare su a addininsu da rayuwarsu ta duniya, tare da neman taimakon Allah da rashin gajiyawa, kuma idan wani abu ya kuɓuce daga cikin haka bayan ya yi iya ƙoƙarinsa da jajircewarsa, to wajibi ne ya nutsar da zuciyarsa ga ƙaddarar Allah da hukuncinsa, kuma ransa ya daɗaɗa da hakan, kuma kada ya jingina hakan ga barin riƙo da sabubban da yake zaton za su

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2664).
[2]. [Alu-Imran (163].

amfane shi da ya aikata hakan, domin lallai ita (Da na sani) a irin wannan yanayi tana buɗe aikin shaiɗan ta hanyar waswasi da baƙin ciki da nadama da damuwa da tawayar imaninsa da yardarsa da ƙaddara.

❖ Abubuwan da ake Fahimta daga Hadisin:

1. Masu imani suna da matakai mabambanta a cikinsa, kuma abin da wajibi shi ne neman cikarsa da ƙarfinsa.
2. Ana so mutum ya kasance mai ƙarfi da kuzari wajen aikata ayyuka masu amfani.
3. Hani game da reni da wulakanci ga wanda yake da raunin imani, domin tabbatar falala ga kowane mumini.
4. Ya kamata musulmi ya kwaɗaitu wajen neman abin da zai amfane shi cikin lamuran addini, kamar neman ilimi mai amfani da aiki na ƙwarai.
5. Ya kamata musulmi ya kwaɗaitu wajen neman abin da zai amfane shi a cikin lamuran duniya kamar neman arziki domin biyan buƙatarsa da buƙatar iyalinsa.
6. Wajabcin neman taimakon Allah, da dogara gare Shi kaɗai cikin dukkan al’amura.
7. Wajabcin riƙo da sabubba masu amfani, ba tare da dogara da su ba ko ga kansa.
8. Wajabcin imani da miƙa wuya ga ƙaddara da hukuncin Allah, da tasirin haka wajen daidaituwar rayuwar musulmi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

WAJABCIN BIYAYYA GA MANZON ALLAH (SAW)

Ɗaya daga cikin mafiya girman alamomin ƙaunar Manzon (SAW), da kuma girmama shi, akwai girmama sunnarsa da aiki da ita, domin sunnarsa ita ce mafi matsayi bayan Alƙur'ani mai girma, kuma wajibi ne a girmama ta kuma ayi aiki da ita, domin ita ma wahayi ce daga Allah Maɗaukaki, Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma ba ya yin magana bisa son rai () Shi ba wani abu ne ba in ban da wahayi da ake yiwo masa)) [1].

Kuma saboda haka ne Allah Maɗaukaki Ya yi umarni da biyayya ga Manzon Allah (SAW), da kuma koyi da shi a wurare masu yawa, fiye da wurare arba'in a cikin Alƙur'ani mai girma, Allah Ya ce: ((Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi biyayya ga Allah, kuma ku yi biyayya ga Manzo)) [2]. Kuma Ya ce: ((Duk wanda ya yi wa wannan Manzo biyayya, to haƙiƙa ya yi wa Allah biyayya ne)) [3]. kuma Ya ce: ((Kuma ku yi biyayya ga Allah da Manzo don a ji ƙan ku a ranar tashin alƙiyama)) [4].

Kuma Allah Maɗaukaki Ya ba da labarin cewa Manzon Allah (SAW) shi ne abin koyi mafi kyawu ga al'ummarsa, sai Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Haƙiƙa kuna da kyakkyawan abin koyi tare da Manzon Allah, ga wanda yake yin kyakkyawan fata game da Allah da ranar lahira, ya kuma ambaci Allah da yawa))[5], Ibnu Kasir Allah ya masa rahama ya ce: "Wannan aya mai girma asali ce mai girma cikin koyi da Manzon Allah (SAW) cikin maganganunsa, da ayyukansa, da halayensa"[6].

Kuma Allah Maɗaukaki Ya sanya biyayya ga Manzon Allah (SAW) sababi na samun ƙaunar Allah da gafarar zunubai. Allah Ya ce: ((Ka

---

[1]. [An-Najm: 3–4].
[2]. [An-Nisā': 59].
[3]. [An-Nisa: 80].
[4]. [An-Nur: 56].
[5]. [Al-Ahzab: 21].
[6]. Tafsirin Ibnu Kasir (6/350).

ce: "In kun kasance kuna son Allah, to ku yi mini biyayya, sai Allah Ya so ku, kuma Ya gafarta muku zunubanku. Kuma Allah Mai gafara ne, Mai jin ƙai)) [1].

Haka kuma Allah Ya sanya saɓa wa Manzonsa (SAW) a matsayin ɓata, Allah Maɗaukaki Ya ce: ((To idan ba su amsa maka ba, to ka sani cewa ba abin da suke bi sai soye-soyen zukatansu kawai. Ba kuwa wanda ya fi ɓacewa kamar wanda ya bi son zuciyarsa ba tare da wata shiriya daga Allah ba. Lalle Allah ba Ya shiryar da mutane azzalumai)) [2].

Kuma Allah Maɗaukaki Ya sanya saɓa wa Manzonsa (SAW) sababin saukar azaba da fitina. Allah Ya ce: ((To lallai waɗanda suke saɓa wa umarninsa su ji tsoron kada wata fitina ta shafe su ko kuma wata azaba mai raɗaɗî ta same su)) [3], wato, su ji tsoron kada fitina ta sami zukatansu kamar kafirci, ko munafurci, ko bidi'a ko azaba mai raɗaɗî da wani abu da cikin uƙubobi na duniya ko a lahira.

Kuma kamar yadda biyayya ga Manzon Allah (SAW) take kasancewa ta hanyar aikata abin da ya umarta, da barin abin da ya hana. Haka nan tana kasancewa ta hanyar koyi da shi cikin siffar gudanar da ibadoji, ta yadda za a yi su kamar yadda yake yi.

Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ku yi salla kamar yadda kuka gan ni ina yin salla)[4]. Kuma Annabi (SAW) ya ce: (Ku koyi ibadarku ta Hajji daga gare ni) [5]. Kuma ya ce: (Duk wanda ya aikata wani aiki ba bisa umarninmu ba, to an mayar mass))[6].

---

[1]. [Alu Imran: 31].
[2]. [Al-Ƙasas: 5].
[3]. [An-Nur: 63].
[4]. Bukhari (631) da Muslim (674) ne suka rawaito shi.
[5]. Muslim ne ya rawaito sh (1297).
[6]. Bukhārī, (2697) da Muslim (1718) ne suka rawaito shi

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

KURAKURAI DA SUKE YAWAN FARUWA A CIKIN ALWALA

Akwai wasu kurakurai da dama da mutane ke yawan aikatawa yayin alwala, waɗanda da ya wajaba a lura da su kuma a nisance su.

❋ **Daga cikin waɗannan kurakurai akwai:**

1. **Furta niyya da baki:** Wannan kuskure ne, domin niyyar da ake buƙata a cikin zuciya take, ba a shar'anta a furta ta da harshe ba; saboda bai tabbata ba daga Annabi (SAW) ya furta niyyarsa ko da sau ɗaya ba, kuma, yin haka akwai takurawa da wahalar da kai a ciki kamar yadda aka sani.
2. **Rashin cika alwala yadda ya kamata:** Ta hanyar rashin game gaɓa da ruwa, wani lokaci Annabi (SAW) ya ga wani mutum yana alwala bai wanke wurin ƙumbar ƙafarsa ba, sai ya ce masa: (Ka koma ka kyautata alwalarka)[1], kuma Annabi (SAW) ya ce wa wanda yake sakaci wurin isar da ruwa ga dukkan sassan ƙafarsa: (Kaicon dugagan da ruwa bai isa gare su ba daga azabar wuta) [2].
3. **Ƙetare iyaka da yawan kwarara ruwa:** Wannan abu ne da aka hana, ba ya daga cikin cika alawala, domin cika alwala, shi ne gudanar ruwa a kan gaɓa da game shi da shi, ba yawan zuba ruwa ba, kuma ya tabbata cewa Annabi (SAW) ya kasance yana yin alwala da ruwan mudu guda ɗaya, kuma yana wanka da ruwan sa'i ɗaya[3].
4. **Rashin cire abubuwa da ke hana ruwa isa ga fata,** kamar kyandir, da gari, da ruwan rini, da jan ƙumba da mata da dama ke amfani da shi a yau.
5. **Rashin wanke tafukan hannu tare da hannaye, da taƙaita da wanke su a farkon alwala kawai:** Kuma abin da yake daidai, shi ne a wanke hannaye daga yatsunsu har zuwa gwiwar hannu.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (432).
[2]. Bukhari (165), da Muslim (242) ne suka rawaito shi.
[3]. Bukhari (201), da Muslim (325) ne suka rawaito shi.

Amma wanke tafukan hannu a farkon alwala mustahabbi ne, amma wanke su tare da hannaye gaba ɗaya wajibi ne.

6. **Rashin shaƙar ruwa cikin hanci yayin alwala**, da taƙaita da wanke hanci daga waje kawai.
7. **Wuce gona da iri wajen wanke gaɓoɓin alwala fiye da sau uku**.
8. Rashin shafar kai gaba ɗaya, da taƙaita da shafar gaban kai kawai saboda tsoron ɓata gyaran gashi.
9. **Wasu mutane suna ɗauka cewa yin wanke al'aura yana daga cikin alwala**: Don haka idan zai yi alwala don salla, sai ya fara da wanke al'aura, wannan kuskure ne, saboda shi wanke al'aura ba ya daga cikin alwala, sai dai yana da alaƙa ne da tsabta bayan buƙatar fitsari ko bayan gida, kuma babu buƙatar maimaitawa yayin alwala.
10. **Rashin motsa zobe ko agogo yayin alwala,** domin ruwa ya isa ƙarƙashinsu, kuma ya game dukkan gaɓar.
11. **Sakaci ta hanyar yin taimama alhali akwai ruwa:** Kamar idan mutum ya kasance a gonarsa ko yawon shakatawa, kuma yana da daman samun ruwa ta hanyar hawa zuwa Masallaci ko kasuwa da waninsu.
12. **Barin salla ga wanda ya rasa ruwa ko ƙasa**; abin da yake wajibi shi ne ya yi salla gwargwadon halin da ya samu kansa a ciki, ko da ba da alwala ba, ko taimama, saboda Allah baya ɗora wa rai abin da bai zai iya ba.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

CUTARWAR ƙURAISHAWA GA MUSULMI

Lokacin da kafiran ƙuraishawa suka ga yawan musulmi yana ƙaruwa a kullum, sai kowace kabila ta fara azabtar da musulmin da ke cikinta, suka riƙa wahalar da su saboda addininsu, kuma manyan mushrikai suka fara cin zarafi da danniya ga muminai masu rauni!

Abdullahi ɗan Mas'ud (RA) yana cewa: "Mutane bakwai su ne farkon waɗanda suka bayyana Musuluncinsu: Manzon Allah (SAW), Abubakr, Ammar, mahaifiyarsa Sumayya, Suhaib, Bilal, da Miƙdad, amma Manzon Allah (SAW) Allah ya kare shi, Allah ya kare shi ta dalilin Baffansa Abu Ɗalib, shi kuma Abubakar, sai Allah Ya kare shi ta dalilin danginsa, sauran mutanen kuwa, mushrikai suka kama su, suka saka musu sulken ƙarfe, suka shanya su cikin rana"[1].

Sai Ammar ɗan Yasir da mahaifansa Allah ya ƙara musu yarda, suka kasance daga cikin farkon waɗanda suka fuskanci cutarwa da azabtarwa, kuma Manzon Allah (SAW) ya kan wuce ta wajen da ake musu azaba, sai ya ce musu: (Ku yi haƙuri, ya ku iyalan Yasir, lallai aljanna ita ce makomarku) [2].

Kuma wata rana, Abu Jahal ya wuce inda ake azabtar da Sumayya, mahaifiyar Ammar, sai ya soka mata mashi a farjinta har ta mutu, wannan ya sa ta zama shahidiya ta farko a Musulunci[3].

Daga cikin waɗanda aka azabtar har wayau, akwai Khabbab ɗan Aratt (RA), mushrikai sun kasance suna tsananta masa azaba, suna cire masa tufafi, suna jefa shi a kan garwashin wuta mai ƙuna, har sai kitsen bayansa ya narke sai ya kashe wutar[4]. Haka nan shi ma Bilal ɗan Rabahb (RA) wanda idan zafin azaba ya tsananta a gare shi ƙarƙashin zafin rana mai tsananin ƙuna, sai ya riƙa cewa: "Allah

---

1. Ahmad (3832), da Ibnu Majah (150) ne suka rawaito shi
2. Ɗabarani (1088), da Hakim (6666) ne suka rawaito shi.
3. Siyaru A'lamin-Nubala (1/176).
4. Hilyatul-Awliya (473).

Ɗaya ne! Allah Ɗaya ne!” [1], sai Abubakr (RA) ya siye shi daga wurin Umayya ɗan Khalaf, ya 'yanta shi, kamar yadda ya sayi mutane daban-daban daga cikin waɗanda ake azabtarwa, ya ‘yanta su, kuma Allah Ya kuɓutar da su ta hanyarsa daga bauta da azabtarwa.

Kuma haƙiƙa shi ma Abubakar (RA) ya samu nasa rabon na cutarwa, domin haƙiƙa an taɓa bugunsa sosai wata rana a cikin Masallaci Mai alfarma, har sai da aka ɗauke shi zuwa gidansa, mutanensa ba su yi zaton zai rayu ba[2].

Kuma cutarwar mushrikai ta kai ga Annabi (SAW), kuma sun fuskantar da nau'o'in cutarwa gare shi, sun ɗora masa ɗan tayin dabba da jininta a kafadarsa yayin da yake cikin sujada[3].

Kuma Uƙba ɗan Abu Mu'aiɗin ya zo wurin Annabi (SAW) a lokacin yana salla a ɗakin Masallacin Ka‘aba, sai ya sanya mayafinsa a wuyarsa, yana shaƙe shi da ƙarfi, sai Abūbakar ya zo ya riƙe kafadarsa, ya ture shi daga Manzon Allah (SAW), sannan ya ce: ((Shin za ku kashe mutum ne saboda kawai ya ce Ubangijinsa Shi ne Allah?))[4],[5].

Duk da wannan zalunci da cin zarafi, Manzon Allah (SAW) ya yi haƙuri, ya cigaba da da'awarsa, ya yi tsayin daka a kan da'awar, wata cutarwa ba ta taɓa kawar da shi ba, kuma wani abin duniya bai taɓa ruɗar da shi ba.

---

[1]. Ibnu Maja ne ya rawaito shi (150).
[2]. Al-Bidayah Wan-Nihayah (3/23).
[3]. Bukhari (3854) da Muslim (1794) ne suka rawaito shi.
[4]. Ighathatul-Lahfan (2/28).
[5]. Bukhari ne ya rawaito shi (3866).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABU UBAIDATA ƊAN JARRAH (RA)

❖ Suna da Haihuwarsa:

Shi ne Abu Ubaida Amiru ɗan Abdullah ɗan Jarrah.

An haife shi ne a shekara ta 40 kafin hijira.

❖ Rayuwarsa da falalarsa:

Ya kasace (RA) mutum ne siriri, gemunsa kaɗan, dogo, mai taƙawa, mai gudun duniya da tsantseni, ana siffanta shi da kyawawan ɗabi'u, da haƙuri, da tawali'u, da yalwar ilimin Alƙur'ani da na sunna.

Yana daga cikin farkon waɗanda suka karɓi Musulunci, kuma daga cikin mutane goma da aka yi musu bushara da aljanna.

Ya yi hijira zuwa Habasha hijira ta biyu, kuma ya halarci dukkan yaƙe-yaƙe tare da Annabi (SAW).

A ranar Yaƙin Uhudu, ya cisge hulan kwano biyu da suka makale a fuskar Annabi (SAW) da haƙoransa, har haƙoran gabansa biyu suka fita, sai ya kasance mafi kyawun mai ɓaɓurka daga cikin mutane[1].

Kuma Annabi (SAW) ya yi masa inkiya da cewa shi ne: "Amintaccen wannan al'umma", dalilin wannan inkiya kuwa shi ne: Mutanen Yaman sun zo wurin Annabi (SAW) suka ce: "Ka aiko mana da mutum da zai koya mana sunna da Musulunci", sai Annabi (SAW) ya kama hannun Abu Ubaida, ya ce: (Lallai kowace al'umma tana da amintacce, kuma amintaccen wannan al'umma shi ne Abu Ubaida ɗan Jarrah)[2].

A zamanin Abubakar As-Siddiƙ Abu Ubaida yana ɗaya daga cikin manyan kwamandoji huɗu da Abubakar ya naɗa don su jagoranci buɗe ƙasar Sham.

---

[1]. Siyaru Alamin-Nubala (1/81).
[2]. Bukhari (3744) da Muslim (2419) ne suka rawaito rawaito shi.

A zamanin Umar ɗan Khaɗɗab kuma, Abu Ubayda ya karɓi jagorancin rundunonin yaƙi, kuma ya samu nasarar buɗe garin Dimashƙa da wasu garuruwa da ƙauyukan ƙasar Sham.

Kuma Umar ɗan Khaɗɗab yana cewa: "Ina fatan da a ce wannan gari cike yake da mazaje kamar Abu Ubayda ɗan Jarrah"[1].

❖ Rasuwarsa:

A shekara ta 18 bayan jijira, Abu Ubaida ya kasance ɗaya daga cikin waɗanda suka kamu da annobar Amwas, kuma ya rasu a sakamakonta, kuma an birne shi a wani gari mai suna Ghaurul-Urdun.

[1]. Siyaru Alamin-Nubala (1/14).

Auna fahimtarka a darusan mako na 10			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah Maɗaukaki: "Shāni'aka"?**		c
	a. Makusancinka	b. Mai sonka	c. Maƙiyinka
Darasin Hadisi	**Tambaya: Mumini mai ƙarfi yafi mumini mai rauni, domin:**		a
	a. Amfaninsa yana kaiwa zuwa ga wasu.	b. Amfaninsa yana taƙaita ne ga kansa.	c. Tsanani damƙarsa ga maƙiyansa
Darasin Aƙida	**Tambaya: Tambaya: Daga cikin mafiya girman nau'o'in ƙaunar Manzon Allah akwai:**		b
	a. Murnar zagayowar ranar haihuwarsa	b. Girmama sunnarsa da aiki da ita	c. Sanya irin inkiyarsa (SAW)
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Daga cikin kura-kuran da ke yawan faruwa a cikin alwala akwai:**		a
	a. Zaton cewa wanke al'aura yana cikin alwala	b. Kurkurar baki da shakar ruwa da kamfata ɗaya	c. Taƙaita da wanke gaɓoɓi sau ɗaya kawai
Darasin Sira	**Tambaya: Daga cikin mutanen da suka fara bayyana Musuluncinsu akwai:**		b
	a. Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas	b. Ammar ɗan Yasir.	c. Abu Sufyan ɗan Ḥarb
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Wane ne ya ce: "Na so da a ce wannan gida cike yake da mazaje kamar Abu Ubaida ɗan Jarrah?**		b
	a. Manzon Allah (SAW)	b. Abubakar As-Ṣiddiƙ	c. Umar ɗan Khaɗɗab

MAKO NA GOMA SHA ƊAYA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-ASR

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
وَٱلۡعَصۡرِ ١ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَفِي خُسۡرٍ ٢ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلۡحَقِّ
وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ ٣﴾

❖ Fassara:

1. Ina rantsuwa da zamani.
2. Lallai mutum yana cikin asara.
3. Sai dai waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, suka kuma yi wa juna wasiyya da gaskiya, suka kuma yi wa juna wasiyya da haƙuri.

❖ Saƙon da Surar ta ƙunsa:

Sabubban tsira daga asara

❖ Bakin Kalmomi

العصر	Al-ʿAṣr	Zamani gaba ɗayansa
الإنسان	Al-Insan	Kowane mutum
خسر	Khusr	Asara da halaka
وتواصوا	Wata wasau	Suka yi wa juna wasiyya
بالحق	Bil-Haƙƙ	Da dukkan alheri, cikin ƙuduri da magana da aiki
بالصبر	Bis-Sabr	Da haƙuri wajen biyayya, da barin saɓo, da kuma yarda da ƙaddarar Allah mai raɗaɗi

❖ Ma’anar Surar a Dunƙule:

Suraratul-Asr sura ce Makkiyya, Allah Maɗaukaki Ya buɗe ta da rantsuwa, ta yadda Ya rantse da zamani gaba ɗayansa kan cewa dukkan mutane suna cikin tabbatacciyar asara da halaka, sai dai waɗanda suka yi imani, waɗanda suka haɗa tsakanin imani da ayyuka na ƙwarai, kuma suka yi wa juna wasiyya da gaskiya cikin ƙuduri da magana da aiki, kuma suka yi wa juna wasiyya da haƙuri da tabbata a kan hakan har zuwa mutuwa, waɗannan su ne waɗanda aka keɓe daga asara ta hanyar shigarsu aljanna gidan rabauta da farin ciki

❖ Abubuwan da za mu koya daga Surar:

1. Muhimmancin lokaci, domin a cikinsa bayi suke ayyukansu da ƙoƙarinsu, kuma saboda haka ne Allah Maɗaukaki ya rantse da shi, kuma ba Ya rantsewa sai da abin da yake da girma.
2. Lallai tafarkin tsira daga asara shi ne imani, da aiki nagari, da yi wa juna wasiyya da gaskiya, da yi wa juna wasiyya da haƙuri.
3. Da waɗannan abubuwa biyu na farko mutum yake cika kansa, kuma da waɗannan biyu na ƙarshe yake cika waninsa; idan aka haɗa waɗannan abubuwa guda huɗu, sai mutum ya tsira daga asara kuma ya rabauta.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR SALLOLI BIYAR DA KANKAREWARSU GA ƘANANAN ZUNUBAI

An karɓo daga Abu Huraira (RA) cewa, Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Salloli biyar, da Jumu'a zuwa Jumu'a, da Ramadan zuwa Ramadan, suna kankare ƙananan zunubban da ke tsakaninsu, idan aka nisanci manyan zunubai**)[1].

❖ Sharhi:

Wannan hadisin yana nuni ne a kan fifikon da Allah Maɗaukaki Ya yi ga waɗannan ibadu guda uku: salloli biyar, sallar Jumu'a, da azumin Ramadan, kuma yana nuni da cewa suna da matsayi maɗaukaki a wajen Allah, da lada mai girma, kuma aikata su ta fuskar da ta dace sababi ne da zai sa Allah Maɗaukaki Ya gafarta zunuban abin da ke dake tsakaninsu -da falalarsa- idan bawa ya nesanci manyan zunubai.

❖ Ababuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Girman falala da ke cikin salloli biyar, sallar Jumu'a, da azumin Ramadan.
2. Karkasuwar zunubai zuwa ƙanana da manya.
3. Haɗarin manyan zunubai, da kuma cewa ba makawa sai an tuba.
4. Manyan zunubai su ne waɗanda shari'a ta tanada musu haddi a duniya, ko alƙawarin narko a lahira, ko aka haɗa aikinsu da tsinuwa ko fushin Allah.
5. Daga cikin misalan manyan zunubai akwai: Shirka da Allah, zina, shan giya, gulma, annamimanci, cin dukiyar maraya, kisa ba tare da haƙƙi ba, da cin dukiyar mutane ta hanyar haram.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (233).

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

HANI GAME DA ƘETARE IYAKA DA WUCE GONA DA IRI WURIN YABON ANNABI (SAW)

Guluwwi: Shi ne wuce iyakar abin da aka shar'anta, Allah Maɗaukaki Ya ce: ((**Kada ku wuce iyaka a cikin addininku**))[1]. Wato, kada ku wuce iyakokin addininku ku yi ƙari a cikinsa.

Amma **Iɗra'i** kuwa: shi ne wuce iyaka wajen yabo, da yin ƙarya a ciki.

Kuma haƙiƙa Annabi (SAW) ya hana wuce gona da iri da ƙetare iyaka cikin yabonsa, ta yadda za a ɗaukaka shi daga matsayin bawa da Manzo, a sanya masa wani abu daga abubuwan da Allah Ya keɓanta da su, Sai Annabi (SAW) ya ce: (Kada ku wuce gona da iri cikin lamarina kamar yadda nasara suka wuce gona da iri cikin lamarin Ɗan Maryam, abin sani kawai, ni bawa ne na Allah, don haka ku ce da ni: Bawan Allah kuma ManzonSa))[2].

Kuma a lokacin da wasu daga sahabbai suka ce wa Annabi (SAW): Kai ne shugabanmu, sai ya ce: (Shugaba Shi ne Allah Mai girma da ɗaukaka)[3].

Kuma a yayin da suka ce: Kai ne mafi falala a cikinmu, kuma mafi girman daraja a cikinmu, sai ya ce: "Ku faɗi maganarku, ko wani ɓangare daga maganarku, kada shaiɗan ya rinjaye ku)[4].

Kuma wasu sun ce masa: Ya Manzon Allah, ya mafi alherinmu, kuma ɗan mafi alherinmu, kuma shugabanmu, kuma ɗan shugabanninmu. Sai ya ce: (Ya ku mutane, ku faɗi maganarku, kuma kada shaiɗan ya ruɗe ku, ni ne Muhammad bawan Allah kuma

---

1. [At-Taubah: 128].
2. Bukhari ne ya rawaito shi (3445).
3. Abu Dawud ne ya rawaito shi (4806).
4. Nasa'i ne ya rawaito shi (1077).

Manzonsa, ba na so ku ɗaukaka ni sama da matsayina wanda Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ba ni)[1].

Sai Manzon Allah (SAW) ya ƙyamaci a yaba masa da waɗannan kalmomi kamar: “Kai ne shugabanmu, kai ne mafi falala daga cikinmu, kai ne mafi girma daga cikinmu, duk da cewa shi ne Mafificin cikin halittu kuma mafi alheri, kuma mafi ɗaukaka, kuma mafi girman halittu baki ɗaya, amma duk da haka ya hana su aikata hakan don ya nesanta su daga wuce gona da iri da ƙetare iyaka wajen yabo, kuma don kare Tauhidi da toshe hanyoyin shirka, sai Annabi (SAW) ya shiryar da su kan cewa su siffanta shi da siffofi biyu, waɗanda su ne mafiya ɗaukakar matsayin da bawa ke iya kaiwa, kuma babu wuce gona da iri ko hatsari ga Aƙida a cikinsu, wato: “Bawan Allah kuma manzonsa”.

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (233).

LARABA: DARSI CIKIN FIƘIHU

ABUBUWAN DA KE WARWARE ALWALA

Abubuwan da ke warware alwala su ne abubuwan da suke ɓata ta kuma su sa lalata ta, kuma su abubuwa ne guda shida:

1) **Abin da ke fitowa daga hanyoyin fitsari ko bayan gida**: fitsari, ko bayan gida, ko iska, ko wani abu makamancin haka, kaɗan ne ko dayawa, saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((Ko ɗaya daga cikinku ya dawo daga bayan gida))[1], da kuma faɗin Annabi (SAW): (Sai dai za a yi tsarki ne daga bayan gida da fitsari da barci)[2].

2) **Gushewar hankali:** ta hanyar barci, suma, hauka, ko wani abu makamancin haka, domin wannan na iya zama sanadiyyar fitar kari, kuma haƙiƙa Manzon Allah (SAW) ya ce: (Sai dai bayan gida, da fitsari da kuma barci) [3], kuma nau'in barcin da ke warware alwala shi ne wanda idan mutum ya yi shi hankalinsa ke gushewa, ta yadda bai iya sanin wanɗanda ke kewaye da shi, amma idan barcin mai sama-sama ne, to ba ya warware alwala, domin sahabban (RA), sau dayawa gyangyaɗi kan kama su, kuma su farka su yi salla ba tare da sake alwala ba[4].

3) Taɓa al'aura ba tare da shamaki ba: Dalilinsa faɗin Manzon Allah (SAW): (Duk wanda ya taɓa al'aurarsa, to ya sake yin alwala)[5], da kuma faɗarsa cewa: (Duk wanda ya taɓa farjinsa, to ya sake alwala) [6].

4) Cin naman raƙumi: Dalilinsa kuwa shi ne tambayar da aka yi wa Manzon Allah (SAW): "Shin dole ne mu yi alwala bayan cin naman tumaki? Sai ya ce: "Idan ka ga dama ka yi, idan kuma ka ga dama, kar ka yi", sai ake ce: Shin dole ne mu yi alwala bayan cin

---

[1]. [An-Nisā': 43].
[2]. Nasa'i ne ya rawaito shi (159).
[3]. Nasa'i ya rawaito shi (159).
[4]. Muslim ne ya rawaito shi (376).
[5]. Abu Dawud (181), da Nasa'i (163) ne suka rawaito shi.
[6]. Ibn Maja ne ya rawaito shi (482).

naman raƙumi? Sai ya ce: "Eh, ka yi alwala bayan cin naman rakumi) [1].

5) Fita daga Musulunci: Fita daga Musulunci yana rushe dukkan ayyuka, ciki har da alwala. Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Duk kuwa wanda ya kafirce wa imani, haƙiƙa aikinsa ya rushe, kuma a ranar lahira yana cikin asararru))[2].

Mas'ala: Wanda ya tabbatar da cewa yana da tsarki, sannan ya shiga cikin shakkar samuwar kari ya zai yi:

Ya tabbata daga Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan ɗayanku ya ji wani abu a cikinsa, sai ya yi shakka ko wani abu ya fito daga gare shi ko a'a, to kada ya fita daga masallaci har sai ya ji ƙara ko ya ji warin iska)[3].

Sai wannan hadisin ya yi nuni ga wata babbar ƙa'ida a cikin fikihu wadda take cewa: "Tabbataccen abu ba ya gushewa saboda shakka.

Saboda haka idan musulmi ya tabbatar da cewa yana da tsarki, sai kuma ya shiga cikin shakkar lalacewar alwalarsa, to yana nan da tsarkinsa, domin tsarkin shi ne asali, kuma shi ne abin da ake da tabbas a kai, kuma tabbataccen abu ba ya gushewa saboda gundarin shakka marar tabbas.

Amma akasin haka, idan ya tabbata cewa ya samu kari, sai kuma ya shiga cikin shakka bayan haka, ko ya sake yin alwala ko bai sake ba, to asali shi ne wanzuwar kari, domin shakka ta shiga cikin tsarkin, saboda haka zai yi alwala.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (369).
[2]. [Al-Ma'ida: 5].
[3]. Bukhari (176) da Muslim (362) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

HIJIRA TA FARKO ZUWA HABASHA

Cutarwar Mushrikai ya tsananta ga waɗanda suka yi imani, kuma cin zarafinsu gare su ya ƙaru, kuma salon da suke azabtar da su ya yawaita, musamman bayi da masu rauni, suna jefa wasu a cikin zafi rana mai tsanani, wasu kuma ana dora musu babban dutse a kirjinsu, don haka, idan aka sake shi ba zai iya zama ba saboda iya tsananin raɗaɗin, da sauran nau'o'in azabtarwar da suke musu.

Abubakar siddiq (RA), ya kasance idan ya wuce ta wurin wani bawa da ake cikin azabtar da shi, sai ya saye shi kuma ya 'yanta shi, sai ya 'yanta Bilal da mahaifiyarsa Hamama, da Amir ɗan Fuhaira, da Ummu Ubais, da Zinnira, da Nahdiyya da 'yarta, har sai da mahaifinsa Abu Ƙuhafata ya ce masa: "Yaro na, na ga kana 'yantar da bayi masu rauni, in ma da a ce lokacin da ka yi hakan ka 'yantar da mazaje ne masu ƙarfi waɗanda za su kare ka kuma su tare maka faɗa?" Sai ya ce: "Ya mahaifina! Lallai ni kam akwai abin da nake nema[1], sai wannan aya ta sauka: ((Kuma lallai za a nesantar da mafi taƙawa daga gare ta (wato wuta) () Wanda yake ba da dukiyarsa yana neman tsarkaka))[2].

Kuma da Manzon Allah (SAW) ya ga irin halin da sahabbansa ke ciki na cutarwa da azabtarwa, alhali kuwa ba su da wani ƙarfi da da za su iya kare kansu saboda ƙarancin yawansu da raunin ƙarfinsu, sai ya umurce su da su yi Hijira zuwa ƙasar Habasha domin Allah Ya ba su mafita daga halin da suke ciki.

Sai mutane goma daga cikinsu suka yi hijira, tare da mata biyar, suka fifita zama a ƙasar da ba ta su ba, kuma ba su san ta ba, kuma mai nisa, suna masu jure wahalhalu da haɗurran hanyoyi don kiyaye addininsu.

---

[1]. Asbabun-Nuzul na Wahidi (456).
[2]. [Al-Lail: 27-18].

Mutumin farko da ya yi hijira tare da iyalinsa don kuɓuta da addininsa shi ne Utsmanu ɗan Affān, tare da matarsa Ruƙayya ɗiyar Manzon Allah (SAW). Kuma sun fita ne zuwa Habasha a watan Rajab, shekara ta biyar daga farkon Annabta, suka zauna a can tsawon watanni uku, sannan suka dawo Makka bayan da labari ya bazu cewa mutanen Makka sun Musulunta.

Amma da suka iso kusa da Makka, sai suka gane cewa lamarin ba haka yake ba, kuma azabtarwar mushrikai ma ƙaruwa ta yi ga da'awar Musulunci da waɗanda suka yi imani da ita, saboda haka wasu daga cikinsu suka shiga Makka a ɓoye, wasu kuma suka shiga cikin kariyar wani mutum daga cikin mutanen Makka, sauran kuma suka zaɓi komawa zuwa ƙasar Habasha.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

KHADIJA ‘YAR KHUWAYLID (RA)

❖ Sunanta da Haihuwarta:

Ita ce Khadija 'yar Khuwaylid ɗan Asad Alƙurashiyya, nasabarta tana haɗuwa da ta Annabi (SAW) a wajen kakansu na huɗu, 'Ƙusayyu ɗan Kilab".

An haife ta ne a Makka shekaru goma sha biyar (15) kafin haihuwar Annabi (SAW).

❖ Rayuwarta da Falalarta:

Khadija Allah ya ƙara mata yarda mace ce mai daraja daga kabilar Ƙuraishawa, ta fito ne daga mafi asalin gidaje wajen nasabarsu da darajarsu, da ƙimarsu.

Annabi (SAW) ya lissafa ta daga cikin mafiya alherin matan duniya[1].

Ta kasance (RA) mawadaciya ce kuma 'yar kasuwa, kuma tana da kaso mai girma na kaifin hankali, da basira, da zurfin tunani, da hangen nesa, saboda haka ta zaɓi Manzon Allah (SAW) ya zama mijinta, ta kuma kasance mata ta gari ga mijinta, kuma ita ce farkon matan Annabi (SAW), kuma ita ce ta farkon macen da ta yi imani da shi, ita ce kuma ta farkon wacce ta goyi bayansa ta taimake shi a farkon da'awarsa, domin haƙiƙa ta kasance tana ba shi kariya daga kafiran Ƙuraishawa, kuma tana rarrashinsa da kanta da dukiyarta.

Kuma a lokacin da aka yi Banu Hashim ƙawanya, Khadija ta yanke shawarar barin ƙabilarta Banu Asad, wacce take da ƙarfi da kariya, domin ta bi mijinta (SAW) da waɗanda suke tare da shi daga Banu Hashim, don ta sha irin wahalar da suke sha na yunwa, da rauni, da ƙunci.

---

[1]. Bukhari (3815) da Muslim (2430) ne suka rawaito shi.

Annabi (SAW) ya samu ’ya’ya daga gare ta kamar: Alƙasim, da Abdullah, waɗannan sun rasu tun suna jarirai, da Zainab, da Ummu Kulsum, da Faɗima.

Wata rana Mala’ika Jibril ya zo wurin Annabi (SAW), ya ce masa: (Ya Manzon Allah! Ga Khadija nan ta zo maka da wani a kushi wanda ke ɗauke da miya; idan ta zo maka, to ka isar mata gaisuwa daga Ubangijinta da kuma ni, kuma ka yi mata bushara da gida a aljanna, wanda aka gina shi da lu’ulu’u, ba hayaniya a cikinsa, kuma ba wahala)[1].

❖ Rasuwarta:

Khadija 'yar Khuwaylid ta rasu ne a watan Ramadan, shekaru uku kafin Hijira, tana da shekaru 65 a lokacin rasuwarta.

Kuma Manzon Allah (SAW) ne ya binne ta a wata unguwa mai suna Hajun, kuma wannan ya faru ne bayan rasuwar Baffan Annabi, Abu Ɗalib da watanni uku, sai abubuwan baƙin ciki da masifu suka yi ta faruwa ga Manzon Allah (SAW).

[1]. Bukhari (3820) da Muslim (24320) ne suka rawaito shi.

Auna fahimtarka a darusan mako na 11			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ma'anar fadin Allah Madaukaki: (Khusr)?**		b
	a. Mutuwa	b. Asara da halaka	c. Ƙarancin dukiya
Darasin Hadisi	**Tambaya: Mene ne manyan zunubai?**		c
	a. Dukkan abubuwan da aka hana.	b. Duk abin da ba shirka ba.	c. Dukkan abin da akwai haddi a kansa a duniya, ko alƙawarin narko a lahira, ko aka haɗa aikata shi da la'ana ko fushi.
Darasin Aƙida	**Tambaya: Me ya sa Annabi (SAW) ya ƙyamaci yabawar Sahabbai gare shi da cewa: "Kai ne shugabarmu, kuma Mafifici a cikinmu, kuma mafi girma a cikinmu?**		c
	a. Domin tawali'u.	b. Don girmama Sahabbansa.	c. Don kare tauhidi da toshe hanyoyin shirka.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Barcin da yake warware alwala shi ne:**		b
	a. Kowanne barci har da gyangyaɗi.	b. Barci mai nauyi da mutum ba ya sanin abin da yake kewaye da shi.	c. Barcin da ya kai ga rufe idanu.
Darasin Sira	**Tambaya: Sahabbai sun yi hijira zuwa Habasha ne a shekara ta:**		b
	a. 3 bayan aiko Annabi.	b. 5 bayan aiko Annabi.	c. 7 bayan aiko Annabi.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Khadija Allah ya ƙara mata yarda tana dangantuwa ne zuwa ƙabilar Banu:**		b
	a. Makhzum.	b. Hashim.	c. Asad.

MAKO NA GOMA SHA BIYU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-HUMAZA

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
وَيۡلٞ لِّكُلِّ هُمَزَةٖ لُّمَزَةٍ ١ ٱلَّذِي جَمَعَ مَالٗا وَعَدَّدَهُۥ ٢ يَحۡسَبُ أَنَّ مَالَهُۥٓ أَخۡلَدَهُۥ ٣ كَلَّاۖ
لَيُنۢبَذَنَّ فِي ٱلۡحُطَمَةِ ٤ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡحُطَمَةُ ٥ نَارُ ٱللَّهِ ٱلۡمُوقَدَةُ ٦ ٱلَّتِي تَطَّلِعُ عَلَى
ٱلۡأَفۡـِٔدَةِ ٧ إِنَّهَا عَلَيۡهِم مُّؤۡصَدَةٞ ٨ فِي عَمَدٖ مُّمَدَّدَةِۭ ٩﴾

❖ Fassara:

1. Tsananin azaba ya tabbata ga duk wani mai yawan ƙyafice mai yawan suka.
2. Wanda ya tara dukiya ya ƙididdige ta.
3. Yana zaton cewa dukiyarsa za ta dawwamar da shi.
4. Faufau! Tabbas lallai sai an jefa shi cikin (wutar) 'Huɗama'.
5. Me kuma ya sanar da kai irin girman 'Huɗama'?
6. Wuta ce ta Allah abar hurawa.
7. Wadda take mamaye zukata.
8. Lallai ita abar kullewa ce da su.
9. A cikin ginshiƙai miƙaƙƙu (da suka kewaye ta).

❖ Abin da Surar ta Ƙunsa:

Gargaɗi game da izgili ga muminai saboda ruɗuwa da yawan dukiya.

❖ Bakin Kalmomi:

ويل	Wailun	Gargadi da bala'i, da tsananin azaba
همزة	Humazah	Wanda yake raina mutane ta hanyar aikinsa ko ishararsa
لمزة	Lumazah	Wanda yake raina mutane da maganarsa

كلا	Kalla	Lamarin ba kamar yadda ake zato ba ne
لينبذن	La Yunbazanna	Tabbas za a jefa shi
الحطمة	Al-Hudamah	Wuta ce da take raga-raga da dukkan abin da aka jefa a cikinta
تطلع على الأفئدة	Tadd̈ali'u Alal-Af'idah	Wutar tana shiga cikin jiki har ta kai ga zukata
مؤصدة	Mu'sadah	Rufaffa kuma kullalla
في عمد ممددة	Fi Amadin Mumaddadah	An kulle ƙofofinta da turaku masu tsayi domin kada su fita daga cikinta

❖ Ma'anar Surar a Dunƙule:

A cikin wannan surar, Ubangiji Mai girma da ɗaukaka ya yi alƙawarin narkon azaba mai raɗaɗi ga dukkan mai giba mai yawan aibata mutane, wanda ba shi da wani buri sai tara dukiya da ƙidaya ta, yana tunanin cewa yawan dukiyarsa zai sa ba zai mutu ba, to sakamakon sa kuwa shi ne a jefa shi cikin wuta mai tsananin ƙuna da ruruwa, wacce take ƙona dukkan abin da aka jefa a cikinta, kuma take ƙona jiki har sai ta kai ga zuwa zukata, kuma an rufe ƙofofinta gaba ɗaya a gare su, ba su da hanyar fita.

❖ Abubuwan da za mu koya daga Surar:

1. Haramcin izgili da ba'a ga wasu, domin hakan yana haifar da gaba da ƙiyayya tsakanin mutane.
2. Wajibi ne mutum kada ya rudu da dukiyarsa, domin babu hanyar da mutum zai dawwama a duniya, kuma ba shi da makawa daga mutuwa da sakamako ba.
3. Gargaɗi game da rowa da shagaltuwa da tara dukiya da kirga ta.
4. Alƙawarin narko mai tsanani da wuta mai ruruwa da aka rufe ƙofofinta, wacce aka tanada ga wanda ke da waɗannan siffofin marasa kyau.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

AYYUKAN DA AMFANINSU KE CI GABA DA GUDANA BAYAN MUTUWA

An karɓo daaga Abu Huraira (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Idan mutum ya mutu, dukkan ayyukansa suna yankewa, sai dai abubuwa uku: sadaka mai gudana, ko ilimi da ake amfana da shi, ko ɗa nagari da yake yi masa addu'a**)[1].

❖ Sharhi:

Allah Ya sanya duniya ta zamto gida na aiki, inda bayinsa suke guzurin abin da zai amfane su a lahira, kuma da sannu waɗanda suka yi sakaci za su yi nadama idan suka bar wannan duniya ba tare da sun tanadi abin da zai sa su farin ciki a lahira ba, domin da mutuwa aiki ke yankewa, kuma a rufe ƙofar tuba, saboda haka, wani abu na lada ba zai ƙara isa ga bawa ba, sai dai idan ya bar abubuwa uku waɗanda Allah - cikin falalarsa - Ya sanya musulmi ya ci gaba da samun ladansu bayan mutuwarsa, waɗannan kuwa su ne:

Na farko: Sadaqa mai gudana bayan mutuwa, wato wacce amfaninta ke ci gaba, kuma ta ƙunshi dukkan wani abin da musulmi ya bari a matsayin waƙafi, kamar fili, kayan amfani, dabba, gina masallaci, ko tona rijiyar.

Na biyu: Ilimin shari'a wanda ake ci gaba da amfana da shi bayan mutuwar mutum, kamar ya koyar da wani mutum, ko rubuta littafi, ko ya yi waƙafi da Alƙur'ani, sai mutane su cigaba da amfani da shi bayan mutuwarsa, ko ya yaɗa ilimin ta hanyoyin zamani da ke adana ilimi a cikinsu har zuwa lokacin da Allah Ya so.

Na uku: Ɗa nagari, wanda ya ƙunshi ɗa na tsatson mutum, ko jika, mace ko namiji; to lallai mahaifinsa na amfana da nagartarsa da addu'arsa ga iyayensa, kuma an keɓance ɗa ne ban da waninsa

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (1631).

domin galibi shi ne ke cigaba da yi wa iyayensa addu’a bayan rasuwarsu.

Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Falalar sadaka mai gudana: da kuma gudanar ladanta ga bawa a kabarinsa.
2. Falalar koyar da ilimi da yaɗa shi: ta kowace irin hanya.
3. Cewa lallai ladan sadaka yana isa ga mamaci, haka ma addu’a da ilimi mai amfani.
4. Falalar aure domin fatn samun ɗa nagari.
5. Muhimmancin kwaɗaituwa wajen tarbiyyar yara kyakkyawar tarbiyya, domin a amfana da nagartarsu da addu'arsu.

TALATA: DARAS CIKIN AƘIDA

GINSHIƘAI DA AKE CIRATO ADDINI DAGA CIKINSU

Ahlus-Sunnah Wal-Jama'a suna da ginshiƙai da suke cirato addininsu daga cikinsu, kuma da su suke sanin abin da Ubangijinsu yake nufinsu da shi.

Waɗannan ginshiƙai guda uku ne:

Ginshiƙi na farko: Shi ne littafin Allah Maɗaukaki.

Ginshiƙi na biyu: Shi ne ingantacciyar Sunnar Annabi (SAW).

Ginshiƙi na uku: Shi ne Ijma'in magabata na ƙwarai.

Waɗannan ginshiƙai guda uku, su ne ginshiƙan da ake cirato addini daga gare su, kuma su ne mashayar shari'a, kuma tushen addinin Musulunci, kuma hujja wajen tabbatar da akidunsa, da ibadodinsa, da halayensa da ladubbansa, wannan kuwa ɗaya ce daga cikin abubuwan da Ahlus-Sunnah wal-Jama'a suka keɓanta da su: Ba sa karɓar akidarsu sai daga ginshiƙi mai ƙarfi da hujja tabbtacciya, ba daga son zuciya, da ra'ayoyi, da mafarkai da makarantansu ba.

Kuma dalilin da ke nuni kan tabbacin waɗannan ginshiƙai na Shari'a shi ne: Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma duk wani abu da kuka yi saɓani a kansa, to sai ku mai da hukuncinsa ga Allah. Wannan Shi ne Allah Ubangijina, gare Shi kawai na dogara, kuma wurinsa kawai nake mayar da al'amarina))[1]. Kuma Ya ce: ((Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi ɗa'a ga Allah, kuma ku yi ɗa'a ga Manzo da kuma majiɓinta lamarinku. Idan kun yi jayayya a kan wani abu, to ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzonsa in kun kasance kun yi imani da Allah da ranar ƙarshe. Wannan shi ne mafi alheri, kuma mafi kyan makoma))[2].

Kuma dalilin da ke tabbatar da Ijma'in magabata a matsayin Hujja shi ne faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma duk wanda yake saɓa wa

[1]. [As-Shura: 10].
[2]. [An-Nisa: 59].

wannan Manzo bayan shiriya ta bayyana a gare shi, yake kuma bin tafarkin da ba na muminai ba, to za Mu bar shi da abin da ya ɗaukar wa kansa, sannan Mu shigar da shi wutar Jahannama; makoma kuwa ta munana)) [1].

Abin da ake nufi da Magabata: Su ne mutanen ƙarni uku na farko waɗanda aka ambata a Hadisin Annabi (SAW) cewa: (Mafi alherin mutane su ne na ƙarnina, sai waɗanda suka biyo bayansu, sannan waɗanda suka biyo bayansu)[2].

Saboda haka, Ahlus-Sunnah suna girmama magabata na ƙwarai, kuma suna koma wa ga maganganunsu da fahimtarsu wajen fahimtar addini da nassoshinsa, musamman sahabbai Allah ya ƙara musu yarda, domin su ne mafiya alherin mutane, kuma mafiya kusa da tushen annabta, kuma mafiya sanin abin da Allah da Manzonsa suke nufi, musamman bayan yaɗuwar bidi'o'i, da ƙarancin ilimi, da lalacewar fahimta da nesantar sunna.

❋ **Amfanin sanin ginshiƙan da ake cirato addinini daga gare su.**

1. Girmama nassoshin shari'a da miƙa wuya gare su.
2. Kuɓuta daga ruɗani da rikice-rikice da ke tasowa daga bambancin ginshiƙai.
3. Ingancin fahimtar nassoshi, da isa zuwa fahimtar abin da Allah da Manzonsa suke nufi.
4. Tsira daga karkacewa cikin aƙida da aiki waɗanda son zuciya da shaiɗan ke haifarwa.

[1]. [An-Nisa: 115].
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (2652).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SHAFA A KAN HUFFI

❖ Hukuncin shafar Huffi:

Lallai addinin Musulunci addini ne na sauƙi da rangwame, yana sanya wa kowane abu hukunce-hukuncen da suka dace da shi, waɗanda ke tabbatar da maslaha da kawar da wahala.

Daga cikin waɗannan hukunce-hukunce akwai shafar huffi, haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya halatta shafar kowane huffi, da fata aka yi shi, ko gashi, ko kyalle, ko wani abu na daban, a halin tafiya ko zama, domin shi wani rangwame ne daga Allah Mai girma da ɗaukaka da sauƙi daga gare Shi ga bayinsa.

Imamu Ahmad Allah Ya masa rahama ya ce: "Ba ni da wani shakka game da shafar huffi, domin akwai Hadisai daga Annabi (SAW) guda arba'in da suka tabbatar da shi [1].

Daga cikin waɗannan Hadisan akwai Hadisin Mugira ɗan Shu'uba (RA) ya ce: Na kasance tare da Annabi (SAW) a halin tafiya, sai na miƙa hannu don in cire masa Huffansa, sai ya ce: (Ka bar su, domin na saka su ne a halin tsarki) sai ya yi shafa a kansu" [2].

❖ Sharuɗɗan shafa a kan huffi:

1. Dole ne ya ssanya su yana da tsarki.
2. Dole ne ya rufe ƙafafu gaba ɗaya; domin idan wani ɓangare na ƙafar ya bayyana, ko kuma abin da aka sa bai kai idon sawu ba, to shafar bai inganta ba.
3. Dole ne ya kasance halal ne; don haka, ba ya halatta a shafi huffin da aka sata, ko safar da aka yi ta da alhariri ga namiji, domin babu rangwame cikin amfani da abin da ya ƙunshi saɓo.
4. Dole ne abin da aka sa ya kasance mai tsarki, domin ba a shafar najasa; kamar abin da aka yi daga fatar dabbar da ta mutu ko kare.

---

[1]. Al-Mughni (1/360).
[2]. Bukhari (206) da Muslim (274) ne suka rwaito shi.

5. Dole ne a yi shafar a cikin lokaci ƙayyadadde; kamar yadda Aliyu (RA) ya ce: "Manzon Allah (SAW) ya sanya kwana uku da dararrakinsu ga matafiyi, da kwana ɗaya da dare ɗaya ga mazaunin gida”[1].

❖ **Yadda ake shafar da sifarta:**

Abin da yake wajaba shi ne shafar wajen huffi, wato samansa; don haka, ba a shar'anta shafar ƙasan huffi ko bayansa ba, saboda faɗin Aliyu (RA) cewa: "Da addini ra’ayi ne, da ƙasan huffi shi ya fi cancantar a shafe shi fiye da samansa, sai dai haƙiƙa na ga Annabi (SAW) yana shafar saman huffinsa)[2]. Kuma ana shafar ƙafar dama ce da hannun dama, ƙafar hagu da hannun hagu, sau ɗaya tak, kuma yana buɗe tsakanin yatsunsa yayin shafar.

❋ **Mas'ala: Idan mutum ya sanya safa guda biyu:**

Idan mutum ya sanya safa guda biyu a tare (ɗaya kan ɗaya), kuma yana da tsarki, to ya halatta ya shafi ta sama daga cikinsu, domin ya sanya shi ne yana da tsarki.

Amma idan ya fara saka na ƙasa, sai ya samu kari, sannan ya sanya ta sama, ko ya fara shafar ta ƙasa, to ba zai shafi ta sama ba.

❖ **Abubuwan da ke lalata shafar a kan huffi:**

Shafar huffi yana lalacewa, kuma dole a cire shi a waɗannan halaye:

1. Idan mutum ya sami kari babba da yake wajabta wanka.
2. Idan an cire huffin guda biyu ko ɗaya daga cikinsu, ko kuma wani ɓangare mai girma na ƙafar mutum ya bayyana.
3. Idan lokacin da aka ƙayyade don shafar ya ƙare.

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (85).
[2]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (162).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

MUSULUNTAR HAMZA DA UMAR (RA)

A wata rana Fir'aunan wannan al’umma, wato Abu Jahal, ya wuce kusa da Manzon Allah (SAW) a wurin dutsen Safa, sai ya cutar da shi kuma ya ci mutuncinsa, amma Manzon Allah (SAW) bai mayar masa da martani ba, sai Abu Jahal ya jefe shi da dutse, sai ya fasa masa kai har jini ya zubo daga kan Manzon Allah (SAW), sai Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib (RA) ya ji labari, bayan ya dawo daga farauta, nan take ya garzaya wajen Abu Jahl da sauri, bai saurari kowa ba, sai da ya isa gare shi, ya ce masa: "Shin kana zagin ɗan ɗan’uwana alhali ni ma ina kan addininsa!", sai ya dake shi da ƙoƙon baka, har ya masa mummunan rauni[1], don haka, farkon Musuluncin Hamza ya kasance ne saboda ƙabilanci, daga baya sai Allah ya buɗe masa ƙirji, ya sadaukar da kansa ga Musulunci, kuma Musulmi suka samu ƙwarin gwiwa da shigowarsa, kuma mushrikai suka rage cin zarafin da suka kasance suna yi.

Kuma bayan kwana uku da Musuluntar Hamza (RA), sai Umar ya fito da takobinsa a zare da nufin ya kashe Annabi (SAW), sai wani mutum ya haɗu da shi ya ce masa: "Ya kai Umar, ina ka nufa ne?” Sai ya ce: "So nake in kashe Muhammad", sai mutumin ya ce masa: “Shin ba zan nuna maka abin da ya fi wannan ban mamaki ba? Lallai ‘yar’uwarka da mijinta Sa'idu ɗan Zaid sun musulunta, sun bar addininka da kake kai". Sai Umar ya canza hanya, cikin fushi ya nufi gidan ‘yar’uwarsa, a lokacin Khabbab ɗan Aratt yana gidan tare da su, kuma yana karanta wani ɓangare daga cikin suratun Ɗaha daga wata takarda, sai Umar ya ji sautin karatun na tashi, sai ya ƙwanƙwasa ƙofar da ƙarfi, ya shiga gidan, ya ce wa Sa'idu: "Bisa

[1]. Hilyatul-Awliya (1/73)

dukkan alamu kun fice daga addininku?” Sai Sa'id ya amsa da cewa: "Ka ba ni labari idan gaskiya tana a cikin wani addinin da ba naka fa, shin za ka iya barinsa?” sai Umar ya dira kansa ya buge shi, sai ‘yar’uwarsa ta zo ta janye shi, sai Umar ya mare ta, har sai da jini ya zubo daga fuskarta.

Bai jima da yin hakan ba, sa zuciyarsa ta yi sanyi, sai ya ce: "Ku ba ni wannan littafin da ke tare da ku", sai suka ƙi ba shi har sai ya yi wanka, sai Umar ya yi wanka sannan ya karanta littafin, kuma yayin da ya ji Khabbab ya ji yadda Umar yake karatun Al-ƙur’ani, sai ya ce masa: "Ka yi bushara, ya kai Umar! Ina fatan addu’ar Manzon Allah (SAW) ta tabbata a kanka: (Ya Allah, Ka ƙarfafa Musulunci da wanda ka fi so daga cikin mutane biyu masu suna Umar; Abu Jahal ko Umar ɗan Khaɗɗab)[1]. Sai Umar ya tafi zuwa gidan Arƙam, ya shiga wurin Manzon Allah (SAW), ya bayyana Musuluncinsa, sai mutanen da ke gidan suka yi kabbara, har sai da waɗanda ke cikin Masallaci suka ji sautin, kuma a lokacin Umar yana ɗan shekara ashirin da shida ne.

Shigowarsa cikin Musulunci ya zama nasara da ƙarfi ga Musulmi, Abdullahi ɗan Mas’ud (RA) ya ce: "Musuluntar Umar ya kasance buɗi ne ga Musulmi, hijirarsa ta kasance zama nasara gare su, shugabancinsa ya kasance rahama, kuma ina rantsuwa da Allah! Mun kasance ba mu iya yin salla a gefen Ka’aba a fili, har sai da Umar ya musulunta, ya yaƙe su har sai da suka bar mu muna yin salla)[2].

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3681).
[2]. Al-Bidaya Wan-Nihaya (3/79).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SAUDATU 'YAR ZAM‘A (RA)

❖ Sunanta da Haihuwarta:

Ita ce Uwar muminai Saudatu 'yar Zam‘a ɗan Ƙaisu ɗan Abdu Shams Baƙurashiyya ‘yar ƙabilar Banu Amir, ana yi mata inkiya da Ummul-Aswad.

An haife ta ne – Allah ya ƙara mata yarda – a Makka.

❖ Rayuwarta da Falalarta:

Ta kasance (RA) mai kyakkyawar halayya, mai daɗin zama, mai daraja mai hankali, ita ce mace ta farko da Annabi (SAW) ya aura bayan rasuwar Khadija (RA), sai ya yi hijira tare da ita zuwa Madina, ta zauna tare da shi kusan shekaru uku kafin ya aure A'isha (RA).

Ta kasance daga cikin mata da suka yi hijira zuwa Habasha, kuma ta halarci yaƙin Khaibar da Hajjin bankwana tare da Manzon Allah (SAW), kuma bayan Manzon Allah (SAW) ya bar duniya, ta lizimci gidanta, kuma bata sake aikin Hajji ba har ta rasu, kuma ta kasance tana cewa: "Na yi aikin Hajji da Umara, don haka, zan lizimci zaman gida kamar yadda Allah Mai girma da ɗaukaka Ya umurce ni” [1].

Ta kasance (RA) mai karamci, mai yan kyauta, tana son yin sadaka, har Umar ɗan al-Khaɗɗab (RA) ya kasance idan ya aiko mata da kuɗi, sai ta rarraba shi ga matalauta[2].

Kuma ya ishe ta girman falala cewa ita ce mace ɗaya da Uwar muminai A’isha (RA) take son ta zama mai irin halayenta da hanyar rayuwarta[3].

---

[1]. Aɗ-Ɗbaƙatul-Kubra na Ibnu Sa‘ad (8/55).
[2]. Al-Bidayah wan-Nihayah (8/245).
[3]. Muslim ne ya rawaito shi (1463).

Kuma daga cikin kyawawan ayyukanta (RA) akwai cewa ta ba da kwananta ga A'isha (RA) cikin dadîn ranta saboda neman yardar Manzon Allah (SAW), bayan ta tsufa[1].

❖ Rasuwarta:

Ta rasu ne a Madina, a ƙarshen zamanin mulkin Umar (RA) bayan ta yi wasiyya da a bai wa A’isha ɗaƙinta (RA).

[1]. Bukhari (1463) da Muslim (5212) ne ya rawaito shi.

Auna fahimtarka a darusan mako na 12			**Amsa ta ƙwarai**
Darasin Tafsiri	**Tambaya: “Allumaza” shi ne mutumin da:**		A
	a. Mai cin mutuncin mutane da maganarsa.	b. Mai cin mutuncin mutane da aikinsa.	c. Mai yi wa mutane makirci da kaidinsa.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Daga cikin abin da ke amfanar mutum bayan mutuwarsa akwai:**		C
	a. Gado mai yawa.	b. Babban matsayi.	c. Ilimi mai amfani
Darasin Aƙida	**Tambaya: Daga cikin ginshiƙan cirato addini a wajen Ahlus-Sunnah akwai?**		B
	a. Mafarke-Mafarke.	b. Ijma’in magabata na ƙwarai.	c. Hankali.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Daga cikin sharuɗɗan shafa a kan huffi akwai:**		B
	a. Shigowar lokacin salla.	b. Huffin ya kasance mai tsarki.	c. Sallar ta kasance ta farilla.
Darasin Sira	**Tambaya: Umar ɗan Khaɗɗab ya Musulunta bayan musuluntar Hamza da:**		C
	a. Wata ɗaya	b. Sati ɗaya	c. Kwanaki uku
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin falalar Sauda (RA) akwai cewa ita ce:**		C
	a. Mafi ilimi daga cikin uyayen Muminai.	b. Annabi (SAW) bai aure mace budurwa ba ban da ita.	c. Ta zauna tare da Annabi (SAW) ita kaɗai tsawon shekaru uku.

MAKO NA GOMA SHA UKU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-FIL

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِأَصۡحَٰبِ ٱلۡفِيلِ ١ أَلَمۡ يَجۡعَلۡ كَيۡدَهُمۡ فِي تَضۡلِيلٖ ٢ وَأَرۡسَلَ
عَلَيۡهِمۡ طَيۡرًا أَبَابِيلَ ٣ تَرۡمِيهِم بِحِجَارَةٖ مِّن سِجِّيلٖ ٤ فَجَعَلَهُمۡ كَعَصۡفٖ مَّأۡكُولِۭ ٥﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai.

1. Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya yi wa ma'abota giwa ba?
2. Ashe bai mayar da makircinsu cikin watsewa ba?
3. Ya kuma aiko musu da tsuntsaye dodo-dodo?
4. Suna jifan su da duwatsu na ƙonanniyar laka?
5. Sai da Ya mayar da su kamar karmami da aka cinye?

❖ saƙon da Surar ta Ƙunsa:

Bayani game da ikon Allah da tsananin damƙarsa ga masu kaidi ga Ɗakinsa mai alfarma.

❖ Baƙin Kalmomi:

أَلَمْ تَرَ	Alam tara	Ashe ba ka sani ba?
أصحاب الفِيل	Ashabil-fīl	Abrahatul-Habashi da rundunarsa waɗanda suka yi niyyar rusa Ka'aba
كَيْدَهُمْ	Kaydahum	Makircinsu da shirin da suka yi don rusa Ka'aba
تَضْلِيل	Tadlil	Asara da lalacewa
أَبَابِيل	Ababil	Gungun tsuntsaye masu bibiyar juna
سجيل	Sijjil	Taɓo da aka dafa

كعصف مأكول	Ka’asfin ma’kul	Kamar karmamin da dabbobi suka ci suka bari

❖ Ma’anar Surar a Dunƙule:

Suratul-Fil sura ce daga cikin surori da suka sauka a Makka, ta ƙunshi bayani ne game da ikon Allah Mai girma da ɗaukaka wajen kare Ɗakinsa mai alfarma da kuma tsare shi, domin kuwa rundunar ma'abota giwa waɗanda Nasara ne da suka mulki ƙasar Yemen, shugabansu Abrahatal-Ashram ya gina wani gida a Sana’a, sai ya kira Larabawa da su yi hajji a cikinsa a maimakon su riƙa yin hajjinsu a Ɗakin Ka'aba mai alfarma.

Manufar da ta sa ya yi haka ita ce girmama ƙasarsa, da kuma karkatar da harkokin kasuwanci da ribar sana’o’i daga Makka zuwa Yaman, a lokacin da ya gama gina cocinsa, sai wani mutum Baƙuraishe ya zo ya ɓata bangon cocin da ba haya kuma ya gudu, yayin da Abrahata ya ji labarin haka sai ya fusata ƙwarai, ya shirya rundunar Habashawa wadda Larabawa ba za su iya fuskantar ta da yaƙi ba, suka tafi don su yaƙi Makka su rusa Ka’aba, yayin da suka iso kusa da Makka, sai Allah Ya aiko musu da tsuntsaye masu yawa, wato tsuntsaye baƙaƙe gungu-gungu da suka taso daga teku, kowanne tsuntsu yana ɗauke da duwatsu na ƙonanniyar laka guda uku: Biyu a ƙafafunsa da ɗaya a bakinsa, sai suka hallaka su, suka darkake su, Allah Ya mayar musu da makircinsu, ba su sami wani alheri ba, wannan kuwa wata alama ce ga mutane game da yadda Allah Maɗaukaki Ya kare Ɗakinsa mai girma, kuma wannan lamari ya faru ne kwanaki hamsin kafin haihuwar Annabi (SAW), kuma ya kasance daga cikin abubuwan ban mamaki da suka gabaci haihuwarsa da kimtsin aiko sa a matsayin annabi.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1. Kariyar Allah Maɗaukaki ga Ɗakinsa mai alfarma, da kuma damƙarsa ga masu yi masa kaidi.

2. Tunatar da Ƙuraishawa game da ni’imar Allah Maɗaukaki a gare su, ta yadda suka kasance makwabta ga Ɗakin Allah wanda hakan ya samar musu da tsaro da ɗaukakar matsayinsu.
3. Cewa lallai dukkan wani makirci ko kaidi da aka yi ba bisa gaskiya ba, to zai koma bala'i ne da hasara ga mai shi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

KWAƊAITARWA GAME DA YAFIYA

DA ƘANƘAN DA KAI

An karɓo daga Abu Huraira (RA), ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Sadaka ba ta taɓa rage wata dukiya ba, kuma Allah ba Ya ƙara wa bawa ta dalilin afuwa face ɗaukaka, kuma babu wanda zai yi tawali'u saboda Allah face Allah Ya ɗaukaka shi**)[1].

❖ Sharhi:

Wannan hadisin ya ƙunshi ambaton falalar wasu ayyuka guda uku daga cikin mafiya girman ibadodi:

Na farko: Sadaka cewa lallai ba ta rage dukiyar mutum, bari dai, ita ƙari ce da albarka, da bunƙasa, da tsari da kariya gare shi daga masifu.

Na biyu: Yafiya ga masu kuskure, cewa lallai ba ya haifar da ƙasƙanci ko wulakanci, bari dai, shi ne asalin ɗaukaka soboda duk wanda aka san shi yin afuwa, da barin kama mutane da laifi ko zarginsu, to yana samun girma da matsayi a zukatan mutane, kuma zai ƙara ɗaukaka da daraja a duniya da lahira.

Na uku: Tawali'u, cewa ba ƙasƙanci ba ne kamar yadda wasu ke tunani, bari dai, Allah Maɗaukaki ne ke ɗaukaka ma'abocinsa, kuma duk wanda ya ƙasƙantar da kansa ga Allah, kuma ya gurfana a gabansa, kuma ya kasance mai saukin hali ga mutane, makusanci gare su kuma mai taushin mu'amala tare da su, to Allah zai ƙara masa ɗaukaka a duniya, kuma Ya sa mutane su ƙaunace shi a zukata, kuma Ya ba shi matsayi mai girma a aljanna.

Sai wannan hadisin ya tattaro ƙofofin kyautatawa gaba ɗaya: kama daga sadaka, ka ga ɗaya daga cikinsu mai kyautatawa ne da dukiyarsa da taimakon mabuƙata, ɗayan kuma mai kyautatawa ne ta

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2588).

hanyar yafiya ga laifuffukan masu kuskure, ɗayan kuma mai kyautatawa ne ta hanyar haƙuri, tawali'u da kyakkyawan hali ga mutane gaba ɗaya, kuma dukkansu su ukun sun wadaci mutane da kyakkyawan hali da taimako, saboda haka sai Allah Ya ɗaukaka su a duniya, tare da abin da Ya tanadar musu na lada a lahira.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1. Falalar sadaka, da bayanin tasirinta ga musulmi ga kansa da dukiyarsa.
2. Falalar yafiya, da manta laifi, da ramawa da abin da ya fi kyawu, da kuma cewa hakan sababi ne na samun ɗaukaka da daraja.
3. Falalar tawali'u, wanda yake haifar da ɗaukaka a duniya a tsakanin mutane, da lada mai girma a lahira.
4. Cewa lallai falalar da aka yi alkawari tana tabbata ne ga wanda ya aikata waɗannan ayyuka saboda Allah kaɗai, ba don riya ba; domin Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya nuna tawali'u saboda Allah, to Allah Zai ɗaukaka shi).
5. Cewa lallai ɗaukaka da daraja suna hannun Allah - tsarki ya tabbata a gare Shi - ne kawai, kuma Shi ke ba wa wanda Ya ga dama.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

GINSHIƘAN AƘIDAR MUSULUNCI

Ginshiƙan Aƙidar Musulunci: Su ne ginshiƙan imani da rukunnansa guda shida, waɗanda Allah Maɗaukaki Ya ambace su a cikin Littafinsa, kuma Manzon Allah (SAW) ya ambace su a cikin sunnarsa.

Su ne: Imani da Allah, da Mala'ikunsa, da littattafansa, da Manzanninsa, da ranar ƙarshe, da ƙaddara ta alheri da ta sharri.

❁ **Waɗannan ginshiƙai guda shida su ne aslin addini saboda dalilai guda biyu:**

- **Na farko:** Lallai imanin bawa ba ya inganta sai bayan ya yi imani da dukkaninsu gaba ɗaya.
- **Na biyu:** Lallai dukkan mas'alolin aƙida da bayananta suna fitowa ne daga waɗannan ginshiƙai guda shida.

❁ **Dalilansu:**

Dalilai masu yawa daga Alƙur'ani da na sunna sun zo game da bayanin rukuna Musulunci, daga cikinsu akwai:

- Faɗin Allah Maɗaukaki: ((Ba wai aikin ɗa'a shi ne ku juyar da fuskokinku mahudar rana ko mafaɗarta ba; sai dai aikin ɗa'a shi ne, wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira da mala'iku da littattafai da annabawa))[1].
- Da Faɗinsa cewa: ((Lallai Mu, kowane abu Mun halitta shi da ƙaddara))[2].
- Da kuma faɗinsa: ((Ya kuma halicci kowanne abu, sannan Ya ajiye shi a irin gwargwadon da ya dace da shi))[3].

Kuma an karɓo daga Umar (RA) ya ce: Wata rana muna zaune wurin Manzon Allah (SAW), Sai wani mutum ya ɓullo mana, mai tsananin

---

1. [Al-Baƙarah: 177].
2. [Al-Ƙamar: 49].
3. [Al-Furƙan: 2].

farin tufafi, mai tsananin baƙin gashi, babu wata alamar tafiya a tare da shi, kuma wanda ya san shi daga cikinmu, har ya zauna kusa da Annabi (SAW); sai ya jingina guiwoyinsa a kan guiwoyinsa, kuma ya ɗaura tafukan hannayensa a kan cinyoyinsa, ya ce: Ya Muhammad, ba ni labari game da Musulunci? Ya ce: Musulunci shi ne ka shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma Annabi Muhammadu Manzon Allah ne, kuma ka tsayar da salla, kuma ka ba da zakka, kuma ka yi azumin watan Ramadan, kuma ka yi hajjin Ɗakin Allah idan ka samu ikon zuwa gare shi, sai yace: Ka yi gaskiya, Sai muka yi mamakinsa yana tambayarsa kuma yana gasgata shi. Sai yace: ka ba ni labari a game da imani? Ya ce: Ka yi imani da Allah, da Mala'ikunsa, da Littatafansa, da ManzanninSa, kuma ka yi imani da ƙaddara alherinta da sharrinta. Ya ce: To ka ba ni labari a game da "Ihsani"? Sai yace: Shi ne ka bauta wa Allah kamar ka na ganin sa, domin in kai ba ka ganinsa, to shi ya na ganin ka. Ya ce: To ka ba ni labari game tashin alƙiyama? Sai ya ce: Wanda a ke tambayarsa a game da ita bai fi wanda ya yi tambayar sani ba. Sai ya ce: To, ka ba ni labarin alamominta? Sai ya ce: Baiwa ta haifi uwar gijiyarta, kuma za ku ga marasa takalma, marasa tufafi, masu kiwon dabbobi suna gina manyan gidaje. Ya ce: Sannan sai ya tafi, sai na zauna na wani lokaci, Sa'annan sai ya ce: Ya kai Umar, shin ka san wane ne mai wannan tambayar? Sai na ce: Allah da Manzonsa Su ka fi sani. Sai yace: Lallai Mala'ika Jibrilu ne, ya zo muku ne domin ya karantar da ku addininku"[1].

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (8).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

WANKAN TSARKI

Wanka yana wajaba a wasu keɓantattun halaye, kuma ana so ya yi a wasu halaye na dabam.

Halayen da wanka ke wajaba a cikinsu su ne kamar haka:

1. Halin fitowar maniyyi, domin faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma idan kuka kasance cikin janaba, to ku yi tsarki))[1]. Da faɗin Annabi (SAW): (Idan ka fitar da ruwan maniyyi, to ka yi wanka)[2].
2. Jima'i, ko da ba tare da inzali ba, domin faɗin Annabi (SAW): (Idan namiji ya zauna tsakanin sassan jikinta guda huɗu sannan ya take ta, to wanka ya wajabta)[3].
3. Musuluntar kafiri, domin Annabi (SAW) ya umarci Ƙais ɗan Asim lokacin da ya musulunta da ya yi wanka)[4].
4. Tsarkin mace daga haila da biƙi, domin faɗin Allah Maɗaukaki: ((Idan mata sun yi wankan tsarki, to ku take su ta inda Allah Ya umurce ku)[5]. Da faɗin Annabi (SAW) ga Faɗima 'yar Abu Hubaish: (Idan jinin haila ya zo, to ki daina salla, idan kuma ya tsaya, to ki yi wanka, ki yi salla)[6].
5. Mutuwa, domin faɗin Annabi (SAW): (Ku yi masa wanka da ruwa da ganyen magarya)[7].

---

[1] [Al-Ma'ida: 6].
[2]. Bukhari (269) da Muslim (303) ne suka rawaito shi.
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (287).
[4]. Abu Dawud (355) da Al-Nasa'i (1/190) ne suka rawaito shi.
[5]. [Al-Baƙarah: 222].
[6]. Bukhari (320) da Muslim (333) ne suka rawaito shi.
[7]. Bukhari (1266) da Muslim (1206) ne suka rawaito shi.

❖ Wankan Sunna da na mustahabbi:

1. Wankan Jumu'a, wanda shi ne mafi ƙarfi cikin wankan da ake so a yi; saboda faɗin Annabi (SAW): (Idan ɗayanku zai tafi Jumu'a, to ya yi wanka)[1].

2. **Wanka tsakanin jima'i biyu**, saboda faɗin Annabi (SAW): (Wannan ya fi tsabta, kuma ya fi kyawu, kuma ya fi tsarki)[2].

3. Wanka a ranar idi, saboda sahabbai Allah ya yarda da su sun kasance suna yin hakan[3].

4. Wanka lokacin ɗaukar haramar Umara ko Hajji, domin Annabi (SAW) ya yi wanka lokacin da zai ɗau harama)[4].

5. **Wanka ga wanda ya farfaɗo daga suma**, saboda Annabi (SAW) ya yi haka lokacin rashin lafiyarsa)[5].

6. **Wanka ga wanda ya yi wankan gawa**, saboda faɗin Annabi (SAW): (Duk wanda ya yi wankan gawa, to ya yi wankan tsarki)[6].

❖ Abubuwan da aka haramta ga wanda yake cikin janaba da makamancinsa:

1. Ba ya halatta ya zauna a cikin masallaci sai dai ya ratsa kawai, saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kada ku kusanci masallatai alhali kuna cikin janaba, sai dai idan kun kasance masu wucewa ne kawai, har sai kun yi wankan tsarki))[7]. Amma idan ya yi alwala, to ya halatta a gare shi ya zauna a cikin masallaci, saboda hakan ya tabbata daga sahabbai)[8].

2. Ba ya halatta ya karanta Al-Ƙur'ani, saboda hadisin Aliyu (RA) ya ce: (Ba abin da ke hana Annabi (SAW) karatun Alƙur'ani sai dai janaba)[9].

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (877).
[2]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (216).
[3]. Malik ne ya rawaito shi (428).
[4]. Tirmizi ne ya rawaito shi (830).
[5]. Bukhari (1266) da Muslim (418) ne suka rawaito shi
[6]. [An-Nisā': 43]. Ibnu Majah ne ya rawaito shi (687).
[7]. [An-Nisā': 43].
[8]. Sa'id bin Mansur ne ya rawaito shi (1557).
[9]. Ahmad ne ya rawaito shi (1014).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

TAKUNKUMI DA ƘURAISHAWA SUKA SAKA WA BANU HASHIM DA BANU MUƊƊALIB

Lokacin da Hamza da Umar Allah ya yarda da su suka musulunta, kuma Musulunci ya yaɗu cikin wasu ƙabilu, kuma Banu Hashim suka ƙi miƙa Manzon Allah (SAW) ga mushrikai da ba shi kariya, wannan abu ya fusata Ƙuraishawa, sai suka haɗu a farkon watan Muharraram na shekara ta bakwai bayan aiko Annabi (SAW), suka yanke shawarar yanke alaƙa da Banu Hashim da Banu Muɗɗalib, suka ce: ba za su yi mu'amala da su ba, ba za su aura daga gare su ba, kuma ba za su sake magana da su ba, kuma ba za su sake zama tare da su ba, har sai sun miƙa Manzon Allah (SAW) don a kashe shi!

Suka rubuta sharuɗɗan wannan yarjejeniya a cikin takarda, suka rataye ta a saman Ka'aba, kuma wanda ya rubuta wannan takarda shi ne Mansur ɗan Ikrima, sai Manzon Allah (SAW) ya yi masa mummunar addu'a, sai Allah Ya sa hannunsa ya shanye.

Sai Banu Hashim da Banu Muɗɗalib suka koma cikin wani ƙwari da ake kira da Shi'ibu Abi Ɗalib, sai dai Abu Lahab, domin shi ya goyi bayan Ƙuraishawa.

Sai suka zauna a cikin wannan kwari cikin wannan yanayi na ƙunci tsawon shekaru uku, babu abin da ke iya isa gare su sai a asirce, har wahala ta kai musu maƙura, aka fara jin kukan yara saboda yunwa, har suka fara cin ganyen bishiyoyi da fatar dabbobi, kuma ba sa iya fita daga kwarin ba sai a watani masu alfarma, don su sayi abin da ayarorin 'yan kasuwa suka kawo Makka, saboda mutanen Makka sun kasance suna ƙara musu farashi don kada su iya saya!

Sai a shekara ta goma bayan aiko Annabi (SAW), wasu daga cikin Ƙuraishawa suka tausaya musu, suka nemi a warware wannan takardar yarjejeniyar, daga cikinsu akwai: Hisham ɗan Amru da Muɗ'im ɗan Adiyy.

Sai Manzon Allah (SAW) ya faɗa wa mutanensa cewa: Allah ya aiko da wani kwaro zuwa ga takardar yarjejeniyar nan, ya cinye dukkan abin da ke cikinta sai dai ambaton Allah Mai girma da ɗaukaka, sai Abu Ɗalib ya fita zuwa wajen Ƙuraishawa, ya faɗa musu abin da Manzon Allah (SAW) ya faɗa game da wannan takarda, sannan ya ce musu: "Idan ya yi ƙarya cikin abin da ya faɗa, to za mu bar muku shi ku yi abin da kuke so da shi; amma idan abin da ya faɗi gaskiya ne, to ku janye wannan takunkumi na zaluncin da kuka yi mana", sai suka buɗe takardar, suka same ta kamar yadda Manzon Allah (SAW) ya faɗa[1], sai suka warware yarjejeniyar, kuma Manzon Allah (SAW) da waɗanda suke tare da shi suka fito daga cikin wannan kwarin bayan wannan takunkumi mai tsawo da wariya ta zalunci.

[1]. Al-Bidayah Wan-Nihayah (3/97).

ASABAR: DARASI CKIN TARIHIN SAHABBAI A'ISHA (RA)

❖ Sunanta da Haihuwarta:

Ita ce: uwar muminai A'isha 'yar Abubakar Siddiƙ Allah Ya ƙara musu yarda, ana mata inkiya da Ummu Abdillah, wato Abdullahi ɗan ’yar’uwarta Asm'u.

An haife ta ne (RA) a shekara ta huɗu bayan aiko Manzon Allah (SAW) da annabta

❖ Rayuwarta da Falalarta:

Ita ce Siddiƙa, ’yar Siddiƙ wadda Allah Ya tsarkake daga saman bakwai, Allah ya ambace ta a cikin Littafinsa, Ya saukar da ayoyi a kanta waɗanda ake cigaba da karantawa har zuwa ranar alƙiyama.

Ta kasance daga cikin mafi sani daga cikin sahabbai, kuma mafi ilimi, kuma mafi yawan riwayar hadisi, kuma mafi kyawun ra’ayi; manyan sahabbai su kan tambaye ta idan wani abu ya rikice musu a cikin addini.

Abu Musal-Ash'ari (RA) ya ce: "Ba mu taɓa samun wani abu da ya rikice mana ba, muka tambayi Aʿisha, face sai mun iliminsa a wurinta"[1], kuma Zuhri ya ce: “Da za a haɗa ilimin A'isha da ilimin sauran iyayen muminai matan Annabi da ilimin dukkan mata, da ilimin Aʿisha ya fi falala"[2].

An yi wa Annabi (SAW) bushara da ita tun kafin ya aure ta; ya zo a cikin Hadisi ya ce: (An nuna min ke a mafarki sau uku, mala’ika ya zo da ke cikin wani ƙyalle na alhariri, sai ya ce: wannan ce matarka, sai na buɗe fuskarki, sai na ga ke ce, sai na ce: idan wannan daga wurin Allah yake, to zai tabbatar da shi)[3].

---

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3823).
[2]. Malik ya rawaito (4/124) a bugun A'zami.
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (3662).

Kuma Annabi (SAW) ya aure ta a Makka alhali tana ’yar shekara shida, kafin hijira da watanni goma sha takwas, sannan mahaifinta ya yi hijira da ita, sai Annabi (SAW) ya tare da ita a Madina a watan Shawwal shekara ta biyu bayan yaƙin Badar, alhali tana ’yar shekara tara, kuma bai taɓa auren wata budurwa ba ban da ita.

Kuma Annabi (SAW) ya ƙaunace ta ƙauna mai tsanani; domin lokacin da aka tambayi Manzon Allah (SAW) cewa: "Wane ne ka fi ƙauna ya Manzon Allah?” Sai ya ce: (A'isha) Ya ce: “To cikin maza fa? Sai ya ce: (Mahaifinta)[1].

Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Fifikon A'isha a kan sauran mata kamar fifikon abincin Saridi ne a kan sauran abinci).

Daga cikin falalarta Allah ya ƙara mata yarda akwai cewa mala'ika Jibrilu (AS) ya aiko mata sallama tare da Annabi (SAW)[2].

Haka kuma daga cikin falalarta akwai cewa Annabi (SAW) idan ya yi rashin lafiya, yana so a kula da shi a ɗakinta.

Kuma haƙiƙa Allah Ya karrama ta da da ƙarewar rayuwar Manzon Allah a lokacin yana ɗakinta bisa cinyarta; tana cewa: "Daga cikin ni’imomin da Allah Ya yi min akwai cewa Manzon Allah (SAW) ya rasu ne a ɗakina, a kuma kwanana, kuma tsakanin kirji na da wuyata"[3].

❖ Rasuwarta:

A’isha (RA) ta rasu ne a Madina a shekara ta hamsin da bakwai, a daren Talata, a rana ta goma sha bakwai ga watan Ramadan, bayan sallar wutiri, tana da shekaru sittin da shida (66).

Kuma da ma ta yi wasiyya da a binne ta da daddare, sai aka binne ta a daren a maƙabartar Baƙi'a, kuma Abu Huraira ne ya yi mata sallar jana’iza.

---

[1]. Bukhari (3769) da Muslim (2431) ne suka rawaito shi
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (3768).
[3]. Bukhari ne ya rawaito (4449).

Auna fahimtarka a darusan mako na 13			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah Madaukaki: "Ababi"?**		A
	a. Gungun tsuntsaye masu bibiyar juna.	b. Gungun tsuntsaye masu nisa da juna.	c. Gungun tsuntaye masu firgitarwa.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Mene ne ladan wanda yake nuna tawali'u ga bayin Allah?**		C
	a. Wadatar arziki.	b. Hasken fuska.	c. Allah zai ɗaukaka shi.
Darasin Aƙida	**Tambaya: Daya daga cikin ginshiƙan Musulunci shi ne:**		B
	a. Kariya ta harshe.	b. Imani da ƙaddara.	c. Kamewa daga cutarwa.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Daya daga cikin halayen da wanka ke wajaba shi ne:**		B
	a. Suma.	b. Musuluntar kafiri.	c. Aikata zunubi.
Darasin Sira	**Tambaya: Wane ne ya rubuta takardar yarjejeniyar yanke hulɗa da Banu Hashim shi ne:**		A
	a. Mansur ɗan Ikrima ɗan Amir.	b. Ikrimah ɗan Abu Jahal.	c. Abu Ɗalib ɗan Abdul-Uzza.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin Abubuwan da A'isha Allah ya ƙara mata yarda ta keɓanta da su akwai:**		A
	a. Manzon Allah (SAW) bai auri budurwa ba ban da ita.	b. Ita ce matar farko da Annabi (SAW) ya aura bayan Khadija.	c. Ita ƙarshen wacce ta rasu cikin matan Manzo (SAW).

MAKO NA GOMA SHA HUƊU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-ƘARI'A

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلۡقَارِعَةُ ١ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ٢ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡقَارِعَةُ ٣ يَوۡمَ يَكُونُ ٱلنَّاسُ كَٱلۡفَرَاشِ ٱلۡمَبۡثُوثِ ٤ وَتَكُونُ ٱلۡجِبَالُ كَٱلۡعِهۡنِ ٱلۡمَنفُوشِ ٥ فَأَمَّا مَن ثَقُلَتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ٦ فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ٧ وَأَمَّا مَنۡ خَفَّتۡ مَوَٰزِينُهُۥ ٨ فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٞ ٩ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا هِيَهۡ ١٠ نَارٌ حَامِيَةُۢ ١١﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro).
2. Mece ce mai ƙwanƙwsa (zukata da tsoro)?
3. Kuma me ya sanar da kai mece ce mai ƙwanƙwasa (zukata da tsoro)?
4. (Ita ce) ranar da mutane za su zama kamar ɗangon fari masu bazuwa.
5. Duwatsu kuma su zama kamar kaɗaɗdiyar auduga.
6. To amma wanda ma'aunan ayyukansa suka yi nauyi.
7. To shi kam yana cikin rayuwa mai gamsarwa.
8. Amma kuma duk wanda ma'aunan ayyukansa suka yi shafal.
9. To shi makomarsa (wutar) Hawiya ce.
10. Kuma me ya sanar da kai mece ce ita?
11. Wuta ce mai tsananin zafi.

❖ Saƙon da Surar ta Ƙunsa:

Tana tsoratar da zukata ta hanyar tunatar da halin da za a shiga a Ranar Ƙiyāma da yadda mutane za su kasance a ma'auninsu.

❖ Baƙin kalmomi:

الْقَارِعَةُ	Al-Ƙari'a	Alƙiyama, an kira ta da "Alƙari'a" ne saboda tana ƙwanƙwasar zukata da firgicinta.
كَالْفَرَاشِ الْمَبْثُوثِ	Kal-Farashil-Mabsus	Kamar ɗangon fari masu bazuwa waɗanda ke haɗuwa da juna.
كَالعِهْنِ الْمَنفُوشِ	Kal-Ihnil-Manfush	Kamar kaɗaɗɗiyar auduga a farkon lamari kenan, daga nan sai ta fara bacewa kaɗan-kaɗan har sai ta kasance kamar ƙura abar watsarwa.
ثَقُلَتْ مَوَازِينُهُ	Thaƙulat Mawazinuh	Ma'aunin ayyukansa na ƙwarai sun nauyaya.
فَأُمُّهُ هَاوِيَةٌ	Fa Ummuhu Hawiyah	Gungun tsuntsaye masu bibiyar juna. Makomarsa ita ce wuta wacce zai faɗa cikinta ta ka.

❖ Ma'anar Surar a Dunƙule:

Surarul-Ƙari'a tana daga cikin surorin da suka sauka a Makka, ta ƙunshi āyoyi goma sha ɗaya dake bayani game tashin ƙiyama da sakamako da halin mutane a ma'aunai, a cikinta Allah Maɗaukaki ya faɗi cewa lallai ƙiyama za ta auku, idan kuwa ta auku, zukatan mutane za su firgita saboda abubuwan masu firgitarwa da abubuwa masu girma dake cikinta, ta yadda mutane saboda yawansu da ruɗewarsu za su zama kamar ƙudajen a cikin taruwarsu da hau-hauwar junansu da watsuwarsu, da ƙwaron gero a taruwarsu da

yaɗuwarsu, kuma duwatsu duk da kafuwarsu da tsayinsu da girmansu su zama kamar gashin da aka warwatsa yana yawo nan da can.

Sa’an nan Allah Maɗaukaki Ya ba da labari game da karkasuwar mutane zuwa gida biyu: Wanda ma’aunin ayyukansa na alheri ya nauyaya, to zai dace da rayuwa mai gamsarwa a cikin aljanna gidan ni‘ima mai dorewa, amma wanda alkhairansa suka yi ƙaranci kuma zunubansa suka yawaita, to makomarsa ita ce wuta gidan halaka, za a jefa shi a cikinta a dankwafe, Allah Madaukaki ya tsare mu daga gare ta.

❖ Abubuwan da za mu koya daga Surar:

1. Tunatarwa game da abubuwa masu tsanani da za su faru ranar ƙiyama da abin da ke cikinta na firgici.
2. Bayanin makomar masu taƙawa da kwaɗaitarwa zuwa gare ta, da tsoratarwa game da makomai kafirai, da gargaɗi game da hakan.
3. Cewa lallai daga cikin aƙidar Ahlus-Sunnah wal-Jama‘ah akwai tabbatar da ma’aunin ayyuka a ranar ƙiyama, kuma ana auna kyawawan ayyuka da shi da munana.
4. Cewa lallai wutar lahira mai ƙuna ce mai tsananin zafi, ta ninka zafin wutar duniya da ninki saba’in.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

TSORATARWA A KAN ZALUNCI

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Zalunci duhu ne a ranar kiyama**). Bukhari da Muslim sun ruwaito[1].

❖ Sharhi:

A cikin wannan Hadisin, Annabi (SAW) yana umurtar mu da mu guji zalunci kuma mu tsoraci faɗawa cikinsa, ga mutum ne, ko dabba, ko aboki, ko maƙiyi, musulmi ne ko kafiri. Sa'an nan Annabi (SAW) ya bayyana dalilin wannan tsoratarwa daga zalunci da cewa azzalumi zai kasance ne a cikin duhu a ranar ƙiyama, ba zai samu hanyar fita daga gare ta ba, a lokacin da hasken muminai yake bayyana a gabansu da damansu.

Abin da ke biyo haka shi ne adalci — ta hanyar tsayuwa da haƙƙin Annabi (SAW), na daga imani da shi da ƙaunarsa, da fifita ƙaunarsa fiye da ƙaunar dukkan halitta.

Kuma daga cikin adalci akwai: biyayya ga iyaye, da sada zumunta, da gaskiya a cikin kasuwanci, da biyan haƙƙin masu hidima da ma'aikata, da tsayuwa da haƙƙin juna tsakanin ma'aurata, kuma duk wanda ya yi sakaci da wani abu daga cikin waɗannan, to azzalumi ne.

Saboda haka, dukkan nau'o'in zalunci duhu ne a ranar ƙiyama; kuma ma'abotansa za su fuskanci uƙuba gwargwadon zaluncinsu, kuma za a saka wa waɗanda aka zalunta daga kyawawan ayyukan masu zalunci, idan kuma kyawawan ayyukansu suka ƙare, to za a ɗibi zunuban waɗanda aka zalunta a danƙara wa waɗanda suka yi zaluncin.

---

[1]. Bukhari (2447) da Muslim (2579) ne suka rawaito shi.

❖ **Abubuwan da za mu koya daga Hadisin:**

1. Gargadi game da zalunci da hatsarin ƙarshensa.
2. Nassoshi sun bayyana cewa zalunci nau’i uku ne:

Na farko: Nau’in da Allah ba Ya gafartawa — shi ne shirka da Allah, kamar yadda Allah Madaukaki ya ce: ((Lallai Allah ba Ya gafarta yi masa shirka))[1].

Na biyu: Nau’in da Allah baya barin komai daga cikinsa, sai ya karɓi hakkinsa gaba ɗaya, shi ne zaluntar bayin Allah ga junansu.

Na uku: Nau’in da yake ƙarƙashin ganin daman Allah, idan Ya ga dama ya azabtar, idan Ya ga dama Ya yafe, shi ne zunuban da suke tsakanin bawa da Ubangijinsa, waɗanda ba shirka ba.

[1]. Bukhari (2447) da Muslim (2579) ne suka rawaito shi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

RUKUNIN FARKO DAGA CIKIN RUKUNAI SHIDA NA IMANI: (IMANI DA ALLAH MAƊAUKAKI)

Imani da Allah yana tabbata ne da abubuwa guda huɗu:

1. Imani da Samuwarsa.
2. Imani da Ribubiyyarsa (Ayyukansa).
3. Imani da Uluhiyyarsa (Cancantarsa da bauta).
4. Imani da Sunayensa da Siffofinsa.

❋ **Al-amari na farko** (wato imani da samuwar Allah Maɗaukaki) yana da dalilai guda huɗu: Fiɗra (Asalin halita), da hankali, da shari'a, da hissi (wato abin da ke faruwa a aikace).

1) **Game da dalilin Fiɗira**: Kowanne halitta an halicce shi ne da fiɗirar imani da Mahaliccinsa ba tare da tunani ko koyarwa ba. Allah Maɗaukaki ya ce: ((Asalin halittar da Allah Ya halicci mutane a kanta))[1], kuma Annabi (SAW) ya ce: ((Babu wani mutum face an haife shi a kan fiɗira (Asalin halittar Allah)[2].

2) **Dalilin hankali kuwa:** Shi ne lallai abubuwan da suka samu dole akwai wanda ya samar da su, kuma halittu dole ne ya zama suna da mahalicci, don ba zai yiwu su halicci kansu ba, kuma ba zai yiwu su zamto haka kawai suka samu ba; don haka dole ne akwai Ubangiji wanda Ya halicce su, sannan bayan halittarsu muka gan su suna tafiya bisa wani tsari mai banmamaki wanda yake hana yiwuwar cewa hakan ya kasance ba zato ba tsammani; domin abin da ya samu da bazato ba tsammani ba ya kasancewa bisa tsari. Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ko kuwa an halicce su ne ba da wani mai halitta ba, ko kuwa su ne masu halittar kansu)), [3] don haka ne lokacin Jubairu ɗan

---

[1]. [Ar-Rum: 30].
[2]. Bukhari (1358) da Muslim (2658) ne suka rawaito shi.
[3]. (Aɗɗur: 35).

Muɗ'im ya ji waɗannan ayoyi, sai ya ce: "Zuciyata ta kusa ta fice! Kuma wannan shi ne farkon abin ya ɗarsu a zuciyata na imani".[1]

3. **Dalili na shari'a**: Saboda lallai dukkan littattafai da suka sauko daga sama suna nuni a kan samuwar Ubangijinsu, kuma abin da ke cikinsu na hukunce-hukuncen adalci waɗanda suke ɗauke da maslahar halittu da labarai na gaskiya waɗanda mutane suka tabbatar da aukuwarsu; su ma sun yi nuni a kan haka, dukkan wannnan dalili ne a kan cewa lallai daga Ubangiji Masani suke.

4. **Amma dalilin hissi (wato abin da ke faruwa gani aikace)**; to yana bayyana ta fuska biyu:

Fuska ta farko: Amsa addu'o'in masu addu'a, da agaza wa waɗanda suke cikin damuwa, cikin Annabawa da Manzanni da salihai, wannan ma duka dalili ne yankakke a kan samuwar Ubangijinsu Mai girma da ɗaukaka, kuma amsa addu'o'in masu addu'a bai gushe ba yana a matsayin al'amari da ake gani har zuwa wannan lokaci ga wanda ya yi gaskiyar fakewa zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki.

Fuska ta biyu: Alamomin annabtakar Annabawa da mu'ujizozinsu, kuma haƙiƙa mutane sun gan su da idanunsu, kuma sun bibiyi juna wurin rawaito su; kamar ayoyin Annabin Allah Nuhu, da Salihu, da Musa, da Isa (AS), da ayoyin Annabinmu Muhammadu (SAW); na tsagewar wata, da tasbihin tsakwankwani a kan tafin hannunsa, da ɓuɓɓugowar ruwa a tsakanin yatsunsa (SAW).

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4573).

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

SIFFAR WANKA, DA SHAFA A KAN BANDEJI

❖ Siffar wanka:

Wankan janaba yana da siffa biyu: siffa mai isarwa, da kuma siffa ta mustahabbanci.

❋ **Siffa mai isarwa**: Ita ce wacce take ɗauke da wajibai kawai.

Yadda ake yin ta shi ne: Mutum ya ɗau niyya a zuciyarsa, sai ya watsa ruwa ya game jikinsa da shi, tare da kurkuran baki da shaƙan ruwa.

❋ **Siffar ta mustahabbanci kuma**: Ita ce wacce take ƙunshe da wajibai da sunnoni.

Yadda ake yin ta kuma shi ne: Mutum ya ɗau niyya a zuciyarsa, sannan ya wanke hannayensa biyu, sannan ya wanke al'auransa, da abin da ya taɓa jikinsa na ƙazanta, sannan ya yi alwala irin alwala da yake yi idan zai yi salla, sannan ya ɗebi ruwa da hannunsa sai ya tsefe tsakanin gashin kansa da shi, yana da shigar da yatsunsa cikin gashinsa, har ya jiƙa fatarsa, sannan ya zuba ruwa a kansa sau uku, sannan ya watsa ruwa a sauran jikinsa; saboda hadisai biyu na A'isha da Maimuna.[1]

Kuma ya wajaba a kan mai wanka da sifofi biyun duka ya bibiyi cikin gashinsa da abin da yake ɓoye a jikinsa; kamar hamatarsa, da cibiyarsa, da lanƙwasar gwiwowinsa, idan kuma yana sanye da agogo ko zobe, to dole sai ya jujjuya su; domin ruwa ya shiga ƙasansu.

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (248-249), da Muslim (316-317).

❖ Shafa a kan bandeji da makamantanshi:

Bandeji: Shi ne abin da ake ɗaure karaya da shi, don ya kama kuma ya haɗe; kamar jibsin da makamantansa, haka kuma da irin su: Manne, da yadi, da tsumma da ake ɗaura su a kan ciwo.

❋ Hukuncin shafa a Kansu a alwala da wanka:

Malamai sun haɗu a kan shar'ancin shafa a kan bandeji da makamantansu a alwala da wanka, da sharaɗi guda biyu:

1. Ya zama akwai buƙatar samuwarsu, ta yadda idan aka cire za a cutu.

2. Ya zama daidai da abin da karayar ko ciwon suke buƙata, idan ya wuce wajen buƙata dole ne ya warware abin da ya ƙaru a kan buƙatar.

❋ Daga cikin hukunce-hukuncen shafa a kan bandeji da makamantansa akwai:

1. Lallai ya wajaba a shafe dukkan bandejin.

2. Lallai shafa a kansa ba shi da wani lokaci ƙayyadajje, za dai a riƙa shafa a kansa har zuwa lokacin cire shi ko kuma warkewan abin da ke ƙarƙashinsu.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

HIJIRA TA BIYU ZUWA HABASHA

Lokacin da Annabi (SAW) ya ga taurin kan mushirikai da ƙaruwar cutarwarsu da ga musulmai, sai Annabi (SAW) ya yi nuni ga sahabbansa da su yi hijira ta biyu zuwa Habasha, sai mutum tamanin da uku suka yi hijira zuwa gare ta a wannan karon, tare da mata sha bakwai daga cikin matansu, suka yi hijira zuwa Habasha, masarautar Nahashi As'hama, sai ya ba su mafaka, ya karrama su, kuma ya amintar da su.

Yayin da Ƙuraishawa suka ji labarin hakan, sai suka aika Abdullahi ɗan Abu Rabi'a da Amru ɗan As a bayansu, sai suka taho wurin Najashi da kyaututtuka don ya mayar musu da musulmai, sai ya ƙi, sai ya raɗa masa cewa: Lallai ai waɗannan suna fadin mummunan magana game da Isa; suna cewa shi bawa ne!

Sai ya kira musulmai zuwa ga majalisarsa – wanda shugabansu shi ne Ja'afar ɗan Abu Ɗalib (RA) -, sai ya tambaye su game da addininsu, sai Ja'afar ɗan Abu Ɗalib (RA) ya yi magana, sai ya bayyana masa halin da suke ciki kafin zuwan Musulunci, da kuma yadda suka zama vayan haka, da kuma abin da Musulunci ya zo da shi na kaɗaita Allah Maɗaukaki da bauta da barín bauta wa gumaka, da abin ya shiryar zuwa gare shi na kyawawan ɗabi'u, sannan ya karanta masa farkon suratu Maryam, wanda yake ƙunshe da labarin haifuwar Annabi Isa ɗan Maryam (AS).

Yayin da ya gama, sai Najashi ya ɗauki wani sanda daga ƙasa, sai ya ce: Bai ƙara komai a kan abin da ke cikin Injila ba ko da kamar wannan sanda ne. Sannan ya ce: Ku tafi, domin ku amintattu ne a ƙasata, duk wanda ya zage ku za a ci taransa. Sai kuma ya ce wa Amru da Abdullahi: Ina rantsuwa da Allah, da za ku ba ni abin da ya kai dutse na zinari, to ba zan miƙa muku su ba! Sannan ya yi umurni da a mayar musu da kyaututtukansu, sai suka dawo a

kunyace da mafi sharri da munin tozarci, sai musulmai kuma suka zauna a can cikin aminci da girmamawa.[1]

[1]. Albidaya wan-nihaya (3/69).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

HAFSA (RA)

❖ Sunanta da haifuwarta:

Ita ce: Uwar muminai, Hafsa ‘yar Umar ɗan Khaɗɗab ɗan Nufail, Nasabarta na haɗuwa da Annabi (SAW) a wajen “Ka’abu ɗan Lu’ayyu).

An haife ta a Makka, kafin aiko Annabi (SAW) da shekara biyar.

❖ Rayuwarta da falalarta:

Ta kasance tana ƙarƙashin Khunaisu ɗan Huzafa Assahami, ɗaya daga cikin waɗannan suka fara musulunta, sun yi hijira tare zuwa Madina, kuma ya halarci yaƙin Badar, sannan sai ya rasu bayan wannan yaƙin,[1] sai Annabi (SAW) ya aure ta bayan rasuwarsa a shekara ta uku bayan hijira, a lokacin tana ‘yar shekara ashirin, sai ta kasance ita ce matarsa ta huɗu.

Ta kasance mai yawan azumi da sallar dare da tsantseni, mai kaifin basira da hankali, an san ta da fasaha da iya magana, kuma tana da huɗubobi da baitoci masu fasaha da azanci; haƙiƙa ta kasance daga cikin mata ‘yan kaɗan waɗanda suka koyi rubutu a wannan lokacin, ta koye shi ne a wajen Shifa’u ‘yar Abdullahi,[2] kuma ya ishe ta daraja kasancewar lallai ita ce ma’abociyar takarda ta farko da aka rubuta Alƙur’ani mai girma a cikinta, wacce Abubakar ya yi umurni da a haɗa ta, sannan ta kasance a wajen Umar bayan rasuwar Abubakar, sannan Umar ya yi wasici da ita ga Hafsa lokacin rasuwarsa,[3] sai ta kiyaye ta a wajenta har sai da Usman ɗan Affan ya neme ta lokacin da ya yi nufin haɗa Alƙur’ani da kwafansa.

---

[1]. Albidaya wan-nihaya (8/30).
[2]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (3887).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (4679).

❖ **Rasuwarta:**

Hafsa (RA) ta rasu a watan Sha’aban, a shekara ta 41 bayan hijra, a Madina, a farko-farkon halifancin Mu’awiya ɗan Abu Sufyan (RA), sai Marwan ɗan Hakam goman Madina a wancan lokacin ya sallace ta, sai aka binne ta a maƙabartar Baƙi’.

Auna fahimtarka a darusan mako na 14			**Amsa ta ƙwarai**
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ma'anar: "Al'ihinil manfush"?**		A
	a. Laka mai zafi.	b. Ƙonannen fata.	c. Yagaggen fata.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Zalincin da Allah ba ya barin komai daga gare shi, bari dai, yana sa a cika shi gaba ɗayansa shi ne?**		C
	a. Cin riba.	b. Zalintar kai.	c. Zalincin bayi sashinsu ga sashi.
Darasin Aƙida	**Tambaya: Daga cikin dalilan hankali a kan samuwar Allah akwai cewa:**		B
	a. Lallai halittu babu makawa suna da mahalicci.	b. Lattattafai da aka saukar daga sama.	c. Amsa addu'oin masu addu'a da agaza wa mabuƙata.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Dole ne idan za a yi wankar janaba ya zama an yi:**		B
	a. Alwala kafin hakan.	b. Game jiki da ruwa.	c. Maimaitawa sau uku.
Darasin Sira	**Tambaya: Jagoran musulmai kuma mai magana da yawunsu a gaban sarkin Habasha shi ne:**		a
	a. Abdullahi ɗan Abbas.	b. Ja'afar ɗan Abu Ɗalib.	c. Umar ɗan Khaɗɗab.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Annabi (SAW) ya auri Hafsa (RA) a shekara ta …….. bayan hijira.**		a
	a. 3	b. 5	c. 7

MAKO NA GOMA SHA BIYAR

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUT-TAKASUR

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
أَلۡهَىٰكُمُ ٱلتَّكَاثُرُ ١ حَتَّىٰ زُرۡتُمُ ٱلۡمَقَابِرَ ٢ كَلَّا سَوۡفَ تَعۡلَمُونَ ٣ ثُمَّ كَلَّا سَوۡفَ
تَعۡلَمُونَ ٤ كَلَّا لَوۡ تَعۡلَمُونَ عِلۡمَ ٱلۡيَقِينِ ٥ لَتَرَوُنَّ ٱلۡجَحِيمَ ٦ ثُمَّ لَتَرَوُنَّهَا عَيۡنَ ٱلۡيَقِينِ
٧ ثُمَّ لَتُسۡـَٔلُنَّ يَوۡمَئِذٍ عَنِ ٱلنَّعِيمِ ٨﴾

❖ Fassara:

1. Alfahari da yawan (‘ya’ya da dukiya) ya shagaltar da ku.

2. Har kuka (mutu kuka) ziyarci ƙaburbura.

3. A’aha! (haka bai kamace ku ba) da sannu za ku sani.

4. Sannan a’aha, da sannu za ku sani.

5. Tabbas da za ku sani, sani na sakankancewa.

6. Tabbas haƙiƙa za ku ga wutar Jahimu.

7. Sannan tabbas haƙiƙa za ku gan ta gani da ido na sakankancewa.

8. Sannan kuma tabbas lallai za a tambaye ku a wannan ranar game da ni’imomin (da kuka mora a duniya).

❖ Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:

Tunatar da ma’abota alfahari da dukiya da ‘ya’ya a duniya azabar ƙabari da hisabi a lahira.

❖ Baƙin kalmomi:

ألهاكم	Alhakum	Ma’ana: Ya shagaltar da ku daga barin ɗa’a ga Allah Maɗaukaki.

التكاثر	Attakasur	Alfahari da yawan dukiya da ‘ya’ya da kayan more rayuwa.
علم اليقين	Ilmal-yaƙin	Ilimi tabbatacce a zukata, wanda ake da yaƙini da shi.
عين اليقين	Ainal-yaƙin	Wato tabbas za ku ga wutar jahimu da idanuwa, a bisa yaƙin ba shakka ba.
النعيم	Anna’im	Dukkan nau’ukan ni’imomi; na lafiya, da aminci, da iyalai, da abinci da makamantansu.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

A cikin wannan surar, Allah Maɗaukaki Yana zargin masu shagaltuwa da tara dukiya da yawaita ta saboda nuna ana da shi da alfahari, masu kuma shagala daga barin abin da aka halicce su don shi, na yin ɗa’a ga Allah da Manzonsa, masu cigaba da gafalarsu har suka mutu aka kai su maƙabartu.

Sai Allah Mai girma da ɗaukaka ya yi tsawatarwa gare su da faɗinsa: (A’aha), wato ba haka ya kamata ku kasance ba, kuma (da sannu za ku san) sakamakon shagalarka daga barin ɗa’a ga Allah, da kawar da kanku daga barin yin guzuri don gidan lahira.

Sannan rantsuwa ya zo daga Allah Maɗaukaki da cewa kowa zai ga wutar jahimu ido da ido, a filin alƙiyama, mushiriki zai gan ta don ya shige ta, shi kuma mumini zai gan ta sai Allah Ya kuɓutar da shi daga gare ta, a wannan lokacin za a tambaye su a kan abin da aka ba su a duniya, na lafiya da lokaci, da abinci, da abin sha, duk wanda ya yi godiya akan su, kuma ya yi dogaro a kansu wurin yin biyayya ga Allah, to ya tsira, wanda kuwa bai yi godiya ba, kuma ya saɓa wa Allah, to da a ba shi sakamakonsa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Alƙawarin narko mai tsanani ga wanda ya shagaltu da tara dukiya da alfahari da ‘ya’ya ga bayin Allah.

2. Ƙabari gida ne na ƙetarewa da ziyara, ba zai ɗau lokaci ba mutane za su bar shi zuwa gidan lahira.

3. Gode wa Allah Maɗaukaki da zuciya yana kasancewa ne ta hanyar tabbatar da ni'imominsa, da ƙudurta cewa Shi ne Mai ni'imtarwa na haƙiƙa, da harshe kuma zai zama ta hanyar danganta masa su, da ambaton su ta hanyar yabo da jinjina gare Shi tsarki ya tabbata a gare Shi, da gaɓoɓi kuma yana kasancewa ta hanyar aikata abin da Allah Ya wajabta, da barin abin da Ya haramta.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

LAZIMTAR GODE WA ALLAH MAƊAUKAKI A KAN NI”IMOMINSA

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Ku yi duba zuwa ga wanda yake ƙasa da ku, kada ku dubi wanda yake sama da ku, wannan shi ya fi dacewa don kada ku raina ni’imar Allah a gare ku**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito.[1]

❖ Sharhi:

Manzon Allah (SAW) yana kwaɗaitarwa game da godiya ga Allah Maɗaukakin Sarki, ta hanyar tabbatar da ni’imominsa, da ambaton su, da dogaro da su wurin yin ɗa’a gare Shi, da aikata subaba masu taimakawa a kan godiya, kuma Annabi (SAW) ya nusar zuwa ga wani sababi mai amfani da magani mai warkarwa, wanda shi ne bawa ya riƙa yin duba a koda yaushe zuwa ga wanda ke ƙasa da shi, ta fuskar hankali da dukiya da mabanbantan ni’imomi, don hakan ya zaburar da shi a kan gode wa Ubangijinsa da yabo a gare Shi, kuma kada ya ce zai na hango wanda ke sama da shi, don kada hakan ya kai shi ga raina ni’imar Allah a gare shi, duk wand a ya aikata haka, to haƙiƙa ya gode wa Ubangijinsa, kuma ya hutar da zuciyarsa, kuma ya ni’imtu da kyawun zuciyarsa da dadîn rayuwarsa.

Kuma haƙiƙa wannan ma’ana ya zo a fili a cikin littafin Allah Maɗaukaki; a inda Allah Mai girma da ɗaukaka Yake cewa: ((Kada kuma ka zura idanuwanka a kan dangogin dadîn da Muka jiyar da wasu daga cikinsu, na adon rayuwar duniya don Mu jarrabe su da shi. Arzikin Ubangijinka kuwa (shi) ya fi alheri ya kuma fi dawwama)).[2]

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4679) da Muslim (2963).
[2]. (Ɗaha: 131).

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Nusar da musulmi zuwa ga mafi falalar hanyoyi masu isar da shi zuwa ga yarda da wadatar zuci.

2. Shar'antakar lura da wanda ke ƙasa a lamura na duniya, don hakan ya zaburar da mutum a kan yarda da godiya, amma a game da lamura na ibada, to ana so mutum ya riƙa hango wanda ke sama da shi, don hakan ya saka shi ƙara ƙoƙari da rigegeniya.

3. Falalar gudun duniya da barin damuwa da ita.

4. Lallai cikin wannan hadisin akwai hanyar kare kai daga dayawa daga cututtukan zuciya; kamar hasada, da ƙeta, da makamantansu.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA RUBUBIYYAR ALLAH MAƊAUKAKI

Imani da rububiyyar Allah Mai girma da ɗaukaka: Shi ne imani da cewa Shi ne Ubangijin komai, ba Shi da abokin tarayya ko kuma mai taimako.

Ma'anar Ubangiji: Shi ne wanda Yake da sifofi guda uku: (Halitta, da Mulki, da kuma Jujjuya al'amura), kuma dukkansu sifofi ne keɓantattu ga Allah Maɗaukaki, don haka, babu mahalicci sai Allah, babu Sarki sai Shi, kuma babu mai jujjuya al'amura koma bayansa.

❋ **Dalili a kan haka shi ne kamar haka:**

❖ Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Haƙiƙa halitta da umarni nasa ne)).[1]

❖ Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Mai yin wannan kuwa) Shi ne Allah Ubangijinku, mulki (kuwa) nasa ne. Waɗanda kuwa kuke bauta wa ba Shi ba, ba su mallaki ko da rigar ƙwallon dabino ba)).[2]

❖ Kuma Allah Ya ce: ((Lalle a cikin halittar sammai da ƙasa da sassaɓawar dare da rana da jiragen ruwa da suke tafiya a kan ruwa da abin da yake amfanar mutane da kuma abin da Allah Ya saukar daga sama na ruwa, Ya rayar da ƙasa da shi bayan mutuwarta, Ya kuma yaɗa duk wata halitta mai tafiya a cikin (ƙasa) da jujjuyawar iska, da kuma girgije da aka hore shi tsakanin sama da ƙasa, lalle akwai ayoyi ga mutane masu hankali))[3]

❖ Kuma Allah Ya ce: ((Allah (Shi ne) Wanda Ya halicce ku sannan Ya arzuta ku sannan Shi zai kashe ku sannan Ya raya ku; shin a cikin abokan tarayyarku akwai wanda zai aikata wani abu daga wannan? Tsarki ya tabbata a gare Shi, Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke tarawa (da Shi)).[4]

❖ Kuma Allah Ya ce: ((Yana daga ayoyinsa cewa Ya halicce ku daga turɓaya, sannan kuma sai ga ku mutane kun warwatsu (a

---

1. (Al-A'araf: 54).
2. (Faɗir: 13).
3. (Albaƙra: 164).
4. (Arrum: 40).

ko’ina) () Yana kuma daga ayoyinsa cewa Ya halitta muku mata daga jinsinku don ku samu nutsuwa gare su, Ya kuma sanya soyayya da jin ƙai tsakaninku. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane masu tunani () Yana kuma daga cikin ayoyinsa halittar sammai da ƙasa da kuma sassaɓawar harsunanku da launukanku. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga ma’abota ilimi () Yana kuma daga cikin ayoyinsa baccinku da daddare da kuma rana da neman falalarsa da kuke yi. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga masu ji (na lura) () Yana kuma daga cikin ayoyinsa nuna muku walƙiya da Yake yi don tsoratarwa da kwaɗaitarwa, Ya kuma saukar da ruwa daga sama, sai Ya raya ƙasa da shi bayan mutuwarta. Lalle a game da wannan tabbas akwai ayoyi ga mutane da suke hankalta)).[1]

Kuma haƙiƙa halittu gaba ɗayansu sun tabbatar wa Allah Tauhidin Rububiyya, kuma sun tabbatar masa jujjuya al’amuran halittunsa, Yana halittan su, kuma Yana raya su, kuma Yana kashe su, ba sa danganta wani abu na ayyukansa ga waninsa; daga cikin haka akwai: Mushirkai a zamanin Annabi (SAW), haƙiƙa sun kasance masu tabbatar da Rububiyyar Allah Maɗaukaki, tare da shirka da suke masa a cikin Uluhiyya; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma idan da za ka tambaye su wane ne ya halicci sammai da ƙasa, da tabbas za su ce Allah Mabuwayi kuma Masani ne Ya halicce su)).[2]

Kuma ba a san wani ba cikin halittu da ya yi inkarin Rububiyyar Allah tsarki ya tabbata a gare Shi, sai dai idan ya kasance mai taurin kai ne, wanda ba ya ƙudurta abin da yake faɗi, kamar yadda ya faru ga Fir’auna, lokacin da ya yi da’awar Uluhiyya, haka bai kasance daga wani ƙuduri ba, bari dai, kawai girman kai ne da musu; Allah Maɗaukaki Ya ce a cikin bayani Annabi Musa ga Fir’auna: ((Musa) ya ce: “Haƙiƙa ka sani ba wanda ya saukar da waɗannan (ayoyin) sai Ubangijin sammai da ƙasa don su zama hujjoji, kuma lalle ina

[1]. (Arrum: 20-24).
[2]. (Azzukruf: 9).

tsammanin kai Fir’auna halakakke ne)),[1] kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Suka kuma musanta su don zalunci da girman kai, alhali kuwa zukatansu sun sakankance da su)).[2]

[1]. (Al-Isra: 102).
[2]. (Annaml: 14).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

TAIMAMA

Wani lokaci, musulmi zai samu kanshi a wani yanayi da zai rasa ruwa a cikinsa, ko kuma akwai ruwan amma ba zai iya aiki da shi ba, to a wannan halin Allah Ya shar'anta abin da zai maye gurbin ruwa; ita ce taimama, ita taimama rangwame ne daga Allah Mai girma da ɗukaka ga bayinsa, kuma wannan na daga cikin kyawun wannan shari'a, kuma na daga cikin abubuwan da wannan al'umma ta Annabi Muhammadu ta keɓanta da shi, Allah Ya keɓance ta da shi a kan waɗanda suka gabace ta, saboda yalwatawa da kyautatawa gare ta daga wajensa.

❖ Hukuncin taimama:

Malamai sun yi ijma'i a kan shar'ancin taimama, da kuma cewa ita ana yin ta a maimakon tsarki da ruwa, a kari (hadasi) ƙarami da babba.

Dalili kuwa shi ne kamar haka:

Faɗin Allah Maɗaukaki: ((Idan kuma kun kasance marasa lafiya ko a halin tafiya, ko ɗaya daga cikinku ya dawo daga bahaya ko kuma kuka sadu da mata kuma ba ku sami ruwa ba, to sai ku nufi doron ƙasa mai tsarki ku yi taimama, sai ku shafi fuskokinku da hannayenku. Lalle Allah Ya kasance Mai afuwa ne, Mai gafara)).[1]

Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (An sanya mun ƙasa ta zama masallaci da abin yin tsarki a gare ni).[2]

❖ Yadda ake taimama:

Za a ɗauki niyya, sannan a ce "Bismillahi", sannan a daki ƙasa sau ɗauya da hannaye biyu, sannan a karkaɗe su, sai a shafi fuska da

[1]. (Alma'ida: 6).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (335).

hannaye da su, sai a shafi bayan hannun dama da hannu na hagu, sannan a shafi bayan hannun hagu da hannu na dama.[1]

❋ **Kuma taimama zai zama ingantacce mai isarwa ne a hali biyu:**

1. Lokacin da aka rasa ruwa; saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((kuma ba ku sami ruwa ba, to sai ku nufi doron ƙasa mai tsarki ku yi taimama)),[2] da faɗin Annabi (SAW): (Lallai ƙasa mai tsarki, abin yin tsarki ne ga musulmi, ko da bai samu ruwa ba har tsawon shekara goma, idan kuma ya samu ruwa, to ya wanke fatarshi da shi).[3] Haka kuma idan yana da ruwa ɗan kaɗan, wanda yana da buƙatar ya sha shi ko ya yi girki da shi, ta yadda idan ya yi tsarki da shi zai cutar da buƙatarshi kuma ya kamu da ƙishi, shi karan kanshi ko wanda yake tare da shi.

2. Lokacin da ba za a iya aiki da ruwa ba; saboda rashin lafiya, ko tsananin sanyi, wanda yake tsoron cutuwa da su idan ya yi amfani da ruwa, kuma babu abin da zai tafasa ruwa da shi a wajensa, saboda faɗin Allah Maɗaukaki ((idan kuma kun kasance marasa lafiya)),[4] kuma ya zo a hadisin Amru ɗan Aas, cewa lallai shi lokacin da aka aika shi a yaƙin "Zatus-salasili" ya ce: "Na yi mafarki a wani dare mai tsananin sanyi, sai na ji tsoron na mutu idan na yi wanka, sai na yi taimama, sai na yi salla wa jama'ata sallar asuba",[5] sai kuma Annabi (SAW) ya tabbatar da shi a kan hakan.

❖ **Abubuwan da suke lalata taimama:**

Su ne abubuwan da suke ɓata ta, suna nan kamar haka:

[1]. Bukhari (347), da Muslim (368) ne suka rawaito.
[2]. (Alma'ida: 6)
[3]. Tirmizi ne ya rawaito shi (124).
[4]. (Alma'ida: 6).
[5]. Ahmad ne ya rawaito shi (4/203), da Abu Dawud (334).

1. Abubuwan da suke lalata alwala da warware ta, saboda taimama ana yin shi ne a maimakon alwala, kuma duk abin da zai lalata alwala, to zai lalata taimama.

2. Samun ruwa ko kuma ikon amfani da shi; saboda faɗin Annabi (SAW): (idan ya samu ruwa, to ya wanke fatarsa da shi).[1]

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (124).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

SHEKARAR BAƙIN CIKI

A shekara ta goma bayan aiko Annabi (SAW), bayan fitowa daga takunkumi da wata shida, Abu Ɗalib ya yi rashin lafiya, kuma ciwo ya tsananta gare shi, haƙiƙa ya kasance bango mai ƙarfi da Annabi (SAW) yake jingunuwa da shi don kare kanshi daga kaidin mushirkai da cutarwarsu, yayin da mutuwa ta riski Abu Ɗalib, Annabi (SAW) ya shiga wajensa, a lokacin akwai Abu Jahal da Abdullai ɗan Abu Umayya a wajensa, sai ya ce: (Ya baffana, ka ce: "La'ilaha illallah", kalma da zan yi maka shaida da ita a wajen Allah), sai Abu Jahal da Abdullahi ɗan Abu Umayya suka ce: Ya kai Abu Ɗalib, addinin Abdulmuɗɗalib za ka bari?! Ba su gushe ba suna masa magana har sai da ya ce: "Ina nan a kan addinin Abdulmuɗɗalib"! sai ya mutu a kan haka, sai Annabi (SAW) ya yi baƙin ciki a kanshi baƙin ciki mai tsanani, sai ya ce: (Tabbas zan nema maka gafara matuƙar ba a hana ni nema maka ba),[1] sai wannan ayar ta sauka: ((Bai kamata ba ga Annabi da waɗanda suka yi imani su nema wa mushrikai gafara, ko da kuwa sun kasance dangi ne na kusa, bayan kuwa ya riga ya bayyana gare su cewa lalle su 'yan wuta ne),[2] haka ita ma wannan ayar ta sauko: ((Lallai kai ba ka shiryar da wanda kake so, sai dai Allah Shi ne Yake shiryar da wanda Yake so)).[3]

Bayan rasuwar Abu Ɗalib da wata uku, sai Khadija (RA) ta rasu, sai masifu suka Yawaita ga Manzon Allah (SAW), kuma baƙin cikin suka riƙa bibiyan juna a gare shi; saboda ta kasance mata tagari kuma mai taimako a gare shi, kuma ta kasance ita ce uwar 'ya'yansa, ta kasance tana taimakon sa tana kuma ƙarfafa shi a lokacin da yake samun kanshi a halin tsanani, kuma tana taimakon sa da dukiyarta da ranta; Annabi (SAW) ya ce game da ita: (Ta yi imani da ni a lokacin da mutane suka kafirce mun, kuma ta gaskata ni a lokacin

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4772), da Muslim (24).
[2]. (Attauba: 113).
[3]. (Alƙasas: 56).

da mutane suka ƙaryata ni, kuma ta yi tarayya da ni cikin dukiyarta lokacin da mutane suka hana ni, kuma Allah Ya azurta ni da ‘ya’yanta, ya kuma hani ‘ya’ya daga waninta).[1]

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (3821), da Muslim (2421).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ZAINAB ‘YAR KHUZAIMA (RA)

❖ Sunanta da haihuwarta:

Ita ce uwar muminai, Zainab ‘yar Khuzaima ɗan Haris ɗan Abdullahi ɗan Amru, ita ‘yar’uwar Maimuna ‘yar Haris ce ta ɓangaren uwa.

An haife ta a Makka, kafin a aiko Annabi (SAW) da shekara goma sha uku.

❖ Rayuwarta da darajojinta:

Ta kasance (RA) mai kamun kai tsarkakakkiya, ‘yar dangi da dangantaka, ta shahara da karamci da kyauta, da ciyar da miskinai da kulawa da su da tausaya musu, har ma an kasance ana kiran ta da “uwar miskinai” a lokacin Jahiliyya; saboda yawan kyatatawarta.[1] Bayan ta yi aure da Annabi (SAW) sai ta ƙara yawaita ayyukan alheri da kyautatawa, sai ta zamto ba za ta samu dinari ko dirhami ba face ta ciyar da miskinai da shi ta hanyar ba su abinci ko tufafi.

Annabi (SAW) ya aure ta a watan Ramadan, a shekara ta uku bayan hijira, hakan ya kasance ne bayan rasuwar mijinta Abdullahi ɗan Jahash a ranar yaƙin Uhudu,[2] sai ta kasance ita ce ta biyar cikin uwayen muminai.

❖ Rasuwarta:

Ta rasu (RA) a shekara ta huɗu bayan hijira, a lokacin tana ‘yar shekara talatin, bayan ta auri Manzon Allah (SAW) da wata biyu ko uku.[3]

---

[1]. Siyaru a’alamin-nubala (3/476).
[2]. Albidaya wan-nihaya (4/90).
[3]. Siyar a’alamin-nubala (3/476).

Sai Annabi (SAW) ya sallace ta, sannan ya binne ta a maƙabartar Baƙi', kuma ita ce farkon wanda aka binne a maƙabartar Baƙi', kuma ta biyu cikin waɗanda suka rasu a rayuwar Manzon Allah (SAW) cikin matansa.

Auna fahimtarka a darusan mako na 15			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar: "Alhakum"?		A
	a. Ya shagaltar da ku daga yin ɗa'a ga Allah.	b. Ya jinkirtar da ku daga aiki.	c. Ya mayar da ku masu girman kai.
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin sabuban raina wasu mutane ga ni'imomin Allah akwai:		C
	a. Dogon buri.	b. Hango wanda yake sama da shi.	c. Zama da masu girman kai.
Darasin Aƙida	Tambaya: Ubangiji Shi ne wanda Yake da sifofi guda uku, su ne:		B
	a. Ji da gani da magana.	b. Halitta da mulki da jujjuya al'amura.	c. Daidaituwa da yarda da rahama.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin abubuwan da suke lalata taimama akwai:		C
	a. Rashin ruwa lokaci mai tsawo.	b. Gama salla.	c. Ikon amfani da ruwa.
Darasin Sira	Tambaya: Daga cikin waɗanda suka tabbatar da Abu Dalib a kan kafirci lokacin da mutuwa ta riske akwai:		A
	a. Abu Jahal.	b. Abu Lahab.	c. Abu Sufyan.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Zainab 'yar Khuzaima ta kasance ana kiran ta da suna ….. a lokacin Jahiliyya.		C
	a. Ummuɗ-Ɗayyibin	b. Ummul-Banin	c. Uwar Miskinai

MAKO NA GOMA SHA SHIDA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUZ-ZALZALA

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

إِذَا زُلۡزِلَتِ ٱلۡأَرۡضُ زِلۡزَالَهَا ﴿١﴾ وَأَخۡرَجَتِ ٱلۡأَرۡضُ أَثۡقَالَهَا ﴿٢﴾ وَقَالَ ٱلۡإِنسَٰنُ مَا لَهَا ﴿٣﴾

يَوۡمَئِذٖ تُحَدِّثُ أَخۡبَارَهَا ﴿٤﴾ بِأَنَّ رَبَّكَ أَوۡحَىٰ لَهَا ﴿٥﴾ يَوۡمَئِذٖ يَصۡدُرُ ٱلنَّاسُ أَشۡتَاتٗا لِّيُرَوۡاْ

أَعۡمَٰلَهُمۡ ﴿٦﴾ فَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٍ خَيۡرٗا يَرَهُۥ ﴿٧﴾ وَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ شَرّٗا يَرَهُۥ ﴿٨﴾

❖ Fassara:

Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.

1. Idan aka girgiza ƙasa, girgizawarta.
2. Kuma ƙasa ta fitar da kayanta, masu nauyi.
3. Kuma mutum ya ce "Mẽne ne ya same ta?
4. A rãnar nan, zã ta faɗi lãbãrinta.
5. Cewa Ubangijinka Ya yi umurni zuwa gare ta.
6. A rãnar nan mutane za su fito dabam-dabam domin a nuna musu ayyukansu.
7. To, wanda ya aikata (wani aiki) gwargwadon ƙwayar zarra, na alheri, zai gan shi.
8. Kuma wanda ya aikata gwargwadon ƙwayar zarra na sharri, zai gan shi.

❖ Saƙon da surar take ƙunshe da shi:

Tunatarwa game da irin wahalhalu na ranar tashin Alƙiyama, da kuma ƙalailaice ƙididdigar hisabi a cikinsa.

❖ Baƙin kalmomi:

زلزلت	Zulzilat	Idan aka jijjiga ta kuma aka karkaɗa ta sabo da tashin alƙiyama.
زلزالها	Zilzalaha	Tsananin girgiza ta
ما لها	Ma laha	Mene ne ya faru da ita, kuma ya sanya ta take tsananin girgiza haka?
يومئذ تحدث أخبارها	Yauma'izin tuhaddisu akhbaraha.	Za ta bayar da labarin dukkannin abubuwan da suka faru a kanta na alkhairi da na sharri, sannan kuma ta bayar da shaida a kanshi.
مثقال ذرة	Misƙala zarratin	Gwargwadon nauyin ƙaramar tururuwa, Ma'anar (Zarra) shine: ƙananan tururuwa.

❖ Ma'anar surar a dunƙule:

Wannan surar tana daga cikin surorin da suka sauƙa a Madina, tazo da saƙo domin tunatarwa game da wahalhalun ranar tashin Alƙiyama da kuma irin ƙalailaice ƙidɗiddigar hisabi da za a yi a cikinsa, sai Allah Maɗaukakin Sarki Yake bayar da labarin cewa: tabbas, lallai, a wannan rana ƙasa za tayi motsi kuma za tayi girgiza mai tsanani, saboda dukkanin abubuwan da suke kanta na duwatsu da gine-gine za su faɗi su ruguje, kuma dukkannin abubuwan da suke cikinta na mamata da kuma taskoki zasu fito waje, sai dukkan wanda ke ganin hakan ya ɗimauce, kuma sai kowanne ɗan'adam ya dinga tambayar cewa: To mene ne ya faru da ita ƙasar ne?.

Sannan, kuma Ubangiji wanda albarkatunsa suka yawaita kuma Shi ma Ya ɗaukaka, sai Ya yi hukunci tsakanin bayinsa, kuma Ya yi musu hisabi a kan dukkan abubuwan da suka aikata, har sai Allah Maɗaukakin Sarki ya umarci ƙasa da tayi furuci, kuma ta bayar da shaida a kan dukkan abin da aka aikata a kanta na alkhairi ko na sharri, a yayin da Allah Ya gama yin hukunci a tsakaninsu, sai su koma daga farfajiyar yanke hukunci ta ranar alƙiyama a rarrabe, kuma suna masu fifiko a tsakanin junansu, domin kuwa za a nuna musu sakamakonsu, kuma babu wani abin da zai tozarta daga cikin ayyukansu, koda kuwa daidai da gwargwadon nauyin tururuwa ne.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Tabbatar da aƙidar cewa; akwai tashi bayan mutuwa, da kuma samun sakamakon abin da aka aikata, da kuma bayanin tsananin wahalhalun ranar tashin alƙiyama.
2. Kwaɗaitarwa a kan dawwama a kan aikata alheri ko da kuwa ya kasance ɗan kaɗan ne, domin kuwa tabbas sai an bijiro da shi ga bawa a ranar tashin alƙiyama, babu makawa.
3. Tsawatarwa a kan aikata sharri ko da kuwa ya kasance ɗan kaɗan ne, saboda tabbas za a bijiro da shi a ranar tashin alƙiyama, ba makawa.
4. Lallai, tabbas, ƙasa zata bayar da shaida a kan dukkan abin da ɗan’adam ya aikata a kanta na alheri ko na sharri.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

ABIN DA ALLAH YAKE LA'AKARI DA SHI GAME DA BAYINSA

An ruwaito daga Abu Huraira (RA), ya ce: Manzon Allah (SAW), ya ce: (**Lallai, tabbas, Allah ba ya kallon gangar jikinku ko dirin surar halittarku, sai dai kawai Shi Allah Yana ganin zukatanku ne da kuma ayyukanku**). [1]

❖ Sharhi:

A cikin wannan hadisi, akwai wani al'amari wanda aka kore faruwarshi, da kuma wani al'amarin wanda aka tabbatar da faruwarshi, al'amarin da aka kore faruwarshi kuwa shi ne: kallon da Allah zai yi zuwa ga gangar jikin bayi da kuma dirin surar halittarsu, da kuma yi musu sakamako a kan hakan. Amma abin da aka tabbatar da faruwarshi kuwa shi ne: kallon da Allah Yake yi zuwa ga dukkanin abin da ke cikin zukatan bayi na tsantsanta bauta ga Allah, da kuma kallonsa zuwa ga ayyukansu, shin ayyuka ne nagartattu ko kuma saɓanin hakan ne.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Lallai samun falalar fifiko tsakanin bayi ba ta hanyar ƙarfin gangar jikinsu ko rauninsu yake kasancewa ba, kuma ba ta hanyar kyawun dirin halittarsu ko muninsa yake kasa ruwa ba, bari dai, kawai fifiko yana samuwa ne a sanadiyyar abin da ke cikin zukatansu na imani, da kuma gaskiya, da ikhlasi da kuma taƙawa.
2. Ya wajaba a kan dukkan musulmi ya dinga kula da halin da zuciyarshi take ciki, da kuma koƙarin inganta kuɗirinsa na zuci, da

[1] . Muslim ne ya rawaito shi (2564).

kuma tsarkake shi daga kowacce irin mummunar siffa, saboda ikhlasi shi ne mai gyara dukkanin ayyukan da gaɓɓai suke yi.

3. Lallai karɓan ayyuka yana ginuwa ne a kan waɗannan sharuɗɗa guda biyu: Ɓoyayyen sharaɗi na cikin zuciya; kuma shi ne tsantsanta niyya ga Allah. Da kuma sharaɗi na zahiri da a kan iya gani a cikin ayyuka ta hanyar dacewa da shiriyar Annabi (SAW).

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA ULUHIYYAR ALLAH (KAƊAITUWARSA DA CANCANTAR BAUTA)

Tauhidin Uluhiyya: Shi ne kaɗaita Allah Mai girma da ɗaukaka da kowane irin nau'i na bauta.

Domin kaga ma'anar (Allah) shi ne: Abin bauta. Wato wanda ake bauta masa tare da son Shi da kuma girmama Shi.

Kuma ma'anar imani da Uluhiyyar Allah shi ne: ƙudurta cewa lallai Allah Shi kaɗai ne abin bauta na gaskiya, wanda ba shi da wani abokin tarayya.

Kuma haƙiƙa Allah Ya tabbatar da Uluhiyyarsa kuma Ya kore uluhiyyar waninsa da dalilai na shari'a da na hankali.

❋ **Daga cikin dalilai na shari'a akwai:**

- Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma Ubangijinku Ubangiji Guda ne. Bãbu wani Ubangiji fãce Shi, Mai rahama, Mai jin ƙai)).[1]
- Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma Allah Ya ce: "Kada ku riƙi abũbuwan bautã biyu. Abin sani kawai, wanda ake bautã guda ne, sa'an nan sai ku ji tsõro Na, Ni kaɗai)).[2]
- Sai kuma Allah Ya bayar da labarin maganar dukkanin Manzanni (AS) ga mutanensu: ((Lallai ne, haƙĩƙa Mun aika Nũhu zuwa ga mutãnẽnsa, sai ya ce: "Yã ku mutãnẽna! Ku bauta wa Allah! Bã ku da wani abin bauta koma bayansa. Lalli ne nĩ, inã tsõrace muku azãbar wani yini mai girma)).[3]

---

[1] . (ALbaƙara: 163).
[2] . (Annhal: 51)
[3] . (Al'A'araf: 59)

- Kuma Allah Ya bayyana ƙarara cewa: dukkanin wani abin bautar da ake bauta wa koma bayan Shi, to bautar ta karya ce, sai Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Wannan! sabõda lallai Allah, Shĩ ne Gaskiya, kuma lallai abin da suke kira koma bayansa shi ne ƙarya. Kuma lallai Allah, Shĩ ne Maɗaukaki, Mai girma)).[1]

❋ **Daga cikin dalilai na hankali kuwa akwai:**

- Lallai tabbas, waɗannan ababen bautar nasu, kwata-kwata ba su da wani abu daga cikin keɓantattun abubuwan da ya kamata a ce wanda ake bauta masa ya ƙebantu da su, saboda kuwa su karan kansu ma halittar su aka yi, wanda ba za su iya halittar komai ba kuma ba za su taɓa iya kawo wani alfanu ba, ko kuma su tunkuɗe wata magunya ba, kamar yadda kuma su ababen bautar nasu ba za su iya mallakar rayuwa ko mutuwa ba. Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma suka riƙi abũbuwan bauta koma bayansa, bã sa yin halittar kõme alhãli sũ ne ake halittã, kuma bã sa mallakar wa kansu wata cũta ko wani amfãni, kuma bã sa mallakar mutuwa kuma bã sa mallakar rãyarwa, kuma bã sa mallakar tãyarwa)).[2] Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Shin, sunã shirka da abin da bã ya halittar kõme, kuma sũ ne ake halittã? () Kuma ba su iya bãyar da taimako gare su, kuma kansu ma, bã su iya taimaka!)).[3]

Idan kuwa wannan shi ne irin hali da ababen bautan nasu suke ciki, to ashe kuwa, bauta musu ya zama mafi wautar al'amura, kuma mafi zama ƙarya fiye da kowacce irin ƙarya, kuma mafi zama wauta fiye da kowacce irin wauta.

- Cewa lallai tabbatarwar da mushirikai suka yi na Tauhidin Rububiyyar Allah (wato: kadaita Allah da ayyukansa) da kuma

[1] . (Alhajji: 62).
[2] . (Alfurƙan: 3).
[3] . (Al-A'araf: 191- 192)

tabbatarwar da suka yi kan cewa shi ne ya halicce su, to hakan yana lazimta musu cewa dole ne, su kaɗaita shi ta fuskar Tauhidin Uluhiyya, ka ga ashe wanda yake yin ni’imar halitta, da kuma samarwa daga babu, da kuma bayar da arzuƙi, shi ne yafi kowa cancantar a yi masa godiya da ibada, da ikhlasi; kamar dai yadda Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Yã ku mutãne! Ku bauta wa Ubangjinku, Wanda Ya halicce ku, kũ da waɗanda suke gabãninku, don ku samu taƙawa! () Wanda Ya sanya muku ƙasa shimfiɗa, sama kuma gini, kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sa'an nan Ya fitar da abinci daga 'ya'yan itãtuwa da shi, sabõda ku. Sabõda haka kada ku sanya wa Allah wasu kĩshiyõyi, alhãli kuwa kuna sane)).[1]

[1] . (Albaƙara: 21-22)

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SALLOLI BIYAR

- **Matsayin salla:**

Salla ita ce ginshiƙin Musulunci kuma mafi ƙarfin rukunai na Musulunci bayan kalmar shahada, kuma haƙiƙa Allah Mai girma da ɗaukaka ya farlanta salla ne a kan Annabinsa Muhammadu (SAW) a cikin daren Mi'iraji tun daga saman sammai bakwai, saɓanin sauran ibadu, kamar yadda kuma ita ce shugaba kuma jagora ta dukkanin ibadu da ake yinsu da gangar jiki, saboda haƙiƙa ta ƙunshi nau'ikan ibadu masu yawa a cikinta, kamar: zikiri, da karatun Alƙur'ani, da tsayuwa a gabansa, da ruku'i, da sujjada, da addu'a, da tasbihi da kabbara.

- **Falalar salloli biyar:**

Haƙiƙa ayoyi da hadisai masu yawa sun zo da bayani a kan falalar sallolin nan guda biyar tare da kuma kwaɗaitarwa akan yin su, daga cikinsu akwai:

- Faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ((Ku kula da sallõli da kuma salla mafificiya. Kuma ku tsaya kuna mãsu ƙanƙan da kai ga Allah)).[1]
- Da kuma faɗin Manzon Allah (SAW): (Salloli guda biyar ɗin nan, da kuma Juma'a zuwa wata Juma'ar, da kuma Ramadana zuwa Ramadana, suna zama kaffarar zunubai da suke samuwa tsakaninsu, matukar dai an guje wa manya-manyan zunubai).[2]
- Da kuma faɗin Manzon Allah (SAW): (Ku ba ni labari mana, idan ya kasance akwai wata ƙorama a ƙofar gidan ɗaya daga cikinku, kuma zai dinga yin wanka a cikinta har sau biyar a kowacce rana,

[1] . Suratul Baƙara: Aya ta (238)
[2]. Muslim ne ya rawaito (233).

shin akwai wata daudɗa da za ta rage tare da shi, sai suka ce: a a, babu wata daudɗar da za ta rage a jikinsa sai ya ce: to kamar haka ne misalin sallolin nan guda biyar, haka Allah Yake kankare kurakurai da su).[1] Abinda ake nufi da (Addaran: shi ne daudɗa ko datti).

- Da kuma fadinsa (SAW): (Shugaba ko jagoran dukkan al'amari shi ne: Musulunci, kuma ginshiƙinsa shi ne salla, kuma mafi ƙololuwar tozonsa shi ne jihadi don ɗaukaka kalmar Allah).[2]

❁ **Kamar yadda kuma alƙawarin narko ya zo a haƙƙin duk wanda ya bar salla ko ya yi sakaci da ita:**

- Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Sai wasu suka maye gurbinsu bãyansu suka tõzarta salla, kuma suka bi sha'awõwinsu. To, da sannu zã su haɗu da wani sharri)).[3]
- Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Su ce musu) "Me ya shigar da ku cikin Saƙara?" () Suka ce: "Ba mu kasance munã cikin mãsu salla ba.")).[4]
- Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Alƙawarin da yake tsakaninmu da su shi ne salla, saboda haka, duk wanda ya bar ta, to haƙiƙa ya kafirce)).[5]

[1]. Bukhari ne ya rawaito (528), da Muslim (667).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito (2616).
[3] . (Maryam: 59).
[4] . (Almuddassir: 42-43)
[5]. Muslim ne ya rawaito (134).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

TAFIYAR ANNABI (SAW) ZUWA ƊA'IF

Masifu ba su gushe ba ɗaya-bayan-ɗaya suna ta cigaba da faruwa ga Manzon (SAW) tun bayan mutuwar baffansa Abu Ɗalib da kuma matarsa Khadija, sannan kuma tsagerancin da mushirikai suke yi masa ya ci gaba da ƙaruwa, kuma cutarwar da suke yi a gare shi ta tsananta, kuma ya ji garin Makka ya masa ƙunci, kai har sai da ya ɗebe tsammanin samun wani sauki daga gare su, sannan kawai sai ya ɗaura niyyar ficewa daga Makka zuwa Ɗa'if, yana mai sa rai ko wata ƙila zai samu wanda za su taimaka masa daga cikin ƙabilar Saƙif, hakan ya faru ne a cikin watan Shawwal, bayan shekara goma da aiko shi a matsayin Manzo, sannan kuma ya yi wannan tafiyar ne tare da yaron gidansa mai suna Zaidu ɗan harisa.

A yayin da suka iso cikin garin Ɗa'if kuwa, sai Annabi (SAW) ya kira su zuwa ga Musulunci, Nan take kawai sai suka gaggauta ƙaryata shi, suka yi inkarin maganarsa, kuma sai suka yi yekuwa domin tara masa mutanensu, sai suka fara jifansa da duwatsu har sai da suka yi masa jina-jina a dunduniyyar ƙafafunsa, kuma suka fasa masa kai, yaron gidansa Zaidu kuma kawai sai ya fara ƙoƙarin ba shi kariya daga cutarwar tasu, har sai da suka samu mafaka a cikin wani lambu mallakar Shaiba da Utba 'ya'yan Rabi'a.[1]

Sannan kuma sai suka kama hanyar dawowa garin Makka daga Ɗa'if, alhali kuwa shi Manzon Allah (SAW) yana cikin damuwa mafi tsananin damuwa, kawai sai ya ɗaga hannayensa guda biyu zuwa sama, ya kuma roƙi Allah ta hanyar yin wata addu'a mai girma, wacce dukkanninta cike take da nuna buƙatuwa da kuma neman mafaka a wajen Allah, sai ya ce: (Ya Allah zuwa gare ka

[1] . Albidaya wan-nihaya (3/135).

nake kai koken raunin ƙarfina, da kuma ƙarancin dabarata, da kuma ƙasƙancin da nake fuskanta a wajen mutane, ya wanda tausayinsa ya fi na dukkannin masu tausayi, kai ne Ubangijin dukkannin masu rauni, kuma kai ne fa Ubangijina, to wane ne wanda za ka jiɓintar da ni zuwa gare shi?, shin zuwa manesanci ne, wanda kawai sai dai ya fusata ni, ko kuma za ka mallakar da al'amarina zuwa ga maƙiyi ne?, Idan har ba Ka yi fushi da ni ba, to fa bazan damu ba, amma sai dai duk da haka fa lafiyarka ita ce mafi yalwa a gare ni, ina neman tsari da hasken fuskarka wanda a sanadiyyarshi ne dukkanin duhu yake haskaka, kuma dukkannin al'amarin duniya da na lahira yake gyaruwa, Ina neman tsari kada fushinka ya riske ni, ko kuma ɓacin ranka ya sauƙa a kaina, gare Ka ake neman yarda har sai Ka yarda, kuma babu wata dabara, kuma babu wani ƙarfi sai dai daga gareka).[1]

A yayin da suke tsaka da tafiya a kan hanya, sai Manzon Allah (SAW) ya ɗaga kansa, kawai sai ga inuwar wani girgije ta lulluɓe shi, kuma kawai sai ga Mala’ika Jibrilu a cikinta, sai Malal'ika Jibrilu ya ce da shi: Lallai Allah Ya ji zancen da mutanenka suka faɗa maka, da kuma irin martani da suka maka, kuma haƙiƙa Ya aiko Mala'ikan Duwatsu zuwa gare ka, domin ka umarce shi da dukkan abin da kake so ya yi musu, sai Mala'ikan Duwatsun ya ce: Ya kai Muhammadu, idan kana so, zan rufto da manyan duwatsu guda biyu na Makka (Wato dutsen Abu Ƙubais da dutsen Ƙu’aiƙu’a)? a kansu, sai Annabi (SAW), ya ce: (a a, bari dai, ina fatan Allah Ya fitar da waɗanda za su bauta wa Allah Shi kaɗai, ba tare da sun haɗa Shi da wani abokin tarayya ba daga cikin tsatsonsu).[2]

[1] . Darimi ne ya rawaito shi (14/139).
[2] . Bukhari ne ya rawaito shi (3231), da Muslim (1795).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

UMMU SALAMA (RA)

- **Sunanta da haifuwarta:**

Ita ce: Ummu Salama, Hindu ‘yar Abu Umayya, daga ƙabilar Banu Makhzum, tafi shahara da alkunyarta “Ummu Salama”, ana danganta ta ne da ɗanta mai suna Salama.

An haife ta ne a garin Makka tun kafin aiko Annabi (SAW), a da shekaru goma sha bakwai (17).

- **Tarihinta da falalarta:**

Ummu salama (RA) ta kasance daga cikin mata mafiya kyawu, kuma mafiya ɗaukakar ɗangi, an san ta a cikin mata da haƙuri da kuma sadaukarwa, ta kasance daga cikin mutanen da suka riga kowa shiga Musulunci, kuma tana daga cikin waɗanda suka yi hijira tun a karon farko.

Ta musulunta tun da wuri, tare da mijinta Abu Salama, wanda ɗan uwane ga Annabi (SAW) ta fuskar shayarwa, kuma ta yi hijira zuwa Habasha tare da shi hijira biyun duka, kuma yayin da ta dawo Makka kuwa, ta fuskanci cutarwa mai yawa daga mushirikai ita da mijin nata gaba ɗayansu.

Sannan sai ta yi hijira zuwa Madina, ba a ɗauki wani tsawon lokaci ba sai mijinta (RA) ya rasu, cikin shekara ta huɗu bayan Hijira. Sai Annabi (SAW) ya aure ta, kafin hakan kuwa, Abubakar (R.A) ya nemi aurenta, amma sai ta ƙi amincewa da hakan, kuma shi ma Umar (R.A) ya nemi aurenta, amma sai ta ƙi amincewa da hakan, sai Annabi (SAW) ya nemi aurenta, sai ta aure shi.

Ta kasance tana cewa dangane da hakan: Na ji Manzon Allah (SAW) yana cewa: (Babu wani musulmi da wata masifa za ta same shi, sai kuma ya faɗi abin da Allah Ya umarce shi da ya faɗi: “Inna lillahi wa innaa ilaihi raaji’uun, Allahumma ajirni fi musibati wa akhlifni khairun minha”, ma’ana (Lallai tabbas dukkannin mu daga Allah muke, kuma zuwa gare shi za mu koma, Ya Allah Ka ba ni lada a kan wannan masifar kuma Ka maye min gurbinta da abin da yake mafi alkhairi ne fiye da ita); face sai Allah Ya maye masa gurbinta da mafi alkhairi fiye da ita. Ummu salama ta ce: A yayinda Abu Salama ya rasu, sai na ce: Waye kuwa daga cikin musulmi yafi Abu Salama alkhairi? Iyalan gidansa ne fa farkon gidan da suka yi hijira zuwa ga Manzon Allah (SAW), Kuma fa tabbas ni ɗin ce na faɗi hakan, sai ga shi kuma Allah Ya maye min gurbinsa da Manzon Allah (SAW).[1]

An san Ummu salama (RA) da ilimi, da kuma fahimtar addini, kuma ta shahara da kaifin hankali da kuma hikima, Annabi (SAW) ya shawarce ta a ranar da aka yi Sulhun Hudaibiya, a daidai lokacin da kowa daga cikin Sahabbai bai tashi ya yi aski da yanka ba, sai ta ce: Ya Annabin Allah, shin kana so su aikata hakan ne? To kawai ka tashi ka fita kuma kada ka yi wa kowa magana daga cikinsu, ko da daidai da kalma daya ce tak, har sai ka je ka soke raƙuminka, kuma ka ƙira wanzaminka ya yi maka aski, sai ya fita alhalin kuwa bai yi wa kowa daga cikinsu magana ba har sai da ya aikata hakan, sai ya soke raƙuminsa, kuma ya ƙira wanzaminsa ya zo ya yi masa aski, a yayin da suka ga hakan, kawai sai suka tashi suma suka soke raƙumansu, sai kuma suka fara yi wa junansu aski, sashensu na yi wa sashi aiki, har kamar sashinsu za su yi faɗa da sashi.[2]

[1]. Muslim ne ya rawaito dashi (918).
[2]. Bukhari ne ya ruwaito shi (2731).

Ta ruwaito Hadisai masu yawa daga Annabi (SAW), kuma ta samu rabautar ɗaukaka ta ganin mala'ika Jibrilu (AS) a lokacin da ya shigo wajen Annabi (SAW) a rikiɗe cikin kamannin Dihyatul kalbi, a lokacin ita kuma tana wajen Annabi (SAW).[1]

- **Rasuwarta:**

Ta kasance (RA) ita ce wadda ta rasu a ƙarshe, daga cikin uwayen muminai, ta rasu ne a ƙarshen shekara ta (61) bayan Hijira, a lokacin tana da shekara casa'in, kuma an binne ta ne a maƙabartar Baƙi'.

[1]. Bukhari ne ya ruwaito shi: (3634).

Auna fahimtarka a darusan mako na 16			**Amsa na ƙwarai**
Darasin Tafsiri	Tambaya: Me ake nufi da “Za ta ba da labaranta”?		B
	a. Za ta fitar da abin da ke cikinta.	b. Za ta ba da labarin abin da ya auku a kanta da alheri da na sharri.	c. Za ta sabunta mazaunanta.
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin sharuɗan karɓan aiki akwai:		C
	a. Yawansa da banbantansa.	b. Ƙoƙari.	c. Tsantsanta niyya ga Allah.
Darasin Aƙida	Tambaya: Tauhidin Uluhiyya shi ne?		A
	a. Kaɗaita Allah da dukkan nau’ukan bauta.	b. Kaɗaita Allah a sunayensa da siffofinsa.	c. Kaɗaita Allah cikin ayyukansa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Yaushe Allah Ya farlanta salla ga Annabinsa (SAW):		B
	a. A daren hijira.	b. A daren Mi’iraji.	c. Bayan buɗe Makka.
Darasin Sira	Tambaya: Annabi (SAW) ya fita don kiran mutanen Ɗa’if a shekara ta:		A
	a. 10 bayan hijira.	b. 8 bayan hijira.	c. 5 bayan hijira.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin abubuwan da suke nuni a kan ƙarfin hankalin Ummu Salama akwai:		C
	a. Matsayanta a yaƙin Badar.	b. Matsayanta a lokacin Isra’i da Mi’iraji	c. Matsayanta a ranar Sulhun Hudaibiyya.

MAKO NA GOMA SHA BAKWAI

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL -ADIYAT

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
وَٱلۡعَٰدِيَٰتِ ضَبۡحٗا ١ فَٱلۡمُورِيَٰتِ قَدۡحٗا ٢ فَٱلۡمُغِيرَٰتِ صُبۡحٗا ٣ فَأَثَرۡنَ بِهِۦ نَقۡعٗا ٤
فَوَسَطۡنَ بِهِۦ جَمۡعًا ٥ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لِرَبِّهِۦ لَكَنُودٞ ٦ وَإِنَّهُۥ عَلَىٰ ذَٰلِكَ لَشَهِيدٞ ٧ وَإِنَّهُۥ لِحُبِّ
ٱلۡخَيۡرِ لَشَدِيدٌ ٨ ۞ أَفَلَا يَعۡلَمُ إِذَا بُعۡثِرَ مَا فِي ٱلۡقُبُورِ ٩ وَحُصِّلَ مَا فِي ٱلصُّدُورِ ١٠ إِنَّ
رَبَّهُم بِهِمۡ يَوۡمَئِذٖ لَّخَبِيرُۢ ١١﴾

- **Fassara:**

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da (dawaki) masu sukuwa suna kukan ciki.
2. Sannan masu bugun ƙyastu da kofatai.
3. Sannan masu kai hari da asuba.
4. Sai suka tayar da ƙura da ita (sukawar tasu).
5. Sai kuma suka shiga tsakiyar taro (da mahayansu)
6. Lalle mutum tabbas mai yawan butulci ne ga Ubangijinsa.
7. Lalle kuma shi shaida ne a kan haka.
8. Lalle shi kuma mai tsananin son alheri ne.
9. Shin bai sani ba ne idan aka bankaɗo abubuwan da suke cikin ƙaburbura?
10. Aka kuma tattaro abubuwan da suke cikin ƙiraza?
11. Lalle a wannan ranar tabbas Ubangijinsu Masani ne game da su.

- **Saƙon da surar ta ƙunsa:**

Tsawatar da ɗan’adam a kan musuntawa, da kwaɗayi, da kuma tunatar da shi game da lahira.

- **Bakin kalmomi:**

العاديات	Al’adiyat	Dawakai masu gudu a filin yaki.
ضبحا	Dabha	Lafazin (Addabhu) na nufin sautin nishinsu a cikin kirjinsu lokacin tsananin gudu.
فالموريات قدحا	Falmuriyat kadha	Masu kesta wuta da kofotunsu.
فالمغيرات صبحا	Falmugirati subha	Wadanda suke kai farmaki a bazata da safiya ga abokan gaba.
نقعا	Nak’a	Kura.
فوسطن به جمعا	Fawasadna bihi jam’a	Sai suka keta tsakiyan taron abokan gaba suna dauke da mahayansu.
لكنود	Lakanud	Musu.
وحصل ما في الصدور	Wa hussila ma fis-sudur	Aka cire abin da ke cikin zukata na da imani da kafirci kuma aka bayyana shi.

- **Ma’anar surar a dunkule:**

Ayoyin nan masu karamci sun kunshi wata rantsuwa mai girma wacce Allah Ya yi ta da dawaki, wadanda suke ma’abota siffofi ne da babu wasu dawakai da suka yi tarayya da su a cikinsu. Sun kasance ma’abota gudu ne, da kesta wuta, da tayar da kura, da kuma kai farmaki, domin kuwa su idan har suka yi irin tasu makurar sukuwar ta karshe, cikin gaggawa, to su fitar da sautin haniniyarsu da kuma numfashinsu, kuma kofatonsu ya kunna wuta a kan dutse

idan yakarce she da daddare, kuma sai su tayar da ƙura, kuma su kai farmaƙi ga abokan gaba, sai su musu bazata da safiya, sai ka ga sun kutsa tsakiyar taron abokanan gabar suna ɗauke da mahayansa.

Wannan rantsuwar an yi ta ne domin ta ƙara ƙarfafa wani haƙiƙanin al'amari mafi girma, wanda shi ne kafircewar ɗan'adam ga Ubangijinsa, da kuma musuntawarsa ga ni'imominsa a kanshi. Shi mutum har kullum yana neman a ba shi abin da haƙƙinsa ne, amma kuma yana hana abin da ake buƙatar ya bayar, yana kuma ƙirga masifu, kuma sai ya manta da ni'imomi, to, shin ko wene irin hali zai shiga idan aka bankaɗo dukkannin abubuwan da ke cikin ƙaburbura? kuma aka fitar da dukkan abin da ke cikinsu na mutane, kuma aka tsayar da su a gaban Allah domin yin hisabi da kuma bayar da sakamako, kuma aka bayyana dukkan abin da ke ɓoye a zukata na ƙudurori da niyyoyi, kuma babu wani abu daga gare su wanda zai ɓuya ga Allah mai ƙididdigewa, kuma masanin komai.

- **Abubuwan da za mu koya daga surar:**

1. Tabbatar da aƙidar cewa akwai tashi bayan mutuwa, da kuma bayar da sakamako.

2. Lallai shi ɗan'adam mai yawan kafirce wa Ubangijinsa ne, sai dai fa kawai idan ya yi imani kuma ya yi aiki nagari.

3. Lallai ɗabi'ar ɗan'adam an gininta ne a kan inkarin haƙƙoƙi da kuma hanasu, koda kuwa haƙoƙoƙin tsakaninsa da Mahaliccinsa ne, ko kuma abokin halitta dan uwansa ne, sai wanda Allah Ya shiryar da shi ne.

4. Lallai tabbas, dukkannin sirrace-sirrace za su bayyana a fili ƙarara, a ranar tashin alƙiyama.

5. Lallai tabbas, son dukiya da kuma ratayuwar zuciya da ita, yana daga cikin sabuban da ke jawo gafala daga tuna lahira.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WAJIBCIN NEMAN YARDAR IYAYE, DA JAN KUNNE A KAN FUSATA SU

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru, Allah (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Samun yardar Allah yana cikin samun yardar iyaye, kuma fushin Allah Yana cikin fushin iyaye).[1]

❖ Sharhi:

Wannan Hadisi dalili ne a kan falala da kuma wajibcin yin biyayya ga iyaye, da kuma cewa sababi ne na samun yardar Allah maɗaukaki, da kuma tsawatarwa a kan saɓa wa iyaye haramcin hakan, da kuma cewa lallai sababi ne da ke jawo fushin Allah, don haka, dukkan wanda ya samu yardarsu, to haƙiƙa ya samu yardar Allah madaukaki, kuma dukkan wanda ya fusatar dasu, to haƙiƙa ya fusatar da Shi.

Kuma irin biyayyar da Allah da Manzonsa (SAW) suka yi umarni da shi, shi ne: Kowane irin kyautatawa ta magana ko ta aiki, kamar tausasawa da kuma tausayawa musu, da nuna musu jin ƙai, da kuma kyautata musu mu'amala, da kuma biya musu dukkannin buƙatunsu, kamar dai yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma ku kyautata wa iyaye, matuƙar kyautatawa)).[2] Wannan kuma an ƙayyade shi da ya zama a abin da ba saɓa wa Allah ba ne; domin lallai babu biyayya ga wani abin halitta wurin saɓa wa Mahalicci.

[1] . Tirmizi ne ya rawaito shi (1899).
[2] . (Annisa'i: 36)

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Wajibcin kyautata wa iyaye, ta hanyar lura da kuma kulawa da su, da kuma tausaya musu, kuma lallai yin hakan, wani sababi ne na samun yardar Allah Maɗaukaki.
2. Haramcin saɓawa iyaye, kuma lallai yin hakan, yana wajabta wa mutum riskar fushin Allah Maɗaukaki.
3. Lallai ana samun sakamakon aiki ne gwargwadon irin jinsin aikin da aka yi, saboda haka, dukkannin wanda ya samu yardar iyayen sa, to shi ma Allah Ya yarda da shi, wanda kuwa ya yi akasin hakan, to shi ma akasin hakan ne zai same shi.
4. Tabbatar wa Allah siffofi guda biyu, siffar yarda da kuma siffar fushi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA SUNAYEN ALLAH DA SIFFOFINSA.

Imani da sunayen Allah da siffofinsa: Shi ne tabbatar da dukkan abin da Allah Ya tabbatar wa kansa, ko kuma Manzonsa (SAW) ya tabbatar masa, na sunaye da siffofi, da kuma kore dukkannin abubuwan da Allah Ya kore wa kansa, ko kuma Manzonsa (SAW) ya kore masa, ba tare da kwatanta yadda yake ba, ko kamantawa, kuma ba tare da karkatarwa ba ko korewa.

Allah maɗaukaki yace: ((Kuma Allah Yanã da sũnãye mãsu kyau. Sai ku rõƙe shi da su, kuma ku bar waɗanda suke yin ilhãdi a cikin sũnãyensa: zã a sãka musu abin da suka kasance sunã aikatãwa)).[1] Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Babu wani abu tamkarsa ba, kuma Shĩ ne Mai ji, Mai gani)).[2]

Kuma sunayen Allah da siffofinsa dakatawa ake yi game da lamarinsu, ba ya halatta a tabbatar da wani abu daga cikinsu ga Allah, face sai da nassin Alƙur'ani, ko ingantacciyar sunna; saboda Shi Allah tsarki ya tabbata a gare shi, shi ne yafi sanin kansa, kuma shi yafi kowa sanin irin abin da ya dace da shi, kuma Manzonsa (SAW) shi yafi dukkannin halittu sanin waye Allah, kuma shi ne mai isar daga gare Shi.

*** Kuma haƙiƙa nassoshi masu yawa sun zo suna masu ambaton sunayen Allah da siffofinsa, don haka wajibi ne a kanmu mu tabbatar da haka kuma mu sallama ga hakan, daga cikin waɗannan nassoshin akwai:**

[1] . (Al-A'araf: 180).
[2] . (Ash-shura: 11).

- Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Allah, bãbu wani Ubangiji fãce Shi, Rãyayye, Mai tsayuwa da kõme, gyangyaɗi ko bacci bã ya kãma Shi)).[1]
- Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Shĩ ne Allah, wanda bãbu abin bautã fãce shi, Mai mulki, Mai tsarki, Aminci, Mai amintarwa, Mai Tsarẽwa, Mabuwãyi, Mai tilastãwa, Mai nuna isa, tsarki ya tabbata a gare Shi daga abin da suke yi na shirka da Shi)).[2]
- Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Mai rahama, Ya daidaita a kan Al'arshi)).[3]
- Kuma Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, yace: (Ubangijinmu Mai girma da ɗaukaka yana sauƙowa zuwa ga saman duniya a cikin kowane dare, a daidai lokacin da ɗaya bisa ukun ƙarshe na dare ya rage, sai Ya dinga cewa: Wa zai kira ni, sai na amsa masa, wa zai roƙe ni na ba shi abin da ya roƙa, wa zai nemi gafarata, sai na gafarta masa)).[4]
- Kuma ya yayin da aka tambayi Imamu Malik game da siffar daidaituwa a kan al’arshi, sai ya ce: shi lafazin daidaituwa kam sananne ne, amma kwatanta tayaya yake kuma, abu ne da ba a san shi ba, kuma yin imani da shi wajibi ne, kuma yin tambaya a kan hakan bidi’a ce”.[5]

Abin da ake nufi: Lallai tabbas yin tambaya domin sanin yaya Allah Ya daidaita a kan al’arshi yana daga cikin ƙirƙirarrun bidi’o'i, kuma hakan shi ne abin da dukkan Ahlus-sunna suka faɗa game dukkannin siffofin Allah.

---

[1] . (Albaƙara: 255).
[2] . (Alhashr: 11).
[3] . (Ɗaha: 5).
[4] . Bukhari ne ya ruwaito shi (1145), da Muslim (758).
[5] . Al-lalaka’i ne ya rawaito shi (3/398).

Kuma lallai ƙungiyoyi biyu sun ɓata a game da sunayen Allah da siffofinsa:

Ta farko daga cikinsu ita ce: Ƙungiyar (Mu'aɗɗila), su ne waɗanda suka yi inkarin sunayen Allah da kuma siffofinsa ko wasu daga cikinsu, suna masu riya cewa lallai tabbatar da su ga Allah yana lazimta kamanta Allah Maɗaukaki da halittunsa, wannan zaton kuwa yana daga cikin mafi munin ƙarya.

Ƙungiya ta biyu ita ce ƙungiyar (Mushabbiha), su ne waɗanda suka kamanta siffofin Allah Maɗaukaki da na bayinsa, alhali kuma suna masu riya cewa lallai yin hakan shi ne abin da za a fahimta daga cikin nassosin ayoyi da hadisai da suke bayani game da sunayen Allah da siffofinsa.

Kuma kowacce ɗaya daga cikin kungiyoyi biyun ta ɓata, kuma ta kauce wa Alƙur'ani da sunna, kuma ta saɓa wa magabatan ƙwarai na wannan al'ummar wajen fahimtar sunayen Allah da siffofinsa, Ibnu Rajab, yace: "Dukkanin magabata na ƙwarai sun haɗu a kan zartar da fahimtar waɗannan nassosin kamar yadda suka zo ba tare da wani ƙari ko ragi ba - wato yana nufin: ayoyi da Hadisai da suke bayani game da siffofin Allah -, kuma dukkan wani abu da fahimtarsa ta rikitar daga cikinsu kuma hankali ya gaza wajen riskar su, kawai sai a mayar da shi zuwa ga Masaninshi".[1]

[1] . Fathul-Bari (2/334).

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

LOKUTAN SALLA

Sallolin farilla suna da keɓantattun lokutansu a cikin sharia, waɗanda ya wajabta a kan kowanne musulmi ya san su, ya kuma kula da su, Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Lallai ne salla tã kasance a kan mũminai, farilla mai ƙayyadadden lõkuta)).[1] Kuma a lokacin da ka tambayi Manzon Allah (SAW) wane aiki ne ya fi soyuwa a wajen Allah? Sai ya ce: (Salla a kan lokacinta).[2]

Lukutan sallolin suna nan kamar haka:

❋ **Lokacin sallar Asubahi:** Yana farawa ne daga ɓulluwar al'fijir na gaske, idan kuma ka kasance a kan tudu (gurin da ba kogi ba), kuma a gefanka babu haske, to idan har ka ga wani miƙaƙƙen haske ta ɓangaren gabas, wanda ya bayyana daga arewa zuwa kudu, to haƙiƙa alfijir ya ɓullo. Kuma lokacin sallar asuba yana ƙarewa da zarar rana ta ɓullo, amma kuma gagguta yin ta a farkon lokacinta shi ne abin da ya fi falala; saboda faɗin Allah Mai buwaya da ɗaukaka: ((Ku yi tsẽre zuwa ga ayyukan alhẽri)).[3]

❋ **Lokacin sallar Azahar:** Yana farawa ne daga zawali, har zuwa lokacin da inuwar kowanne abu za ta zama daidai da shi, ta fuskar tsawo. Kuma abin da ake nufi da (zawali) shi ne karkacewarta daga barin tsakiyar sama zuwa ga bangaren yamma, kuma akan iya sanin hakan ta hanyar kafa wani itacen katako ko sanda a cikin ƙasa, matuƙar inuwarsa tana raguwa, to rana batayi zawali ba, a yayin da kuma ta tsaya a waje ɗaya ba ta raguwa, kuma ta fara ƙaruwa, to tabbas haƙiƙa rana ta riga ta yi zawali, kuma loakcin sallar Azahar ya yi.

---

[1] . (Annisa'i: 103).
[2] . Bukhari ne ya ruwaito shi (527), da Muslim (85).
[3] . Suratul Baƙara (143).

Amma kuma alamar da ake gane zawali ta hanyar awanni, to kawai sai ka raba lokacin da yake tsakanin ɓullowar rana zuwa faɗuwarta kashi biyu, to wannan shi ne zawali, idan muka ƙaddara cewa rana tana ɓulluwa ƙarfe shida na safe, kuma tana faɗuwa karfe shida na yamma, to lokacin zawali shi ne ƙarfe goma sha biyu na rana kenan. Kuma gaggauta yin sallar Azahar a farkon lokacinta shi ne ya fi falala, sai dai fa idan cikin lokacin tsananin zafin rana ne, to sunna ne a jinkirta yin ta, a kuma sanyaya ta zuwa kusa da sallar La'asar, saboda faɗin Annabi (SAW): (Idan zafi ya tsananta, to ku sanyaya yin salla, saboda tabbas, shi tsananin zafi daga hucin jahannama yake).[1]

❋ **Lokacin sallar La'asar):** Shi kuma yana farawa ne tun daga ƙarshen lokacin sallar Azahar har zuwa lokacin hantsin bora, wato sakaliyar la'asar, daf da faɗuwar rana kenan, lokacin larurinta kuma zai cigaba har zuwa faɗuwar rana, kuma an sunnanta a gaggauta yin ta a farkon lokacinta.

❋ **Lokacin sallar Magariba:** Shi kuma yana farawa ne tun daga faɗuwar rana har zuwa lokacin da jaja-jajan sauran hasken rana da kuma shafaƙi za su gushe daga sararin samaniya, gwargwadon lokacinsa kuwa ta hanayar sa'o'i; to ya kan yi tsawo kuma ya kan yi gajarta, bisa ga saɓanin yanayin lokacin shekar, amma kuma ya kan kai-kumo a tsakanin sa'a ɗaya da kwata, zuwa sa'a ɗaya da rabi da minti uku. kuma Sunna ce a gaggauta yin ta.

❋ **Lokacin sallar Isha'i:** Yana farawa ne tun daga lokacin bacewar jan shafaƙi, kuma yana ƙarewa a lokacin da dare ya raba, kuma alamar rabin dare ya yi ta hanyar sa'o'i, ita ce: Lokacin ke tsakanin faɗuwar rana har zuwa ɓulluwar alfijir, sai ka raba shi gida biyu, to wannan shi ne ƙarshen lokacin sallar Isha'i. Idan kuma muka ƙaddara cewa: rana tana faɗuwa ne daidai ƙarfe biyar, alfijir kuma

[1] . Bukhari ne ya ruwaito shi (533), da Muslim (643).

yana ketowa ne ƙarfe biyar na asubahi, to tsakiyar dare za ta kasance ita ce: ƙarfe goma sha ɗaya na dare kenan, kuma sallar Isha’i lokacin larurinta yana zarcewa har zuwa ketowar alfijir.

Kuma mustahabbi ne a jinkirta yin sallar Isha’i har zuwa ƙarshen lokacinta, wato daf lokacin tsakiyar dare, matuƙar dai idan yin hakan ba zai zama mai wahalarwa ba, saboda haƙiƙa, "Annabi (SAW), yana son ya jinkirta yin salar] Isha’i".[1] Idan kuma jinkirtawar za ta wahalar da mamu, to mustahabbi ne a gaggauta yin ta, domin a kawar da wahalar, kuma domin kwaɗayin yin ta a cikin jam’i, saboda yin salla cikin jam’i wajibi ne, shi kuma jinkirta yin sallar Isha’i mustahabbi ne, don haka, ba za a bar aikata wajibi saboda mustahabbi ba.

[1] . Bukhari ne ya ruwaito shi (522) da Muslim (643).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ISRA'I DA MI'IRAJI

Bayan baƙin cikin da ya samu Annabi (SAW) a cikin shekarar da ake ƙira: (shekarar bakin ciki), da kuma irin ƙoƙarin kunyatarwa da mutanen Ɗa'ifa suka yi masa, sai Ubangijinsa ya lallashe shi, ya kuma karrama shi da samun damar tafiya ta Isra'i da Mi'iraji, (Isra'i: Shi ne tafiyar cikin dare daga Makka, Mi'iraji kuma: Shi ne tafiyar da aka yi ta hawa sama daga Masallacin Ƙudus har zuwa sama ta bakwai), an yi wannan tafiya ne don darajta Annabi da karrama shi; ((Tsarki ya tabbata ga wanda Ya yi tafiyar dare da bãwansa da dare, daga Masallaci mai alfarma zuwa ga Masallaci mafi nĩsa wanda Muka sanya albarka a kwewayensa, dõmin Mu nũna masa daga ãyõyinmu. Lallai ne Shi, shĩ ne Mai ji, Mai gani)).[1]

Sai aka yi Isra'i da Manzon Allah (SAW), tun daga Masallacin mai alfarma har zuwa Masallacin Ƙudus yana haye a kan wata dabba da ake ƙira "Buraƙ", yana tare da mala'ika Jibrilu (AS), Sai Annabi (SAW) ya sauƙa a Masallacin Ƙudus ya kuma yi limancin salla ga Annabawa.

Sannan sai aka yi sama da shi tun daga Masallacin Ƙudus har zuwa sama ta ɗaya, sai mala'ika Jibrilu ya nemi izinin a buɗe masa ƙofa, sai aka buɗe masa, sai ya ga Annabi Adamu (AS) a sama ta ɗaya.

Sannan sai aka sake hawa da shi zuwa sama ta biyu, sai ya ga Annabi Yahaya, da kuma Annabi Isa ɗan Marayama (AS).

Sannan aka sake hawa da shi zuwa sama ta uku, sai ya ga Annabi Yusuf ɗan Annabi Ya'aƙuba a cikinta.

[1] . (Isra'i: 1).

Sannan aka sake hawa da shi zuwa sama ta huɗu, sai ya ga Annabi Idrisa (AS).

Sannan sai aka sake hawa da shi zuwa sama ta biyar, sai yaga Annabi Haruna ɗan Imrana (AS).

Sannan aka sake hawa da shi zuwa sama ta shida, sai ya ga Annabi Musa ɗan Imrana (AS).

Sannan sai aka sake hawa da shi zuwa sama ta bakwai, sai ya ga Annabi Ibrahim (AS) a cikinta.

Kuma kowanne daga cikin Annabawan da ya gansu sai da ya yi masa maraba da zuwa, kuma ya tabbatar da annabtarsa.

Sannan sai aka sake yin sama da Manzon Allah (SAW), har zuwa wajen (Sidratul Muntahaa) wato Magaryar Tiƙewa, sai ya yi ta ganin manya-manyan ayoyin Ubangijinsa a can.[1]

Kuma a can ne ya ga Mala'ika Jibrilu ido da ido, a cikin kamanninsa kamar yadda Allah ya halicce shi, kuma ya yi ta ganin ababen gani masu yawa na 'yan aljanna da kuma ni'imarsu, ya kuma ga 'yan wuta da iren-iren azabarsu, Sai aka farlanta masa yin salloli; guda biyar a aikace, amma kuma hamsin a lada.[2]

A yayin da ya wayi gari, sai ya ba wa mutanensa labarin abin da ya faru gaba ɗaya, sai ƙaryatawarsu gare shi ta sake tsananta, har ma suka nemi ya siffanta musu yadda Masallacin Ƙudus yake, kawai sai Allah Ya yaye masa shi, sai ya siffanta musu shi kamar yadda yake, har ma ya ba su labarin ayarinsu, game da zuwansa da dawowarsa,

[1]. Muslim ne ruwaito shi (162).
[2]. Bukhari ne ruwaito shi (3207), da Muslim (164).

ya kuma ambata musu lokacin dawowarsa, amma hakan bai ƙara musu komai ba face ƙara ƙaryata shi.[1]

Amma su kuma muminai, sai wannan tafiyar ta zamto musu jarabawa, tamkar dai wani zakaran-gwajin-dafi na gaggauta gaskatawarsu ga labarin Allah da Manzonsa (SAW), da kuma ƙara ƙarfin imaninsu da gaibu, saboda hakane ma, aka yi wa Abubakar laƙabi da sunan Siddiƙ, saboda tsabar gaskatawarshi ga wannan labari na abin da ya faru, ba tare da ya yi wani kokonto ba.[2] Sai Allah Ya saukar – game da hakan - faɗinsa:[3] ((Kuma ba Mu sanya abin da ya gani wanda Muka nũna maka ba, fãce dõmin fitina ga mutane)).[4]

[1]. Albidaya wan-nihaya (3/139).
[2]. Dala'ilun-nubuwa na Baihaƙi (2361).
[3]. Tafsirin Ɗabari (384).
[4]. (Isra'i: 60)

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ZAINAB Y'AR JAHSHU (RA)

❖ Sunanta da haifuwarta:

Ita ce Zainab 'yar Jahshu, ɗan Riyab ɗan Khuzaima, Uwar muminai, kuma 'yar gidan goggon Manzon Allah (SAW).

An haife ta Makka tun kafin aiko Manzon Allah (SAW), da shekara goma sha bakwai.

❖ Tarihinta da falalarta:

Zainab (RA) ta kasance kyakkyawa ce kuma mai kamun kai, mai yawan azumi, kuma mai yawan tsayuwar sallar dare, mai son alkhairi da kuma yin sadaƙa, da ma dukkannin dangogin ayyukan alheri, tana yin aikin rini da hannayenta, sai ta sayar da kayan sana'ar nata, sai kuma ta yi sadaka ga mabuƙata, da miskinai.[1]

A wani lokaci, Umar ɗan khaɗɗab ya taɓa aika mata da saƙon wata kyauta, sai ta ce: Allah ya gafarta wa Umar, kawai sai ta fara rabar da kyautar ga danginta da kuma marayun da ke ƙarƙashin kulawarta.[2]

A'isha (SAW) tana cewa game da siffar Zainab: "Ban taɓa ganin wata mata da ta fita alheri ba, ko kuma wacce ta fi ta yawan yin sadaka, ko yawan sada zumunci, ko yawan sadaukar da kanta ga dukkannin abin da ke jawo kusancin Ubangiji Mai buwaya da ɗaukaka".[3]

---

[1]. Hakim ne ya ruwaito shi (3/26).
[2]. Aɗɗabaƙatul-kubra na Ibnu Sa'ad (8/109).
[3]. Bukhari ne ya ruwaito shi (2581) da Muslim (2441).

Kuma ita ce wacce Annabi (SAW) ya ke nufi da faɗinsa: (Wacce zata riga ku haɗuwa da ni ita ce wacce ta fi ku tsawon hannu [wato yawan kyauta da sadaka].[1]

Allah Ya zaɓe ta ga Annabi (SAW) kuma Ya aura masa ita da kanshi, hakan yana cikin faɗin Allah Maɗaukaki: ((To a lõkacin da Zaidu ya ƙãre bukãtarsa daga gare ta, Mun aura maka ita)).[2] Sai ta kasance tana yi wa sauran matan Annabi (SAW) alfahari, har ma tana cewa: "Ku danginku ne suka aurar da ku, ni kuma Allah ne Ya aurar da ni da kansa, tun daga saman sammai bakwai".[3] Kuma a aurenta ayoyin hijabi suka sauka.[4]

Zainab (RA) ta rawaito wani adadi na hadisai daga Manzon Allah (SAW), kuma ita ce wacce ta fi ƙarfafa A'isha (RA) ta kuma rarrashe ta a lokacin da aka mata ƙazafi.[5]

❖ Rasuwarta:

Zainab 'yar Jahshu ta rasu ne a Madina, a shakara ta ashirin bayan hijira, kuma ta kasance ita ce farakon wacce ta fara haɗuwa da Annabi (SAW), sai Umar ɗan kaɗɗab ya sallace ta, sai aka binne ta a maƙabartar Baƙi'i.

---

[1]. Muslim ne ya ruwaito shi (2453).
[2]. (Al-Ahzaab: 37)
[3]. Bukhari ne ya ruwaito shi (7320).
[4]. Bukhari ne ya rawaito shi (7420).
[5]. Bukhari ne ya rawaito shi (4141), da Muslim (2770).

Auna fahimtarka a darusan mako na 17			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar "Al'adiyat"?		C
	a. Mahaya masu yaƙi.	b. Mala'ikun rahama.	c. Dawakai masu gudu a filin yaƙi.
Darasin Hadisi	Tambaya: Ana ƙayyade biyayya ga iyaye ya zama:		C
	a. A lokuta na sarari.	b. Da rana ban da daddare.	c. A abin da ba saɓa wa Allah ba ne.
Darasin Aƙida	Tambaya: Sunayen Allah Maɗaukaki da siffofinsa:		B
	a. Ijtihadi ne, suna karɓar ƙari.	b. Ba ijtahadi ba ne, don haka ba ya halatta a tabbatar da wani abu cikinsu ga Allah sai da nassi.	c. Suna banbanta gwargwadon zamani da muke rayuwa a cikinsa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Ƙarshen lokacin sallar La'asar shi ne:		C
	a. Lokacin kaucewar rana daga tsakiyar sama.	b. Lokacin gushewar ja da shafaƙi daga sama.	c. Lokacin da rana ta yi fatsi-fatsi dab da lokacin faɗuwarta.
Darasin Sira	Tambaya: An yi isra'i da Manzon Allah (SAW) daga Masallacin Ƙudus a kan:		A
	a. Alburaƙu.	b. Alƙaswa'u.	c. Aljad'a'u.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Zainabu (RA) ta kasance tana yi wa mata alfahari da cewa:		C
	a. Allah Ya barranta ta a sama na bakwai.	b. Allah Ya yi mata sallama daga sama na bakwai.	c. Allah Ya ɗaura aurenta a sama na bakwai.

MAKO NA GOMA SHA TAKWAS

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI:

SURATUL-ƘADAR:

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ فِي لَيۡلَةِ ٱلۡقَدۡرِ ١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ ٢ لَيۡلَةُ ٱلۡقَدۡرِ خَيۡرٞ مِّنۡ أَلۡفِ
شَهۡرٖ ٣ تَنَزَّلُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَٱلرُّوحُ فِيهَا بِإِذۡنِ رَبِّهِم مِّن كُلِّ أَمۡرٖ ٤ سَلَٰمٌ هِيَ حَتَّىٰ مَطۡلَعِ
ٱلۡفَجۡرِ ٥﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai.

1. Lalle Mu Muka saukar da shi (Alƙur'ani) a daren Lailatul-Ƙadari (dare mai daraja).
2. Mene ne ya sanar da kai mece ce Lailatul-Ƙadari?
3. (Daren) Lailatul-Ƙadari ya fi wata dubu alheri.
4. Mala'iku da Jibrilu suna ta saukowa da dukkanin al'amura a cikinsa da izinin Ubangijinsu.
5. Aminci ne shi (daren dukkansa) har zuwa hudowar alfijir.

❖ Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:

Bayani a kan falalar daren Lailtul-ƙadari

❖ Bakin kalmomi:

إنا لأنزلناه	Inna anzalnahu	Ma'ana: Mun fara sauƙar da shi.
ليلة القدر	Lailaitul-ƙadari	Dare mai daraja, da girma, da rubuta ƙaddarori.
والروح فيها	War-ruhu fiha	Shi ne Jibril (AS).

من كل أمر	Min kulli amr	Da kowane al’amari da Allah Ya zartar da faruwansa a wannan shekara.
سلام هي	Salamun hiya	Aminci da kwanciyar hankali.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

Wannan sura tana daga cikin surorin da aka saukar a Makka. Allah Maɗaukaki Yana ba mu labari a cikinta game da falalar wani dare mai girma da ɗaukaka, wanda Allah Ya sanya masa sha’ani mai girma a cikinsa, Ya kuma fifita shi a kan dukkan dararen da ke cikin shekara, shi ne daren yanke hukunce-hukunce da ƙaddara, wanda Allah Maɗaukaki Yake zartar da abin da Ya ga dama cikin abubuwan da za su faru a duniya, da raba arziƙinta, da ajalin abubuwan da ke cikinta har zuwa ƙarshen shekara.

Kuma shi ne daren da Allah Maɗaukakin Sarki Ya keɓance shi da saukar da mafificin littafinsa a cikinsa, kuma shi ne daren da Allah Ya sanya falalar yin aikin alheri a cikinsa har ta fi ta yin aikin alheri a cikin watanni dubu, kuma haƙiƙa, dukkannin mala’iku - ciki har da mala’ika Jibrilu - sukan sauko da izinin Allah Maɗaukakin Sarki, tare da dukkan al’amarin da Allah Ya zartar kuma Ya hukunta cewa zai faru.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Tabbatar da gaskiyar wahayi, da sauƙowar Alƙur’ani daga wajen Allah Maɗaukakin sarki.
2. Tabbatar da aƙidar yarda da hukunci da kuma ƙaddarar Allah.
3. Lallai farkon sauƙar Alƙur’ani zuwa ga Manzon Allah (SAW), ya kasance ne a daren Lailatul-Ƙadari dake cikin watan Ramadana.

4. Falalar daren Lailatul-Ƙadari da kuma kira zuwa ga neman shi, da kuma rabauta da irin falalar dake cikinshi.
5. Falalar yin ibada a cikin daren Lailatul-Ƙadari da kuma cewa tabbas ta fi yin ibada a cikin watanni dubu, don haka, duk wanda ya ribace shi, to shekarunsa ne suka ninku, ninki mai yawan.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

DABI'UN DA SUKE GYARA ZUKATA

An karɓo daga Anas ɗan Malik (RA), ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: ((**Akwai wasu ɗabi'u guda uku, waɗanda zuciyar musulmi da ke siffantuwa da su ba ta zama mai ƙullata ba, tsantsanta aiki ga Allah, da yin nasiha ga shugabanni ko al'ummar musulmai, da kuma lazimtar jam'ar musulmai, domin kuma lallai addu'arsu tana kewaye su**)). [1]

❖ Sharhi:

Faɗin Annabi (SAW): (zuciyar musulmi da ke siffantuwa da su ba ta zama mai ƙullata ba), Ma'ana: haƙiƙa waɗannan ɗabi'u guda uku zukata suna gyaruwa a sanadiyarsu, kuma suna tsarkaka daga ha'inci da kuma sharri, lallai mummuni ba ya yin ha'inci cikin waɗannan abubuwan guda uku, kuma nufin aikata sharri wanda zai nesanta shi daga gaskiya ba zai taɓa shiga ransa ba.

Kuma waɗannan ɗabi'u sune suke kore samuwar ha'inci da sharri daga zuciya:

Na farko: Tsarkake niyyar yin dukkan aiki domin Allah shi kaɗai; wato abin da ake nufi: Ta hanyar da mutum musulmi zai nufaci yin aiki domin neman yardar Allah ba wani abin duniya na daban ba koma bayan Allah.

Na biyu: Nasiha ga shuwagabannin musulmi: nasiha ita ce: nufin alheri ga wanda ake yi wa nasiha. Ma'anar yi wa shuwagabanni da jagorori ko limamai nasiha kuwa shi ne: Mutum ya yi musu biyayya

[1]. Ibnu Maja ne ya ruwaito shi (230–3056), da Ahmad (16784).

cikin gaskiya, ya kuma yi musu addu’a tagari, kuma kada ya yi musu tawaye ko fito-na-fito.

Na uku: Lazimtar jama’ar musulmai, wato: Dacewa da su cikin ingantacciyar aƙida, da kuma yin aiki nagari tare da su, kamar sallar juma’a, da sallar jam’i, da ma waɗansun hakan.

Ma’anar faɗin Annabi (SAW): (Lallai addu’arsu tana kewaye da su), shi ne: Lallai adddu’ar musulmai kewaye take da su, tana zama sababin tsare su daga kaidin sheɗan, ta kuma kare su daga faɗawa ramin ɓata, kuma a cikin wannan hadisi akwai faɗakarwa a kan cewa dukkan wanda ya fice daga taron jama’ar musulmai, to fa ba zai taɓa samun albarkarsu ba, saboda ya fita daga abin da addu’ar tasu ta kewaye.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Wajibcin yin (Iklasi), wato tsantsance ibada ga Allah tsarki ya tabbata a gare Shi, saboda lallai shi ikhlasi ɗaya ne daga cikin sharuɗa guda biyu na ƙarɓar ayyuka, na biyun kuwa shi ne: Bin koyarwar Manzon Allah (SAW).
2. Wajibcin biyayya ga shuwagabanni da kuma jagorori limamai cikin gaskiya da kuma barin yi musu tawaye ko fito-na-fito.
3. Wajibcin lazimtar jama’ar musulmai, ta hanyar yin dace da su cikin ingantacciyar aƙida da kuma aiki nagari.
4. Lallai duk wanda ya yi riƙo da waɗannan ɗabi’u guda uku, to zuciyarsa za ta gyaru kuma za ta tsarkaka daga ha’inci da sharri.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA MALA'IKU

Malaa'iku: wasu talikai ne na fake (wato waɗanda ba a ganinsu), waɗanda aka halicce su daga haske, Allah Ya ba su cikakkiyar damar yin ibada gare Shi, da jayuwa ga umarninsa, da kuma ƙarfi a kan zartar da shi; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Gõdiya ta tabbata ga Allah, Mai fãra halittar sammai da ƙasã, Mai sanya malã'iku manzanni mãsu fukãfukai, bibbiyu, da uku-uku da hurhuɗu)).[1]

Kuma adadinsu yana da dayawa sosai, babu wanda ya isa ya kiyaye yawansu sai Allah Maɗaukakin Sarki Shi kaɗai; kuma haƙiƙa ya tabbata a cikin ƙissar Mi'iraji cewa: (Lallai Annabi (SAW) an ɗauke shi har zuwa (Baitul Ma'amur), wato gidan da malaa'iku suke raya shi da ibada a sama, wanda a kullum mala'iku dubu saba'in ne suke salla a cikinsa, idan kuma suka fita daga cikinsa, to ba za su sake dawowa ba, har abada). [2]

❋ **Kuma imani da mala'iku yana ƙunshe da abubuwa guda huɗu:**

Na farko: Imani da samuwarsu.

Na biyu: Imani da sunayen waɗanda muka san sunayensu daga cikinsu, kamar Jibrilu da Mika'ilu, amma kuma waɗanda ba mu san sunayensu ba, to sai sai mu yi imani da su a dunƙule.

Na uku: Imani da abin da muka sani na siffofinsu, kamar siffar mala'ika Jibrilu (AS), saboda haƙiƙa Annabi (SAW) ya bayar da labarin cewa: Lallai ya ga mala'ika Jibrilu a cikin siffar halittarsa,

---

[1]. (Alfaɗir: 1).
[2]. Bukhari ne ya ruwaito shi (3674), da Muslim (409).

yana da fuka-fikai har guda ɗari shida sun mamaye fadin sararin samaniya.

Na huɗu: Imani da abin da muka sani na ayyukansu na gama-gari, kowa-da-kowa, da kuma wasu keɓantattun ayyuka na waɗansu daga cikinsu.[1] Kuma daga cikin gamagarin ayyukansu akwai: Tasbihi ga Allah Maɗaukaki, da bauta masa dare da rana.

Kuma haƙiƙa wasu daga cikinsu suna da keɓantattun ayyuka; misali: Mala'ika Jibrilu, shi amintaccen Allah ne kuma Manzonsa mai isar da wahayi zuwa ga Annabawa da kuma Manzanni, shi kuma Mika'ilu: Shi aka wakiltar da sauƙar da ruwa sama da tsuro da tsirrai, Israfilu kuma: Shi ne aka wakiltar don busa ƙaho lokacin tashin alƙiyama, akwai kuma Mala'ikan mutuwa, wanda aka ɗaura wa zare rai lokacin mutuwa, Maliku kuma mai lura da wuta.

❋ **Kuma imani da mala'iku yana samar da wasu fa'idoji masu girma kamar haka:**

Na farko: Sanin girman Allah Maɗaukakin Sarki da ƙarfinsa, saboda lallai girman abin halitta yana nuni a kan girman Mahalicci.

Na biyu: Gode wa Allah Maɗaukakin Sarki bisa kulawarshi ga mutane, ta yadda Ya wakilta musu waɗanda za su ɗinga ba su kariya ko kiyaye su da kuma kula da maslaharsu.

Na uku: Son mala'iku, sakamakon abin da suke yi na bauta wa Allah Maɗaukakin Sarki, da kuma kyautata wa bayinsa da suke yi.

[1]. Bukhari ne ya ruwaito shi (3232), da Muslim (174).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

LADUBBAN TAFIYA ZUWA SALLA

Dukkannin musulmi suna da matuƙar buƙatar sanin ladubba na sharia da ake yin su kafin salla, saboda yin shiri ga wanann ibada mai girma, da kuma ba da muhimmanci ga sha'aninta.

Kuma daga cikin waɗannan ladubban akwai abubuwa kamar haka:

1. Yin sammakon fita domin tafiya zuwa ga salla, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Kuma idan da a ce sun san irin abin da ya ke cikin yin sammako, to da sai sun yi ta rige-rige wajen zuwa gare shi).[1]
2. Tafiya zuwa masallaci da ƙafa, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Dukkan wanda ya yi alwala daga gidansa, sannan ya tafi zuwa wani ɗaki daga cikin ɗakunan Allah, domin ya sauƙe wata farilla daga cikin farillan Allah, to takun ƙafafuwansa guda biyu, za su kasance: ɗaya daga cikinsu yana kankare masa zunubansa, dayan kuma yana daga masa darajarsa).[2]
3. Tafiya masallaci cikin nutsuwa da tsanaki, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Kada ku tafi zuwa gare ta (wato salla) alhali kuna gaggawa, ku dai ku tafi zuwa gare ta alhalin kuna cikin nutsuwa, dukkan abin da kuka riska, to kawai ku sallace shi, kuma dukkan abin da ya wuce ku, to sai ku ciko shi, domin ɗayanku zai kasance kamar yana cikin salla ne matuƙar dai ya nufaci tafiya zuwa salla).[3]
4. Sunna ce idan mutum zai shiga masallaci, ya fara gabatar da kafar sa ta dama wajen shiga, sai kuma ya ce: (A'uzu billahil-Azim, wabi wajhihil-karin, wa sulɗanihil-ƙadim, minash-shaiɗanir-rajim), wato: (Ina neman tsarin Allah Mai girma, da fuskarsa mai karamci,

---

[1]. Bukhari ne ya ruwaito shi (652), da Muslim (437).
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (666).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (908), da Muslim (602).

da kuma ikonsa na tun fil-azal, daga shaiɗan jefaffe daga rahamar Allah).[1] Sai kuma ya ce: (Allahummaftahli abwaba rahmatika), wato (Ya Allah Ka buɗe min ƙofofin rahamarka), idan kuma zai fita sai ya ce: (Allahumma inni as'aluka min fadlik), wato (Ya Allah lallai ni ina rokon Ka, Ka ba ni daga falalarka).[2] Sai kuma ya gabatar da kafarsa ta hagu.

5. Idan mutum ya shiga masallaci, to sai ya yi iya ƙoƙarinsa wajen ganin ya kasance a sahun farko, sannan sai ya yi salla raka'a biyu, na gaisuwar masallaci, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan da a ce mutane sun san abin da yake cikin kiran salla da kuma sahun farko, sannan kuma ya zamanto ba za su iya samun su ba har sai idan sun yi ƙuri'a a kansu, to kuwa tabbas da sai sun yi ƙuri'ar).[3]

6. Shagaltuwa da ambaton Allah Mai buwaya da ɗaukaka, da kuma karantun Alƙur'ani, da nafulfili, da guje wa wargi, kamar haɗa 'yan yatsu ko waninsa, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Idan ɗayanku ya yi alwala, sannan sai ya fita ya nufi masallaci, to kada ya dinga haɗa hunnunsa (wato domin yin wasa da su), saboda lallai shi a cikin salla yake).[4]

7. Rashin kutsawa cikin firar duniya ko kuma zantukan ƙila-wa-ƙala, saboda lallai jiran salla ita ma salla ce, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Bawa ba zai gushe ba yana cikin salla, matuƙar dai yana zaune a gurin da ya yi sallarsa, mala'iku kuma suna (yi masa addu'a suna) cewa: "Ya Allah Ka gafarta masa, ya Allah Ka yi masa rahama").[5]

8. Idan aka tsayar da iƙamar salla, to haƙƙi ne mai ƙarfi a kan limami da mamunsa su bayar da mahimmanci a kan daidaita sahu,

---

[1]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (466).
[2]. Muslim ne ya ruwaito shi (713).
[3]. Bukhari ne ya ruwaito shi (652), da Muslim (437).
[4]. Abu Dawuda ne ya ruwaito shi (562).
[5]. Muslim ne ya ruwaito shi (649).

da kuma toshe dukkan wata kafa, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ku daidaita sahunku, domin lallai shi daidaita sahu yana daga cikar sallah).[1] Kuma Manzon Allah (SAW) ya kuma cewa: (Lallai ne ku daidaita sahunku, ko kuma lallai ne Allah zai sanya tsaɓani a tsakaninku),[2] kuma abin da ake nufi da daidaita sahu shi ne: Daidaita shi ta yadda duga-dugan ƙafafu da kuma kafaɗu za su zama daura da juna.

9. Aikata dukkannin sababban da za su samar da kushu'i (wato ƙanƙan da kai ga Allah), saboda shi ne mafi girman manufar yin salla; kuma haƙiƙa Allah Ya yabi masu kushu'i a inda Yake cewa: ((Lallai ne, Mũminai sun sãmi babban rabõ () Waɗanda suke masu ƙanƙan da kai a cikin sallarsu)).[3] Kuma yana samuwa ne ta hanyar hararo girman Allah a cikin zuciya, da kuma saduda gare Shi, da kuma bijiro da zuciya ta hanyar yin kai-kawo wajen tunani da la'akari ga abin da mutum ke karantawa, ko kuma yake sauararo.

[1]. Bukhari ne ya ruwaito shi (723), da Muslim (433).
[2]. Bukhari ne ya ruwaito shi (717), da Muslim (436).
[3]. (Almuminun: 1-2)

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

MUBAYA'AR AƘABA TA FARKO

Manzon Allah (SAW) ya kasance cikin kowacce shekara ya kan fita domin zuwa aikin hajji, sai ya bijiro da da'awarsa ta shiga Musulunci ga ƙabilun larabawa masu zuwa Makka, duk da cewa kuwa mushirikai su kan hana shi, kuma suna ƙuntata masa, kuma Manzon Allah (SAW) yana cewa: (Shin akwai wani mutumin da zai ɗauke ni ya kai ni wajen mutanensa? saboda haƙiƙa ƙuraishawa sun hana ni isar da maganar Ubangijina),[1] yana yin wannan shelar alhali kuwa baffansa Abu Lahabi yana bin sa a bayanshi kuma yana cewa wa mutane: "Kada ku saurare shi, haƙiƙa shi ɗin nan makaryaci ne".[2]

Kuma daga cikin abin da Allah Ya sauƙaƙe wa 'yan ƙabilar Ausu da Khazraj akwai cewa: Su sun kasance suna jin labari daga wajen yahudawan garin Madina cewa: lallai akwai wani Annabi da za a aiko shi na wannan zamanin, har ma suna musu barazana da cewa: Tabbas sai mun haɗu da shi mun kashe ku irin kisan da aka yi wa Adawa da Samudawa, saboda haka su kuma mutanen Madina sun kasance suna yin aikin hajji kamar dai yadda sauran larabawa suka saba yin aikin hajji, amma su kuma yahudawa ba sa yin aikin hajjin. A yayin da mutanen Madina suka ga Manzon Allah (SAW) yana ƙiran mutane zuwa ga yin imani da Allah, kuma suka ga alamomin gaskiya tattare da shi, sai suka ce: Ya ku mutanen mu! Wallahi wannan shi ne Annabin da yahudawa suke muku alwashi da barazana da zuwansa, don haka kada ku bari su rigaye ku zuwa gare shi.[3]

---

[1]. Abu Dawuda ne ya ruwaito shi (4734), da Tirmizi (2925).
[2]. Ɗabarani ne ya ruwaito shi (4582).
[3]. Albidaaya wan-nihaaya (4/371).

Sai waɗansu mutane guda shida suka zo wajen Manzon Allah (SAW), dukkansu kuma ‘yan ƙabilar Khazraj ne, su ne: Abu Umamata As’adu ɗan Zurara, da kuma Aufu ɗan Haris, da kuma Rafi’u ɗan Malik, da kuma Jabir ɗan Abdullahi, sai Manzon Allah (SAW) ya bijiro musu da da’awarsa ta shiga Musulunci, sai suka yi gaggawar shiga cikin alheri, kuma suka musulunta, kuma suka yi masa alƙawarin cewa lallai za su isar da wannan da’awar tashi zuwa ga mutanensu, kuma hakan ya kasance ne a cikin shekara ta goma sha ɗaya bayan an aiko Manzon Allah (SAW), sai suka koma zuwa Madina, kuma suka fara kiran mutanensu zuwa shiga addinin Musulunci.[1]

A yayin da shekara ta zagayo, sai mutane guda goma sha biyu daga cikinsu suka zo wajen Manzon Allah (SAW), sai Manzon Allah (SAW) ya haɗu da su a Mina, daidai gurin Aƙaba, sai ya ce da su: Ku yi min mubaya’a a kan cewa lallai ba za ku yi wa Allah shirka da komai ba, ba za ku yi sata ba, ba za ku yi zina ba, ba za ku kashe ‘ya’yanku ba, ba za ku zo da ƙarya ba wacce za ku ƙirƙire ta a gaba gare ku da kuma bayanku, kuma ba za ku saɓa ba cikin aikin alheri, to duk wanda ya cika alkawarin hakan daga cikinku, to, ladansa yana wajen Allah.[2] Sai suka yi masa mubaya'a a kan hakan, sai ta kasance ita ce mubaya’ar Aƙaba ta farko a cikin shekara ta goma sha biyu da aiko Manzon Allah (SAW).

Kuma bayan aikin hajji ya ƙare Manzon Allah (SAW) sai ya aika musu da Mus’ab ɗan Umair, da kuma Ibnu Ummi Maktum, domin su koyar da su karatun Alkur’ani,[3] Sai Musulunci ya yaɗu a Madina ya bayyana ƙarara, kuma mutane masu yawa suka Musulunta, har

[1]. Albidaya wan-nihaya (4/371).
[2]. Bukahri ne ya ruwaito shi (17).
[3]. Bukhari ne ya ruwaito shi (3952).

ya zamo babu wani gida da ya rage a Madina face sai da Musulunci ya shiga cikinsa.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

JUWAIRIYYA ‘YAR HARIS (RA)

❖ Sunanta da haifuwarta:

Ita ce Uwar Mummunai, Juwairiyya ‘yar Haris, ɗan Abu Dirar, shugaban ƙabilar Banu Musɗaliƙ, a baya sunanta yakasance "Barra", sai Manzon Allah (SAW) ya sanya mata suna: "Juwairiyya".[1]

An haife ta ne kafin Hijira da kimanin shekaru goma sha biyar.

❖ Rayuwarta da falalarta:

Juwariyya (RA) ta kasance ɗaya daga cikin mafiya kyawun mata, kuma mafiya jin tsoron Allah, mai yawan tasbihi da hamdala ga Allah Maɗaukaki, mai yawan sadaka, duk da cewa tana da karancin abin hannu, ta ruwaito hadisai masu yawa daga Manzon Allah (SAW), kuma Ibnu Abbas da Jabir da Ibnu Umar dukkansu sun ruwaito hadisai daga wajenta, kai har dama sauran waɗansu jama'ar daban. Haka kuma, ta kasance daga cikin mafiya girman albarka cikin mutanenta, kuma hakan zai bayyana gare mu a cikin labarin aurenta da Annabi (SAW), a yayin da ta kasance daga cikin ribatattun yaƙin Banu Musɗalik, sai ta zo wajen annabi (SAW) tana roƙonsa a kan ya taimaka mata don ta fanshi kanta, sai Annabi (SAW) ya saye ta, kuma sai ya ‘yanta ta, kuma ya aure ta, sai sauran musulmai suka yi ta ‘yanta ribatattun yaƙin dake hannunsu domin karrama ta, sai kuma suka dinga cewa: “Ai waɗannan surukan Manzon Allah ne (SAW).[2]

[1] . Muslim ne ya ruwaito shi (2140)
[2] . Abu dawuda ne ya fitar da shi (3931)

❖ Rasuwarta:

Juwairiyya (RA) ta rasu ne a Madina, kuma an binne ta a makabartar baƙi’ i, hakan kuma ya kasance ne a cikin watan Rabi’ul Auwal ɗin shekara ta hamsin da shida (56) bayan hijirar Manzon Allah (SAW), a cikin zamanin halifancin Mu’awiya ɗan Abu Sufyanu.

Auna fahimtarka a darusan mako na 18			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Me ake nufi da “ruhi” a suratul-ƙadar?		A
	a. Jibrilu.	b. Muhammadu (SAW).	c. Mala’ikan mutuwa.
Darasin Hadisi	Tambaya: Me ake nufi da ƘKullata a faɗin Annabi (SAW): “Abubuwa guda uku mai siffantuwa da su ba za a same shi da ƙullata ba”?		C
	a. Sata.	b. Wuce gona da iri.	c. Ha’inci da ƙeta.
Darasin Aƙida	Tambaya: Mala’ika da aka ɗaura wa busa cikin ƙaho shi ne:		C
	a. Jibrilu.	b. Mika’ilu.	c. Israfilu.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Sunna ne idan mutum ya fito daga masallaci ya ce:		B
	a. Allahummu iftah li abwaba rahmatika.	b. Allahumma inni as’aluka min fadlika.	c. Gufranaka.
Darasin Sira	Tambaya: Mubaya’a ta Aƙaba ta kasance ne a shekara ta …. Bayan aiko Annabi:		C
	a. 6.	b. 9.	c. 11.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Nasabar Juwairiyya ‘yar Haris (RA) yana komawa ne zuwa ga:		A
	a. Bunul-Musɗaliƙi.	b. Banun-Nadir.	c. Banu Ƙuraiza.

MAKO NA GOMA SHA TARA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI:

SURATUL-BAYYINA (1)

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
لَمۡ يَكُنِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ مُنفَكِّينَ حَتَّىٰ تَأۡتِيَهُمُ ٱلۡبَيِّنَةُ ١
رَسُولٞ مِّنَ ٱللَّهِ يَتۡلُواْ صُحُفٗا مُّطَهَّرَةٗ ٢ فِيهَا كُتُبٞ قَيِّمَةٞ ٣ وَمَا تَفَرَّقَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ
ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَتۡهُمُ ٱلۡبَيِّنَةُ ٤ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ
حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ ٥﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai.

1. Waɗanda suka kafirta daga ma'abota littafi da mushirikai ba su zamanto masu barin abin da suke kai (na kafirci) ba har sai hujja bayyananniya ta zo musu.
2. (Watau) Manzo daga Allah da zai riƙa karanta (musu) takardu masu tsarki.
3. (Waɗanda) a cikinsu akwai hukunce-hukunce masu ƙima.
4. Waɗanda kuma aka bai wa littafi ba su rarraba ba sai bayan da hujja bayyananniya ta zo musu.
5. Ba a kuma umarce su ba sai don su bauta wa Allah suna masu tsantsanta addini gare Shi, suna masu kauce wa ɓarna, suna kuma tsayar da salla, kuma suna ba da zakka. Wannan kuwa shi ne addinin miƙaƙƙiyar hanya.

❖ Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:

Bayanin cikar Manzoncin Annabi Muhammad (SAW) da bayyanarta..

❖ Baƙin kalmomi:

منفكين	Munfakkina	Masu barin kafircinsu
البينة	Albayyinatu	Alama bayyananniya da hujja fayatacciya, wacce aka yi alƙawarinta, kuma shi ne Annabi Muhammadu (SAW).
صحفا مطهرة	Suhufan muɗahhara	Wanda aka tsaftace su daga ƙarya, kuma aka kiyaye su daga shedan.
فيها كتب قيمة	Fiha kutubun ƙayyima	Labarai na gaskiya, da umurce-umurce na adalci.
تفرق	Tafarraƙa	Sun yi saɓani, alhali da can sun haɗu a kan ingancin annabtakarsa.
مخلصين	Mukhlisina	Masu neman yardar Allah.
حنفاء	Hunafa'a	Wato masu karkata daga addinai gaba ɗayansu zuwa ga addinin Musulunci.
دين القيمة	Dinul-ƙayyima	Wato addinin tafarki miƙaƙƙe.

❖ Ma'anar ayoyin a dunƙule:

Allah Mai ɗaukaka da buwaya Yana bayar da labarin cewa ma'abota littafi daga cikin yahudu da nasara da kuma mushirikai ba su kasance daga cikin masu bari bauta wa gumaka ba, ba su kuma yi hannun riga ba da abin da suke kanshi na addinin da suke bin sa, har zuwa lokacin da hujja ta zo musu, wacce ita ce: Annabi Muhammad (SAW), wanda yake karanta musu littafin Ubangijinsu, a yayin da bayyananniyar hujja ta zo musu wacce kuma take wajabta wa ma'abotanta haɗuwa a kanta, sai suka rarrabu kashi-kashi, daga

cikinsu akwai waɗanda suka yi imani, daga cikinsu kuma akwai waɗanda suka kafirce, bayan kuwa da can tun kafin aiko Manzon Allah (SAW) sun kasance kansu a haɗe wajen jiran zuwansa, kuma a shirye suke da su yi imani da shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga ayoyin:

1. Lallai dukkanin addinai - in ban da Musulunci - to karkatattu ne daga barin gaskiya, kuma ƙarya da gaskiya ne suka cakuɗu a cikinsu, kuma ba su cancanci su shiryar da mutane ba.

2. Lallai littattafan Annabawa sun zo ne da asali guda ɗaya da kuma addini guda ɗaya tak, kuma shi ne tsarkake bauta ga Allah shi kaɗai, da kuma karkace wa shirka.

3. Lallai dukkanin annabawa sun yi wa al'ummominsu bishara da aiko annabinmu Muhammad (SAW), kuma sun umarce su da yin imani da shi matuƙar sun riske shi.

4. Lallai tafarki miƙaƙƙe kuma ingantaccen addini wanda ke tabbatar da rabauta shi ne: Bauta wa Allah shi kaɗai, da kuma tsayar da salla da bayar da zakka.

5. An keɓance ambaton salla da kuma zakka saboda ɗaukakar da suke da ita, da kuma irin girman matsayin da suke da shi a cikin addini.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR AZUMTAR LITININ DA ALHAMIS

An karbo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Ana bijiro da ayyuka a ranar Litinin da Alhamis, don haka, ni ina so a bijiro da aikina, alhali ina da azumi**).[1]

❖ Sharhi:

Azumi yana daga cikin mafiya falalar ibadu waɗanda mutum yake samun kusanci ga Allah a sanadiyarsu, kuma haƙiƙa Annabi (SAW) ya kasance yana kwaɗaitarwa a kan yin azumi, kuma shi da kansa yana yawaita yin azumin nafila, duk da haka kuma akwai wasu kwanaki waɗanda bayanin ƙarin falala da kwadaitarwa a kan azumtarsu ya zo, daga cikinsu akwai ranar Litinin da Alhamis; saboda haƙiƙa dukkanin ayyukan 'yan'adam na alheri da na sharri na ɗa'a da na saɓo, ana bijiro da su zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki a kowane mako a cikin waɗannan kwanaki biyu, kuma Annabi (SAW) ya kasance yana kwaɗayin a bijiro da ayyukansa na alheri alhali yana ibadar azumi, ya kan yi hakan ne saboda ayyuka nagari idan har ibadar azumi ta kasance tare da su, to sai ya ɗaukaka darajarsu ya kuma tsantsance su ga Allah Mai girma da ɗaukaka.

❖ Abubuwan da za mu koya daga wannan hadisin:

1. Falalar yin ibadar azumi, kuma lallai Manzon Allah (SAW) ya kasance yana yawaita yin shi.
2. Falalar azumtar ranakun Litinin da Alhamis, da kuma kwaɗaitarwa a kan yin shi.
3. Tabbatar da bijiro da ayyukan bayi ga Allah a kowane Litinin da Alhamis na kowane mako.

---

[1]. Tirmizi ne ya ruwaito shi (742).

4. Gaggawar Annabi (SAW) zuwa ga ayyukan alheri duk da cewa an gafarta masa dukkanin zunubansa, saboda nuna cikakkiyar bautarsa ga Ubangijinsa da kuma jin girman Allah a kansa, da kuma gode masa bisa ga ni’imominsa, da nusarwa da kuma shiryarwa ga al’ummarsa.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA LITTATTAFAI

Abinda ake nufi da littattafai shi ne: littattafan da Allah Maɗaukakin Sarki ya saukar zuwa ga manzanninsa don su zamo rahama ga halittu, da shiriya a gare su, saboda a sanadiyyarsu za su isa zuwa ga rabautar duniya da ta lahira, kuma bayanai da suke nuni a kan ma'anar saukar da littattafai sun zo a cikin ayoyi masu yawa:

- Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Alif Lam Mim () Allah, bãbu wani abin bauta bisa cancanta sai Shi, Rãyayye, Tsayayye a kan komai () Yã sassaukar da Littãfi a gare ka da gaskiya, yana mai gaskatãwa ga abin da ke gaba gare shi, kuma Allah Yã saukar da Attaura da Linjĩlã () A gabãni, suna shiryar da mutãne, kuma Ya saukar da littattafai mãsu rarrabẽwa. Lallai ne waɗanda suka kãfirta da ãyõyin Allah, suna da azãba mai tsanani. Kuma Allah Mabuwayi ne, Ma'abucin azãbar rãmuwa)).[1]
- Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Dukkan yabo ya tabbata ga Allah wanda Ya saukar da Littafi wa bãwansa kuma bai sanya karkata ba a gare shi () Madaidaici, dõmin Ya yi gargaɗi da azãba mai tsanani daga gare shi, kuma Ya yi bishãra ga mũminai, waɗanda suke aikata ayyuka na ƙwarai da (cẽwa) sunã da wata lãdã mai kyau)).[2]
- Da kuma faɗinsa Maɗaukakin Sarki: ((Albarka ta tabbata ga wanda Ya saukar da (Littãfi) mai rarrabẽwa ga bãwansa, dõmin ya kasance mai gargaɗi ga halitta)).[3]

---

[1]. (Alu-Imran: 1-4)
[2]. (Alkahf: 1-2)
[3]. (Alfurƙan: 1).

❋ **Kuma imani da littattafai yana ƙunshe da al'amura guda huɗu:**

Na farko: Imani da cewa lallai saukarsu daga wajen Allah gaskiya ne, kuma tabbas maganarsa ce a cikinsu, Allah Ya saukar da su ta hanyar mala'ika zuwa ga wanda ya so daga cikin manzanninsa.

Na biyu: Imani da sunan waɗanda muka san sunansu daga cikin waɗannan littattafan, kamar Alkur'ani da Attaura, da Injila, da Zabbura, amma waɗanda ba mu san sunansu ba, to kawai sai mu yi imani da su a dunƙule.

Na uku: Gaskata dukkanin abin da ya inganta na labarai da ke cikinsu, kamar labaran Alkur'ani da kuma labaran da ba a canza su ba na littattafai da suka gabata.

Na hudu: Aiki da hukunce-hukuncen da ke cikin littafin da aka saukar mana – wato Alƙur'ani mai girma -, da yarda da kuma miƙa wuya a gare shi; saboda shi ne wanda ya shafe hukunce-hukuncen dukkanin littattafan da suka gabata, Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma Mun saukar da Littãfi zuwa gare ka da gaskiya, yanã mai gaskatã abin da ke gaba gare shi na littafi, kuma mai rinjaye ne a kansa)).[1] Ibnu Abbas ya ce: "Ma'anar (kuma mai rinjaye a kansa) shi ne: Mai yin hukunci a kansa.[2]

❋ **Imani da littattafai yana samar fa'idoji masu girma, daga cikinsu akwai:**

Na farko: Sanin kulawar Allah ga bayinsa, ta yadda ya saukar musu da littattafansa da zai shiryar da su.

---

[1]. (Alma'ida: 48)
[2]. Tafsirin Ibnu Kasir (3/16).

Na biyu: Sanin hikimar Allah cikin shari’arsa ta yadda Ya shar'anta wa kowaɗanne mutane irin abin da ya dace da su, kamar yadda Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kowanne daga cikinku Mun sanya musu tsari na shari’a da tsari na rayuwa)).[1]

Na uku: Gode wa Allah Maɗaukakin Sarki bisa ga karramawarsa ga bayinsa ta hanyar sauƙar musu da maganarshi, da kuma shari’arshi.

Na huɗu: Riƙo da littafin Allah ta hanyar karanta shi, da kuma yin aiki da shi, saboda lallai akwai haske da shiriya a cikinsa, kuma a sanadiyarshi ne ake samun rabautar duniya da lahira.

[1]. (Alma’ida: 48).

LARABA: DARASI CIKIN FIKIHU

RUKUNAN SALLA

Salla: Ibada ce mai girma wadda ta ƙunshi maganganu da ayyuka, kuma waɗannan maganganu da ayyuka sun kasu kashi uku, akwai: **Rukunai, Wajibai da kuma Sunnoni**.

❋ **Rukunai**: Su ne abubuwan da ɓangarorin sallar ke ginuwa da su, kuma rukuni ba ya faɗuwa idan aka bar shi da gangan ko kuma da rafkanuwa ko jahilci, dukkan wanda ya bar wani rukuni da gangan to sallarsa ta ɓaci, idan kuma ya kasance rafkanuwa ce, to sai ya koma zuwa gare shi idan har ya kasance a cikin raka'ar da yake ciki ne, saboda ya sake yin shi da ma sauran abubuwan da ke biyo bayansa, idan kuma ya kasance a cikin wata raka'ar ce, to wannan raka'ar da ya bar rukuni a cikinta ta ɓaci, kuma raka'ar da take bayanta ita ce za ta tsaya a matsayinta, kuma a cikin duka hali guda biyun za a yi sujjadar rafkanuwa.

❋ **Su kuma wajibai:** Idan mutum ya bar wani abu daga cikinsu da gangan to sallarsa ta ɓaci, idan kuma da mantuwa ne to ba ta baci ba, kuma ba zai dawo gare shi ba, bari dai, kawai zai ƙarfafa shi ne ta hanyar yin sujjadar rafkanwa.

Daga cikin abin da ya gabata, zai bayyana ƙarara cewa lallai su rukunai sun fi ƙarfi sama da wajibai, saboda shi rukuni salla ba za ta taɓa inganta ba sai da shi, amma shi wajibi kuwa ana yin sujjadar rafkanuwa a maimakonshi.

❋ **Su kuma sunnoni:** Salla ba ta ɓaci a sanadiyyar barin wani abu daga cikinsu, ko da kuwa da gangan ne, ko mantuwa, sai dai kuma akwai samun ƙarin lada a cikin aikata su.

Su rukunan salla goma sha huɗu ne, ga bayani a kansu kamar haka:

1. Tsayuwa ga mai iko; saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Ka yi salla a tsaye, amma idan ba za ka iya ba, to ka yi a zauna).[1]

2. Kabbarar harama, ta hanyar faɗin: (Allahu Akbar), saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Idan za ka yi salla, to sai ka yi kabbara).[2]

3. Karatun suratul-Fatiha: Saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Babu salla ga dukkan wanda bai karanta suratul Fatiha ba).[3]

4. Ruku'i: Saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Sannan ka yi ruku'i har sai ka nutsu a cikin ruku'in).[4]

5. Ɗagowa daga ruku'i da daidaituwa a tsaye bayan ɗagowar, saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Sannan sai ka ɗago daga ruku’i har sai ka daidaita a tsaye).[5]

6. Sujjada a kan gaɓɓai guda bakwai: saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (An umarce ni da yin sujjada a kan gaɓoɓi guda bakwai: Goshi; sai kuma yayi nuni da hannunsa zuwa ga hancinsa, da hannaye guda biyu, da gwiwoyi, da saman ‘yan ƙafa).[6]

7. Ɗagowa daga sujjada.

8. Zama tsakanin sujjada guda biyu: Saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Sannan sai ka ɗago daga sujjadarka har sai ka nutsu a zauna).[7]

---

[1] . Bukhari ne ya ruwaito shi (1117).
[2]. Bukhari ne ya ruwaito shi (6251), da Muslim (397).
[3]. Bukhari ne ya ruwaito shi (756), da Muslim (394).
[4]. Bukhari ne ya ruwaito shi (6251), da Muslim (397).
[5]. Bukhari ne ya ruwaito shi (6251), da Muslim (397).
[6]. Bukhari ne ya ruwaito shi (809), da Muslim (490).
[7]. Bukhari ne ya ruwaito shi (6251), da Muslim (397).

9. Nutsuwa a cikin dukkanin rukunai: Saboda fadin Manzon Allah (SAW), ga mutumin nan da bai nutsu a cikin sallarsa ba: (Ka koma ka sake salla, saboda lallai kai ba ka yi salla ba).[1]

10. Tahiyar ƙarshe, saboda umarnin Manzon Allah (SAW) da shi.[2]

11. Zama domin yin tahiyar karshe.

12. Salatin Annabi (SAW) a cikin tahiyar ƙarshe: Kuma abin da ya fi shi ne ya yi ta da lafuzan salatin Ibrahimiyya, amma kuma kowanne lafazi ma ka yi ya wadatar.

13. Jeranta tsakanin rukunai.

14. Sallama: Saboda fadin Manzon Allah (SAW): (Kuma abin da yake halattar da ita shi ne sallama).[3]

[1]. Bukhari ne ya ruwaito shi (6251), da Muslim (397).
[2]. Nasa'i ne ya ruwaito shi (2/240).
[3]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (61), da Tirmizi (3).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

MUBAYA‘AR AƘABA TA BIYU

A yayin da shiga Musulunci ya yawaita a garin Madina kuma ya bayyana, sai dayawa daga cikin mutanen Madina suka zo aikin hajji, hakan ya kasance a cikin shekara ta goma sha uku ne bayan aiko Manzon Allah (SAW), kuma shugabansu ya kasance shi ne: Albara’u ɗan Ma'arur (RA), sai suka magantu da Manzon Allah (SAW) a cikin garin Makka a sirrince, suka kuma yi yarjejeniya a kan za su haɗu da juna a tsakiyar kwanakin jargi (wato kwanaki uku da suke bayan ranar sallar layya), a gurin Aƙaba a cikin duhun dare.

A yayin ɗaya bisa ukun wannan daren ya yi, sai mazaje guda saba in da uku (73), da kuma mata guda uku (3), daga cikin mutanen Madina suka sulale a ɓoye suka zo wajen Manzon Allah (SAW). Sai Manzon Allah (SAW) ya zo musu, tare da baffansa Abbas yana mai ƙarfafa mubaya’ar, duk da cewa a wannan lokacin shi Abbas yana kan addinin mutanensa, kuma sai Abbas ya kasance shi ne farkon wanda ya yi magana sai ya ce da su: Idan kun kasance kuna ganin cewa lallai za ku cika masa alƙawarin abin da kuka kira shi dominsa, kuma za ku zamanto masa masu ba shi kariya daga dukkanin wanda ya saɓa masa, to ku aikata abin da kuka ɗora wa kanku na yin hakan, idan kuwa kuna ganin cewa lallai za ku zama masu miƙa shi ga abokan gabarsa, kuma za ku kunyata shi ku tozarta shi, bayan kuma ya fito zuwa gare ku, to tun daga yanzu gwara ku kyale shi”. [1]

Sai suka ce: Ya Manzon Allah, a kan wanne abu za mu yi maka mubaya’a, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: A kan ji da kuma biyayya, a cikin halin nashadi ko kasala, da ciyarwa a cikin halin kunci ko yalwa, da kuma umarni da kyakkyawa da kuma hani daga

[1]. Abidaya wan-nihaayah (3/160).

mummuna, kuma ku tabbatar cewa za ku taimake ni idan na zo muku garin Yasriba, sai ku ba ni kariya daga irin abin da kuke kare kawunanku da matanku da ‘ya’yanku daga gare shi, ku kuma sakamakonku shi ne Aljanna.[1]

Sai As’ad ɗan Zurara ya ce: “Ku bi a hankali dai ya ku mutanen Yasriba! Lallai fa mu ba mu zo wajensa ba face sai da muka san cewa lallai shi Manzon Allah ne, lallai fitar da shi a yau ɗin nan, to tamkar rabuwa ne da larabawa gaba ɗaya, da kuma kashe mafiya alherinku, kuma akwai yiwuwar za ku shiga yaƙi, in dai za ku iya yin haƙuri a kan haka, to ku yi shi, idan kuwa kuna tsoroce wa kawunanku, to ku ƙyale shi, domin hakan ya fi zama muku uzuri a wajen Allah”. Sai suka ce: Ya kai As’adu ɗan Zuara, muna rantsuwa da Allah ba za mu bar wannan mubaya’a ba, kuma ba za mu janye ta ba. Sai mutane suka tashi, sai suka yi mubaya’a ga Manzon Allah (SAW), ɗaya bayan ɗaya, sai aka sanya wa wannan mubaya’ar suna, “Mubaya’ar Aƙaba mai girma”.[2]

Sai Manzon Allah (SAW) ya zaɓi waɗansu wakilai guda goma sha biyu daga cikinsu a wannan daren, kuma su ne: As’ad ɗan Zurara, da Sa’ad ɗan Rabi’u, da Abdullahi ɗan Rawaha, da Rafi’u ɗan Malik, da Bara’u ɗan Ma’arur, da Abdullahi ɗan Amru ɗan Haram - wanda shi ne mahaifin Jabir, kuma ya musulunta a wannan daren – da Sa’ad ɗan Ubada, da Munzir ɗan Amr, da Ubada ɗan Samit, waɗannan guda taran daga ƙabilar Khazraji suke.

Daga ƙabilar Ausu kuma akwai mutum uku, su ne: Usaidu ɗan Khudair, da kuma Sa'ad ɗan Khaisama, da Rifa’atu ɗan Abdul-Munzir, a yayin da aka gama wannan mubaya’ar, sai Annabin Allah

[1]. Ahmad ne ya rawaito shi (1445).
[2]. Ibnu Hibban ne ya rawaito shi (7012).

(SAW) ya yi wa musulmai izinin yin hijira zuwa garin Madina, sai mutane suka fara yin hijira.

ALHAMIS: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

MAIMUNA ‘YAR HARIS (RA)

❖ Sunanta da haihuwarta:

Ita ce Maimuna ‘yar Haris, matar Annabi (SAW), kuma ‘yar uwar Ummu-Fadl matar Abbas, kuma goggon Khalid ɗan Walid, kuma goggon Abdullahi ɗan Abbas (RA). Abbas ya kasance shi ne yake jiɓintar al’amarinta, sai ya aurar da ita ga Manzon Allah (SAW) bayan mutuwar mijinta Abu Ruhumi ɗan Abdul’uzza, kuma aurenta da Annabi (SAW) ya kasance ne a wani guri mai suna (Sarifa), kusa da Makka, bayan dawowarsa daga umara ta ramako, cikin shekara ta bakwai, kuma ta kasance ita ce mata ta ƙarshe da Manzon Allah (SAW) ya aura.

❖ Rayuwarta da darajojinta:

Ta kasance daga cikin waɗanda suka yi wa annabi (SAW) mubaya’a a Makka tun kafin hijira, ta shahara da tsantseni da kuma nagarta da jin tsoron Allah Maɗaukakin Sarki. Ɗan yar uwarta Yazidu ɗan Asammu yana cewa: “Lallai ita ta kasance mafi tsoron Allah daga cikinmu, kuma mafi sada da zumuncinmu”.[1]

Kuma haƙiƙa annabi (SAW) ya yi mata shaida da imani na gaske, da kuma tabbatuwarsa a cikin zuciyarta, sai ya ce: (‘Yan’uwa mata mummunai su ne: Maimuna da Ummul-Fadl da Asma'u).[2]

❖ Rasuwarta:

Ta rasu a shekara ta sittin da ɗaya bayan hijira, a zamanin halifancin Yazidu ɗan Mu’awiya, a lokacin tana da shekara tamanin, kuma

[1]. Hakim ne ya ruwaito shi: (4/34)
[2]. Nasaa i ne ya ruwaito shi: (8387)

mutuwarta da binne ta duka sun kasance ne a Sarifa, wato wajen da Manzon Allah (SAW) ya aure ta kenan.

Auna fahimtarka a darusan mako na 19			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah Maɗaukaki "Hunafa'a"?		C
	a. Tabbatattu a cikin addini.	b. Masu ƙasƙantar da kai ga Ubangijinsu.	c. Masu karkace wa dukkan addinai zuwa ga Musulunci.
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin abubuwa da ranar Litinin ta keɓanta da su akwai:		A
	a. Bijiro da ayyuka a cikinta.	b. Saukowar mala'iku a cikinta.	c. Tashin alƙiyama a cikinta.
Darasin Aƙida	Tambaya: Abin da ake nufi da Littattafai shi ne:		B
	a. Alƙur'ani mai girma.	b. Dukkan littattafan da Allah Ya saukar wa Manzanninsa.	c. Attaura da Injila da Alƙur'ani kawai.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Aiki da ba ya faɗuwa da gangan, ko da rafkanuwa, ko da jahilci ana kiransa da suna:		C
	a. Sunna.	b. Wajibi.	c. Rukuni.
Darasin Sira	Tambaya: Shugaban Ansarawa a mubaya'ar Aƙaba ta biyu shi ne:		A
	a. Albara'u ɗan Ma'arur.	b. Sa'ad ɗan Mu'azu	c. Mus'ab ɗan Umair.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Wanda ya jiɓinci aurar da Maimuna ga Manzon Allah (SAW) shi ne:		C
	a. Khalid ɗan Walid.	b. As'adu ɗan Zurara..	c. Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib.

MAKO NA ASHIRIN

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI:

SURATUL-BAYYINAH (2)

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ فِي نَارِ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَآۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ شَرُّ ٱلۡبَرِيَّةِ ٦ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أُوْلَٰٓئِكَ هُمۡ خَيۡرُ ٱلۡبَرِيَّةِ ٧ جَزَآؤُهُمۡ عِندَ رَبِّهِمۡ جَنَّٰتُ عَدۡنٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُۚ ذَٰلِكَ لِمَنۡ خَشِيَ رَبَّهُۥ ٨﴾

❖ **Fassara:**

6. Lalle waɗanda suka kafirta daga ma’abota littafi da mushirikai suna cikin wutar Jahannama suna masu dawwama a cikinta. Waɗannan su ne mafiya sharrin halitta.

7. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari, waɗannan su ne mafiya alherin halitta.

8. Sakamakonsu a wajen Ubangijinsu gidajen Aljanna ne na dawwama waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu suna madawwama a cikinsu har abada; Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi. Wannan kuma (sakamako ne) ga wanda ya ji tsoron Ubangijinsa.

❖ **Saƙon da surar ke ƙunshe da shi:**

Bayanin ladan wanda ya gaskata Manzancin Annabi Muhammad (SAW), da kuma sakamakon wanda ya kafirce masa.

❖ **Bakin kalmomi:**

البرية	Albariyya	Halittu; saboda lallai Allah Ya halicce su kuma Ya samar da su.
عدن	Adnin	Tabbatuwa da wanzuwa.

رضي الله عنهم	Radiyallahu anhum	Wato saboda imaninsu da ayyukan ɗa'arsu.
ورضوا عنه	Wa radu anhu	Wato da ladansa da aljannarsa.

❖ Ma'anar ayoyin a dunƙule:

A cikin waɗannan ayoyi, Allah Maɗaukakin Sarki Yana yin hukunci a kan waɗanda suka kafirce ne daga cikin ma'abota littafi da kuma mushirikai cewa: Lallai suna cikin wutar Jahannama, kuma su masu dawwama ne a cikinta, saboda kafircewarsu da Allah, da kuma ƙaryatawarsu ga Manzonsa (SAW), kuma lallai su ne mafiya sharrin halittu gaba ɗaya, saboda sun san gaskiya, amma sun kau da kai daga gare ta, amma kuma waɗanda suka yi imani da Allah da Manzonsa kuma suka yi aiki nagari, to akwai mafi kyawun sakamako da mafi kyawun siffofi a gare su, suna cikin aljanna ta ni'ina, suna masu dawwama a cikinta, kuma sune mafiya alherin halittu baki ɗaya, haƙiƙa Allah Ya yarda da su saboda bin umarninsa da kiyaye dokokinsa, kuma suma sun yarda da abin da Allah Ya ba su na ni'ima madawwamiya ta din-din-din.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Bayanin ladan wanda ya yi imani kuma ya tsaya a kan addinin Musulunci, kuma shi ne samun yardar Allah da kuma dawwama a cikin gidan aljanna.
2. Bayanin sakamakon dukkan wanda ya kafirce kuma ya juya baya daga barin addinin Allah, wanda shi ne haɗuwa da fushin Allah da kuma dawwama a cikin wutar Jahannama.
3. Lallai mummunai su ne mafiya alherin halitun Allah, kuma lallai tabbas kafirai su ne mafiya sharrin halittun Allah baki ɗaya.
4. Falalar jin tsoron Allah Maɗaukakin Sarki, kuma lallai shi ne sababin samun yardar Allah.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR SALLAR WUTIRI

An karbo daga Aliyu (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Ya ku ma'abota Alƙur'ani! Ku dinga yin sallar wutiri, saboda lallai Allah wutiri ne, (wato Shi ɗaya ne) kuma yana son wutiri**).[1]

❖ Sharhi:

Wutiri sunna ce mai ƙarfi, Annabi (SAW) ba ya barin yin ta, a halin bulaguro ko halin zaman gida, a halin lafiya, ko na rashin lafiya, saboda wutiri yana daga cikin sunayen Allah Maɗaukakin Sarki, Saboda kuma Shi Allah ɗaya ne a zatinsa da ayyukansa da siffofinsa, amma kuma halittunsa gaba ɗayansu shafa'i ne, an haliccesu ne biyu-biyu, shi kuma Allah tsarki ya tabbata a gare shi, Yana son dukkanin abin da ya dace da sunayensa da siffofinsa, Shi Mai ilimi ne kuma Yana son ilimi, Mai kyautatawa ne kuma Yana son kyautatawa, Mai kyau ne, kuma Yana son kyau, kuma wutiri ne, (wato Mara), kuma Yana son wutiri.

Saboda haka annabi (SAW) ya kwaɗaitar da al'ummarsa a kan yin sallar wutiri, ya kuma keɓance kwaɗaitarwarsa ga ma'abota Alƙur'ani waɗanda su ne masu haddace shi da karanta shi, kuma an keɓance su ne da ambato saboda ƙarin ɗaukakarsu da kuma ba su muhimmanci ɗoriya a kan sauraran bayi, kuma saboda suna da fifiko a kan wasunsu, ka ga kenan su ɗin ababen koyi ne, jagorori ne, kuma su mutanen Allah ne, kuma keɓantattunsa ne, kuma suna da ilimi da zai kai su ga aikin samun kusanci ga Allah, sai umarnin ya fi ƙarfi a gare su duk da cewa yin sallar wutiri abu ne da ake nema daga kowa-da-kowa.

---

[1]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (1416).

Kuma kowanne musulmi yana da damar yin sallar wutiri a cikin kowanne ɓangare na dare; cikin farkonsa ko tsakiyarsa, ko kuma ƙarshensa. Kuma dukkan wanda ya ji tsoron kada barci ya yi galaba a kansa, to sai ya yi wuturinsa kafin ya kwanta barci, ko da kuwa raka'a ɗaya ce, amma duk wanda kuwa yake kyautata tsammanin cewa zai farka a karshen dare, to yin sallar wutirinsa a ƙarshen daren shi yafi falala, saboda shi ne daidai lokacin saukar Ubangiji tsarki ya tabbata a gare shi, da kuma amsawarsa ga addu'o'in bayinsa.

❖ **Abubuwan da za mu koya daga wannan hadisin**:

1. Lallai wutiri sunna ce mai ƙarfi, barinta ko yin sakaci da ita bai kamata ba.
2. Tabbatar da siffar so ga Allah Maɗaukakin Sarki.
3. Lallai sallar wutiri ita ce mafi ƙarfi da falalar nafulfili.
4. Lallai yana daga cikin rahamar Allah da kuma sauƙaƙawarsa ga bayinsa kasancewar Ya shar'anta musu yin sallar wuturi a cikin adadi da siffofi mabambamta.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA MANZANNI

Imani da manzanni: Shi ne gaskatawa ta yankan shakku cewa lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya aiko da wani Manzo cikin kowacce al'umma, wanda yake kiran su zuwa ga bauta wa Allah Shi kaɗai ba tare da wani abokin tarayya ba; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma lallai ne, haƙĩƙa, Mun aiko wani Manzo a cikin kõwace al'umma da (ya ce da su): "Ku bauta wa Allah, kuma ku nĩsanci dãgũtu)).[1] Kuma Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma bãbu wata al'umma fãce wani mai gargaɗi yã zo mata)).[2]

Su kuma manzanni su ne mafiya falalar halittu kuma zaɓaɓɓunsu, Allah Ya zaɓe su, ya kuma yarda da su, domin ɗaukar saƙonsa da isar da shi, da kuma isar da addininsa; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Allah Yana zaɓan manzanni daga cikin mala'iku, haka ma daga cikin mutane. Lallai Allah Mai ji ne kuma Mai gani)).[3]

Kuma farkon manzanni shi ne: Annabi Nuhu (AS); Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Lallai ne Mu, Mun yi wahayi zuwa gare ka, kamar yadda Muka yi wahayi zuwa ga Nũhu da annabãwa daga bãyansa)).[4] Na ƙarshensu kuma shi ne Annabi Muhammadu (SAW); Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, sai dai shĩ Manzon Allah ne kuma cikamakon Annabãwa)).[5]

Kuma su manzanni mutane ne da aka halicce su, ba su da wani abu daga cikin abubuwan da Allah Ya keɓanta da su na ayyuka ko na

---

[1]. (Annahal: 36).
[2]. (Fadîr: 24).
[3]. (Alhaj: 75).
[4]. (Annisa'i: 163).
[5]. (Al-Ahzab: 40).

cancantar bauta; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce game da Annabinsa Muhammadu (SAW): ((Ka ce: "Bã na mallaka wa kaina wani amfãni, kuma haka ba na tunkuɗe wata cũta, fãce abin da Allah Ya so. Kuma dã na kasance inã sanin gaibi, dã lallai ne, nã Yawaita samar da alhẽri, kuma cũta bã zã ta shãfe ni ba, nĩ ba kowa ba ne face mai gargaɗi, kuma mai bishãra ga mutãne waɗanda suke muminai)).[1]

❋ **Kuma imani da manzanni ya ƙunshi al'amura guda hudu:**

Na farko: Imani da gaskata cewa lallai su 'yan aike ne daga Allah Maɗaukakin Sarki.

Na biyu: Imani da sunayen waɗanda muka san sunayensu daga cikinsu, amma kuma waɗanda ba mu san sunayensu ba, to sai mu yi imani da su a dunƙule.

Na uku: Gaskata abin da ya tabbata daga gare su na labaransu da hadisansu.

Na huɗu: Aiki da shari'ar wanda aka aiko shi zuwa gare mu, wanda shi ne Annabi Muhammadu (SAW); Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((To, Ina rantsuwa da Ubangijinka, ba za su yi ĩmãni ba, sai sun yarda da hukuncinka cikin abin da ya shiga tsakãninsu na saɓani, sannan kuma ba su sãmu wani ƙunci a cikin zukãtansu ba, daga abin da ka hukunta, kuma su sallama sallamãwa ta gaskiya)).[2]

❋ **Kumu imani da manzanni yana da fa'idoji masu girma, daga cikinsu akwai:**

Na farko: Sanin rahamar Allah Maɗaukakin Sarki, da kulawar shi ga bayinsa, ta yadda ya aiko musu manzanni domin su shiryar da su

[1] . Suratul Araaf: (188)
[2] . Suratun Nisaa i: (65)

zuwa ga hanyar Allah Maɗaukakin Sarki, su kuma bayyana musu yadda za su bauta masa, saboda hankalin mutane ba zai iya kaɗaituwa wajen yin hakan ba.

Na biyu: Gode wa Allah Maɗaukakin Sarki a kan wannan ni’ima mai matuƙar girma.

Na uku: Son manzanni (AS), da girmama su da kuma yabon su da irin abin da ya dace da su.

LARABA: DARASI CIKIN FIKIHU

WAJIBAN SALLA DA SUNNONINTA

❖ **Wajiban salla guda takwas ne, su ne:**

1. Dukkanin kabarbari in ban da kabbarar harama.
2. Faɗin (Sami'Allahu liman hamidah) ga limami, da kuma me yin sallah shi kaɗai.[1]
3. Faɗin (Rabbana wa lakal-hamdu).[2]
4. Faɗin (Subha Rabbiyal-Azim) a cikin ruku'i, kuma sau ɗaya shi ne wajibin, amma sunna ce a faɗa sau uku.[3]
5. Faɗin (Subhana-Rabbiyal-A'ala), kuma sau ɗaya shi ne wajibi, amma kuma faɗinsa sau uku sunna ce.[4]
6. Faɗiin (Rabbig-firli) a tsakanin sujjada guda biyu, kuma sau ɗaya shi ne wajibi, amma kuma faɗinsa har sau uku sunna ce.[5] kuma roƙon gafarar Allah idan aka yi da kowanne irin lafazin ma, to ya wadatar.
7. Zama domin yin tahiyar farko.[6]
8. Karanta tahiyar farko, wacce ita ce: "Attahiyyatu lillahi, was-salawatuɗ-ɗayyibatu, assalamu alaika, ayyuhan-nabiyyu, wa rahmatullahi, wa barakatuhu, assalamu alaina, wa ala, ibadul-lahis-salihina, ash-hadu an-la-ilaha illal-laahu, wa ash-hadu anna, Muhammadan abduhu wa rasuluhu".[7]

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (796).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (796).
[3]. Muslim ne ya rawaito shi (772).
[4]. Muslim ne ya rawaito shi (772).
[5]. Nasa'i ne ya rawaito shi (1144).
[6]. Bukhari ne ya rawaito shi (6230), da Muslim (402).
[7]. Bukhari ne ya rawaito shi (2630), da Muslim (402).

❖ **Sunnonin salla:**

Sunnonin salla nau'i biyu ne: Sunnoni na maganganu, da sunnonin na ayyuka.

Nau’i Na Farko: Sunnoni na maganganu**,** su suna da yawa, daga cikin su akwai: Addu’ar buɗe salla, da faɗin “A’uzu billahi minash-shaiɗanir-rajim”, da faɗin: “Bismil-lahir-Rahmanir-Rahim” da faɗin: “Amin”, da karanta abin da ya sawwaka daga cikin Alƙur'ani bayan karatun fatiha a cikin raka’o'i biyu na farko, da tsawaita karatun raka'ar farko a kan na raka’a ta biyu, da bayyana karatu a cikin sallar da ake bayyanawa, da kuma sirranta shi a cikin sallar da ake sirrantawa, da kuma faɗin wannan addu ar: “Mil’as- samawaati wa mil’al-ardi, wa mil’a ma shi’ita min shai’in ba’adu”, da neman tsarin Allah bayan gama karatun tahiyar karshe kafin sallama, ta hanyar faɗin: “Ya Allah ina neman tsarinka daga azabar wutar Jahannama, da azabar ƙabari, da fitinar rayuwa da ta mutuwa, da fitinar Dujal”, da kuma yin addu’a ta neman abin da mutum yake so daga wajen Allah bayan tahiyar karshe.

Nau’i na biyu: Sunnoni na aikace-aikace, kamar ɗaga hannaye biyu a yayin kabbarar harama, da lokacin sunkuyawa domin yin ruku’i, da kuma yayin ɗagowa daga ruku’i, da ɗaura hannun dama a kan na hagu, da ɗora su duka a kan kirji a halin tsayuwa, da kallon wajen yin sujjada, da ɗaura hannaye biyu a kan gwiwowi a yayin ruku’i, da sanya kai daidai da gadon baya, kada ya sunkuyar da shi kuma kada ya ɗaga shi sosai, da nesanta cikinsa daga cinyoyinsa, da nesanta cinyoyi daga ƙwabrinsa a cikin sujjada, da zama na “Tawarruki”, (wato zama a kan mazaune) a tahiya ta karshe, da kuma zaman “Iftirashi”, (wato zama a kan ƙafar hagu da kafa ta dama) a zaman da ba na ƙarshe ba.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

SHIRI DOMIN HIJIRAR ANNABI

Bayan mubaya'ar Aƙaba ta biyu, Annabi (SAW) ya yi wa Musulmi izinin yin hijira zuwa Madina, sai mutane suka yi yunƙuri yin ta, tare da abin da take ɗauke da shi na sadaukar da maslahohi da dukiyoyi, sai Abu Salama ya kasance farkon wanda ya fita shi da matarsa Ummu Salama (RA), sannan sai mutane suka fita a kai a kai, sashinsu na biye da sashi, har ya zama babu wanda ya rage a Makka sai wanda mushirkai suka kama a bisa tilas, shi kuma Annabi (SAW) sai ya zauna yana jiran izini daga Ubangijinsa, tare da Abubakar da Ali (RA), su ma sun dakata ne da umurninsa gare su.

Daga cikin waɗanda suka yi hijira kuma suka sadaukar da dukiyarsu akwai: Suhaibu (RA), domin shi lokacin da ya nufaci yin hijira, kafiran Ƙuraishawa sun ce da shi: Ka zo ba ka da komai, sai dukiyarka ta yawaita a wajenmu, har ka kai matsayin da ka kai, sannan kuma ka ce za ka fita da ranka da dukiyarka?! Wallahi hakan ba zai faru ba. Sai ya ce: Yanzu idan na ba ku dukiyata za ku ƙyale ni na tafi? Sai suka ce: E. Sai ya ce: Ina shaida muku cewa lallai haƙiƙa na bar muku dukiyata. Sai labarin haka ya isa wurin Manzon Allah (SAW), sai ya ce: (Ciniki ya yi riba, ciniki ya yi riba, ciniki ya yi riba).[1]

Kuma yayin da Abubakar (RA) ya nemi izinin yin hijira, sai Manzon Allah (SAW) ya ce da shi: (Kada ka yi gaggawa; Ina fatan Allah Ya haɗa ka da abokin tafiya), sai Abubakar ya tanadi ababen hawa guda biyu, sai ya ɗaure su a gidansa yana ciyar da su, yana jiran Allah Maɗaukakin Sarki Ya ba da izinin yin hijira ga Manzonsa (SAW).[2]

Yayin da mushirkai suka ga sahabban Manzon Allah (SAW) suna fita kuma suna tafiya da bayi da mata, sai suka kamu da tsoro da firgici; saboda Annabi Muhammadu (SAW) yana da matuƙar

[1]. Hakim ne ya rawaito (3/450).
[2]. Albidaya wan-nihaya (4/444).

jagoranci da tasiri, sahabbansa kuma sun kai maƙura wurin fansa da niyya, ga kuma ƙabilar Ausu da Khazraj suna cikin maƙuran ƙarfinsu da garkuwansu, Madina kuma waje ne mai hatsari; saboda tana kusa da Makka, kuma ayarin kasuwanci na bi ta nan.
Sai shugabannin ƙabilu suka taso, suka kuma taru a gidan tattaunawarsu, sai Ibilis ya halarci wannan taro a kamannin wani dattijo daga Najid, sai wasu suka ce a kori Annabi (SAW), wasu kuma suka ce a kama shi, amma ba su haɗu a kan kowane ɗaya daga cikin waɗannan ra'ayoyi biyun ba.

Sannan sai suka haɗu a kan cewa a kashe shi, kuma a samu mutum ɗaya daga kowace ƙabila ya yi tarayya wurin kashe shi, sai su dake shi da takobi dukan mutum ɗaya, in ya so jininsa ya rarrabu cikin ƙabilu, ta yadda Banu Abdi Manaf ba za su iya yaƙan su gaba ɗayansu ba, sai su yarda da karɓar diyya.[1]
Kuma sun kasance suna da yaƙinin cewa wannan shiri nasu zai yi nasara, sai dai Allah Mai rinjaye ne a kan al'amarinsa, sai Jibrilu ya sauka da wahayi daga Allah yana mai ba shi labarin makircin da Ƙuraishawa suka yi, da kuma cewa haƙiƙa lallai Allah Ya yi masa izinin yin hijira; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma ka tuna lokacin da waɗanda suka kafirta suke ƙulla maka makirci don su tsare ka to kuma su kashe ka ko su kore ka. Suna kuma shirya makirci Allah kuma Yana mayar musu sakamakon makircinsu. Allah kuma Shi ne Ya fi masu makirci iya sakayyar makirci)).[2]

[1]. Albidaya wan-nihaya (4/439).
[2]. (Al'Anfal: 30).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SAFIYYA ‘YAR HUYAYYU (RA)

❖ Sunanta da haifuwarta:

Ita ce Uwar muminai Safiyya ‘yar Huyayyu ‘yar Ahɗab, daga ƙabilar Banu Nadir, kuma nasabarta na danganuwa zuwa ga Annabi Haruna ɗan Imran.

❖ Rayuwarta da falalarta:

Safiyya (RA) ta kasance daga cikin jagororin mata masu yawan ibada, da kaifin hankali, da tsantseni, da gudun duniya, da nagarta, da yawan sadaka, haka kuma, ta kasane mai daraja, ‘yar dangi, kuma mai kyawun halitta.

Ta rawaito hadisai masu yawa daga Annabi (SAW), kuma dayawa daga cikin sahabbai sun rawaito daga gare ta, daga cikinsu akwai: Abdullahi ɗan Umar, da Anas ɗan Malik, da Aliyyu ɗan Hussain.

Annabi (SAW) ya aure ta a shekarar da aka yi yaƙin Khaibar, shekara ta bakwai bayan hijira, a lokacin tana ‘yan shekara sha bakwai, tana daga cikin mata da aka kama a yaƙin Khaibar, sai Annabi (SAW) ya ba ta zaɓi tsakanin abu biyu, ko ya ‘yanta ta sai ta koma wurin ahalinta, ko kuma ta musulunta ya aure ta, sai ta zaɓi Allah da Manzonsa, sai ta musulunta, sai Manzon Allah (SAW) ya aure ta.[1]

Kuma ta kasance a baya ta taɓa yin mafarkin wannan aure nata; ya zo a hadisi cewa: Annabi (SAW) ya tambaye ta game da alamun bugu da ke idonta, sai ta ce: Lallai ni na taɓa yin mafarki irin mafarkin da mutum ke yi a cikin bacci, a cikin mafarkin na ga wani wata ya faɗo a kan cinyata, sai na ba da labarin haka ga mijina, sai ya mare ni, sai ya ce: Wato sarkin Yasrib (Madina) kike so ko?![2]

---

[1]. Albidaya wan-nihaya (4/216).
[2]. Ɗabarani ne ya rawaito (177).

Annabi (SAW) ya yabe ta, kuma ya yabi nasabarta; haƙiƙa wata rana ya shiga wajenta sai ya riske ta tana kuka, sai ya ce: (Me ya saka ki kuka?), ta ce: An ce da ni ‘yar bayahude. Sai ya ce: (Ke lallai ‘yar Annabi ce, kuma baffanki ma Annabi ne, ga shi kuma kina ƙarƙashin Annabi a matsayin matar aure);[1] Abin da ake nufi da babanta shi ne Annabi Haruna (AS), Baffanta kuma Annabi Musa (AS), mijinta kuma Annabi Muhammadu (SAW).

Daga cikin abubuwan da Annabi (SAW) yake bayyana mata na so akwai cewa wata rana ya so ya ɗauke ta a kan raƙumi, sai ya kafa mata cinyarsa don ta hau, sai ta ji nauyin a ce ta ɗaura ƙafarta a kan cinyarsa, a maimakon haka sai ta ɗaura guiwowinta a kan cinyarsa, sai ta hau.

A jinyar da Annabi (SAW) ya yi lokacin wafatinsa, matansa sun taru a wajensa, sai Safiyya ta ce: Ina rantsuwa da Allah ya Manzon Allah, tabbas zan so a ce wannan jinya da kake fama da ita ni ne nake fama da ita ba kai ba. Sai Annabi (SAW) ya ce: (Ina rantsuwa da Allah tabbas da gaske take maganar nan).[2]

Rasuwarta:

Safiyya (RA) ta rasu a shekara ta 50 bayan hijira, a lokacin halifancin Mu’awiya (RA), an kuma binne ta a maƙabartar Baƙi’.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito (3894).
[2]. Hakim ne ya rawaito (4/29).

Auna fahimtarka a darusan mako na 20			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah Maɗaukaki: "Fi jannati adnin"?		A
	a. A aljannatai na ni'ima da tabbatuwa.	b. A aljannar Firdausi maɗaukakiya.	c. A kasuwar aljanna.
Darasin Hadisi	Tambaya: Mene ne hukuncin sallar wutiri?		C
	a. Farilla ce a kan kowa.	b. Farillace ta kifaya.	c. Sunna ce mai ƙarfi.
Darasin Aƙida	Tambaya: Wane ne farkon Manzanni?		B
	a. Idris	b. Nuhu.	c. Ibrahim.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin Wajiban salla akwai:		A
	a. Faɗin: "Rabbana wa lakal hamdu".	b. Karatun Fatiha.	c. Tasowa daga ruku'i.
Darasin Sira	Tambaya: Farkon wanda ya fita don yin hijira shi ne:		C
	a. Abubakar Siddiƙ.	b. Aliyyu ɗan Abu Ɗalib.	c. Abu Salama.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Annabi (SAW) ya auri Safiyya 'yar Huyayyu a shekara ta:		A
	a. 7 bayan hijira.	b. 8 bayan hijira.	c. 9 bayan hijira.

MAKO NA ASHIRIN DA ƊAYA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUT-TIN

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلتِّينِ وَٱلزَّيۡتُونِ ١ وَطُورِ سِينِينَ ٢ وَهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ٱلۡأَمِينِ ٣ لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِيٓ أَحۡسَنِ تَقۡوِيمٖ ٤ ثُمَّ رَدَدۡنَٰهُ أَسۡفَلَ سَٰفِلِينَ ٥ إِلَّا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فَلَهُمۡ أَجۡرٌ غَيۡرُ مَمۡنُونٖ ٦ فَمَا يُكَذِّبُكَ بَعۡدُ بِٱلدِّينِ ٧ أَلَيۡسَ ٱللَّهُ بِأَحۡكَمِ ٱلۡحَٰكِمِينَ ٨﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin ƙai

1. Ina rantsuwa da ɓaure da zaitun.
2. Da dutsen Ɗuri Sinana.
3. Da wannan gari amintacce (wato Makka).
4. Haƙiƙa mun halicci mutum a kan mafi kyan diri.
5. Sannan Muka mayar da shi mafi ƙasƙancin ƙasƙantattu.
6. Sai fa waɗanda suka yi imani, suka kuma yi ayyuka nagari, to su kam suna da lada ba mai yankewa ba.
7. To (kai kafiri) me ya sa kake ƙaryata ranar sakamako bayan haka?
8. Ashe Allah ba Shi ne Mafi iya hukuncin masu hukunci ba?

❖ Saƙon da surar ta ƙunsa:

Tunatarwar Allah ga mutun a kan ni’imar daidaita halittarsa da ya yi, da kuma cikar Manzanci na ƙarshe.

❖ Bakin kalmomi:

وطور سينين	Wa ɗuri sinin	Dutsen Ɗuri Sina, wanda Allah Ya yi magana da Annabi Musu (AS) a kansa.
وهذا البلد الأمين	Wa hazal-baladil-amin	Garin Makka.
في أحسن تقويم	Fi ahsani taƙwim	A cikin mafi kyawun halitta.
أسفل سافلين	Asfala safilin	Wuta
غير ممنون	Gairu mamnun	Wanda ba ya yankewa.
أليس الله بأحكم الحاكمين	Alaisallahu bi Ahkamil-hakimin	Don haka, ba zai yuwu a ce ya bar bayinsa kara zube ba, ba a umurtan su ba a hana su, ba a ba su lada, kuma ba a musu uƙuba.

❖ Ma’anar surar a dunƙule:

Wannan sura tana daga cikin surori da suka sauka a Makka, waɗanda suke farawa da rantsuwa, Allah Mai girma da ɗaukaka Ya yi rantsuwa da waɗannan bishiyoyi guda biyu: Ɓaure da Zaitun; saboda amfaninsu mai yawa, da kuma cewa suna da yawa a ƙasar Sham, wacce ita ce wajen annabtakar Annabi Isa (AS), sannan Ya rantse da Ɗuri sinana, wajen annabtakar Annabi Musa (AS), ya kuma bi bayansu da rantsuwa da gari amintacce, wato: “Makka”, wacce ita ce mahallin annabtakar Annabinmu Muhammmadu (SAW), babu shakka lallai waɗannan wajaje guda uku wajaje ne masu tsarki, kuma daga gare su aka turo uku daga cikin manyan manzanni.

Abin da aka yi rantsuwa a kansa kuma shi ne: Ƙayatacciyar halittar da Allah Ya yi wa mutum; saboda Allah Ya halicce shi da cikakkiyar halitta, mai madaidaitan gaɓoɓi, mai tsayayyen dirin jiki, bai rasa komai ba cikin abubuwan da yake da buƙata na zahiri da na baɗini,

amma tare da waɗannan ni’imomi, dayawa daga cikin halittu suna baudɗewa daga gode wa Allah Mai ni’imtarwa, suna shagaltuwa da wasa da wargi, haƙiƙa sun yardar wa kawunansu ƙasƙantattun al’amura, da munanan ɗabi’u, sai Allah Ya jefa su mafi ƙasƙancin waje a wutar Jahannama, wajen masu saɓo masu bijire wa Ubangijinsu, amma wanda Allah Ya karrama shi da imani da aiki nagari; to wannan yana da darajoji maɗaukaka, da lada mara yankewa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Bayanin matsayin waɗannan bishiyoyi guda biyu (ɓaure da zaitun), da girman amfaninsu.
2. Bayanin darajar Makka da alfarmarta, da kuma cewa ita abar girmamawa ce kuma amintacciya.
3. Bayanin matsayin ƙasar Sham, da kuma cewa lallai ita ƙasa ce mai albarka.
4. Bayanin falalar da Allah Ya yi wa mutum, yayin da ya halicce shi cikin mafi kyawun halitta, da mafi daidaituwar dirin jiki.
5. Cewa lallai Allah Mai girma da ɗaukaka Shi ne Mafi iya hukuncin masu hukunci kuma mafi adalcinsu, a cikin ƙaddararsa da shari’arsa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI TSORATARWA A KAN ƘAURACEWA DA GABA DA JUNA

An kaɓo daga Abu Huraira (RA), cewa lallai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ana buɗe ƙofofin aljanna a duk ranar Litinin da ranar Alhamis, sai a gafarta wa kowane bawa da ba ya haɗa wani abu da Allah a bauta, sai dai mutumin da a tsakaninsa da ɗan'uwansa akwai gaba, sai a ce: Ku saurara wa waɗannan har sai sun shirya tsakaninsu, Ku saurara wa waɗannan har sai sun shirya tsakaninsu, Ku saurara wa waɗannan har sai sun shirya tsakaninsu).[1]

❖ **Sharhi:**

Daga cikin mafi bayyanar siffofin 'yan aljanna akwai: Tsaftar zukatansu, da kuɓutarsu daga ƙeta da gaba da ƙullata da hasada; domin lallai Allah Maɗaukakin Sarki Yana gusar da haka daga zukatansu, har sai sun zamo 'yan'uwa masu son juna a aljanna.

A wannan hadisi kuwa, Manzon Allah (SAW) yana bayyana cewa lallai wannan siffa abu ne da ake so kowane mumini ya zama yana da shi; saboda ana buɗe ƙofofin aljanna a duk ranar Litinin da Alhamis; saboda yawan rahama da ke sauka a cikinsu, da yawan gafara da yafiya ga halittu, sai a gafarta zunubin kowane bawa da ba ya shirka ga Allah, sai dai mutumin da a tsakaninsa da ɗan'uwansa musulmi akwai saɓani, na gaba ko yanke zumunci, ko husuma, sai a ce wa mala'iku: Ku saurara wa waɗannan mutane biyu, ku jinkirta gafarta zunubansu har sai sun shirya kuma sun gusar da gabar da ke tsakaninsu.

❖ **Abubuwan da za mu koya daga hadisin:**

1. Falalar ranar Litinin da Alhamis
2. Hani a kan gaba da ƙauracewar musulmi a Tsakanin junansu.

[1]. Muslim ne ya rawaito (2565).

3. Wajibcin yin gaggawan yin sulhu, da barin ci gaba da husuma sama da kwana uku.
4. Ana kawar da ƙauracewa ta hanyar sallama, idan ɗayansu ya yi sallama ga ɗayan, to ƙauracewar ta gushe.
5. Cewa lallai gafarta wa kowane ɗaya daga cikinsu yana ginuwa ne a kan tsaftarsa da gushewar gabarsa, abokinsa ya janye ko bai janye ba.
6. Lallai Allah Mai girma da ɗaukaka yana so bayinsa su zamo masu haɗin kai ba masu rarrabuwa ba, masu son junansu ba masu gaba ba.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA RANAR LAHIRA

Ranar lahira: Ita ce ranar alƙiyama, an kira ta da ranar ƙarshe ne saboda babu wata rana bayanta; saboda ‘yan aljanna za su tabbata a gidajensu, ‘yan wuta ma a gidajensu, kuma shi ne abin da hikima ta zartar, wato Allah Maɗaukaki Ya sanya wa wannan halitta makoma da zai musu sakayya a cikinta a kan abin da Ya shar’anta musu kuma Ya saka musu a kai; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ko kuna tsammani ne cewa Mun halicce ku ne ba manufa kuma ku ba za a dawo da ku gare Mu ba)).[1]

❋ **Kuma imani da ranar lahira yana ƙunshe da al’amura guda huɗu:**

Na farko: Imani da abin da zai kasance a ƙabari na tambayar mala’iku biyu, da azabar ƙabari da ni’imarsa; saboda haƙiƙa hadisi ya tabbata daga Annabi (SAW) cewa ya ce: (Ba dan kada ku daina binne mamatanku ba, da na roƙi Allah Ya jiyar da ku game da azaban ƙabari abin da nake ji daga gare shi), sannan ya juyo da fuskarsa, sai ya ce: (Ku nemi tsarin Allah daga azabar ƙabari), sai suka ce: Muna neman tsarin Allah daga azabar ƙabari, ya ce: (Ku nemi tsarin Allah daga azabar ƙabari), suka ce: Muna neman tsarin Allah daga azabar ƙabari.[2]

Na biyu: Imani da tashi daga ƙabari, kuma shi ne raya matattu daga ƙaburburansu; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Sannan kuma lallai tabbas bayan haka za ku mutu () Sannan kuma haƙiƙa za a tashe ku ranar alƙiyama)),[3] kuma Manzon Allah (SAW) Ya ce: (Za a tashi mutane ranar alƙiyama babu takalma a ƙafafunsu, tsirara, da kuma loɓa).[4]

Na uku: Imani da hisabi da sakamako a kan ayyuka; Allah Maɗauakaki Ya ce: ((Za Mu kuma sanya ma’auni na adalci a ranar

---

[1]. (Al-Mu’minun: 115).
[2]. Muslim ne ya rawaito (7142).
[3]. (Al-Muminun: 15-16).
[4]. Bukhari ne ya rawaito (6527), da Muslim (2859).

alƙiyama, sannan ba za a zalunci kowane rai da komai ba, ko da ya zama gwargwadon ƙwayar komayya ne, za Mu zo da shi. Kuma Muni sa Masu hisabi!)).[1] Kuma Annabi (SAW) ya ce: Lallai Allah zai kusanto da mumini, sai Ya ɗaura masa suturarsa ya suturce shi, sai Ya ce: Shin ka tuna da laifi kaza? Shin ka tuna da laifi kaza? Sai ya ce: E ya Ubangijina, har sai idan ya tabbatar masa da zunubansa, ya kuma tabbatar a ransa cewa ya halaka; sai ya ce: Na suturce maka su a duniya, kuma Ni zan gafarta maka su yau, sai a bashi takardar kyawawan ayyukansa, amma ka ga kafiri da munafukai, sai a shaidu su ce: ((Waɗannan su ne suka yi Ubangijinsu ƙarya. Ku saurara, la'anar Allah ta tabbata a kan azzalumai)).[23]

Na huɗu: Imani da aljanna da wuta, da kuma cewa su makoma ne na har abada ga halittu; Allah Maɗaukai Ya ce: ((Lallai mutanen kirki tabbas suna cikin ni'ima () Lallai kuma fajirai tabbas suna cikin wutar Jahima () Za su ƙonu da ita ranar sakamako)).[4]

❋ **Kuma imani da ranar lahira yana haifar da abubuwa masu girma kamar haka:**

Na farko: Kwaɗaituwa wurin yin aikin ɗa'a, tare da fatan samun sakamako a wannan ranar, da guje wa aikata saɓo don tsoron uƙubarsa.

Na biyu: Rarrashin mumini a game da abin da ya kuɓuce masa daga wannan rayuwa ta duniya mai ƙarewa, da abin da yake fatan samun sa na ni'ima da lada a ranar lahira dawwamammiya.

---

1. (Al-Anbiya: 47).
2. (Hudu: 18).
3. Bukhari ne ya rawaito (2442).
4. (Al-infiɗar: 13-15).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

ABUBUWAN DA BA A SO A YI SU A SALLA

Akwai wasu ayyuka da ba sa lalata salla, sai dai kuma suna tauye cikarta da ladanta, sai aka yi hani a kansu a matsayin ababe da ake ƙi, waɗanda su ne kamar haka:

1. Mutum ya yi salla alhali fitsari ko ba haya ya matse shi, yana ta matse shi, ko kuma a gaban wani abinci da yake son cinsa; saboda faɗin Annabi (SAW): (Babu salla idan aka kawo abinci, ko kuma wanda fitsari ko ba haya ya matse shi).[1]
2. Waiwaye a cikin salla ba tare da buƙata ba; saboda faɗin Annabi (SAW): (Shi wani abu ne da shedan yake ƙwacewa a sallar bawa).[2]
3. Rufe idanu biyu a salla; saboda hakan yana kama da aikin majusawa a wajen bautansu na wuta.
4. Rufe baki da wani abu a salla ba tare da buƙata ba; saboda Annabi (SAW) Ya yi hani a kan mutum ya rufe bakinsa da wani abu.[3]
5. Haɗa tsakanin yatsu; saboda hani da Annabi (SAW) ya yi a kai.[4]
6. Naɗe tufafi da ɗage gashi idan ya sauka; Manzon Allah (SAW) ya ce: (An umurce ni da ni sujjada a kan gaɓoɓi, kuma kada na tattare gashi ko tufafi).[5]
7. Shimfiɗa zira'in hannu a sujjada; saboda faɗin Annabi (SAW): (Ku daidaitu a sujjada, kuma kada ɗayanku ya shimfiɗa zira'insa biyu irin shimfiɗawar kare).[6]
8. Zaman kare a cikin salla; saboda Annabi (SAW) ya yi hani a kan yin zaman kare a salla.[7]

---

1. Muslim ne ya rawaito (560).
2. Bukhari ne ya rawaito (751).
3. Abu Dawuda ne ya rawaito (643), da Tirmizi (379).
4. Hakim ne ya rawaito (1/206).
5. Bukhari ne ya rawaito (815), da Muslim (490).
6. Bukhari ne ya rawaito (822).
7. Ahmad ne ya rawaito (276).

Abin da ake nufi da zaman kare shi ne mutum ya shimfiɗa ƙafafunsa biyu, wato ya sanya samansu ya kalli ƙasa, sannan ya zauna a kan dunduniyarsa.

Siffa ta biyu ta zaman kare kuma ita ce mutum ya kafa cinyoyinsa biyu da ƙaurinsa biyu, sai kuma ya zauna a kan mazaunansa. Dukkansu sifofi biyun ba a so ana yin su.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

HIJIRA

Yayin da Allah Maɗaukaki Ya yi iznin hijira ga Manzonsa (SAW), sai ya tafi gidan Abubakar (RA) a tsakiyar rana, sai ya nemi izini, sai aka masa izinin shihga, sai Annabi (SAW) ya ce: (Ka fitar da waɗanda suke tare da kai), sai Abubakar ya ce: Ina fansarka da mahaifina, ai su iyalanka ne ya Manzon Allah. Ya ce: (To ni fa an mun izinin fita), sai Abubakar ya ce: Shi na aboce ka ne. Manzon Allah (SAW) ya ce: “E”.

Sannan Manzon Allah (SAW) ya dawo gidansa yana jiran dare ya yi,[1] sai ya umurci Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (RA) da ya zo ya yi bacci a kan shimfiɗarsa, ya kuma lulluɓu da kuren bargonshi ɗan Hadaramaut, ya ce kuma babu abin da yake tsoro daga gare su da zai same shi. Yayin da dare ya yi, sai mushirkai suka zo don su zartar da shirinsu na kashe Manzon Allah (SAW), sai suka tsayar da wasu mazaje a ƙofan gidansa, ta yadda idan ya fito ta wajensu za su kashe shi.

Sai Annabi (SAW) ya fito a lokacin da ake bacci cikin dare, sai ya keta tsakaninsu ta gaban gidansa, alhali a wannan lokacin Allah Ya makantar da idanuwansu, sai ya ɗibi ƙasa a tafin hannu, sai ya watsa a kawunansu,[2] yana mai karanta faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ((Muka kuma sanya wani shamaki a gabansu da kuma shamaki a bayansu, sai Maka lulluɓe musu idanuwa, don haka ba sa gani)).[3]

Sai ya isa gidan Abubakar (RA), sai suka fita tare, kuma sun ɗauki hayan Abdullahi ɗan Uraiƙid, saboda ya kasance masanin hanya ne

---

[1]. Albidaya wan-nihaya (4/444).
[2]. Albidaya wan-nihaya (4/441).
[3]. (Yasin: 9).

sosai, kuma ƙwararre, sai suka amintar da shi a kan haka, tare da cewa shi ya kasance yana kan addinin mutanensa, sai suka bashi abababen hawansu guda biyu, kuma suka yi alƙawarin haɗuwa da shi a kogon Saur bayan kwana uku.[1]

Sai suka kama hanya zuwa kogon Saur da yake saman wani dutse a kudancin Makka, wanda ke da nisan tafiyar kilomita huɗu daga Masallaci mai Alfarma, sai suka ɓuya a cikinsa.

Sai hankalin Ƙuraisahawa ya tashi lokacin da suka tabbatar cewa Manzon Allah (SAW) ya ci nasarar kuɓuce musu, sai suka ɗauki niyya bin sa, da kuma alƙawarin raƙuma ɗari ga wannan ya samo su, sai mahaya suka tsananta bincike a kansu, masana gane alamomin taku kuma suka shagaltu da bin bayansu.

Sai suka bincika su a kwararruka da tudu da duwatsu, har ƙafafunsu suka iso ƙofar wannan kogo, sai Allah Ya makantar da su daga ganinsu, sai Abubakar (RA) ya ce wa Manzon Allah (SAW): Da ɗayansu fa zai sunkuyar da kansa da tabbas zai gan mu! Sai Manzon Allah (SAW) ya mayar masa da amsa da shahararren maganar nan tashi: (Ya Abubakar me kake tsammani game da mutane biyu da Allah ne na ukunsu).[2] Sai kafiran Makka suka koma a ƙasƙance a wulaƙance saboda fitar Manzon Allah (SAW) daga tsakaninsu, ba tare da sun ci nasarar cimma shirinsu a kansa ba!

Abdullahi ɗan Abubakar ya kasance yana jin abin da ake faɗi a Makka sai ya riƙa kawo musu labari, ita kuma Asma'u 'yar Abubakar tana kawo musu abinci, Amir ɗan Fuhaira – yaron gidan

[1]. Bukhari ne ya rawaito (2263).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (3653), da Muslim (2381).

Abubakar – shi kuma yana kiwon awaki domin ya gusar da guraben takunsu.[1]

Bayan sun yi kwanan uku, sai Ibnu Uraiƙiƈ ya zo musu da taguwaninsu, sai suka hau kansu, sai Abubakar ya goya Amir ɗan Fuhaira a bayansa, Ibnu Uraiƙiƈ kuma sai shiga gabansu a kan taguwarsa, Abubakar (RA) ya kasance yana yawaita waiwaye saboda tsorace wa Manzon Allah (SAW), amma shi Annabi (SAW) ba ya waiwayowa.

Yayin da suka bi ta wajen unguwar ƙabilar Banu Mudlij, sai Suraƙatu ɗan Malik shugaban Mudlij ya gan su, sai ya hau dokinsa ya kama hanyar neman su, har sai da iso kusa da su, kuma ya ji karatun Manzon Allah (SAW), sai Abubakar ya ce: Ya Manzon Allah, ga Suraƙatu ɗan Malik ya riske mu! Sai Annabi (SAW) ya masa mummunan addu'a, sai ƙafafun dokinsa suka nitse a ƙasa, sai ya ce: Lallai a sanadiyar addu'arku ne wannan abin ya same ni, ku yi mun addu'a kuɓuta, ni kuma na yi muku alƙawari na kautar da mutane daga gare ku, sai Manzon Allah (SAW) ya yi masa addu'a, sai ya kuɓuta, sai ya roƙi Manzon Allah (SAW) da ya rubuta masa takarda da za ta lamunce masa amintuwa daga Annabi da Muslmai, sai Abubakar ya rubuta masa a takarda ta fata, sai ya koma yana ce wa mutane: Haƙiƙa an isar muku abin da ke wannan waje.[2]

Sai Manzon Allah ya bi ta haimar Ummu Ma'abad a cikin wannan tafiya tashi, sai ya yi baccin ƙailula a wajenta, sai ta ga alamomin annabtakarsa a kan tinkiyarta, da tatsan nono mai yawa da ta yi a shekara mai fari, abin da ya fi ƙarfin hankali.[3]

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito (5807).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (3906).
[3]. Albidaya wan-nihaya (4/476).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

UMMU HABIBA (RA)

❖ Sunanta da haifuwarta:

An san ta da Ummu Habiba, asalin sunanta shi ne: Ramlatu ‘yar Abu Sufyan ɗan Sakhr ɗan Harb ɗan Umayya.

An haife ta kafin hijira da shekara talatin, kuma tana daga cikin ‘ya’yan baffan Annabi (SAW), cikin matansa babu wacce tafi kusa da shi ta fuskar dangantaka kamar ta, kuma cikin matansa babu wanda ya kai ta yawan sadaka, ko wanda ya aure ta alhali tana waje mai nisa sama da nata.

❖ Tarihinta da falalarta:

Ta kasance tana daga cikin mata da suka musulunta tun farko, ta musulunta a farko-farkon Musulunci ita da mijinta Ubaidullahi ɗan Jahash, kuma sun yi hijira tare zuwa Habasha, sannan sai mijinta ya yi ridda ya shiga addinin kirastanci, ita kuma ta yi riƙo da addininsa, sai Allah Mai girma da ɗaukaka ya sauya mata shi da mafi alherin mutum.[1]

Sai Manzon Allah (SAW) ya aika wa Najashi sarkin Habasha yana mai neman aurenta, sai Najashi ya aika wa Ummu Habiba hadimarta ta sanar da ita, yayin da ta mata albishir da haka, sai ta mata kyautar awarwaro guda biyu da zoben azurfa da ke hannunta saboda farin ciki da abin da ta mata albishir da shi, kuma daman ta yi mafarki cewa wani mutum ya kira ta da “Uwar Muminai”, sai kuma

[1]. Siyaru a’alamin-nubala (2/219).

mafarkin nata ya tabbata, sai ta zama ɗaya daga cikin uwayen muminai.[1]

Kuma Najashi da kansa ne ya ɗaura auren Ummu Habiba da Manzon Allah (SAW) a cikin wasu jama'a ta musulmai, daga cikinsu akwai Ja'afar ɗan Abu Ɗalib (RA), sai Najashi ya ba da sadakinta a maimakon Annabi (SAW) har Dinari ɗari hudu,[2] sannan sai ta zo Madina bayan buɗe Khaibar don ta rayu da Manzon Allah (SAW).

Babanta Abu Sufyanu ya zo wajenta don ya haɗu da Manzon Allah (SAW) ya kuma nemi ya ƙara tsawon lokacin tsagaita wuta, yayin da ya so ya zauna a kan shimfiɗar Annabi (SAW) sai ta hana shi ta ma naɗe shimfiɗar, sai ya ce: Ya ke 'yata, ƙyamar na zauna a kan wannan shimfiɗar kike ko ko shimfiɗar ne bai dace da ni ba? Sai ta ce: a a, bari dai, wannan shimfiɗar Annabi (SAW) ce, kai kuma mutum ne mushiriki.[3]

Ta rawaito hadisai daga Manzon Allah (SAW), kuma mutane dayawa sun rawaito daga gare ta, daga cikinsu akwai: Mu'awiya, da Anbasa, da Anas ɗan Malik, da Zainabu 'yar Abu Salama.

Ummu Habiba (RA) ta tattara ta ba da lokacinta gaba ɗaya ga ibada bayan rasuwar Manzon Allah (SAW) har sai da mutuwa ta riske ta. A'isha (RA) ta ce: Ummu Habiba ta kira ni a lokacin rasuwarta, sai ta ce: Haƙiƙa an samu irin abin da ake samu tsakanin kishiyoyi na saɓani a tsakaninmu, ina fatan Allah Ya gafarta mana ni da ke abin da ya faru, sai na ce: Allah Ya gafarta miki hakan gaba ɗayansa, ya kuma yafe miki, kuma ya miki afuwa. Sai ta ce: Kin faranta mun rai,

[1]. Siyaru a'alamin-nubala (1/442).
[2]. Siyaru a'alamin-nubala (1/442).
[3]. Siyaru a'alamin-nubala (2/223).

ke ma Allah Ya faranta miki. Sai ta aika wa Ummu Salama, sai ta faɗa mata irin abin da ta faɗa wa A'isha.[1]

❖ Rasuwarta:

Ta rasu ne a zamanin Mu'awiya (RA), a shekara ta arba'in da huɗu bayan hijra, sai aka binne ta a Madina.

[1]. Hakim ne ya rawaito (4/24).

Auna fahimtarka a darusan mako na 21			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Me ake nufi da gari amintacce?		B
	a. Dutsen Ɗuri Sinana.	b. Makka.	c. Ƙudus.
Darasin Hadisi	Tambaya: Ana buɗe ƙofofin aljanna a ranar:		B
	a. Alhamis da Juma'a.	b. Litinin da Alhamis.	c. Asabar da Lahadi.
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin abubuwan da imani da ranar lahira ya ƙunsa akwai:		A
	a. Imani da tambayar mala'iku biyu.	b. Imani da siffofin mala'iku.	c. Imani da mu'ujizozin Annabawa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin abubuwan da ba a son yin su a salla akwai:		C
	a. Barin karanta Fatiha.	b. Addu'a kafin sallama.	c. Zaman shedan a salla.
Darasin Sira	Tambaya: Wanda ya bi Annabi (SAW) da abokinsa a hanyarsu ta hijira shi ne:		B
	a. Ikrima ɗan Abu Jahal.	b. Suraƙatu ɗan Malik.	c. Abu Sufyanu ɗan Harb.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Asalin sanan Ummu Habiba matan Annabi (SAW) shi ne:		C
	a. Tumadir 'yar Amru.	b. Faɗimatu 'yar Asad.	c. Ramlatu 'yar Abu Sufyan.

MAKO NA ASHIRIN DA BIYU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-ALAƘ (1)

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
ٱقۡرَأۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلَّذِي خَلَقَ ١ خَلَقَ ٱلۡإِنسَٰنَ مِنۡ عَلَقٍ ٢ ٱقۡرَأۡ وَرَبُّكَ ٱلۡأَكۡرَمُ ٣
ٱلَّذِي عَلَّمَ بِٱلۡقَلَمِ ٤ عَلَّمَ ٱلۡإِنسَٰنَ مَا لَمۡ يَعۡلَمۡ ٥ كَلَّآ إِنَّ ٱلۡإِنسَٰنَ لَيَطۡغَىٰٓ ٦ أَن رَّءَاهُ
ٱسۡتَغۡنَىٰٓ ٧ إِنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلرُّجۡعَىٰٓ ٨﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai rahama, Mai jin ƙai

1. Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, wanda Ya yi hakitta.
2. Ya halicci mutum daga gudan jini.
3. Ka yi karatu alhali Ubangijinka Shi ne mafi karamci.
4. Wanda Ya koyar ta hanyar alƙalami.
5. Ya koyar da mutum abin da bai sani ba.
6. Tabbas! Lallai mutum haƙiƙa yana yin ɗagawa.
7. Don ya ga kansa yana cikin wadata.
8. Lallai kuma zuwa ga Ubangijinka ne makomar take.

❖ Abin da surar ta ƙunsa:

Halin mutum tsakanin shiryiwa da wahayi, da ɓatarsa ta hanyar girman kai da jahilci.

❖ Bakin kalmomi:

علق	Alaƙ	Dunƙulallen jini mai kauri.
كلاّ	Kalla	Tabbas.
ليطغى	La yaɗga	Tabbas! Yana wuce iyaka wurin girman kai da saɓo.

أن رآه استغنى	An ra’ahus-tagna	Wato a lokacin da ya ga cewa ya wadatu da dukiyarsa da ‘ya’yansa ko girmansa.

❖ Ma’anar ayoyin a dunƙule:

Suratul-Alaƙi tana daga cikin surori da aka saukar a Makka, kuma ana kiran ta da suratu: “Iƙra”, kuma ita ce farkon abin da ya sauka a Alƙur’ani, Allah Maɗaukaki Ya buɗe ta da ambaton ni’imar da Ya yi wa Manzonsa Mai daraja (SAW) na wahayi, ya kuma rufe ta da umurtar sa da sujjada da neman kusantar Shi Mai girma da ɗaukaka.

Sai aka fara ta da umarnin Allah Maɗaukaki ga Manzonsa (SAW) da ya yi karatu, ya kuma fara karatun nasa da ambaton sunan Ubangijinsa, sannan sai Allah Maɗaukaki Ya tunatar da shi da wata ni’ima daga cikin ni’imominsa masu girma, wacce ita ce cewa lallai Shi Ya sanar da mutum ta hanyar rubutu da alƙalami, sai Ya ba shi abin da bai sani ba na ilmomi da sani.

Sannan Allah Maɗaukaki Ya ambaci wata haƙiƙa da kowa yake gani, da wata siffa tabbatacci a halittar mutum, ita ce cewa shi saboda jahilicinsa da zaluncinsa idan ya ga cewa ya wadata da dukiyarsa da ‘ya’yansa da matsayinsa, kuma ba shi da buƙatuwa cikin wani abu zuwa ga waninsa; sai ya yi ɗagawa, da jiji da kai, da zalunci, ya kuma hana haƙƙoƙi, ya rena masu rauni, kuma ya yi izgili ga waninsa, ya mance cewa lallai ga Ubangijinsa makomarsa take!

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Shar’ancin fara karatu da ambaton sunan Allah Maɗaukaki; don haka ne ma aka buɗe surorin Alƙur’ani da basmala, amma ban da Suratut-Tauba.
2. Albarkar da ke cikin ambaton Allah Maɗaukaki a magana da ayyuka da cin abinci da shan abin sha da dukkan komi.

3. Baiwar Allah ga mutum, ta yadda Ya samar da shi daga gudan jini, sannan Ya halicce shi mataki bayan mataki, ya kuma ba da kulawa wajen jujjuya shi, kuma Ya rene shi da ni’imomi da ba za su ƙirgu ba.
4. Lallai ni’imar rubutu da alƙalami tana daga cikin mafiya girman ni’imomin Allah a kan mutane; saboda abin da take ɗauke da shi na kiyaye ilimi da sani, da tsayuwar maslahar addini da duniya.
5. Hatsarin wadata idan ta sabbaba girman kai da nisantar gaskiya.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WAJIBCIN TUBA ZUWA GA ALLAH

An karɓo daga Agarru ɗan Yasar Almuzani (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Ya ku mutane, ku tuba zuwa ga Allah, kuma ku nemi gafararsa, domin ni lallai ina tuba a yini sau ɗari**).[1]

❖ Sharhi:

Annabi (SAW) yana fuskantar da kira gamammiya mai ɗauke da umurni da istigfari da tuba zuwa ga Allah, yana kuma ba da labari - saboda kwaɗaitar da al'ummarsa - cewa lallai yana tuba kuma yana istigfari sau ɗari a yini, tare da cewa shi Annabi (SAW) an gafarta masa abin da ya gabatar na zunubai da abin da zai zo a gaba; hakan ya kasance ne saboda cikar bautartakarsa ga Ubangijinsa, da dawwamar ratayuwarsa da ambatonsa, da sanin girman haƙƙinsa a kansa, da gazawar bawa a kan gode wa ni'imar da aka masa ko ya ya kuwa ya yi aiki, idan wannan ya kasance shi ne halin Annabi (SAW), to mu muka fi cancanta da komawa zuwa ga Allah, da tuba, da istigfari, da dawowa, duk wanda ya yawaita tuba da istigfari; za a kankare masa zunubansa, kuma zuciyarsa za ta yi haske, kuma gafala za ta bar shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Wajibcin tuba zuwa ga Allah Maɗaukaki; domin lallai umurni yana hukunta wajibci.
2. Lallai waɗanda ake fuskantar wa wannan umarnin su ne mutane gaba ɗaya ba tare da togaciya ba.

[1]. Muslim ne ya rawaito (2702).

3. Lallai lura da yanayin ibadar Annabi (SAW) da ƙasƙantar da ƙansa ga Ubangijinsa, yana sa a yi koyi da shi, da kuma ƙara ƙaimi wurin aikata ayyukan nagartattu.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA ƘADDARA

Nassoshi dayawa ne daga littafin Allah Maɗaukaki da sunnar Manzonsa (SAW) waɗanda suke nuni a kan cewa lallai al'amura suna gudana ne da ƙaddarar Allah Maɗaukaki, gwargwadon yadda hikimarsa ta zartar, da kuma cewa lallai Allah Maɗaukaki Ya san abubuwa kuma Ya ƙaddara su tun fil'azal, da kuma cewa suna aukuwa ne daidai da abin da Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ƙaddara; daga cikinsu akwai:

- Faɗin Allah Maɗaukaki: ((Lallai Mu, kowane abu Mun halitta shi da ƙaddara)).[1]
- Da faɗinsa: ((Al'amarin Allah kuwa ya kasance mai tabbata ne ba makawa)).[2]
- kuma Annabi (SAW) ya ce a hadisin Jibril: (Kuma ka yi imani da ƙaddara, mai kyansa da mara kyansa).[3]

❋ **Kuma imani da ƙaddara yana ƙunshe da ababe guda huɗu:**

Na farko: Ilimin Allah Maɗaukaki, sai mutun ya yi imani da cewa lallai Allah Maɗaukaki Masani ne ga dukkan komai, a dunƙule kuma a rarrabe, wanda ya wuce tun fil'azal, da wanda zai zo har abada.

Na biyu: Rubutu, sai ka yi imani da cewa lallai Allah Maɗaukaki Ya rubuta dukkan abubuwan da Ya ƙaddara su a Lauhul-Mahafuz.

Game da waɗannan lamura guda biyu ne Allah Ta'ala Yake cewa: ((Shin ba ka sani ba cewa lallai Allah Yana sane da abin da yake

---

[1]. (Alƙamar: 49).
[2]. (Al'Ahzab: 38).
[3]. Muslim ne ya rawaito (8).

cikin sama da wanda yake ƙasa? Lallai wannan yana cikin littafi (wato Lauhul-Mahafuzu). Lallai wannan mai sauƙi ne a wurin Allah)).[1] Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Allah Ya rubuta abubuwan da Ya ƙaddara wa halittu kafin Ya halicci sammai da ƙasa da shekara dubu hamsin).[2]

Na uku: Ganin dama, wato imani da ganin damar Allah zartacciya, da kuma cewa dukkan abin da zai kasance yana kasancewa ne da nufin Allah; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma Ubangijinka Yana halittar abin da Ya ga dama Yana kuma zaɓar (abin da Ya ga dama)).[3]

Na huɗu: Halitta, wato imani da cewa lallai Allah ne Ya halicci dukkan halittu kuma Ya samar da su daga babu; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Allah ne Mahalicci dukkan komai)),[4] Ya kuma cewa: ((Kuma Ya halicci kowane abu, sannan Ya ƙaddara shi ƙaddarawa)).[5]

❖ **Kuma imani da ƙaddara yana da amfani mai girma, wanda ya ƙunshi abubwa kamar haka:**

Na farko: Dogaro da Allah wurin aikata sababi, ba dogaro a kan sababi ba; saboda komai da ƙaddarar Allah Maɗaukaki yake samuwa.

Na biyu: Kada mutum ya ruɗu da kansa lokacin da ya samu biyan buƙatarsa; saboda samuwarsa ga wannan abin da sauƙaƙewar Allah ne.

---

1. (Alhaj: 70).
2. Muslim ne ya rawaito (6690).
3. (Alƙasas: 68).
4. (Azzumar: 62).
5. (Alfurƙan: 2).

Na uku: Samun natsuwar zuciya da kwanciyar hankali; saboda haka, mumini ba zai yi baƙin ciki ba idan abin da yake so ya kuɓuce masa, ko kuma abin da yake ƙi ya same shi; saboda hakan da ƙaddarar Allah ne, game da haka ne Allah Maɗaukakin Sarki Yake cewa: ((Babu wani abu da ya samu na musiba a bayan ƙasa, ko kuma ga kawunanku face yana cikin Littafin (Lauhul-Mahafuz) tun kafin Mu halicce ta (wato halittar). Lallai wannan a wurin Allah mai sauƙi ne () Don kada ku yi baƙin ciki a kan abin da ya kuɓuce muku, kada kuma ku yi fariya da abin da Ya ba ku, Allah kuwa ba Ya son duk wani mai taƙama, mai fariya)).[1]

Kuma Annabi (SAW) yana cewa: (Abin mamaki game da lamarin mumini! Lallai al'amarinsa gaba ɗayansa alheri ne, babu kuma wannan yake da hakan face mumini; Idan abin farin ciki ya same shi sai ya yi godiya, sai abin ya zama masa alheri, kuma idan abin da zai cutar da shi ya same shi sai ya yi haƙuri, sai wannan ma ya zama alheri gare shi).[2]

[1]. (Alhadid: 22-23).
[2]. Muslim ne ya rawaito (7425).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

KURAKURAI DA AKE YAWAITA YIN SU A SALLA

Akwai wani adadi na saɓawa da kurakurai da ake yi a salla, waɗanda suka yaɗu a tsakanin mutane, wanda ya wajaba a faɗaku da su kuma a nisance su, daga cikinsu akwai:

1. Ɗaga kai sama, yana daga cikin abubuwan da aka haramta yin su a salla; saboda faɗinsa (SAW): (Lallai mutanen da suke ɗaga kawunansa sama a cikin salla su daina, ko kuma lallai za a ɗauke musu ganinsu).[1]

2. Gabatar da kabbarori ko jinkirta su daga wajajensu, wajajen nasu kuma su ne motsi da ke tsakanin sunkuyawa da ɗagowa, abin da aka shar'anta shi ne kabbara ta zama tsakanin rukuni biyu, a ruku'i, kabbara tana kasancewa ne a lokacin sunkuyawa zuwa ruku'in, saboda haka, kada a fara kafi haka, kuma kada a jinkirta shi zuwa bayansa.

3. Wasa da motsi a salla, da shagaltuwa da taɓa hanci da gemu da tufafi, da yawan gyaran murya da makamantansa na fitar da sauti ba tare da buƙata ba, wannan gaba ɗayansa na daga cikin wasa wanda idan ya yawaita sai ya lalata salla; haƙiƙa ya zo daga Huzaifa (RA) cewa lallai shi ya ga wani mutum ba ya cika ruku'i da sujjada, sai ya ce da shi: "Ba ka yi sallah ba, kuma da za ka mutu a haka, da ka mutu a kan wani addini da ba da shi aka turo Annabi Muhammadu (SAW) ba".[2]

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (429).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (758).

4. Buɗe wani bangare na cinya, ta hanyar sanya gajeren wando da makamancinsa, wannan yana lalata salla; Manzon Allah (SAW) ya ce: Ka rufe cinyarka, domin lallai cinya al'aura ce).[1]

5. Lallai waɗansu marasa lafiya suna jinkirta salla daga lokacinta; saboda kasancewarsa yana kan gado, kuma ba zai iya sauka daga kanshi ba, ko kuma ba zai iya gusar da najasa da yake ɗauke da ita ba, ko kuma babu ƙasa da zai yi taimama tare da shi, ko kuma ba shi da wanda zai taimake shi, sai ya ce: Zai yi sallar daga baya idan uzurina ya kau. Wannan kuma babban kuskure ne, da kuma tozarta salla, abin da yake wajibi shi ne ya yi salla a yanayin da yake a kan lokaci, kuma sallarsa za ta isar masa, ko da kuwa ya yi salla ba tare da taimama ba, ko da tufafi mai najasa, ko kuma ya fuskanci wajen da ba alƙibla ba, Allah Mai girma da ɗaukaka Ya ce: ((Ku ji tsoron Allah gwargwadon ikonku)).[2]

6. Rigayar liman, domin lallai bin liman da koyi da shi yana daga cikin wajibai, kuma yana tabbata ne ta hanyar jiran liman har sai kabbararsa ta yanke, sai ya bi shi bayan haka; Manzon Allah (SAW): (Lallai an sanya liman ne don a kwaikwaye shi, don haka, idan ya yi kabbara, kuma ku yi kabbara, kada ku yi kabbara har sai ya yi, kuma idan ya yi ruku'i kuma ku yi ruku'i, kada kuma ku yi ruku'i har sai ya yi).[3] Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Yanzu ɗayanku ba ya tsoron idan ya ɗaga kansa kafin liman, Allah Ya mayar da kansa ya koma kan jaki, ko kuma Allah Ya mayar da halittarsa ta koma irin ta jaki).[4]

---

[1]. Tirmizi ne ya rawaito (2796), da Ahmad (2493).
[2]. (Attagabun: 16).
[3]. Abu Dawuda ne ya rawaito (603).
[4]. Bukhari ne ya rawaito (691), da Muslim (427).

Kuma mamu yana da yanayi huɗu tare da liman:

1**. Bin sa**: Shi ne ayyukan mamu su zama bayan na liman, kuma wannan shi ne abin nema, kuma da shi ne koyi da aka shar'anta yake tabbata.

2. **Daidaitawa**: Ita ce motsin mamu ya yi daidai da na liman, wannan aikin makaruhi ne.

3. **Saɓawa**: Ita ce mamu ya yi jinkiri bayan liman har sai liman ya fara wani rukuni na daban, wannan bai halatta ba; saboda ya bar koyi.

4. **Rigayar liman:** Ita ce mamu ya riga liman kabbara, ko ruku'i, ko sujjada, ko sallama, ko wanin haka, wannan aikin ba halatta ba, kuma duk wanda ya aikata shi a bisa jahilci ko mantuwa, to dole ya dawo ya sake yin shi bayan liman.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ƊABI'AR RAYUWA A MADINA

Madina ta kasance ana kiran ta da "Yasriba" kafin zuwan Musulunci, sai Allah da Manzonsa suka saka mata suna "Madina", kuma haƙiƙa ƙungiyoyi na mutane daban-daban sun zauna a cikinta a lokaci ɗaya:

Ƙungiya ta farko: Musulmi, su kama kashi biyu ne: Muhajirai da Ansarawa.

Muhajirai: Su ne waɗanda suka zo daga Makka, suka gudo da addininsu, kuma adadinsu yana da yawa sosai, domin suna tahowa kowane rana, hijira zuwa Madina ta kasance ba mai yankewa ba, ga duk wanda ya yi imani da Allah da Manzonsa, kuma a farkon lamari ba su da wani aiki da suke yi, ba su kuma da dukiya da suka mallakar.

Amma Ansarawa: Su ne mutanen Madina, daga ƙabilun Ausu da Khazraj, waɗanda suka wanzu a cikin ƙasarsu da gidajensu da dukiyoyinsu, kuma kafin Musulunci akwai gaba da ƙiyayya a tsakaninsu, sai Musulunci ya zo ya kore wannan ƙiyayyar, sai suka zama 'yan'uwan juna da ni'imar Allah.

Ƙungiya ta biyu: Mushirikai da ba su yi imani ba, kuma suna cikin ƙabilun Madina, su ma sun kasu kashi biyu: Daga cikinsu akwai waɗanda suke kokonton barin addinin iyaye, amma ba su ɗauki wata gaba ga Musulmai a zukatansu ba, waɗannan kam ba su jima a kan haka ba suka musulunta suka kuma tsantsanta addininsu ga Allah, akwai kuma wani ɓangare na biyu cikin mutanen mushirikan Madina waɗanda suke ɓoye ƙiyayya ga musulmai, sai dai kuma suna da buƙatar su bayyana so da tsaftar zuciya ga musulmi, waɗannan

su ne munafukai, na gaba-gabansu shi ne Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul, domin lallai ƙanilun Ausu da Khazraj sun haɗe gabanin zuwan Annabi (SAW) a kan za su shugabantar da shi ya zama sarki a gare su, sai kuma suka karkata daga gare shi suka shiga musulunci, sai Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul ya bayyana cewa ya shiga musulunci bayan yaƙin Badar, amma kuma ba ya barin wata dama da zai samu face sai ya yi amfani da ita wajen shirya makirci ga musulmai.

Ƙungiya ta uku: Yahudawa da ƙabilunsu guda uku (Banu Ƙainuƙa', da Banun-Nadir, da Banu Ƙuraiza), kuma Banu Ƙainuƙa' da Banun-Nadir sun kasance abokan ƙawance ne ga ƙabilar Khazraj, unguwarsu kuma na cikin Madina, su kuma Banu Ƙuraiza abokan ƙwancen ƙabilar Ausu ne, su kuma unguwarsu na gefen Madina, kuma waɗannan yahudawa sun kasance ƙwararru ne a fannoni neman kuɗi, masu kasuwanci ne na dabino da giya da hatsi da tufafi, kuma sun kasance maciya riba, sun cin dukiyoyin larabawa, haka kuma, sun kasance ma'abota makirci da dasisa da ha'inci, suna tada yaƙe-yaƙe Tsakanin ƙabilun Ausu da Khazraj, yayin da Musulunci ya zo sai malaminsu Abdullahi ɗan Salam (RA) ya musulunta, gamagarinsu kuma suka kafurta, suka tunkari Manzon Allah (SAW) da idanun ƙiyayya da gaba da warware alƙawurra.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABU AYYUB AL'ANSARI (RA)

❖ Sunansa da haifuwarsa:

Shi ne sahabin nan mai daraja, Khalid ɗan Zaidu, ɗan Kulaib, ɗan Sa'alaba Annajjari Al'ansari Alkhazraji.

❖ Rayuwarsa da falalarsa:

Abu Ayyub (RA) ya kasance daga cikin marubuta wahayi, da marawaita hadisi, kuma ya kasance daga cikin mafiya karamci da kyauta cikin sahabbai duk da talaucinshi da ƙarancin abin hannunshi, kuma yana daga cikin mafiya himma da ƙarfi cikinsu.

Shi ne ma'abocin mashahurin gidan nan da Annabi (SAW) ya sauka a cikinsa yammacin hijirarsa zuwa Madina, saboda taguwarsa mai suna "Alƙaswa'u" ta gurfana a gaban gidan Abu Ayyub, sai ya sauƙa a gidan, sai Abu Ayyub da matarsa suka karɓi baƙuncin Annabi (SAW) suka kuma yi masa hidima sosai.[1]

Sai Abu Ayyub da iyalansa sun kasance a ɓangaren gidan na sama, Manzon Allah (SAW) kuma a ɓangarensa na ƙasa, sai Abu Ayyub ya farka a wani dare, sai ya ce: Yanzu ma riƙa tafiya a saman kan Annabi (SAW)! Sai suka karkace suka kwana a gefe, yayin da gari ya waye sai ya ambaci haka ga Annabi (SAW), sai Annabi (SAW) ya ce: (Ɓangaren ƙasa ya fi mun sauƙi), sai Abu Ayyub ya ce: Ba zan hau wata runfa da kake ƙarƙashinta ba, sai Annabi (SAW) ya koma ɓangare sama, shi kuma Abu Ayyub ya dawo ƙasa.

[1]. Siyaru a'alamin-nubala (2/406).

Kuma Abu Ayyub ya kasance yana yi wa Annabi (SAW) abinci, idan aka zo masa da shi sai ya yi tambaya a kan wurin da yatsun Annabi (SAW) ya taɓa, sai ya bibiyi wajen yatsun nasa.[1]

Abu Ayyub (RA) ya halarci mubaya'ar Aƙaba, da yaƙin Badar, da Uhud, da Khandaƙ, da sauran yaƙoƙi tare da Manzon Allah (SAW), yana mai ba da kansa da dukiyarsa ga Allah Ubangijin talikai.

Bayan wafatin Manzon Allah (SAW), bai yi fashin Halartar wani yaƙi da musulmai suka yi ba, duk yadda wajen yaƙin ya kai wurin nisa da wahalar tafiya.

❖ Rasuwarsa:

Abu Ayyub (RA) ya halarci buɗe Ƙusdandiniyya a zamani halifanci Mu'awiya (RA), a lokacin ya zama dattijo da ya kai shekara tamanin a duniya, ya kasance yana karanta faɗin Allah Maɗaukaki ((Ku fita yaƙi kuna da kuzari ko ba ku da shi)),[2] yana kuma cewa: "Ba na tsammanin kaina face mai kuzari ko mara kuzari",[3] sai ya yi yaƙi har ya yi shahada a wannan yaƙin a shekara ta hamsin bayan hijira, sai aka binne shi a can.

[1]. Muslim ne ya rawaito (2053).
[2]. (Attauba: 41).
[3]. Ibnu Sa'ad ne ya rawaito (3/485).

Auna fahimtarka a darusan mako na 22			**Amsa na ƙwarai**
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar "Al'alaƙ"?		A
	a. Gudan jini mai kauri.	b. Gudan jini.	c. Ruwa ƙasƙantacce.
Darasin Hadisi	Tambaya: Annabi (SAW) ya kasance yana tuba a yini sau:		C
	a. 10.	b. 50.	c. 100.
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin abubuwan da imani da ƙaddara ya ƙunsa akwai:		C
	a. Imani da sunayen waɗanda muka sani daga mala'iku.	b. Imani da azabar ƙabari da ni'marsa.	c. Imani da cewa lallai dukkan abin da yake faruwa da yana faruwa ne da nufin Allah.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Mene ne hukuncin mai salla ya ɗaga kansa sama:		B
	a. Halal ne.	b. Haram ne.	c. Makaruhi ne.
Darasin Sira	Tambaya: Ana kiran Madina da suna …… kafin zuwan Musulunci.		C
	a. Ɗaba.	b. Bakka.	c. Yasrib.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Abu Ayyub Al'ansari (RA) ya shahara da cewa shi ne:		B
	a. Mai kiran sallar Manzon (SAW) Allah a Ƙuba.	b. Wanda ya karɓi baƙuncin Annabi (SAW) a gidansa.	c. Shugaban ƙabilar Khazraj.

MAKO NA ASHIRIN DA UKU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-ALAƘ (2)

﴿أَرَءَيْتَ ٱلَّذِى يَنْهَىٰ ۝٩ عَبْدًا إِذَا صَلَّىٰٓ ۝١٠ أَرَءَيْتَ إِن كَانَ عَلَى ٱلْهُدَىٰٓ ۝١١ أَوْ أَمَرَ بِٱلتَّقْوَىٰٓ ۝١٢ أَرَءَيْتَ إِن كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰٓ ۝١٣ أَلَمْ يَعْلَم بِأَنَّ ٱللَّهَ يَرَىٰ ۝١٤ كَلَّا لَئِن لَّمْ يَنتَهِ لَنَسْفَعًۢا بِٱلنَّاصِيَةِ ۝١٥ نَاصِيَةٍ كَٰذِبَةٍ خَاطِئَةٍ ۝١٦ فَلْيَدْعُ نَادِيَهُۥ ۝١٧ سَنَدْعُ ٱلزَّبَانِيَةَ ۝١٨ كَلَّا لَا تُطِعْهُ وَٱسْجُدْ وَٱقْتَرِب ۩ ۝١٩﴾

❖ Fassara:

9. Ka ba ni labarin wanda yake hana.
10. Bawa yayin da ya yi salla.
11. Ka ba ni labari idan (shi bawan) ya kasance a kan shiriya.
12. Ko kuma ya yi umarni da taƙawa.
13. Ka ba ni labari idan (shi mai hanawar) ya ƙaryata ya kuma ba da baya.
14. Shin bai sani ba cewa Allah Yana ganin (sa).
15. A’aha! Tabbas idan bai hanu ba to za Mu ja shi ta makwarkwaɗar kai.
16. Makwarkwaɗar kai mai ƙaryatawa, mai aikata laifi.
17. To ya kirawo majalisar tasa.
18. Mu kuma lallai za Mu kirawo (mala’iku) zabaniyawa.
19. Faufau! Kada ka bi shi, ka kuma yi salla, ka kusanta (ga Allah).

❖ Saƙon da ayoyin suka ƙunsa:

Halin mutum tsakanin shiryuwa da wahayi, da ɓatarsa ta dalilan girman kai da jahilci.

❖ Sababin saukar ayoyin:

Lallai Abu Jahal ya zo wurin Annabi (SAW) alhali yana salla a Masallaci mai alfarma, sai ya yi yunƙurin hana shi yin sallar, ya ce: Tabbas idan na gan shi yana salla, to tabbas sai na taka wuyansa! Sannan ya juya a tsorace, sai aka ce da shi: Me ya faru? Ya ce: Tabbas haƙiƙa wani babban rami na wuta ya katange tsakanina da shi! Sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Da ya kusanto ni, da tabbas sai mala'ika ya yayyaga shi gaɓa-gaɓa).[1]

أرأيت الذي ينهى عبدا إذا صلى	Ara'aital-lazi yanha, abdan iza salla	Shi ne Abu Jahal (Amru ɗan Hisham), yana yi wa Annabi (SAW) mafi munin ƙiyayya.
لئن لم ينته	La'in lam yantah	Ma'ana: Idan bai daina cutar da Manzonmu Muhammadu (SAW) da hana shi yin salla a bayan Maƙamu Ibrahim.
لنسفعن بالناصية	Lanasfa'an bin-nasiya	Tabbas za Mu ja makwarkwaɗanshi da gaban kanshi, Mu kuma jefa shi a wutar Jahannama.
فليدع ناديه	Falyad'u nadiyah	Ya kirawo majalisarsa da abokan zamansa.
سندع الزبانية	Sanad'uz-zabaniyah	Masu kula da Jahannama.

❖ Ma'anar ayoyin a dunƙule:

A cikin waɗannan ayoyi akwai tsawatarwa mai tsanani ga wannan mutumin nan da ya cutar da Annabin Allah (SAW), kuma ya yi gaba da shi, kuma ya yi nufin hana shi yin salla, da bayanin cewa lallai aikinsa da mummunar ɗabi'arsa suna sa masu hankali su nisanci irinsa; Shi daman mai tafiya a kan shiriya kuma mai umarni da

[1]. Bukhari ne ya rawaito (4958), da Muslim (2797).

taƙawa ana gaba da shi kuma ana yaƙan shi, har ma a dake shi a ja kunnenshi?!

Sannan jan kunne da tsawatarwa suka zo a kan cewa idan bai hanu daga cutar da Manzon Allah (SAW) da far masa a cikin sallarsa ba; to tabbas za Mu ja makwarkwaɗarsa, kuma za Mu ja shi zuwa Jahannama a idon mutane.

Sannan aka rufe surar da nusar da Manzon Allah (SAW) a kan kada ya saurare shi, kuma lallai ya ci gaba da biyayya ga Ubangijinshi, da salla da neman kusanci gare Shi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Shar'ancin sujjadar tilawa a lokacin da aka karanta ayoyin sujjada, kuma daga cikinsu a wannan surar akwai faɗinsa Maɗaukaki: ((Ka yi salla kuma ka kusanta ga Ubangijinka)).

2. Lallai girman kai da jahilci dasassun abubuwa ne a ɗabi'ar mutum, idan har ba a tsaftace shi da imani da taƙawa ba.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR YAWAITA KARATUN ALƘUR'ANI

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Duk wanda ya karanta harafi ɗaya daga littafin Allah, to yana da lada, kuma duk lada ɗaya za a ninka ta sau goma, ba ina nufin faɗin: "Alif Lam Mim" shi ne harafi ba, sai dai: "Alifun" harafi ne, "Lamun" ma harafi ne, haka "Mimun" ma harafi ne**).[1]

❖ Sharhi:

Karanta Alƙur'ani mai girma na daga cikin ƙofofin samun ladaddaki masu yawa, wanda kowane musulmi ya kamata ya yi kwaɗayin samun su, ya kuma keɓance wani abu da zai na karantarwa a Alƙur'ani kuma ba tare da ya bari ba, kuma a wannan hadisin Manzon Allah (SAW) yana bayyana cewa duk wanda ya karanta littafin Allah, to yana da lada goma a kan kowane harafi guda ɗaya.

Kuma faɗinsa (SAW): (Ba ina nufin "Alif Lam Mim" shi ne harafi ɗaya ba), wato ba wai harufa ukun a dunƙule yake nufi ba, bari dai, abin da yake nufi shi ne: "Alifun" harafi ne, "Lamun" ma harafi ne, kuma "Mimun" ma harafi, sai a bawa wanda ya karanta hakan lada talatin, wannan kuma ni'ima ce mai girma da kuma lada mai gwaɓi.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Bayanin falalar karatun Alƙur'ani mai girma, da kwaɗaitarwa a kansa.

2. Lallai ladan kowane harafi daga Alƙur'ani shi ne lada goma.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito (2912).

3. Yalwar rahamar Allah da karamcinsa, ta yadda ya ninka ladaddakin ibadu saboda falala daga gare shi da karamci.

4. Kiyayewa daga ƙaurace wa Alƙur'ani mai girma.

❋ Ibnul-Ƙayyim Allah Ya yi masa rahama ya ambaci nau'ikan ƙaurace wa Alƙur'ani, waɗanda su ne kamar haka:

Na farko: Ƙaurace wa imani da shi.

Na biyu: Ƙaurace wa karanta shi da sauraron shi.

Na uku: Ƙaurace wa tadabburinshi da ƙoƙarin fahimtar shi da sanin abin da Allah Yake nufi da shi.

Na huɗu: Ƙaurace wa aiki da shi, da dakatawa a wajen abin da ya halalta da wanda ya haramta.

Na biyar: Ƙaurace wa alƙalantar da shi da koma wa gare shi a ginshiƙan addini da rassansa.

Na shida: Ƙaurace wa neman waraka da magani da shi a cututtukar zukata da na gangar jiki.

Dukkan waɗannan za su shiga ƙarƙshin faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ((Manzo kuma ya ce: "Ya Ubangijina, lallai mutanena sun riƙi wannan Alƙur'ani abin ƙaurace wa")).[1] [2]

[1]. (Alfurƙan: 30).
[2]. Alfawa'id na Ibnul-Ƙayyim (82).

TALATA: DARASI CIKIN AƙIDA

MAS'ALOLIN DA KE DA ALAƘA DA ƘADDARA

Mas'ala Ta Farko: Lallai Imani da ƙaddara ba ya kore tabbatar da ganin dama da zabi ga bawa, wannan kuwa da dalilin shari'ah da abin yau da kullum suka tabbatar.

- Amma dalilin shari'ah: Haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya tabbatar wa bawa ganin dama, Allah Ya ce: ((Saboda haka wanda ya ga dama ya riƙi kyakkawar makoma zuwa ga Ubangijinsa)) [1].
- Amma dalili na yau da kullum: Shi ne cewa lallai kowane mutum yana babbance tsakanin abin da ya ke faruwa bisa ganin damansa, kamar tafiya da cin aɗanci da saye da siyarwa, da kuma abin da ke faruwa ba bisa ganin damansa ba, kamar karkarwa da faɗuwa, sai ya danganta na farkon ga zaɓinsa ban da na biyun.

Mas'ala Ta Biyu: Lallai ganin daman bawa yana ɗan ganin damar Allah Maɗaukaki ne, da ikonsa, ba ya fita daga hakan, don kuwa duniya gaba ɗaya mallakar Allah Maɗaukaki ne, don haka kuwa ba wani abu da zai kasance cikin mulkinsa ba tare da ganin damansa ba; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Wanda ya ga dama daga cikinku ya bi hanya madaidaiciya () Kuma ku ba za ku iya ganin dama ba sai Allah Ubangijin talikai Ya ga dama)) [2].

Mas'ala Ta Uku: Ba ya halatta ga baligi mai hankali ya kafa hujja da ƙaddara akan aikinsa na sabo da zunubi; saboda dalilai kamar haka:

Na Farko: Wannan hujjar mushrikai ce; Allah Maɗaukaki Ya ce: "Waɗanda suke yin shirka za su ce: ((Da Allah Ya ga dama, da ba mu yi shirka ba, haka iyayenmu da ba su yi ba, kuma da ba mu

---

[1]. [An-Naba'i: 39].
[2]. [At-Takwir: 28-29].

haramta wani abu ba". Kamar haka ne waɗanda suka gabace su suka karyata, har suka ɗanɗani azabarmu))[1].

Na Biyu: Annabi (SAW) ya yi umurni da aiki, kuma ya yi hani ƙarara ga dogaro akan ƙaddara; Annabi (SAW) ya ce: (Babu wani daga cikinki face an rubuta mazauninsa a wuta ko Aljanna" Sai wani mutum daga cikin mutane ya ce: Ashe ba ma saki jiki ba. Annabi (SAW) Ya ce: "A'a, ku yi aiki, don kuwa ko ana yassare masa abin da aka halicce shi domin shi ne)[2].

Na Uku: Lallai muna ganin yadda mutum ke ƙoƙari da kwaɗayi akan al'amuran duniyarsa har sai ya cimma su, amma ba ma ganin shi yana barin hakan yana mai kafa hujja da ƙaddara; to don me zai kafa hujja da ƙaddara wurin tozartar da al'amuran addininsa?!

Na Huɗu: Mutum ba ya yarda da wannan hujjan idan da wani zai yi masa ta'addanci ya ƙwace dukiyarsa ko ya keta alfarmarsa, idan ya zama ba ya yarda da hakan cikin da ta'addanci wani gare shi, to ta yaya zai yarda da hakan a cikin ta'addancinsa ga haƙƙin Allah Maɗaukaki?!

❖ **Haƙiƙa ƙungiyoyi biyu sun ɓace a game da ƙaddara:**

Na Farkonsu: Ita ce Jabriyyah, waɗanda suka ce: Lallai shi bawa an tilasta shi ne akan aikinsa, kuma ba shi da nufi ko iko.

Na Biyun: Ita ce Ƙadariyyah, waɗanda suka maida bawa mai 'yanci ne a nufinsa da ganin damansa, kuma ganin damar Allah Maɗaukaki ba shi da wani tasiri a cikinsa.

---

1. [Al-An'am: 148].
2. Bukhari (4663) da Muslim (6675) ne suka rawaito shi.

Dukkan waɗannan ƙungiyoyi sun bace kuma sun karkakace daga hanyar Al-ƙur’ani da Sunnah da tafarkin magabata na ƙwarai wurin fahimtar hukuncin Allah da ƙaddararsa.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SUJJADAR RAFKANNUWA

Kasancewa rafkanuwa da mantuwa na iya bijirowa dan Adam, kuma Shaiɗan na ƙoƙarin hargitsa masa sallah da kuma shagaltar da zuciyarsa daga barin sallar; wannan ya sa Allah Ya shar'antawa mai sallah idan ya yi rafkannuwa ya yi sujjada a ƙarshen sallarsa; don turbuɗe hancin Shaiɗan da kuma cike tawayar da aka samu, haka kuma don neman yardar Allah Mai Rahma.

❖ Sabubban da ke sa a yi Sujjadar Rafkannuwa:

Wajiɗan yin sujadar rafkanuwa saboda abubuwa uku:

Ƙari, Ragi da Shakka.

- **Ƙari**: Kamar idan mai sallah ya rafkana sai ya ƙara wani aiki, kamar tsayuwa ko ruku'u ko sujada ko ya yi salla raka'a biyar ga sallah mai raka'a huɗu, to idan ya gane ya yi ƙari yayin da yake cikin sallah, to dole sai ya dawo daga wannan ƙarin, sannan ya yi sujada rafkanuwa domin karin bayan sallama.
- **Ragi**: shi kuwa ragi ya kasu kashi biyu ne; akwai rage rukuni, akwai rage wajibi.

  Idan mai sallah ya rage wani rukuni daga cikin rukunnan sallah, wajibi ne gare shi ya koma ga wannan rukunin, idan ya kasance a cikin raka'ar da yake ciki ne, sai ya zo da wannan rukuni da ya rage da abin da ya biyo bayansa, idan kuwa a cikin wata raka'ar ya tuna; to raka'ar da ya manta da wancan rukunin ta ɓaci, raka'ar da ta zo bayanta sai ta tsaya a makwafinta, sai ya yi sujadar rafkannuwa gabanin sallama wato (Ƙabaliyya).

  Amma rage wajibi; kamar mutum ya rage wani wajibi daga cikin wajiban sallah, misali: Ya manta da tahiyar farko ko yin tasbihi cikin

ruku'u ko sujada, ko ya manta da fadin: "Rabbigfir li", ko kabbarar ciratuwa zuwa wata gaba, to a wannan yanayin wannan wajidan ya fadi a kansa, sai ya yi sujjada gabanin sallama wato (Kabaliyya).

- **Shakka**: Kamar idan mutum ya yi shakka game da adadin raka'o'i ko ya yi shakka game da aikata wani wajibi ko rukuni, a irin wannan yana da halaye biyu:

  Hali Na Farko: Idan shakkan tare da yiwuwar aikata abubuwan suka yi kankankan ba tare da ya iya rinjayar da dayansu ba; to a wannan halin zai yi aiki ne da tabbas (wato yakini) wanda shi ne mafi karanci, wato kamar bai aikata ba kenan, sai ya yi sujjada kabaliya saboda fadar Manzo (SAW): (Idan dayan ku ya yi shakka a cikin sallarsa, ya rasa raka'a na wa ya yi; uku ne ko hudu? To ya hurgar da shakkan, sai ya yi gini akan abin da ya ke da tabbaci, sannan ya yi sujada biyu kafin sallama) [1].

  Hali Na Biyu: Idan zatonsa ya rinjaya ga dayan abubuwa biyun, to sai ya yi aiki da abin da ya rinyajar, sai ya yi sujjada biyu na rafkannuwa bayan sallama, saboda fadin Manzo (SAW): (To ya yi kirdadon abin da shi ne daidai, sai ya gina akansa, sannan ya yi sallama, sai ya yi sujada biyu bayan ya sallame) [2].

❖ Bigiren Sujadar Rafkanuwa:

Ya bayyan daga abin da ya gabata cewa abin da da ya fi kuma shi aka sunnanta; Mutum ya yi sujjadar rafkanuwa kafin sallama idan ya yi ragi, kari kuma ya yi bayan sallama, idan kuma shakka ya yi ba tare da rinjayarwa ba sai ya yi kafin sallama, idan kuwa ya rinjayar da wani abu sai ya yi sujadar bayan sallama, wannan shi ne

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (571).
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (571).

mafi dacewa, kuma wajibi na samuwa da yin sujadar rafkanuwa kafin sallama ko bayanta.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

SHIGAR ANNABI (SAW) MADINA

Labarin fitowar Annabi (SAW) daga Makkah da nufatowarsa ga Madina ya ishi mutanen Madina, sai suka kasance kullum suna fita zuwa wani wuri mai suna Harrah suna jiransa, a ranar Litinin Sha Biyu ga watan Rabi'ul Auwal sun sake fita kamar yadda suka saba, da yini ya yi tsawo, kuma garjin rana ya yi tsanani, sai suka koma gidajensu, sai Manzon Allah (SAW) ya fuskanto su, wanda ya fara ganin shi kuwa wani mutum ne daga cikin Yahudawa, sai ya yi yekuwa da babban murya, yana musu albishir da isowar Annabi (SAW), sai mutanen Madina suka fito suna murna suna farin ciki.

Da farko, Manzon Allah (SAW) ya sauka ne a Ƙuba' wurin Kulthum ɗan Hidmi, sai mutanen Madina suka zo suna masa sallama, wanda da yawansu ba su kai ga ganin shi ba, sun ɗauka Abubakar (RA) shi ne, saboda matukar kama da ya yi da shi, da zafin rana ya yi tsanani sai Abubakar (RA) ya miƙe yana yi wa Annabi (SAW) inuwa da wani tufafi, nan fa mutane suka gane wanene Manzon Allah (SAW) [1].

Annabi (SAW) ya zauna a Ƙuba' na wasu kwanaki, ya kuma kafa masallaci a nan, sannan ya shiga Madina, taguwarsa ba ta gushe ba tana zagayawa da shi, ba za ta wuce wani gida daga gidajen Mutanen Madina ba face sun yi kwaɗayin ina ma ta sauka a wurinsu, har sai da ta iso wurin da Masallacinsa ya ke sai ta kwanta, wanda wurin filin wasu marayu ne a unguwar Banun-Najjar, a gaban gidan Abu Ayyub Al-Ansari (RA), sai Annabi (SAW) ya sakko daga kanta, nan take Abu Ayyuba ya ɗauki jakar Manzon Allah (SAW) zuwa gidansa don ya riga kowa ba shi masauke, sai Manzon Allah (SAW) ya sayi

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (3906).

wannan filin, ya gina Masallaci, sannan ya gina wa iyalansa ɗakuna a gefensa[1].

Gina masallacin Annabi shi ne abu na farko da Annabi (SAW) ya yi, ya mayar da shi wurin sallah da ibada, da kuma tsangaya da musulmai ke koyon al'amuran addininsu a cikinsa, haka kuma majlisi ne na shawarwari, kuma mahaɗa ne na 'yan uwantaka da haɗin kai, kuma mazauni ga mutane masu yawa daga cikin talakawan Muhajirai.

Abu na biyu da Annabi (SAW) ya yi shi ne haɗa 'yan uwantaka tsakanin mutanen Makka da mutanen Madina, 'yan uwantaka da ta shafe ƙabilancin jahiliyya, kuma ta disashe bambancin nasaba da launi, ta kuma cika zukatansu da ruhin so da fifita wani akan kai, har mutanen Madina suka cewa Annabi (SAW) ka raba mana gonakan daɗananmu tsakaninmu da 'yan uwanmu, ya ce: (A'a, ku ɗauke mana dawainiyar shayar da su, sai mu yi tarayya a kan amfaninsu), Suka ce: "Mun ji, mun kuma bi."

Abu na uku da Annabi (SAW) ya yi shi ne ƙulla yarjejeniyar zaman lafiya tare da Yahudawa, da rubuta hakan a rubutu da ke ƙunshe da sasanni da za su tsare haƙƙoƙin Musulumi da na Yahudawa.

[1]. As-Siyar: (2/406).

ALHAMIS: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABU ZARRIN AL-GIFARI (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne: Abu Zarrin, Jundub ɗan Junada ɗan Ƙais ɗan Amru Al-Gifari

An haife shi a wurin da ake kira Wadi Waddana, inda kabilar Gifar suka kasance a zaune.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Abu Zarrin Al-Gifari (RA) ya kasance mutum ne mai tsayi, mai cikar gemu, sannan yana cikin daɗaɗɗu a Musulunci, yana kuma cikin manyan Sahabbai da masu falala, masani ne, jarumi, mai karamci, mai faɗar gaskiya, ba ya tsoron zargin mai zargin a kan al'amarin Allah.

Daga cikin misalan hakan, matsayarsa a ranar da ya musulunta, inda ya ce: "Na rantse da wanda raina ke hannunsa, zan shelanta musuluntata da babban murya a tsakiyar mushrikai". Haka ya fito har ya zo masallaci, ya ɗaga muryarsa da kalmar shahada: 'Na shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma lallai Muhammadu Manzon Allah ne", nan take mushrikai suka far masa da duka har sai da suka kai shi ƙasa, Abbas (RA) ya zo ya kare shi, yana ce musu: "Kaiconku, ba ku san cewa daga ƙabilar Gifar ya ke ba? Ashe ba hanyar 'yan kasuwanku ba ne zuwa garin Sham?" Sai ya ceci shi daga wurin su, washegari, Abu Zarrin ya ƙara maimaita irin haka, suka ƙara dukansa, suka rufar masa, Abbas ya ƙara kare shi, ya kuɓutar da shi daga hannunsu[1].

[1]. Bukhari (3861) da Muslim (2474) ne suka rawaito shi.

Daga lokacin da ya musulunta ya wuce garinsu, ya zauna a can yana kiran su ga Musulunci, raɗan garin suka musulunta, a lokacin da Manzon Allah (SAW) ya iso Madina ragowar raɗan suka musulunta su ma[1], daga nan ne Abu Zarrin ya bar garin Gifar, ya yi ƙaura zuwa ga Annabi (SAW), ya lazimce shi, har ya yi jihadi tare da shi.

Annabi (SAW) ya yabe shi wata rana da faɗinsa: (Ƙasa ba ta taɓa ɗaukar wani mutum ba, ko sama ta yi masa inuwa ga wani mutum mai gaskiyar zance ba kamar Abu Zarrin) [2].

Abu Zarrin (RA) ya riƙe matsayin mai fatawa a lokacin halifancin Abubakar da Umar da Usman, kuma ya kasance abin kwantance ne a gudun duniya da son talakawa, idan albashinsa ya zo daga Baitul mali, sai ya kira hadiminsa, ya umurce shi ya siyo abin da zai ishe shi na shekara ɗaya, sannan ya canza abin da ya rage na dukiyar zuwa kuɗi ya raba wa talakawa[3].

❖ Rasuwarsa:

Abu Zarrin Allah (RA) ya rasu ne a wurin da ake kira Rabazah, a shekara ta Talatin da ɗaya, Abdullahi ɗan Ma’aud (RA) ne ya masa sallah.

---

[1]. Siyaru A’lamin-Nubala (2/53).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3801).
[3]. Siyaru A’lamin-Nubala’ (2/72).

Auna fahimtarka a cikin darussan mako na 23			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Wa ake nufi da faɗin Allah: "Ka ba ni labarin wanda ya hana. Bawa yayin da ya yi sallah"?**		c
	a. Abu Lahabi	b. Uƙubah ɗan Abu Mu'az	c. Abu Jahl
Darasin Hadisi	**Tambaya: Daga cikin nau'o'in ƙauracewa Alƙur'ani akwai:**		c
	a. Rashin yiwa Alkur'ani kwalliya	b. Rashin rataya Ayoyi a bango	c. Barin neman waraka da shi
Darasin Aƙida	**Tambaya: Daga cikin mas'aloli dake da alaƙa da ƙaddara, lallai mashi'ar bawa:**		a
	a. Ta na ɗan na Allah ne	b. Tana cikin gashin kanta ne daga mashi'ar Allah	c. Ba wanda ke da iko a kanta
Darasin Fiƙihu	**Tambaya: Idan mutum ya yi rafkanuwa sai ya yi raka'a biyar a maimakon huɗu?**		b
	a. Zai yi ƙabaliya	b. Zai yi ba'adiya	c. Ba sujada akan shi
Darasin Sira	**Tambaya: Farkon wanda ya ga Annabi yana shigowa Madina wani mutum ne daga:**		a
	a. Yahudawa	b. Aus	c. Khazraj
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Abu Zarrin ya riƙe mukami a halifancin Abubakar na:**		b
	a. Zakkah	b. Fatawa	c. Baitul-Mali

MAKO NA ASHIRIN DA HUDU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUD-DUHA

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلضُّحَىٰ ١ وَٱلَّيۡلِ إِذَا سَجَىٰ ٢ مَا وَدَّعَكَ رَبُّكَ وَمَا قَلَىٰ ٣ وَلَلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ لَّكَ مِنَ ٱلۡأُولَىٰ ٤
وَلَسَوۡفَ يُعۡطِيكَ رَبُّكَ فَتَرۡضَىٰٓ ٥ أَلَمۡ يَجِدۡكَ يَتِيمٗا فَـَٔاوَىٰ ٦ وَوَجَدَكَ ضَآلّٗا فَهَدَىٰ ٧
وَوَجَدَكَ عَآئِلٗا فَأَغۡنَىٰ ٨ فَأَمَّا ٱلۡيَتِيمَ فَلَا تَقۡهَرۡ ٩ وَأَمَّا ٱلسَّآئِلَ فَلَا تَنۡهَرۡ ١٠ وَأَمَّا بِنِعۡمَةِ
رَبِّكَ فَحَدِّثۡ ١١﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin kai

1. Ina rantsuwa da lokacin hantsi.
2. Da kuma dare idan ya yi tsit.
3. Ubangijinka bai bar ka ba, kuma bai ki ka ba.
4. Kuma lallai lahira ta fi maka alheri a kan duniya.
5. Kuma lallai Ubangijinka zai ba ka har sai ka yarda (da abin da Ya ba ka).
6. Shin bai same ka maraya ba sai Ya hada ka (da mai kula da kai)?
7. Ya kuma same ka marashin shiriya Ya shiryar (da kai)?
8. Ya kuma same ka matalauci Ya wadata (ka)?
9. Don haka maraya fa kada ka yi masa fin karfi.
10. Mai tambaya kuma kada ka daka masa tsawa.
11. Amma kuma game da ni'imar Ubangijinka sai ka ba da labari.

❖ Sababin saukar surar:

Annabi (SAW) ya yi rashin lafiya, sai bai iya tashi don yin sallar dare ba tsawon dare biyu ko uku, sai wata mata ta ce masa: ‘Ya Muhammadu! Ina gani shaiɗanin ka ya ƙyale ka, ga shi bai zo maka ba har dare biyu ko uku. Sai Allah Ya saukar da wannan surar[1].

❖ Saƙon da Surar ke ƙunshe da shi:

Kulawar Allah ga Annaɗansa, a farkon al’amarinsa da ƙarshensa.

❖ Baƙin Kalmomi:

سجى	Sajaa	Ya lullube duniya da duhunsa da shiru
ما ودعك	Maa wadda’aka	Bai bar ka ba
وما قلى	Wa maa kalaa	Bai ki ka ba lokacin da wahayi ya yi jinkirin zuwa maka.
فآوى	Fa’awaa	Sai Ya kula da kai
ضالا	Dallan	Marashin Shiriya: Ba ka san wahayi ba, kuma ba ka san Al-Kur’ani ba.
فهدى	A’ilan	Matalauci.
فلا تقهر	Fala tak-har	Kar ka munanta ma’amala gare shi, kuma kar ka karbi dukiyarsa
تنهر	Tanhar	Yi masa tsawa

[1]. Siyaru A’lamin-Nubala’ (2/72).

❖ Ma'anar Surar a Dunƙule:

Suratud-Duha sura ce makiyya, an buɗe ta da rantsuwa guda biyu, wanda ke nuni a kan lokuta biyu na harkoki da na nutsuwa), don tabbatar da cewa Allah Maɗaukaki Bai rabu da Manzonsa (SAW) ba kuma bai ƙyamace shi ba, kuma lallai abin da Ya tanada masa a lahira na matsayi Maɗaukaki ya fi alheri fiye da abin da Ya karrama shi da su a nan duniya, kuma lallai Allah Maɗaukaki Zai ba shi kyauta mai girma har sai ya gamsu.

Da yake jumu'ar da za ta yi kyau tun daga laraba ake gane ta, sai Allah Ya ambaci cewa fa Annabi (SAW) ya kasance maraya ne, sai Ya kula da shi, kuma marashin shiriya sai Ya kyautata shiriyarsa, kuma matalauci Ya wadata shi, bayan haka sai Allah Ya umurce shi da ya kyautata shi ma ta hanyar darajta maraya, kar kuma ya kyari mai tambaya, sannan kuma ya rinka ba da labarin ni'imar Allah (gare shi).

❖ Aɗan da za a Koya daga Surar:

1. Lallai Annabi (SAW) na da matsayi na musamman wurin Ubangijinsa da ba bu wani matsayi da ya kai shi.
2. Bayyana falalar karrama maraya da kula da shi.
3. Wajibcin jin kan masu rauni da tausasa musu.
4. Godiya bisa ni'imomi na daga cikin haƙƙoƙin Allah a kan bayinsa.
5. Bayyanar da ni'ima da ba da labarinta ba tare da almubazaranci ko girman kai ba, wannan ma ana ƙirga shi cikin godiya; kamar yadda Manzo (SAW) ya ce: (Lallai Allah Ya na so Ya ga alamun ni'imarSa ga bawanSa) [1].

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (2819).

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

DAGA CIKIN SABUBBAN KARƁAR ADDU'A

An karɓo daga Abu Hurairah Allah Ya kara masa yarda, ya ce: Manzon Allah (SAW) Ya ce: (Addu'o'i uku karɓaɓɓu ne, babu kokwanto a kansu, addu'ar wanda aka zalunta, da addu'ar matafiyi, da addu'ar mahaifi ga dansa)[1].

❖ Sharhi:

A cikin wannan Hadisi, Annabi (SAW) ya bayyana wasu addu'o'in da Allah ba Ya mai da su, ana karɓar su ko shakka babu, wanda su ne: addu'a daga wanda aka zalunta, ko da kuwa kafiri ne aka zalunce shi, lallai Allah Yana karɓar addu'arsa a kan wanda ya zalunce shi, da kuma addu'ar matafiiyi, idan ya roki Allah Maɗaukaki a halin tafiyarsa, da kuma addu'an mahaifi; ko uba ko uwa, haka kuma addu'ar ta kirkice ko mummuna ga dansa.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1. Musatahabbi ne yawaita addu'a a halin tafiya, don bigiren karɓar addu'a ne.
2. Tsoratarwa daga zalunci da kuma bayyana cewa addu'ar wanda aka zalunta karɓaɓɓiya ce ko da kafiri ne.
3. Tsoratarwa daga saɓa wa iyaye da kuma guje wa mummunar addu'arsu, don kuwa ba a mayar da ita.

[1]. Abu Dawud (1536) da Tirmizi ne suka rawaito shi (3448).

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

IMANI DA GAIBU

Gaibu: shi ne duk wani abi da ya ɓoyu.

Shi gaibu gaba ɗayansa ba wanda ya san shi sai Allah Maɗaukaki, wanna ya ƙunshi abin da ya faru a baya, ko yanzu, ko kuma abin da nan gaba zai kasance, haka kuma duk matsayin da bawa zai kai da girmansa da ƙarfinsa, ko kuma ya kasance yana da wasu hanyoyi da ƙere-ƙere, ba zai iya sanin gaibu ba, don kuwa ilimin gaibu na daga cikin abin da Allah Maɗaukaki Ya keɓanta da shi ((Masanin ɓoye da sarari ne Mabuwayi, Mai hikima)) [1].

Kuma Annaɗanmu (SAW) wanda shine fiyayyen halitta, kuma mai matsayi mai girma wurin Allah kuma sha yabo, bai san gaibu ba, kuma bai ce ya sani ba, Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ka ce: Ni ba zan ce da ku a wajena taskokin Allah suke ba, kuma ni ban san gaibu ba, kuma ni ba zan ce da ku mala'ika ne ba, ni ba abin da nake bi sai abin da aka yi mini wahayinsa)) [2].

A'isha (RA) ta ce: "Duk wanda ya raya cewa Manzon Allah (SAW) Ya na bada labarin abin da zai kasance gobe, to hakika ya yi wa Allah babbar karya, alhali Allah Maɗaukaki Ya na cewa: ((Ka ce (da su): Duk wanda yake cikin sammai da kasa in ba Allah ba ba wanda ya san gaibu))[3].

Sai dai Allah kan iya tsinkayar da wasu cikin Manzanninsa wani abu na labarurrukan gaibi don wata hikima da Ya sani; kamar yadda Allah Ya ce: ((Shi ne Masanin gaibu, sannan ba Ya bayyana gaibunsa

---

1. [At-Tagabun: 18].
2. [Al-An'am: 50].
3. [An-Naml: 65].

ga wani () Sai manzo da Ya yarda da shi, kuma lallai Ya kan sanya masa tsaro ta gabansa da ta bayansa)) [1].

Don haka duk abin da ya riske mu na irin wannan gaibun a cikin Al-ƙur'ani da Sunnah wajibi ne imani da shi; domin imani da gaibu ginshiƙi ne daga cikin ginshiƙan aƙida, kuma asali ne daga cikin asalullukan addini, imani ba ya inganta sai da shi; don haka ne ma mai gasgata shi ya cancanci a siffanta shi da imani da tsoron Allah, kamar yadda Allah Ya ce: ((Wannan littafi ne da babu kokwanto a cikinsa; shirya ne ga masu takawa. Waɗanda suke yin imani da gaibi…))[2].

- **Imani da gaibi yana da tasiri mai girma, daga cikin su a kwai:**

1. Ji koda yaushe cewa Allah na kallon ka, da tuna kusancin Mala'iku gare ka, wanda hakan ke ƙarawa bawa tsoron Allah da tsayuwa akan addininsa.
2. Kasancewa a faɗake da kuma cikin shiri domin gidan lahira, da abin da ke cikinta na wahalhalu tsayuwa da hisabi da siradi da mizani.
3. Riskan rauni da ke cikin ilimin halitta, da irin girma da buwaya da ke cikin ilimin Mahalicci; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ba abin da aka ba ku na ilimi sai dan kaɗan)) [3].
4. Dogaro ga Allah, tare da riko da sabubba.

[1]. [Al-Jinni: 26-27].
[2]. [Al-Baƙarah: 2-3].
[3]. [Al-Isra'i: 85].

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SUJJADAR TILAWA DA TA GODIYA

❖ Sujjadar Tilawa:

Sujjadar Tilawa sujjada ce da Allah Ya shar'anta yayin karantawa wasu Ayoyi da sauraron su domin kusanci gare Shi, da bauta gare Shi, da kuma kankan da kai ga grimansa, da gurfana gaba gare Shi, Annabi (SAW) ya ce: (Idan ɗan'adam ya karanta Aya mai sujada, sai Ya yi sujada, Shaiɗan zai koma gefe yana kuka, yana cewa: Ya kaiconsa! An umurci ɗan'adam ya yi sujjada ya yi, zai samu aljanna, ni kuma an umurce ni in yi sujada na ƙi, ni kuma wuta zan shiga)[1].

Abdullahi ɗan Umar Allah Ya ƙara musu yarda ya ce: "Annabi (SAW) ya kasance yana karanta surar da akwai sujjada a cikinta sai ya yi sujjada, sai mu ma mu yi sujadan tare da shi, har ɗayanmu ya rasa wurin da zai sa goshinsa".[2]

❖ Ayoyin Sujjadar Tilawa:

Ayoyin da ake sujada a cikin Al-Kur'ani iri biyu ne:

- Ayoyin da ke umurtar musulmi da ya yi sujada karara, sai ya yi gaggawan da'a ga Mahaliccinsa.
- Ayoyin da cikin aka bada kabarin wasu manyan halittu sun yi sujada; sai bawa ya yi sujada shi ma yana mai koyi da su.

❖ Hukuncin Sujjadar Tilawa:

Sujadar tilawa mustahabbi ce ga mai karatu da kuma mai saurare, a cikin sallah ko wajen sallah, idan mai karatu bai yi sujadan ba, to mai saurare ba za iyi sujada ba don kuwa mai saurare yana ɗan mai

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (81).
[2]. Bukhari (1076) da Muslim (575) ne suka rawaito shi.

karatu ne wurin hukunci. Amma wanda ya ke jiyo karatu ba da nufin saurara ba to ba a shar'anta masa sujadar tilawa ba, saboda abin da aka ruwaito daga Usman (RA) cewa ya wuce wani mai karatu yana karanta wurin sujada, sai bai yi sujada ba, ya ce: "Mai saurare ne ke sujada" [1].

❖ Aɗan da ake faɗi a cikin Sujjadar Tilawa:

- (Subhana rabbiyal a'laa) kamar yadda ake fada a sujadar sallah.
- (Subhanakallahumma rabbana wa bihamdika, allahummgh-fir li) [2].
- (Sajada wajhi lillazee khalakahu wa shaƙƙa sam'ahu wa basarahu bi haulihi wa ƙuwwatihi) [3].
- (Allahummak-tubli biha indaka ajran, wa da' anni biha wizran, waj-alha li inda zukhran, wa taƙabbalha minni kama taƙabbaltaha min abdika Dawud) [4].

❖ Wasu hukunce-hukuncen da suka shafi sujjadar tilawa:

- Sunna ce ga sujadar tilawa: tsarki da kuma fuskantar alkibla.
- Ana kabbara don sujadar tilawa a cikin sallah lokacin tafiya sujjadar da yayin ɗagowa, amma a wajen sallah ana yi ne lokacin tafiya sujjadar kawai.

❖ Sujjadar godiya:

Sunna ce yin sujadar godiya idan ɗayan waɗannan abubuwa ya faru:

- Yayin da wata ni'ima ta sabunta, kamar wanda aka mishi albishir da shiryuwan wani, ko musuluntar sa, ko samun nasarar

---

[1]. Abdur-Razzaƙ ya ruwaito shi (3/334).
[2]. Bukhari (794) da Muslim (484) ne suka rawaito shi.
[3]. Abu Dawud (1414) da Tirmizi (580) ne suka rawaito shi.
[4]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3424)

musulmi, ko aka masa albishir da samun karuwar haihuwa, da makamantan haka.

- Yayin da wata musiba ta kauce wa mutum, kamar wanda ya tsira daga nutsewa cikin ruwa, ko gobara, ko kisa, ko wata halaka, ko ɓarayi, an ruwaito daga Abu Bakrata (RA) cewa “Lallai Annabi (SAW) idan wani abin farin ciki ya same shi ko an masa albishirin da shi, sai ya gurfana yana mai sujada, yana godiya ga Allah Maɗaukaki) [1].

[1]. Abu Dawud ne ya rwaito shi (2774).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

YAƘIN BADAR BABBA

❖ Tarihinsa:

Yaƙin Badar ya faru ne a sha bakwai ga watan Ramadan a shekara ta biyu na hijira. Wannan yaƙi wani babban lamari ne da ya faru inda Allah Ya rabe tsakanin gaskiya da karya, kuma Ya ɗaukaka musulunci da musulmai, Ya ƙasƙanta kafirci da kafirai.

❖ Sabuban faruwarsa:

Sabuban faruwar wannan yaƙin: Labari ya iske Annab (SAW) cewa ayarin Kuraishawa sun fuskanta daga Sham karkashin jagorancin Abu Sufyan, mazaje talatin, ayari ne mai girma, suna dauke da dukiya mai yawa, sai Annabi (SAW) ya kwaɗaitar da mutane ga su fita su tare su, ko Allah Zai ba su sa'a a kansu, Annabi (SAW) bai shirya wani gagarumin shiri ba, kuma bai matsawa kowa sai ya fita ba, don bai yi tsammanin cewa zai hadu da rundunar Makkah ba ne maimakon ayarin Abu Sufyan.

❖ Abubuwan da suka faru a cikinsa:

Manzo (SAW) ya fito ne da mutane ɗari uku da 'yan kai, babu wani cikinsu da ke da doki sai mutane biyu, Zubair ɗan Awwam da Al-Miƙdad ɗan Amrin (RA), sai kuma raƙuma saba'in, sahabbai suna canji wurin hawa rakumi ɗaya, in wannan ya hau, sai ya sauka wani ya hau, sai Annabi (SAW) ya naɗa Abdullahi ɗan Ummi Maktum (RA) shugaba a Madina kuma wanda zai jagorancin sallah.

Shi kuwa Abu Sufyan labarin fitowar Annabi (SAW) ya iske shi da kuma abin da ya nufa, sai ya tura wani mutum zuwa Makkah don ya shelantawa Ƙuraishawa su garzayo ga ayarinsu fa don su ba su kariya. Nan take mushrikai suka taho cikin gaggawa, suka fito cikin

dukkansu, babu wani cikin masu darajarsu face sai da ya fito, suka shiryo rundunan mayaƙa dubu, da dawakai ɗari, da sulke guda dari shida, da raƙuma masu yawan gaske, ba a san adadin su ba.

Nan ne fa Annabi (SAW) ya nemi shawarar sahabbansa gabanin yaƙin, suka ba shi amsa da mafi alkhairin amsa, daga ciki akwai maganar Sa'ad ɗan Mu'az: "Na rantse da Allah, ya Annaɗan Allah, inda za ka kutsa da mu cikin teku da mun kutsa tare da kai, ka ja mu mu je kawai, ya Annaɗan Allah, cikin albarkar Allah!" [1].

Waɗannan maganganu da tabbatuwansu sun kayatar tare da faranta ran Manzon Allah (SAW), ya ce: (Ku tafi, kuma ina muku albishir, lallai Allah Ya mini alƙawarin ɗayan jama'an nan guda biyu) Ya ce: "Nan ne wurin makasar wane, nan ne makasar wane gobe in Allah Ya so" Abdullahi ɗan Mas'ud (RA) ya ce: (Na rantse da Wanda Ya aiko shi da gaskiya, ba wani cikinsu da ya kuskure inda Annabi (SAW) ya nuna a matsayin makasarsa) [2].

Haka Annabi (SAW) ya ci gaba da shiryawa da tsara rundunar, ya ba da tutar jagoranci ga Mus'ab ɗan Umair, ya raba rundunar zuwa bataliyan muhajirai, ya ba Aliyu dan Abu Ɗalib tuta, da bataliyan Ansar ya ba Sa'ad ɗan Mu'azu tuta, a bangaren dama kuma ya sai Zubair ɗan Awwam, ɓangaren hagu kuma Al-Miƙdad dan Amrin, sai jagoranci na gaba ɗaya na hannunsa (SAW).

Kuma musulmai suka ginawa Annabi (SAW) wani daki a kan wani tsauni mai tsawo, suka zabi wasu mutane da za su yi gadin sa, muslulmai suka kwana cikin daren cikin aminci da natsuwa, gyangyadi ya kwashe su, Annabi (SAW) kuwa ya kwana yana sallah, yana roƙon Ubangijinsa, haka har yaƙi ya fara ya yi tsanani,

[1]. Al-Biɗayah Wan Nihayah (3/262).
[2]. Al-Biɗayah Wan-Nihayah (3/262).

Annabi (SAW) ya dage da addu’a, da ƙanƙan da kai ga Allah sosai, har mayafinsa na faɗuwa daga kafaɗunsa, Abubakar (RA) yana gyara masa, yana ce masa: “Ya Manzon Allah, lallai Allah Zai cika maka alƙawarin da Ya yi maka”.

Shi kuma Annabi (SAW) ya na cewa: (Ya Allah, idan waɗannan mutane suka halaka, ba masu bauta maka a ban ƙasa ba)[1]. Wannan shi ne labarin da Allah Ya ba da a cikin faɗinSa: ((Ku tuna lokacin da kuke neman taimakon Ubangijinku, sai Ya amsa muku cewa: Ni zan kawo muku ɗauki na mala’iku dubu masu bibiyar juna))[2].

❖ Sakamakon yaƙin:

Annabi (SAW) ya ɗan gyangyaɗa, sannan ya ɗaga kansa yana cewa: (Albishirinka Abubakar! Taimakon Allah Ya zo maka, ga Jibrilu nan ya riƙe linzamin dokinsa yana sukuwa a kansa daidai Thanayan Naƙ’i)[3].

Sai Allah Ya ƙarfafi ManzonSa (SAW) da wata runduna daga wurinsa, musulmi suka samu nasara, aka tunɓuke tushen kafirai, aka kashe mutane saba’in cikin mushrikai, mafi yawansu jagorori ne da gwarazansu, kamar Abu Jahl, da Umayyah ɗan Khalaf, aka kama mutane saba’in, sauran kuma suka gudu suna ƙasƙantattu, shi kuwa Annabi (SAW) ya dawo Madina cikin izza da Allah Ya taimaka masa da ita.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (1763)
[2]. [Al-Anfal: 9].
[3]. Siratu Ibnu Hisham (1/626).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABU MUSA AL-ASHA'RI (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shine sahabi mai daraja Abdullahi ɗan Ƙais ɗan Haddar, Abu Musa Al-Asha'ari, ya shahara da sunansa da alkunyarsa a lokaci guda, mahaifiyarsa ita ce Zabyah 'yar Wahab daga ƙabilar Akkin, ta muslunta kuma ta rasu a Madina.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Ya kasance jagora ne daga cikin jagororin sahabbai (RA), mai karamin jiki ne, sadauki ne wurin yaƙi, masanin fikihu, mai kaifin basira wurin fatawa da alkalanci.

Ya zo Makkah ne a farkon bayyanar musulnci, ya musulunta, kuma ya yi hijira guda biyu duka, Annabi (SAW) ya yi masa addu'a, ya ce: (Allah Ka gafartawa Abdullahi ɗan Ƙais zunubbansa, Ka shigar da shi mashiga ta daraja ranar Alkiyama)[1].

Haka kuma Annabi (SAW) ya shugabantar da shi, shi da Mu'azu dan Jabal ga mutanen Yaman, ya daura kowannensu ga wani yanki[2].

An tambayi Aliyu ɗan Abi Ɗalib (RA) game da matsayin Abu Musa (RA) a ilimi, ya ce: (An rina shi a ilimi rinawa)[3].

Haka kuma ya kasance yana da daddadan murya wurin karanta Al-ƙur'ani, mai zaƙin tilawa, mai tsananin kushu'i, Annabi (SAW) ya

---

[1]. Bukhari (4323) da Muslim (2498) ne suka rawaito shi.
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (4341).
[3]. Siyaru A'lamin-Nubala (2/388).

ce masa: (Da ka gan ni daren jiya ina sauraren karatunka, lallai an ba ka sarewa daga cikin sarewar iyalin Annabi Dawud)[1].

Umar ɗan Khaɗɗab (RA) ya kasance duk sanda ya ga Abu Musa, sai ya kira shi don ya karanta masa Al-ƙur'ani, ya ce masa: (Ka sa mana shauƙi ga Mahallicinmu, ya kai Abu Musa) [2].

Abu Musa (RA) ya kasance ɗaya daga cikin jagorori da Allah Ya ba su nasarar cin yaƙi, ya halarci buɗe Sham, da buɗe Ahwaz da Asbahan, sannan daga baya ya karɓi jagorancin Basrah, sai ya zauna a Kufah bayan nan, mutanen Basrah suka ko yi fiƙihu a hannunsa, ya kuma kasance ɗaya daga cikin masu hukunci da Aliyu da Mu'awiyah (RA) suka yarda da su lokacin rikicin Siffin.

Ya yi ƙoƙari sosai wurin yawaita ibada a ƙarshen rayuwarsa, har aka ce masa: "Ka haƙura mana haka, ka tausayawa kanka", sai ya ce: "Lallai doki idan aka sake shi don tsere, da ya kusanto wurin tsayawa, sai ya tattara dukkan karfinsa don ya ƙarasa tseren, abin da ya rage mini a ajalina bai kai hakan ba" [3].

❖ Rasuwarsa:

Abu Musa (RA) ya rasu ne a shekara ta arba'in da biyu a Makkah, wasu kuma suka ce a Kufah ya rasu.

---

[1]. Bukhari (5048) da Muslim (793) ne suka rawaito shi.
[2]. Siyaru A'lamin-Nubala (2/398).
[3]. Shu'abul Iman (13/202).

Auna Fahimtarka - a cikin darussan mako na 24				Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsir	**Tambaya: Menene ma'anar faɗin Allah Maɗaukaki: "A'ilan"**			a
	[a] Marashin shiriya	[b] Talaka	[c] Maraya	
Darasin Hadisi	**Tambaya: Addu'ar wanda aka zalunta akan wanda ya zalunce shi karbabbiyace:**			c
	[a] Idan wanda aka zalunta musulmi ne	[b] Idan azzalumin kafiri ne	[c] Ko da wanda aka zalunta kafiri ne	
Darasin aƙida	**Tambaya: Menene Gaibu?**			a
	[a] abin da ya ɓoyu kuma nisa da gabobi	[b] abin da zai faru nan gaba	[c] Abubuwan da suka faru can baya kawai	
Darasin fiƙihu	**Tambaya: Yaya halin Shaiɗan ya ke idan mutum ya yi sujda ga Allah?**			a
	[a] Kuka ya ke yi	[b] Dariya ya ke yi	[c] Izgilanci ya ke yi	
Darasin sira	**Tambaya: Yaƙin Badar ya faru ne a shekara ta:**			b
	[a] 2H	[b] 3H	[c] 4H	
Darasin tarihin Sahabbai	**Tambaya: Annabi tsira da aminci ya yi wa Abu Musa Al-Ash-ari shaida da:**			b
	[a] Dacewa a harbi	[b] Kyawun sauti	[c] Cikar hankali	

MAKO NA ASHIRIN DA BIYAR

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUSH-SHARH

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
أَلَمۡ نَشۡرَحۡ لَكَ صَدۡرَكَ ۝١ وَوَضَعۡنَا عَنكَ وِزۡرَكَ ۝٢ ﴾ ﴿ٱلَّذِيٓ أَنقَضَ ظَهۡرَكَ ۝٣ وَرَفَعۡنَا لَكَ
ذِكۡرَكَ ۝٤ فَإِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ۝٥ إِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ۝٦ فَإِذَا فَرَغۡتَ فَٱنصَبۡ ۝٧ وَإِلَىٰ رَبِّكَ
فَٱرۡغَب ۝٨ ﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin Kai

1. Shin ba Mu yalwata maka kirjinka ba?
2. Muka kuma sauke maka nauye-nauyenka?
3. Wanda ya nauyayi bayanka?
4. Muka kuma ɗaukaka maka ambatonka?
5. To lallai tsanani yana tare da sauki.
6. Lallai tsanani yana tare da sauki.
7. Saboda haka idan ka gama (harkokinka) sai ka kafu (wajen bautar Allah).
8. Sannan kuma ka yi kwaɗayi wajen Ubangijinka kawai.

❖ Saƙon da Surar ɗauke da shi:

Bayanin abin da Allah Ya karrama Annaɗansa da shi na yalwata masa ƙirjinsa, da gafarta masa zunubbansa, da kuma ɗaukaka ambatonsa.

❖ Bakin kalmomi:

وضعنا	Wada’na	Mun sauke kuma mun gafarta
وزرك	Wizraka	Zunubbanka

أنقض	Ankada	Nauyaya
فإذا فرغت	Fa iza faraghta	Idan ka gama (Harkokinka)
فانصب	Fansab	Sai ka kafu
فارغب	Farghab	Ka yi kwaɗayi

❖ Ma'anar Surar a Dunƙule:

Suratul Sharh tana cikin Surorin Makkah, kuma a cikinta akwai bayanin falalar Allah Maɗaukaki ga Manzonsa, guda uku:

Na Farko: Faɗaɗa ƙirjinsa, don ya karɓi wahayi da shari'o'in addini; kuma ya shirya don abin da zai haɗu da shi daga mutanensa na munanan maganganu.

Na Biyu: Ɗaukaka matsayinsa; kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Domin Allah Ya gafarta maka abin da ya gabata na zunuɗanka, da kuma wanda ya jinkirta))[1].

Na Uku: Ɗaga ambatonsa; domin Allah Maɗaukaki ya haɗa sunansa da sunanSa a cikin tahiya, da cikin kiran sallah, da ikama, da sauransu.

Sannan Surar ta ƙare da babban bushara, cewa duk inda aka samu tsanani da wahala, sauki da yayewa na na tafe tare da ita. Don haka ne ma Annabi ya ce (SAW): (Lallai tare da tsanani akwai sauƙi)[2].

[1]. [Al-Fath: 2].
[2]. Tirmizi ne ya rawaito shi (2517).

❖ **Abubuwan da za a koya daga Surar:**

1) Bayanin ni'imar Allah Mai girma da ɗaukaka ga Manzonsa, da girman matsayinsa a wurin Allah.
2) Albishir da yaye kunci daga Allah, da kuma cewa lallai tare da wahala akwai sauƙi koyaushe.
3) Lallai ne Musulmi ya yi kwaɗayin samun abin da ke wurin Ubangijinsa Shi Kaɗai, kuma kada ya yi kwaɗayin wani abu sai daga falalarsa, kuma kada ya yi fatan samun wani abu sai daga gare shi.
4) Rayuwar mumini babu wargi ko shirme, ko zaman kawai a cikinta.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

BARIN SHAGALTUWA DA ABIN DA BAI SHAFI MUSULMI BA

An daga Abu Hurairah (RA) ya ce Manzon Allah: Ya ce (SAW): (**Daga cikin kyawun musuluncin mutum, akwai barin abin da bai shafe shi ba**)[1].

❖ Sharhi:

Wannan hadisin ginshiki ne mai girma wurin ladabtar da kai da tsarkake ta, da kare ta daga tawaya da nakasu, da duk abubuwan da ba su da muhimmanci ko amfani. Yana cikin kyawun musuluncin mutum da cikar imanin: barin abin da bai shafe shi ba, na magana da kallo, da sauarare, da taba (wani abu), da tafiya da tunani, da sauran al'amura na fili da na ɓoye.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) Wannan Hadisin ginshiki ne wurin cikar dabi'u a wurin musulmi, kuma alama ce da yake kawatuwa da ita a wurin 'yan uwa da makusanta.
2) Lallai a cikin barin abin da bai shafi mutum ba akwai tsare lokacinsa, da kubutar addininsa.
3) A cikin hadisin akwai zaburarwa akan ribatan lokaci wurin abin da zai amfani mutum; idan ya zama barin abin da bai shafi mutum ba yana cikin kyawun musuluncin mutum, to lallai shagaltuwa da abin da ya shafi mutum na cikin kyawun musuluncinsa.
4) Fifiko tsakanin Musulumi a cikin musulunci; da kuma cewa lallai yana ƙara kyau da wasu ayyuka.

---

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (2318).

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

MA'ANAR SHIRKA DA KARKASUWARTA

❖ Karkasuwar Shirka:

Shirk ta kasu kashi biyu:

Shirka babba mai fitarwa daga musulunci, da shirka ƙarama wacce ba ta fitarwa daga musulunci.

- **Babbar Shirka:** Shi ne daidaita wanin Allah da Allah cikin abin da ya kebanci Allah, kamar yadda Allah Ya bada labari game da mushrikai: ((Mun rantse da Allah, tabbas mun kasance (a duniya) cikin bata bayyananne. Lokacin da muke daidaita ku da Ubangijin talikai))[1].

Wannan kashin shi ne shirkar da Allah ba Ya gafarta shi; kamar yadda Ya fada: ((Lallai Allah ba Ya gafartawa a yi masa shirka, Yana kuwa gafarta abin da bai kai shirka ba ga wanda Ya ga dama. Duk wanda ya yi wa Allah shirka, to hakika ya bata manisanciyar bata))[2].

Daga cikin misalan ta na fili: karkatar da wani abu daga cikin nau'o'in ibada ga wanin Allah Maɗaukaki, kamar mutum ya roki wanin Allah, ko ya yi yanka ga wanin Allah, ko ya yi alwashi ga wanin Allah, ko ya nemi kusanci ga ma'abota kaburbura, ko aljanu da shaidanu da wani abu cikin nau'o'in ibada.

- **Ƙaramar Shirka:** Ita ce duk wani abu da ya zo a cikin shari'ah da sunan shirka amma bai kai matsayin babbar shirka ba. Wannan ya kunshi dukkan wata kafa ko hanya da za ta kai ga shirka babba, irin su niyoyi, da maganganu da ayyuka kamar riya da jiji da kai da chamfi.

---

[1]. [Ash-Shu'ara: 97-98].
[2]. [An-Nisa'i: 116].

❖ Bambanci tsakanin shirka babba da shirka ƙarama:

Nassoshi sun bayyana cewa akwai bambance-bambance tsakanin shirka babba da ƙarama, mafi muhimmanci:

1. Lallai shirka babba na fitarwa daga musulunci, ita kuwa karama ba ta fitar da mutum daga musulunci.
2. Ita shirka babba na dawwamar da ma'abocinta cikin wuta, shirka karama kuma ba ta dawwamar a wuta.
3. Babbar shirka na rusa dukkan ayyuka, ita kuwa shirka karama ba ta rusa dukkan ayyuka, sai dai tana rusa aikin da aka yi ta ne a ciki.
4. Shirka babba na wajabata kin mai yin ta gaba ɗaya, da rashin son sa, komai kusancin sa kuwa, amma ita shirka karama ana ki da adawa da mai aikata ta gwargwadon abin da ke tare da shi ne na shirkan, sai a so shi a jiɗance shi gwargwadon abin da ya ke da shi na tauhidi.
5. Ita shirka ƙarama na tauye imani ne, amma ita shirka babba tana warware imani ne ta bata shi baki ɗaya.

LARABA: DARASI CIKIN FIKIHU

SALLAR JAM'I

❖ Falalarta:

Musulmai sun yi ittifaki a kan cewa yin salloli guda biyar, cikin jam'i a masallaci yana daga cikin mafi girman ayyukan da'a, kuma alama ce babba daga cikin alamomin musulunci, nassoshi masu yawa sun zo da bayanin falala da girman ladan sallar jam'i. Daga ciki:

- Fadin Allah Madaukaki: ((Cikin wasu dakuna wadanda Allah Ya yi umurni a daukaka, a kuma ambaci sunanSa a cikinsu, (Wasu mazaje) suna tasbihi gare Shi a cikinsu safe da yamma. Wasu mazaje ne wandada kasuwanci da saye da sayarwa ba ya shagaltar da su daga ambaton Allah da kuma tsai da sallah da ba da zakka, suna jin tsoron ranar da zukata da idanuwa suke raurawa))[1].
- Da fadin Allah: ((Lallai mai raya masallatan Allah shi ne kawai wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, ya kuma tsayar da sallah, kuma ya ba da zakka, bai kuma ji tsoron wani ba sai Allah. To wadannan tabbas suna cikin shiryayyu))[2].
- Annabi (SAW) ya ce: (Sallar jam'i ta fi falala a kan sallar mutum daya da daraja ashirin da bakwai)[3].
- Da fadin Annabi (SAW): (Ana nunnuka sallar mutum a cikin jama'ah a kan sallarsa cikin dakinsa ko shagonsa da ninki ashirin da biyar; saboda idan ya yi alwala, ya kyautata alwalar, sannan ya fito zuwa masallaci, ba abin da ya fito da shi sai salla, babu wani taku da zai yi face an daga shi da daraja daya, kuma an yafe masa da wannan takun zunubi daya, idan kuwa ya yi sallar, Mala'iku ba za

---

1. [An-Nur: 36-37].
2. [At-Taubah: 18].
3. Bukhari: (645) Muslim: (650) ne suka rawaito shi

su gushe ba suna masa addu'a matukar yana wurin sallar (suna cewa): Ya Allah Ka ambace shi (Cikin mala'iku masu daraja da ke tare da Kai, Ya Allah Ka yi masa rahama) [1].

❖ Hikamar da ke cikinta:

Allah Ya shar'anta sallar jam'i ne don wasu maslahohi masu girma da alfanu na zahiri, daga ciki akwai:

- Sadar da zumunci tsakanin musulmi, da kauna da soyayyar juna tsakaninsu, da kau da kiyayya da yanke alaka da bakin ciki.
- Bayyanar da karfin musulmi da hadin kansu da taruwansu; wanda ke fusata makiyansu.
- Samun nishadi wurin aikata aiki na kwarai lokacin da musulmi ke kallon nishadin 'yan uwansa musulmi.
- Maƙwabta su san halin da da makwabtansu ke ciki; su gaida marasa lafiya, da jana'izar mamata, da taimakon mabukaci, da karantar da jahili.

❖ Hukuncinta:

Sallar jam'i a masallatai wajibi ne ga maza ban da mata da yara a sallolin biyar na yini da dare, dalili akan hakan:

- Faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma idan ka kasance a cikinsu, sai ka yi musu limancin sallah, to sai wata kungiya su tsaya tare da kai))[2].
- Da Faɗin Annabi (SAW): (Lallai mafi nauyin sallah ga munafukai it ace sallar isha'i da sallar asubahi, da kuwa sun san irin abin da ke cikin su (na falala) da sun halarce su ku da rarrafe ne. Kuma na himmatu akan in umurci a tada sallah, sai in umurci wani mutum ya jagoranci mutane sallah, sai ni da wasu mazajen dauke da

[1]. Bukhari: (647) Muslim: (694) ne suka rawaito shi
[2]. [An-Nisa'i: 102].

itacen wuta, mu nufi wasu mutanen da ba su halartan sallah (cikin jam'i), in kona musu gidajensu da wuta)[1].

- Da fadin Annabi (SAW) ga wancan makahon da bai da dan jagora zuwa masallaci: (Shin kana jin kiran sallah?" Ya ce: Eh. Ya ce masa: "To ka amsa)[2].

[1]. Bukhari: (644) Muslim: (651) ne suka rawaito shi
[2]. Muslim rawaito shi (653).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRAH

YAƘIN BANU ƘAINIƘA'I

❖ Tarihinsa:

Wannan yaƙi ya faru ne ranar Asabar a tsakiyar watan Shawwal, a shekara ta biyu na hijira, wato dai bayan shuɗewar nasarar da Musulmi suka samu a yaƙin Badar da ƙasa da wata ɗaya.

❖ Sabaɗan faruwarsa:

Wannan yaƙi ya kasance ne da ɗaya daga cikin ƙabilun Yahudawa a Madina, wato Banu Ƙainiƙa, waɗanda sun kasance 'yan kasuwa ne kuma masu buga zinari, dalilin yi musu ƙawanyar shine wata mata daga cikin Musulmi ta je wurin wani mai sana'ar buga zinari cikin yahudawa, sai bayahuden ya nemi ya yi mata wayo don ta buɗe fuskanta a kasuwa, sai ta ƙi, sai wani cikin yahudawan ya ƙulle mata tufafinta ta baya, tana miƙewa sai tsiraicinta ya bayyana, sai suka fashe mata da dariya, sai wani cikin Musulman da ke kasuwar ya kai mata ɗauki, ya kashe bayahuden da ya aikata haka, sai su ma yahudawan suka fusata, sai suka kashe shi musulmin[1].

❖ Abubuwan da suka faru a yaƙin:

Lokacin da Annabi (SAW) ya samu labarin warware alƙawarin da suka yi, da kuma ƙaruwan ƙiyayya a zukatansu, da bayyanar da adawa ga Musulmi, sai ya shirya rundunarsa, ya ɗaura wa Abu Lubabah Bashir ɗan Abdilmunzir alhakin kula da garin Madina, sai Annabi (SAW) ya tafi ya yaƙe su, ya kuma yi musu ƙawanya na tsawon sati biyu, adadinsu ya kai ɗari bakwai, har suka amince za su kasance ƙarƙashin shugabancin Musulmi, hakan ya faru ne a tsakiyan watan Zul-ƙa'ada.

---

[1]. Al-Biɗayah Wan-Nihayah: (5/319)

❖ Sakamakon yaƙin:

Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul ya je wurin Annabi (SAW) ya nema musu alfarma, ya kuma nace wa Annabi (SAW) a kan ya yafe musu, don sun kasance abokan ƙabilar Khazraj ne, shi kuwa shi ne shugaban Khazraj, sai Annabi (SAW) ya ƙyale su, amma kasancewar tsoro ya shiga zukatansu da yawa daga cikinsu sun fice zuwa Sham da Khaibar[1].

[1]. Al-Bidayah Wan-Nihayah (5/320).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABU HURAIRAH (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Abu Hurairah, Abdur-Rahman ɗan Sakhr Ad-Dausiy; ya fada game da sunansa da alkunyarsa: “Da sunana a jahiliyya Abdu Shamsin (Bawan Rana), sai Annabi (SAW) ya sa mini suna Abdur-Rahman, shi kuwa alkunyata Abu Hurairah, na kasance ina kiwon awaki ga mutane na, kuma ina da wata mage da na ke wasa da ita, sai suka mini alkunya da ita"[1].

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Abu Hurairah (RA) ya kasance mai farar fuska, ma’abocin gemu ja, mai saukin kai, da natsuwa, mai taushin hali, ya musulunta ne a shekara bakwai ta hijira, tsakanin yaƙin Hudaibiya da Khaibar, ya musulunta ne a garin sun a ‘Dausu’, a hannun Aɗ-Ɗufail dan Amr (RA), sannan ya taho Madina yana mai hijira.

Ya fada (RA): “Lokacin da na taho wurin Annabi (SAW) na fadi (wannan baitin waken): “Kai wannan dare, ga tsawo ga wahala, duk da dai yau (raina) ta tsira daga kasar kafirci”.

Wani bawa nawa ya gudu a kan hanya, da na iso wurin Annabi (SAW) na yi masa mubaya’a, kwatsam ina wurin Annabi (SAW) sai ga wannan bawana, sai Annabi (SAW) ya ce mini; “Abu Hurairah ga bawanka”. Sai na ce: “Na saɗaukar da shi don fuskar Allah, na ‘yanta shi”[2].

Abu Hurairah (RA), ya kasance cikin mutanen Suffah fakiran, mai lazimtar masallaci, mai hakuri da tsanani da rashi, ya ce: “Na gan ni

---

[1]. Siyarul A’lamin-Nubala (2/587).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (2531).

ina birgima tsakanin mimbarin Manzon Allah (SAW) da dakin A'ishah (RA), ina suma, wanda ya zo na iya daura ƙafarsa a wuyan, a yi tsammanin ko ni mahaukaci ne, ba hauka tare da ni, ba abin da ke damun face yunwa"[1].

Abu Hurairah (RA) ya kasance mafi haddace hadisan Manzon Allah (SAW) a cikin sahabbai, kuma ya fi su yawan hadisai, jagora ne, masanin fikihu ne, yana jin (hadisi) sai ya haddace, yana kuma saurare sai ya haddace. Imamul Bukhari ya ce game da shi: "Kimanin ma'abota ilim dari takwas ne suka ruwaito daga wurin sa, kuma shi ne mafi kaifin hadda cikin waɗanda suka ruwaici hadisi a zamaninsa"[2].

Musulmi sun hadu a kan son sa da girmama shi, da tsare matsayinsa da darajarsa, yana faɗa da bakinsa: "Wallahi ba wani musulmi da Allah Ya halitta da zai ji labari na face ya so ni." Aka tambaye shi: "Ta ya ya ka san haka?" Ya ce: "Mahaifiyata ta kasance mushrika ce, na kasance ina kiran ta ga Musulunci, ta na ki, wata rana ina kiran ta, sai ta jiyar da ni mummunar magana game da Manzon Allah (SAW), abin da ban ji dadi ba. Sai na je wurin Manzon Allah (SAW), ina kuka, na ba shi labarin abin da ya faru, na roke shi ya yi mata addu'a, ya ce: "Ya Allah Ka shiryi mahaifiyar Abu Hurairah" sai na wuce don in mata albishir, ina zuwa na taras da kofa a rufe, sai na jiyo ƙarar ruwa, sai ta ji alamar motsina, sai ta ce: 'Tsaya inda ka ke.' Sannan daga baya ta buɗe kofa tana sanye da silkenta da ta gaggauta sa mayafinta, sai ta ce: "Na shaida babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma lallai Muhammad bawan Allah kuma manzonSa ne", sai na koma wurin Manzon Allah (SAW), ina kuka saboda murna, kamar yadda na yi kuka saboda baƙin ciki, na ba shi

[1]. Bukhari: 7324]
[2]. [At-Tazkirah Na Zahabi (1/33)

labari, sai na ce: “Ka roƙa Allah Ya sa so na da na mahaifiyata ga bayinsa muminai.” Sai Annabi (SAW) ya ce: (Ya Allah Ka sa son wannan bawan naka da mahaifiyarsa ga bayinKa muminai, ka sa soyayyarsu gare su)[1].

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu ne a wurin da ake kira Al-Aƙik, a shekara ta hamsin da tara, yana ɗan shekara saba’in da takwas, sai aka ɗauke shi zuwa Madina, sarkin Madina Walid ɗan Utbah ɗan Abu Sufyan ya yi masa sallah.

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2491)

Auna Fahimtarka a cikin darussan mako na 25				Amsa ta ƙwarai
Darasin tafsir	**Tambaya: Menene ma'anar "Fansab"?**			C
	[a] Ka yi ƙoƙari wurin neman arziki	[b] Ka dogara ga Allah	[c] Ka dage a cikin ibada	
Darasin hadisi	**Tambaya: Daga cikin kyawun musuluncin mutum:**			B
	[a] Ya bar abin da ya shafe shi ba	[b] bar abin da bai shafe shi ba	[c] Ya bar abin da bai shafe shi ba	
Darasin akida	**Tambaya: Mai aikata shirka babba:**			B
	[a] Za a auna kyawawan ayyukansa da munana	[b] Allah ba zai gafarta masa ba	[c] In Allah Ya ga dama zai gafarta masa, ko kuma ya azabtar da shi	
Darasin fikihu	**Sallar maza a cikin jam'i a masallaci, sau biya:**			A
	[a] wajibi ne	[b] mustahabbi ne	[c] sharadi ne	
Darasin sira	Tambaya: Yaƙin Banu Kainuka' ya faru ne bayan yaƙin:			A
	[a] Badar	[b] Uhudu	[c] Khandak	
Darasin tarihin sahabbai	**Tambaya: Sunan Abu Huraira a lokacin Jahiliyya:**			C
	[a] Abdul-Ka'aba	[b] Abdul-Uzza	[c] Abdu-Shams	

MAKO NA ASHIRIN DA SHIDA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIR

SURATUSH-SHAMS

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلشَّمۡسِ وَضُحَىٰهَا ۝١ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا تَلَىٰهَا ۝٢ وَٱلنَّهَارِ إِذَا جَلَّىٰهَا ۝٣ وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰهَا ۝٤

وَٱلسَّمَآءِ وَمَا بَنَىٰهَا ۝٥ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا طَحَىٰهَا ۝٦ وَنَفۡسٖ وَمَا سَوَّىٰهَا ۝٧ فَأَلۡهَمَهَا فُجُورَهَا

وَتَقۡوَىٰهَا ۝٨ قَدۡ أَفۡلَحَ مَن زَكَّىٰهَا ۝٩ وَقَدۡ خَابَ مَن دَسَّىٰهَا ۝١٠ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ بِطَغۡوَىٰهَآ ۝١١ إِذِ

ٱنۢبَعَثَ أَشۡقَىٰهَا ۝١٢ فَقَالَ لَهُمۡ رَسُولُ ٱللَّهِ نَاقَةَ ٱللَّهِ وَسُقۡيَىٰهَا ۝١٣ فَكَذَّبُوهُ فَعَقَرُوهَا فَدَمۡدَمَ

عَلَيۡهِمۡ رَبُّهُم بِذَنۢبِهِمۡ فَسَوَّىٰهَا ۝١٤ وَلَا يَخَافُ عُقۡبَٰهَا ۝١٥﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin Kai

1. Ina rantsuwa da rana da walharta.
2. Da kuma wata idan ya bi ta (wato ranar).
3. Da kuma wuni idan ya bayyana ta.
4. Da kuma dare idan ya lullube ta.
5. Da kuma sama da gininta.
6. Da kuma kasa da shimfidarta.
7. Da kuma rai da daidaitarsa.
8. Sai Ya kimtsa masa (gane) lalacewarsa da takawarsa.
9. Hakika wanda ya tsarkake shi (ran) ya rabauta.
10. Hakika kuma wanda ya ɗanne shi da sabo ya tabe.
11. Samudawa sun karyata saboda dagawarsu.
12. Yayin da mafi tsagerancinsu ya zabura.
13. Sai Manzon Allah ya ce da su: “Ku bar taguwar Allah da (ranar) shanta”.
14. Sai suka karyata shi sannan suka soke ta, sai Ubangijinsu Ya kama su da azaba saboda zunuɗansu.

15. Kuma ba Ya tsoron abin da zai biyo bayanta.

❖ **Saƙon da Surar ke ɗauke da shi:**

Ƙarfafa muhimmancin tsarkake rai da ayyukan da'a da rantsuwa mafi tsawo, da hasarar wanda ya gurɓata ta da ayukan sabo.

❖ **Bakin Kalmomi:**

تلاها	Talaha	Ya bi rana wurin bullowa	فألهما	Fa Alhamaha	Ya bayyana mata
جلاها	Jallaha	Ya yaye duhun dare, ya kauda shi	فجورها	Fujuraha wa tak-waha	Hanyar alkhairi da hanyar sharri
يغشاها	Yagshaha	Yana rufe kasa da duhunsa	زكاها	Zakkaha	Ya tsarkake ta ya kuma habbaka ta da da'a
طحاها	Ɗahaaha	Ya shimfida ta	خاب	Khaba	Ya yi hasara
سواها	Sawwaaha	Ya cika halittar ta	دساها	Dassaha	Ya boye ransa kuma ya tauye ta da ayyukan sabo
بتقواها	Bi Taƙwaaha	Saboda dagawarsu da wuce iyakarsu a cikin sabo	فدمدم	Fa damdama	Ya saukar musu da ukuba
ناقة الله	Nakatallahi wa suk-yahaa	Ku kiyayi taguwar Allah, kar ku cutar da ita, ko ku yi ta'addanci ga abin shayarwanta	فسواها	Fa Sawwaaha	Ya game su da uƙuba; ba wanda ya kubuce mata cikin su

فعقروها	Fa Aƙaruuha	Sai suka yanka ta	عقباها	Uƙbaha	Ƙarshen abin da ya sauka gare su.

❖ Ma'anar Surara a Dunƙule:

Wannan surah ce makkiya, Allah Maɗaukaki Ya rantse a farkon ta da halittunsa masu girma, waɗanda ke nuni ga cikar ƙudirarsa Maɗaukaki da kaɗaituwarsa, Ya rantse a kan tsiran wanda ya tsarkake ransa,Ya kuma tsaftace ta da imani da da'a, da kuma hasarar wanda ya tozarta ta da kafirci da saɓo.

Sai Allah Ya buga misali ga hakan da Samudawa, da irin abin da ya sauka gare su; don dukkan wani mai ƙaryatawa, mai kangara ya dau izina da su, don kuwa su din da suka karyata Manzonsu, suka yanka taguwa, sai Allah Ya halakar da su dukkan su, kuma Shi Allah ba Ya tsoron ƙarshen halakan su da abin da ya sauka gare su; don kuwa ba a tambayar Shi game da abin da Ya aikata, kuma Ya saukar musu abin da suka cancanta.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1. Muhimmancin tsarkake rai da tsaftace ta daga munanan niyya da ayyuka da ɗabi'u.
2. Lallai Allah Maɗaukaki Ya halicci ran dan'adam a shirye ta ke ta karɓi alkhairi ko sharri, ga ikon tantance ɗayan hanyoyi biyu (mai kyau da mara kyau).
3. Lallai zunubbai sababban uƙubobi ne a duniya.
4. Lallai masu taimakekeniya a kan saɓo suna tarayya cikin zunubi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

KARHANCIN YAWAITA MAGANA DA TAMBAYA DA LALATA DUKIYA

An karɓo daga Abu Hurairah (RA), ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lallai Allah Ya yardar muku abubuwa uku, Ya kyamatar muku abubuwa uku; Ya yardar mu ku bauta masa Shi kaɗai, kar ku haɗa Shi da kowa, kuma ku riƙe igiyar Allah dukkanku, kuma kar ku rarrabu, Ya kuma kyamatar muku an ce, ya ce, da yawan tambaya, da tozarta dukiya)[1].

❖ Sharhi:

A wannan Hadisin an tabbatar da siffar yarda ga Allah, da abubuwan da ke kewaya da ita, kuma an tabbatarwa Allah da ki, da abubuwan da ke kewaye da ita; daga falalar Allah da karamcinSa ga bayinsa shi ne Ya umurce su kuma Ya yardan musu abin da akwai maslaharsu, da farin cikinsu a nan duniya da kuma lahira; na tsayuwa da bauta masa ba tare da abokin hadi ba, da tsarkake addini gare Shi, kuma su riƙe igiyarsa, wanda ita ce addininSa da ya ke tsani ne tsakaninsa da bayinsa, sai tsayu da shi suna masu haɗa kai a kan ɗa'a da taƙawa.

Haka kuma Allah Ya kiwa bayinsa duk abin da zai sadar da cutuwa gare su, kuma a cikin sa akwai taɓewar su a nan duniya da lahira, daga cikin haka: "yawaita an ce ka ce" don kuwa yana daga abin da ke jawo ƙarya, da faruwan fitintinu, da saɓani tsakanin zukata, da shagaltuwa da abubuwa marasa amfani a kan masu amfani, haka kuma Allah Ya ƙyamaci 'yawan roƙo' kamar roƙon dukiya da duniya ba tare da bukata ba ko lalura, da kuma tambayar ilimi ta fuskan ta'annuti da gajiyarwa, haka kuma Ya kiwa bayinsa 'tozarta dukiya'

[1]. Muslim: ne ya rawaito shi (1715)]

ko dai ta hanyar barin ta ba tare da an tsare ta ba, har a sace ko ta salwanta, ko kuma ta hanyar ciyar da ita cikin al'amura da ke cutarwa, ko marasa amfani.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1. Tabbatar wa Allah siffar yarda, ta yadda ya dace da girmansa da ɗaukakarsa.
2. Son da Allah Ya ke yiwa a kaɗaita shi, wanda kuma shi ne manufar halittan aljanu da mutane.
3. Wajibcin takatsantsan daga shirka, babba ce ko ƙarama.
4. Muhimmancin riƙo da addini, da haɗuwan bayin a kai, da taimakekeniyarsu a kan ɗa'a da taƙawa.
5. Wajibcin kiyaye harshe daga maganar cikin abin da bai da amfani.
6. Muhimmancin kwaɗayi wurin tsare dukiya da kuma ciyar da ita cikin al'amura masu amfani.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

MISALAN SHIRKA ƘARAMA

Shirka karama na da misalai masu yawa, wanda bayanin su ya zo cikin Al-ƙur'ani da Sunnah, daga ciki:

1. **(Riya):** Shi ne bayyanar da ibada da nufin mutane su ga ni, don su yaɓi mutum a kai, wannan shirka ne cikin niyoyi da manufofi, kuma yana kore kamalar tauhidi, kuma yana rusa aikin da ya gwamu da shi, kuma hatsarin riya ga wannan al'ummar ya fi hatsarin Dujal; don ɓoyuwarsa, da mummunar tasirinsa, Annabi ya ce (SAW): (Mafi tsoron abin da na ji muku tsoro shi ne shirka karama) Su ka ce: (Mece ce shirka ƙarama, ya manzon Allah?' Ya ce: (Riya) [1].
2. **Rantsuwa da Wanin Allah:** saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Duk wanda ya yi rantsuwa da wanin Allah ya kafirta ko kuma ya yi shirka)[2], ya kuma ce: "Lallai Allah Ya hane ku ku yi rantsuwa da iyayenku"[3].
3. **faɗin Allah "Ba don allah ba da kai" ko "Allah ya ga dama, kai ma ka ga dama" ko "Ban da wani sai allah sai kai" ko "Wannan daga albarka allah ne da albarkarka"**: Abin da ya ke daidai shi ne a ce: "Ba don allah ba, sannan kai", da "allah ya ga dama, sannan kai ma ka ga dama" da makamantan haka, sai a sa ganin damar bawa ta zama bayan ganin damar Allah, don harfin (wawun) "da" a Hausa)) a harshen larabci yana fa'idantar da daidaito da haɗaka, amma kalmar (summa "sannan" a Hausa)) yana fa'idantar da jerantawa da jinkiri; Abdullahi ɗan Abbas (RA) ya ce game da faɗin Allah: ((Kada ku sanya wa Allah kishiyoyi alhalin kuna sane)) [4]. "Kishiyoyi shine shirka, wanda ya ke a ɓoye fiye da

---

[1]. Ahmad (23680) da Ɗabarani (4301) ne suka rawaito shi.
[2]. Tirmizi (1535) da Abu Dawud (3251) ne suka rawaito shi.
[3]. Bukhari (6647) da Muslim: (1646) ne suka rawaito shi.
[4]. [Al-Baƙarah: 22]

takun tururuwa a kan baƙin dutse cikin duhun dare, shi ne mutum ya ce: ‘Na rantse da Allah da rayuwarka ya kai wane’, ko ‘na rantse da rayuwata’ kuma ya ce: ‘Ba don wannan karyar ba da ɓarayi sun shigo mana (gida) jiya’. ‘Ba don agwagin da ke gidan nan ba da barayi sun zo’, da faɗin mutun ga abokinsa: "Allah Ya ga dama, kuma kai ma ka ga dama’, da faɗin: ‘Ba don Allah da wane ba"[1].

4. **Sanya Laya da Kambu da Guru**: Don yaye bala’i ko tunkuɗe shi, ko don tsoron kambun baka ko aljanu, wannan duk shirka ne karami, don yin hakan ba sababi ba ne na shari’ah ko kuma na yadda Allah Ya ƙaddara. Duk waɗannan ƙarerayi ne ga shari’ah da kuma ƙaddara, wanda mai aikata su ba zai kubuta daga ratayuwar zuciyarsa gare su ba wurin son wani abu ko tsoron wani abu.

5. **Mutum Ya Nufi Manufar Duniya da Wani Aiki da Ake Yi Don neman yardar Allah:** shi ma shirka ne karami, kuma yana rusa ladan aikin da ya faru a cikin sa, kamar wanda ya yi aikin hajji ko ya kira sallah ko ya limanci mutane don kudi, ko ya koyi ilimi na addini don a ambace shi ko a ji shi, Annabi ya ce (SAW): (Bawan dinari ya halaka, bawan dirhami ya halaka, bawan tutafi ma ya halaka, bawan katifa ma ya halaka; inda an ba shi sai ya yarda, idan aka kuwa ba a ba shi ba sai ya yi fushi)[2].

[1]. Ibnu Abi Hatim (230) ne ya rawaito shi.
[2]. Bukhari: (2887) ne ya rawaito shi.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

HUKUNCE-HUKUNCEN LIMANCI DA SALLAR JAM'I

Limanci da sallar jam'i na da hukunce-hukunce masu yawa, ya kamata musulmi ya san su, ya kuma ladabtu da su, daga cikin su:

1. Mustahabbancin kusantar da ma'abota hankali da fahimta kusa da liman, su ne ma'abota falala da hankali da hakuri da bi sannu, sai su kasance kusa da liman a bayan sa, saboda Annabi (SAW) ya ce: (Ma'abota hankali da tunani su biyo bayana, sannan waɗanda suke ɗan su, sannan waɗanda suke bi musu) [1]. Hikimar da ke cikin hakan shi ne: su tada liman a karatu idan bukatar hakan ta kasance, kuma zai iya maye wani cikinsu idan wani abu ya same shi.
2. Ba ya inganta yin nafila bayan tada ikamar farilla, idan ladan ya fara iƙamar sallah, ba ya halatta ga wani ya fara sallar nafila, saboda Annabi (SAW): (Idan an tsaida sallah to ba wata sallah sai ta farilla) [2]. Amma idan an tsaida sallar ne bayan ya riga ya fara nafilars to sai ya cika ta ba tare da tsawaitawa ba, kuma zai iya yanke ta ma.
3. Ba ya inganta mutum ya yi sallah shi kadai tilo a bayan sahu, saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Ba sallah ga mutum shi kadai bayan sahu)[3]. Haka kuma Annabi (SAW) ya ga wani mutum yana sallah shi kaɗai a bayan sahu, sai ya umurce shi da ya sake sallah[4], domin wajibi na faduwa in akwai ajizanci.
4. Idan liman ya yi rafkanuwa a sallarsa; sai maza su yi tasbihi, su kuma mata su yi tafi, Annabi ya ce (SAW): (Tasbihi na maza ne, tafi kuma na mata ne) [5].

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (432).
[2]. Muslim ne ya rawaito (710).
[3]. Ahmad (4/23) da Ibnu Maja (1003) ne suka rawaito shi.
[4]. Ahmad (4/228) da Abu Dawud (682) ne suka rawaito shi.
[5]. Bukhari (1203) da Muslim (422) ne suka rawaito shi.

5. Idan liman ya tashi zuwa ga wata raka'a ta kari, to wadanda ke bayan sa ba za su bi shi ba, kawai za su yi tasbihi ne, su jira shi ya zauna, duk wanda ya tsaya yana sane sallarsa ta baci.
6. Idan liman ya kuskure wurin karatu, to mahaddaci mafi kusa da shi ne zai tada shi, bai kamata a yi yamutsa wurin da yawan sautuka.
7. Abin da ya ke sunnah shi ne masbuki ya shiga sallah a duka halin da ya taras da liman; a tsaye ne ko a ruku'u ko sujada ko makamancinsa.
8. Idan masbuki ya shigo sallah alhali liman na halin ruu'u, to za iyi kabbarar harama a tsaye, sannan ya yi kabbara ta biyu sai ya yi ruku'u; don ita kabbarar harama dole ne a yi ya a tsaye, amma kabbarar ruku'u an sunnanta a yi ta ne bayyana kabbarar harama, idan ya wadatu da kabbarar harama kawai hakan ya wadatar da shi daga yin kabbarar ruku'u.
9. Idan liman ya gama sallama ta biyu, sai masbuki ya tashi don kawo abin da ya kubuce masa na sallah, yana cikin kuskure abin da was uke aikatawa na yayin da liman ya ke sallama, wannan ba ya halatta.
10. Idan wasu mutane sun yi jinkirin halarta jam'i tare da limami ratibi, kuma sallah ta kubuce musu, ya halatta gare su su yi jam'i na biyu a wannan masallacin, saboda gamewar fadin Manzo (SAW): (Sallar mutum tare da wani ya fi tsarki fiye da sallarsa shi kadai) [1].
11. Idan wanda ya zo a makare shi kadai ne, to an so ga wani daga cikin wadanda suka yi sallah su yi sallar tare da shi da niyyar nafila; saboda fadin Annabi (SAW) ga wani mutum da ya halarci masallaci bayan an gama jam'i: (Wa zai yi sadaka ga wannan ya yi sallah tare da shi?) Sai wani mutumi ya mike ya yi sallah tare da shi[2].

[1]. Abu Dawud: (554) da Nasa'i (2/104) ne suka rawaito shi.
[2]. Tirmizi (220) da Ahmad (3/5) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRAH

YAƘIN UHUƊU

❖ Tarihin Yaƙin:

Yaƙin Uhuɗu ya faru ne a ranar bakwai ga Shawwal, a shekara ta uku da hijira.

❖ Sabuban Faruwar Yaƙin:

Kuraishawa sun kasance sun kunshi haushi bayan faduwar su a yaƙin Badar, da kashe musu manyan mayakansu, wannan ya sa suka dau azama akan dawo da martabarsu tsakanin sauran ƙabilu, da kuma ɗaukan fansa daga Annabi (SAW) da musulmai.

❖ Abubuwan da suka Faru a Yaƙin:

Abu Sufyan ya fara tara Ƙuraishawa, yana karfafa su ga yaƙar Musulmi, ya tara kusan mayaka dubu uku, tare da su akwai dawakai dari biyu, da sulke dari bakwai, da rakuma dubu uku, su ka taho da matansu don kar ma su gudu, ya fuskanto garin Madina, ya sauka kusa da Uhuɗu.

Lokacin da Annabi (SAW) ya ji labarin hakan, sai ya nemi shawarar sahabbai; shin musulmi za su je su same su ne ko kuma su zauna a Madina? Sai wasu cikin su cikin waɗanda yaƙin Badar ya kubuce musu suka bada shawaran a fita zuwa inda suke, wasu kuma suka bada shawarar a tsare Madina, kuma a yi yaƙin a cikin ta, sai ‘yan farkon suka nacewa Annabi (SAW), sai ya shiga gidansa, ya sanyi sulken yaƙinsa, ya fito gare su, yana mai tattara azamarsa, sai suka ce: “In kuma ka so ka zauna a Madina, to ka zauna.” Sai Annabi

(SAW) ya ce: (Ba ya kamata ga wani Annabi ya sanya sulken yaƙi ya cire har sai ya yi yaƙi)[1].

Sai ya shugabantar da Ibnu Ummi Maktum (RA) ga Madina, ya fita da mayaka dubu, da sulke dari, da dakuna hamsin, ya raba su bataliya uku: bataliyan muhajirai wanda tutarsu ke tare da Mus'ab ɗan Umair, da bataliyan Aus wanda tutarsu ke tare da Usaid ɗan Hudair, da bataliyan Khazraj, tutar su kuma na wurin Hubab ɗan Munzir.

A kan hanya munafikin Allah, Abdullahi ɗan Ubayyu ya dawo da kimanin mabiyansa su dari uku, yana mai hakikancewa cewa Annabi ya ki don ra'ayinsa! Sai Annabi (SAW) ya ci gaba da tafiya tare da waɗanda suke tare da shi har suka isa duwatsun Uhud, sai ya baiwa dutsen baya, ya daura maharba su hamsain, shugabansu shine Abdullahi ɗan Jubair (RA), ya ce musu: "Ko da kun ga mu tsuntsaye na tsintar namanmu, kar ku bar wannan wurin har sai na aiko gare ku, kuma ko da kun ga mun yi nasara akan maƙiya, mun take su, kar ku bar wannan wurin har sai na umurce ku da hakan"[2].

Sai aka fara yaƙi, a farkon yini kuwa nasara ta kasance ga Musulmi, sai maharban suka ce: Ya jama'ah, ga fa ganima, ma'abocinku fa ya yi nasara, me ku ke jira? Abdullahi ibn Jubair (RA) ya ce: "Kun manta da abin da Manzon Allah ya ce ne?" Suka ce: Wallahi sai mun je wurin mutanen, mu ma mu samu ganima[3], sai suka sauka daga wurin da aka tsayar da su, sai mayaka mushrikai suka hango wannan giɗan, suka biyo suka wuce ta, nan kuwa abin da Allah Ya nufa na saukar jaraba ga musulmi ya kasance!

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi ba tare da isnadi ba (7369).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (3039).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (3039).

❖ Sakamakon yaƙin:

Kusan Musulmi saba'in ne suka yi shahada, daga cikin su akwai Hamzah da Abdullahi dan Jahash, da Mus'ab dan Umair (RA), har mushrikai suka kai ga Annabi, sai wasu mutane goma cikin musulmi suka shiga tsakanin su da shi, har aka kashe su, sannan sai Dalha ga yo kan su mushrikan har ya kore su daga wurin sa, shi kuma Sa'ad ibn Abi Waƙƙas ya yi ta harbi kuma yana dacewa, sai Annabi (SAW) ya ce masa: (Harbe su, babana da mamata fansa ne gare ka) [1]. kuma an jiwa Manzon Allah (SAW) ciwo a fuskarsa mai daraja, aka karya masa hakoran gaba na kasa da dutse, aka masa rotse a kai, mushrikai suka yi ta jifansa har ya fadi kasa, wasu karafa biyu daga hulan ƙwano suka shiga fuskar Manzo (SAW), sai Abu Ubaida[2], ya zare su, Malik ibn Sinan ya tsotse jini daga ciwonsa[3], har Annabi (SAW) ya yi ƙoƙarin ya hau wani dutse anan ya kasa, sai Dalha ya zauna a kasansa har Annabi (SAW) ya hau[4], har lokacin sallah ya yi, ya yi sallah a zaune[5]. sai labari ya yaɗu a cikin musulmi cewa an kashe Manzon Allah (SAW), haka har sai da ya fuskanto, Ka'ab ɗan Malik ne ya fara gane shi a cikin hulan ƙwano, sai ya yi shela da babbar murya: 'Ya ku musulmi, albishirinku, ga Manzon Allah nan!', sai Annabi (SAW) ya yi masa ishara da ya yi shiru[6], sai Musulmai suka taru a wurinsa, sai Ubayyu dan Khalaf ya taho akan ingarman doki, da nufin kashe Manzon Allah (SAW), sai Annabi (SAW) ya ɗauki wani mashi, ya jefa shi a makoshinsa, ya faɗo, haka ya mutu a kan hanyarsa ta komawa Makkah[7].

---

[1]. Bukhari: (4057) da Muslim: (2412) ne rawaito shi
[2]. [Siyaru A'alamin-Nubala: (1/8).
[3]. Tarikhul-Islam: (2/193).
[4]. Tarikhul-Islam (2/193).
[5]. Al-Biɗayah Wan-Nihayah (5/415).
[6]. Al-Biɗayah Wan-Nihayah (5/411).
[7]. Hakim ne ya rawaito shi (3263).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI USAMA ƊAN ZAID (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Sahabi mai daraja Usama ɗan Zaid ɗan Harisa ɗan Sharahil, bararren bawan Manzon Allah (SAW) kuma masaoyinsa, ana masa alkunya da Abu Muhammad, an haife shi ne a Makkah shekara ta bakwai kafin hijrah.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Usama (RA) ya kasance da ne ga wasu musulmai biyu masu karamci, suna cikin farkon musulmai waɗanda suka riga musulunta, kuma suka fi su soyayya ga Manzon Allah (RA), da kusanci sosai gare shi, su ne: Zaid ɗan Harisa, hadimin Annabi (RA) da Ummu Aiman wacce ta raini shi.

Usama ya samu falalar Annabi (SAW) ne ya raine shi tun yana karami, kuma ya so shi sosai, har ya kasance Annabi (SAW) yana daukan sa shi da Husain ya ce: (Ya Allah, ina son su Ka so su)[1].
Haka kuma Usama ya yi fice duk da ƙarancin shekarun da da jarumta da hikima, Annabi (SAW) ya jagorantar da shi yana dan shekara goma sha takwas, akan rundunar da ta yaƙi Sham, kuma cikin rundunar akwai manyan Muhajirai da Ansarawa, daga cikin su akwai Abubakar da Umar, Annabi (RA) ya rasu kafin rundunar ta motsa, sai Abubakar Allah Ya kara masa yarda ya zarta da ita[2].

❖ Rasuwarsa:

Usama (RA) ya rasu a ƙarshen mulkin Mu'awiya (RA), shekara ta 54 na hijira, an kuma birne shi a maƙabartar Baƙi'a.

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (3747).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (3730).

Auna Fahimtarka a cikin darussan mako na 26				Amsa ta ƙwarai
Darasi cikin tafsiri	**Tambaya: Suratush Shams na karafa:**			C
	[a] Falalan jihadi da ladansa	[b] Falalan sadaka da ciyarwa	[c] Muhimmancin tsarkake rai da ayyukan da'a	
Darasi cikin hadisi	**Tambaya: Daga cikin aɗanda Allah Ya ki wa bayinSa; wulakanta dukiya, hakan na faruwa ne:**			A
	[a] Ta hanyar kashe su wurin abubuwa masu cutarwa ko marasa amfani	[b] ta hanyar ciyar da shi ga waɗanda ba iyalai da 'yan uwa ba	[c] Ta hanyar ciyar da shi ga waɗanda ba iyaye da 'ya'ya ba	
Darasi cikin aƙida	**Tambaya: Rantsuwa da ba da Allah ba, ana kirga shi a matsayin:**			B
	[a] Shirka babba	[b] Shirka karama	[c] Karamin zunubi	
Darasi cikin fiƙihu	**Tambaya: An so su yi sallah bayan liman:**			C
	[a] Yara kanana	[b] Makwabtan masallaci	[c] Ma'abaota hankali da basira	
Darasi cikin sira	**Tambaya: Musibu sun afkawa musulmi lokacin Uhud saboda:**			B
	[a] Dawowan Ibn Salul	[b] Sabawa umurnin Manzo da maharba suka yi	[c] Basirar Abu Sufyan	
Darasi cikin sahabbai	**Tambaya: Usama dan Zaid ya kasance an san shi:**			A
	[a] Masoyin Manzon Allah	[b] Mai gadin Manzon Allah	[c] Wanda Mala'iku su ka yiwa inuwa	

MAKO NA ASHIRIN DA BAKWAI

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-LAIL

سمحبِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَغۡشَىٰ ١ وَٱلنَّهَارِ إِذَا تَجَلَّىٰ ٢ وَمَا خَلَقَ ٱلذَّكَرَ وَٱلۡأُنثَىٰٓ ٣ إِنَّ سَعۡيَكُمۡ لَشَتَّىٰ ٤
فَأَمَّا مَنۡ أَعۡطَىٰ وَٱتَّقَىٰ ٥ وَصَدَّقَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٦ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلۡيُسۡرَىٰ ٧ وَأَمَّا مَنۢ بَخِلَ
وَٱسۡتَغۡنَىٰ ٨ وَكَذَّبَ بِٱلۡحُسۡنَىٰ ٩ فَسَنُيَسِّرُهُۥ لِلۡعُسۡرَىٰ ١٠ وَمَا يُغۡنِي عَنۡهُ مَالُهُۥٓ إِذَا
تَرَدَّىٰٓ ١١ إِنَّ عَلَيۡنَا لَلۡهُدَىٰ ١٢ وَإِنَّ لَنَا لَلۡأٓخِرَةَ وَٱلۡأُولَىٰ ١٣ فَأَنذَرۡتُكُمۡ نَارٗا تَلَظَّىٰ ١٤ لَا
يَصۡلَىٰهَآ إِلَّا ٱلۡأَشۡقَى ١٥ ٱلَّذِي كَذَّبَ وَتَوَلَّىٰ ١٦ وَسَيُجَنَّبُهَا ٱلۡأَتۡقَى ١٧ ٱلَّذِي يُؤۡتِي مَالَهُۥ
يَتَزَكَّىٰ ١٨ وَمَا لِأَحَدٍ عِندَهُۥ مِن نِّعۡمَةٖ تُجۡزَىٰٓ ١٩ إِلَّا ٱبۡتِغَآءَ وَجۡهِ رَبِّهِ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٢٠ وَلَسَوۡفَ
يَرۡضَىٰ ٢١ سجى

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin kai

1. Ina rantsuwa da dare idan ya lullube (da duhunsa).
2. Da kuma wuni idan ya bayyana.
3. Da kuma halittar namiji da mace.
4. Lallai aikinku ya sha bamban.
5. To wanda ya ba da (hakkokin da ke kansa) ya kuma yi takawa.
6. Ya kuma gaskata (sakamako) mafi kyau.
7. To lallai ne za Mu saukaka masa (hanyar) Aljanna.
8. Amma kuma wanda ya yi rowa (da hakkin Allah) ya kuma wadatu (da neman lada).
9. Kuma ya karyata (sakamako) mafi kyau.
10. To lallai ne za Mu hore masa (hanyar) wuta.

11. Dukiyarsa kuma ba za ta amfane shi ba idan ya gangara (cikin wuta).
12. Lallai bayyana hanyar shiriya a kanmu yake.
13. Kuma lallai lahira da duniya namu ne.
14. Don haka ina yi muku gargadin wata wuta mai ruruwa.
15. Ba mai shigar ta sai mafi tsiyacewa.
16. Wanda ya karyata ya kuma ba da baya.
17. Kuma lallais za a nesantar da mafi takawa daga gare ta.
18. Wanda yake ba da dukiyarsa yana neman tsarkaka.
19. Ba kuwa wani da ya yi masa wata ni'ima da za a saka masa (a kanta)
20. Sai dai don neman Fuskar Ubangijinsa Madaukaki.
21. Kuma lallai zai yarda (da sakamakon da za a ba shi).

❖ Sakon da Surar ke ƙunshe da shi:

Bayanin halayen halittu game da imani da Allah, da ciyarwa a tafarkinSa, da halin kowane mutane.

❖ Bakin Kalmomi:

يغشى	**Yagshaa**	Yana lullubewa kasa da duhunsa	بالحسنى	Bil Husna	Da lada ga ayyukansa
تجلى	**Tajalla**	Ya yaye da haskensa	لليسرى	Lil yus-ra	Dukkan alkhairi da farin ciki
لشتى	**Lashatta**	Ya sha bamban	للعسرى	Lil ursa	Dukkan wahala da tabewa
أعطى	**A'aƊa**	Ya bada dukiyarsa yana mai sadaka	وما يغني	Wa ma yugni	Ba zai amfane shi ba

تردى	Taradda	Ya auka cikin wuta	لا يصلاها	La Yaslaha	Ba zai shige ta ba, ya dandani zafinta
إن علينا للهدى	Inna Alaina lal huda	Bayyana hanyar shirya na kanmu ne, don falala da rahama daga gare mu.	وسيجنبها	Wa Sayujanna buha	Da sannu zai nuisance ta
تلظى	Talazza	Tana ruruwa	تجزى	Tujza	Za a masa tukuici; don ciyarwarsa ba tukuici ba ne ga wanda ya kyautata masa.

❖ Ma’anar Surar a Dunƙule:

Suratul Lail tana daga cikin surorin Makkah, Allah Ya yi rantsuwa uku a cikinta a jere a kan cewa ayyykan mutane sun bambanta, wasu cikin ayyukan shiriya ne, wasu kuma ɓata ne, duk wanda ya ciyar da dukiyarsa, kuma ya ji tsoron Ubangijinsa, yana mai gasgata kyakkyawan makomar a kan aikinsa, Allah zai sauƙaƙa masa aljanna, wanda kuwa ya yi rowa, kuma ya wadatu da dukiyarsa, ya kuma ƙaryata kyakkyawan makoma a kan aikinsa, Allah zai sauƙaƙa masa hanyar wuta, kuma dukiyarsa da ya yi rowar ta ba za ta amfane shi bai dan ya fada cikin azabar. Sannan Allah Ya ambaci cewa Ya ɗauki ragamar bayanin hanyar shiriya da falalarsa, kuma al’amarin rayuwa biyu nasa ne; rayuwar duniya da ta lahira, Ya na gudanar da su yadda Ya ga dama, sannan sai Allah Ya yi gargaɗi game da wuta ai ruruwa, wacce aka yi tanadin ta don taɓaɓɓu, masu takawa kuma suna tsira.

❖ **Abubuwan da za a koya daga Surar:**

1. Sakamako na kasancewa ne daidai da aiki; duk wanda ya kyautata a duniya, za a saka masa da mafi kyau a lahira.
2. Sunnar Allah Maɗaukaki shi ne Ya datar ga shiriya wanda ke kaunar shiriyar, ya kuma neme ta, ya yi kwaɗayi gare ta.
3. Ciyar da dukiya a tafarkin Allah sababi ne na ƙaruwansa da tsarkakansa, da samun lada mai girma a lahira.
4. Kwaɗaitarwa ga tsarkake rai da tsaftace ta da aiki na ƙwarai.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

ROƙONALLAH ALKHAIRIN DUNIYA DA NA LAHIRA

Daga Abdullahi dan Mas'ud (RA) ya ce: Annabi (RA) ya kasance yana wannan addu'ar: "Ya Allah ina roƙon Ka shirya, da taƙawa, da kamun kai, da wadata)[1].

❖ Sharhi:

Annabi (SAW) ya koya mana a cikin sunnoninsa masu yawa addu'o'in da ke jawo alkhairai da albarkatu, kuma suke tsarewa daga sharrori da bakin ciki; daga cikin su akwai wannan addu'ar, wacce ta ke daga cikin dunkulallun addu'o'i da masu amfani sosai; saboda ta tattaro roƙon Allah alkhairan addini da duniya; saboda shiriya it ace ilimi mai amfani, takawa kuma ita ce aiki na ƙwarai, kuma da su ne addini ke inganta. Shi kuwa kamun kai shi ne barin dogaro ga abin da ke hannun halittu, wadata kuma ita wadatuwa da Allah da ƙana'a da arzikinsa, wanda da su ne duniya ke kyautatuwa.

Don haka duk aka azurta da shirya, da taƙawa, da kamun kai, da wadata; rayuwa daddata za ta tabbatu gare shi, zai kuma samu jin dadi biyu na duniya da lahira, kuma zai sami duk abin nema, zai kuma kubuta daga dukkan abin tsoro.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin

1. Yakamata Musulmi ya dage wurin yin addu'o'in da Annabi ya karantar; domin lafuzzanta taƙaitattu ne, ga yalwar ma'ana, da tattaro alkhairi mai yawa.
2. Samun ilimi mai amfani da aikin na ƙwarai na cikin manyan ni'imomi da Allah ke yi wa bawa.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2721).

3. Lallai wanda ke mallakar amfani da cuta da shiriya shi ne Allah Shi kaɗai, ba wani mala’ika makusanci ba, ko Annabi manzo ba, ko waninsu ba.

TALATA: DARASI CIKIN AKIDA

DALILAI DA HUJJOJI A KAN ƁACIN SHIRKA

Dalilai da hujjoji bayyanannu da ke nuni a kan ɓacin shirka da zargin ma'abotanta suna da yawa, kuma mabambanta ne, ga wasu daga ciki:

Na Farko: Lallai kyautata halittan duniyar sama da na ƙasa, da yadda yake a tsare tunda aka halicce shi, da yadda ya ke jere, da yadda sashe ke hade da sashe wurin kyau da cika, da yadda aka hore sa don amfanin halittu dukkansu, dalilin ne a kan cewa mai gudanar da shi Ɗaya ne, kuma Ubangijinsa ɗaya ne, abin bauta ɗaya ne, babu wani abin bauta in ba Shi ba, kuma babu Mahallici sai Shi, kamar yadda Allah Ya faɗa: ((Ba za ka ga wata tangarda ba a cikin halittar Allah Mai rahama ba))[1].

Da faɗin Allah Madaukaki: ((Ko kuwa wane ne ya halicci sammai da kasa, ya kuma saukar muku da ruwa daga sama, sannan Muka tsirar da (shukokin) gonaki masu kayatarwa, ba kuwa za ku iya tsirar da bishiyoyinsu ba? Shin akwai wani abin bauta na gaskiya tare da Allah? A'a, su dai mutane ne da suke kauce wa gaskiya () Ko kuwa wane ne ya sanya kasa wurin zama, ya kuma sanya koramu a tsattsakinta, kuma ya sanya mata turaku, kana kuma ya sanya shamaki tsakanin kogunan nan biyu (na ruwan dadi da na ruwan zartsi)? Shin akwai wani abin bauta da gaskiya tare da Allah? A'a, yawancinsu dai ba sa ganewa))[2].

Na Biyu: Duk abin da ake bautawa koma bayan Allah mai rauni ne ta kowace fuska, kuma ajizi ne, gajiyayye, bai mallakawa kansa ko wanin sa amfani ko cuta ba, ko rayuwa ko mutuwa, ko bayarwa ko

---

[1]. [Al-Mulk: 3]
[2]. [An-Naml: 60-61].

hanawa, haka kuma ba ya siffantuwa da wata siffa daga cikin siffofin Allah Ubangijin gaskiya, to ta ya ya za bautawa wannan ya kasance haka?! Ta ya za a ƙaunaci alkhairi, ko a ji tsoron wanda wannan ne siffar shi, Allah Madaukaki Ya ce: ((Shin sa rika hada (Allah) da abin da ba ya halittar komai, hasali ma su ne ake halitta () Kuma ba za su iya taimaka musu ba, ba kuma za su iya taimaka wa kawunansu ba () Kuma in da za ku kirawo su zuwa shiriya, to Lallai ba za su bi ku ba. Duk daya ne a gare ku kun kirawo su, ko kuma kun yi shiru () Lallai waɗanda kuke kira ba Allah ba bayi ne kamarku, to ku kirawo su mana, sai su kuma su amsa muku idan kun kasance masu gaskiya ne () Shin wai suna da kafafun da suke tafiya da su ne; ko suna da hannayen da suke damka da su, ko kuma suna da wasu idanuwa da suke gani da su; ko suna da wasu kunnuwa da suke saurare da su? Ka ce: “Ku kirawo abokan tarayyarku, sannan ku shirya mini makirci kuma kada ku saurara mini () Lallai Majiɗancin lamarina Shi ne Allah Wanda Ya saukar da Littafi; kuma Shi Yake jiɗantar lamarin salihan bayi () Waɗanda kuke kira ba Shi ba kuwa, ba za su iya taimakon ku ba, kuma ba za su iya taimaka wa kawunansu ba () Kuma idan da za ku yi kiran su zuwa ga shiriya, to fa ba za su ji ba; kuma za ka gan su suna kallon ka, alhali kuwa ba sa gani)) [1].

Na Uku: Abu ne sannane ba shakka cewa bautan da mushrikai suke yi wa Annabawa ko salihai ko mala’iku, lallai su din da ake bautawa sun shagaltu daga barinsu ta hanyar buƙatuwan su a wurin Allah da aikin na ƙwarai, da rigegeniya wurin kusanci da Ubangijinsu; suna kaunar rahamarsa, suna tsoron azabarsa; to ta ya ya za a kuma bautawa wanda wannan shi ne halin sa? Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Waɗancan da suke bauta wa, su ma suna neman hanya ne zuwa ga Ubangijinsu, a cikinsu wa zai fi kusanci? Suna kuma ƙaunar

[1]. [Al-A’raf: 191-198]

rahamarsa, kuma suna tsoron azabarSa. Lallai azabar Ubangijinka ta kasance abar tsoro ce))[1].

Na Huɗu: Lallai Allah Maɗaukaki Ya bayyana cewa duk abubuwan da ake bautawa da ba Shi ba, sun cika sabubban kar amsawa masu kiran su, saboda dai su din ba su mallaki ko da daidai da kwayar zarra ba a cikin sammai ko a ƙassai, ba su mallaka komai ba a ƙashin kansu ba cikakken iko ko kuma ta hanyar haɗaka, babu wani cikin abubuwan bauta da ke taimakon Allah ko ya dafa masa a cikin mulkinsa ko a gudanar da al'amuransa, kuma ceto ba ta amfani a wurin Allah sai ga wanda Ya bada izini, Allah Madaukaki Ya ce: ((Ka ce: "Ku kirawo waɗanda kuka riya (cewa su ne iyayen giji) ba Allah ba;" ba sa mallakar wani abu daidai da kwayar zarra a cikin sammai ko a cikin kasa, ba kuma su da wata tarayya a cikinsu, ba Shi kuma da wani mataimaki daga cikinsu () Kuma ceto ba ya amfani a wurinSa sai ga wanda Ya yi wa izinin yin sa))[2].

[1]. [Al-Isra'i: 57].
[2]. [Al-Saba': 22-23].

LARABA: DARASI CIKIN FIKIHU

SUNNONI NA YAU DA KULLUM (RAWATIB)

❖ Falalar Sunnoni masu karfi da adadinsu:

Bayanin falalar sunnoni ratibai da fayyace adadinsu a cikin fadin Manzo (SAW) (Babu wani bawa musulmi wanda zai raka'a goma sha biyu domin Allah, a matsayin nafila ba farilla; face Allah Ya Madaukaki gina masa wani gida a aljanna: hudu kafin Azahar, da biyu bayan La'asar, da raka'a biyu bayan Magriba, da kuma raka'a biyu bayan I-sha', da kuma biyu kafin Asubahi)[1].

Mafi karfin wannan nafilolin shi ne: nafilar Asubahi, saboda fadin Manzon Allah (SAW): (Raka'a biyu na Al-fijir ya fi alkhairi fiye da duniya da adanda da ke cikinta)[2].

Da fadin A'ishah (RA): "Babu wani cikin nafilfili da Annabi (SAW) ya fi kula da ita irin yadda ya ke kula da raka'atal fajri"[3].

An shar'anta takaita ta, da karanta Suratul-Kafirun da Suratul-Ikhlas a cikinta[4].

Idan wata nafila ta kubuce wa musulmi, to an sunnanta masa ramuwa, saboda Annabi ya rama raka'atal fajri tare da sallar asubahi, lokacin da bacci ya dauke shi[5].

❖ Wurin da yin Nafila ya fi falala:

Yin nafila a gida – in hakan ya samu – shi ya fi falala a kan yin a masallaci, saboda fadin Manzo (SAW): "Ku sanya sallolinku (na

---

1. Muslim ne ya rawaito shi (728).
2. Muslim ne ya rawaito shi (725).
3. Bukhari (1169) da Muslim (724) ne suka rawaito shi
4. Muslim (726) ne ya rawaito shi.
5. Ibnu Maja (11550) da Ibnu Khuzaima (1117) ne suka rawaito shi.

nafila) a gidajenku, kar ku maida su ƙaburbura”[1]. A cikin hakan akwai alfanu masu yawa:

- Akwai: tsarkake niyya, da ɓoye aiki daga idon mutane.
- Akwai: ƙarin khushu’i a cikinta.
- Akwai kuma: raya gidaje da ambaton Allah, da saukar rahama da albarka ga mutanen gidajen, nesantan Shaiɗan daga wurinsu.

❖ **Hikimar da ke cikin shar’anta Sunnonin ratibai:**

Akwai hikimomi da alfanu da malamai suka zaƙulo na sunnoni rawatibai, daga cikin su:

- Nafilolin da ake yi gabanin farilla a cikin su akwai shiri da kimtsa rai don ibada, bayan da ta shagaltu da al’amuran duniya, tana nesa da halin khushu’i da ya ke shi ne ruhin ibada; don haka ne aka shar’anta yin su tare da asubahi da azahar; don abin da ke gabatan su na lokaci mai tsawo ba sallar farilla a cikin su.
- Amma nafilolin da ke bayan farilla; ya tabbata a Hadisi cewa nafiloli suna cike tawaya da nakasu da suka kasance cikin sallar farillah; Annabi (SAW) ya ce: “Lallai farkon abin da za a yi wa mutane hisabi akai ranar Alƙiyama na ayyukansu shi ne sallah; Ya ce: Ubangijinmu Maɗaukaki zai cewa mala’ikunsa, alhali ya sa fi su sani: Ku duba sallar bawana, ya cika ta ko ya tauye ta? Idan ta kasance a cike sai a rubuta ta a cike, in kuwa ta kasance akwai wani abu da ya tawaya a cikinta, sai Ya ce: Ku duba shin bawana na da wata nafila? Idan ya na da ita sai Ya ce: Ku cika wa bawana farillarsa da nafilarsa”[2].

[1]. Bukhari (432) da Muslim (777) ne suka rawaito shi.
[2]. Abu Dawud: (864) ne ya rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

YAƘIN BANUN-NADIR

❖ Lokacin da ya auku:

Yakin Banun Nadir ya auku ne a watan Rabi'ul Auwal na shekara ta huɗu ta hijira.

❖ Sababban yaƙin:

Rikicin yakin ya faro ne lokacin da sahabi mai daraja Amru ɗan Umayyah Ad-Damri (RA) ya yi kuskuren kashe wasu mutane biyu daga ƙabilar Banu Kilab, ya na zaton suna cikin maƙiya, sai Annabi (SAW) ya yi nufin haɗa diyyarsu daga musulmai da waɗanda ya yi ƙawancen zaman lafiya da su, sai ya nufi masallacin Ƙuba A ranar Asabar, ya yi sallah cikinsa, sannan ya nufi Banun-Nadir, ya buƘaci su yi musharaka wurin biyan diyar wadancan mutane biyu da aka kashe; saboda ƙawancen zaman lafiya da aka yi da su na hukunta haka, sai suka ce: 'Za mu bayar'[1].

Manzon Allah (SAW) da Abubakar da Umar da Aliyu da wasu cikin sahabbansa (RA) suka zauna a wata katanga ta Yahudawa, sai Yahudawa suka haɗa baki, suka yanke shawarar warware ƙawamcen da kuma yaudarar Manzon Allah (SAW), suka ce: 'Wanene zai rifto da wannan garu a kan Muhammad ya kashe shi?' Sai Amru dan Jahash ya ce zai aikata haka, nan take Allah Ya sanar da Manzonsa (SAW) abin da suke nufin aikatawa, ya tashi nan da nan, kuma bai tsaya ba sai a Madina, sai wani ya je ya sanar da sahabban Annabi cewa ya ga Annabi yana shigowa ganuwan Madina, su ka ta shi suka

[1]. Al-Bidayah Wan-Nihayah (5/534).

bi shi, sai Annabi (SAW) ya ba su labarin abin da Allah Ya sanar da shi na al'amarin Banun-Nadir[1].

❖ Abubuwan da suka faru a yaƙin:

Manzon Allah (SAW) ya aika Muhammad ɗan Maslamah zuwa ga Banun-Nadir yana umurtar su da ficewa daga garin Madina, ya kuma ba su kwana goma su tattara kayayyakinsu, a yayin da Yahudawa ke shirin ficewa, sai ga jagoran munafinci Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul ya na musu tayin su zauna, yana mai hujja ta cewa ai tare da shi akwai mutane dubu biyu da za su shiga ganuwarsu, kuma a shirye suke su mutu dominsu, kuma game da haka ne Allah Ya saukar da fadinSa: ((Ba ka ga waɗanda suka yi munafunci suna cewa 'yan uwansu waɗanda suka kafirta daga ma'abota littafi: Tabbas idan aka fitar da ku, lallai za mu fita tare da ku, ba kuma za mu bi wani mutum game da ku ba har abada, kuma idan aka yake ku tabbas za mu taimake ku." Allah kuma Ya san tabbas karya suke yi))[2].

Don haka sai jagoran Banun-Nadir, Huyayyu ɗan Ahdab ya yi kwaɗayin zama, ya kuma aika wa Manzon Allah (SAW) yana ce: "Lallai mu ba za mu fita daga gidajenmu ba, ka aikata abin da ka ga dama" Sai suka yi garkuwa a katangunsu da ganuwowinsu masu ƙarfi a kudancin Madina.

Da sakonsu ya iske Annabi (SAW), sai ya zaburar da mutane a kan a yaƙe su, ya shirya runduna, ya sa Ibnu Ummi Maktum shugaba a Madina. Sai Annabi (SAW) ya fita yana jagorantar rundunar, Aliyu ɗan Abu Ɗalib kuma na rike da tuta, sai Annabi (SAW) ya musu ƙawanya na tsawon dare shida, ya yi umurnin an sare dabinunsu a

[1]. Al-Bidayah Wan-Nihayah (5/535).
[2]. [Al-Hashr:11].

kuma ƙona su, kamar yadda Allah Ya ce: ((Duk abin da kuka sare na wata bishiyar dabino ko ku ka bar ta a tsaye a kan tushiyoyinta, to da izinin Allah ne, don kuma Ya kunyata fasikai))[1].

❖ Sakamakon yaƙin:

Da Banun-Nadir suka ga tsananin musulmi da yadda munafukai suka bar su; sai suka nemi Annabi (SAW) ya tsare jinenansu kuma ya ƙyale sus u fice, da sharaɗin duk abinn da suka iya ɗauka a kan raƙumansu in dai ba makami ba ne a bar musu, sai Manzo (SAW) ya amince da hakan, manyansu irinsu Huyayyu ɗan Akhdab da Salam ɗan Abi Huƙaiƙ suka fice tare da iyalansu da dukiyoyinsu zuwa Khaibar, wasu kuma daga cikin su suka wuce Sham, mutum biyu ne kaɗai cikinsu suka muslunta, su ne: Abu Sa'ad ɗan Wahab da Yamin ɗan Umair ɗan Ka'ab[2].

A dalilin wannan yaƙin ne Allah Ya saukar da Suratul Hashr, Abdullahi ɗan Abbas ya kasance yana kiran wannan surah da Suratu Banin-Nadir[3].

---

1. [Al-Hashr: 5].
2. Al-Bidayah Wan-Nihayah (5/538).
3. Bukhari (4882) da Muslim: (3031) ne suka rawaito shi.

ASABAR: DARASI CIKIN SAHABBAI

USAID ƊAN HUDAIR (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne: Baban Yahya, Usaid da Al-Hudair, dan Simak ɗan Atik, mutumin Madina, Al-Ausi, Al-Ash-hali, mahaifinsa ya kasance mahayin mutanen Aus a yakokkin da Khazraj, garkuwan Waqim ta kasance ta sa ce, shi ne kuma ya kasance jagoransu a ranar yakin Bu'as, a lokacin aka kashe shi.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Usaid (RA) ya kasance ya iya rubutu da harbi da ninƙaya, ya gaji matsayi da jarumta da kyauta daga mahaifinsa, ya kasance kafin ya musulunta yana daga cikin jagororin Madina, da masu darajar Larabawa, da maharbansu masu hazaka, lokacin da ya shiga Musulunci, ya karbi shiriya, sai izzarsa ta ƙasaita, darajarsa ta ƙaru, sai ya kasance daga cikin mataimakan Allah Maɗaukaki da Manzonsa.

Usaid (RA) ya musulunta ne bayan mubaya'ar Aƙaba ta farko, a hannun Mus'ab ɗan Umair (RA) a garin Madina. Sannan ya shaida mubaya'ar Aƙaba ta biyu, ya kuma kasance jagora ne ga Banu Abdil Ash-hal[1]. Ya kuma halarci yaƙin Uhudu da sauran yaƙoƙi da suka zo bayan ta, an yi masa rauni bakwai a yaƙin Uhud, ya tabbata a wannan yakin tare da Annabi (SAW) lokacin da mutane suka watse, a lokacin halifancin Umar, Usaid ya kasance cikin waɗanda suka halarci buɗe Baitul-Makdis.

[1]. Siyaru A'lamin-Nubala (1/341).

Annabi (SAW) ya yabe shi ya ce: (Madalla da wannan mutumi, Usaid ɗan Hudair)[1].

A'ishah (RA) ta ce: "Mutane uku daga cikin mutanen Madina daga ƙabilar Banu Abdil-Ash-hal babu wanda ya fi su falala bayan Manzon Allah (SAW), su ne: Sa'ad ɗan Mu'az da Usaid ɗan Hudair, da Abbad ɗan Bishir"[2].

Abubakar Siddiƙ (RA) ya kasance yana girmama shi, kuma ba ya gabatar da wani a kansa.

Yana daga cikin abubuwan mamaki a tarihinsa: Abin da ya faru da shi na karama lokacin da ya kasance tare da Abbad ɗan Bishir a wurin Manzon Allah (SAW) a cikin wani dare mai duhu, lokacin da suka fito daga wurin Manzo (SAW), sai sandar ɗaya daga cikinsu ta yi haske, har suka kasance suna amfani da haskenta suna tafiya, suna kaiwa wurin da za su rabu sai sandar kowannensu ta yi haske[3].

Haka kuma Mala'iku sun sakko saman kansa kamar lema, saboda zaƙin muryarsa da ya ke karanta maganar Allah[4].

❖ Rasuwarsa:

Usaid dan Hudair (RA) ya rasu a watan Sha'aban, shekara ta Ashirin, Umar dan Khattab ne ya yi masa sallah, ya kuma ɗauki gawarsa har ya birne shi a makabatar Baƙi'a.

---

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3797).
[2]. Hakim ne rawaito shi (3/229).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (3805)
[4]. Bukhari: (59118) da Muslim: (796) suka rawaito shi.

Auna fahimtarka cikin darussan mako na 27				Amsa ta warai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Menene ma'anar "Taradda"?**			C
	[a] Ya rasa dukiyarsa	[b] Ya yi rashin lafiya	[c] Ya fada cikin wuta	
Darasin Hadisi	**Tambaya: Menene ake nufi da (Huda-Shiriya)**			B
	[a] Gaskiya	[b] Ilimi mai amfani	[c] Aiki na kwarai	
Darasin Akida	**Tambaya: Daga cikin dalilai karara da hujjoji bayyanannu aka bacin shirka da zargin ma'abotansa:**			C
	[a] Yawan mala'iku	[b] Nau'antuwan mutane	[c] Tsaruwan duniya	
Darasin Fikihu	**Tambaya: Mafi karfi a cikin sunnoni ratibai:**			B
	[a] Sunnar jumu'ah	[b] Sunnar asubahi	[c] Sunnar Azahar	
Darasin Sira	**Tambaya: Shugaban Banun Nadir shi ne:**			A
	[a] Huyayyu dan Akhtab	[b] Abdullahi ibn Salul	[c] Salam dan Abil Hukaik	
Darasin Tarihin sahabbai	**Daga cikin karamomin Usaid dan Hudair:**			C
	[a] Maganar tsuntsaye gare shi	[b] Sallamar aljanu gare shi	[c] Hasken sandarsa	

MAKO NA ASHIRIN DA TAKWAS

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIR

SURATUL-BALAD

سمحبِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ سجى

لَآ أُقۡسِمُ بِهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ١ وَأَنتَ حِلُّۢ بِهَٰذَا ٱلۡبَلَدِ ٢ وَوَالِدٖ وَمَا وَلَدَ ٣ لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِي
كَبَدٍ ٤ أَيَحۡسَبُ أَن لَّن يَقۡدِرَ عَلَيۡهِ أَحَدٞ ٥ يَقُولُ أَهۡلَكۡتُ مَالٗا لُّبَدًا ٦ أَيَحۡسَبُ أَن لَّمۡ
يَرَهُۥٓ أَحَدٌ ٧ أَلَمۡ نَجۡعَل لَّهُۥ عَيۡنَيۡنِ ٨ وَلِسَانٗا وَشَفَتَيۡنِ ٩ وَهَدَيۡنَٰهُ ٱلنَّجۡدَيۡنِ ١٠ فَلَا ٱقۡتَحَمَ
ٱلۡعَقَبَةَ ١١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلۡعَقَبَةُ ١٢ فَكُّ رَقَبَةٍ ١٣ أَوۡ إِطۡعَٰمٞ فِي يَوۡمٖ ذِي مَسۡغَبَةٖ ١٤ يَتِيمٗا ذَا
مَقۡرَبَةٍ ١٥ أَوۡ مِسۡكِينٗا ذَا مَتۡرَبَةٖ ١٦ ثُمَّ كَانَ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَتَوَاصَوۡاْ بِٱلصَّبۡرِ وَتَوَاصَوۡاْ
بِٱلۡمَرۡحَمَةِ ١٧ أُوْلَٰٓئِكَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَيۡمَنَةِ ١٨ سمحوَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِنَا هُمۡ أَصۡحَٰبُ ٱلۡمَشۡـَٔمَةِ
١٩ عَلَيۡهِمۡ نَارٞ مُّؤۡصَدَةُۢ ٢٠سجى

❖ Fassara

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin kai

1. Ina rantsuwa da wannan gari (na Makka).
2. Alhali kuwa kai an halatta maka wannan gari.
3. (Na rantse) da mahaifi da abin da ya haifa.
4. Hakika Mun halicci mutum cikin wahala.
5. Yanzu mutum yana tsammanin cewa wani ba zai sami iko a kansa ba?
6. Yana cewa: "Na batar da dukiya mai dimbin yawa".
7. Shin yana tsammanin cewa ba wanda ya gan shi?
8. Shin ba Mu sanya masa idanuwa biyu ba ne?

9. Da harshe da kuma labba biyu?
10. Muka kuma bayyana masa hanyoyi biyu?
11. Sai bai ketare hanya mai wahala ba?
12. Me kuma ya sanar da kai mece ce hanya mai wahala?
13. (Watau) ‘yanta wuyaye (bawa ko baiwa).
14. Ko kuma ciyarwa a wata rana ta yunwa.
15. Ga maraya ma’abocin kusanci.
16. Ko miskini ma’abocin talauci.
17. Sannan kuma ya zama daga waɗanda suka yi imani, suka yi wa junansu wasiyya da yin hakuri kuma suka yi wa juna wasiyya da tausayawa.
18. Waɗannan su ne ma’abota dama.
19. Waɗanda kuwa suka kafirce wa ayoyinmu, su ne ma’abota hagu.
20. A kansu akwai wuta abar kullewa.

❖ Saƙon da Surar ke ɗauke da shi:

Bayanin talaucin mutum da wahalarsa da hanyoyin tsirarsa.

❖ Bakin Kalmomi:

	La Uƙsimu	Ma’ana: Ina rantsuwa, harfin (Laa) na karfafa rantsuwa ne	النجدين	An-Najdaini	Hanyoyin alkhairi da na sharri

حل	Hillun	Mazauni	فلا اقتحم	Fala-ƙtahama	Shin ba zai ketare?
لبدا	Lubada	Dimbin yawa	العقبة	Al-Aƙabah	Wahalar lahira
وهديناه	Wa Hadain ahu	Mun bayyana masa	فك رقبة	Fakku Raƙabah	‘Yanta wuyaye bawa daga bauta
مسغبة	Masgab ah	Yunwa	الميمنة	Al-Maiman ah	Dama; yadda za a yi gefen dama da su zuwa Aljannah
ذا مقربة	Za Makrab ah	Ma’aboc in kusanci	المشئمة	Al-Mash’a mah	Hagu: yadda za a yi gefen hagu da su zuwa wuta
ذا متربة	Za matraba	Talaka da ba shi da komai	مؤصدة	Mu’sada h	Kullalliy a abar rufewa

❖ Ma'anar Surar a Dunƙule:

Suratul Balad surah ce makiyya, ta fara da rantsuwar Allah da wannan gari, wanda shi Makkah wacce Annabi (SAW) ya kasance mazauni ne a cikinta, sannan Allah Ya rantse da uba da abin da ya haifa, wanda shi Adam da zurriyarsa, cewa lallai an halicci dan Adam cikin wahala da tsanani, amma tare da hakan yana tsammanin shim ai karfi ne, kuma ba wanda ke da ikon akan shi, yana mai alfahari da dukiyarsa, yana kuma ciyar da ita wurin sabon Allah, yana tsammanin ba wanda ke ganin sa, yana lura da shi! Tare da cewa Allah Shi ne wanda Ya halicce shi, kuma Ya ba shi ni'imomi masu yawa, Allah Ya halitta mi shi idanuwa biyu da harshe da labba biyu, da wasu ni'imomin da ba su ba, to abin da ya ke wajaba gare shi shine ya ciyar da dukiyarsa ga ayyukan alkhairi; kamar ciyar da mai jin yunwa, ɗaukar dawainiyar maraya da miskini; don kuwa masu aikata hakan su ne muminai, ma'abota dama, amma waɗanda suka kafircewa Allah da Ayoyinsa su kuma su ne ma'abota hagu, za a yi wuta da su, a rufe su a cikin ta ruf.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1. Byanin darajar garin Makkah da matsayinta a wurin Allah Maɗaukaki, da cewa ita ce gari mai alfarma har zuwa ranar alƙiyama.
2. Lallai mutum an halicce shi ne cikin wahala, rayuwarsa ba ta rabuwa da wahalhalu da tsanani.
3. Wajibi ne ga musulmi ya karbi ƙaddarar Allah da zuciya mai haƙuri, da gaɓoɓi masu godiya, kar ya yi ƙorafi ko ya bijire, don ya samu yardar Allah Maɗaukaki.
4. Lallai ciyar da mabuƙata a lokacin tsanani na cikin ayyuka masu falala.
5. Lallai imani da Allah Maɗaukaki, da wasici da hakuri da tausayawa na daga cikin sababban shiga Aljanna.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR IMANI DA SAKAMAKON WANDA YA MUTU A KANSA

An karɓo daga Abdullahi ɗan Amru Allah Ya kara yarda a gare su, ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Duk wanda ya ke son a nesanta shi daga wuta, kuma a shigar da shi Aljanna; to mutuwarsa ta zo masa yana mai imani da Allah da ranar lahira, kuma ya so wa mutane irin abin da ya ke so wa kansa**)[1].

❖ Sharhi:

Shiga aljanna da tsira daga wuta sune manufar da kowane musulmi ke ƙoƙarin ya cimma, kuma zai gabatar da komai duk darajarsa don hakn, a cikin wannan hadisin Annabi (SAW) ya sa ambaci sabubba biyu don cimma wannan kuduri:

Na Farko: Tsayuwa da hakkokin Allah Maɗaukaki; ta hanyar imani da shi, da ranar lahira, da abubuwan da ke biye da hakan na rukunnen imani da ayyukansa.

Na Biyu: Tsayuwa da hakkokin bayi; ta hanyar kyautata musu, da mu'amala kyakkyawa da yake so shi ma a yi masa irin ta.

❖ Abububuwan da za a koya daga Hadisin:

1. Shiga Aljanna da tsira daga wuta shi ne babban manufar kowane musulmi da ya yi imani da Allah da ranar lahira.
2. Kwaɗaitarwa a kan koyan rukunnan imani da abubuwan da suke lazimtawa.
3. Kwaɗaitarwa ga tabbata a kan addini, da haƙuri a kan imani, da bibiyan sabubban hakan, har mutuwa ta zo wa mutum.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (1844).

4. Lallai a cikin riƙo da littafin Allah da sunnah akwai kubuta daga fitintinu, da kariya daga ɓata, da kuma shiriya daga ɗimuwa.
5. Lallai so wa mutane alkhairi na daga cikin ayyuka masu daraja, da mu’amalantar su da mafi kyawun abin da ya ke so a mu’amalance shi da shi.

TALATA: DARASI CIKIN AKIDA

ILLOLIN SHIRKA DA TASIRINTA

Shirka na da munanan tasiri da illoli masu hatsari da halakarwa, daga cikin su akwai:

1. Lallai shirka ita ce mafi sharrin laifuka, kuma mafi girman zunubai, Annabi (SAW) ya ce: (Ashe ba na sanar da ku mafi griman zunubai ba?" Sahabbai suka ce: A sanar da mu ya Manzon Allah, sai ya ce: "Shirka da Allah, da saɓa wa iyaye)[1].
2. Lallai shirka rashin sanin girman Allah Maɗaukaki ne, kuma kamanta halittunsa ne da shi, kuma aibu ne da Allah Ya tsarkaka daga shi, don haka duk wanda ya yi shirka, ya tabbatarwa Allah abin da Allah Ya tsarkake kansa daga shi, wannan kuwa shi ne ainihin saɓa wa Allah da kangara gare Shi!
3. Lallai shirka babba Allah ba Ya gafarta ta, idan mutum ya mutu yana aikata ta; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai Allah ba Ya gafarta a yi shirka da Shi, amma Ya na gafarta abin da ba bai kai shirk aba ga wand Ya ga dama. Kuma duk wanda ya yi shirka da Allah, to haƙiƙa ya kirkiri wani gagarumin laifi)) [2].
4. Lallai shirka babba tana rusa dukkan ayyuka; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma da a ce sun yi shirka, to lallai da duk abin da suka kasance suna aikatawa ya rushe)) [3]. Haka kuma Allah Ya ce: ((Tabbas idan ka yi shirka lallai aikinka zai ɓaci, kuma tabbas za ka kasance daga asararru)) [4].
5. Lallai shirka babba na lizimta wuta ga ma'abocin a, kuma ta haramta masa Aljanna, Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai duk wanda ya shirka da Allah, to hakika Allah Ya haramta masa shiga Aljanna, kuma makomarsa ita ce wuta, kuma azzalumai ba su da wasu

---

[1]. Bukhari: (6871) da Muslim: (88) ne suka rawaito shi.
[2]. [An-Nisa'i: 48].
[3]. [A-An'am: 88].
[4]. [Az-Zumar: 65].

mataimaka))[1]. Haka kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: ((Duk wanda ya mutu ba ya shirka da Allah da wani abu zai shiga Aljanna, wanda kuwa yam utu yana shirka da Allah zai shiga wuta))[2].

6. Lallai shirka ita ce mafi girman zalunci da ƙage, domin shi ne ajiye abu ba a wurin sa ba, duk wanda ya bauta wa wanin Allah haƙiƙa ya ajiye ibada ba a wurinta ba, kuma ya karkatar da ita ga wanda bai cancance ta ba, wannan kuwa shi ne mafi girman zalunci, kuma mafi munin kirkira; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai ita shirka zalunci ne mai girma))[3]. Haka kuma Allah Ya ce: ((Kuma duk wanda ya yi shirka da Allah, to hakika ya kirkiri wani gagarumin laifi))[4].

7. Lallai Allah Maɗaukaki da Manzonsa sun barranta daga mushrikai, Allah Ya ce: ((Kuma sanarwa daga Allah da Manzonsa ga mutane ranar babbar sallah cewa, lallai Allah da Manzonsa babu ruwansu da mushrikai))[5].

---

[1]. [Al-Ma'ida: 72].
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (93).
[3]. [Lukman: 13].
[4]. [An-Nisa'i: 48]
[5]. [At-Taubah: 3].

LARABA: DARASI CIKIN FIKIHU

SALLAR WUTIRI

❖ Hukuncinta:

Wutiri sunnah ce mai karfi, Annabi (SAW) ya kadaitar kuma ya zaburar akan yin ta; Annabi ya ce (SAW): ((Lallai Allah wutiri ne (tilo ne) yana son witiri))[1]. Haka kuma ya ce: (Ku yi wutiri ya ku ma'abota Al-Kur'ani, domin Allah wutiri ne Ya na son wutiri) [2].

❖ Lokacinta:

Lokacin wutiri: daga bayan sallar Isha'i zuwa bullowar Al-fijir; saboda fadar Manzon Allah (SAW): (Lallai Allah Madaukaki Ya yi muku dadi da wata sallar, wannan sallar ta fi mu ku alkhairi fiye da jajayen rakuma, ita sallar wutiri, sai Allah Ya sa muku ita tsakanin isha'i zuwa bullowan alfijir) [3].

Sallar wutiri a ƙarshen dare ya fi falala akan farkon ta, duk wanda ya kasance yana ta tabbacin zai tashi a ƙarshen dare, to jinkirta sallar wutiri gare shi ya fi falala, duk wanda bai da tabbacin tashi to sai ya yi wutirin gabanin ya kwanta. Annabi (SAW) ya ce: (Duk wanda ya ji tsoron ba zai tashi ba ƙarshen dare to ya yi wutiri a farkon sa, wanda ko ke kwaɗayin tashi ƙarshen dare to ya yi wutiri ƙarshen dare; domin sallar ƙarshen dare ta kasance lokacin halartar (mala'iku), shi ne ya fi falala)[4].

---

[1]. Bukhari (6410) da Muslim (2677) ne suka rawaito shi.
[2]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (1416).
[3]. Abu Dawud: (1418) da Tirmizi (452) ne suka rawaito shi.
[4]. Muslim ne ya rawaito shi (755).

❖ Siffar sallar wutiri da adadin raka’o’inta:

Mafi karancin ta raka’a ɗaya ce; saboda faɗin Manzo (SAW): (Wutiri raka'a ɗaya ce a ƙarshen dare)[1].

Mafi cikar kamala a sallar wutiri shi ne raka’a uku da sallama biyu, yana kuma halatta jero raka’o’in da sallama ɗaya, sai ya yi tahiya ɗaya, don kada ta yi kamanceceniya da sallar magriba, kuma an so a karanta Suratul A’la a raka’ar farko, da Suratul-Kafirun a raka’ah ta biyu, sai Suratul Ikhlas a raka’ah ta uku[2].

Adadin wutiri mafi yawa shi ne raka’ah goma sha ɗaya, za a yi su raka’a biyu-biyu, sai ya yi raka’a ɗaya da za iyi wutiri da ita ga sallarsa, saboda faɗin A’ishah Allah Ya kara yarda a gare ta: “Manzon Allah (SAW) ya kasance yana sallar dare raka’ah goma sha ɗaya, yana sallama tsakanin kowane raka’a biyu, sai ya yi wutiri da ɗaya"[3].

Ya halatta ya yi wutiri da raka biyar ko bakwai, abin da ya fi shi ne yin raka’a biyu-biyu, yana da damar ya jero su duka sai ya zauna a raka’ar karshe, saboda fadar Ummu Salamah allah Ya kara mata yarda: “Manzon Allah (SAW) Ya kasance yana wutiri da raka’a biyar ko bakwai, ba ya rabewa tsakaninsu da sallama ko magana"[4].

Idan mutum ya yi wutiri da raka’a tara a jere, zai zauna a raka’a ta takwas, ya yi tahiyar farko, sai ya tashi ya yi raka ta tara ya sallame[5].

Idan wutiri ta kubucewa mutum cikin dare; to sunnah ne ramawa lokacin walha amma mara ba tilo ba, idan ya kasance al’adar mutum ne ya yi wutiri da raka’a uku, sai ya yi raka’a huɗu, idan raka’a biya

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (752).
[2]. [An-Nasa’i: (1736).
[3]. Muslim ne ya rawaito shi (736).
[4]. Ibnu Maja ne ya rawaito shi (1192).
[5]. Ibnu Hibban ne ya rawaito shi (2442).

ce al’adarsa sai ya yi raka’a shida, saboda aikin Manzon Allah (SAW)[1].

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (746).

ALHAMIS: DARASIN SIRA

YAƘIN GWALALO (AHZAB)

❖ Lokacin da ya auku:

Yaƙin Ahzab ya faru ne a watan Shawwal, shekara ta biyar bayan Hijrah.

❖ Sababbansa:

Sababin wannan yaƙi shi ne Yahudawan da Annabi (SAW) ya fitar daga Madina zuwa Khaibar, sai shugabanninsu mutum ashirin suka je wurin Ƙuraishawa, suka nemi ɗaukinsu a kan su yaƙi Manzon Allah (SAW), suka yi musu alƙawarin lallai za su taimake su, sai Ƙuraishawa suka amsa musu, shi ne suka fita zuwa ƙabilar Gaɗfan, nan ma suka gayyace su, suma suka amsa musu.[1]

❖ Abubuwan da suka faru a yaƙin:

Ƙuraishawa sun fito bisa jagorancin Abu Sufyan ɗan Harb, su kuma Gaɗfan sun fito ƙarkashin jagorancin Uyaina ɗan Hisn, Banu Murrah da Banu Ashja' da Banu Asad sun fito tare da su, waɗannan rundunoni suka tunkaro Madina, da rundunar da mayaƙansa sun kai dubu goma.

Lokacin da Manzon Allah (SAW) ya ji labarin tahowarsu, sai ya umurci musulmi su shirya, wanda lokacin sun kai kusan dubu uku, ya umurce su da su haƙa wani rami da zai zama shamaki tsakanin mushrikai da garin Madina, hakan kuwa ya kasance ne bisa shawarar Salman Al-Farisi ya bayar, musulmai suka aikata hakan suna masu gaggauta harin kafirai akansu, sun wahala sosai iyakar wahala, ga yunwa, sun kasance suna ɗaukar turɓaya a kafaɗunsu, suna masu haƙuri a kan tsanani, suna rera waƙoƙi da baituka, suna

[1] Al-Bidayah Wan-Nihayah (6/12).

masu yaƙinin samun taimakon Allah Ubangijinsu, haka har suka kammala haƙar ramin, mushrikai suka sauka a gefen Madina, suka yi wa muslumi ƙawanya na tsawon wata ɗaya.[1]

A wannan halin ne Huyayyu ɗan Akhɗab shugaban Banun-Nadir ya fito zuwa Banu Ƙuraizah, ya haɗu da shugabansu Ka'ab ɗan Asad, bai gushe ba yana ba shi baki har sai da ya sa shi ya warware alƙawarin da ke tsakanin shi da Annabi (SAW), sai Banu Ƙuraizah suka haɗa kai tare da waɗannan rundunoni a kan yaƙar Annabi (SAW), bala'i ya yi tsanani a kan Musulmi, zukatan munafukai da masu rauni suka raurawa, [2] kamar yadda Allah Ya faɗa: ((A lokacin da suka zo muku ta samanku da ƙasanku, da kuma yayin da idanuwa suka kauce wa (ganin komai sai maƙiya), zukata kuma suka cika da tsoro, kuka riƙa zace-zace game da Allah))[3].

Amma Manzon Allah (SAW) da sahabbansa su kam zukatansu sun cika da yaƙini, harsunansu kuma sun cika da addu'a, ya kasance daga cikin addu'o'in da yake yi akwai: (Ya Allah, Wanda Ya saukar da Littattafai, Mai gaggawan hisabi, Ka ruguza waɗannan rundunar, Ya Allah Ka ruguza su, Ka girgiza su)[4].

❖ Sakamakon yaƙin:

Allah Ya aikata wani al'amari ga rundunonin kafirai daga wurinsa, Ya kuma ɗaiɗaita haɗakarsu, abin da ya faru kuwa shi ne Nu'aim bin Mas'aud bin Amir Al-Gadfani Allah Ya ƙara masa yarda, Ya musulunta, sai ya gudo a ɓoye daga mutanensa zuwa ga Annabi (SAW) sai ya koma ya shirya wata dabara da wayonsa; wacce ta jefa tsaɓani da rabuwan kai a sahun mushrikai da Yahudawa[5], sannan

1. Al-Bidayah Wan-Nihayah (6/14).
2. Al-Bidayah Wan-Nihayah (6/35).
3. [Al-Ahzab: 10].
4. Bukhari (4115) da Muslim (1742) ne suka rawaito shi.
5. Al-Bidayah Wan-Nihayah: (6/59)

Allah Ya cika nasararsa ta hanyar aiko iska da mala’iku da suka girgiza su, kuma tsoro da firgici suka cika zukatansu, wannan ya sa suka kasa cimma wata matsaya, tantunansu kuma suka kasa tsayawa saboda iska, sai suka yi asara suna ƙasƙantattu, suka koma a wulaƙance, sai Allah Maɗaukaki Ya saukar da farkon Suratul-Ahzab game da wannan yakin.

ASABAR: DARASI CIKIN SAHABBAI

BILAL ƊAN RABAH

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne sahabin nan mai daraja: Bilal ɗan Rabah, mahaifiyarsa itace: Hamamah. An haife shi a Makkah, shekara ta 42 gabanin hijira.

❖ Rayuwarsa da Falalarsa

Bilal Allah Ya kara yarda a gare shi ya kasance baƙin fata, mai ƙaramin jiki, ga tsayi, matsakaicin gaɓɓai, ya musulunta da wuri, ya kasance bawa ne daga cikin bayi, ya kuma kasance daga cikin waɗanda suka riga shiga musulunci, mai gaskiya ne, mai haƙuri, mai tsananin haƙuri, da ɗauke cutarwa a tafarkin Allah; Umaiyyah dan Khalaf ya kasance idan rana ta yi tsanani, sai ya fito da shi, ya umurce a kawo dutse mai girma, sai a ɗaura mishi a ƙirjinsa, y ana ce mi shi: ‘wallahi ba za ka gushe ba a haka har sai ka mutu, ko kuma ka kafircewa Muhammadu, ka bautawa Lata da Uzza! [1].

Su kuma bayin Umayyah suna kwantar da shi a kan cikinsa, suna danne shi, suna cewa: ‘Addininka Lata da Uzza’ Shi kuma yana cewa: Allah ne Ubangijina, Shi kaɗai Ya ke, Shi kaɗai Ya ke[2].

Ya fuskanci cutarwa mai yawan gaske daga Abu Jahal da waninsa.

Abdullahi dan Mas’ud Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: “Waɗanda suka fara bayyanar da musuluncinsu mutane bakwai ne: Manzon Allah (SAW), da Abubakar, da Ammar da mahaifiyarsa Sumayyah, da Suhaib da Bilal da Miƙdad. Shi Annabi (SAW) Allah Ya tsare shi (daga cutarwan Ƙuraishawa) dalilin aminsa Abu Dalib, shi kuma Abubakar da danginsa, amma sauran mushrikai sun kama su suka

[1]. Al-Bidayah Wan-Nihayah: (3/57).
[2]. Siyaru A’alamin-Nubala’ (1/352)]

sanya musu sulken ƙarfe, suka shan ya su a tsakar rana, ba wani cikin su face ya mika wuya gare su akan abin da suka nufa, banda Bilal, don kuwa ya saudaukar da ransa ga Allah, sun daure shi suka ba yara shi suna kewaya sasan Makkah da shi, shi kuwa yana cewa: "Allah Shi Kadai Yake, Shi Kadai Ya ke" [1].

Bilal ya halarci yaƙin Badar da dukkan yakokin Annabi, Bilal ya keɓanta da kasancewarsa shin ladanin farko a Musulunci, kuma shine ladanin Manzon Allah (SAW), ya kasance yana masa kiran sallah lokacin rayuwarsa, a halin tafiya ko zaman gida.

Annabi (SAW) ya yi masa shaida da Aljannah yayin da ya taɓa ce masa lokacin sallar Asubahi**:** (Ya kai Bilal, ba ni labarin mafi darajar aikin da ka aikata a Musulunci, don kuwa lallai na ji ƙarar takalminka a gaba gare ni a cikin aljannah) [2]. Sai Bilal ya ba da amsa da cewa: Ba wani aiki da na aikata da nake sa rai da shi face duk san da ana yi alwala, ko cikin dare ne ko cikin yini, sai na yi sallah da wannan alwalar gwargwadon abin da Allah Ya rubuta mini.

❖ Rasuwarsa:

Bilal bin Rabah Allah ya kara yarda a gare shi ya rasu ne a Dimashk, aka birne shi a maƙabartarta, a shekara ta ishirin, yana dan shekara sittin da uku.

[1]. Ibnu Majah: (150) ne ya rawaito shi
[2]. Bukhari (1149) da Muslim (2428) ne suka rawaito shi.

Auna fahimtarka a cikin darussan mako na 28			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsir	**Tambaya: Menene ma'anar: "An-Najdain"?**		A
	[a] Hanyar alkhairi da hanyar sharri	[b] Dare da yini	[c] Duniya da lahira
Darasin Hadisa	**Tambaya: Daga cikin sabbubun shiga aljanna da tsira daga wuta tsayuwa da**		C
	[a] Da haƙƙin Allah Maɗaukaki	[b] Haƙƙin halittu	[c] Haƙƙin Allah da haƙƙin halittu
Darasin Aƙida	**Tambaya: Mafi sharrin zunubbai kuma mafi girmansu shi ne:**		A
	[a] Shirka	[b] zina	[c] Kisan kai
Darasin Fiƙihu	**Tambaya: Lokacin wutiri shi ne:**		B
	[a] Tsakanin sallar magriba zuwa bullokwan alfijir	[b] Tsakain sallar isha'i zuwa bullowan alfijir	[c] Tsakanin sallar isha'i zuwa bullowan rana
Darasin Sira	**Tambaya: Yaƙin Ahzab ya faru ne a shekara ta:**		A
	[a] 5H	[b] 6H	[c] 7H
Darasin tarihin Sahabbai	**Tambaya: Bilal ya kebanta da kasancewarsa:**		A
	[a] Ladanin farko a musulunci	[b] shahidin farko a musulunci	[c] Farkon wanda ya harba mashi a muslunci

MAKO NA ASHIRIN DA TARA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL FAJR (1)

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلۡفَجۡرِ ١ وَلَيَالٍ عَشۡرٖ ٢ وَٱلشَّفۡعِ وَٱلۡوَتۡرِ ٣ وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَسۡرِ ٤ هَلۡ فِي ذَٰلِكَ قَسَمٞ لِّذِي حِجۡرٍ ٥ أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِعَادٍ ٦ إِرَمَ ذَاتِ ٱلۡعِمَادِ ٧ ٱلَّتِي لَمۡ يُخۡلَقۡ مِثۡلُهَا فِي ٱلۡبِلَٰدِ ٨ وَثَمُودَ ٱلَّذِينَ جَابُواْ ٱلصَّخۡرَ بِٱلۡوَادِ ٩ وَفِرۡعَوۡنَ ذِي ٱلۡأَوۡتَادِ ١٠ ٱلَّذِينَ طَغَوۡاْ فِي ٱلۡبِلَٰدِ ١١ فَأَكۡثَرُواْ فِيهَا ٱلۡفَسَادَ ١٢ فَصَبَّ عَلَيۡهِمۡ رَبُّكَ سَوۡطَ عَذَابٍ ١٣ إِنَّ رَبَّكَ لَبِٱلۡمِرۡصَادِ ١٤﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin kai

1. Na rantse da alfijir.
2. Da kuma darare goma.
3. Da kuma abin da yake cika da kuma mara.
4. Da kuma dare lokacin da yake tafiya (cikin duhu).
5. Shin a game da waɗannan akwai rantsuwa (mai gamsarwa) ga mai hankali?
6. Shin ba ka ga yadda Ubangijinka Ya aikata ba ga Adawa?
7. (Watau kabilar) Iramu ma'abociyar tsawo.
8. Wadda ba a halicci irinta ba a cikin garuruwa (a tsananin karfi).
9. Da kuma Samudawa waɗanda suka fafe duwatsu a wurin da ake kira Wadil-Ƙura.
10. Da kuma Fir'auna ma'abocin turaku.
11. Waɗanda suka yi ɗagawa a cikin garuruwa.
12. Suka kuma yawaita barna a cikinsu.
13. Sai Ubangijinka Ya saukar musu azaba mai tsanani.
14. Lallai Ubangijinka tabbas Yana nan a madakata.

❖ Sakon da surar take dauke da shi:

Bayanin karshen dagawa.

❖ Bakin kalmomi

وليال عشر	Wa layalin Ashr	Rantsuwa ne da dareran goman farko na Zul Hijja, da kuma irin darjarta da suke da shi na ayyuka.
والشفع والوتر	Wash shaf'i wal Watr	Rantsuwa na da kowane aure da tilo
والليل إذا يسر	Wal Laili iza yasri	Ya gudu da duhunsa. Amsar rantsuwar an an shafe ta, abin da ake kaddarawa shi: Wallahi za a tashe ku (ranar alkiyama)
جابوا	Jabu	Sun yanke
بالواد	Bil wad	
لذي حجر	Li zi hijr	Ma'abocin hankali
إرم	Iram	Kabilar Iram
ذات العماد	Zatul Imad	Ma'abociyar karfi, da dogayen ginegine da akan turaku.
ذي الأوتاد	Zil Autad	Ma'abocin rundunoni da suka tannatar da mulkinsa.
لبالمرصاد	La bil mirsad	Yana kallon masu sabo, Ya na musu talala, sannan sai Ya kama su.

❖ Ma'anar Surar a Dunkule:

Wannan surah ta fara da rantsuwa gudu hudu manya, wadanda suka kunshi abubuwa da dama, wadanda ke nunawa kowane mai hankali ikon Mahaliccinsu da Mai gudanar da su, kuma lallai bauta ba wanda ya cancanta a yi gare shi sai Shi kadai. Sannan ayoyi suka zo da ambaton al'ummomi da suka gabata: Adawa, da Samudawa, da mutane Fir'auna, da irin abin da ya sauka gare su

sakamakon ƙaryatawan da suka yiwa Manzanninsu, kuma a cikin hakan akwai ishara ga mushrikan Ƙuraishawa da wasun sun a kafirai cewa fa abin da ya sauka ga wadancan al'ummomi da suka gabata zai sauka gare su su ma.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar

1) Falalar goman ƙarshe na Zul-Hijjah akan sauran.
2) Lallai waɗannan halittu da kunshi hikima mai ban kaye, da kira mai ban mamaki, dalili ne mai gamasarwa kuma hujja ce isasshiya don imani da Mahaliccinsu, kuma Makaginsu.
3) Lallai hankali lafiyayye shine wanda ya ke nunawa ma'abocinsa sanin Allah Maɗaukaki, da kuma imani da Shi.
4) Lallai dalilin gushewar ni'momi ga al'ummomin da suka gabata shi ne ɗagawarsu da kafircinsu, tare da suna amfana da ni'imomin Allah Maɗaukaki.
5) Lallai cikin ambaton halin da al'ummomin baya suka kasance akwai wa'azi da abin lura.

LITININ: DARASIN HADISI

KWADAITARWA A KAN KHUSHU'I A CIKIN SALLA

An karɓo daga Abu Ayyub Al-Ansariy Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: Wani mutum ya zo wurin Annabi (SAW) sai ya ce: Ka mini wa'azi, a takaice. Sai Annabi (SAW) ya ce: (**Idan ka tashi yin salla, ka yi salla ta mai bankwana, kar ka faɗi wata magana da gobe za ka zo kana neman afuwa akanta, ka ɗebe tsammani daga abin da ke hannun mutane**).[1]

❖ Sharhi

Wannan hadisi ya kunshi wasiyoyi masu girma, idan bawa ya yi riƙo da su al'amuransa za su cika kuma za su daidaita:

Wasiya Ta Farko: Cika sallah, ta hanyar cika rukunnanta da wajibanta da sunnoninta, da cimma matsayin kyautatawa a cikinta, da halarto cewa shi mai bankwana ne a cikin ta, kamar ba wata sallar da zai kara yi sai ita, alfanun sallah a wannan yanayin shi ne tana hana ma'abocin ta aikata munanan dabi'u, kuma ta na kwadaitar da shi ga aikata kyawawan dabi'u; saboda irin tasirin da take da shi wurin haska zukata da kara imani.

Wasiya Ta Biyu: Tsare harshe, duk wata magana da za ka bukaci sai ka nemi yafiya da bada uzuri a kanta bayan ka yi ta, to ka bar ta kawai; don kuwa idan ka furta wata magana shi kenan ta mallake ka, ka zama bawan wannan maganar, ƙila ta jawo maka wata matsalar da ba zaka iya kauce mata ba, shi kuwa neman yafiya da ba da uzuri ko dai ya zama ga Allah ne da tuba; don kuwa barin zunubi ya fi alkhairi akan neman gafara bayan aikata zunubi, ko kuma wurin mutane ne za ka nemi yafiya da ba da

1 [Ahmad ne ya rawaito shi (235450]

hanzari; shi kuwa haƙƙinsu ba ya faɗuwa sai sun yafe, ko ka nema yafiyar.

Wasiya Ta Uku: Karfafa rai ga dogaro ga Allah Shi kaɗai, da ɗebe tsammani daga abin da ke hannun mutane, a cikin al'amuran duniya da lahira, kar ka tambayi kowa sai Allah, kar ka yi kwaɗayi sai ga falalar Allah; don debe tsammani daga mutane kariya ne, duk wanda ya cira rai daga wani abu sai ya wadatu daga barin shi.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) Muhimmancin tsaida sallah ta yadda rukunnai da wajibai da mustahabbai za su tabbata.
2) Muhimmancin khushu'i da halarto da zuciya a cikin sallah, da kuma halarto da ganawa da Allah.
3) Lallai ya kamata ga musulmi ya kiyaye harshen sa, kar ya furta maganar da za jawo warware ta ko kuma bada hakuri.
4) Wajibcin dogara ga Allah wurin neman arziki, da dogaro gare shi, da roƙon Shi daga falalarsa, da kuma wadatuwa daga nema wurin mutane.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

SABUBBBAN SHIRKA DA HANYOYINTA

Saboda hatsarin shirka babba shari'ah ta toshe duk wata kafa da za ta kai ga faɗawa cikinta, Annabi (SAW) ya tsoratar daga duk wani sababi da zai kai gare shi.

Daga cikin sabubun da hanyoyi da aka hana:

Na Farko: Wuce iyaka game da salihai, wannan na daga cikin mafi girma na shirka da Allah Maɗaukaki, Annabi (SAW) ya ce: "Ina muku kashedi da wauce iyaka, saboda abin da ya halaka waɗanda suke gabanin ku shi ne wuce iyaka"[1]. Dalilin wuce iyaka game da mutanen ƙwarai shi ne sababi na farko na bayyana shirka a ban ƙasa; a cikin mutane Annabi Nuhu, lokacin da malamansu suka mutu, sai Shaiɗan ya yi wahayi ga mutanen su cewa su ƙafa alamomi a wuraren zamansu, su ƙira su da sunayensu, sai suka aikata hakan, amma ba su bauta musu, har sai da suka mutu, aka manta ilimi, sai aka bauta musu[2].

Lallai wannan yana daga cikin makircin shaidan; yana faraway da kira ne ga wuce gona da irin game da bayin Allah na ƙwarai, da girmama kaburburansu, sannan sai ya jefa a cikin zukatan mutane damfaruwa ga ƙaburburan da sunan son ma'abotanta, ko kuma raya cewa ana karɓar addu'a wurin ƙaburburan, sannan sai ya kai su zuwa ga ƙira da bautan ma'abota ƙaburburan, da riƙe ƙabarin a matsayin wani gunki da ake bautawa, ana kewaya shi, ana yanka a wurin shi!

Na Biyu: Gina masallatai akan kaburbura, da zana hotuna a cikinsu, lallai Manzon Allah (SAW) Ya tsawatar daga hakan

1 Ahmad (1851), da Nasa'i: (3057) ne suka rawaito shi.

2 Bukhari: (4920) ne ya rawaito shi

tsawatarwa mai tsanani, shi ya sa ma lokacin da Ummu Habibah da Ummu Salamah Allah Ya kara yarda a gare su, suka ambatawa Annabi (SAW) wani coci da suka gani a Habasha, a cikin sa akwai hotuna da zane-zane, sai ya ce: "**Lallai** wadancan (mutane) idan mutum kirki ya mutu a cikin su, sai su gina masallaci a kabarinsa, su yi wadancan hotunan, lallai wadancan sune mafi sharrin halittu a wurin Allah ranar Alkiyama"[1].

Haka kuma ya ce: "Ya Allah Kar ka sa ƙabarina ya zama wani bauta da ake bautawa, Allah Ya tsinewa wasu mutane da suka riki kaburburan Annabawansu a matsayin masallatai."[2]

Haka kuma ya ce: "Ku saurara! Lallai waɗanda ke gabaninku sun kasance suna rikar kaburburan Annabawansu a matsayin masallatai, ku saurara, kar ku riƙi ƙabarina a matsayin masallaci, lallai ni na hane ku daga hakan."[3]

Na Uku: Gine-gine a kan ƙaburbura, ko yi musu daɓe ko ɗaura musu hasumiya da makamancin haka, wannan ma yana cikin dalilan shirka na zahiri, an karbo da Jabir Allah Ya ƙara masa yarda, ya ce: "Annabi (SAW) ya hana a daɓe ƙabari, ko a zauna akansa, ko a yi gini akansa"[4].

1 Bukhari (3873), da Muslim (528) ne suka rawaito shi.

2 Bukhari (437), da Muslim (530) ne suka rawaito shi.

3 Muslim (532) ne ya rawaito shi.

4 Muslim (970) ne ya rawaito shi.

LARABA: DARASI CIKIN FIKHU

SALLAR WALAHA

❖ Ma’anarta:

Sallar ce da ake yin ta a farkon yini, tsakanin ɗagawan randa zuwa zawalin ta.

❖ Falalarta:

Hadisai masu yawa sun zo game da falala da mustahabbancin sallar Walha, ga wasu:

Hadisin Abu Hurairah Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: “Masoyina (SAW) ya mini wasiya da abubuwa uku: Azumin kwanaki uku a kowane wata, da raka’a biyu na walha, da kuma in yi wutir kafin in kwanta[1].

Da faɗin Manzon Allah (SAW): “Kowace gaba a jikin dan Adam na wayan gari akwai sadaka akan ta; dukkan tasbihi sadaka ne, dukkan hamdala ma sadaka ne, dukkan kabbara ma sadaka ce, umurni da kyakkyawa sadaka ne, hani daga mummuna ma sadaka ne, abin da zai wadatar ga hakan shi ne raka’a biyu na walha"[2].

❖ Lokacinta:

Lokacin ta na farawa ne daga ɗagawan rana gwarwadon mashi, ma’ana bayan bullowan rana da gwargwadon sa’a ɗaya, har zuwa gab da zawali wato "karkacewar rana daga tsakiyar sama"; wato dai kafin kiran sallar Azahar kenan da gwargwadon kwatan awa.

Mafi falalar lokacinta shi ne ƙarshen lokaci, idan zafi ya yi tsanani, saboda faɗin Manzon Allah (SAW): “Sallar masu yawan

1 Bukhari (1178) da Muslim (721) ne suka rawaito.

2 Muslim ne ya rawaito shi (720).

komawa ga Allah tana kasancewa ne lokacin da ƙananun rafkuma suke jin zafin kasa”[1].

Ma’ana lokacin da zafin rana ya tsananta, sai ƙananun rafkuma su kwanta saboda tsananin zafin.

1 Muslim ne ya rawaito shi (748).

ALHAMIS: DARASI CIKN SIRA

YAƘIN BANU ƘURAIZA

❖ Lokacin da ya auku:

Wannan yaƙi ya faru ne a shekara ta biyar na hijira, bayan Musulmi sun dawo daga yaƙin Ahzab.

❖ Sababban yaƙin

Sababin yaƙin shine warware alƙawari da Banu Ƙuraizah suka yi da shigar su cikin rundunonin taron dangi, sai Mala'ika Jibril ya zo wurin Annabi bayan dawowa daga yaƙin Ahzab, ya ce masa: "Ka ajiye makaminka? Na rantse da Allah mu kam ba mu ajiye ba, don haka ka fita gare su." Sai Annabi (SAW) ya ce: "Zuwa Ina?" Sai Jibrilu ya ce: "Nan, nan" sai ya yi ishara ga Banu Kuraizah[1].

❖ Abubuwan da suka faru a yaƙin:

Annabi (SAW) ya umurci mai shela, ya yi shela cikin mutane: "Kar wanda ya yi sallar La'asar sai a cikin Banu Ƙuraizah" [2]. ya daura Ibnu Ummi Maktum a garin Madina. Ya kuma zaburar da rundunar musulmai suka nufi gidajen Banu Ƙuraizah, su dubu uku. Tutuar ta kasance a wurin Aliyu dan Abi Ɗalib, su ka kewaye kasar su, da shugabansu Ka'ab ɗan Asad ya ga haka sai ya bijirowa mutanensa zabi uku:

- Ko dai su mika wuya su shiga addinin Muhammad.
- Ko kuma su kashe zurriyarsu, sai su fita su yi yaƙi.
- Ko kuma su afkawa Manzon Allah da sahabbansa a wata ranar Asabar Yayin da musulmi suka amincewa sharrinsu.

1 Bukhari ne ya rawaito shi (4117).

2 Bukhari ne ya rawaito shi (4119).

Mutanensa suka ki amincewa kowacce cikin zabin, haka wannan kawanyar ta ci gaba har tsawon dare ashirin da biyar, sai Allah Ya sanya tsoro da firgici a cikin zukatansu, suka kasa jure wannan takunkumi da aka musu, ƙarshe dai suka amince su ka karɓi zama ƙarƙashin hukuncin Manzon Allah (SAW).

❖ Sakamakon yaƙin:

Lokacin da suka sauka ga hukuncin Manzon Allah (SAW) sai Aus suka ce: 'Ya Manzon Allah, lallai Banu Ƙuraizah sun aika abin da ka san sun aikata, kuma su kawayen Khazraj ne, su kuma Khazraj kawayen mu ne, sai Annabi ya ce: "Shin ba za ku amince wani cikin ku ya yi hukunci game da su ba?" Sai suka ce: Mun amince. Sai Annabi ya ce: "Na damƙa hakan ga Sa'ad ɗan Mu'az" Su ka ce: Mun amince. Sai Annabi (SAW) ya aika Sa'ad ɗan Mu'az ya zo, ya kasance a madina a yi Rauni lokacin yaƙin Ahzab, ya hau jaki ya taho, su kuma su nace mishi: Ka kyauta wa bararrun bayinka, don kuwa Annabi (SAW) ya baka damar hukunci akan su.

Lokacin da Sa'ad ya isa wurin Annabi (SAW) sai suka sauko da shi, suka ce masa: Ya kai Sa'ad lallai waɗannan mutane sun shiga cikin hukuncinka. Ya ce: 'Kuma hukuncina zai zartu a kansu?' Suka ce: Eh, da ma akan musulmi. Sai Ya ce: Da kuma kan duk wanda ke nan? Ya yi nuni ga gefen da Manzon Allah (SAW) ya ke don girmamawa da darajta shi. Annabi (SAW) ya ce: "Eh, da kai na." Sai ya ce: 'Hukuncina shi ne a kashe mayaƙansu, sannan a kama zurriyarsu a matsayin bayi.' Sai Annabi (SAW) ya ce: "Ka yi hukunci da hukuncin Allah Mamallaki"[1].

1 Bukhari: (4122) da Muslim (1769) ne suka rawaito shi.

Sai Annabi (SAW) ya yi umurnin a kashe duk wanda gashin mara ya fito masa, a kyale wanda bai fito masa ba, aka sare musu kai a wanu rami da aka haka a kasuwar Madina, sun kai tsakanin su dari shida zuwa bakwai. Aka kashe tare da su tare da shugaban Banun-Nadir wato Huyayy ibn Akhdab, wanda ya kasance ya shiga cikin kariyar Banu Kuraizah lokacin yaƙin Ahzab, ya kuma ƙira su da su kwance alƙawari. A kuma raba dukiyar Banu Kuraizah a tsakanin musulmi; sojin kaf ana da kaso ɗaya, mahaya kuma suna da kaso uku, akwai mahaya talata da shi a cikin musulmi[1].

1 Al-Fusol (175).

ASABAR: DARASI CIKIN RAUWAR SAHABBAI

JA'AFAR ƊAN ABU ƊALIB

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Abu Abdillah, Ja'far ɗan Abu Ɗalib da Abdul-Muɗɗalib, dan amin Annabi, kuma shakikin Aliyu Allah Ya kara musu yarda.

An haife shi a Makkah shekara ta 34 gabanin hijira, don haka ya girmi dan uwansa Aliyu da shekara goma.

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Ja'far Allah Ya kara yarda a gare shi ya kasance ɗaya daga cikin waɗanda suka gabata ga musulunci, kuma Annabi (SAW) ya yi yaɗo a gare shi da cewa: "Ka na kama da ni a halitta da dabi'a"[1] Abu Hurairah ya ce: "Bayan Manzon Allah, ba wanda ya kai Ja'far bin Abi Ɗalib iya sa takalmi da taka ƙasa."[2]

Ya kuma kasance yana son miskinai, yana zama da su, yana musu hidima, Abu Hurairah ya faɗa game da shi: "Ja'far ya kasance mafi alkhairin mutane ga miskinai"[3]

Ja'far ya hijira zuwa Habasha, saboda kyawun ɗabi'ansa da karfin hujjarsa ne Najashi da waɗanda suka bi shi suka musulunta, yadda ya yi kariya kariya mai tsanani ga musulman da suka yi hijira zuwa Habasha, lokacin da ayarin Ƙuraishawa suka zo wurin Najashi suna neman ya mika su, sai Ja'afar Allah Ya kara yarda a gare shi ya karanta masa farkon Suratu Maryam, har sai da Najashi ya yi kuka, ya jiƙa gemunsa, suma fadafawansa suka yi

1 Ibnu Hibban ne ya rawaito shi (7046).

2 Al-Isabah (1/237).

3 Bukhari ne ya rawaito shi (5432).

kuka har suka jiƙa littattafansu, sai Najashi ya ce: "Lallai wannan maganar ta fito ne daga alkukin da Annabi Musa ya zo da shi'[1].

Sai Ja'afar ya zauna a Habasha har zuwa shekara ta bakwai na hijira, sannan ya dawo Madina lokacin Annabi na Khaibar, Annabi ya yi murna sosai yayin da gan shi, ya sumbancin tsakanin idanuwansa, yana cewa: "Ban san da wane cikin biyun nan zan yi farin ciki ba; da bude Khaibar ne ko da dawowan Ja'far?"[2].

❖ Rasuwarsa

Ja'far Allah Ya kara yarda a gare shi, ya yi shahada yana da shekara araba'in a yaƙin Mu'tah, a watan Jumadal Ula na shekara ta takwas. Abdullahi dan Umar ya na cewa: "Na tsaya akan Ja'far a wannan ranar alhalin an kashe shi, na kirga masa suka da duka guda hamsin a jikinsa, ba wanda ya kasance a bayansa"[3].

Annabi (SAW) ya yi bakin cikin a kan kashe sosai, ya kuma yi masa shaida da ni'imatuwa musamman a Aljannah, ya ce: "Na ga Ja'far ɗan Abu Ɗalib a matsayin mala'ika yana shawagi tare da mala'iku da fukafukai biyu"[4].

1 Siyaru A'lamin-Nubala (1/216).

2 Al-Biɗayah Wan-Nihayah (4/207).

3 Bukhari ne ya rawaito shi (4260).

4 Tirmizi ne ya rawaito shi (3763).

Auna fahimtarka cikin darussan mako na 29			Amsa ta kwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Menene ma'anar "Zil Autad"?**		C
	a. Ma'abocin dukiya mai yawa.	b. ma'abocin ginegine da binaye.	c. Ma'abocin sojoji da suke tsare mulkinsa.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Haƙƙin mutane ba ya faduwa sai da…?**		C
	a. Istigfari	b. Yawan ayyuka na kwarai	c. Maida haƙƙin da neman su yafe
Darasin Aƙida	**Tambaya: Daga cikin hanyoyi da kafofi da ke kaiwa ga shirka babba akwai:**		B
	a. Kusancin kaburbura	b. wuce iyaka game da salihai	c. almubazzaranci
Darasin Fiƙihu	**Tambaya: Wane ne Annabi ya yi masa wasiyya da sallar walha?**		A
	a. Abu Hurairah	b. Ibnu Mas'ud.	c. Jabir bin Abdullah.
Darasin Sira	**Tambaya: Dalilin yaƙin Banu Kuraizah shi ne:**		C
	a. Yaye tsiraicin musulma a kasuwa.	b. Kashe wani karamin yaro daga cikin musulmi.	c. Warware alkawari da shigan su cikin yaƙi.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin waɗanda suka musulunta a hannun Ja'afar akwai:**		A
	a. An-Najashi	b. Ibnul Julanda.	c. al-Mukaukis

MAKON NA TALATIN

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-FAJR (2)

﴿فَأَمَّا ٱلۡإِنسَٰنُ إِذَا مَا ٱبۡتَلَىٰهُ رَبُّهُۥ فَأَكۡرَمَهُۥ وَنَعَّمَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَكۡرَمَنِ ١٥ وَأَمَّآ إِذَا مَا ٱبۡتَلَىٰهُ فَقَدَرَ عَلَيۡهِ رِزۡقَهُۥ فَيَقُولُ رَبِّيٓ أَهَٰنَنِ ١٦ كَلَّاۖ بَل لَّا تُكۡرِمُونَ ٱلۡيَتِيمَ ١٧ وَلَا تَحَٰٓضُّونَ عَلَىٰ طَعَامِ ٱلۡمِسۡكِينِ ١٨ وَتَأۡكُلُونَ ٱلتُّرَاثَ أَكۡلٗا لَّمّٗا ١٩ وَتُحِبُّونَ ٱلۡمَالَ حُبّٗا جَمّٗا ٢٠ كَلَّآۖ إِذَا دُكَّتِ ٱلۡأَرۡضُ دَكّٗا دَكّٗا ٢١ وَجَآءَ رَبُّكَ وَٱلۡمَلَكُ صَفّٗا صَفّٗا ٢٢ ﴾ ﴿وَجِاْيٓءَ يَوۡمَئِذِۭ بِجَهَنَّمَۚ يَوۡمَئِذٖ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ وَأَنَّىٰ لَهُ ٱلذِّكۡرَىٰ ٢٣ يَقُولُ يَٰلَيۡتَنِي قَدَّمۡتُ لِحَيَاتِي ٢٤ فَيَوۡمَئِذٖ لَّا يُعَذِّبُ عَذَابَهُۥٓ أَحَدٞ ٢٥ وَلَا يُوثِقُ وَثَاقَهُۥٓ أَحَدٞ ٢٦ يَٰٓأَيَّتُهَا ٱلنَّفۡسُ ٱلۡمُطۡمَئِنَّةُ ٢٧ ٱرۡجِعِيٓ إِلَىٰ رَبِّكِ رَاضِيَةٗ مَّرۡضِيَّةٗ ٢٨ فَٱدۡخُلِي فِي عِبَٰدِي ٢٩ وَٱدۡخُلِي جَنَّتِي ٣٠ ﴾

❖ Fassara:

1. Amma kuma mutum idan Ubangijinsa Ya jarrabe shi sai Ya karrama shi, Ya kuma yi masa ni'ima, sai ya ce: "Ubangijina Ya karrama ni."
2. Amma kuma idan Ya jarrabe shi, sai Ya kuntata masa a arzikinsa, sai ya ce: "Ubangijina Ya wulakanta ni."
3. Faufau, ba haka ba ne; ku ba kwa karrama maraya ne.
4. Kuma ba kwa kwadaitar da juna kan ciyar da miskinai.
5. Kuma kuna cinye dukiyar gadon marayu mummunan ci.
6. Kuma kuna son dukiya so mai yawa.
7. Ba haka ne ba, idan aka girgiza kasa matukar girgiza.
8. Ubangijinka kuma Ya zo tare da mala'iku sahu-sahu.

9. Aka kuma zo da Jahannama a wannan ranar. To fa a wannan ranar ne mutum zai tuna (sakacinsa), ta yaya wannan tunawar za ta yi masa amfani?
10. Zai ce: "Kaitona, ina ma da na gabatar (da ayyukan alheri) a rayuwata!"
11. To a wannan ranar ba wani ɗaya da zai yi azaba irin azabarsa (watau Allah).
12. Ba kuma ɗaya da zai yi ɗauri irin ɗaurinsa.
13. (Za a ce): Ya kai wannan rai mai nutsuwa.
14. Ka koma zuwa ga Ubangijinka kana mai yarda (da sakamako), abin yarda.
15. Don haka ka shiga cikin bayina.
16. Ka kuma shiga aljannata.

❖ **Saƙon da surar take ɗauke da shi:**

Faɗakarwa game da hikimar jarabawa da tunatarwa game da lahira.

❖ **Bakin kalmomi:**

ابتلاه	**Ibtalahu**	Ya jarrabe shi
فقدره	**Fakadara**	Ya kuntata
ولا تحاضون	**Wa la tahadduna**	Ba kwa kwaɗaitar da junanku
تراث	**Turasa**	Dukiyar gado
صفا صفا	**Saffan Saffa**	Sahu masu yawa
أنى له الذكرى	**Anna lahuz zikra**	Tunawa ba zai amfane shi ba; don lokacin ta ya wuce
لما	**Lamma**	Mai tsanani

جما	**Jamma**	Na wuce iyaka
دكا	**Dukkat**	Aka girgiza
وجاء ربك	**Wa ja'a rabbuka**	Zuwa irin wanda ya dace da girmansa; don ya yi hukunci tsakanin bayi
ولا يوثق	**Wa la yusiku**	Ba za a ɗaure da sarƙoƙi da mari ba
وثاقه	**Wasakahu**	Irin ɗaurinsa da sarƙoƙi da mari.

❖ **Ma'anar ayoyin a dukule:**

Waɗannan ayoyi suna tabbatar da sunnonin Allah wurin jaraba bayinsa da alheri ko sharri, kuma lallai bayarwansa ko hanawarsa ba dalili ba ne a kan yarda ko fushi; bari dai, Yana yalwatawa ne don jarabawa da gwaji, haka kuma Yana kuntatawa don jarabawa da gwaji, Yana jarabarwa da bada ni'imomi, haka kuma Yana jarabawa da hani.

Bayan nan sai siyaƙin magana ya koma ga waɗanda ake magana da su cewa fa lallai halayensu da al'adarsu ga marayu da miskinai da kuma kaunarsu ga dukiyoyi da gado, na fayyace tsananin kwaɗayinsu da rowansu, da kuma yadda suke fifita wannan mai karewar a kan mai wanzuwa.

Sannan sai Allah Ya rufe surar da ambaton tashe-tashen hankular ranan alƙiyama da irin nadamar da masu sakaci za su yi a lokacin da za su fuskanci azaba a ranar, da irin burinsu na ina ma da sun gabatar da ayyuka na ƙwarai da za su tsirar da su a wannan yini, amma rai mai natsuwa wanda ya gabatar da ayyuka na ƙwarai, kuma

bai yi sakaci ba, to za a kira shi zuwa ga shiga aljanna cikin tawagar waɗanda aka karrama cikin bayin Allah.

Abubuwan da za mu koya daga Surar:

1) Lallai ba duk wanda aka yalwata masa arzikinsa ba ne mai daraja a wurin Allah, haka kuma ba duk wanda aka kuntata masa arzikinsa ba ne wulakantacce a wurin Allah.

2) Lallai daga cikin siffofin mumini akwai yarda da ƙaddara da hukuncin Allah, idan aka ba shi sai ya yi godiya, idan kuma aka jarabce shi sai ya yi hakuri.

3) Lallai yana daga cikin siffofin mumini darajta marayu, da kwadaitarwa wurin ciyar da masu jin yunwa daga fakirai da miskinai.

4) Lallai dan Adam zai yi nadama nadama mai tsanani a kiyama idan ya ga Jahannama, a lokacin da nadama ba za ta yi amfani ba.

5) Wajibcin bayar da gado ga waɗanda suka cancance ta maza da mata, yara da manya.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

HANI A KAN FATAN MUTUWA YAYIN SAUKAR CUTA

An karbo daga Anas (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Kada ɗayanku ya yi burin mutuwa don wata cuta da ta same shi, idan ya zama ba makawa sai ya yi burin mutuwar to ya ce: Ya Allah Ka raya ni matuƙar rayuwar ce alheri gare ni, Ka kashe ni idan mutuwa ce alheri gare ni**).[1]

❖ Sharhi:

A cikin wannan hadisi akwai hani game da burin mutuwa saboda wata cuta da ta sauka ga bawa; na rashin lafiya ne ko talauci, ko tsoro, ko faɗawa cikin wani tsanani ko hatsari; don a cikin hakan akwai barna mai yawa, daga ciki:

- Lallai cikin shi akwai fushi da fusata da hukuncin Allah da ƙaddararsa, shi kuwa mumini an umurce shi ne da haƙuri da neman lada.
- Lallai hakan na raunana rai, kuma yana jefa (mutum) cikin ɗebe tsammani, yana kuma haifar da ƙunci da kasala.
- Lallai saukan mutuwa na yanke wa bawa ayyuka na ƙwarai, waɗanda yake matuƙar buƙatar su.
- Lallai bawa bai san abin da zai tarar ba bayan mutuwarsa, ta yuwu ya guje wa wannan cutar zuwa ga abin da ya fi ta muni, na azabar ƙabari da wahalhalunsa.

Don haka, abin da ya kamata ga bawa: shine ya yi hakuri a kan wannan cutar da ta same shi, ya kuma miƙa al'amarinsa ga Allah, Wanda Ya san abin da yake alheri da maslaha gare shi; don haka ne ma Annabi (SAW) ya ce a ƙarshen hadisin: "…Idan ya zama ba makawa sai ya yi burin mutuwar to ya ce: Ya Allah Ka raya ni

1. Bukhari (6351) da Muslim (2680) ne suka rawaito shi.

madamar rayuwar ce alheri gare ni, Ka kashe ni idan mutuwa ce alheri gare ni.”

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1) Haramcin burin mutuwa saboda cuta da ta sauko wa musulmi, kamar talauci, ko rashin lafiya, ko tsoro.

2) Ana so idan baƙin ciki da damuwa suka yi tsanani ga musulmi ya yi haƙuri, ya kuma koma ga Allah da marairaicewa da addu’a.

3) Wajibcin tawakkali ga Allah da miƙa al’amura gare Shi, domin Shi ne Wanda Ya san alheri da amfani ga bawansa.

4) Lallai rayuwa kyauta ce daga Allah, kuma dama ce don dacewa mai girma; don haka ya kamata ga musulmi ya raya ta da imani da ayyuka na kwarai.

5) Sunna ta yi nuni a kan halaccin fatan mutuwa don tsoron fitina a cikin addini; saboda hadisin Manzo da ya ce: “Ya Allah idan Ka yi nufin wata fitina ga bayinka, to Ka ɗauke ni gare Ka, ba tare da ta shafe ni ba.”[1]

1. Tirmzi (3235) ne ya rawaito shi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

KAFIRCI, MA'ANARSA DA NAU'UKANSA

Kafirci (Alkufru): shi ne kishiyan imani. Kamar yadda imani ya ke magana ne da aiki da ƙudiri, haka shi ma kafirci yana kasancewa magana da aiki da ƙudiri da shakka da kuma bari. Kafirci na kasancewa da barin imani da Allah, ko rashin imani da wani abu cikin addininsa, ko ta dalilin ƙaryatawa, ko shakka ko girman kai ko son rai, haka kuma kafirci na faruwa da ayyuka ko maganganu waɗanda shari'a ta ƙirga su a matsayin kafirci.

Tsawatarwa mai tsanani da gargadi da jan kunne sun zo game da kafirci, Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai Allah Ya la'anci kafirai, Ya kuma tanadar musu da (wutar) Sa'ira. Masu dawwama ne a cikinta har abada; kuma ba za su sami wani majibinci ko mataimaki ba. A ranar da za a riƙa jujjuya fuskokinsu cikin wuta, suna cewa: Kaiconmu, ina ma da mun bi Allah, mun bi Manzo!))[1]

❋ **Kafirci ya kasu kashi biyu:**

Kafirci babba wanda ke fitarwa daga Musulunci, da kafirci ƙarami wanda ba ya fitarwa daga Musulunci.

Kashi na farko: Shi ne kafirci babba, shi kuma yana da nau'uka biyar:

Nau'i Na Farko: Kafircin karyatawa; dalilinsa shi ne faɗin Allah Maɗaukaki: ((Wane ne ya fi zalunci kamar wanda ya ƙaga wa Allah ƙarya ko kuma ya ƙaryata gaskiya lokacin da ta zo masa? Yanzu ashe babu mazaunar kafirai a ciki Jahannama?))[2].

1 [Al-Ahzab: 64-66].

2 [Al-Ankabut: 68].

Nau’i Na Biyu: Kafircin ƙi da girman kai; dalilina shi ne faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma ka tuna lokacin da Muka ce wa Mala’iku: “Ku yi sujada ga Adam” Sai duk suka yi sujjada, in ban da Iblis, sai ya ƙi, ya kuma yi girman kai, kuma ya tabbata cikin kafirai)).[1]

Nau’i Na Uku: Kafircin Shakka; dalilinsa faɗin Allah Maɗaukaki: ((Ya kuma shiga gonarsa yana mai zaluntar kansa, ya ce: "Ba na tsammanin cewa wannan za ta ƙare har abada. Kuma ba na tsammanin alƙiyama za ta tashi, kuma ko da an mayar da ni wurin Ubangijina to lallai zan sami canji fiye ma da ita.” Abokinsa ya ce da shi yana mai mahawara da shi: “Yanzu ka kafirce wa Wanda Ya halicce ka daga ƙasa, sannan (kuma) daga maniyyi, sannan Ya daidaita ka (ka zama) mutum? Sai dai ni kam Allah Shi ne Ubangijina, ba kuwa zan haɗa wani da Ubangijina ba))[2].

Nau’i Na Huɗu: Kafircin Bijirewa (Kau Da Kai); dalilinsa faɗin Allah Maɗaukaki: ((Waɗanda kuwa suka kafirta suna bijire wa abin da aka yi musu gargaɗi da shi ne))[3].

Nau’i Na Biyar: Kafircin Munafunci; dalilansa faɗin Allah Maɗaukaki: ((Wannan kuwa saboda cewa sun yi imani sannan suka kafirta, sai aka rufe zukatansu, saboda haka su ba sa fahimta))[4].

Kashi na biyu: Shi ne ƙaramin kafirci, ana kuma kiran shi da kafircin aiki, shi ne duk wani abu da shari’a ta kira shi da sunan kafirci, amma bai kai matsayin kafirci babba ba, yana da misalai, ga wasu daga ciki:

1 [Al-Baƙarah: 34].

2 [Al-Kahf: 35-38].

3 [Al-Ahƙaf: 3].

4 [Al-Munafikun: 3].

- Abin da ya zo cikin fadin Annabi (SAW): (Abubuwa biyu a cikin mutane; kafirci ne; sukar danganta, da kuka ga mamaci).[1]
- Rantsuwa da wanin Allah, Annabi (SAW) ya ce: (Duk wanda ya rantse da wani ba Allah ba ya kafirta ko ya yi shirka).[2]
- Yakar musulmi; Annabi (SAW) ya ce: (Zagin musulmi fasikanci ne, yakar shi kuma kafirci ne).[3]

1 Muslim ne ya rawaito shi (67).

2 Tirmizi (1535) da Abu Dawud (3251) ne suka rawaito shi.

3 Bukhari: (48) da Muslim: (64) ne suka rawaito shi.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

LOKUTAN DA AKA HANA YIN SALLA A CIKINSU

❖ Bayanan lokutan hani:

Shari'ah ta zo da bayanin lokuta da aka hana yin sallolin nafila a cikin su; su ne kamar haka:

Lokaci Na Farko: Daga ɓullowar alfijir zuwa ɓullowar rana da ɗagawanta gwargwadon mashi, ana kimanta shi da kamar ɗaya bisa huɗun sa'a bayan bullowar rana.

Lokaci Na Biyu: Yayin daidaiton ranar a tsakiyar sama, wato dai gabanin azahar da kimanin ɗaya bisa huɗun sa'a, har zuwa lokacin kaucewar rana daga tsakiyar sama, kuma lokacin Azahar ya shiga.

Lokaci Na Uku: Bayan sallar La'asar har faduwar rana.

❖ Dalilai:

Amma dalilai a kan hakan su ne kamar haka:

- Faɗin Manzon Allah (SAW): (Babu salla bayan bayyanar alfijir har sai rana ta hudo, kuma babu salla bayan La'asar har sai rana ta faɗi)[1].
- Da hadisin Uƙuba ɗan Amir ya ce: "Lokuta uku, Manzon Allah (SAW) ya hana mu salla da birne mamatanmu a cikinsu; lokacin da rana ta ke ɓullowa har sai ta daga, da lokacin da ganjin rana ke tsayawa, har sai ranar ta karkata, da lokacin da take ƙoƙarin faɗuwa har sai ta faɗi"[2].

1. Bukhari (586) da Muslim (827) ne suka rawaito shi.

2. Muslim ne ya rawaito shi (831).

❖ **Hukuncin yin salla a lokutan hani:**

Ba ya halatta a yi sallar nafila a cikin waɗannan lokuta, sai dai abubuwan da dalili ya togace su, waɗanda su ne kamar haka:

- Rama salloli na farilla tare da nafulfuli da suke tare da su, saboda faɗin Manzon Allah (SAW): (Duk wanda ya bar salla saboda bacci ko kuma ya manta ta, to ya yi ta idan ya tuna).[1]
- Yin sallolin da suke da sababi na musamman, kamar sallar jana'iza, gaisuwar Masallaci, da raka'o'i biyu na ɗawafi.

❖ **Hikimar keɓance waɗannan lokuta da hani:**

Manzon Allah (SAW) ya bayyana hikimar hana yin salla a cikin waɗannan lokuta, inda ya bayyana cewa: Kafirai suna bauta wa rana ne yayin fitowarta da kuma lokacin faduwarta, saboda haka ya hana Musulmi kamanceceniya da su a waɗannan lokutan.

Sai Annabi (SAW) ya ce: (Lallai rana tana fitowa a lokacin fitowarta a tsakanin ƙahonin shaiɗan, kuma a wannan lokacin kafirai suna yin sujada gare ta). Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Saboda lallai ita tana fuɗuwa a tsakani kahonni biyu na shaɗan, kuma a wannan lokacin kafiran suna mata sujjada). [2]

Amma game da lokacin daidaituwar rana a tsakiyar yini, haƙiƙa Manzon Allah (SAW) ya ce: (Saboda a wannan lokaci ana rura wutar Jahannama).[3]

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (684).
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (832).
[3]. Muslim ne ya rawaito shi (832).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

MUBAYA'A TA RIDWAN

❖ Lokacin faruwarta:

Ta a faru ne a watan Zulƙa'da, na shekara ta shida bayan hijira.

❖ Dalilan faruwarta:

Labarinta ya fara ne a lokacin da Manzon Allh (SAW) ya yi mafarkin cewa ya shiga Masallaci mai alfarma tare da sahabbansa, kuma ya karɓi makullan ɗakin Ka'aba, kuma sun yi ɗawafi da umara, sai ya ba wa sahabbai labarin haka, sai suka yi farin ciki suka yi murna, kuma suka zaci cewa hakan zai faru a wannan shekarar tasu, sai Manzon Allah (SAW) ya sanar da sahabbansa cewa zai yi umara, sai suka yi shirin tafiya tare da shi.[1]

❖ Abubuwan da suka faru:

Manzon Allah (SAW) da Sahabbansa sun nufi Makka cikin ihrami ba tare da makami ba, adadinsu ya kai kimanin dubu ɗaya da ɗari biyar, a lokacin da suka kusanci Makka, sai Ƙuraishawa suka ji labarin haka, sai suka tattaro abokan ƙawancensu, suka fito daga Makka domin hana su yin Umara, sai Khalid bin Walid wanda bai musulunta ba a lokacin, ya tunkari Musulmai da rundunar mahaya mutum ɗari a wani waje da ake kira "Kura'ul Gamim", sai Manzon Allah (SAW) ya kauce masa ya sauya hanya, sai ya bi hanyar "Hudaibiyya" daga ƙasan Makka, shi kuma Khalid sai ya koma yana mai gargaɗi ga Ƙuraishawa.[2]

Sai Ƙuraishawa suka aika 'yan aike zuwa ga Manzon Allah (SAW) don su hana su shiga Makka, shi kuma Manzon Allah (SAW) ya

---

[1]. Tafsirin Ɗabari (22/257).
[2]. Buhari ne ya rawaito (2731).

tabbatar musu da ce shi bai zo don yaƙi ba, sai ya aika musu Usman bin Affan (RA) a matsayin jakada don ya tabbatar musu da manufarsa, sai Usman ya shiga Makka, sai suka bijiro masa cewa ya yi ɗawafi, sai ya ƙi, ya ce: har sai Manzon Allah (SAW) ya yi, sai Ƙuraishawa suka riƙe shi a wajensu.[1]

❖ Sakamakonta:

Labari ya iso wa Manzon Allah (SAW) da sahabbansa cewa an kashe Usman (RA), a wannan lokacin sai Manzon Allah (SAW) ya kira sahabbansa zuwa ga yin mubaya'a, sai sahabbai suka masa mubaya'a a kan cewa ba za su gudu ba, wasunsu kuma suka masa mubaya'a a kan mutuwa, sai Manzon Allh (SAW) ya kama hannunsa, ya ce: (Wannan a maimakon Usman).[2]

Kuma wannan mubaya'a ta auku a ƙarƙashin bishiya, kuma an saka mata suna "Mubaya'a ta ridwan", Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce game da ita: ((Haƙiƙa Allah Ya yarda da muminai yayin da suke yi maka mubaya'a a ƙarƙashin bishiyar nan, to Allah Ya san abin da yake cikin zukatansu, sai Ya saukar musu da nutsuwa Ya kuma saka musu da buɗi na kurkusa)).[3] Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wanda zai shiga wuta daga cikin waɗanda suka yi mubaya'a a ƙarƙashin bishiyar nan).[4]

---

[1]. Albidaya Wan Nihaya (4/167).
[2]. Albidaya wan Nihaya (4/168).
[3]. Suratul Fath: 18.
[4]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (4653).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

HAMZA ƊAN ABDUL-MUƊƊALIB (RA)

❖ Sunansa da Haifuwarsa:

Shi ne sahabi mai daraja Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib ɗan Hashim ɗan Abdu-Manaf, baffan Manzon Allah (SAW), kuma ɗan uwansa na reno, ana kiran shi da "Zakin Allah kuma Zakin Manzon Allah SAW", kuma ana masa alkunya da Baban Umara ko Baban Ya'la, saboda 'ya'yansa Umara da Ya'la.

An haife shi a Makka a shekara ta 54 kafin hijira.

❖ Tarihinsa da falalarsa:

Hamza (RA) ya kasance mutum ne mai karamci kuma mai saukin hali, mai ƙarfin gabbai, mai jan fuska, gwarzo a filin daga, idanuwansa na yin ja idan ya yi fushi.

Ya halarci yaƙoƙi da daban-daban kafin musulunci; kamar yaƙin Fijar da makamantansa, kuma ya kasance mafi ƙarfin gwarzon matashi a cikin Ƙuraishawa, kuma mafi tsananin jarumi, kuma mafi ƙarfi a wajen kai farmaki.

Ya musulunta a ƙarshen shekara ta shida bayan aiko Manzon Allah (SAW); don taimakon Annabi (SAW) wajen ba shi kariya daga Fir'aunan wannan al'umma, wato Abu Jahal, a lokacin da ya cutar da Annabi (SAW) kuma ya ci mutuncinsa, har ma ya fasa masa kai da dutse, sai Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib ya ji labarin haka, sai ya kama hanya yana sauri, kuma bai tsaya a wajen kowa ba a kan hanyarsa, sai ya ce wa Abu Jahal: Shin ɗan ɗan'uwana za ka zaga

alhali ina kan addininsa?! Sai ya bige shi da bakansa ya fasa masa kai mumminan fasawa.[1]

Musuluntar Hamza a farkon lamari ta kasance kashi ne kawai, sai kuma Allah Ya buɗe zuciyarsa ga addini daga baya, kuma musulmai suka samu ƙarfi da shi, har sai da bala'i ya tsananta ga Ƙuraishawa, suka kame daga wani ɓangare na cutarwarsu.

Hamza (RA) ya halarci yaƙin Badar, kuma ya yi bajinta matuƙar gaske a cikinta, har ma wani daga cikin fursunonin yaƙin kafirai ya ce: Wane ne mutumin nan da ke da alamar gashin jumuna? Suka ce: Hamza ne. Ya ce: Wannan mutumin ya yi mana ɓarna sosai!.[2]

Har-wa-yau, Hamza ya halarci yaƙin Uhudu, a wannan yaƙin ya kasance yana yaƙi a gaban Manzon Allah (SAW) da takobi guda biyu, yana cewa: "Ni ne Zakin Allah"[3], sai ya kashe mutum talatin da ɗaya daga cikin mushirkai, a yayin da yake cikin wannan yaƙi sai kwatsam ya yi tuntuɓe har ya faɗi a kan gadon bayansa, sai sulkensa ya yaye daga tunbinsa, sai Wahashi yaron gidan Jubairu ɗan Muɗ'im ya jefa masa mashi sai ya kashe shi, kuma mushirkai suka lalata gangar jikinsa, yayin da Annabi (SAW) ya gan shi sai baƙin cikinsa ya tsananta game da abin da ya gani, kuma ya damu damuwa mai tsanani, sai ya ce: (Shugaban shahidai shi ne Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib).[4]

❖ Rasuwarsa:

Hamza (RA) ya yi shahada a ranar yaƙin Uhudu, kuma ya kasance yana ɗan shekara hamsin da tara a lokacin da aka kashe shi, sai aka

---

[1]. Hilyatul Auliya (2/673).
[2]. Zadul ma'ad (3/166).
[3]. Hakim ne ya rawaito shi (3/194).
[4]. Hakim ne ya rawaito shi (4884).

binne shi, shi da ɗan ‘yar’uwarsa Abdullahi ɗan Jahash a ƙabari guda.

Auna fahimtarka a darusan mako na 30			Amsa na ƙwarai
DARASIN TAFSIRI	Tambaya: Mece ce ma'anar (Ƙadara alaihi rizƙahu)"		A
	a. Ya ƙuntata	b. Ya yalwata	c. Ya ƙarar
DARASIN HADISI	Tambaya: Mustahabbi ne ga mumini idan damuwa ta tsananta gare shi ya yi:		B
	a. Ya miƙa wuya ya sallama mata.	b. Ya yi haƙuri, kuma ya nemi mafaka a wajen Allah ta hanyar ƙanƙan da kai da addu'a.	c. Ya fita daga garinsa zuwa wani gari daban.
DARASIN AƘIDA	Tambaya: Daga cikin nau'ukan babban shirka akwai:		B
	a. Boyayyar shirka	b. Taurin kai da girman kai	c. Kukan mutuwa
DARASHIN FIƘIHU	Tambaya: Daga cikin lokuta da ake hana yin sallar nafila a cikinsu akwai:		A
	a. Bayan sallar asuba	b. Bayan sallar azahar	c. bayan sallar Magariba
DARASIN SIRA	Tambaya: Daga cikin sabuban mubaya'a ta Ridwan akwai:		C
	a. Zuwan rundunar rumawa	b. Haɗuwar ƙungiyoyi	c. Jita-jitan kashe Usman
DARASIN TARIHIN SAHABBAI	Tambaya: Hamza (RA) ya yi shahada a ranar:		B
	a. Yaƙin Badar	b. Yaƙin Uhudu	c. Yaƙin Khandaƙ

MAKO NA TALATIN DA DAYA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-GASHIYA (1)

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡغَٰشِيَةِ ١ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ ٢ عَامِلَةٞ نَّاصِبَةٞ ٣ تَصۡلَىٰ نَارًا حَامِيَةَۢ ٤ تُسۡقَىٰ مِنۡ عَيۡنٍ ءَانِيَةٖ ٥ لَّيۡسَ لَهُمۡ طَعَامٌ إِلَّا مِن ضَرِيعٖ ٦ لَّا يُسۡمِنُ وَلَا يُغۡنِي مِن جُوعٖ ٧ وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٖ نَّاعِمَةٞ ٨ لِّسَعۡيِهَا رَاضِيَةٞ ٩ فِي جَنَّةٍ عَالِيَةٖ ١٠ لَّا تَسۡمَعُ فِيهَا لَٰغِيَةٗ ١١ فِيهَا عَيۡنٞ جَارِيَةٞ ١٢ فِيهَا سُرُرٞ مَّرۡفُوعَةٞ ١٣ وَأَكۡوَابٞ مَّوۡضُوعَةٞ ١٤ وَنَمَارِقُ مَصۡفُوفَةٞ ١٥ وَزَرَابِيُّ مَبۡثُوثَةٌ ١٦﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai rahama Mai jinƙai

1. Shin labarin mai lullubewa da tsoro ya zo maka?
2. Wasu foskoki a wannan ranar ƙasƙantattu ne.
3. Masu aiki ne tukuru masu shan wahala.
4. Za su shiga wuta mai tsananin ƙuna.
5. Za a shayar da su daga idon ruwa mai tsananin zafi.
6. Ba su da wani abinci sai na ƙayar tsidau.
7. Ba ya sa ƙiba kuma ba ya maganin yunwa.
8. Waɗansu fuskokin kuwa a wannan ranar ni’imtattu ne.
9. Masu gamsuwa ne da (sakamakon) ayyukansu.
10. (Suna) cikin Aljanna maɗaukakiya.

11. Ba a jin zancen banza a cikinta.

12. A cikinta akwai marmaro mai gudana.

13. A cikinta akwai gadaje maɗaukaka.

14. Da kofuna a ajijjiye.

15. Da matasan kai a jejjere.

16. Da dardumai a shisshimfiɗe.

❖ Saƙon da ayoyin suka ƙunsa:

Tunatarwa game da lahira, da abin da ke cikinta na lada da uƙuba.

❖ Baƙin kalmomi:

الغاشية	Algashiya:	Ita ce alƙiyama wacce take lulluɓe mutane da ababen tsoronta
خاشعة	Khashi'a:	A ƙasƙance a wulaƙance
عاملة ناصبة	Amilatun nasiba:	Masu ƙoƙari da gajiya wurin aiki amma za su shiga wuta
تصلى نارا	Tasla naran:	Za su shiga wuta kuma zafinta zai ƙona su
حامية	Hamiya:	Mai tsananin ruruwa
آنية	Aniya:	Mai tsananin zafi
ضريع	Darih:	Wani tsuro ne mummuna mai ƙayoyi
لسعيها	Lisa'yiha:	Saboda ayyukan nagartattu da suka yi a duniya
لاغية	Lagiya:	Maganar wargi da na ƙarya

فيها عين جارية	Fiha ainun jariya:	Masu ɓuɓɓugo da ruwa
فيها سرر مرفوعة	Fiha sururun marfu’a:	Ababen zama madaukaka
وأكواب موضوعة	Wa akwabun maudu’a:	Kofuna da aka tanade su ga masu sha
ونمارق مصفوفة	Wa namariƙu:	Filolluka
وزرابي مبثوثة	Wa zarabiyyu mabsusa	Dardumomi shimfiɗaɗɗu

❖ Ma’anar ayoyin a dunƙule:

Waɗannan ayoyi suna bayanin cewa fuskokin kafirai za su kasance ƙaskantattu a ranar ƙiyama, saboda abin da zai same su na taɓewa da wulaƙanci, za su kasance a gajiye kuma a ɗaɗɗaure cikin sarƙoƙi da dabaibayi, zasu ƙone cikin wuta mai tsananin zafi, kuma za su sha daga wani marmaron ruwa mai tsananin ƙuna, abincinsu kuma ba komai ba ne a Jahannama face bishiyar ƙaya, daga mafi sharrin abinci kuma mafi muninsa, wanda ba shi da wani abu da abinci yake da shi na amfani, domin shi ba ya amfanar da jiki, kuma ba ya tunkuɗe yunwa.

Amma muminai a wannan ranar; suna cikin yanayi na ni’ima da murna da farin ciki, alamunsu suna bayyana a fuskokinsu, suna masu yarda da sakamakon Allah ga ayyukansu, maganarsu magana ce mai kyawu da amfani, yana faranta rai kuma yana saka murna, yana ƙunshe da ambaton Allah, da ambaton ni’imominsa masu yawa

a gare su, maramaran ruwa suna ɓuɓɓugowa a gefensu, suna jujjuya ta inda suke so, haƙiƙa an tanada musu wajajen zama, an ƙawata su da nau'uka mabanbanta na ababen kwalliya da girmamawa, na kofuna, da gadaje, da filolluka, da katifu, abin da zai faranta musu rai, kuma zukatansu su yi farin ciki.

❖ Abubuwan da za mu koya daga ayoyin:

1. Tunatarwa game da nau'ukan azabar da za a yi wa taɓaɓɓu, da ƙasƙanci da wulaƙanci, da ayyuka masu wahala, da ƙonuwa da wuta, da shayar da ruwa mai tsananin zafi, da ciyar da su wani tsuro mai ƙayoyi.

2. Cewa lallai fuskokin muminai a aljanna za su kasance ni'imtattu, ta yadda har alamun ni'ima da murna da farin ciki zai bayyana a cikinsu.

3. Cewa lallai ni'imomin aljanna kala-kala ne, daga cikinsu akwai ababen ci, ababen sha, da bishiyoyi, da benaye, da ƙoramu, da kyawawan mata, daga cikinsu kuma akwai abin da ya fi waɗannan gaba ɗayansu girma, shi ne ganin Allah Maɗaukakin Sarki da yardarsa gare su.

4. Cewa daga cikin abubuwa da suke damun rayukan mutane akwai: yasasshen zance, da maganar ƙarya, da ta banza, kuma haƙiƙa Allah Ya tsaftace kunnuwan muminai a aljanna daga gare su.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR AMBATON ALLAH

An karɓo daga Abu Musa Al'ash'ari (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Misalin wanda yake ambaton Ubangijinsa, da wanda ba ya ambatonsa, kamar misalin rayayye da matacce ne**).[1]

❖ Sharhi:

Wannan yana daga cikin mafi girman hadisai game da bayani a kan mahimmancin zikiri da falalarsa; ta yadda aka sanya zikiri ya zama kamar ruhi ga gangan jiki, a duk lokacin da bawa ya kasance mafi ambaton Allah, to zai zama mafi rayuwa, sai ya ga kyakkyawan aiki a matsayin kyakkyawa, mummuna a matsayin mummuna, gaskiya a matsayin gaskiya, haka kuma ƙarya a matsayin ƙarya, kuma duk lokacin da ya nisanci ambaton Allah Maɗaukaki Sarki, sai ya zama kamar matacce, wanda ba shi da rayuwa, kuma ba shi da amfani, ga shi rayayye da gangan jikinsa, amma matacce ta zuciya, kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Shin yanzu wanda ya kasance matacce (kafiri), sai Muka rayar da shi, kuma Muka sanya masa haske (na shiriya), yana tafiya da shi cikin mutane, (yanzu) zai zama kamar wande yake cikin duhu (na kafirci), ta yadda ba zai fita daga cikinsa ba)).[2]

❖ Abubuwan da za mu koya daga wannan Hadisin:

1. Wannan hadisi dalili ne a kan cewa zikiri shi ne rayuwar ruhi, kamar yadda ruhi shi ne rayuwar jiki, wannan kaɗai ya isa ya zama zaburarwa da kwaɗaitarwa.

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (6407).
[2]. (Al'an'am: 122).

2. Cewa zuciya idan gafalarta ta tsawaita daga barin ambaton Allah, sai ƙeƙashewa mai nisantarwa daga aikin alheri ya tsananta gare ta.

3. Cewa lallai kuɓuta daga mutuwar zuciya da ƙeƙashewarta tana kasantuwa ne da ambaton Allah Maɗaukakin Sarki.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

MUNAFURCI; MA'ANARSA DA NAU'UKANSA

❖ Hatsarin Munafurci:

Allah Maɗaukaki Ya bayyana munafukai a cikin fiye da aya guda yana siffanta su da siffofin sharri gaba ɗaya, Sai Ya ce: ((Lallai munafukai suna cikin matakin ƙarshe na can ƙarƙashin wuta)).[1]

Ya kuma ce: ((Suna ganin suna yaudarar Allah ne da waɗanda suka yi imani, amma kuwa ba kowa suke yaudara ba sai kawunansu, kuma su ba sa jin hakan () Akwai wata cuta (ta munafurci) a cikin zukatansu, sai Allah Ya ƙara musu wata cutar, kuma suna da wata azaba mai raɗaɗi saboda ƙaryar da suke yi)).[2]

Kuma saboda hatsarin munafurci, Sahabbai Allah ya ƙara musu yarda suna tsoron su faɗa cikinsa. Ibn Abi Mulaika ya ce: "Na riski mutum talatin daga Sahabban Manzon Allah (SAW), duk suna jin tsoron munafurci wa kawunansu".[3]

❖ Nau'ukan Munafurci:

Munafurci nau'i biyu ne: Na ƙuduri (i'tiqadi), da na aiki (amali).

Nau'i farko: Munafurcin Ƙuduri shi ne bayyana Musulunci da ɓoye kafirci. Wannan shi ne babbar munafurci, kuma daga cikin sifofinsa akwai:

❖ Ƙaryata Manzon Allah (SAW) ko kuma ƙaryata wani ɓangare daga abin da ya zo da shi.
❖ Yin ƙiyayya ga Manzon Allah (SAW) ko kuma ƙiyayya da wani ɓangare daga abin da ya zo da shi.

---

1. (Annisa'i: 145).
2. (Albaƙara: 9-10).
3. Bukhari ne ya rawaito shi da ta'aliƙi (48).

❖ Ƙin taimakon addini da jindaɗi idan ya raunata.

Nau’i na biyu: Munafurci na aiki, wato ƙaramin munafurci, abin da ake nufi da shi shi ne ayyukan da aka bayyana a cikin ayoyi ko hadisan da suka siffanta munafukai, amma ba tare da ta kore musu imani daga zuciya gaba ɗaya ba, wannan nau’in ba ya sa mutum ya fita daga Musulunci, amma hanya ce zuwa ga hakan.

Sifofinsa sun haɗa da:

Abin da Annabi (SAW) ya ce cikin faɗinsa: (Alamomin munafuki guda huɗu ne: idan ya yi magana, sai ya yi ƙarya; idan ya yi alƙawari, sai ya saɓa; idan aka amince masa, sai ya ci amana; idan ya yi husuma, sai ya yi fajirci).[1]

Daga cikinsa harwayau akwai barin salla cikin jama’a a masallaci, domin wannan yana daga cikin siffofin munafukai.

❖ **Bambanci tsakanin Babban munafurci da ƙaraminsa:**

Nassoshi sun nuna akwai bambanci tsakanin babban munafurci da ƙarami, daga cikin mafi mahimmancinsu akwai:

1. Cewa babban munafurci yana fitar da mutum daga Musulunci gaba ɗaya, ƙaramin kuwa ba ya fitar da mutum daga Musulunci.

2. Cewa babban munafurci yana da alaƙa da ƙuduri na zuciya, shi kuma ƙaramin yana da alaƙa da ayyuka ne kawai.

3. Cewa babban munafurci ba ya samuwa a wajen mai imani, shi kuma ƙarami yana iya samuwa daga muminin gaskiya.

4. Cewa babban munafurci yawanci mai shi ba ya tuba, saɓanin ƙaramin munafurci, lallai ma’abocinsa yana iya tuba.

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (34) da Muslim (58).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SALLAR JUMA'A

❖ Falalarta:

Ranar Juma'a ita ce mafi falala daga cikin ranakun mako, Annabi (SAW) ya ce: (Mafi alheri daga cikin ranakunku shi ne ranar Jumma'a; a cikinta aka halicci Adamu, a cikinta aka shigar da shi Aljanna, a cikinta aka fitar da shi daga gareta).[1] Kuma Annabi (SAW) ya kuma cewa: (Allah Ya kautar da al'ummu da suka shuɗe gabaninmu daga zaɓar ranar Juma'a, Yahudawa sun zaɓi Asabar, Nasara sun zaɓi Lahadi, sai Allah Ya kawo mu, sai kuma Ya datar da mu da ranar Jumma'a).[2]

❖ Hikimar Juma'a:

Juma'a ita ce mafi girma lokutan haɗuwar musulmi da kuma alamun haɗin kantsu. Allah ya shar'anta taruwa domin salla a cikinta, kuma ya umurci muminai da halartar ta umurni na tilas, kuma ya shar'anta wa wannan haɗuwa yin huɗuba don tunatar da su da girman ni'imomin Allah a kansu, da kuma kwaɗaitar da su a kan godiya a bisa waɗannan ni'imomi, kuma Ya umurce su umurni na tilas da su saurare ta.

❖ Hukuncinta:

Sallar Juma'a farilla ce ta wajibi a kan maza, kamar yadda Allah ya ce: ((Ya ku waɗanda suka yi imani! Idan aka kira salla a ranar Jumma'a, ku yi gaggawar zuwa ambaton Allah, ku bar sayayya, wannan ne mafi alheri a gare ku idan kun kasance kuna da sani)).[3]

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (1410).
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (865).
[3]. (Aljum'a: 9).

Kuma Annabi (SAW) ya yi gargaɗi mai tsanani a kan barinta, ya ce: (Mutane su daina barin zuwa Jumma'a, ko kuwa Allah zai yi rufi a kan zukatansu, sannan su kasance daga cikin gafalallu).[1]

❖ Hukunce-hukuncenta:

Juma'a tana da hukunce-hukunce waɗanda ya kamata kowane musulmi ya san su kuma ya riƙa aikata su:

1. Wajibi ne a yi shiru don sauraron huɗuba, kuma haramun ne yin magana yayin da liman yake huɗuba, saboda faɗin Annabi (SAW) ya: (Idan ka ce wa abokinka: yi shiru, alhali liman yana huɗuba, to haƙiƙa ka yi yasasshen zance).[2] Wato: Ka faɗi magana yasasshiya, wacce ita maganar banza abin mayarwa.

2. Haramun ne a ketare mutane yayin huɗuba, saboda yana cutar da masu salla, da kuma shagaltar da su daga sauraron huɗuba, kuma haƙiƙa Annabi (SAW) ya ce wa mai tsallake mutane: (Zauna, domin haƙiƙa ka cutar).[3]

3. Ba a so ana raba Tsakanin mutum biyu, ta hanyar ƙuntata musu da shiga tsakaninsu alhali babu wani giɓi a tsakanin nasu, saboda faɗinsa (SAW): (Duk wanda ya yi wanka ranar Jumma'a, ya tsarkake jikinsa da abin da ya sawwaƙa, sannan ya shafa ko ya sanya turare, sannan ya fita masallaci, bai raba tsakanin mutane biyu ba, sai ya sallaci abin da aka rubuta masa, sai ya yi shiru bayan fitowar liman, to za a gafarta masa abin da ke tsakanin wannan Juma'a da wacce ta gabace ta).[4]

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (860).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (394) da Muslim (851).
[3]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (1118) da Nasa'i (3/103).
[4]. Bukhari ne ya rawaito shi (910).

4. Duk wanda ya riski raka'a ɗaya tare da liman, to ya samu sallar Jumma'a, saboda faɗin Manzo (SAW): (Duk wanda ya riski raka'a guda daga salla Juma'a, to haƙiƙa ya riski sallar Juma'a).[1]

5. Sallar Jumma'a ba ta da sallar nafila ta ratibi gabaninta, amma mutum zai iya yin sallar nafila sakakkiya yadda ya so; saboda kwaɗaitarwar da Annabi (SAW) ya yi game da haka cikin faɗinsa: (Sai ya sallaci abin da sawwaƙa),[2] amma nafila ta ratibi bayanta, to mutum zai yi salla raka'a biyu ko kuma huɗu, saboda zuwan hakan gaba ɗaya daga Annabi (SAW).[3]

[1]. Nasa'i ne ya rawaito shi (1425).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (910).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (937) da Muslim (881-882).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

SULHUN HUDAIBIYYA:

❖ Lokacin da aka yi shi:

An yi shi ne a watan Zulƙa'da, a shekara ta shida bayan Hijira.

❖ Dalilansa:

Bayan Mubaya'a ta Ridwan, Ƙuraishawa sai suka yi gaggawar aika Suhailu ɗan Amr domin yin yarjejeniya ta sulhu tare da Manzon Allah (SAW), yayin da Annabi (SAW) ya gan shi, sai ya ce yana mai fatan samun mafita: (Haƙiƙa al'amuranku za su sauƙaƙa gare ku).[1]

❖ Abubuwan da suka faru:

An cimma yarjejeniya tsakanin Musulmai da Ƙuraishawa, kuma an yi ittifaƙi a kan abubuwa kamar haka:

1. Annabi (SAW) zai koma a wannan shekara ba zai shiga Makka ba, saboda kada larabawa su ce ya shiga ne da ƙarfi. Amma idan shekara ta zagayo musulmi za su shige ta, sai su yi kwana uku a cikinta, da makamai na mahaya, wato takubba, kuma Ƙuraishawa ba za su cutar da su ba.

2. Za a dakatar da yaƙi Tsakanin ɓangare biyun tsawon shekara goma, mutane su zauna lafiya a cikinsu.

3. Cewa duk ƙabilar da ta so ta shiga ƙarƙashin ƙawancen Annabi (SAW), to ta shiga, wacce kuma take son shiga ƙarƙashin Ƙuraishawa, to ita ma ta shiga, kuma duk wani ta'addanci da za a yi gare ta, zai zama ta'addanci ne ga abokiyar ƙawancenta nata.

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (2731).

4. Idan wani daga Kuraishawa ya gudu zuwa wajen Annabi (SAW), dole a mayar da shi gare su, amma idan wani daga Musulmai ya koma wurin Kuraishawa, ba za a mayar da shi ba.[1]

Sannan Annabi (SAW) ya kira Aliyyu don ya rubuta wannan yarjejeniyar, sai Annabi (SAW) ya yi masa shifta ya ce: (Rubuta: Bismillahir-Raḥmanir-Raḥim), sai Suhailu ya ce: "Ba mu san Rahman ba, ka rubuta: Bismika Allahumma." Sai Annabi (SAW) ya umurci Aliyyu da ya rubuta hakan.

Sannan sai Annabi (SAW) ya ce ya rubuta: (Wannan shi ne abin da Muhammadu Manzon Allah ya yi sulhu a kan shi), sai Suhailu ya ce: "Da mun yarda cewa kai Manzon Allah ne ai da mun bi ka, a'a, rubuta: "Muhammadu ɗan Abdullahi",[2] sai ya umurci Aliyyu da ya goge lafazin "Manzon Allah", sai Aliyyu ya ƙi, sai Manzon Allah (SAW) ya goge da hannunsa. A nan rubuta wannan takarda ya kammalu, sai ƙabilar Khuza'a suka shiga ƙarƙashin ƙawancen Manzon Allah (SAW), ƙabilar Banu Bakar kuma suka shiga ƙarƙashin ƙawancen Kuraishawa.

❖ Sakamakonsa:

Sahabbai Allah ya ƙara musu yarda sun shiga cikin damuwa mai tsanani saboda ba su shiga Makka ba domin yin umara, kuma sun ji wannan sulhu kamar zalunci ne ga musulmai, da kuma cewa Manzon Allah (SAW) ya karɓi sharuɗɗan Kuraishawa duk da mubaya'a ta Ridwan da aka yi, a lokacin da Annabi (SAW) ya umurce su da su cire ihraminsu kuma su yanka hadayarsu babu wanda ya tashi daga cikinsu, saboda yadda hakan ya yi musu zafi, sai Annabi (SAW) ya shiga wajen Ummu Salma ya faɗa mata abin

[1]. Alfusul (185).
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (1784).

da ya faru, sai ta ce: “Ya Annabin Allah! Ka na son hakan? Ka fita sannan kada ka ce wa kowa komai har sai ka yanka dabbarka, kuma ka kira mai askinka ya yi maka aski. Sai ya aikata hakan, yayin da sahabbai suka ga haka, sai suka tashi suka yi yanka, kuma suka fara yi wa juna aski, har kamar sashinsu zai kashe sashi.[1]

Sannan ba su daɗe ba har sai da Allah ya nuna musu hikimar Annabi (SAW), da iliminsa ga abin da zai biyo baya na al’amura da suka shafi buɗe Makka, da shigar mutane da yawa cikin Musulunci gungu-gungu, kuma yayin da suke kan hanyar dawowarsu, sai Allah ya saukar wa Manzonsa (SAW) suratul fathi, sai baƙin cikinsu ya koma farin ciki, sannan suka fahimci cewa dukkan alheri na cikin miƙa wuya ga umurnin Allah da umarnin Manzon Allah (SAW), kuma sai Allah Ya yaye musu dukkan wata damuwa, saboda abin da surar take ɗauke da shi na albishir da buɗe Makka da nasara da kuma yarda da su; har Annabi (SAW) ya ce: (Lallai an saukar mun da wata sura a wannan daren, wacce na fi son ta fiye da abin da rana ta haskaka a kansa, ((Lallai Mu ne Muka yi maka buɗi, buɗi mabayyani)).[2]

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (2731).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (4177).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

KHALID ƊAN WALID (RA):

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne: Khalid ɗan Walid ɗan Mughira ɗan Abdullahi ɗan Amr ɗan Makhzum; ana kiransa da Abu Sulaiman, mahaifiyarsa ita ce Lubaba ‘yar Harisu, ‘yar’uwa ce ga Maimunatu ‘yar Harisu matar Annabi (SAW).

An haife shi a Makkah, a shekara ta 30 kafin hijira.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Khalid (RA) yana daga cikin manyan shugabannin Ƙuraishawa a jahiliyya, kuma yana daga cikin jarumai da ba su da yawa a shugabanci, da jagorantar rundunar sojoji, da ra’ayi, da hikima.

Ya musulunta (RA) a watan Safar shekara ta takwas bayan hijira, tare da Amr ɗan As da Usman ɗan Ɗalha, sai suka zo wajen Manzon Allah (SAW), yayin da ya gan su sai ya ce wa sahabbansa: (Makka ta jefa muku waɗanda ta fi so).[1]

Annabi (SAW) ya yabi jarumtarsa da gwarzantakarsa, ya ce: (Madalla da bawan Allah Khalid ɗan Walid, shi takobi ne daga takuban Allah).[2]

Kuma Abubakar (RA) ya ce: “Mata sun kasa haifo mutum kamar Khalid”.[3]

Ya halarci buɗe Makka tare da Manzon Allah (SAW), sannan ya halarci yaƙin Hunain, da Ɗa’if, da rusa gunkin Uzza, kuma ya

---

[1]. Arraudul-unuf (5/94).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito shi (3846).
[3]. Tarikhud-Ɗabari (3/358).

jagoranci Musulmi a Yaƙin Mu’ta bayan shahadar jagororinsu guda uku, sai Allah ya ceci Musulmi a hannunsa. Ya na cewa (RA): “Haƙiƙa takuba guda huɗu sun ƙarye a hannuna ranar yaƙin Mu’ta, babu abin da ya saura a hannuna sai wani takobi ƙiran Yaman”.[1]

Kuma Annabi (SAW) ya aika shi zuwa wurin Ukaidar Duma, sai ya kamo shi ya zo da shi, kuma Abubakar ya aika shi a matsayin jagoran runduna zuwa yaƙan Musailima da mutanen da suka yi ridda, sai ya ba da mamaki sosai wurin yaƙar su, sannan sai Abubakar Siddiƙ ya jagorantar da shi a kan sauran komondojin sojoji, kuma ya shugabantar da shi a kan yaƙan Farisa da Rum, sai ya yaƙi Iraƙi, kuma ya yi musu fatafata har sai da ya samu nasara a kansu, sannan ya keta sahara daga iyakokin Iraƙi zuwa ƙasar Sham, kuma ya halarci yaƙoƙin Sham, ya yi ƙawanya ga garin Damaskus, sannan ya buɗe garin, shi da Abu Ubaida, babu wani masaka da ya rage a jikinsa face sai ka ga tambarin shahidai a ciki.[2]

❖ Rasuwarsa:

Khalid ɗan Walid (RA) ya rasu a birnin Himsa, a shekara ta ashirin da ɗaya bayan hijira, a lokacin yana ɗan shekara sittin.

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4265).
[2]. Siyaru a’alamin-bubala (1/367).

Auna fahimtarka a darusan mako na 31			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar "Namariƙ"?		B
	a. Shimfiɗu	b. Filolluka	c. Gadaje
Darasin Hadisi	Tambaya: Kuɓuta daga mutuwar zuciya da ƙeƙashewarta tana kasancewa ne da:		A
	a. Yawan ambaton Allah.	b. Abinci mai gina jiki.	c. Bacci da sauri.
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin siffofin munafurci akwai:		B
	a. Saɓa alƙawari	b. Ƙin taimakon addini.	c. Kukan mutuwa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Sallar Juma'a farilla ce ta ainun a kan:		C
	a. Dukkan musulmi.	b. Maza da mata.	c. Maza.
Darasin Sira	Tambaya: Wanda ya rubuta yarjejeniyar sulhu shi ne:		A
	a. Aliyyu ɗan Abu Ɗalib.	b. Suhailu ɗan Amr.	c. Budailu ɗan Warƙa.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Khalid ɗan Wali (RA) ya musulunta a shekara ta:		C
	a. 6 bayan hijira	b. 7 bayan hijira	c. 8 Bayan hijira

MAKO NA TALATIN DA BIYU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-GASHIYA (2)

﴿أَفَلَا يَنظُرُونَ إِلَى ٱلْإِبِلِ كَيْفَ خُلِقَتْ ﴿١٧﴾ وَإِلَى ٱلسَّمَآءِ كَيْفَ رُفِعَتْ ﴿١٨﴾ وَإِلَى ٱلْجِبَالِ كَيْفَ نُصِبَتْ ﴿١٩﴾ وَإِلَى ٱلْأَرْضِ كَيْفَ سُطِحَتْ ﴿٢٠﴾ فَذَكِّرْ إِنَّمَآ أَنتَ مُذَكِّرٌ ﴿٢١﴾ لَّسْتَ عَلَيْهِم إِلَّا مَن تَوَلَّىٰ وَكَفَرَ ﴿٢٣﴾ فَيُعَذِّبُهُ ٱللَّهُ ٱلْعَذَابَ ٱلْأَكْبَرَ ﴿٢٤﴾ إِنَّ إِلَيْنَآ إِيَابَهُمْ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ إِنَّ عَلَيْنَا حِسَابَهُم ﴿٢٦﴾﴾

❖ **Fassara:**

17. Shin ba sa duban raƙumi yadda aka halicce shi?

18. Da kuma sama yadda aka ɗaga ta?

19. Da kuma duwatsu yadda aka kakkafa su?

20. Da kuma ƙasa yadda aka shimfiɗa ta?

21. To ka yi wa'azi, lallai kai mai wa'azi ne kawai.

22. Kai ba mai tilasta su ba ne.

23. Sai dai wanda ya ba da baya kuma ya kafirce.

24. To Allah zai azabtar da shi azaba mafi girma.

25. Lallai zuwa gare mu ne makomarsu take.

26. Sannan kuma a kanmu ne hisabinsu yake.

❖ **Saƙon da ayoyin suke ƙunshe da shi:**

Yin duba cikin alamomi da suke nuni a kan ikon Allah.

❖ **Bakin kalmomi:**

سطحت	Sudîhat	An shimfiɗa ta
فذكر	Fa zakkir	Ka yi musu wa'azi kuma ka tsoratar da su daga azabar Allah
بمصيطر	Bi musaidir	Wato ba ka da wani ikon tilasta musu yin imani.
إيابهم	Iyabahum	Makomarsu bayan mutuwa.

❖ Ma'anar ayoyin a dunƙule:

A waɗannan ayoyi Allah Maɗaukakin Sarki Yana kwaɗaitar da dukkan mutane a kan yin tunani game da halittun Allah da suke nuni a kan kaɗaita Shi, saboda haka, su kalli raƙumi da ƙayattaciyar halittarsa, da kuma yadda Allah Ya horar da shi ga bayi, kuma Ya hore musu shi don ababen da suke buƙata na amfani.

Kuma su yi duba zuwa ga manyan duwatsu kafaffu, da kuma yadda aka sanya su don ƙasa ta samu tabbatuwa da su, don kada ta girgiza, kuma aka sanya ababen amfani masu yawa da ma'adanai daban-daban a cikinsu.

Kuma su yi duba zuwa ga ƙasa yadda aka shimfiɗa ta da faɗi, kuma aka sauƙaƙa yin tafiya a cikinta, domin halittu su samu tabbatuwa a samanta, kuma su samu daman noma ta da gina ta.

Sannan sai Allah Maɗaukaki ya umurci Manzonsa (SAW) da ya tunatar da mutane, ya yi musu wa'azi, ya gargaɗe su, kuma ya tsoratar da su, domin shi an aiko shi ne don ya kira halittu zuwa ga Allah kuma ya tunatar da su, ba a aiko shi don tilasta musu ba, kuma ba a wakilta shi don kula da ayyukansu ba, idan ya isar da abin da aka umarce shi, to babu wani zargi a kansa bayan haka.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Kwaɗaitar da mutane a kan yin tunani game da halittun Allah waɗanda suke nuni zuwa ga kaɗaita Shi.

2. Halittar raƙumi na daga cikin mafi girman ayoyin Allah, haƙiƙa an horar da shi ga mutum, kuma an tanade shi don hawa da ɗaukan kaya, tare da wasu ababen amfani daban-daban da yake da su.

3. Cewa daga cikin ayoyin Allah akwai kafa duwatsu, domin su kamar turaku suke wajen tabbatuwar da ƙasa.

4. Cewa daga cikin ayoyin Allah akwai shimfiɗa ƙasa, da kuma miƙar da ita kamar gado ko shimfiɗa, da kuma abin da aka sanya a cikinta da doronta na ni'imomi da ayoyi da ba za su ƙirgu ba; ((Kuma a cikin ƙasa akwai alamu ga masu yaƙini)).[1]

5. Cewa aikin mai kira zuwa ga Allah shi ne kira zuwa ga Allah Maɗaukaki, ba wai shiryarwa ba, saboda shiriya tana hannun Allah Maɗaukaki Shi kaɗai.

[1]. (Azzariyat: 20).

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR SADA ZUMUNCI

An karɓo daga Anas ɗan Malik (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Wanda yake so a yalwata masa arzikinsa, kuma a tsawaita masa rayuwarsa, to ya sada zumuncinsa**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito.[1]

❖ Sharhi:

Wannan hadisi yana kwaɗaitarwa a kan sada zumuta, kuma yana bayyana cewa tana jawo abin da bawa yake so na yalwar arziki da tsawon rai, kuma wannan gaskiya ne a haƙiƙaninsa, domin Allah shi ne Mahaliccin abubuwa da sababansu, saboda haka, kamar yadda bawa ya sada zumuncinsa da alheri da kyautatawa, kuma ya sanya jin dadi da farin ciki a zukatansu, haka Allah zai tsawaita rayuwarsa, kuma ya yalwata arzikinsa, kuma ya buɗe masa ƙofofin albarka, abin da ba zai iya samu ba tare da wannan sababi mai girma ba.

Kuma sada zumunci na kasancewa ne ta hanyar ziyartar ‘yan’uwa, da duba halinsu, da bincikan labarinsu, da daɗaɗa magana gare su, da taimaka musu a kan alheri, da bayar da da sadaqa ga talakawansu da kyauta ga mawadatansu, ba tare da la’akari da sadawarsu da kyautatawarsu gare shi ba; Haƙiƙa Annabi (SAW) ya ce: (Ba mai sada zumunci ba ne wanda sai an masa zai yi, sai dai mai sada zumunci shi ne wanda idan aka yanke masa zumunci sai ya sada shi).[2]

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (5986) da Muslim (2557).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (5991).

❖ Abubuwan da zamu koya daga Hadisin:

1. Wajibcin kwaɗaituwa zuwa ga sada zumunci; domin musulmi ya samu ladansa a duniya da lahira.

2. Bayani a kan cewa sada zumunci sababi ne na samun ƙaruwar arziki da tsawon rayuwa.

3. Tabbatar da sabuba na shari’a, domin Annabi (SAW) ya tabbatar da sababi, wanda shi ne sada zumunci, da kuma abin da ke samuwa daga sababi, wanda shi ne tsawon rai da yalwar arziki.

TALATA: DARASI CIKI AƘIDA

BIDI'A CIKIN ADDINI:

❖ Hukuncin bidi'a cikin addini:

Addinin Musulunci ya haramta kirkirar bidi'a a cikin addini ta hanyar ƙari ko ragi ko canzawa; Hakan ya kasance ne saboda addini na Allah ne, Ubangijin talikai, Shi ya saukar da shi, ya cika shi, ya kare shi, don haka asali a cikin ibadodi shi ne tsayawa bisa abin da aka zo da shi, ba a bauta wa Allah sai da abin da ya shar'anta a cikin littafinsa ko a harshen Manzonsa (SAW); Manzo (SAW) ya ce: (Duk wanda ya ƙirƙiri wani abu a cikin al'amarinmu (addini) wanda ba ya cikinsa, to ba karɓaɓɓe ba ne),[1] A wata riwaya kuma: (Duk wanda ya aikata wani aiki da ba a bisa al'amarinmu yake ba, to ba a karɓa ba).[2]

Amma ƙirƙira a cikin al'ada da sha'anin rayuwa, wannan halal ne, ba ya shiga ƙarƙshin hani; domin asali a al'adu shi ne halacci da yardar shari'a, kamar sabbin kayan amfani da mutane suka ƙirƙira, da kuma na'urori na zamani.

❖ Nau'ukan bidi'a cikin addini:

Nau'i na farko: Bidi'a ta furuci da aƙida; kamar aƙidojin ƙungiyoyin ɓata, irin Khawarij, Qadariyya, Murji'a, da maganganunsu da suka saɓawa nassosin shari'a.

Nau'i na biyu: Bidi'ar ƙirƙirar ibadodi na aiki; ta yadda mutum zai ƙirƙiri ibada wadda babu ita a cikin shari'a, kamar ƙirƙiro salla sabuwa ko azumi da ba a shar'anta shi ba.

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (2695) da Muslim (1718).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (7350) da Muslim (1718).

Nau'i na uku: Bidi'a ta hanyar ƙari a cikin ibada da aka shar'anta ta; kamar wanda ya ƙara raka'a ta biyar a cikin sallar azahar ko la'asar, ko kuma ya yi ƙari a kan adadin azumi watan Ramadan kafin watan ko bayansa.

Nau'i na huɗu: Bidi'a ta canza sifar ibada da aka shar'anta; kamar ya yi ta da wani salo wanda bai zo a shari'a ba; kamar yin zikiri da aka shar'anta cikin jama'a da murya ɗaya da ake rera ta, ko kuma tsanantawa da ya saɓa wa sunna.

Nau'i na biyar: Bidi'a ta keɓance wani lokaci da ba a shar'anta ba ga wata ibada da aka shar'anta; kamar keɓe ranar tsakiyar watan Sha'aban da darenta da azumi ko da salla; domin azumi da salla duk suna da asali a shari'a, amma keɓance su ga wannan lokaci na musamman sai da hujja.

❖ Shin akwai bidi'a mai kyau a cikin addini?

Dukkan nau'ukan bidi'a a cikin addini haramun ne kuma abin ƙi ne, kuma babu wani abu da ake kira bidi'a mai kyau, domin Manzon Allah (SAW) ya yi hukunci a kan dukkan bidi'a cewa bata ce. Ya ce: (Ahir ɗinku da ƙirƙirarrun al'amura, domin kowane ƙirƙirarren abu bidi'a ne, kuma kowace bidi'a ɓata ce),[1] kuma haramtawa yana bambanta gwargwadon nau'in bidi'a: akwai wacce kafirci ce da shirka, akwai kuma wacce tsani ce zuwa ga shirka, akwai kuma wanda yake fasiƙanci ne da saɓo.

[1]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (4607) da Tirmizi (2676).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SUNNONIN RANAR JUMA'A:

Ranar Juma'a na da sunnoni da ladubba da ake so ayi su, ya kamata ga musulmi ya himmantu da su ya kuma kwaɗaitu a kansu, daga ciki akwai:

1. An sunnanta yin wanka a ranar Juma'a, kuma ya dace a dage da yin sa ba a bar shi ba, musamman ga masu wari mara daɗi; Manzo (SAW) ya ce: (Wankan Juma'a wajibi ne a kan kowane baligi).[1]

2. An sunnanta tsafta da sanya turare, da gusar da abin da ya dace a gusar daga jiki, kamar faratu, da gashin da shari'a ta yi umurni da a aske shi; Annabi (SAW) ya ce: (Babu wani mutum da zai yi wanka a ranar Juma'a, ya tsarkake kansa daidai gwargwado, ya shafa mai daga man da yake da shi, ko ya sanya turare daga turaren gidansa, sannan ya fita ba tare da ya raba tsakanin mutane biyu ba, ya sallaci abin da aka rubuta masa, ya yi shiru idan liman yana magana, face Allah ya gafarta masa tsakanin wannan Juma'ar da wacce ta gabata).[2]

3. Haka kuma an sunnanta wa mutum ya sanya mafi kyawun tufafinsa a ranar Juma'a, saboda faɗinsa (SAW): (Me zai hana ɗayanku ya sayi tufafi biyu domin ranar Juma'a banda tufafin aikinsa?).[3]

4. An sunnanta fita da wuri zuwa sallar Juma'a, da kuma shagaltuwa da yin nafila, da zikiri, da karatun Alƙur'ani har sai liman ya fito don yin huɗuba; Manzo (SAW) ya ce: (Duk wanda ya yi wankan Juma'a irin wankan janaba, sannan ya fita a cikin sa'a ta farko,

---

1. Bukhari ne ya rawaito shi (879) da Muslim (846).
2. Bukhari ne ya rawaito shi (883).
3. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (1078).

kamar ya yi sadaka ne da rakumi, duk wanda ya fita a cikin sa'a ta biyu, kamar ya yi sadaka ne da saniya, duk kuwa wanda ya fita a cikin sa'a ta uku, kamar ya yi sadaka ne da rago mai ƙaho, duk wanda ya fita a cikin sa'a ta hudu, kamar ya yi sadaka ne da kaza, kuma duk wanda ya fita a cikin sa'a ta biyar, to kamar ya yi sadaka ne da ƙwai, idan liman ya fito sai mala'iku su halarto don su saurari zikiri).[1]

5. An sunnanta tafiya a ƙafa zuwa sallar Juma'a, da barin abin hawa; Manzo (SAW) ya ce: (Duk wanda ya wanke jikinsa ranar Juma'a kuma ya yi wanka, kuma ya yi sammako kuma ya fita a kan lokaci, kuma ya tafi masallaci a kan ƙafarsa bai hau abin hawa ba, kuma ya zauna kusa da liman, sannan ya saurari huɗuba bai yi wargi ba; to yana da ladan aikin shekara na azumi da salla a maimakon kowane taku).[2]

6. An sunnanta wa wanda zai shiga masallaci ranar Juma'a kada ya zauna har sai ya yi salla rala'a biyu; saboda gamammen umarnin manzon Allah (SAW) da haka,[3] kuma ya taƙaita ta idan liman ya kasance yana huɗuba.

7. An sunnanta yawaita salati ga Annabi (SAW) a ranar Juma'a da darenta; saboda faɗinsa (SAW): (Ku yawaita salati a gare ni ranar Juma'a).[4]

8. An sunnanta karanta suratul Kahafi a yinin Juma'a, kuma ana so a kirdadi lokacin amsa addu'o'i; saboda faɗinsa (SAW): Duk wanda

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (881) da Muslim (850).
[2]. Ahmad ne ya rawaito shi (10073) da Abu Dawuda (345).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (930).
[4]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (1047) da Nasa'I (3/91).

ya karanta suratul Kahafi a ranar Juma’a, to Allah zai haskaka masa abin da ke tsakanin Juma’a biyu).[1]

An sunnanta yawaita addu’a a yinin Juma’a, kuma ana so mutum ya kirdadi lokacin amsa addu’o’i; saboda fadîn sa (SAW): (Lallai cikin Juma’a tabbas akwai wani lokaci da babu wani bawa musulmi da zai dace da shi alhali yana tsaye yana addu’a, yana ruƙon Allah wani abu, face sai Allah Ya ba shi wannan abun).[2]

[1]. Hakim ne ya rawaito shi (2/368).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (935) da Muslim (852).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

YAƘIN KHAIBAR

❖ Lokacin aukuwarsa:

Yaƙin ya auku ne a farkon shekara ta bakwai bayan hijira, bayan dawowar Annbi (SAW) daga sulhun Hudaibiyya da kwana ashirin.

❖ Sabuban aukuwarsa:

Annabi (SAW) ya ƙudurci aniyar yaƙar yahudawa saboda ɓarnarsu mai girma, da kuma zugi da suke yi a kan cutar da musulmi; haƙiƙa yaƙin Ahzab ma su suka tsara shi, kuma su ne suka zuga Banu Ƙuraiza a kan ha'inci da yaudara.

❖ Abubuwan da suka faru:

Khaibar wani gari ne da yake kudancin Madina, a kan hanyar Sham, yana da tazarar kilomita 153 daga Madina, a cikinsa akwai mayaƙa yahudawa dubu goma, kuma ganuwarsu na daga cikin mafiya ƙarfin ganuwowi, kuma sun tanadi abinci da ruwa da zai ishe su tsawon watanni a cikin ganuwar tasu, amma hakan bai kashe guiwar musulmi ba, sai Annabi (SAW) ya fita zuwa garin, sannan ya ba da umarnin kada wanda ya bi shi sai wanda aka yi sulhun Hudaibiyya da mubaya'ar Ridwan da shi; saboda ƙarfin imaninsu da tabbatuwarsu, sai rundunar musulmi ya kama hanya har ya tsaya wani kwari da ake kira Arraji', a tsakanin yahudawa da ƙabilun Gadfan; damin su raba tsakaninsu, ta yadda Gadfan ba za su kawo wa Khaibar ɗauki ba, kuma tabbas, Gadfan da jin su labarin yaƙan Khaibar da Annabi (SAW) zai yi, take sai suka yi shiri suka kama hanya don taimakon yahudawa, sai dai musulmi sun yaɗa labarin cewa su za su tafi yaƙan Gadfan ne, don haka, sai suka juya baya

suka koma, sai Allah Ya isar wa musulmi sharrin yaƙinsu, sai musulmi suka fara yin ƙawanya ga Khaibar.[1]

❖ Sakamakonsa:

An ta buɗe ganuwowi, su kuma yahudawa sai gudu suke daga wannan ganuwar zuwa wancan, har sai da musulmi suka iso wurin wani ganuwa mai ƙarfi da aka gagara buɗe ta, sai suka kasance a wajensa kwanaki masu yawa amma ba su iya buɗe shi ba, sai Manzo (SAW) ya ce: (Tabbas zan ba da wannan tuta gobe ga wani mutumin da Allah zai yi buɗi a hannunsa, mutumin yana son Allah da Manzonsa, kuma Allah da Manzonsa su ma suna son sa), sai musulmi suka kwana suna jiran su san wane ne mutumin, yayin da gari ya waye, sai Annabi (SAW) ya kira Aliyyu ɗan Abu Ɗalib, haƙiƙa ya kasance a lokacin yana fama da ciwon ido, sai Annabi (SAW) ya yi tofi a idonsa, kuma ya masa addu'a, sai ya warke albarkacin Manzon Allah (SAW),[2] sai ya ba shi tutar, sai Allah ya yi buɗi a hannunsa, kuma musulmi suka ci nasarar, sai mutum kusan ashirin suka yi shahada Allah Ya ƙara musu yarda gaba ɗayansu, sai ya yahudawa suka tarwatse mummunan tarwatsewa.

Sai kuma Annabi (SAW) ya so ya kore su, amma sai suka nemi a kan za su zauna a garinsu su ci gaba da noma, in ya so musulmi su ɗauki rabin amfanin gona da 'ya'yan itatuwa, sai Annabi (SAW) ya yarda.[3]

---

[1]. Albidaya wan-nihaya (6/251).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (4210).
[3]. Bukhari ne ya rawaito shi (2329) da Muslim (1551).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SUHAIBUR-RUMI (RA)

❖ Sunansa:

Shi ne Suhaibu ɗan Sinan ɗan Malik ɗan Abdu Amr, daga banu Namir, ɗaya daga cikin ƙabilun Rabi'a ɗan Nizar, ya shahara da "Suhaibu Arrumi" saboda ya zauna a Rum lokaci mai tsawo, kuma babansa ko baffansa ya kasance gomna ne a ƙarƙashin Kisra.[1]

An haifi Suhaibu a tsuburin Furatu, kusa da Nainawa, a shekara ta 35 kafin hijira, sai aka kama shi a cikinta a matsayin fursunan yaƙi, sannan aka kawo shi Makka, sai Abdullahi ɗan Jud'an ya saye shi.

❖ Rayuwarsa da darajojinsa:

Suhaibu (RA) ya kasance mai tsananin jan launin fata ne, ba dogo ba kuma ba gajere ba, mai yawan gashin kai, yana sanya masa lalle, kuma ya kasance (RA) aboki ne ga Annabi (SAW) tun kafin a aiko shi, yayin da aka aiko shi ya kasance daga cikin mutanen farko da suka musulunta; Abdullahi ɗan Mas'ud (RA) ya ce: "Farkon waɗanda suka bayyana musuluncinsu mutum bakwai ne: Manzon Allah (SAW), da Abubakar, da Ammar, da mamarsa Sumayya, da Suhaibu, da Bilal, da Miƙdad, amma shi Manzon Allah (SAW) sai Allah ya ba shi kariya ta hanyar baffansa Abu Ɗalib, amma Abubakar, sai Allah Ya ba shi kariya ta dalilin danginsa, amma sauran mutanen sai mushirkai suka kama su, suka saka musu sulke na ƙarfe, sannan suka shanya su a rana".[2]

Suhaibu (RA) ya kasance mai tsantsene, mai sauƙin hali, mai tsoron Allah, jarumi, mai karamci, yana sadaukar da ransa da dukiyarsa

---

[1]. Siyaru A'alamin-nubala (2/17).
[2]. Ahmad ne ya rawaito shi (3823) da Ibnu Maja (150).

saboda Allah, kuma ba ya tsoron talauci; ya shahara (RA) da faɗin Annabi (SAW) gare shi: (Ya kai baban Yahaya! Kasuwanci ya yi riba, kasuwanci ya yi riba, kasuwanci ya yi riba),[1] abin da ya sa ya faɗa haka shi ne: wato a lokacin da ya so ya yi hijira zuwa Madina, mutanen Makka suka tare shi, sai ya watsar da masunsa, kuma ya kasance yana daga cikin maharba ƙwararru, sai ya ba su zaɓi tsakanin ya harbe su da masunsa, ko kuma ya nuna musu wurin da ya ajiye dukiyarsa da sharaɗin za su kyale shi, sai suka bar sa, sai ya yi hijira tare da Aliyyu ɗan Abu Ɗalib, kuma su biyun su ne ƙarshen waɗanda suka yi hijira daga Makka, kuma a kanshi ne aka saukar da faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ((Kuma daga cikin mutane akwai wanda ya sayar da kansa don neman yardar Allah, kuma Allah Mai tausayi ne ga bayi)).[2], [3]

Bayan rasuwar Annabi (SAW), Suhaibu ya zauna a Madina, ya kasance abin girmamawa a tsakanin sahabbai, suna tabbatar masa da matsayinsa, kuma suna ba shi girmansa, haƙiƙa Umar ɗan Khaɗɗab Allah Ya ƙara masa yarda lokacin da aka soke shi ya yi wasici da Suhaibu ya yi salla ga musulmai, har zuwa lokacin da ‘yan komitin shura za su zaɓi sabon halifa da zai gaje shi.[4]

❖ Rasuwarsa:

Suhaibu (RA) ya guji fitina tun daga lokacin shahadar Usman (RA) har zuwa rasuwarsa a shekara ta 38 bayan hijira a Madina, sai aka binne shi a maƙabartar Baƙi.

---

[1]. Hakim ne ya rawaito shi (3/450).
[2]. (Albaƙara: 207).
[3]. Tafsirin Ɗabari (4/248).
[4]. Albidaya wan-nihaya (10/209).

Auna fahimtarka a darusan mako na 32			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar faɗinsa Maɗaukaki (Bi musaiɗir)?		B
	a. Mai bi	b. Mai iko	c. Mai ha'inta
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin fa'idodin sada zumunta akwai:		C
	a. Yawan 'ya'ya	b. Waraka daga cututtuka.	c. Yalwar arziki.
Darasin Aƙida	Tambaya: Ƙirƙira cikin al'adu da lamuran duniya:		A
	a. Halal ne	b. Abin ƙi ne.	c. Haram ne.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin abin da aka sunnanta a ranar Juma'a akwai:		B
	a. Keɓance ta da azumi da salla	b. Yawaita salati ga Annabi (SAW).	c. Yalwata ciyarwa ga iyalai.
Darasin Sira	Tambaya: Yaƙin Khaibar ya auku ne a shekara ta:		C
	a. 5 bayan hijira.	b. 6 bayan hijira.	c. 7 bayan hijira.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Nasabar Suhaibu (RA) yana komawa zuwa ga:		C
	a. Rumawa	b. Ƙuraishawa	c. Banu Numair

MAKO NA TALATIN DA UKU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-A'ALA

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
سَبِّحِ ٱسۡمَ رَبِّكَ ٱلۡأَعۡلَى ١ ٱلَّذِي خَلَقَ فَسَوَّىٰ ٢ وَٱلَّذِي قَدَّرَ فَهَدَىٰ ٣ وَٱلَّذِيٓ أَخۡرَجَ
ٱلۡمَرۡعَىٰ ٤ فَجَعَلَهُۥ غُثَآءً أَحۡوَىٰ ٥ سَنُقۡرِئُكَ فَلَا تَنسَىٰٓ ٦ إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۚ إِنَّهُۥ يَعۡلَمُ
ٱلۡجَهۡرَ وَمَا يَخۡفَىٰ ٧ وَنُيَسِّرُكَ لِلۡيُسۡرَىٰ ٨ فَذَكِّرۡ إِن نَّفَعَتِ ٱلذِّكۡرَىٰ ٩ سَيَذَّكَّرُ مَن يَخۡشَىٰ
﴿وَيَتَجَنَّبُهَا ٱلۡأَشۡقَى ١١ ٱلَّذِي يَصۡلَى ٱلنَّارَ ٱلۡكُبۡرَىٰ ١٢ ثُمَّ لَا يَمُوتُ فِيهَا وَلَا يَحۡيَىٰ ١٣ ١٠
قَدۡ أَفۡلَحَ مَن تَزَكَّىٰ ١٤ وَذَكَرَ ٱسۡمَ رَبِّهِۦ فَصَلَّىٰ ١٥ بَلۡ تُؤۡثِرُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ١٦ وَٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ
وَأَبۡقَىٰٓ ١٧ إِنَّ هَٰذَا لَفِي ٱلصُّحُفِ ٱلۡأُولَىٰ ١٨ صُحُفِ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ ١٩﴾

❖ **Fassara:**

1. Ka tsarkake sunan Ubangijinka Mafi ɗaukaka.

2. Wanda Ya yi halitta sai Ya daidaita ta.

3. Wanda kuma Ya ƙaddara abubuwa sannan Ya shiryar da halittarsa.

4. Wanda kuma Ya fitar da makiyaya.

5. Sai Ya mayar da ita duddugaggiya mai baƙi.

6. Za Mu karantar da kai (Alƙur'ani) don haka ba za ka manta ba.

7. Sai abin da Allah Ya ga dama, Lallai Shi yana sane da bayyanannen abu da kuma abin da yake ɓuya.

8. Kuma za Mu sauƙaƙe maka (al'amura) mafiya sauƙi.

9. To ka yi wa'azi idan wa'azin zai yi amfani.

10. Wanda yake tsoron Allah zai wa'aztu.

11. Mafi shaƙiyanci kuma zai nisance shi.

12. Wanda zai shiga wuta mafi girma.

13. Sannan ba zai mutu a cikinta ba kuma ba zai rayu (rayuwa mai dadi) ba.

14. Haƙiƙa wanda ya tsarkaka ya rabauta.

15. Ya kuma ambaci sunan Ubangijinsa sannan ya yi salla.

16. Ba haka ba, ku dai kuna fifita rayuwar duniya ne.

17. Lahira kuwa ita ta fi alheri ta kuma fi wanzuwa.

18. Lallai wannan batu tabbas yana cikin littattafan farko.

19. Littaffatan Ibrahim da Musa.

❖ Saƙon da surar ta ƙunsa:

Tunatar da rayukan mutane da rayuwar lahira, da kuma kuɓutar da su daga ratayuwa da duniya.

❖ Bakin kalmomi:

سبح اسم ربك	Sabihismi rabbika	Ka tsarkake Ubangijinka kana mai ambaton sunansa da harshenka.
الأعلى	Al'a'la	Wanda yake da ɗaukaka ف a zati da ɗaukaka ta matsayi, da ɗaukaka ta rinjaye.
فسوى	Fasawwa	Ya inganta halittarsa kuma Ya kyautata ta.
فهدى	Fahada	Ya saukake masa abin da zai dace da shi

لليسرى	Lilyusra	Zuwa ga hanya sauƙaƙka a shari'arka da rayuwarka.
يصلى النار	Yaslan nar	Zai shige ta kuma zai ƙonu da zafinta
أخرج المرعى	Akhrajal mar'a	Ya tsirar da ciyayi
غثاء	Ghusa'an	Busasshen ciyawa
أحوى	Ahwa	Wanda ya canza
إلا ما شاء الله	Illa masha Allah	Sai abin da Allah Ya yi nufin sauke tilawarsa da hukuncinsa, Ya kuma mantar da kai shi.
تزكى	Tazakka	Ya tsarkake kansa daga saɓo, ya ƙawata shi da ɗa'a.
إن هذا	Inna haza	Ana nufin wanda ya zo a faɗinsa: (Haƙiƙa wanda ya tsakake kansa ya rabauta).

❖ Ma'anar surar a dunƙule:

Suratul Aʿla yana daga cikin surori da aka saukar a Makka, ana kuma kiran ta da Suratu Sabbih, ta zo ne don ta yi magana game da Allah Maɗaukaki, ta kuma tsayar da dalilai a kan girmansa da ikonsa, ta kuma yi bayanin cewa shi ne mafi girma, Mahalicci, Maƙagin halittu, Mai shiryar da bayinsa da halittunsa, Mai ƙaddara arzikinsu da al'amuransu, kuma Masani ga abin da ya ɓuya da abin da ya bayyana. Sai kuma surar ta zo wa Manzon Allah (SAW) da bishara guda biyu masu girma:

Ta farko: Cewa Allah Ta'ala Ya kare shi daga mantuwa, don haka ba zai manta abin da aka yi masa wahayi da shi ba.

Ta biyu: Cewa Allah Ya sauƙaƙa masa (SAW) karɓar wahayi, sai ya kasance ba a taɓa ba shi zaɓi tsakanin abubuwa biyu ba face sai ya zaɓi mafi sauƙinsu.

Bayan haka sai umurni ya zo wa Manzon Allah (SAW) da ya isar da saƙo da tunatarwa ga dukkan mutane, amma muminin da yake tsoron azabar Allah sai ya faɗaku ya kuma wa'aztu, amma kafiri taɓaɓɓe kuwa sai ya bijire mata har sai ya faɗa wuta, yana mai dawwama, ba zai mutu a cikinta ba bare ya huta, kuma ba zai rayu rayuwa mai daɗi ba, kuma sai surar ta ƙare da bayyana cewa falala da cin nasara gaba ɗaya zai samu ga wanda ya tsarkake kansa, kuma ya tuna Ubangijinsa, kuma ya yi sallarsa ta farilla, kuma bai fifita abin da zai ƙare ba a kan abin da zai dawwama.

Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Kwaɗaitarwa a kan bincikan ayyukan zukata da gyara su, da kuma tsarkake rai da tsaftace shi.

2. Kwaɗaitarwa a kan neman kusanci zuwa ga Allah Maɗaukaki ta hanyar salla da zikiri da zakka.

3. Wajabcin tsoron Allah a halin ɓuya da halin bayyana; domin Shi Allah Maɗaukaki Yana sane da abin da ke bayyane da wanda yake ɓoye.

4. Taɓewa yana haɗe da yin watsi da ambaton Allah da yin biyayya gare Shi, kuma ƙarshensa wuta ce mai ƙuna.

LITININ: DARASI CIKIN HADISIN

MUTUM YANA TARE DA WANDA YAKE SO

An karɓo daga Abu Musa Al'ash'ari (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Mutum yana tare da wanda yake ƙauna**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito.[1]

❖ Sharhi:

Wannan hadisin yana bayyana cewa mutum zai tashi a lahira tare da waɗanda yake ƙaunarsu a duniya; domin ƙauna shaida ce ta tsananin ratayuwar zuciyar mai ƙauna da wanda yake ƙauna, da dace da shi a cikin halayensa da koyi da shi a cikin aikace-aikacensa, don haka ya kamata musulmi ya girmama ƙaunar Manzannin Allah da mabiyansu salihai a cikin zuciyarsa; domin yana daga falalar Allah da karamcinsa ya sada shi da su, ko da aikinsa ya gaza nasu. Saboda haka ne Anas (RA) ya ce: "Babu abin da ya faranta mana rai bayan musulunci kamar wannan maganar Annabi (SAW): (Lalle kai kana tare da wanda kake ƙauna), to ni ina ƙaunar Allah da Manzona, da Abubakar da Umar, kuma ina fata in kasance tare da su ko da ban yi irin ayyukansu ba".[2]

Idan haka yake a cikin ƙaunar halittua tsakanin junansu, to yaya kuwa game da wanda ya ƙaunaci Allah Maɗaukaki, ya gabatar da ƙaunarsa da tsoronsa a kan komai? To, lallai shi yana tare da Allah, kuma wanda yake tare da Allah, to Allah yana tare da shi; Allah Maɗaukaki ya ce: ((Lallai Allah yana tare da masu taqawa, da kuma waɗanda suke masu kyautatawa)).[3]

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito (6170) da Muslim (2641).
[2]. Muslim ne ya rawaito (2639).
[3]. (Annahlu: 128).

❖ Abubuwan da za mu koya daga Hadisin:

1. Matsayin ƙauna saboda Allah Maɗaukaki, ba don duniya ko dukiya ba, saboda ita ce wacce za ta amfani ma'abocinta a duniya da ƙarin imani da kyakkyawan abin koyi, kuma a lahira ya haɗu da wanda yake ƙaunarsa cikin rahamar Allah.

2. Ya kamata musulmi ya zaɓi abokan zamansa da abokansa; domin ya kasance tare da su ko da aikinsa ya gaza.

3. Wajibi ne a yi hattara daga ƙaunar fajirai da fasikai; domin wannan ƙauna za ta haɗa shi tare da su a lahira, sai ta koma azaba da la'antar juna.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

MATSAYAN MAGABTA GAME DA BIDI'A:

Magabata na ƙwarai suna da bayyananniyar matsaya a kan fito-na-fito bidi'o'i da yaƙar su da inkarin su da mafi tsananin inkari.

Daga cikin waɗannan matsayoyi akwai: Abin da Addarimi ya ruwaito cewa Abu Musa Al'asha'ari (RA) ya zo ƙofar Abdullah ibn Mas'ud (RA), sai ya zauna har sai da ya fito. Sai ya ce masa: Ya Aba Abdirrahman, lallai ni na ga wani abu a masallaci wanda na ƙi yarda da shi, kuma ina godiya ga Allah ban ga komai ba sai alheri. Ya ce: Mene ne? Ya ce: Idan ka rayu, zaka gan shi. Ya ce: Na ga wasu mutane a masallaci a zaune sun yi da'ira suna jiran salla, a kowace da'ira akwai mutum, kuma a hannayennsu akwai tsakwankwani, sai yake cewa: Ku yi kabbara sau ɗari, sai su yi kabbara sau ɗari, sai ya ce: Ku yi hailala sau ɗari, sai su yi hailala sau ɗari, sai ya ce: Ku yi tasbihi sau ɗari, sai su yi tasbihi ɗari. Ya ce: Me ka ce musu? Ya ce: Ban ce musu kome ba, saboda na jira ra'ayinka. Ya ce: Me ya hana ba ka umarce su da su ƙirga munanan ayyukansu ba, ka kuma ba su tabbacin cewa ba za a tozarta musu kyawawan ayyuka ba? Sai ya tafi muka tafi tare da shi, har sai da ya iso wajen ɗaya daga cikin waɗannan da'irorin, sai ya tsaya a kansu ya ce: Wane irin abu nake ganinku kuna aikatawa? To ku ƙirga munanan ayyukanku, ni ina tabbatar muku da cewa ba za a tozarta muku kyawawan ayyukanku ba. Kaitonku ya ku al'ummar Muhammad! Abin mamaki saurin halakarku! Ga sahabban Annabinku (SAW) suna nan da yawa, ga tufafinsa ba su lalace ba, ga kofunansa shansa ba su karye ba, ina rantsuwa da Wanda raina ke hannunsa, ko dai lallai ku kuna kan wata shiriya da tafi shiriyar Muhammadu, ko kuma ku masu buɗe ƙofar bidi'a ne! Suka ce:

Wallahi, ya Aba Abdirrahman, ba ma nufin komi sai alheri. Ya ce: Ai akwai masu nufin alheri dayawa amma ba su dace da shi! Lallai Manzon Allah (SAW) ya ba mu labari cewa akwai wasu mutane suna karatun Alƙur'ani amma ba zai wuce maƙoshinsu ba. Ina rantsuwa da Allah, ban sani ba, watakila mafi yawansu daga cikinku ne. Sai ya bar su ya juya daga gare su. Sai Amr ɗan Salama ya ce: Mun ga mafi yawansu suna yaƙar mu a ranar Nahrawan tare da khawarijawa.[1]

Kuma daga cikin waɗannan matsayoyi akwai: Abin da ya zo daga Imam Malik ɗan Anas Allah ya jikansa da rahama, cewa wani mutum ya zo wurinsa ya ce: Daga ina zan ɗau ihrami? Sai ya ce masa: Daga wurin miƙatin da Manzon Allah (SAW) ya kayyade kuma ya ɗau ihrami. Sai mutumin ya ce: Idan na ɗauki ihrami daga nesa fiye da shi fa? Sai Malik ya ce: Ba na ganin hakan daidai ne. Sai ya ce: Me kake ƙi a hakan? Ya ce: Ina tsorace maka fitina. Sai mutumin ya ce: Wace fitina ce a cikin ƙarin alheri? Ya ce: Lallai Allah Maɗaukaki ya ce: ((To su yi hattara waɗanda suke saɓa wa umarninsa, kada wata fitina ta same su ko kuma wata azaba mai raɗaɗi ta same su)),[2] Kuma wace fitina ce girmanta ya kai a ce kai an keɓance ka da wata falala da Manzon Allah (SAW) ma bai keɓantu da ita ba?[3]

---

[1]. Darimi ne ya rawaito a muƙaddimar Sunan (210).
[2]. (Annur: 63).
[3]. Alkhaɗîb ya ambace shi a littafin Alfaƙihu wal-mufaƙƙihu (1/146) da Baihaƙi da Muƙaddimar Assunanul-kubra (236).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SALAR JANA'IZA:

Ya kamata a duk lokacin da aka ambaci mutuwa mutum ya yi duba ya yi tunani game da wannan haƙiƙa, ya kuma tuna cewa lallai ita ce makomarsa a wanna duniya, sai ya yi tanadi don lahira, kuma ya yi mata guzurin aiki nagari, kuma ya gaggauta tuba daga zunubai, da mayar da haƙƙoƙi da abubuwan da ya karɓa a bisa zalunci.

Wannan haƙƙin mutum ne a bisa kansa, amma haƙƙin wanda ya mutu a kan 'ya'uwansa, to haƙiƙa Allah Ya sanya wa 'yan'uwantaka ta imani haƙƙoƙi da za su ci gaba da gudana har bayan mutuwa, sai Allah Maɗaukaki Ya sha'ranta wa musulmi yin bankwana ga ɗan uwansa da ya mutu da wani aiki mai girma da wata salla mai albarka, wacce take ƙunshe da ƙankan da kai ga Allah da neman ya karrama shi da gafararsa da rahamarsa, Ya kuma kankare masa zunubansa, kuma Ya karɓi ceton musulmi gare shi; Annabi (SAW) ya ce: (Idan za ku yi salla ga mamaci, to ku tsantsanta masa addu'a).[1]

❖ Hukuncin Sallar Jana'iza:

Sallar jana'iza farilla ce ta kifaya, idan wasu suka yi ta, to laifi zai sauka a kan sauran; Annabi (SAW) ya ce ranar da Najashi ya rasu: (Lallai wani ɗan'uwanku ya mutu, don haka ku tashi ku masa salla).[2]

Kuma an sunnanta gaggauta shirya gawa, wajen wanke ta, da saka mata likkafani, da mata salla, da tafiya da ita, da binne ta; saboda faɗinsa (SAW): (Ku yi gaggawar shirya gawa, saboda ita idan ta

[1]. Abu Dawuda ne ya rawaito (3199).
[2]. Muslim ne ya rawaito (952).

kasance ta gari ce, to zuwa ga alheri za ku gabatar da ita, idan kuwa ta kasance koma bayan haka, to, sharri kuke azawa a wuyoyinku).[1]

❖ Falalar sallar jana'iza:

Manzon Allah (SAW) ya ce game da falalar sallar jana'iza: (Duk wanda ya halarci gawa har aka mata salla, yana da ƙiradi guda ɗaya, duk kuwa wanda ya halarce ta har aka binne ta, to yana da ƙiradi guda biyu), aka ce masa: Mene ne ƙiradi biyu? Ya ce: (Kwatankwacin manyan duwatsu guda biyu).[2]

❖ Rukunan sallar jana'iza:

Rukunenta: Su ne ginshiƙanta da take ginuwa da su, waɗanda ba ta inganta sai da su, su guda bakwai ne:

- tsayuwa ga wanda yake da iko.

- Kabbarori guda huɗu.

- Karanta fatiha bayan kabbara ta farko.

- Salati ga Annabi (SAW) bayan kabbara ta biyu.

- Addu'a ga mamaci bayan kabbara ta uku.

- Sallama.

- Da kuma jera Tsakanin rukunai.

❖ Addu'o'i da suka zo game da sallar jana'iza:

An sunnanta yin addu'a ga mamaci da addu'ar da ta zo daga Annabi (SAW):

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito (1351) da Muslim (944).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (1325) da Muslim (945).

(اللهم اغفر لحينا وميتنا، وشاهدنا وغائبنا، وصغيرنا وكبيرنا، وذكرنا وأنثانا, اللهم من أحييته منا فأحيه على الإسلام، ومن توفيته منا فتوفه على الإيمان).

(اللهم اغفر له وارحمه، وعافه واعف عنه، وأكرم نزله، ووسع مدخله، واغسله بالماء والثلج والبرد، ونقه من الخطايا كما نقيت الثوب الأبيض من الدنس، وأبدله دارا خيرا من داره، وأهلا خيرا من أهله، وزوجا خيرا من زوجه، وأدخله الجنة، وأعذه من عذاب القبر، ومن عذاب النار).

وإن كان الميت صغير قال: (اللهم اجعله سلفا لوالديه وفرطا وأجرا).

(Ya Allah Ka gafarta wa rayayyenmu da mataccenmu, da halartaccenmu da wanda ba ya nan, da ƙaraminmu da babbanmu, da namijimu da macenmu, ya Allah duk wanda Ka raya shi daga cikinmu, Ka raya shi a kan Musulunci, duk wanda kuma ka ɗauki ransa daga cikinmu, to ka ɗauki ranshi a kan imani).[1]

(Ya Allah Ka gafarta masa Ka jiƙansa, Ka yafe masa Ka yi masa afuwa, Ka Girmama masauƙinsa, Ka yalwata makwancinsa, Ka wanke shi da ruwa da ƙanƙara da raɓa, Ka tsaftace shi daga kusakurai kamar yadda Ka tsaftace farin tufafi daga dauɗa, Ka sauya masa gidansa da gidan da ya fi shi, da iyalai da suka fi nashi iyalan, da mata da tafi tashi matar, Kuma Ka tsare shi daga azabar ƙabari, da kuma azabar wuta).[2]

Idan mamacin yaro ne kuma sai ya ce: (Ya Allah Ka sanya shi ya zama gabataccen tanadi da taska da lada ga mahaifansa).[3]

Idan kuma ya yi koma wani irin addu’a ne ba wannan ba shi ma ya yi babu damuwa.

---

1. Abu Dawuda ne ya rawaito (3201) da Tirmizi (1024).
2. Muslim ne ya rawaito (963).
3. Abdurrazzaƙ ne ya rawaito (6589).

❖ Rama sallar jana’iza:

Duk wanda wani sashi na sallar jana’iza ya kuɓuce masa, to kawai ya bi liman a inda ya riske shi, idan ya yi sallama sai ya rama abin da ya kuɓuce masa da a bisa siffarsa, wanda kuwa sallar gaba ɗaya ta kuɓuce masa, to yana da damar ya yi masa salla a maƙabarta, kafin a binne shi ko bayan haka; saboda aikin Annabi (SAW) a labarin matar nan da take hidima wa masallaci.[1]

[1]. Bukhari ne ya rawaito (458) da Muslim (956).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

YAƘIN MU'UTA:

❖ Lokacin da ta auku:

Ta auku ne a watan Jumada akhira, ta shekara ta takwas bayan hijira.

❖ Sababanta:

Yaƙin mu'uta ta auku ne a matsayin martini a kan kashe Alharis ɗan Umar Al'azdi (RA), a lokacin da Manzo (SAW) ya aika shi zuwa ga Ƙaisar sarkin Rum don ya kira shi zuwa ga musulunci, sai wani gomna da ke ƙarƙashin rumawa da ake kira Shurahbil ɗan Amru Algassani ya tare shi a hanyarsa ya kashe shi, yayin da Annabi (SAW) ya samu labarin haka sai ya yi fushi, ya kuma kira musulmi zuwa ga jihadi.

❖ Abubuwan da suka faru:

Yaƙin Mu'uta yana daga cikin mafiya mahimmancin yaƙoƙin da musulmai suka yi da rumawa, Manzo (SAW) ya shirya masa runduna da take ɗauke da mayaƙa dubu uku, sai ya ɗaura musu jagorori guda uku, ya kira sunansu a jejjera: Zaidu ɗan Harisa, idan aka kashe shi, sai Ja'afar ɗan Abu Ɗalib, idan shi ma aka kashe shi, sai Abdullahi ɗan Rawaha,[1] sai Manzon Allah (SAW) ya futa tare da su zuwa wani sashi na hanya ya yi musu bankwana, sai suka tafi har labari ya iso gare su cewa Hiraƙla sarkin Rum ya fito zuwa gare su cikin mayaƙa dubu ɗari, tare da shi akwai Maliku ɗan Zafila cikin waɗansu dubu ɗarin daga kiristocin larabawa.

Sai musulmi suka yi shawara a can, suka ce: Za mu rubuta wa Manzon Allah (SAW) saƙo mu nemi umurninsa ko kuma ya ƙara mana mayaƙa. Sai Abdullahi ɗan Rawaha (RA) ya zaburar da

[1]. Bukhari ne ya rawaito (4261).

mutane, ya ce da su: “Ya ku mutane, ina rantsuwa da Allah lallai abin da kuke ƙi tabbas shi ne abin da kuka fito kuna neman, wato shahada, kuma mu ai ba ma yaƙan mutane da adadi, ko ƙarfi, ko yawa, kaɗai muna yaƙan su ne da wannan addini da Allah Ya karrama mu da shi, saboda haka ku kama hanya, ƙarshen lamarin ba komai ba ne face ɗaya daga cikin biyu kyawawa: ko dai nasara ko ko shahada”.[1]

Sai mutane suka yarda da maganarsa, sai suka yunƙura, har sai da suka isa garin Mu’uta, wani ƙauye a ƙasar Sham, sai rundunoni guda biyun suka haɗu a nan, sai yaƙi ya tsananta, sai Zaidu ɗan Harisa (RA) ya yi shahada, alhali tuta kuma tana hannunsa, sai Ja’afar ɗan Abu Ɗalib (RA) ya karɓe ta, ya sauka daga kan dokinsa, sai ya ɗaure shi, sai ya yi yaƙi har sai da aka yanke hannunsa na dama, sai ya riƙe tutar da hannunsa na hagu, shi ma aka yanke shi, sai ya rungumi tutar sannan ya yi shahada, sai Abdullahi ɗan Rawaha Al’ansari (RA) ya karɓi tutar, shi ma ya yi yaƙi har sai da ya yi shahada, sai Manzon Allah (SAW) ya sanar da mutuwarsu ga mutane a Madina kafin labarinsa ya iso musu, idanuwansa suna ta zubar da hawaye, bayan mutuwar waɗannan jagorori guda uku, sai musulmai suka zaɓi Khalid ɗan Walid a matsayin sabon jagoransu, sai Allah Ya kawo ɗauki a hannunsa.[2]

❖ Sakamakonsa:

Lokacin da Khalid ɗan Walid ya karɓi tuta sai ya yi wani tsari na fita daga filin daga, don ya yi gefe da rundunar, ya kuma kuɓutar da musulmai daga abokan gaba, yayin da dare ya yi duhu sai ya sauya wuraren mayaƙa, sai ya sanya sojojin ɓangaren dama suka koma hagu, ‘yan gaba kuma suka koma baya, sai ya nemi mahaya da su ci

[1]. Ɗabari ne ya rawaito (15011).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (4262).

gaba da gudu don su tada ƙura su kuma sa magabta su zaji cewa wasu sojojin ne na ƙari suka zo, sai tsoro ya shiga cikin Rumawa, sai Khalid ya umurci sojoji da su fice daga filin daga, sai musulmai suka juya baya suka koma, sai Allah Ya kare su daga sharrin kafirai, duk da yawan abokan gaba da ƙarancin musulmai ba a kashe cikin musulmi ba face mutum sha biyu kawai, amma an kashe dayawa cikin rumawa, sai wannan yaƙi ya zama tsoratarwa ne da kuma shimfiɗa ga yaƙan rumawa da zai biyo bayan wannan, kuma sababin shigar dayawa daga ƙabilu addinin Allah; kamar ƙabilar banu Sulaim, da Ashja'u, da Gaɗfan, da Zubyan, da sauransu.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SHABBAI

JULAIBIB (RA):

❖ Sunansa da haifuwarsa:

Shi ne Julaibib, sahabi mai daraja, ba a san shi ba sai da wannan sunan nashi, kuma ba a san kwanan watan haifuwarsa ba, kuma ana cewa: Shi ya kasance yana daga ƙabilar banu Sa'alaba ne abokan ƙawancen ansarawa.

❖ Rayuwarsa da falalarsa:

Ya kasance mai sauƙin kai, mai kyakkyawan hali, jarumi da ba ya tsoron mutuwa, kuma ya kasance talaka, ga kuma muni da gajarta, Manzon Allah (SAW) ya bijiro masa da maganar aure, sai ya ce: "Aiko ba za ka samu wacce za ta so ni", sai Manzon Allah (SAW), (Lallai kai a wajen Allah mai darajan ne ba abin kyalewa ba),[1] sai Annabi (SAW) ya nema masa auren 'yar wani mutum cikin mutanen Madina, amma shi mutumin da matarsa kamar ba su so hakan, sai 'yar tasu ta ji abin da Manzon Allah (SAW) ya nema, sai ta ce: Yanzu ƙin karɓar umarnin Manzon Allah (SAW) za ku yi?! Sai ta karanta faɗin Allah Maɗaukaki ((Kuma bai dace ga mumini ko mumina idan Allah da Manzon suka zartar da wani lamari ya zama suna da zaɓi cikin lamarinsu ba),[2] kuma ta ce: Na yarda kuma na miƙa wuya, ku ba da ni gare shi, saboda lallai ba zai tozarta ni ba, sai Annabi (SAW) ya mata addu'a ya ce: (Ya Allah Ka kwaranyo mata da alheri sosai, Kada kuma Ka sanya rayuwarta ta zama ƙunci).[3]

❖ Rasuwarsa:

---

[1]. Abu Ya'ala ne ya rawaito (3343).
[2]. (Al'ahzab: 36).
[3]. Ahmad ne ya rawaito (4/422).

Manzon Allah (SAW) ya rasa shi a wani yaƙi, sai ya ba da umurnin a nemo shi, sai suka same ya kashe mutum bakwai cikin mushirkai sannan aka kashe shi, suna gefanshi a mace, sai Annabi (SAW) ya zo ya tsaya a kansa, sai ya ce: (Ya kashe mutum bakwai), sai kuma ya masa addu'a, ya ce: (Wannan nawa ne ni ma nashi ne), sannan Annabi (SAW) ya ɗauke shi a kan hannayensa, ba shi da wata makara face shi, sai ya binne shi, kuma bai masa salla ba.[1]

[1]. Muslim ne ya rawaito (2472).

Auna fahimtarka a darusan mako na 33			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar faɗinsa Maɗaukaki (Ahwa)?		A
	a. Wanda ya sauya	b. Mai ƙarfi	c. Sabo
Darasin Hadisi	Tambaya: Za a tada mutum ranar alƙiyama tare da:		C
	a. Iyalansa	b. Danginsa.	c. Wanda yake ƙauna.
Darasin Aƙida	Tambaya: Wane ne ya ja kunnen wanda ya yi tambaya game da saɓa wa umurmin Manzon Allah (SAW kuma ya hana shi ɗaukan ihrami daga wami waje daban:		B
	a. Abdullahi ɗan Mas'ud	b. Imanu Malik.	c. Imamul Auza'i.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Nawane rukunen sallar jana'iza?		A
	a. Huɗu ne	b. Biyar ne.	c. Shida ne.
Darasin Sira	Tambaya: Musulmai sun yaƙi….. a yaƙin Mu'uta:		B
	a. Farisawa.	b. Rumawa.	c. Ƙuraishawa.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Julaibib (RA) ya kashe mushirkai ….. kafin ya yi shahada:		C
	a. Uku	b. Biyar	c. Bakwai

MAKO NA TALATIN DA HUƊU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUD-DARIK (1)

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
وَٱلسَّمَآءِ وَٱلطَّارِقِ ١ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا ٱلطَّارِقُ ٢ ٱلنَّجۡمُ ٱلثَّاقِبُ ٣ إِن كُلُّ نَفۡسٖ لَّمَّا
عَلَيۡهَا حَافِظٞ ٤ فَلۡيَنظُرِ ٱلۡإِنسَٰنُ مِمَّ خُلِقَ ٥ خُلِقَ مِن مَّآءٖ دَافِقٖ ٦ يَخۡرُجُ مِنۢ بَيۡنِ
ٱلصُّلۡبِ وَٱلتَّرَآئِبِ ٧ إِنَّهُۥ عَلَىٰ رَجۡعِهِۦ لَقَادِرٞ ٨ يَوۡمَ تُبۡلَى ٱلسَّرَآئِرُ ٩ فَمَا لَهُۥ مِن قُوَّةٖ
وَلَا نَاصِرٖ ١٠﴾

❖ **Fassara:**

Da sunan Allah Mai rahama Mai jinkai

1. Na rantse da sama da (tauraro) mai zuwa cikin dare.
2. Me ya sanar da kai mai zuwa cikin dare?
3. Tauraro ne mai keta (duhu) da haskensa.
4. Ba wani rai face akwai mai tsaron sa.
5. To mutum ya duba mana, daga me aka halicce shi?
6. An halicce shi ne daga wani ruwa mai ingizar juna.
7. Mai fita daga tsakanin tsatso da karankarma.
8. Lallai Shi (Allah) Mai iko ne a kan dawo da shi.
9. A ranar da za a bayyana asirai.
10. To ba shi da wani karfi ko wani mataimaki.

❖ Sakon da surar ta kunsa:

Bayani a kan kudurar Allah da ikonsa wurin halittan mutum da dawo da shi.

❖ Bakin kalmomi:

والطارق	Waddarik	Tauraron da yake bayyana da dare
وما أدراك ما الطارق	Wa ma adaraka maddarik	Me ya sanar da kai lamarin wannan tauraro mai girma?!
الثاقب	Assakib	Mai haske mai walkiya
إن كل نفس لما	In kullu nafisin lamma	Babu wani rai face
حافظ	Hafiz	Mala'ika da yake kiyaye ayyukansu
دافق	Dafik	Mai zuba cikin mahaifa a gaggauce
الصلب	Assulbi	Kashin kadon baya
الترائب	Attara'ib	Kasusuwan kirji
رجعه	Raj'ihi	Dawo da shi rayayye bayan mutuwa
تبلى السرائر	Tublas-sarar'ir	Za a bankada, a bayyana ababen da suke buya cikin zukata

❖ Ma'anar ayoyin a dunkule:

Suratud-Darik sura ce Makkiya, Allah Madaukaki Ya fara ta da rantsuwa mai girma, domin ya yi rantsuwa ne da daya daga cikin ayoyinsa na halitta kayatacciya, wacce ita ce sama da taurarinta masu haske, kuma rantsuwar Allah Madaukaki da halittarsa tana nuni a kan girmansa Mai buwaya da daukaka; saboda lallai girman halitta dalili ne a kan girman Mahalicci, abin da aka yi rantsuwa a kansa kuma shi ne kulawar Allah mai zurfi, da kuma cewa babu wani mutum face hakika Allah Ya wakilta masa wani mala'ika da yake kiyaye masa ayyukansa; don a saka masa da su a ranar alkiyama.

Sannan sai Allah tsarki ya tabbata a gare Shi Ya tunatar da shi da wani dalili daga cikin mafi bayyanar dalilai a kan ƙudurarsa a kan tayar da shi da masa hisabi, wanda shi ne ya yi tunani ya yi duba cikin asalin halittarsa da farkonsa, saboda wanda ya samar da shi daga ruwa mai tunkuɗuwa mai fita daga wannan waje mai wahala, yana da ikon ya mahyar da shi kuma ya dawo da shi ranar lahira, a wannan lokacin kuma za a tona asiran zukata da ababen da suka ɓuya cikinsu, sai sirri ya koma sarari, sai nagartar masu nagarta ta bayyana, da fajircin masu fajirci, kuma mutum a wannan lokaci ba shi da komai face miƙa wuya da sakankancewa, ba shi da wani ƙarfi da zai tunkuɗe hakan daga gare shi, kuma babu wani mai taimako cikin halittu da zai iya taimakonsa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga ayoyin:

1. Tunatarwa game da raunin mutum tun daga lokacin halittar sa da tashinsa, wanda hakan zai hana shi girman kai da taurin kai.

2. Cewa lallai cikin halittar mutum akwai ayoyi da ya wajaba a kansa ya yi tuntuntuni game da su, da ni’imomi da wajibi ne a kansa ya yi godiya a kan samun su.

3. Tunatarwa a kan cewa lallai ayyukan bayi na alheri da na sharri ana ƙididdige su kuma ana kiyaye su.

4. Tsoratarwa game da ɓoye sharri da ɓarna, saboda Allah Masani ne ga bayinsa cikin dukkan abin da suke ɓoyewa ko suke bayyanawa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

TSORATARWA A KAN FUSHI:

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Wani mutum ya zo, sai ya ce: Ya Manzon Allah, Ka yi mun wasiya. Annabi (SAW) Ya ce: (**Kada ka yi fushi**), sai ya maimaita masa tambaya sau da dama, ya dai ce masa: (**Kada kai yi fushi**).[1]

❖ Sharhi:

Maganar Annabi (SAW): "Kada ka yi fushi" tana ƙunshe da nusarwa guda biyu manya a kan nisantar fushi:

Na farko: Umurni da yin abubuwan da ke hana fushi a lokacin da aka samu dalilinsa; na danne zuciya, da horar da kai a kan huƙuri da juriya, da shirya ta a kan jure cutarwar halittu, idan aka datar da bawa da haka, sai ya kasance a shirye yake a kan sababin fushi, da tunkuɗe shi da juriyarsa da haƙurinsa.

Na biyu: Umurni da barin aiwatar da abin da zai zo bayan fushi; domin wasu lokuta mutum ba zai iya hana fushinsa ba, amma zai iya barin zartar da shi; ta hanyar tunawa da wasiyyar Annabi (SAW), da kuma hana kansa magana ko aiki da fushinsa zai jawo shi, da kuma tunawa da abin da fushi zai iya jawowa na illoli marasa kyau.

❖ Abubuwan da za mu koya daga Hadisin:

1. Mahimmancin neman wasiyya daga malamai da salihai.

2. Cewa hani a kan wani abu yana nufin hani a kan sababinsa, da umarni da abin da zai taimaka wajen barinsa.

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito (6116).

3. Wajibcin horar da kai a kan kyawawan ɗabi'u, da juriya da haƙuri, da kuma cewa hakan na daga cikar ƙarfin hankali da addini.

4. Cewa duk wanda ya hana kansa faɗawa cikin tasirin fushi, a haƙiƙanin lamari yana daidai da wanda bai yi fushi ba.

5. Cewa cikin umarnin Allah Maɗaukaki da umarnin Manzonsa (SAW) akwai alheri da rabauta ga Musulmi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

MISALAN BIDI'A:

Bidi'o'i a addini ba su gushe ba suna sabantuwa kuma sana samuwa ɗaya bayan ɗaya, sai Allah Ya tanadar musu wanda zai yaƙe su daga cikin malamai masu zurfin ilimi ta hanyar bayyana su da fayyace su; wannan kariya ne daga Allah ga shari'arsa, da kuma kiyaye addininsa.

❖ **Daga cikin misalan waɗannan bidi'o'i akwai:**

1. Abin da ya yaɗu a wajen wasu Musulmi na yin bikin maulidi, wato bikin haihuwar Annabi (SAW), a watan Rabi'ul Awwal daga kowace shekara, wannan bidi'a ce mummuna, domin ba ta da asali a cikin Alƙur'ani da Sunna, da aikin magabata na ƙwarai, 'yan shi'ar Faɗimiyya ne suka ƙirƙiro bayan ƙarni na huɗu na hijira, haka kuma yin bikin daren Isra'i da Mi'iraaji, ko bikin hijirar Annabi zuwa Madina, dukkanin waɗannan suna daga cikin bidi'o'i da ba su da dalili a kansu, kuma sahabbai ba su aikata su ba, haka kuma waɗanda suka biyo bayansu cikin ƙarnoni masu falala, da ace alheri ne da sun fi mu cancanta da yin su, domin su sun fi ƙaunar Annabi (SAW) fiye da mu, kuma sun fi girmama shi, kuma sun kasance mafiya son aikata alheri, kuma sun fi gaggawar aikata aiki nagari, sai su sun san cewa son Annabi (SAW) da girmama shi suna kasancewa ne ta hanyar bin sa, da biyayya gare shi, da bin umurninsa, da raya sunnarsa a fili da ɓoye, da yaɗa abin da ya zo da shi.

2. Tabarruki da wurare da gurabe da ƙaburbura da mutane, rayayyu da matattu; Wannan na daga cikin bidi'o'in da aka ƙirƙira, wanda ya shigo wa Musulmi ta hanyar aƙidun bautan wanin Allah, kuma shar'ancinsa bai tabbata ba, ba a zamanin (SAW) ba, haka kuma ba

a zamanin halifofinsa shiryayyu ba, bari dai Umaru ɗan Khaɗɗab (RA), ya sare bishiyar da ke Hudaybiyya wadda aka yi mubaya'a a ƙarƙashinta, lokacin da ya ga wasu mutane suna zuwa suna tabarruki da ita.[1]

3. Karanta suratul-Fatiha a wajajen taro, domin keɓance Fatiha da haka bai zo ba kwata-kwata, kuma ba a aikata shi ba sai a baya-baya.
4. Keɓance watan Rajab da umara da ake kira "Rajabiyya", da kuma keɓance shi da salloli, da azumi, da yanka.
5. Rungumar wasu zikirori da aka ƙirƙira, saɓanin zikirori da aka shar'anta, ta fuskar lafazi, da yadda ake yin su, da lokutansu.
6. Keɓance daren tsakiyar Sha'ban da yinin tsakiyar watan Sha'aban da azumi.

❖ **Illolin bidi'o'i da mummunan tasirinsu:**

1. Bidi'o'i tsani ne zuwa kafirci, kuma hanya ne na rusa addini; domin suna raunana girman shari'a a zuciya, kuma suna hana bin Alƙur'ani da Sunna.
2. Bidi'o'i sun fi zama sharri a kan manyan zunubai; saboda abin da ke cikinsa na sukan addinin Allah, da jingina masa tawaya.
3. Bidi'o'i suna kashe Sunna, kuma suna sa a kyamaci aiki da ita; wannan ya isa ya zama sababin karkacewar zukata da lalacewarsu.
4. Bidi'a na daga cikin manyan sabuban mummunan ƙarshe; domin mai aikata zunubi yana sane da cewa laifi yake yi, kuma akwai fatan zai iya tuba daga gare shi, shi kuma ɗan bidi'a yana ɗaukar bidi'arsa a matsayin addini da zai kusanci Allah da shi, sau dayawa tuba na haramta a gare shi, sai a jarrabe shi da mummunan ƙarshe!

[1]. Ibnu Abi Shaiba ne ya rawaito (2/73) da Ibnu Sa'ad a Ɗabaƙat (2/100).

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

ZIKIRORI BAYAN SALLA

An shar'anta wa Musulmi gaggauta yin zikirori da aka shar'anta bayan ya idar da sallarsa, daga cikinsu akwai:

Na farko: Faɗin (**Astagfirullah**) sau uku, da faɗin: (**Allahumma antas-salam wa minkas-salam, tabarakta ya zal jalali wal ikram**).[1]

Na biyu: Faɗin: (**La ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu, lahul-mulku wa lahul-hamdu wa huwa ala kulli shai'in ƙadir, Allahumma la mani'a lima a'aɗaita wa la mu'ɗiya lima mana'ta, wa la yanfa'ul-zaljaddi minkal-jaddi**).[2]

Na uku: Faɗin: (**La ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu, lahul-mulku wa lahul-hamdu wa huwa ala kulli shai'in ƙadir, la haula wa la ƙuwwata illa billah, la ilaha illallahu wa la na'budu illa iyyahu, lahunni'matu wa lahulfadlu wa lahus-sana'ul hasan, la ilaha illallahu mukhlisina lahuddina wa lau karihal kafirun**).[3]

Na huɗu: Tasbihi da hamdala da kabbara, kuma suna da sifofi guda huɗu:

- Siffa ta farko: Mutum ya ce: "**Subhanallah**" ƙafa goma, "**Alhamdu lillah**" ƙafa goma, "**Allahu Akbar**" ƙafa goma.[4]

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (591).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (844) da Muslim (593).
[3]. Muslim ne ya rawaito (594).
[4]. Bukhari ne ya rawaito (6116) da Muslim (595).

- Siffa ta biyu: Ya ce: "**Subhannallah**" ƙafa ashirin da biyar, "**Alhamdu lillah**" ƙafa ashirin da biyar, "**Allahu Akbar**" ƙafa ashirin da biyar, "**La'ilaha illallah**" ƙafa ashirin da biyar.[1]

Siffa ta uku: Ya ce: "**Subhallah**" ƙafa talatin da uku, "**Alhamdu lillah**" ƙafa talatin da uku, "**Allahu Akbar**" ƙafa talatin da huɗu.[2]

Siffa ta huɗu: Ya ce: "**Subhanallah**" ƙafa talatin da uku, "**Alhamdu lillah**" ƙafa talatin da uku, "**Allahu Akbar**" ƙafa talatin da uku, "**La ilaha illallahu wahdahu la sharika lahu, lahul-mulku wa lahul-hamdu wa huwa ala kulli shai'in ƙadir**" cikoton ɗari.[3]

Kuma yana da daman ya haɗa tsakanin tasbihi da hamdala da kabbara, sai ya ce: "**Subhanallah, walhamdu lillah, wallahu Akbar**", sai ya ta yi har sai ya kai talatin da uku.[4]

Na biyar: Karanta ayatul-kursiyyi; Annabi (SAW) ya ce: (Duk wanda ya karanta ayatulkursiyyi bayan kowace salla ta farilla, babu abin da zai hana shi shiga aljanna sai mutuwa).[5]

Na shida: Karanta ƙula'uzai, wata: (Ƙul huwa, da Falaƙi da Nasi) bayan kowace salla, da maimaita su bayan sallar asuba da ta Magariba sau uku; An rawaito daga Uƙuba ɗan Amir (RA) ya ce: "Manzon Allah (SAW) ya umurce ni da na karanta ƙula'uzai bayan kowace salla".[6]

---

1. Tirmizi ne ya rawaito (6116), da Nasa'i (1350).
2. Muslim ne ya rawaito (596).
3. Muslim ne ya rawaito (597).
4. Bukhari ne ya rawaito (843).
5. Nasa'i ne ya rawaito (9848).
6. Abu Dawuda ne ya rawaito (1523).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

BUƊE MAKKA

❖ Lokacin aukuwarsa:

Buɗe Makka ya auku ne a rana ta ashirin ga watan Ramadan, a shekara ta takwas bayan hijira.

❖ Sababansa:

Sababinsa: shi ne warware sulhun Hudaibiyya da Ƙuraishawa suka yi, ta hanyar ta'addanci da ƙabilar banu Bakr (abokan ƙawancen Ƙuraishawa) ga ƙabilar Khuza'a (abokan ƙawancen musulmi), ta yadda suka kashe adadi mai yawa daga cikinsu, Ƙuraishawa kuma sun kasance suna ba su makami kuma suna taimakon su a kan ta'addanci a Harami a sirrance, a lokacin ba a wuce shekara ɗaya da wata tara da yin sulhun Hudaibiyya ba, sannan sai Ƙuraishawa suka yi nadama a kan warware alƙawari da suka yi, sai suka aika Abu Sufyan ɗan Harb zuwa ga Manzon Allah (SAW) don ya ƙarfafa yarjejeniyar, sai ya zo Madina, ya bijiro wa Annabi (SAW) hakan, amma Annabi (SAW) bai mayar masa da amsa ba, sannan ya tafi wurin Abubakar (RA), sai ya neme shi da ya yi wa Manzon Allah (SAW) magana sai ya ƙi, sannan ya tafi wurin Umar (RA) sai ya kausasa masa, ya ce: "Kuma ni kake so na aikata haka?! Ina rantsuwa da Allah da ace ba ni da komai face ɗan ƙanƙanin abu da sai na yaƙe ku da shi", sai kuma ya tafi wurin Aliyyu (RA) shi ma bai yarda ya aikata hakan ba, sai ya nemi Faɗima 'yar Manzon Allah (SAW) Allah ya ƙara mata yarda da ta umurci ɗanta Alhassan da ya zama kariya ga mutane, sai ta ce: "Dana bai kai ya aikata haka ba,

kuma babu wanda zai iya ba da kariya daga Manzon Allah (SAW),[1] sai Abu Sufyan ya dawo Makka ba tare da buƙata ta biya ba!

❖ Abubuwan da suka faru:

Annabi (SAW) ya umurci Musulmi da su shirya, su kuma yunƙuro don tafiya, sai ya yi amfani da sirri wurin shirya rundunar sojoji, ya kuma roƙi Allah Mai girma da ɗaukaka da Ya katange Ƙuraishawa daga samun labari, sai Ubangijinsa Mai girma da ɗaukaka Ya amsa masa.[2]

Sai rundunar ta kama hanya a ranar goma ga watan Ramadan, cikin mayaƙa dubu goma, sai Annabi (SAW) ya rarraba su zuwa runduna biyar, kuma Annabi (SAW) ya kasance shi ne jagora a kan runduna ta farko, amma sauran rundunonin sai ya sanya wa kowannensu jagora, waɗanda su ne: (Azzubair ɗan Awwam, Khalid ɗan Walid, Abu Ubaida ɗan Jarrah, da kuma Ƙais ɗan Sa'ad ɗan Ubada), kuma ya umarce kowane jagora da ya shiga Makka ta wani ɓangare ayyananne, amma kada su far wa kowa sai wanda ya yaƙe su.

❖ Sakamakonsa:

Musulmi sun shiga Makka ba tare da yaƙi ba, sannan suka nufaci Ka'aba, yayin da Annabi (SAW) ya ga Ka'aba, sai ya yi kabbara mai yawa, sai su ma suka yi kabbara tare da shi har sai da Makka ta girgiza, sannan sai suka yi shiru bayan umurnin da Annabi (SAW) ya yi musu da hakan, farkon abin da ya fara kuwa shi ne ɗawafi, sai ya riƙa kewaye Ka'aba, kuma ya riƙe rushe kowane gunki da ke kewane da ita, yana kuma karanta faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma ka ce: "Gaskiya ta zo, ɓarna kuma ta watse. Lallai da ma can ita

[1]. Albidaya wan-nhaya (4/280).
[2]. Albidaya wan-nihaya (4/280).

ɓarna watsattsiya ce”)),[1] sannan sai Annabi (SAW) ya aika ƙananan rundunoni zuwa ga unguwannin da suke kewaye da Makka don su kira su zuwa ga Musulunci.

[1]. (Al’isra: 81).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ZAIDU ƊAN SABIT (RA)

❖ Sunansa da haifuwarsa:

Shi ne sahabin nan kuma ɗan sahabbai Zaidu ɗan Sabit, babansa Sabit ɗan Dahhak Al'ansari, mamarsa kuma ita ce Annuwaru 'yar Malik Al'ansariya.

An haifi Zaidu a Madina, kafin hijira Annabi (SAW) zuwa gare ta da shekara goma sha biyu.

❖ Rayuwarsa da falalarsa:

Zaidu ɗan Sabit (RA) ya kasance ɗan ƙarami a lokacin da Manzon Allah (SAW) ya zo Madina, kuma ya kasance daga cikin sahabbai da suka koyi rubutu daga fursunonin yaƙin Ƙuraishawa bayan yaƙin Badar, sai ya rawaici hadisai daga Annabi (SAW), kuma ya koyi Alƙur'ani a wajensa, sai ya zama ɗaya daga cikin masu rubuta wahayi kuma daga cikin masana Fiƙihu a Madina, duk da ƙanƙantan shekarunsa; Har ma Annabi (SAW) ya ce game da shi: (Wanda ya fi sanin rabon gado cikin al'ummata shi ne Zaidu ɗan Sabit).[1]

Bayan rasuwar Annabi (SAW) Zaidu (RA) ya zama mai ba wa mutane fatawa a Madina, kuma malamin makarantar Alƙur'ani a nan, kuma an san shi da hikima da ra'ayi mai kyawu; a ranar da musulmi suka haɗu a ƙarƙashin saƙifa ta banu Sa'ida don zaɓan halifa ga musulmi, Zaidu ya faɗi magana mai ɗauke da hikima: "Lallai Manzon Allah (SAW) ya kasance daga cikin muhajirai, kuma lallai shugaba zai kasance ne kawai daga muhajirai, mu kuma

[1]. Abu Ya'ala ne ya rawaito (5763) da Baihaƙi (12549).

masu taimakon sa ne kamar yadda muka kasance masu taimakon Manzon Allah (SAW)".[1]

Abubakar (RA) ya shugabantar da shi a kan raba ganimar yaƙin Yarmuk, kuma yayin da ya yi nufin tattara Alƙur'ani sai ya shugabantar da Zaidu a kan wannan aikin; yana cewa (RA): "Sai na tashi na bibiyi Alƙur'ani ina tattara shi daga fatu da ƙashin kafaɗu da ganyen dabino da zukatan mazaje".[2]

Haka kuma a zamanin halifancin Usman ɗan Affan, kalmar Zaidu ta kasance ita ce hujja kuma yankakken hukunci a kan dukkan Alƙur'ani da kuma tabbatar da shi.

Haka kuma, Umar ɗan Khaɗɗab (RA) ya ba shi matsayin alƙalanci, kuma ya kasance yana ɗaura masa shugabancin Madina idan zai yi hajji.

❖ Rasuwarsa:

Zaidu (RA) ya rasu a shekara ta arba'in da biyar bayan hijira, a zamanin Mu'awiya (RA), kuma an binne shi a maƙabartar Baƙi, a ranar rasuwarsa ne ibnu Abbas (RA) ya ce: "Haƙiƙa tabbas an binne ilimi mai yawa yau".[3]

---

[1]. Ahmad ne ya rawaito (21617).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (4986).
[3]. Siyaru a'alamin-nubala (2/440).

Auna fahimtarka a darusan mako na 34			**Amsa na ƙwarai**
Darasin Tafsiri	Tambaya: Allah Maɗaukaki Ya yi rantsuwa da “Aɗɗariƙ” wanda shi ne:		A
	a. Tauraron da yake fitowa da dare	b. Hasken lokacin asuba	c. Shafaƙin lokacin faɗuwar rana
Darasin Hadisi	Tambaya: Lokacin da wani mutum ya nemi Annabi (SAW) ya masa wasiyya, ya masa wasiyya ne da faɗin:		B
	a. Ka rintsa idonka	b. Kada ka yi fushi.	c. Ka lura da tunaninka.
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin illolin bidi’a akwai:		C
	a. Cewa tana jawo toshe arziki.	b. Cewa lallai tana tasiri ga lafiyar hankali.	c. Cewa tana daga cikin sabuban mummunan ƙarshe.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin ayoyi da aka shar’anta karanta su bayan kowace salla akwai:		C
	a. Ayoyin ƙarshe suratul-Baƙara	b. ayoyin ƙarshen suratu Alu-imran.	c. Ayatul-kursiyyi.
Darasin Sira	Tambaya: Buɗe Makka ya auku ne a shekara ta:		B
	a. 7 bayan hijira.	b. 8 bayan hijira.	c. 9 bayan hijira.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Zaidu ɗan Sabit (RA) ya ƙware a ilimin:		A
	a. Rabon gado	b. Nasaba	c. Tafsiri

MAKO NA TALATIN DA BIYAR

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUD-DARIK (2)

﴿وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلرَّجۡعِ ﴿١١﴾ وَٱلۡأَرۡضِ ذَاتِ ٱلصَّدۡعِ ﴿١٢﴾ إِنَّهُۥ لَقَوۡلٞ فَصۡلٞ ﴿١٣﴾ وَمَا هُوَ بِٱلۡهَزۡلِ ﴿١٤﴾ إِنَّهُمۡ يَكِيدُونَ كَيۡدٗا ﴿١٥﴾ وَأَكِيدُ كَيۡدٗا ﴿١٦﴾ فَمَهِّلِ ٱلۡكَٰفِرِينَ أَمۡهِلۡهُمۡ رُوَيۡدَۢا ﴿١٧﴾﴾

❖ Fassara

11. Na rantse da sama ma'abociyar dawo (da ruwa).

12. Da kuma ƙasa ma'abociyar tsagewa (Shuka su fito).

13. Lallai shi (Alƙur'ani) magana ce mai tsage gaskiya.

14. Kuma shi ba zancen banza ba ne.

15. Lallai su (kafirai) suna ƙulla mummunan makirci.

16. Ni kuma ina shirya musu mummunan sakamako.

17. To sai ka saurara wa kafirai, ka saurara musu kaɗan.

❖ Saƙon da ayoyin suka ƙunsa:

Gaskiyar Alƙur'ani da ingancinsa.

❖ Bayin kamomi:

والسماء ذات الرجع	Wassama'i zatir-raj'i	Ma'abociyar ruwa mai maimaituwa.
والأرض ذات الصدع	Wal'ardi zatis-sad'i	Ma'abociyar tsagewa don shukoki su fito.
إنه لقول فصل	Innahu laƙaulun fasl	Mai rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya.
أمهلهم رويدا	Amhilhum ruwaida	Lokaci ɗan kaɗan.

❖ Ma’anar ayoyin a dunƙule:

Allah Maɗaukakin Sarki Yana rantsuwa a cikin waɗannan ayoyi da halittu masu girma, waɗanda bayi suke ganinsu a kullum, sai ya yi rantsuwa da sama wacce saukar da ruwa a kai a kai, sai Ya raya matacciyar ƙasa da shi, Ya kuma shayar da mutane da dabbobi da shi, sannan Ya yi rantsuwa da ƙasa, wacce take tsagewa don shukoki da ‘ya’yan itatuwa su tsuro, sai rayayyu su samu abincinsu da dukiyoyinsu daga gare ta, babu wani abu da zai ragu musu daga hakan.

Amma abin da aka yi rantsuwa a kansa, shi ne gaskiyar wannan alƙur’ani da aka saukar wa Annabi Muhammadu (SAW), da kuma cewa shi magana ne na gaskiya, wanda ya kai maƙura wurin bayani da fayyacewa, mai rarrabe tsakanin gaskiya da ƙarya, gaskiya ne ba wargi ba kuma ba wasa ba.

Sai dai ita ɗabi’ar masu ƙaryatawa ita ce mayar da wannan kira ta hanyar makirce-makirce masu yawa, da inkarin gaskiya ta hanyar dabarbaru mabanbanta, waɗanda Alalh Yake lalata su da shirinsa, kuma Yake rusa su tanyar uƙuba; don Ya bayyana addininsa, Ya kuma taimaki littafinsa, kuma Ya ɗaukaka Manzonsa (SAW), sai dai sunnar Allah Maɗaukaki ita ce talala ga waɗannan kafirai, don haka kada yi gaggawan neman a azabtar da su ko a halakar da su; saboda wannan yana da lokaci da babu kokonto a cikinsa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga waɗannan ayoyi:

1. Bayanin gaskiyar Alƙur’ani mai girma, da ƙarfin hujjrsa.

2. Kariyar Allah ga muminai, da kiyaye su daga kaidin kafirai.

3. Raunin kaidin kafirai idan aka kwatanta shi da shirin Allah Maɗaukakin Sarki.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

HARAMCIN GIRMAN KAI

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Ba zai shiga aljanna ba wanda cikin zuciyarsa akwai koda kwatankwacin ƙwayar zarra ne na girman kai), sai wani mutum ya ce: Lallai ɗaya daga cikinmu yana son a ce tufafinsa yana da kyau, kuma takalminsa ma na da kyau. Sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lallai Allah kyakkyawa ne, Yana son mai kyau, girman kai shi ne take gaskiya da rena mutane).[1]

❖ Sharhi:

Wannan hadisi yana nuni a kan cewa girman kai yana wajabta shiga wuta, kuma yana hana shiga aljanna, ko da ɗan ƙarami ne a cikin zuciyar bawa, sannan Annabi (SAW) ya bayyana cewa girman kai nau'i biyu ne:

Na farko: Yin girman kai wa gaskiya, wanda shi ne mayar da gaskiya, da take ta, da ƙin karɓar shi; saboda Allah Maɗaukakin Sarki Ya wajabta wa bayi sauke kansu ga gaskiyar da Allah Ya aiko Manzanninsa da ita, kuma su gabatar da shi a kan ra'ayoyinsu da soye-soyen zukatansu, duk wanda ya mayar da ita, to shi mai girman kai ne kuma abin yi wa alƙawari ne da narkon azaba.

Nau'i na biyu: Girman kai ga halittu, ta hanyar raina su da wulaƙanta su da yin izgili gare su, da rage musu daraja ta hanyar maganarsa ko aikinsa, wannan nau'i yana samuwa ne saboda jijin mutum da kansa, da ganin cewa ya fi waninsa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

[1]. Muslim ne ya rawaito (91).

1. Girman kai yana daga cikin manyan zunubai, waɗanda suke sabbaba faɗawa cikin azabar Allah.

2. Mahimmancin tsaftace zuciya daga girman kai; saboda lallai aljanna gida ce mai dadi, wacce take haramtuwa ga kowane mai girman kai.

3. Wajibcin guje wa mayar da gaskiya tabbatacciya a Alƙur'ani mai girma ko sunnar Manzo (SAW), da kuma cewa hakan yana cikin girman kai.

4. Wajibcin ƙanƙan da kai ga musulmi, da sassauta mu'amala gare su, kuma girman kai na haramta a gare su.

5. Cewa kyawu na zahiri da kwalliya na tufafi da abin hawa ba sa shiga cikin girman kai, da sharaɗin ya zama babu almubazzaranci ko raina wasu a cikinsa.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

RABE-RABEN ZIYARTAR ƘABURBURA

❋ Ziyartar ƙaburƀura ta kasu kashi biyu:

Ziyara da shira'a ta yarda da ita, da ziyara ta bidi'a.

- **Ita ziyarar da shiri'a ta yarda da ita**, ita ce wacce take kasance da wata manufa da aka shar'anta, misali:

1. Ya nufi sallama ga mamata da addu'a gare su.

2. Ya nufi salla ga mamaci sallar jana'iza.

3. Ya nufi tuna mutuwa da gidan lahira.

Waɗannan ziyarori shari'a ta yarda da su kuma tana so a riƙa yin su, saboda sunna ta yi nuni a kan shar'antuwarsu; ya zo a sahihu Muslim cewa: Manzon Allah (SAW) ya ce: (Da na hana ku ziyartar ƙaburbura, yanzu ku ziyarce su), a riwayar Tirmizi kuma ya ce: (Saboda lallai tana tunatarwa game da lahira),[1] kuma ya zo a Bukhari da Muslim cewa wata mata baƙa ta kasance tana yin hidima a masallaci, sai ta rasu, sai Annabi (SAW) ya yi tambaya game da ita, sai suka ce: Ta rasu. Ya ce: (Me ya hana ku sanar da ni? Ku nuna mun ƙabarinta), sai ya je ya mata salla.[2]

- **Na biyu**: **Ziyara ta bidi'a**, ita ce wacce take kasancewa saboda wata manufa haramtacciya, misali:

1. Ya ziyarci mamata don ya roƙe su buƙatarsa, wannan shirka ce mai girma, daga jinsin bautar gumaka.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (1977), da Tirmizi (1054).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (460), da Muslim (956).

2. Ya roƙi Allah Maɗaukaki Sarki yana mai tawassuli da mamaci; kaman wanda zai ce: Ya Allah ni ina tawassuli zuwa gare ka da Annabinka, ko da haƙƙin shehi wane, wannan yana daga cikin bidi'o'i da kuma hanyoyin shirka.

3. Ya zaci cewa roƙon Allah a wajen ƙaburbura abin amsawa ne. Wannan shi me yana cikin bidi'o'i munana da ijma'in malamai, don haka ne Annabi (SAW) ya kausasa magana game da haka, har ma ya ce: (Ya Allah kada kada ka mayar da ƙabarina ya zama gunki da za a riƙa bauta masa).[1]

[1]. Bukhari ne ya rawaito (437), da Muslim (530).

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

ZAKKA

❖ Mahimmancin zakka:

Zakka farilla ce daga cikin farillan musulunci, kuma ita ce mafi mahimmancin rukunansa bayan salla, kuma haƙiƙa Allah Maɗaukakin Sarki Ya haɗa ta da salla a waje tamanin da biyu; wanda haka yana nuni a kan girma matsayinta, da cikar alaƙa tsakaninta da salla.

❖ Dalilan wajibcinta:

- Allah Maɗaukaki Sarki Ya ce: ((Ku tsayar da salla kuma ku ba da zakka)).[1]
- Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ka karɓi wata sadaka daga dukiyoyinsu, wacce za ta tsakake su kuma ka tsarkake su da ita)).[2]
- Kuma Annabi (SAW) ya ce: (An gina musulunci a bisa ginshiƙai biyar: Shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, kuma Annabi Muhammadu bawan Allah ne, da tsayar da salla, da bayar da zakka, da azumin watan Ramadan, da aikin hajji).[3]

❋ **Kamar yadda kuma alƙawarin narko mai tsanani ya zo a haƙƙin wanda ya bar zakka ko ya yi sakaci da ita:**

- Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Kuma waɗanda suke ɓoye zinariya da azurfa ba sa ciyar da ita saboda Allah, to ka yi musu albishir da wata azaba mai raɗaɗî () Ranar da za a narkar da su a cikin wutar jahannama sannan a yi wa fuskokinsu da kuyaɓunsu da bayansu lalas da su, a (a ce da su): “Wannan shi ne abin da kuka taskace wa kanku, sai ku ɗanɗani abin da kuka kasance kuna taskacewa”).[4]

---

[1]. (Albaƙara: 43).
[2]. (Attauba: 103).
[3]. Bukhari ne ya rawaito (8), da Muslim (16).
[4]. (Attauba: 34-35).

- Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wani ma'abocin taska, wanda ba ya ba da zakkarta, face sai an narkar da ita a cikin wutar Jahannama, sai a mayar da su kamar faranti, sai a riƙa yi wa kuyaɓunsa da goshinsa lalas da ita, har sai Allah Ya yi hukunci a tsakanin bayinsa a wani yini da tsawonsa ya kai gwargwadon shekara dubu hamsin, sannan sai ya ga hanyarsa, ko dai zuwa aljanna, ko kuma zuwa wuta).[1]

❖ A kan wa zakka take wajaba?

Zakka tana wajaba ne a kan kowane musulmi da ya mallaki nisabi na dukiya, na miji ne ko ko mace, balagagge ko yaro, mai hankali ko mahaukaci, sai waliyyin yaro ko mahaukaci ya jiɓinci fitar da zakka daga dukiyarsu; saboda shi zai tsaya a maimakonsu wurin ba da haƙƙoƙi; Umar (RA) ya ce: "Ku riƙa juya dukiyar marayu, saboda kada zakka ta cinye ta".[2]

Hikimar wajabta zakka:

An shar'anta zakka ne saboda wata hikima maɗaukakiya, da manufofi masu girma, daga cikinsu akwai:

1. Gode wa Allah a kan ni'imar yalwar dukiya da Ya yi ga mutum.

2. Tsarkake dukiya da haɓaka ta da sauke albarka a cikinta, da tafiyar da sharrinta, da kare ta daga lalacewa da taɓarɓarewa.

3. Tsarkake mai ba da zakka daga ƙauro da rowa, da horar da shi a kan sakin hannu da ciyarwa saboda Allah.

4. Tsarkake mai ba da zakka daga dattin zunubai da kurakurai.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (1648).
[2]. Abdurrazzaƙ ne ya rawaito (6773).

5. Rarrashin talaka, da biyan buƙatar masu ƙaramin hali da marasa abin hannu.

6. Tabbatar da ƙauna tsakanin al’umma; sai mai wadata ya rarrashi zuciyar talaka da ita, ya kuma tunkuɗe masa ƙeta da hasada.

7. Tabbatar da gaskiyar imani; don haka ne aka kira ta da sadaka; saboda gaskiyar imanin ma’abocinta a lokacin da ya ba da abin da yake so don neman yardar Allah.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

YAƘIN HUNAINI

❖ Lokacin da aka yi shi:

An yi shi ne a watan Shawwal, a shekara ta takwas bayan hijira.

❖ Sabuban faruwarsa:

Yayin da aka buɗe Makka, ƙauyuka da suke kusa da Makka sun girgiza saboda tsoro da firgici, sai Maliku ɗan Auf Annasri ya haɗa runduna daga ƙabilar Hawazin don yaƙan musulmi, sai kuma wasu ƙabilu suka mara wa Hawazin baya; kamar Saƙif da Banu Nasr bin Mu'awiya, da Banu Jusham, da Banu Sa'ad bin Bakr, da Bashar, da wasu mutane daga ƙabilar Banu Hilal bin Amir, kuma suka tafi tare da matansu da dabbobinsu don kada su gudu.[1]

❖ Abubuwan da suka faru:

Yayin da labarinsu ya iso wa Manzon Allah (SAW), sai ya aika Abdullahi ɗan Abu Hadrad Al'aslami, sai ya binciko masa labarin hali da suke ciki, sannan sai Manzon Allah (SAW) ya yi shirin gamuwa da su, sai ya ari sulke daga Safwan ɗan Abu Umayya, ya kuma karɓi bashin wani adadi na kuɗi daga gare shi, sai ya kama hanya zuwa gare su cikin mutum dubu goma waɗanda suka kasance tare da shi lokacin buɗe Makka, tare da mutum dubu biyu cikin waɗanda suka musulunta a wannan ranar, sai ya wakilta Attab ɗan Asid a Makka, a lokacin yana ɗan shekara Ashirin.[2]

Sai Manzon Allah ya bi ta wajen wata bishiya da mushirkai suke girmamawa a lokacin da yake kan hanyarsa , ana kiran wannan bishiya da "ma'bociyar rataya", sai wasu daga cikin jahilan

---

[1]. Alfusul (204).
[2]. Alfusul (204).

larabawa suka ce: Ka nema mana ma'bociyar rataya kamar yadda waɗannan suke da ita. Sai ya ce: (Ina rantsuwa da wanda raina ke hannunsa, kun faɗi irin abin da mutanen Musa suka faɗa: ((Ka sanya mana abin bauta irin abin bautarsu, ya ce lallai ku mutane ne da ba ku da sani),[1] lallai wannan tafarki ne, tabbas da sannu za ku bi tafarkin waɗanda suka shuɗe gabaninku).[2]

Sannan sai Annabi (SAW) ya kama hanya cikin runduna mai girma, har ma wasu daga cikinsu suka kamu da jiji da kai, sai suka ce: In dai dan rashin yawa ne, to yau ba za a ci nasarar a kanmu ba! Yayin da suka isa Hunain, wanda shi ɗin wani kwari ne daga cikin kwarurruka Tihama, yana isowa sai ya yi karo da Hawazin sun yi musu kwanton ɓauna a lokacin duhun asubahi, sai suka far wa musulmi a bazata, sai musulmi suka juya baya ba wanda yake waiwayen ɗan'uwansa;[3] wannan shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ((Da kuma ranar yaƙin Hunaini lokacin da yawanku ya rude ku sai yawan naku bai amfana muku komai ba, ƙasa kuma ta yi muku ƙunci duk da yalwarta, sannan kuka juya kuna masu ba da baya)).[4]

❖ Sakamakonsa:

Manzon Allah (SAW) ya tsaya tare da wasu jama'a cikin sahabbai, daga cikinsu akwai: Abubakar, da Umar, da Ali, da baffansa Abbas, da 'ya'yansa Fadlu da Ƙusamu, da Abu Sufyan, da ɗansa Ja'afar, da wasu mutanen, shi kuma Manzon (SAW) a wannan ranar yana haye kan godiyarsa, yana fuskantar da ita wajen abokan gaba, shi kuma

[1]. (Al'Araf: 138).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito (2180).
[3]. Alfusul (205).
[4]. (Attauba: 25).

Abbas yana rika da linzaminta yana hana ta tafiya, yana mai cewa: (Ni ne Annabi ba karya, Ni ne dan AbdulMuddalib).[1]

Sannan ya umurci Abbas da ya yi kira – da yake mutum ne mai babban murya – ya ce: (Ya ku taron Ansarawa, ya ma'abota suratul-Bakara), yayin da suka ji wannan kira, sai suka dawo kamar yadda ka san rakuma ne masu shauki 'ya'yansu, a wannan lokacin sai yaki ya kaure ya kuma tsananta, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Yanzu ne yaki ya yi zafi), sai ya dibi fararen tsakwankwani a tafin hannunsa, sai ya watsar da su, sai ya ce: (Ina rantsuwa da Ubangijin Ka'aba sun tarwatse).

A wannan ranar Aliyyu dan Abu Dalib ya kasance shi ne ya fi dukkan mutane tsananin yaki a gabansa,[2] sai Allah Ya jefa tsoro a zukatan Hawazin, ba su iya jurewa ba, sai suka gudu, musulmai kuma suka rika bin su suna kashe wasu suna kuma kama wasu, sai suka kashe kusan mutum arba'in a cikinsu, su kuma musulmi ba a kashe cikinsu ba face mutum hudu.[3]

[1]. Bukhari ne ya rawaito (2930).
[2]. Abu Ya'ala ne ya rawaito (3606), da Dabarani (2758).
[3]. Alfusul (207).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

KHABBABU ɗAN ARATTU (RA)

❖ Sunansa da haifuwarsa:

Shi ne Khabbabu ɗan Arratu ɗan Jandal Attamimi.

An haife shi a Najid a shekara ta 36 kafin hijira, kuma an kama shi (RA) yana ɗan ƙarami a matsayin fursunan yaƙi, sai ya koyi ƙera takuba da makamai har ya ƙware, sai ya shahara da haka a Makka.

❖ Tarihinsa da falalarsa:

Ya musulunta (RA) tun farkon musulunci, ya kasance shi ne na shidan mutane shida da suka fara musulunta, ya kasance yana daga cikin waɗanda ake azabtarwa saboda Allah Mai girma da ɗaukaka,[1] kuma ya kasance (RA) mai gaskiya, amintacce, ma'abocin hankali da hikima duk da ƙanƙantan shekarunsa.

Daga cikin labarinsa akwai: Cewa ya kasance yana tafiya wurin Sa'id ɗan Zaid da Faɗimatu 'yan Khaɗɗab don ya karanta musu Alƙur'ani, yayin da Umar ɗan Khaɗɗab ya ji labarin musuluntarsu – a lokaci bai musulunta ba – sai ya tafi wajensu a fusace, sai ya ƙwanƙwasa ƙofa da ƙarfi, ya kuma shiga wajensu, a lokacin akwai wata takarda da take ɗauke da suratu Ɗaha yana karanta ta gare su, sai Umar ya ce: Ku ba ni wannan takarda da take tare da ku, sai suka ƙi, suka ce sai ya yi wanka, sai jikinsa ya yi sanyi, sai ya yi wanka, sannan sai ya karanta takardar, yayin da Khabbab ya ji karatun Umar, sai ya ce da shi: Ina maka albishir, wallahi ni ina fatan Allah Ya keɓance ka da da'awar Annabinsa (SAW); saboda lallai ni na ji shi jiya yana cewa: (Ya Allah Ka ɗaukaka musulunci da wanda kafi

[1]. Hilyatul-Auliya (471).

son sa daga cikin mutane biyun nan masu suna Umar; Abu Jahal, ko kuma Umar ɗan Khaɗɗab).[1]

Khabbabu (RA) a ƙarshen rayuwarsa ya samu wadata bayan talauci, sai ya ba da dukiyarsa ga mabuƙata cikin talakawa da miskinai, sun kasance suna zuwa gidansa sai ya ba su abin da suke so, bai taɓa rufe ƙofarsa gare su ba, kuma bai saka mata makulli ba.

❖ Rasuwarsa:

Khabbabu (RA) ya rasu a garin Kufa, a shekara ta talatin da bakwai bayan hijira, a lokacin yana ɗan shekara saba'in da uku, sai Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (RA) ya sallace shi.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito (3681).

Auna fahimtarka a darusan mako na 35			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Daga cikin abin da za mu fahimta daga Suratuɗ-Ɗariƙ akwai:		A
	a. Kariyar Allah ga muminai	b. Falalar sallar dare	c. Falalar jure cutarwa daga musulmi.
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin abubuwan da ba za su shiga cikin girman kai ba akwai:		B
	a. Raina ƙanana	b. Kwalliya da tufafi.	c. Mayar da gaskiya.
Darasin Aƙida	Tambaya: Zato da wasu mutane suke yi cewa roƙon Allah karɓaɓɓe ne idan aka yi a wajen ƙaburbura:		B
	a. Kafirci ne mai girma.	b. Bidi'a ce mummuna.	c. Halal ne.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin abubuwan da suke nuni a kan girman matsayin zakka akwai cewa Allah Ya haɗa ta da salla a waje:		C
	a. 55	b. 79.	c. 82.
Darasin Sira	Tambaya: Komandan mushirkai a yaƙin Hunaini shi ne:		B
	a. Ka'ab ɗan Malik	b. Malik ɗan Auf.	c. Aufu ɗan Haris.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Khabbab (RA) ya shahara da ƙera:		A
	a. Takuba	b. Tufafi	c. Ƙofofi

MAKO NA TALATIN DA SHIDA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-BURUJ

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلۡبُرُوجِ ١ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡمَوۡعُودِ ٢ وَشَاهِدٖ وَمَشۡهُودٖ ٣ قُتِلَ أَصۡحَٰبُ ٱلۡأُخۡدُودِ ٤
ٱلنَّارِ ذَاتِ ٱلۡوَقُودِ ٥ إِذۡ هُمۡ عَلَيۡهَا قُعُودٞ ٦ وَهُمۡ عَلَىٰ مَا يَفۡعَلُونَ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ شُهُودٞ ٧ وَمَا نَقَمُواْ
مِنۡهُمۡ إِلَّآ أَن يُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ٨ ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ
شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٩ إِنَّ ٱلَّذِينَ فَتَنُواْ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ ثُمَّ لَمۡ يَتُوبُواْ فَلَهُمۡ عَذَابُ جَهَنَّمَ وَلَهُمۡ
عَذَابُ ٱلۡحَرِيقِ ١٠ إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَهُمۡ جَنَّٰتٞ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۚ ذَٰلِكَ
ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡكَبِيرُ ١١ إِنَّ بَطۡشَ رَبِّكَ لَشَدِيدٌ ١٢ إِنَّهُۥ هُوَ يُبۡدِئُ وَيُعِيدُ ١٣ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلۡوَدُودُ ١٤ ذُو
ٱلۡعَرۡشِ ٱلۡمَجِيدُ ١٥ فَعَّالٞ لِّمَا يُرِيدُ ١٦ هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ٱلۡجُنُودِ ١٧ فِرۡعَوۡنَ وَثَمُودَ ١٨ بَلِ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ فِي تَكۡذِيبٖ ١٩ وَٱللَّهُ مِن وَرَآئِهِم مُّحِيطُۢ ٢٠ بَلۡ هُوَ قُرۡءَانٞ مَّجِيدٞ ٢١ فِي لَوۡحٖ مَّحۡفُوظِۭ ٢٢﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai

1. Na rantse da sama ma’abociyar manziloli.
2. Da ranar da aka yi alƙawarin zuwanta.
3. Da mai shaida da kuma abin yi wa shaida.
4. An la’anci ma’abota rami (na azabtar da muminai).
5. Na wuta mai ruruwa.
6. Yayin da suke zaune a gefenta.
7. Alhali su suna kallon abin da suke aikata wa muminai.

8. Babu kuwa abin da suke tuhumar su da shi sai don kawai sun yi imani da Allah Mabuwayi, Sha-yabo.

9. Wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa. Allah kuma Mai ganin komai ne.

10. Lalle waɗanda suka azabtar da muminai maza da muminai mata sannan ba su tuba ba, to suna da azabar Jahannama, suna kuma da azabar ƙuna.

11. Lalle waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari suna da gidajen Aljanna waɗanda ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu. Wannan kuwa shi ne babban rabo.

12. Lalle damƙar Ubangijinka tabbas mai tsanani ce.

13. Lalle Shi ne Yake farar (da komai) Yake kuma dawo (da shi).

14. Shi ne kuma Mai gafara, Mai ƙaunar (bayinsa na ƙwarai).

15. Ma’abocin Al’arshi Mai girma.

16. Mai aikata abin da Yake nufi.

17. Shin labarin runduna ya zo maka?

18. (Su ne) Fir’auna da Samudawa.

19. A'a, su dai waɗanda suka kafirta suna cikin ƙaryatawa ne.

20. Allah kuwa Yana kewaye da su (da iliminsa).

21. A'a, shi dai Alƙur’ani ne mai girma.

22. A cikin Lauhul-Mahafuzu.

❖ Saƙon da surar ta ƙunsa:

Bayanin ƙarfin Allah Maɗaukakin Sarki, da cikakken iliminsa, da taimakonsa ga masoyansa, da damƙarsa ga magabtansa.

❖ Baƙin kalmomi:

ذات البروج	Zatil-buruj	Ma'abociyar masauƙai da rana da wata ke bi ta kansu.
واليوم الموعود	Walyaumul-mau'ud	Ita ce ranar alƙiyama
وشاهد ومشهود	Wa shahidun wa mash-hud	Rantsuwa ne da kowane mai shaida da zai ba da shaida, da kuma duk wanda za a ba da shaida a kansa.
شُهود	Shuhud	Halartattu
فتنوا	Fatanu	Suka ƙona su da wuta
الحريق	Alhariƙ	Mai ƙonawa
البطش	Baɗsh	Damƙa
قُتِل	Ƙutila	An la'ance su, an azabtar da su, kuma an halaka su.
أصحاب الأخدود	Ashabul-ukhdud	Waɗanda suka yi tono a ƙasa don ƙona muminai.
النارِ ذاتِ الوقود	Annari zatil-waƙud	Abin da ake ƙestawa kuma ake kunna wuta da shi
يُبدِئُ	Yubdi'u	Ya fari halittar halittu.
ويُعيد	Wa yu'id	Yake raya su bayan mutuwarsu
الوَدود	Alwadud	Masoyin masoyansa, Abin so a gare su
المَجيد	Almajid	Mai girma

❖ Ma'anar ayoyin a dunƙule:

Suratul-Buruj sura ce Makkiya, Ubangijinmu Mai girma da ɗaukaka ya buɗe ta da mafi girman rantsuwa, saboda ya yi rantsuwa da sama ma'abociyar masauƙai, wanda su ne masauƙan rana da wata guda goma sha biyu, ta yadda tafiyarsu ke tsaruwa a cikinsa a bisa

ƙayataccen tsari, sannan sai Allah Mai girma da ɗaukaka Ya yi rantsuwa da yini da aka yi alƙawarin zuwansa, wanda Allah Ya yi wa bayinsa alƙawari da cewa zai tattara su alƙawari da ba za a saɓa shi ba, sannan Ya yi rantsuwa da dukkan mai ba da shaida da duk wanda aka yi shaida a kansa a duniya da lahira; saboda bayyana cikakken ƙarfinsa da iliminsa mai faɗi, da kuma alƙawarin narko ga masu laifi, waɗanda suka azabtar da muminai, ta hanyar uƙuba da damƙa mai tsanani, duk wanda yake son ɗaukan izina, to ya yi duba zuwa ga abin da Allah Ya yi da Fir'auna, da Samudawa maɓarnata, amma waɗanda suka yi imani da Allah kuma suka masa biyayya ta hanyar sauke farillai da ya ɗaura musu, da barin abin da ya haramta musu, to suna da rabo mai girma a aljanna wacce take ɗauke da ƙoramu da benaye da lambuna.

❖ Abubuwan da za mu koya daga surar:

1. Tafiyar rana da wata a magudanansu a cikin ƙayataccen tsari wanda zai sa a yi tuntuntuni game da ikon Allah.

2. Tunatarwa game da amfani mai girma da ke samuwa cikin gudanar rana da wata, na ƙirgen watanni da zangogi, da shekarun halittu, da lokutan noma.

3. Daga cikin sabuban tsira akwai fifita kuɓutar imani a kan kuɓutar gangan jiki.

4. Tuba da ta cika sharuɗanta tana kankare zunubai, kuma tana rushe abin da ya gabace ta.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

KWAƊAITARWA A KAN KAMEWA

DA WADATAR ZUCI

An rawaito daga Abdullahi ɗan Amr (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Haƙiƙa ya rabauta, duk wanda ya musulunta, kuma aka azurta shi da daidai buƙatar shi, kuma Allah Ya wadatar da shi da abin da ya ba shi**).[1]

❖ Sharhi:

Annabi (SAW) ya yi albishir ga wanda ya haɗa waɗannan sifofi guda uku da rabauta, wacce ita ce rabauta da dukkan abin da ake nema kuma ake so, da kuɓuta daga kowane abin tsoro mai firgitarwa; saboda waɗannan sifofi suna tattare da alkhairai na addini da na duniya; domin shi bawa idan aka shiryar da shi zuwa ga Musulunci, addinin da Allah ba ya karɓar wani addini koma bayansa, kuma da shi ake rabauta da lada, kuma ake kuɓuta daga azaba, sannan ya samu arziki da zai ishe shi, wanda zai sa ya kame hannunsa daga roƙon halittu, sannan Allah Ya cika masa ni'imarsa ta hanyar wadatar da shi da abin da ya ba shi, sai ya yarda da abin da ke wajensa na arziki, kuma ransa bai kwaɗaitu zuwa ga abin da ke bayan haka; to haƙiƙa ya samu cikakkiyar rabauta da jin daɗin duniya da lahira.

❖ Abubuwan da za mu koya daga hadisin:

1. Lallai Jin daɗin mutum da rabautarsa suna cikin cikar addininsa, da arziki daidai buƙatarsa, da wadatuwarsa da abin da Allah Ya ba shi.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (1054).

2. Cewa lallai arziki da ake yabo shi ne wanda ake samun ƙarfin yin ibada da shi, kuma wanda ake shagala a kansa gwargwadon buƙata.

3. Falalar wadatar zuci, da kuma cewa lallai yana daga cikin sabuban rabauta.

TALATA: DARASIN AƘIDA

CETO:

Ceto: Shi ne shiga tsakani don wani, domin jawo masa alheri, ko kawar da wani sharri.

Kuma batun neman ceto yana daga cikin manyan shubuhohin mushrikai a da da kuma yanzu, a lokacin da suke kiran wanin Allah da kuma bauta musu. Sai su yi ikirarin cewa lallai su suna neman su yi musu ceto ne a wurin Allah, sai su riƙa cewa: Lallai Annabawa da salihai da mala'iku suna da babbar alfarma a wurin Allah, kuma suna da manyan matsayi, don haka muke kiran su domin su yi mana ceto a wurinsa.

Kuma Allah Maɗaukaki ya ambaci wannan shubuhar tasu a cikin fadinsa: ((Kuma suna bauta wa wani ba Allah ba, abinda ba zai cutar da su ba kuma ba zai amfane su ba, kuma suna cewa: "Waɗannan su ne masu cetonmu a wurin Allah". Ka ce: Shin yanzu za ku ba wa Allah labarin abin da bai sani ba ne a cikin sammai ko kuma a bayan ƙasa? Tsarki ya tabbata gare shi, kuma Ya ɗaukaka daga abin da suke shirka da shi)).[1]

❋ **Martani ga wannan batacciyar shubuhar tana kasancewa ta bangarori guda biyu:**

Na farko: Lallai Allah Maɗaukaki Ya bayyana cewa lallai ceto mallakar Allah ne Shi kaɗai, Yana bayar da izini ga wanda Ya so, kuma Yana hana shi idan Ya so, kuma ba a neman sa sai daga gare Shi. Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ka ce: Ceto gaba ɗaya na Allah ne,

[1] [Yunus 18]

mulkin sammai da ƙasa na shi ne kaɗai, sannan kuma wurinsa ne kaɗai za a komar da ku))[1].

Na biyu: Lallai Mahalicci ba kamar abin halitta ba ne, kuma ba ya halatta a kwatanta Allah Mawadaci, Mai girma, Mai tsinkayar komai, kuma Makusanci, da sarakuna da shugabanni masu buƙatar ministoci da masu taimako waɗanda suke kammala mulkinsu, kuma suke sanar da su halin da talakawansu ke ciki, kuma suke buƙatar tsani da mai shiga tsakani daga cikin manya da ƙusoshi domin su isa gare su da kuma tambayarsu.

Kuma lallai Allah Maɗaukakin sarki babu abin da zai ɓuya gare Shi, kuma ya wadatu daga dukkan wani abu koma bayansa, kuma shi ne mafi jinƙai ga bayinsa fiye da jinƙan uwa ga ɗanta.

❖ **Saboda haka ne ceto a cikin Alƙur'ani da Hadisi ya kasu kashi biyu:**

Kashi na farko: Ceto wanda aka tabbatar: Shi ne wanda ake nema daga Allah, domin Ya bayar da shi ga mai ceto da wanda ake masa ceto, kuma ba a neman shi daga wurin abin halitta; domin shi mallakar Allah ne Shi kaɗai, kuma wannan tabbataccen ceto yana da sharuɗɗa guda biyu:

❖ Sharaɗi na farko: Izinin Allah ga mai ceto don ya yi ceto; saboda fadin Allah Maɗaukaki: ((Wane ne ya isa ya yi ceto a wurinsa in ba da izininsa ba?))[2].

❖ Sharadi na biyu: Yardar Allah ga mai ceto da kuma wanda za a masa ceto; saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma ba za su yi ceto ba sai ga wanda Ya yarda daga bayinsa))[3].

[1] [Az-Zumar 44].
[2] [Al-Baƙara 255].
[3] [Al-Anbiya'i :28].

Da kuma faɗinsa: ((A wannan ranar ceto ba ya amfani sai ga wanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa izini, kuma Ya yarda da maganarsa))[1]. **Kashi na biyu:** ceto da aka kore shi: Shi ne wanda mushrikai suke nema daga wanin Allah; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Saboda haka ceton masu ceto ba zai amfane su ba))[2].

Domin lallai Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da Annabawan da suka zo gabaninsa ba su shar'anta cewa mutane su nemi ceto daga mala'iku, ko daga Annabawa, ko daga salihai ba. Kuma babu wanda ya aikata haka daga cikin sahabbai ko tabi'ai, kuma babu wanda ya halatta hakan daga cikin manyan malamai guda huɗu, ko wasu daga cikin malaman musulmi.

[1] [Ṭaha :109].
[2] [Al-Muddassir 48].

LARABA: DARASI CIKI FIƘIHU

ZAKKAR KUƊAƊEN TAKARDA

Mutane a da sun kasance suna mu'amala da zinariya da azurfa, suna sayen kaya da su, kuma suna auna farashin abubuwa da su. A wannan zamani kuwa, wancan mu'amalar ta gushe; inda aka maye gurbinsu da kuɗaɗen takarda; kamar Riyal da Dirham da Dinar, da Dala, sai kuɗaɗen takarda suka zama kuɗaɗe masu zaman kansu, saboda yarjejeniyar mutane a kansu a wannan zamani.

❖ Hukuncin Zakkar Kuɗaɗen Takarda:

Zakka ta wajaba a cikin kuɗaɗen takarda idan sun kai nisabi, kuma shekara ta zagayo musu; saboda fadin Allah Maɗaukaki: **(**Ka karɓi sadaka daga dukiyoyinsu da za ka tsarkake su kuma ka gyara musu halaye da ita, ka kuma yi musu addu'a. Lalle addu'arka nutsuwa ce a gare su. Allah kuwa Mai ji ne, Masani)[1].

❖ Nisabin Kuɗaɗen Takarda:

Nisabi shi ne iyakan da idan dukiya ta kai shi, to zakka ta wajaba a cikinta, kuma ba ta wajaba idan bai kai ba. kuma nisabin kuɗaɗen takarda shi ne nisabin zinariya da azurfa, ana auna shi su su. Kuma abin da aka sani shi ne nisabin azurfa koyaushe shi ne gram (595), don haka sai mu duba ƙimarsa da abin da yake daidai da shi a Riyal a ƙarshen shekara.

Mu ɗauka cewa farashin gram ɗaya a yau misali ya kasance Riyal uku (3), sai mu ninka nisabin azurfa (595) da farashin gram a wannan ranar, abin da ya fito shi ne nisabin kuɗaɗen takarda.

[1] [At-Tauba 103].

(595 × 3 = raiyal 1785) Wannan shi ne nisabi, kuma shi ne mafi ƙarancin dukiya da zakka ta wajaba a cikinta.

❖ **Nawa ne ya wajaba a fitar a zakkar kuɗaɗen takarda?**
Zakkar kuɗaɗen takarda kamar zakkar zinariya da azurfa ce, ana wajabta kashi ɗaya bisa arba'in (2.5 %) a kansu.

Kuma hanyoyin lissafa hakan suna da yawa, mafi sauƙi shi ne: a raba jimillar kuɗin gaba ɗaya gida arba'in, abin da zai fito shi ne rubu'in kaso ɗaya cikin goma (2.5%).

Misali: Idan dukiyar da aka mallaka ta kai riyal (40,000): (40,000 ÷ 40 = riyal 1,000) wannan shi ne abin da ya wajaba a fitar domin talakawa da makamantansu.

❖ **Yadda ake zakkar albashin wata-wata da ake ajiye:**
Ma'aikacin da yake karɓar albashi a kowane wata, kuma yana adana wani kaso daga cikinsa, yana da hanyoyi biyu na zakkar abin da ya adana:

- **Hanya ta farko:** Ya fitar da zakkar dukkan kaɗaɗen a ƙarshen shekara. Ta haka zai kasance ya fitar da zakkar abin da shekara ta zagayo masa, kuma ya gaggauta zakkar abin da bai kai shekara ba; domin yana halatta a gaggauta zakka kafin cikar shekara.
- **Hanya ta biyu:** Ya rika fitar da zakkar kowane wata dabam-dabam, bisa la'akari da da kowane kuɗi ya fara shigowa, sannan ya fitar da zakkarsa bayan ya cika shekara. Amma hanya ta farko ita ce mafi sauƙi, kuma mafi taƙaita wahala ga mutum.

ALHAMIS: DARASIN SIRA

YAƘIN ƊA'IF

❖ Lokacin faruwarsa:

Yaƙin Ɗa'if ya faru a cikin watan Shawwal, shekara ta takwas bayan hijira.

❖ Dalilan faruwarsa:

Shan kashi da gudun Malik bn ʻAwf an-Naṣrī sarkin Hawāzin, sannan shigarsa tare da kabilar Thaqīf cikin ƙasurgumin garin Ṭā'if.

❖ Abubuwan da suka faru:

Manzon Allah (SAW) ya tashi daga Hunain zuwa Ɗā'if, sai ya yi musu ƙawanya da runduna har tsawon kwana ashirin, yana harba musu makamin manjaniƙ, kuma ya lalata bayyanannen dukiyarsu mai yawa, ya sare gonakin inabinsu, sannan ya juya daga gare su, ya nufi Jiʻrana. A can ne tawagar Hawazin suka zo masa a matsayin Musulmi, sai ya mayar musu da ʻyaʻyansu, waɗanda suka kai dubu shida, a cikinsu akwai Shaima'u ʻyar Haris ɗan Abdul'uzza, ʻyar'uwar Manzon Allah (SAW) ta shayarwa, sai ya girmamata kuma ya tausaya mata har ta koma garinta.

Ya sanya Malik ɗan Auf Annasri ya zama shugaba ga waɗanda suka musulunta daga cikin mutanensa, kuma lallai ya musulunta, kuma musuluncinsa ya yi kyau, ya kuma yi wa Manzon Allah (SAW) waƙar yabo sananniya[1].

[1] Alfusul (209).

❖ Sakamakon Yaƙin:

Manzon Allah (SAW) ya fara raba manyan ganimomin da suka samu a yaƙin Hunain, kuma ya ga dacewar wannan karon a ba su ga waɗanda ake ƙoƙarin lallashin zukatansu, wato shugabannin Ƙuraishawa sabin musulunta; kamar Abu Sufyan da Uyaina da Aqra', da Suhail ɗan Amr. Sai ya rarraba musu, wasu raƙumi ɗari, wasu raƙuma hamsin, har ya ba wa Safwana dan Umayya rakuma ɗari uku, bai ba wa wani ba'ansarawae komai ba, saboda sa kankancewarsa da abin da Allah ya kawata na imani a cikin zukatansu, kamar dai sun ji wani damuwa a cikin zukatansu, kuma ba su fahimci hikimar da aka nufa cikin hakan ba, As'ad ɗan Ubada bai iya mallakar ransa ba, har saí da ya zo wajen Manzon Allah (SAW) ya ba shi labarin abin da ke kaikawo a tunanin mutane, sai Manzon Allah (SAW) ya tara ansarawaawa su kaɗai, kuma ya yi musu huɗuba, yake cewa: (Ya ku taron ansarawa ! Ashe ban same ku batattu ba sai Allah ya shiryar da ku ta dalili na?, kuma kun kasance a warwatse, sai Allah ya haɗa zukatanku a dalilina, kuma kun kasance talakawa, sai Allah ya wadatar da ku ta dalilina, duk abin da ya fada sai su ce: "Allah da manzonsa su ne mafi falala", sa'an nan ya ce, shin ba za ku yarda mutane su tafi da tumaki da raƙuma, ku kuma ku tafi da Manzon Allah (SAW) zuwa gidajenku ba, na rantse da wanda rayuwar Muhammadu ke hannunsa, ba don hijira ba da na kasance mutumin Madina, da mutane za su bi wata hanya da na bi hanyar ansarawa, su ansarawa kamar rigata ta ciki mai manne da fata ta ne, su kuma sauran mutane kamar rigata ta sama ne, ya Allah ka yi rahama ga ansarawa da 'ya'yan ansarawa da jikokin ansarawa). Sai ansarawa suka yi kuka har sai da hawaye ya

jika gemukansu, kuma suka ce mun yarda da Manzon Allah ya zama kasonmu kuma rabonmu[1].

Sai Manzon Allah ya yi haramar Umra daga Alji'rana ya shiga Makka, lokacin da ya gama Umrarsa sai ya koma Madina, ya shugabantar da Attab ɗan Ased a aikin Hajji wannan shekara, kuma shi ne farkon wanda ya jagoranci aikin hajji a cikin shugabannin musulmai[2].

[1] Bukhari (4330) Ahmad (11730) ne suka rawiato shi.
[2]. Alfusul (209).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

KHUBAIB ƊAN ADIYYU (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa

Shi ne Khubaib ɗan Adiyyu ɗan Malik Al'ausiyyu Al'ansiyyu.

An haife shi a Madina kafin aiko Annabi

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Ya kasance - Allah ya ƙara masa yarda- mayaƙi ne ƙwararre, sananne ne a wajen ƙarfi da jarumta, ya halarci yaƙin Uhudu, kuma shi ne farkon wanda aka tsire don kariya ga addinin Allah, lokacin da ya yi tarayya cikin waɗanda aka tura Arraji', wanda manzon Allah (SAW) ya tura shi zuwa ƙabilu biyu na Adal da Ƙarah, lokacin da suka nemi Manzon Allah (SAW) da ya aiko musu wanda zai koya musu Alƙur'ani da shari'ar Musulunci, sai ya tura su sai suka yaudare su, suka kashe mafi yawansu, Khubaib ya faɗa hannu a matsayin fursuna, sai suka sayar da shi ga mushirikan Makkah, sai Abu Sirwa'ata Uƙbata ɗan Haris ya karɓe shi domin yakashe shi a makwafin mahaifinsa da aka kashe a badar, sai ya tafi da shi zuwa tan'eem, sai Khubaib ya ce ku bani dama in yi Salla raka'a biyu, sai suka bar shi, sai ya sallace su, sannan ya ce: "Wallahi ba don kar ku ce ina da rauni ba da na ƙara wasu raka'o'in, sa'an nan ya yi waƙe yana cewa:

Ban damu ba yayin da za a kashe ni ina musulmi a kowane ɓangare mutuwata ta kasance, Kuma hakan a kan addinin Allah, idan ya so sai ya yi albarka a kan kowace gaɓa tawa da za a yayyanke[1].

[1] Bukhari (7402).

Rasuwarsa:

Ya yi shahada (RA) ta hanyar rataya a garin Makka shekara ta huɗu bayan hijira, kuma Amru ɗan Umayya ya ɗauke shi a ɓoye cikin dare ya tafi da shi ya binne shi.

Auna fahimtarka a darusan mako na 36			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: menene ma'anar "Al-Buruj"?**		**B**
	a. Fadì mai girma.	b. Hanyoyin da rana da wata ke wucewa ta cikinsu.	c. giragizai masu kauri.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Abin yabo daga cikin arziki shi ne:**		**A**
	a. wanda aka samu ƙarfin bautar Allah da shi, kuma aka shagaltu da shi gwargwadon buƙata.	b. abin da ya ishi na baya bayan mutuwar mai gida.	c. wanda mutum yake samun sa cikin wahala da tsanani.
Darasin Aƙida	**Tambaya: ceto na karkasuwa a cikin Alƙura'ni da Sunna zuwa:**		**C**
	a. gamammen ceto da keɓantaccen ceto.	b. Ceto a duniya da ceto lahira	c. Ceto tabbatacce da korarre.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Abin da ke wagibi a cikin zakkar kuɗin takarda shi ne:**		**A**
	a. 2.5%.	b. 5%.	c. 10%.
Darasin Sira	**Tambaya: YaƘin Da'if ya faru a shekara ta:**		**B**
	a. 7 bayan hijira	b. 8 bayan hijira	c. 9 bayan hijira.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin matsayin Khubaib Allah ya ƙara masa yarda, akwai kasancewarsa:**		**C**
	a. Farkon wanda ya yi hijira zuwa Madina.	b. Farkon jagoran runduna a Musulunci.	c. Farkon wanda aka gicciye a musulunci.

MAKO NA TALATIN DA BAKWAI

ASABAR: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUL-INSHIƘAƘ (1)

﴿إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنشَقَّتۡ ١ وَأَذِنَتۡ لِرَبِّهَا وَحُقَّتۡ ٢ وَإِذَا ٱلۡأَرۡضُ مُدَّتۡ ٣ وَأَلۡقَتۡ مَا فِيهَا
وَتَخَلَّتۡ ٤ وَأَذِنَتۡ لِرَبِّهَا وَحُقَّتۡ ٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡإِنسَٰنُ إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَىٰ رَبِّكَ كَدۡحٗا فَمُلَٰقِيهِ ٦
فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ ٧ فَسَوۡفَ يُحَاسَبُ حِسَابٗا يَسِيرٗا ٨ وَيَنقَلِبُ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِۦ
مَسۡرُورٗا ٩ وَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ وَرَآءَ ظَهۡرِهِۦ ١٠ فَسَوۡفَ يَدۡعُواْ ثُبُورٗا ١١ وَيَصۡلَىٰ سَعِيرًا ١٢
إِنَّهُۥ كَانَ فِيٓ أَهۡلِهِۦ مَسۡرُورًا ١٣ إِنَّهُۥ ظَنَّ أَن لَّن يَحُورَ ١٤ بَلَىٰٓۚ إِنَّ رَبَّهُۥ كَانَ بِهِۦ بَصِيرًا ١٥﴾

❖ Fassara:

1. Idan sama ta tsattsage.

2. Ta kuma saurari Ubangijinta, kuma ya wajaba (ta saurara).

3. Kuma idan ƙasa aka miƙe ta.

4. Ta kuma jefar da abin da yake cikinta ta wofinta.

5. Ta kuma saurari Ubangijinta kuma ya wajaba (ta saurara).

6. Ya kai mutum, lallai kai mai yin aiki ne tuƙuru zuwa ga Ubangijinka, to mai haɗuwa da Shi ne.

7. To amma duk wanda aka bai wa littafinsa a hannunsa na dama.

8. To za a yi masa hisabi mai sauƙi.

9. Ya kuma juyo zuwa ga iyalinsa yana farin ciki.

10. Amma wanda kuwa aka bai wa littafinsa ta bayan bayansa.

11. To zai yi kiran halaka.

12. Zai kuma shiga (wutar) Sa’ira.

13. Lallai a da shi ya kasance mai farin ciki ne cikin iyalinsa.

14. Lallai ya yi zaton ba zai koma (ga Allah) ba.

15. Haka yake, (zai koma), lallai Ubangijinsa Ya kasance Mai ganin sa ne.

❖ Sakon da Surar ta Ƙunsa:

Tunatar da mutum game da rauninshi, da yadda halaye suke jujjuyawa da shi, sa'an nan komawarshi ga Ubangijinshi.

❖ Bakin kalmomi:

انشقت	**Inshakkat**	Ta kece, ta yage da giragizai.
أذنت لربها	**Azinat lirabbiha**	Ta yi wa Ubangijinta biyayya.
وحقت	**Wa hukkat**	Kuma aka wajabta mata ta yi biyayya.
مدت	**Muddat**	Aka shimfida ta, kuma aka yalwata ta, kuma aka nike duwatsunta.
ألقت	**Wa alkat**	ta watsar da abin da yake cikin cikinta.
كادح إلى ربك	**Kadihun ila rabbika**	mai tafiya ne zuwa ga Allah, kuma mai aiki ne da alhairi ko sharri.
كتابه	**Kitabahu**	ai takardun ayyukanshi.
وينقلب	**Wa yankalibu**	Kuma ya koma
يدعو ثبورا	**Yad’u subura**	Yana kiran halaka ga rayuwarshi
لن يحور	**Lan yahur**	Ba zai koma ga Allah ya yi masa hisabi ba.

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

A cikin waɗannan ãyoyi Allah yana bayyana abin da zai kasance a alƙiyama na daga canzawar abubuwa masu girma, sama za ta yage kuma ta tsage, kuma ƙasa za ta daidaita, kuma a niƙe abubuwan dake kanta na gine-gine da abubuwa masu tsayi, kuma a jefar da abin da ke cikinta na daga matattu da taskoki, kuma a shinfiɗa ta irin shinfiɗawar fata, sai ta yalwata ga dukkan mutanen da ke madakata, dukkan wannan domin biyayya ne ga Allah maɗaukaki, da miƙa wuya gare shi, kuma an wajabta musu su ji kuma suyi ɗa'a, domin lallai su horarru ne masu jujjuyawa ne gare shi, tsarki ya tabbata gare shi

Sannan nan ya fuskantar da maganar zuwa ga mutum don tunatar da shi lallai shi mai tafiya ne mai gaggawa zuwa ga Allah, mai aiki ne a cikin tafiyar ko na alheri ko sharri, zai tarar da ayyukanshi, kuma za a saka mishi a kansu.

Idan aka ba shi takardun ayyukan shi da damanshi; to ya samu tsira, kuma sakamakon shi zai kasance mai sauƙi, za'a bijiro masa da ayyukansa a gare shi ba tare da tattaunawa da tsanani ba, saɓanin kafiri wanda za a ba shi littafinsa ne da hagunsa ta bayansa, sai ya yi ihu yana cewa kaicona, kuma yana kiran halaka wa kansa.

❖ Abubuwan da za mu koya daga Ayoyin:

1) Risinawar sama da ƙasa ga Ubangijinsu, da ciratuwa zuwa gare shi.

2) Lallai kowane mutum mai tafiya ne mai komawa ne, ko dai ga alheri ko ga sharri.

2) Lallai ma'abota imani da tsoron Allah za a yi musu hisabi mai sauƙi, shi kawai bijiro da ayyuka ne, ba tare da an tattauna a kansu ba.

4) Lallai duk wanda aka bibiye shi a hisabi haƙiƙa ya halaka; domin shi baya iya mallakar wata hujja ko uzuri.

5) Lallai alamar rabauta a ƙiyama ita ce karɓar littafi da dama, kuma alamar taɓewa ita ce karɓansa da hagu.

6) lallai sakaci a duniya da afkawa sha’awace-sha’awacenta sakamako ne na rashin yaƙini game da tashi bayan mutuwa da kuma hisabi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI: KWAƊAITARWA A KAN TAUSAYIN MUTANE

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi ya ce: manzon Allah (SAW) ya ce: (**Duk wanda ba ya tausayin mutane, to shi ma Allah ba zai tausaya masa ba**). Bukhari da Muslmin ne suka rawaito shi[1].

❖ Sharhi

Hadisin yana nuni da lafazinsa a kan cewa lallai duk wanda ba ya tausayin mutane, to Allah ba zai tausaya masa ba. Kuma abin da za a iya fahimta daga hadisin kuma shi ne cewa duk wanda yake tausayin mutane, to shima Allah zai tausaya masa; tausayin bawa ga halittu yana daga cikin mafi girman sababban da suke sanya Shi ma Allah ya tausaya masa, kuma rasa shi yana daga mafi girma masu yankewa daga rahamar Allah, kuma masu hana samun rahamarsa, kuma bawa yana cikin matuƙar buƙatar rahamar Allah, domin lallai shi ba zai samu wani alheri ba a duniyarsa da lahirarsa sai da ita, saboda haka, idan yana so a ƙara masa wannan rahamar, to sai ya zo da sababban ta, kuma daga cikinsu akwai tausayin bayi da kyautatawa gare su, kamar yadda ya zo a cikin faɗin Allah maɗukaki: ((lallai rahamar Allah kusa take da masu kyautatawa))[2]. Kuma su ne masu kyautatawa a cikin bautar Allah, kuma masu kyautatawa zuwa ga bayin Allah.

Kuma tausayin da bawa yake siffantuwa da shi nau'i biyu ne:

1. Tausayi na ɗabi'a, haƙiƙa Allah ya ɗaura zukatan wasu bayin a kanta.
2. Tausayin da ake samarwa kai, bawa yana samun shi ne ta hanyar ƙoƙari, da tunanin ladan da zai samu a wurin Allah.

---

[1] Bukhari (6013) Muslim (2319) ne suka rawaito shi.
[2] l A'raf (56).

❖ Abubuwan da za mu koya daga Hadisin:

1. Lallai tausayi ɗabi'a ce mai girma wanda Musulunci ya kwaɗaitar a kan ƙarfafa shi a zuciyar musulmi.

2. Lallai tausayin juna tsakanin mutane sababi ne na samun rahamar Allah a gare su.

3. Tabbatar da siffar rahama ga Allah maɗaukaki.

4. Lallai sakamako yana kasancewa ne daga jinsin aiki.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA:

TAWASSALI

Tawassuli: Shi ne neman kusanci zuwa ga wani abu da kuma isa zuwa gare shi, kuma abin da ake nufi da Kalmar “Wasila”: Shi ne kusanci; Allah maɗaukaki ya ce: ((kuma ku nemi abin da zai sada ku da shi))[1], ma’ana: kusanci zuwa gare shi – tsarki ya tabbata a gare Shi – ta hanyar yi masa biyayya da bin yardar sa.

Saboda haka, lallai abin da yake wajibi ga mumini shi ne ya kwaɗaitu wurin aikata abin da zai kusantar da shi ga Allah maɗaukaki da yardarsa da karɓar addu’arsa, kuma ya bi kowace hanya da tsani don samun hakan, sai dai yana da muhimmanci wannan hanyar ta zamo ingantacciya kuma wacce shari’a ta yarda da ita, kuma wadda Allah ya yi umarni da ita, idan bata kasance haka ba to ta kasance haramtacciya wacce take kaiwa ga fushin Allah ba ga yardarsa ba.

❖ Rabe-Raben Tawassuli:

Daga abin da ya gabata, tawassali ya kasu kashi biyu:

Tawassali wanda shari’a ta yarda da shi, da tawassali wanda aka hana, kuma kowannensu yana da nau'ukansa.

❋ Tawassali wanda shari’a ta yarda da shi, daga cikin nau’ukansa akwai:

1) Neman kusanci zuwa ga Allah ta hanyar sunayensa da siffofinsa, sai bawa ya roƙe shi da su kuma ya ƙanƙantar da kai zuwa gare Shi, kamar yadda Allah ya yi umarni a cikin faɗinsa: ((Allah kuma Yana da sunaye mafiya kyau, don haka ku roƙe Shi da su; kuma ku rabu

[1] [Al-Ma’ida: 35].

da waɗanda suke fanɗarewa game da sunayensa; da sannu za a yi musu sakamakon abin da suka kasance suna aikatawa))[1].

2) Neman kusanci zuwa ga Allah ta hanyar yin imani da aiki na gari; kamar yadda Allah ya faɗa game da ma'abota Imani: ((Ya Ubangijinmu, lallai mu mun ji wani mai kira yanayin kira zuwa imani cewa: “Ku yi imani da Ubangijinku;” sai mukayi imani. Ya Ubangijinmu, Ka gafarta mana zunubanmu, kuma Ka kankare mana kurakuranmu, kuma Ka karɓi rayukanmu tare da mutane masu ɗa’a))[2]

Kuma kamar yadda ya zo a cikin hadisin mutane ukun da wani ƙaton dutse ya haye kansu ya rufe musu kofar kogon, sai suka yi tawassali gare shi da kyawawan ayyukansu, sai Allah ya yaye musu[3].

3) Neman kusanci zuwa ga Allah ta hanyar kaɗaita shi; kamar yadda Annabi Yunus amincin Allah ya tabbata a gare shi ya yi tawassali ((sai ya kira (Mu) a cikin duffai yana cewa: “Ba wani abin bauta da gaskiya sai Kai (ya Allah), tsarki ya tabbata a gare Ka!))[4].

4) Neman kusanci zuwa ga Allah ta hanyar tabbatar da laifi; kamar yadda Annabi Musa ya yi tawassali zuwa ga Allah: ((Ya ce: "Ya Ubangijĩna! Lallai na zãlunci kaina, saboda haka, ka gafarta min”))[5].

5) Neman kusanci zuwa ga Allah ta hanyar nuna rauni da buƙatuwa zuwa gare Shi Maɗaukaki; kamar yadda Annabi Ayyub ya yi tawassali zuwa ga Allah ((“Lallai cuta ta same ni, Kai ne kuwa Mafi jin ƙan masu jin ƙai!”))[6]

---

1. [A’raf: 180].
2. [Alu-Imran:193].
3. Bukhari (2272) da Muslim (2743) ne suka rawaito shi
4. [Al-Anbiya: 87].
5. [Al-Ƙasas (16].
6 [Al-Anbiya: 83].

5) Neman kusanci zuwa ga Allah ta hanyar neman addu'ar nagartattun bayi rayayyu; Kamar yadda Sahabbai suka kasance suna yi a yayin da suka rasa ruwan sama sai su nema daga Manzon Allah (SAW) ya roƙa musu ruwa, yayin da kuma ya rasu sai suka koma wurin baffansa Abbas sai ya roƙa musu.

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

WAƊANDA AKE BA WA ZAKKA

Waɗanda ake ba wa Zakka su ne waɗanda suka cancance ta, waɗanda ake ba su zakka, kuma bai halatta a ba wa wasunsu ba, kuma su ne nau'ukan mutane takwas waɗanda Allah ya ƙididdige su a faɗinsa: ((Dukiyoyin Zakka na matalauta ne kaɗai da miskinai da ma'aikatanta da waɗanda ake lallashin zukatansu da kuma game da 'yanta bayi da waɗanda ake bi bashi da kuma wajen jihadi saboda Allah da matafiyi. Farilla ce daga Allah. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima))[1].

Saboda haka ba ya halasta a ba da Zakka ga wasu da ba waɗannan ba, da wasun haka na ayyukan alheri, kamar gina masallatai da haƙa rijiyoyi.

Kuma waɗannan ɓangarori su ne kamar haka:

1) **Matalauta**: Su ne waɗanda ba sa samun wani abu na abinci, ko abin sha, ko tufafi, ko wurin zama, ko kuma suna samun abin da ba zai ishe su ba.

2) **Miskinai**: Su ne waɗanda suke samun kaso mafi yawa na abin da zai ishe su ko rabinsa, ba wanda zai ishe su ba, kamar wanda yake da dubu ɗaya kuma yana buƙatar dubu biyu, da makamancin haka, kuma ana bawa faƙirai da miskinai abin da zai ishe su na tsawon shekara.

3) **Masu aikin zakka**: Su ne waɗanda shugaba ya ɗaura su kuma yake aika su domin tattaro zakka, ko rubuta ta, ko rarraba ta ga waɗanda suka cancanceta, sai shugaba ya ba su haƙƙinsu daga Zakka, kuma wanda abokinsa ko makusancinsa ya ba shi zakkarsa

[1] [At-Tauba: 60].

domin ya raba ta ba zai shiga cikin wannan ba, domin shi ba ya daga cikin masu aiki a kanta, shidai kawai wakili ne.

4) **Waɗanda ake rarrashin zukatansu**: Su ne mutanen da shugaba yake ba su Zakka domin su kame daga cutar da mutane, Ko kuma don lallashi zukatansu in sun kasance kafirai ne, kuma don tabbatarwa da ƙarfafa imaninsu insun kasance musulmai ne masu raunin imani.

5) '**Yanta Bayi:** Abin da ake nufi a nan shi ne mallakekken bawa musulmi: ana siyan shi da dukiyar Zakka a 'yanta shi, domin ya zama ɗa, kuma musulmi wanda aka kama a wurin maƙiya ana karbo shi da dukiyar Zakka.

6) **Waɗanda ake bi bashi**: Abin da ake nufi shi ne wanda ya ɗauki bashi wanda ba a kan saɓon Allah ba, to wannan ana bashi daga Zakka domin ya biya bashinsa, haka nan wanda ya ɗau bashi don ya gyara tsakanin mutane biyu, wanda yake sulhunta tsakanin mutane, da kashe wutar ƙiyayya, za'a bashi daga Zakka ko da ya kasance mai kuɗine.

7) **Masu yaki bisa tafarkin Allah**: Su ne mayaƙa a tafarkin Allah waɗanda ba su da albashi a cikin baitil-mali, to, waɗannan ana biyan su daga dukiyar Zakka.

8) **Matafiyi**: Shi ne wanda ya bar garinsa, kuma yake buƙatar kuɗi, saboda ƙarewar abin da yake tare da shi ko ya ɓata, to wannan ana ba shi abin da zai isar da shi garinsa.

Hukuncin ba da Zakka ga Makusanta:

Mustahabbi ne mutum ya ba da Zakka ga 'yan uwansa makusanta mabuƙata, waɗanda ciyar da su baya kanshi, gwargwadon kusancinsu, domin faɗin manzon Allah (SAW): (Sadakarka ga

miskini sadaka ce kawai, amma ita ga dangi abu biyu ce: sadaka da kuma sada zumunta)[1].

Kuma baya halatta mutum ya ba da ita ga makusantan da wajibinsa ne ya ciyar da su; kamar ubanni, da uwaye, da mata, ka kanne maza, da ka kanne mata, da ‘ya’ya, da ‘ya’yan ‘ya’ya da makamancin haka.

[1] Abu Dawuda (2839), Tirmizi (658).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

YAƘIN TABUKA

❖ Lokacin aukuwarsa:

Ya faru a watan Rajab, a shekara ta tara bayan hijira

❖ Sababin aukuwarsa:

Ya yin da Allah ya saukar da: ((Ku yaƙi waɗanda ba sa yin imani da Allah da lahira, ba kuma sa haramta abin da Allah da Manzonsa suka haramta, kuma ba sa yin addini na gaskiya, daga waɗanda aka bai wa littafi har sai (sun yarda) za su ba da jizya da hannunsu alhali suna ƙasƙance))[1].

Sai Manzon Allah (SAW) ya yi yekuwa ga mutanen Madina da kewayanta daga larabawan ƙauye zuwa ga jahadi, kuma ya sanar da su yaƙar Rumawa.

❖ Abubuwan da suka faru a cikinsa:

Manzon Allah (SAW) ya kasance babu yaƙi da zai yi nufin shi face sai ya boye shi da wani batu, banda wannan yaƙin nashi, lallai shi ya ba su labarinsa, kuma ya yi musu umarni da su yi masa shiri, domin tsananin makiyansu da yawansu, da nisan hanya da wahalarta, kuma da kasancewar ta dace da lokacin zafi, kuma da kasancewarta shekara ce ta fari, saboda haka ne aka kira wannan rundunar da suna "Jaishul Usra" (wato rundunar tsanani), sai musulmi suka yi shiri domin hakan, kuma Usman ɗan Affan ya bayar da dukiya mai yawa saboda wannan yaki, har sai da Annabi

[1] [At-Tauba: 29].

(SAW) ya ce:(Babu abin da zai cutar da Usman bayan wannan rana)[1].

Sai Annabi (SAW) ya tashi tare da kimanin mutane dubu uku sai ya bar ragamar kula da Madina a hannun Muhammad ɗan Maslama, sai Abdullahi ɗan Ubayyu tushen munafurci ya ƙi fita don kafirci da taurin kai, kuma munafukai dayawa suka zauna tare da shi, yawansu ya kai kusan mutum tamanin (80), kuma wasu musulmai suma suka saɓa ba su je ba, daga cikin su akwai, Murarata ɗan Rabi'a, da Ka'abu ɗan Malik, da Hilalu ɗan Umaiyya, sannan Allah ya yafe musu bayan dawowar Manzon Allah (SAW) da darare hamsin, kuma Allah ya yi uzuri ga wanda bai samu abin hawa, ko kuma guzurin da zai ishe shi ba, su ne masu kukan nan waɗanda Allah Ya yi magana a kan su a inda Yake cewa: ((Haka kuma babu (laifi) a kan waɗanda idan sun zo maka don ka ba su abin hawa sai ka ce: “Ba ni da abin hawan da zan ba ku,” sai suka juya idanuwansu suna kwararar da hawaye don baƙin cikin ba su sami abin da za su ciyar ba))[2].

Kuma Annabi (SAW) ya wuce ta gidajen samudawa a kan hanyarshi, sai ya umurci sahabbai da kada su shiga gidajen face suna masu kuka[3], kuma kada su sha daga rijiyoyinsu, sai dai rijiyar taguwa, kuma abin da suka kasance sun kwaɓa wannan ruwan da shi to su ciyar da shi raƙuma[4], kuma yayin da suka iso Tabuka sai suka samu wani marmaron ruwa yana fitar da ɗan ruwa kaɗan, sai ruwansa ya yawaita don albarkar Annabi (SAW) tare da abin da aka gani a wannan yaƙi na yawaitar abinci domin albarkar addu'arsa (SAW) har duka suka ci daga gare shi, kuma suka cika dukkan wani

[1] Tirmizi ne ya rawaito shi (3701).
[2] [At-Tauba: 92].
[3] Bukhari (433) da Muslim (2980) ne suka rawaito shi.
[4] Muslim ne ya rawaito shi (2981).

mazubin dake tare da wannan runduna[1], kuma haka nan lokacin da suka ji ƙishi sai ya roƙi Allah, sai wani girgije ya zo sai ya yi ruwa, sai suka sha har suka ƙoshi, sannan wannan girgijen bai wuce wannan rundunar ba[2].

❖ Sakamakon Yaƙin:

Yayin da Annabi (SAW) ya isa wurin, sai ya yi sulhu da Yuhanna ɗan Ru'ba na garin Aila, kuma ya aika Khalid zuwa ga Ukaidir na garin Duma shima ya yi sulhu da shi, kuma ya mayar da shi, kuma bai haɗu da wani maƙiyi daga Rumawa ba.

Sannan Manzon Allah (SAW) ya dawo Madina, kuma ya yi umarni da a rushe masallacin da aka riƙe shi don cutarwa (Masjidud-Dirar), kuma dawowarsa daga wannan yaƙi ya kasance a watan Ramadan ne shekara ta tara bayan hijira, kuma Allah ya saukar da dukkan suratul Baƙara a cikinta[3].

[1] Muslim ne yarawaito shi (27).
[2] Ibnu Hibban ne ya rawaito shi (1383).
[3] Alfusul (212).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI:

ZAIDU ƊAN HARISA (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Zaidu ɗan Harisa ɗan Harahil ɗan Abdil Uzza ɗan Imru'ul-ƙais, alkunyar sa ita ce Abu Usama, kuma ana masa laƙabi da "Masoyin Manzon Allah".

An haife shi kafin hijira da shekara arba'in da uku, a cikin mutanensa Banu Kalb.

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Shi ne shugaban bayi, kuma abin so ga Manzon Allah (SAW), kuma baban abin sonshi, kuma Manzon Allah (SAW) ba ya nuna so sai ga mutumin kwarai, Annabi (SAW) ya ce: (Ya kai Zaid kai masoyina na ne, kuma daga gare ni, kuma zuwa gare ni, kuma mafi soyuwar mutane a gare ni)[1].

Zaidu ya taso a gidan Manzon Allah (SAW) yana ƙarami, ya kasance ana kiran shi da suna "Zaid ɗan Muhammad" har sai da aka saukar da faɗin Allah: ((Ku danganta su ('ya'yan riƙo) ga iyayensu maza shi ne adalci a wurin Allah))[2].

Kuma lokacin da aka Aiko da Annabi (SAW) ya kasance cikin farko-farkon waɗanda suka musulunta, kuma ya kasance farkon wanda ya musulunta cikin bayi.

Annabi (SAW) ya aura masa 'yar baffansa Zainab 'yar Jahash, sannan Zaidu ya sake ta, sai Annabi (SAW) ya aure ta, kuma a game da haka ne aka saukar da faɗin Allah Maɗukaki ((to lokacin da Zaidu

[1] Ahmad (21777) ne ya rawaito shi.
[2] [Al'Ahzab: 5].

ya gama buƙatarsa da ita (matarsa Zainab), Mun aurar maka ita))[1], kuma ba a ambaci wani cikin sahabban Annabi (SAW) ba a cikin Alƙur'ani ban da shi.

Ya halarci yaƙin Badar da Uhud da Khandaƙ, da Hudaibiyya da Khaibar Allah ya ƙara masa yarda, kuma ya kasance shugaba a yaƙoƙi bakwai, kuma Annabi (SAW) ya sanya shi ya kula da Madina lokacin da ya fita zuwa Muraisi', kuma ya kasance shi ne kwamanda na farko a yaƙin Mu'uta, sai ya ɗauki tuta kuma ya tabbata har sai da ya faɗi yana Shahidi a wancan yaƙin[2].

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu – (RA) - a yaƙin Mu'uta, a shekara ta takwas (8), a lakacin yana da shekaru hamsin da biyar (55).

[1] [Ahzab: 37]
[2] Bukhari (4261).

Auna fahimtarka a darusan mako na 37			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah maɗukaki: (Lan yahur)?		B
	a. Ba zai tuba daga saɓo ba.	b. Ba zai koma ga Allah ya yi masa hisabi ba.	c. Ba za a tashe shi tare da masu lefi ba.
Darasin Hadisi	Tambaya: Tausayi wanda bawa yake siffantuwa da shi nau'i biyu ne:		A
	a. Na ɗabi'a da wanda ake koya.	b. Wanda ya taƙaita a kan mai shi da wanda ke kaiwa zuwa ga wani.	c. Na gaskiya da na ƙarya.
Darasin Aƙida	Tambaya: Me ake nufi da kalmar "Al-Wsilah" a cikin faɗin Allah: "Wabtagu Ilaihil-wasilah"?		A
	a. Neman yarda.	b. Neman kusanci.	c. Yankewa.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Me ake nufi da ba da Zakka “a tafarkin Allah"?		A
	a. Mayaƙan sa kai a tafarkin Allah.	b. Dukkan ayyukan ɗa'a da kyautatawa.	c. Duk wanda ake fatan musuluntarsa ko ƙarfin imaninsa.
Darasin Sira	Tambaya: An ambaci rundunar musulmi a yaƙin tabuka da suna:		C
	a. Rundunar budi	b. Rundunar haƙuri	c. Rundunar tsanani.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin matsayin Zaidu ɗan Harisa Allah ya ƙara masa yarda akwai cewa lallai shi ne:		C
	a. Farkon wanda ya yaƙi garuruwan rumawa.	b. Farkon wanda ya haddace Alƙur’ani.	c. Farkon wanda ya musulunta cikin bayi.

MAKO NA TALATIN DA TAKWAS

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI:

SURATUL INSHIKAK (2)

﴿فَلَآ أُقۡسِمُ بِٱلشَّفَقِ ١٦ وَٱلَّيۡلِ وَمَا وَسَقَ ١٧ وَٱلۡقَمَرِ إِذَا ٱتَّسَقَ ١٨ لَتَرۡكَبُنَّ طَبَقًا عَن طَبَقٖ ١٩ فَمَا لَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ ٢٠ وَإِذَا قُرِئَ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقُرۡءَانُ لَا يَسۡجُدُونَ ۩ ٢١ بَلِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يُكَذِّبُونَ ٢٢ وَٱللَّهُ أَعۡلَمُ بِمَا يُوعُونَ ٢٣ فَبَشِّرۡهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٢٤﴾

❖ Fassara:

16. To ina rantsuwa da shafaƙi.

17. Da kuma dare da abin da ya tattara.

18. Da kuma wata idan ya cika.

19. Tabbas za ku hau wani mataki bayan wani mataki.

20. To mai ya same su ne ba sa yin imani?

21. Idan kuma an karanta musu Alƙur'ani ba sa yin sujjada?

22. A'a, su dai waɗanda suka kafirce suna ƙaryatawa ne.

23. Allah kuwa Shi Ya fi sanin abin da suke ɓoyewa (a zukatansu).

24. To ka yi musu albishir da azaba mai raɗaɗi.

25. Sai dai waɗanda suka yi imani, suka kuma yi ayyuka nagari, to suna da lada marar yankewa.

❖ Saƙon da Surar ke ɗauke da shi:

Tunatar da mutum game da rauninshi, da yadda halaye suke jujjuyawa da shi, sa'an nan komawarshi ga Ubangijinshi.

❖ Baƙin Kalmomi

بالشفق	Bishshafaƙ	Da sama idan ta yi ja Ya yi n faɗuwar rana.
وسق	Wasaƙ	Ya haɗe.
اتسق	Ittasaƙ	Haskensa ya cika, kuma ya haskaka.
طبقا عن طبق	Ɗabaƙan ‘an ɗabaƙ	Yanayi daban-daban, da halaye mabanbanta
يوعون	Yu’un	Abin da suke ɓoyewa a cikin ƙirajen su na daga taurin kai da ƙarya.
غير ممنون	Gairu mamnuun	Wanda ba ya yankewa, kuma ba shi da tawaya.

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

Allah Yana rantsuwa da “shafaƙi” shi ne sama ta yi ja a Ya yi n faɗuwar rana, kuma ya rantse da dare, da abin da duhunsa yake tattarowa na daga halittu, da kuma wata da haskensa, cewa lallai mutam yana tafiya a kan wasu yanayi daban-daban, da halaye mabanbanta, yana farawa daga ɗigon maniyyi, zuwa ga gudan jini, zuwa wata tsoka, zuwa hura masa rai, zuwa mutuwa, zuwa tashi bayan mutuwa, amma duk da haka zuciyar kafiri ba ta motsawa da imani, kuma ba ta khushu'i idan ta ji ana karanta Al'ƙur'ani! To waɗannan Allah yanayi musu bushara da azaba mai raɗaɗi, amma waɗanda suka yi imani da Allah waɗanda suka yi aiki na ƙwarai, to su suna da sakamako madauwami da kuma lada wanda ba ya yankewa.

❖ **Abubuwan da za a koya daga Surar:**

1) Lallai canzawar mutane daga wani hali zuwa wani hali, tsa kanin tsanani da yalwa, da nagarta da lalcewa, dalili ne da ke nuna girman mulkin Allah, da ikonsa a kan tayar da mutane bayan sun mutu.

2) Lallai shafaƙi da jan yanayinsa, da dare da duhunsa, da wata da cikarsa, na daga cikin mafi girman ayoyi ga masu lura.

3) Wajibcin ba wa Alƙur'ani haƙƙinsa na girmamawa da darajantawa, Allah maɗaukaki yana cewa: ((Kuma idan an karanta musu Alkur'ãni, ba sa yin sujjada)).

LITININ: DARASI CIKIN HADISI:

HASSADAN FATA A LAMARIN ILIMI DA CIYARWA

An ƙarbo daga Abdullahi ɗan Mas'ud Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Babu hassada sai cikin abubuwa biyu: Mutumin da Allah ya ba shi dukiya, sai ya ɗaura shi a kan bayar da ita a kan hanyar da ta dace, da mutumin da Allah ya ba shi hikima (ilimi) sai yake hukunci da ita kuma yake koyar da ita**). Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi[1].

❖ Sharhi:

Nassoshin shari'a sun bayyana cewa lallai hassada nau'i biyu ce:

Nau'i na Farko: hassada haramtacciya kuma abar zargi ce a kowane hali ita ce mutum ya yi fatan gushewar ni'ima ta addini ko ta duniya daga ɗan uwanshi, to wannan nau'in shi ne wanda yake cinye kyawawan ayyuka mamar yadda wuta take cin itace.

Nau'i na Biyu: hassada wacce aka halasta ta, ita ce wacce mutum ba zai yi fatan gushewar ni'ima daga wani ba, sai dai ya yi fatan samun irinta, ko kuma wacce ta fi ta, ko wacce bata kai ta ba, shi ne ake nufi da “gibɗa” a larabci, kuma mafi cikar nau’ukanta shi ne abin da ya kasance cikin al'amurran addini.

***Kuma Annabi (SAW) ya ambaci siffar mutane biyu a cikin hadisin, ya nuna cewa su ne mafi girma cikin masu yin gibɗa:

Nau'i na Farko: Shi ne wanda yake da dukiyar da ya same ta ta hanyar halal, sannan aka datar da shi wurin bayar da ita wajen alheri da aikin ɗa'a da haƙƙoki na wajibi da na mustahabbi; to wannan yana daga cikin mafi girman dalili na gaskiyar imani.

---

[1] Bukhari (73) da Muslim (816) ne suka rawaito shi.

Nau'i na Biyu: shi ne wanda yake da ilimi da hikima da Allah ya sanar da shi, sai aka datar da shi wajen koyar da su da yin hukunci da su a tsa kanin mutane.

Saboda haka, waɗannan ni'imomi guda biyu su ne mafi cancantar a yi gibɗa a kansu, don abin da yake cikin su na kyautatawa, wanda babu abin da zai yi daidai da shi.

❖ **Abubuwan da za koya daga Hadisin:**

1) Bayanin cewa lallai ita hassada daga cikin ta akwai wacce aka hana kua akwai wacce take abin yabo, kuma ita ce wacce ake kira gibɗa.

2) Falalar dukiya da wadata idan ma'abocinsu ya yi abin da ya dace da su.

3) Lallai kyauta da bayarwa a tafarkin ɗa'a yana daga cikin mafi girman ni'imomi waɗanda suka cancanci Musulmi ya yi fatan samunsu.

4) Lallai koyar da ilimi mai amfani wanda bayin Allah za su samu shiriya da shi, to wannan yana daga cikin ni'imomi mafiya girma waɗanda Allah yake baiwar su ga wanda ya so.

5) Lallai neman abin da ba wannan ba na daga ababen duniya da jin daɗinta, ba sa daga cikin ababen da ake so.

6) Lallai abin da yake wajibi shi ne gode wa Allah a kan dukkanin ni'imomin da ya yi wa bawa; ta hanyar yin aiki da ita cikin abin da zai yardar da Allah.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDAH

TAWASULLI (2)

Mun gabatar a baya cewa tawassuli nau'i biyu ne: tawassuli wanda shari’a ta yarda da shi, kuma bayaninsa ya gabata, da kuma tawassuli haramtacce za mu yi bayanin shi a cikin wannan darasi.

❖ **Tawassuli wanda aka haramta:** Shi ne wanda aka ƙage shi, wanda ba wani dalili da ya yi nuni zuwa gare shi.

Kuma yana da nau’uka daban-daban, daga cikin su akwai:

1) Tawassali da neman addu'a daga matattu hakan ba ya halasta domin matacce ba ya iya amfanar da rayayye da komai, ba da addu'a ba ko da wanina, kuma babu wani dalili daga shari'a da yake nuni a kan halascinsa, bari dai, dalili ya yi nuni a kan haramcinsa, domin Umar ɗan Khaɗɗab Allah ya ƙara masa yarda da waɗanda suke tare da shi cikin sahabbai Ya yin da aka yi musu fari sun nemi a yi musu ruwa kuma sunyi tawassali da addu'ar rayayye, kuma ba su yi tawassuli da Annabi (SAW) ba bayan mutuwarsa, tare da cewa suna da ikon yin hakan; kuma don haka ne Umar Allah ya ƙara masa yarda ya ce:"ya Allah lallai mu munkasance muna tawassali zuwa gare ka da Annabinka da ka yi mana ruwa, to yanzu muna tawassali zuwa gare ka da baffan Annabinka ka yi mana ruwa”[1], saboda haka, da ya kasance neman addu'a daga mamaci ya halasta da ba su ketare Annabi (SAW) ba zuwa ga waninshi cikin waɗanda ba su kai shi ba.

2) Yin tawassali hanyar neman tsani da kuma ceto daga matacce, wannan da shi ne asalin aikin mushirikai; kamar yadda Allah maɗaukaki ya ce: ((Suna kuma bauta wa wani ba Allah ba, abin da ba zai cutar da su ba ba kuma zai amfane su ba, suna kuma cewa:

[1] Bukhari ne ya rawaito shi (1010).

“Waɗannan su ne masu ceton mu a wurin Allah.” Ka ce: “Shin yanzu za ku ba Allah labarin abin da bai sani ba ne a cikin sammai ko kuma a bayan ƙasa? Tsarki ya tabbata a gare Shi Ya kuma ɗaukaka daga abin da suke shirka da Shi))[1].

3) Yin tawassali zuwa ga Allah maɗaukaki da halittu, sawa’un da zatinsu ne ko da darajarsu ko da matsayinsu, kamar wanda zai ce: "ya Allah lallai ni ina tawassali zuwa gare ka da annabinka ko da wane, ko kuma ya ce: ya lallai ina tawassali zuwa gare ka da matsayin annabinka, ko kuma ina roƙon ka da haƙƙin annabinka, ko kuma wanin shi daga mutanen ƙwarai, to wadannan dukkaninsu suna daga cikin al'amura waɗanda aka haramta, da kuma bidi'o'i ababen ƙyama; saboda ababe masu zuwa:

- Lallai Allah maɗaukaki bai sanya zatin wani mahaluƙi ya zamo dalilin amsar addu'a ba, kuma bai shar'anta hakan ga bayinsa ba, kuma ibada ba ta tabbata sai da ingantaccen dalili bayyanan.

- Lallai Allah maɗaukaki babu wani haƙƙi na wani daya wajaba a kansa, kawai dai lallai shi ne yake yin falala ga hilitta, sai ya sanya wa kansa haƙƙi domin karamcinsa da falalarsa; kamar yadda Allah maɗaukaki ya ce: ((kuma taimakon muminai ya zama haƙƙi ne a kanmu))[2], sai mai biyayya ya cancanci sakamako, sai a yi masa baiwar kusanci da amsa addu'a, to wannan shi ne haƙƙi na falala da ni'imtarwa, ba wai haƙƙi irin wanda mutum yake nama a wurin wani mutum ba.

- Lallai wannan haƙƙin da Allah Ya yi falalar shi ga bawanshi shi wani haƙƙi ne wanda ya keɓanta da shi, zai amfanar da bawa da shi, kuma ba shi da wata alaƙa da waninsa, saboda haka, idan ya yi

[1] [Yunus: 18]
[2] [Ar-Rum: 48].

tawassali da shi ga waninsa, to ya kasance ya yi tawassali ga abin da bai cancanta ba, kuma ba zai amfanar da shi da komai ba.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU:

ZAKKAR BASHI

Mas'aloli da dama suna da alaƙa da zakkar bashi:

❖ **Mas'ala ta Farko:** Shin akwai Zakka a kan wanda ake bi bashi?

Mutumin da yake da bashi a kanshi shi ne ake kira da suna “almadyun”, Zakka tana wajaba ne a kan shi cikin abin da yake wurinsa na dukiya, amma da zai biya bashin da ake binshi kafin cikar zagayowar shekara, kuma babu abinda zai rage awurin shi; to babu Zakka a kansa, kuma Usman ɗan Affan Allah ya ƙara masa yarda ya kasance yana umartan wanda ake bi bashi da ya biya bashinsa kafin lokacin Zakka ya yi.

❖ **Mas'ala ta Biyu:** Shin akwai Zakka a kan wanda yake bin bashi?

Bashinka da yake wurin mutane nau'i biyu ne:

Na Farko: Bashin da kake sa ran za a biya ka: ta yadda ya kasance a hannun mawadaci mai iko biya; to wannan zaka fitar da zakkar shi a ko wace shekara, domin shi tamkar dukiyar da ta ke hannunka ne.

Na Biyu: Bashin da baka tsammanin za a biya ka: shi ne wanda ya kasance a hannun wanda ba shi da shi, ko mai musa bashin, ko mai taurin bashi, to wannan Zakka bata wajaba a cikin shi.

❖ **Mas'ala ta Uku:** Idan mutum yana bin wani bashi; shin zai iya yafe mishi, kuma ya lissafa shi cikin Zakka?

Hukunci: hakan baya halasta, domin a cikin hakan akwai ba da kariya ga dukiyar Zakka; ta yadda mutum ya riƙi yafe wannan bashin da bai samu damar karɓan shi ba a matsayin abin da zai hana

shi fitar da abin da yake kanshi na Zakka, sai dai ida aka ba wa talaka rabonshi daga Zakka, sai ya mayar da shi ga wanda ya bashi domin ya biya bashin shi, hakan ya halasta.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

SHEKARAR JAKADU

Shekarar Jakadu: Ita ce shekara ta tara bayan hijira, an kira ta da haka ne saboda yawan ayari da suka zo Madina daga sassa daban-daban na Jazirar larabawa suna musulunta suna ba da mubaya'a, bayan buɗe Makka da yaƙin Hunain da Tabuk, ƙabilu da yawa sun rika zuwa wajen Manzon Allah (SAW). Adadin su ya haura jakadu saba'in, daga cikinsu akwai: Jakadun Banu Tamim, Banu Amir, Banu Sa'ad ɗan Bakr, Abdulƙais, Banu Hanifa, Ɗaiyi'u, Banu Zubaid, Kinda, sarakunan Himyar, Banu Haris ibn Ka'ab, Hamdan, Adi ibn Hatim, Farwa bin Musaik Almuradi, Ṣurad bin Abdullah Al'azdi, da Farwa ibn Amr Aljuzaami.

Dukkansu sun zo suna miƙa wuya ga Musulunci, suna shiga cikin addinin Allah jama'a-jama'a, kamar yadda Allah ya ce: ((Idan nasarar Allah ta zo da kuma buɗe (Makka) () Ka kuma ga mutane suna shiga addinin Allah jama'a-jama'a, () To ka yi tasbihi da yabon Ubangijinka, ka kuma nemi gafararsa. Lalle Shi Ya kasance Mai karɓar tuba ne))[1].

A wannan shekara ne Annabi (SAW) ya aika Abu Bakar Siddiƙ Allah ya ƙara masa yarda a matsayin jagorancin aikin hajji. Bayan ya fita daga Madina tare da waɗanda suke tare da shi, Allah Madaukaki ya saukar da waɗannan ayoyi farkon suratut-taba: ((Allah da Manzonsa ba ruwansu da waɗanda kuka yi alƙawari da su daga cikin mushirikai () To sai ku tafi ku wala a bayan ƙasa tsawon wata huɗu…))[2], har zuwa fadinsa: ((Kuma sanarwa daga

[1] [An-Nasr:1-3].
[2] [At-Tauba 1].

Allah da Manzonsa zuwa ga mutane Babbar Salla cewa, lalle Allah da Manzonsa babu ruwansu da mushrikai))[1].

Sai Annabi (SAW) ya aiko Ali Allah ya ƙara masa yarda da surat Bara'a, yana kiran mutane da cewa: "Babu wani mushriki da zai yi hajj bayan wannan shekara, kuma babu wani da zai yi ɗawafi a ka'aba tsirara". Ya kuma fitar da yarjejeniyoyinsu, banda wanda yake da yarjejeniya da aka ƙayyade, to za a bar ta har zuwa ƙarshen wa'adinta[2].

[1] [At-Tauba: 3].
[2] Bukhari (4655) da Muslim (1347) ne suka rawaito shi.

ASABAR: DARASI CIKIN RAYUWAR SAHABBAI ABDULLAHI ƊAN MAS'UD (RA)

❖ Sunan sa da haihuwarsa:

Shi ne: Abdullahi ɗan Mas'ud ɗan Gafil ɗan Habib ɗan Shams Alhuzali, ana yi masa inkiya da Abu "Abdirrahman". An haife shi ne a Makka kusan shekaru ashirin kafin aiko da Manzon Allah (SAW).

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Allah ya ƙara masa yarda, ya kasance yana da ramamme ne, ƙafafunsa sirara, kuma ya kasance daga cikin masu mafi kyawun tufafi da ƙamshi. Ya shahara da gaskiya tun kafin Musulunci.

Ya kasance daga cikin farkon waɗanda suka shiga Musulunci, ya musulunta kafin Annabi (SAW) ya shiga Darul Arƙam[1], ya ce: "Haƙiƙa na kasance na shidan mutune shida, kuma babu wani musulmi a doron ƙasa sai mu"[2].

Ya shahara da ƙarfin Imani da yaƙini, kuma shi ne mutum na farko da ya karanta Alƙur'ani a fili a Kaʿba bayan Manzon Allah (SAW), ya yi hijira zuwa Habasha sau biyu, sannan ya yi hijira zuwa Madina, ya halarci yaƙin Badar da dukkan sauran yaƙe-yaƙe tare da Manzon Allah (SAW).

Kuma Ibnu Abbas Allah ya ƙara masa yarda ya kasance ma'abocin sirrin Manzon Allah (SAW), mai kula da takalmansa, asuwakinsa, da ruwa alwalarsa a tafiya, yana saka masa takalma, sannan ya yi

[1] Ibnu Sa'ad (3/1/107)
[2] Ibnu Hibban ne suka rawito shi (796).

tafiya a gabansa da sanda, idan ya zo majalisa sai ya cire masa takalman, ya ɗora su a hannunsa, sannan ya ba shi sandar.

Kuma ya kasance ana kamanta shi da Annabi (SAW), a halayyarsa da dabi'arsa. Kuma yayin da aka tambayi Huzaifa cewa wane mutum ne ya fi kama da Annabi (SAW) wajen halayya, sai ya ce: "Lallai mafi kama da Annabi wurin halayyarsa daga fitowarsa daga gida zuwa dawowa shi ne Ibn Umm ʿAbd (wato Ibn Masʿud)"[1].

Manzon Allah (SAW) ya yaba masa a wurare da dama. Daga ciki akwai lokacin da ya hau bishiyar arak don ya samo wani abu, sai iska ta tashi ta sai kafafunsa suka bayyana, mutane suka yi dariya saboda sirantarsu. Sai Annabi (SAW) ya ce: (Na rantse da wanda rayuwata take a hannunsa, kafafunsa suna da nauyi a ma'auni a ƙiyama fiye da Dutsen Uhudu)[2].

Haka kuma ya sheda masa da ƙwarewa a karatun Alƙur'ani ya ce: "Wanda yake son ya karanta Alƙur'ani sabo kamar yadda aka saukar, to ya karanta bisa karatun Ibn Umm Abdin"[3].

Ibn Mas'ud ya ce: "Na rantse da wanda babu abin bauta da gaskiya sai shi, babu wani sura daga cikin Littafin Allah da aka saukar face na san inda aka saukar da ita, babu wata aya da aka saukar face na san dalilin saukar ta. Idan na san akwai wani wanda ya fi ni sanin Littafin Allah kuma rakumi na iya kai ni wurinsa, zan yi tafiya in je wurinsa"[4].

Sahabbai sun tabbatar masa da wannan ilimi, Umar ɗan Khaɗɗab Allah ya ƙara masa yarda ya aike shi zuwa Kufa a matsayin malami

[1] Bukhari ne ya rawaito shi (2762).
[2] Ahmad ne ya rawaito shi (1/114).
[3] Ahmad (35) da Ibnu Hibban (7066) ne suka rawaito shi.
[4] Bukhari (5002) da Muslim (2463) ne suka rawaito shi.

mai fiƙihu. Ya ce: “Na fifita ku da ʿAbdullahi a kan kaina”[1], Abu Musa Al’ashʿari Allah ya ƙara masa yarda ya ce: “Kada ku tambaye ni komai muddin wannan masani yana tsa kaninku”[2].

❖ Rasuwarsa:

Ya bar Kufa ya cigaba da zama a Madina har sai da ya rasu a shekara ta 32H, yana da shekaru kusan sittin da ƙari, an binne shi a maƙabartar Baƙi’.

[1] Hakim ne ya rawaito shi (3/388).
[2] Bukari ne ya rawaito shi (6736).

Auna fahimtarka cikin darussan mako na 38			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Me ake nufi da shafaƙi?		a
	a. Sama ta yi ja yayin faɗuwar rana.	b. Sama ta yi ja yayin fitowar rana.	c. Sama ta yi ja yayin zazzaɓin wata.
Darasin Hadisi	Tambaya: Me ake kiran nau'in hassada wacca take abar yabo?		a
	a. Gibɗa	b. Gillu	c. Hiƙdu
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin haramtaccen tawassali akwai:		b
	a. Tawassali da ayyuka na gari	b. Tawassali da natsayin Annabi (SAW).	c. Tawassali da addu'ar iyaye.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Zakka tana wajaba a kan wanda yake bin bashi idan bashin ya kasance a kan:		c
	a. Wanda ba shi da kuɗi kuma talaka	b. Mai dukiya kuma mai taurin bashi.	c. Mai kuɗi kuma mai damar biya.
Darasin Sira	Tambaya: Shekarar jakadun jama'a ita ce shekara ta:		b
	a. Takwas bayan hijira	b. tara bayan hijira	c. goma bayan hijira
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin matsayin Abdullahi ɗan Mas'ud:		c
	a. Shi ne farkon wanda ya yi hijira zuwa Madina.	b. Farkon akƙalin musulmi a Sham	c. Farkon wanda ya karata Alƙur'ani a bayyane bayan manzon Allah (SAW)

MAKO NA TALATIN DA TARA

LAHADI: DARASIN TAFSIRI

SURATUL MUƊAFFIFIN (1)

﴿وَيۡلٞ لِّلۡمُطَفِّفِينَ ١ ٱلَّذِينَ إِذَا ٱكۡتَالُواْ عَلَى ٱلنَّاسِ يَسۡتَوۡفُونَ ٢ وَإِذَا كَالُوهُمۡ أَو وَّزَنُوهُمۡ يُخۡسِرُونَ ٣ أَلَا يَظُنُّ أُوْلَٰٓئِكَ أَنَّهُم مَّبۡعُوثُونَ ٤ لِيَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥ يَوۡمَ يَقُومُ ٱلنَّاسُ لِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦ كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ ٱلۡفُجَّارِ لَفِي سِجِّينٖ ٧ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا سِجِّينٞ ٨ كِتَٰبٞ مَّرۡقُومٞ ٩ وَيۡلٞ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُكَذِّبِينَ ١٠ ٱلَّذِينَ يُكَذِّبُونَ بِيَوۡمِ ٱلدِّينِ ١١ وَمَا يُكَذِّبُ بِهِۦٓ إِلَّا كُلُّ مُعۡتَدٍ أَثِيمٍ ١٢ إِذَا تُتۡلَىٰ عَلَيۡهِ ءَايَٰتُنَا قَالَ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٣ كَلَّاۖ بَلۡۜ رَانَ عَلَىٰ قُلُوبِهِم مَّا كَانُواْ يَكۡسِبُونَ ١٤ كَلَّآ إِنَّهُمۡ عَن رَّبِّهِمۡ يَوۡمَئِذٖ لَّمَحۡجُوبُونَ ١٥ ثُمَّ إِنَّهُمۡ لَصَالُواْ ٱلۡجَحِيمِ ١٦ ثُمَّ يُقَالُ هَٰذَا ٱلَّذِي كُنتُم بِهِۦ تُكَذِّبُونَ ١٧ كَلَّآ إِنَّ كِتَٰبَ ٱلۡأَبۡرَارِ لَفِي عِلِّيِّينَ ١٨ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا عِلِّيُّونَ ١٩ كِتَٰبٞ مَّرۡقُومٞ ٢٠ يَشۡهَدُهُ ٱلۡمُقَرَّبُونَ ٢١﴾

❖ Fassara:

1. Tsananin azaba ya tabbata ga masu tauye ma’auni.
2. Waɗanda idan suka auna daga wajen mutane suna cikawa fal.
3. Idan kuwa su za su aunar, da mudu ne ko da sikeli, to sai su tauye.
4. Yanzu waɗannan ba sa zaton cewa su lalle za a tashe su?
5. A wata rana mai girma?
6. Da mutane za su tsaya gaban Ubangijin talikai?
7. Tabbas, lalle littafin fajirai yana cikin Sijjinu.
8. Me kuma ya sanar da kai me ake ce wa Sijjinu?
9. Littafi ne rubutacce.
10. Tsananin azaba a wannan ya tabbata ga masu ƙaryatawa.
11. Waɗanda suke ƙaryata sakamako.

12. Babu kuwa mai ƙaryata ta sai duk wani mai shisshigi mai yawan saɓo.
13. Idan ana karanta masa ayoyinmu sai ya ce: “Wannan tatsuniyoyi ne na mutanen farko.
14. A'a, abin ai ba haka ba ne; abin da suke aikatawa ne ya yi tsatsa a zukatansu.
15. Tabbas! Lalle su haƙiƙa ababan kangewa ne daga (ganin) Ubangijinsu a wannan rana.
16. Sannan kuma lalle su tabbas masu shiga wutar Jahimu ne.
17. Sannan za a ce: “Wannan ne abin da kuka kasance kuna ƙaryata shi.
18. Tabbas! Lalle littafin mutanen kirki haƙiƙa yana cikin Illiyyuna.
19. Me ya sanar da kai mene ne *Iliyyuna*?
20. Wani littafi ne rubutacce.
21. (Mala’iku) makusanta suke halartar sa.

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Gargaɗi ga masu ƙaryatawa azzaluma game da alƙiyama, da albishir ga mumina.

❖ Baƙin kalmomi:

للمطففين	Lilmuɗaffifin	Waɗanda suke tauye ma’auni
يخسرون	Yukhsirun	Suna rage ma’auni
يظن	Yazunnu	Yana tunani
كتاب الفجار	Kitabal fujjari	Littafin ayyukansu
سجين	Sijjin	Ƙuntataccen kurkuku
مرقوم	Marƙum	Rubutacce; kamar zane a jikin riga wanda ba zai gogu ba.
معتد	Mu’tadin	Azzalumi mai wuce gona da iri.
أثيم	Asim	Mai yawan zunubi

أساطير	Asadir	Tatsuniyoyi
ران	Rana	Ya rufe
لمحجوبون	Lamahjubun	Za a hana su ganin Ubangijinsu
لفي عليين	La fi illiyyin	A wani wuri madaukaki

❖ Ma’anar Ayoyin a Dunkule:

Suratul Mudaffifin sura ce makkiyya, tana yi wa wadanda suke rage sikeli da ma’auni narkon azaba mai tsanani, kuma tana tunatar da su cewa za a tashe su kuma a musu hisabi a rana mai dauke da tsanani mai girma, inda mutane za su tsaya a gaban Ubangijin halittu, ya musu hisabi a kan kananan zunubbansu da manyansu.

A ranar lahira makomar fajirai ita ce kunci da kurkuku na dindindin, za a hana su ganin Ubangijinsu, kamar yadda tsatsa ta rufe zukatansu a duniya daga ayoyin Allah da fatan haduwa da shi, kamar yadda suka karyata ayoyin, suka ce labarai ne da tatsuniyoyi saboda girman kai da inkarin gaskiya, kuma tabbas an rubuta musu wannan makoma kuma an gama da batunsa.

Kuma kamar yadda makomar fajirai ta kasance mafi kaskanci wuri kuma mafi kunci, to lallai makomar mutanen kirki ita ce mafi daukakar wurare kuma mafi fadi, kuma tabbas an riga an rubuta musu wannan sakamako, ba za ta gushe ba kuma ba za ta canza ba, Mala’ikun da ke kusa da kowace sama suna sanin kowane kundin da aka rubuta.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Haramcin tauye sikeli da ma’auni, kuma shi ne: mutum ya dauka fiye da kima ko ya rage da gangan, ko da kuwa kadan ne.

2) Lallai kwadayi yana sa daga cikin munanan halaye a cikin ‘yan kasuwa, kuma babu wanda yake kuɓuta daga gare shi sai mai tsoron Allah.

3) Lallai tuna tsananin ƙiyama yana daga cikin manyan abubuwan da ke tsoratarwa daga zunubi.

4) Lallai abin da ka shuka shi zaka girba; sabod haka yayin da kafirai suka katange kansu daga ayoyin Allah, sai Allah Ya katange su daga ganinsa a lahira.

5) Hatsarin zunubai da laifuka, domin su ne sababin rufe zuciyar mutum da tsatsa

LITININ: DARASIN HADISI

HANI GAME DA BINCIKEN AIBUKAN MUTANE DA ƘIYAYYA DA JUNA

An karɓo daga Abu Huraira Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Ina gargaɗin ku game da zato, domin zato shi ne zance mafi ƙarya, kuma kada ku riƙa bin ƙwaƙƙwafi, kuma kada ku riƙa bin bin diddigi, kada ku yi ƙiyayya da juna, ku kasance bayin Allah 'yan'uwan juna, kuma kada mutum ya nemi aure a kan neman ɗan'uwansa har sai ya aura ko ya bari**)[1].

❖ Sharhi

Shari'a ta kwaɗaitar game da sasanci tsakanin musulmai da ƙarfafa zumunci da haɗin kai a tsakaninsu, kuma ta hana dukkan abin da zai sa rarrabuwar kai da ƙiyayya da gaba, a cikin wannan Hadisin, Annabi (SAW) ya yi gargaɗi game da wasu sabubban da ke haifar da gaba: ya hana zato mara tabbatacci, domin yawancin zato ƙarya ne, kuma ta hana binciken aibukan mutane, kuma ta hana bin diddigin neman labarai da ƙoƙarin sanin halin da mutane ke ciki, kuma Allah ya umarce mu da mu kasance 'yan'uwa a tafarkin Allah, masu ƙaunar juna, kuma idan wani musulmi ya nemi auren wata, ba ya halatta wani ya yi masa ƙwace har sai ta bayyana cewa ya bar ta, domin kada ya ji wani abu a ransa.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) Gargaɗi game da mummunan zato, domin ƙaryar da ke ciki ta fi gaskiyar yawa.

2) Haramcin bin ƙwaƙƙwafin musulmi don gano aibukansu.

[1] Bukhari ne ya rawaito shi (6064).

3) Haramcin bin diddigi, domin hakan ɗaura wa kai abin da da ba a umurce mu da shi ba ne.

4) Kwaɗaitarwa game da lizimtar abin da Manzon Allah (SAW) ya yi umarni da shi, shi ne mu kasance ’yan’uwa masu ƙaunar juna a tafarkin Allah.

5) Haramcin neman aure a kan neman auren wani, har sai ya bayyana cewa ya janye.

TALATA: DARASIN AƘIDA

NEMAN TAIMAKO DA NEMAN AGAJI

Neman taimako (Al-isti'ana): shi ne neman taimako wajen samun abin da ake nema.

Neman agaji (Al-istigasa): shi ne neman kawar da tsanani.

❖ **Neman taimako da agaji daga Allah Maɗaukakin Sarki:**

Allah ya umarce mu da mu fuskance shi domin neman taimako da agaji, saboda hakan wani sashe na na tabbatar da bauta ga Allah Maɗaukaki, domin duk wanda ya tabbatar da cewa Allah shi ne abin bauta, zai nemi taimako daga gare shi shi kaɗai, domin shi ne mai cikakkiyar kamala kuma mai ikon taimakon bayinsa.

Allah ya ce: ((Kai kaɗai muke bauta wa, kuma kai kaɗai muke neman taimakonsa))[1].

Allah ya yi yabo ga bayinsa muminai inda ya ce: ((Ku tuna lokacin da kuke neman taimakon Ubangijinku, sai Ya amsa muku cewa: “Ni zan kawo muku ɗauki na mala’iku dubu masu bibiyar juna.))[2].

Kuma ya zo a cikin hadisi, Annabi (SAW) ya ce: (Idan zaa ka nemi taimako, to ka nema daga Allah)[3], kuma idan wani abu ya dame shi ya ce: (Ya rayayye ya tsayayye, da rahamarka nake neman agaji)[4]

[1] [Al-Fatiha: 5].
[2] [Al-Anfal: 9].
[3] Tirmizi (2516) da Ahmad (2763) ne suka rawaito shi
[4] Tirmizi ne ya rawaito (3524).

❖ **Neman taimako da agaji daga halitta: Shi kuma nau'i biyu ne:**

Nau'i na farko: Neman taimako da agaji daga mahalukin da ke raye kuma a gabanka cikin abin da yake iyawa. Wannan halal ne, Allah ya ce: ((Ku yi taimakekeniya a kan ayyukan nagarta da taƙawa))[1]**.** Kuma Allah Ya faɗa a cikin ƙissar annabi Musa cewa: "((sai ɗan ƙabilar tasa ya nemi taimakonsa a kan wanda yake daga maƙiyansa))[2]. Kuma Ya ce game da Zulƙarnaini: ((Ya ce, "Abin da Ubangijina Ya ba ni ya fi (abin da za ku ba ni), sai dai ku taimake ni da ƙarfi don in sanya shamaki tsakaninku da su))[3].

Nau'i na biyu: Neman taimako daga matattu, ko daga wanda ba ya nan, ko cikin abin da babu wanda zai iya sai Allah, misali neman agaji daga matattu wajen warkar da mara lafiya ko kawar da damuwa, wannan babban shirk ne, Allah Ya ce: ((Kuma idan Allah Ya shafe ka da wata cuta, to ba wanda ya isa ya yaye ta sai Shi; kuma idan Ya shafe ka da wani alheri, to Shi Mai iko ne a kan komai))[4] Kuma Ya ce: ((Wane ne ya fi ɓata fiye da wanda yake bauta wa wani ba Allah ba, wanda ba zai amsa masa ba har zuwa alƙiyama, kuma su (ababen bautar) rafkanannu ne game da bautar da suke yi musu?))[5].

[1] [Al-Ma'ida: 2].
[2] [Al-Ƙasas:15].
[3] [Al-Kahf: 95].
[4] [Al-An'am: 17].
[5] [Al-Ahƙaf: 5].

LARABA: DARASIN FIƙIHU

ZAKKAR HANNAYEN JARI DA NA FILAYE DA GIDAJE

❖ Zakkar hannayen jari:

Mutane sun kasu gida biyu a dalilin sayen hannayen jari:

Sashe na farko: Wanda yake saye da sayar da hannayen jari ta hanyar bibiyar kasuwar hannun jari da alamomin, Ana kiransa da suna mai ciniki (Mudarib); wannan wajibi ne ya fitar da Zakka duk shekara, saboda hukuncin hannayen jari irin hukuncin kayayyakin kasuwanci ne, saboda haka, zai ƙididdige darajar hannayen jarinsa a ƙarshen shekara, ya fitar da kashi 2.5% (ɗaya bisa huɗun goma cikin ɗari).

Sashe na biyu: Wanda ya mallaki hannayen jari da niyyar zuba jari na lokaci mai tsawo, don samun riba ake rarrabawa; to a nan idan kamfanin ya bayyana a fili cewa shi ne yake fitar da zakka, ko kuma tsarin ƙasar ya wajabta wa kamfanoni fitar da Zakka kamar yadda yake a kamfanonin da ke ƙasar Saudiyya to a wannan yanayin, ba abin da ya hau kan mai hannun jari.

❖ Zakkar ƙadarori:

Abin da ake nufi da kadara a nan shi ne: Abin da mutum yake mallaka na filaye ko gine-gine da aka yi a kansu; kamar ƙananan gidaje, manyan gidaje, dakuna da wuraren hutawa.

❖ Zakkar Filaye ta bambanta da bambancin nufin waɗanda suka mallake su; suna da halaye guda huɗu:

Na farko: Mutum ya mallake su da niyyar amfani na kashin kansa don gini ko zama da makamantan haka; a wannan hali babu Zakka a cikinsu duk yawansu; domin sun koma cikin dukiyar amfani, haka

kuma, ƙadarar da mai ita ya saya don kare dukiya kawai ba tare da niyyar kasuwanci ko samun riba ba; babu Zakka a cikinsa.

Na biyu: Mutum ya mallake su da niyyar kasuwanci da karin darajarsu tsawon shekaru; to a nan za a fitar da Zakka kowace shekara gwargadon ƙimarsu a kasuwa, sawa'un farashin su ya ƙaru a kan farashin da aka saye su ko ya ragu.

Daga ciki har da: sayen taswirorin filaye da suke nesa da ga gari don jiran lokacin da mutane za su nemi wurin da kuma hauhawar farashinsu; to wadannan ana fitar da zakkarsu, domin an tanadar da su don kasuwanci kuma manufarsu ita ce bunƙasar dukiya. Kuma gwargwadon abin da za a fitar shi ne rubu'in goma cikin ɗari (2.5%).

Na uku: Mutum ya mallake su don haya da amfana kuɗaɗen shigarsu; kamar manyan gidaje da shagunan ajiye kaya da ɗakuna da aka sa musu kaya, da otel-otel; waɗannan ba a fitar da Zakka daga ƙadaran kansa, sai dai za a fitar daga kuɗaɗen hayan da aka karɓa idan an ajiye su suka kai shekara.

Na huɗu: Mutum ya mallake su da niyyar noma da aikin gona; to a nan babu Zakka a kan filyaen ko gidajen, sai dai za a fitar da Zakkar daga amfanin gonar da ribar da aka samu daga gare su.

ALHAMIS: DARASIN SIRA

HAJJIN BANKWANA

A Ranar Asabar, 25 ga watan Zulhijja ta shekara ta goma bayan hijira, Annabinmu Muhammad (SAW) ya fita zuwa babban hajjin sa (Hajjin bankwana), ya fita tare da dandazon mutane masu yawa da ba wanda ya san adadinsu sai Allah, sun fi dubu ɗari, matayensa tara suna tare da shi a cikin darbukansu, ya fito daga Madina da rana bayan ya yi salla, ya gyara gashin kansa, ya shafa mai; sai ya nufi miƙatin Zulhulaifa bayan la'asar, ya sauka ya kwana a can.

A rana ta biyu, ya yi wanka zuwa lokacin azahar don don ɗaukar harama, A'isha Allah Ya ƙara mata yarda ta shafa masa turare, sai ya sanya kwarjallensa da mayafinsa, ya hau taguwarsa mai suna Ƙaswa, ya ɗauki haramar hajj da umra a tare, wato (ƙirani).

Annabi (SAW) ya tafi da hadayarsa tun daga Zulhulaifa, yana talbiyya, sai Jibril ya zo ya umurce shi da ya umarci sahabbansa su ɗaga murya da talbiyya, domin ita tana daga cikin alamomi na hajji[1].

Bayan tafiya ta tsawon kwanaki takwas, ya isa Makka a daren lahadi, huɗu ga watan Zulhijja, ya sauka a wata unguwa mai suna (Zu ɗuwa) wacce ake kira a yau da (Hayyu Jarwal), ya kwana a can, da gari ya waye ya yi sallar asuba, ya yi wanka don shiga Makka, ya shige ta ne da rana daga wurin da ake kira da (Saniyyatu Kada'i), wadda ake kira yanzu: (Alhajun), ya shiga Masallaci Mai alfarma da hantsi ta ƙofar Bani Shaiba, wacce take kusa da ƙofar da a yanzu take ɗauke da lamba (22), ya yi Ɗawaful-ƙudum, ya yi sa'ayi tsakanin Safa da Marwa, Sannan ya zauna a Makka ranakun Lahadi, Litinin, Talata, Laraba, da daren Alhamis; sai da safiyar Alhamis a

[1] Abu Dawud ne ya rawaito shi (1814).

takwas “Tarwiya” ya nufi Mina tare da mutane, ya fara sauran ayyukan hajji.

Ya kwana a Mina daren Juma’a, tara ga watan Zulhijja, da safe ya tafi Arfa, ya sami tanti a (Namira), ya sauka ya huta; da rana bayan rana ta yi zawali ya umarni da a shirya masa abin hawansa Ƙaswa, sai ya je “Baɗnu Urana”, ya yi wa mutane huɗuba ma girma, ya kafa ƙa’idojin Musulunci; kusan sahabbai dubu arba’in suka halarta, Allah ya yarda su duka.

An haɗa sallar azahar da la’asar, sannan ya hau abin hawansa ya shiga Arafa, ya tsaya a gabashinta kusa da duwatsu, ya karkata zuwa ga alƙibla, ya ci gaba da addu’a har rana ta faɗi, daga nan ya tafi Muzdalifa, ya haɗa sallar magriba da isha’i a can, ya kwanta har asuba, ya yi asuba a farkon lokacinta, daga nan ya zo kusa da Dutsen Almashʿarulhram, ya fuskanci Alƙibla, ya ambaci Allah, ya girmama Shi, ya yi hailala, ya yi addu’a har gari ya waye sosai, sai ya tafi zuwa Mina kafin fitowar rana, ya jefi Jamratul Aƙaba. Sannan ya yi wata huɗuba mai girma, mai ratsa zuciya, ya yi bankwana da mutane. Sai ya yanka hadaya ɗari, ya aske kansa, ya rarraba gashinsa tsakaninsu: rabin ya ba wa Abu Ɗalha, rabin kuma aka rarraba tsa kanin mutane.

Kuma A’isha ta shafa masa turare bayan ya aske kansa. Daga nan Annabi (SAW) ya nufi Makka, ya yi “Ɗawaful ifada” yana a kan abin hawansa saboda mutane sun yi masa kewaye shi suna tambayarsa kuma su yi koyi da shi. Sannan ya yi sallar azahar a Makka, ya koma Mina, ya kwana a can dararen kwanakin Sallah (Ayyamuttashriƙ) yana jifan “Jamarat” a kowace rana bayan zawali.

A rana ta farko ya ya sake yin wata huɗuba mai girma, ya yi wasiyya, ya yi gargadi, ya yi ja kunne, ya sa suka yi shaida a kansu cewa ya isar da saƙo kuma ya sauke amana.

Yayin da ya yi jifan “Jamarat” a rana ta goma sha uku, sai ya nufi Makka ya sauka a wuri mai suna “Abɗah”, ya yi sallar azahar da la’asar da magrib, da isha’i, ya ɗan yi bacci, daga baya a ƙarshen dare ya kira a tashi, sai ya gangaro zuwa Masallaci Mai alfarma a daren goma sha huɗu, ya yi Ɗawafin bankwana, sannan ya yi sallar asuba da mutane, ya karanta Suratuɗ-Ɗur, daga nan ya kama hanya tare da musulmi zuwa Madina.

Da haka ne aikin hajjinsa ya kammala, Allah ya cika masa addininsa, tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a ko da yaushe har zuwa sakamako.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SA'AD ƊAN UBADA (RA)

❖ Sunan sa da Haihuwarsa:

Shi ne sahabi mai daraja: Sa'ad ɗan Ubada ɗan Dulaim ɗan Harisa Alkhazraji Al'anṣari Assa'idi. Ana kiran sa Abu Sabit, an haife shi ne a Madina kafin aiko Annabi.

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Ya kasance, Allah ya ƙara masa yarda, shi ne jakadan Banu Sa'ida, shugaban ƙabilar Khazraj kafin Musulunci, a jahiliyya an san shi da iya rubutu da harbi da iyo; kuma suna kiran wanda ya kware a waɗannan: "Kamili"[1].

Ya kasance jarumi, mai kyauta, mai tawali'u, mai adalci, mai tausayi, mai biyayya ga uwa, mai tsananin kishi a kan matayens, kuma mai ƙyamar duniya duk da cewa yana da arziki.

Ya halarci (Bai'atul Aƙaba) tare da mutanen madina saba'in, yana daga cikin wakilai guda goma sha biyu, kuma ya nuna jarumta a yƙin Badar; lokacin da Annabi (SAW) ya yi shawarwari da musulmi, sai Sa'ad ya tashi ya ce: "Na rantse da wanda rayuwata take a hannunsa, da ka umarce mu mu tsallaka ta cikin teku da dawakai, da mun tsallaka; kuma da ka umurce mu mu nufi Barkil Gimadi da mun yi[2]". Haka kuma ya halarci yaƙin Uhudu da Khandaƙ da Hunain da Fathu Makka. Ya kasance cikin waɗanda aka zaɓa don ya zama khalifa bayan rasuwar Annabi (SAW) [3].

[1] Al-Bidaya wan-Nihaya (9/607)
[2] Muslim ne ya rawaito shi (1779).
[3] Bukhari ne ya rawaito shi (3667).

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu, Allah ya ƙara masa yarda, a shekara ta 14 bayan hijira, a garin Hauran a Sham.

Auna fahimtarka a cikin darussan Mako na 39			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: me ake nufi da kalmar “Almuɗaffifun”?		a
	a. Waɗanda suke tauye ma’auni.	b. Waɗanda ba sa bada aro.	c. Waɗanda suke guman musulmi.
Darasin Hadisi	Tambaya: Annabi (SAW) ya hana “Tahassus”, kuma shi ne:		b
	a. Saurin fushi	b. Neman sani labaran abin da ba ya nan.	c. Kullata da hassada.
Darasin Aƙida	Tambaya: Hukuncin neman taimakon mamata don warkar da marasa lafiya da yaye damuwowi:		c
	a. Makaruhi	b. Ƙaramar shirka.	c. Babbar shirka
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Wanda yake kasuwancin hannayen jari wurin saye da sayarwa ta hanyar bibiyar kasuwanninn hannun jari da manuni:		a
	a. Zakka ta wajaba a kansa.	b. Zakka ba ta wajaba a kansa.	c. Mustahabbi ne ya ba da Zakka ba wajibi ba.
Darasin Sira	Tambaya: An ambaci rundunar musulmi a yaƙin tabuka da suna:		b
	a. Zakka	b. Rundunar haƙuri	c. Rundunar tsanani.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Annabi (SAW) ya fito don aikin hajjin banƙwana a shekara ta:		c
	a. Tara bayan hijira.	b. Goma bayan hijira	c. Goma sha ɗaya bayan hijira.

MAKO NA ARBA'IN

LAHADI: DARASIN TAFSIRI

SURATUL MUDAFFIFIN (2)

﴿إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ لَفِي نَعِيمٖ ٢٢ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ٢٣ تَعۡرِفُ فِي وُجُوهِهِمۡ نَضۡرَةَ ٱلنَّعِيمِ ٢٤
يُسۡقَوۡنَ مِن رَّحِيقٖ مَّخۡتُومٖ ٢٥ خِتَٰمُهُۥ مِسۡكٞۚ وَفِي ذَٰلِكَ فَلۡيَتَنَافَسِ ٱلۡمُتَنَٰفِسُونَ ٢٦ وَمِزَاجُهُۥ مِن
تَسۡنِيمٍ ٢٧ عَيۡنٗا يَشۡرَبُ بِهَا ٱلۡمُقَرَّبُونَ ٢٨ إِنَّ ٱلَّذِينَ أَجۡرَمُواْ كَانُواْ مِنَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ يَضۡحَكُونَ
٢٩ وَإِذَا مَرُّواْ بِهِمۡ يَتَغَامَزُونَ ٣٠ وَإِذَا ٱنقَلَبُوٓاْ إِلَىٰٓ أَهۡلِهِمُ ٱنقَلَبُواْ فَكِهِينَ ٣١ وَإِذَا رَأَوۡهُمۡ قَالُوٓاْ إِنَّ
﴿فَٱلۡيَوۡمَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنَ ٱلۡكُفَّارِ هَٰٓؤُلَآءِ لَضَآلُّونَ ٣٢ وَمَآ أُرۡسِلُواْ عَلَيۡهِمۡ حَٰفِظِينَ ٣٣
يَضۡحَكُونَ ٣٤ عَلَى ٱلۡأَرَآئِكِ يَنظُرُونَ ٣٥ هَلۡ ثُوِّبَ ٱلۡكُفَّارُ مَا كَانُواْ يَفۡعَلُونَ ٣٦﴾

❖ **Fassara:**

22. Lalle masu biyayya tabbas suna cikin ni’ima.
23. Suna kan gadaje suna kallo.
24. Za ka gane hasken ni’ima a fuskokinsu.
25. Ana shayar da su giyar da aka rufe bakin mazubinta.
26. Har ƙarshensa ƙamshin almiski ne.
27. To game da wannan kuwa lalle masu gasa su yi gasa.
28. Mahaɗinsa kuma daga ruwan tasnimu yake.
29. Wani idon ruwa wanda bayi makusanta ne suke sha daga gare shi
30. Lalle waɗanda suka yi manyan laifuka sun kasance suna yi wa waɗanda suka yi imani dariya a duniya.
31. Kuma idan suka wuce ta wajensu sai su riƙa zunɗen su.
32. Idan kuma sun koma wurin iyalinsu sai su komo suna masu farin ciki.
33. Kuma idan sun gan su sai su ce: “Lalle waɗannan ɓatattu ne”.
34. Ba a kuwa aiko su don su zama masu tsaron su ba.

35. To a wannan rana ne waɗanda suka yi imani za su yi wa kafirai dariya.
36. Daga kan gadaje suna kallo.
37. Shin an saka wa kafirai abin da suka kasance suna aikatawa?

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Gargaɗi ga masu ƙaryatawa azzalumai game da ranar alƙiyama, da albishir ga mumina da ita.

❖ Baƙin Kalmomi:

الأرائك	Al'ara'iki	Gadaje da aka ƙawata su da labulaye da tufafi
نضرة	Nadratan	Annuri
رحيق	Rahiƙin	Tataccen giya
ختامه مسك	Khitamuhu misk	Ƙarshensa ƙamshin almiski ne
ومزاجه	Wa mizajuhu	Mahaɗinsa
تسنيم	Tasnim	Idon ruwa a saman aljanna
يشرب بها	Yashrabu biha	Suke sha daga gares hi kuna suke jin daɗi
يتغامزون	Yatagamazun	Sashensu na zunɗe ga sashensu da idanunsu saboda izgilanci
انقلبوا	Inƙalabu	Su dawo
فاكهين	Fakihin	Suna farin ciki da izgilancinsu ga muminai
حافظين	Hafizin	Masu tsaronsu suna masu kiyaye ayyukansu
ثُوِّب	Suwwiba	Saka wa

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

Allah Maɗaukaki Yana bayyana cewa bayinsa nagartattu za su koma zuwa ga ni'ima tabbatacciya ta dindindin ga zuciya da ruhi da kuma

gangar jiki, za su rika zama a kan gadon alfarma da aka ɗaukaka, kuma aka ƙawata shi da shimfiɗu masu kyau, za su ga abin da aka tanadar musu na ni'ima, kuma za su kalli fuskar Ubangijinsu Mai karamci, duk wanda ya kalle su zai ga annuri da hasken ni'ima a fuskokinsu, abin shansu shi ne mafi daɗin abin sha, wato giya tatacciya da aka gauraya da ruwan (Tasnim) ƙarshenta kuma ƙanshin almiski ne tsarkakakke, saboda wannan ni'ima ne ya zama wajibi a yi rige-rige wurin aikata kyawawan ayyuka, da kuma guje wa makomar masu laifi, wanda akwai bambanci mai girma tsakaninsu da bayin Allah nagartattu; domin haƙiƙa sun kasance suna yin dariya da izgili ga muminai a duniya, suna yin zunɗe da farin cikin yi musu izgili yayin wucewarsu ta inda suke, ba tare da sun yi tunanin hisabi da azaba ba, sun haɗa tsakanin muzgunawa da kuma jin cewa suna cikin aminci, suna ɗaukar kansu a matsayin shiryayyu, kuma suna ɗaukar muminai a matsayin ɓatattu, suna ƙirƙirar ƙarya suna dangantawa ga Allah, kuma su ba a wakilta su a kan kula da mutane ba, suna bibiyarsu kuma suna jifansu da kowane irin aibu, saboda haka, sakamakonsu a lahira ya dace da aikinsu, muminai za su yi dariya lokacin da suka gan su suna jujjuyawa cikin azaba suna, alhali muminai suna cikin aminci da kwanciyar hankali.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Lallai rige-rige mai amfani shi ne wanda ake yi domin samun matsayi mai girma a Aljanna.

2) Lallai mafi girman ni'ima ga mutanen Aljanna ita ce kallo zuwa ga Ubangijinsu Mai girma da ɗaukaka.

3) Lallai izgili ga masu addini siffa ce daga cikin siffofin kafirai.

LITININ: DARASIN HADISI

KWAƊAITARWA GAME DA DASHE DA SHUKA ITATUWA

An rawaito daga Jabir Allah ya ƙara masa yarda ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Babu wani musulmi da zai dasa itace ko shuka wani abin shuka wanda mutum ko tsuntsu ko wata dabba za su ci face sai ya zama sadaka gare shi**)[1].

❖ Sharhi

A cikin wannan hadisin, Annabi (SAW) yana faɗakarwa game da falalar dasa itace da shuka, da kuma cewa babu wani musulmi da zai dasa wani abu ko ya shuka har amfaninsa ya kai ga wasu halittu daban, kamar wani mutum ya ci daga gare shi, ko tsuntsu, ko dabba, ko ma wasu ƙananan halittun ƙasa face ya samu lada na sadaka, an keɓance musulmi da ambato ne domin shi ne yake amfana da ladan sadaka a duniya da lahira, amma kafiri ba ya samun lada na lahira daga ayyukansa.

❖ Abubuwan da za a koya da su daga Hadisin:

1) Lallai hanyoyin samun lada nau'uka mabambanta ne kuma suna da yawa, daga ciki akwai dasa itace.

2) Bayanin falalar shuka, da kuma cewa duk abin da musulmi ya shuka to yana da ladan duk wanda ya ci daga gare shi.

3) Kwaɗaitarwa game da gina ƙasa da raya ta da abin da zai amfanar da mutane.

[1] Bukhari (2320) da Muslim (1553) ne suka rawaito shi.

4) Falalar ƙoƙari wajen samar da abu mai amfani da zai kai ga sauran halittu.

5) Falalar tausayi da jinƙai ga dabbobi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

TABARRUKI (NEMAN ALBARKA)

❖ Lallai daga cikin ƙa'idojin da aka kafa a cikin shari'a akwai cewa: Bauta ba ta karɓuwa sai da sharuɗɗa biyu muhimmai:

- **Na farko: T**tsarkake niyya domin Allah Maɗaukaki).
- **Na biyu: Bin Annabi** (SAW).

Allah Maɗaukakin sarki Ya ce: ((Duk wanda yake fatan haɗuwa da Ubangijinsa, to ya aikata aiki nagari, kuma kada ya yi wa Ubangijinsa shirka cikin bautarsa))[1].

❖ **Kuma akwai wata ƙa'ida wacce ita ce cewa: Asali a cikin ibada shi ne haramci, har sai ta tabbata da ingantaccen dalili.**

Manzon Allah (SAW) yana cewa: (Duk wanda ya ƙirƙiri wani abu a cikin wannan al'amarin namu (wato addini) wan da ba ya cikinsa ba, to an mayar masa)[2].

Idan waɗannan ƙa'idoji guda biyu sun tabbata kuma sun fito fes, sai a san cewa:

Lallai daga cikin mas'aloli da mutane da dama suke faɗawa cikin kuskure game da su akwai batun tabarruki, sawa'un da mutane, ko duwatsu, ko wurare, ko zamuna, wanda hakan ya haifar da bidi'o'i da ƙirƙirarrun abubuwan waɗanda Allah bai saukar da wata hujja a kansu ba.

Ma'anar tabarruki ita ce: Neman albarka, albarka kuma ita ce: yawan alheri, da ƙaruwarsa da dorewarsa.

---

[1] [Al-Kahf:110].
[2] Bukhari (2690) da Muslim (1718) ne ya rawaito shi.

Idan musulmi yana son albarka a dukiyarsa, rayuwarsa, lokacinsa da zuriyarsa, to ya wajaba ya nemi albarkar ta hanyoyin da shari'a ta halatta.

Saboda haka, ana iya kasa tabarruki zuwa kashi biyu: Tabarruki da aka halatta, da Tabarruki da aka haramta.

Tabarruki da aka halatta shi ne wanda ya cika sharuɗɗa biyu:

- **Shaɗi na farko:** A samu wani dalili da yake tabbatar cewa wannan al'amari yana da albarka.
- **Sharaɗi na biyu:** A yi tabarruki da shi ta hanyar da Manzon Allah (SAW) ya shar'anta.

Idan aka rasa ɗaya daga cikin sharuɗɗan guda biyu, to wannan tabarruki ya haramta.

Kuma za a keɓance wa kowane ɗaya daga cikin waɗannan nau'uka biyu darasi na musamman, kuma z aza ambaci misalai da nau'ukansa.

LARABA: DARASIN FIƘIHU

KURA-KURAI DA KE YAWAN FARUWA WAJEN FITAR DA ZAKKA

Akwai wasu kura-kurai da matsaloli da ke yawan faruwa wajen fitar da zakka, wanda ya zama dole a lura da su kuma a nisance su, daga cikinsu akwai:

1- Rashin lura da jinkirta fitar da zakka daga lokacin da ya zama dole a fitar da ita, wannan laifi ne mai girma, domin ba ya halatta a jinkirta ta, sai dai idan akwai wani uzuri na shari'a da ya hana mutum ya fitarwa, saboda ita zakka idan lokacin fitar da ita ya yi, to ta zama haƙƙin masu ita, kuma haramun ne a hana su ko a jinkirta musu. Allah Maɗaukaki ya ce: ((Waɗanda kuma suke akwai haƙƙi sananne a cikin dukiyoyinsu.

() Ga mai roƙo da wanda ake hana wa saboda ba ya roƙo))[1].

2- Wasu suna zaton cewa ba ya halatta a gabato da fitar da zakka kafin lokacin da ya wajaba a fitar da ita, amma zance mafi inganci shi ne: Yana halatta a gabato da fitar da ita kafin lokacin, idan mutum ya ƙasance ya mallaki nisabinta, musamman idan maslahar talakawa ko musulmi gaba ɗaya cikin hakan, to, ya halatta ya gabato da ita da kafin lokacinta da wata guda, ko sheƙara guda, ko shekaru biyu, amma ba ya halatta sama da shekaru biyu, domin shi ne mafi ƙololuwar abin da ya zo, an rawaito Hadisi cewa lallai Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi wa Abbas rangwame kan gabato da fitar da zakdarsa kafin lokacinta da shekaru biyu[2].

Wasu mutane sun fi son watan Ramadan ya ƙasance shi ne watan da za su riƙa fitar da zakkarsu a cikinsa, don haka idan lokacin fitarwar ya ƙasance bayan Ramadan ne, to ya halatta ya gabatar da ita zuwa Ramadan. Amma idan lokacin ya ƙasance kafin Ramadana ne to, ba

[1] [Ma'arij 24-25].

[2] Abu Dawud (1624) da Tirmizi (678) ne suka rawaito shi.

ya halatta a jinkirta ta daga lokacin wajabcinta kamar yadda ya gabata.

4- Bayar da ita ga kowa saboda sakaci ko son kai; Wannan ba ya halatta, domin zakka ba ta amfani, kuma ba ta sauke nauyin da ke kan mutum har sai an bayar da ta ga wanda Allah Ya ce a ba, domin Allah Maɗaukaki Shi da kansa ya raba dukiyoyin zakka a cikin faɗinsa cewa : ((Abin sani dukiyoyin zakka na matalauta ne kaɗai da miskinai da ma'aikatanta da waɗanda ake lallashin zukatansu da kuma game da 'yanta bayi da waɗanda ake bi bashi da kuma wajen jihadi saboda Allah da matafiyi. Farilla ce daga Allah. Allah kuwa Masani ne, Mai hikima))[1].

Saboda haka wajibi ne a yi matuƙar ƙoƙari wajen binciko waɗanda suka cancance ta, sai dai idan mutum ya yi ƙoƙarin bincike, sai ya bayar da ita ga wanda zatonsa ya rinjaya kan cewa shi ne wanda ya cancance ta, sai daga baya ya bayyana cewa ba shi ba ne wanda ya cancance ta, to hakan ya isar masa, kuma zunubi yana kan wanda ya karɓa.

5- Rashin fitar da zakka daga dukiyar ƙananan yara da mahaukata da waɗanda suka rude saboda tsufa da makamantansu; masu kula da su ne za su fitar musu zakka, Umar ɗan Khattab Allah Ya ƙara masa yarda ya ce: (Ku riƙa yin kasuwanci da dukiyoyin marayu, zakka ba ta cinye su"[2].

Haka kuma A'isha Allah ya ƙara mata yarda tana da marayu a gidanta, tana kuma fitar da zakka daga dukiyarsu[3].

6- Dogaro da kalandar miladiyya wajen lissafin lokacin da fitar da zakka; domin abin da ya wajaba shi ne a lissafa ta da kalandar hijiriyya, wato lissafin wata, domin su ne lokuta na shari'a, Allah

[1] [At-Tauba: 60].
[2] Abdurrazzaƙ ne ya rawaito shi (6773).
[3] Malik ne ya rawaito shi (1/251).

Maɗaukaki ya ce: ((Suna tambayar ka dangane da jirajiran wata. Ka ce: “Su lokuta ne don amfani ga mutane da tantance lokacinHajji))[1].
7- Mutum ya fitar da ita bisa tilas, domin wajibi ne musulmi ya fitar da ita cikin dadin rai, yana mai gaskata wajabcinta, kuma yana mai neman kusanci da ita ga Ubangijinsa Mai girma da ɗaukaka, Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: (Abubuwa guda uku duk wanda duk ya aikata su to, ya ɗanɗani zaƙin imani: wanda ya bauta wa Allah Shi kaɗai, kuma ya san cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, sannan ya bayar da zakka daga dukiyarsa cikin dadin rai, mai maimaituwa gare shi a kowace sheƙara"[2].

[1] [Al-Baƙara: 189].

[2] Abu Dawud (1582) da Baihaƙi (4/95) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA RASUWAR ANNABI (SAW)

Lokacin da Annabi (SAW) ya dawo daga Hajjin bankwana, ya zauna a Madina cikin abin da ya yi saura daga watan Zul-Hijja, da Muharram, da Safar, sai ya fara rashin lafiya a ranar Alhamis farkon watan Rabi‘ul-Awwal, a lokacin yana ɗakin Maimuna Allah Ya ƙara mata yarda, kuma ya fara ne da ciwon kansa mai daraja, amma duk da haka ya ci gaba da kwana a ɗakunan matansa, har sai da hakan hakan ya yi masa tsanani, sai ya nemi izini daga gare su kan ya cigaba da jinya a ɗakin A’isha Allah Ya ƙara mata yarda, suka kuma yi masa izini, sai ya zauna cikin jinyan har tsawon kwanaki goma sha biyu.

Kuma a cikin sallar Isha’i na ranar Alhamis kafin rasuwarsa da kwanaki huɗu, ciwonsa ya tsananta, jikinsa ya ɗau zafi, kuma ya yi ta suma, Bilal ya ƙasance yana zuwa yana sanar da shi lokutan sallah, sai Annabi (SAW) yake cewa: “Ku umarci Abubakar ya ja mutane salla, sai aka ce masa: Ya Manzon Allah, lallai Abubakar mutum ne mai raunin zuciya, idan ya tsaya a wurinka ba zai iya jiyar da mutane ba, sai Annabi (SAW) ya sake maimaita umarninsa, ya ce: “Ku umarci Abubakar ya ja mutane sallah, sai Abubakar Allah ya ƙara masa yarda ya riƙa ja mutane sallah a waɗancan kwanaki.

A daidai lokacin hantsin ranar Litinin, sha biyu ga watan Rabi‘ul-Awwal, a sheƙara ta goma sha ɗaya bayan Hijira, tsananin cutar mutuwa ya fara sauka a kan Manzon Allah (SAW) kuma alamun magagin mutuwa suka bayyana tare da shi, A’isha Allah ya ƙara mata yarda ƙasance a kusa da shi, sai ta kwanto da shi a jikinta, sai ya ɗaga ɗan yatsarsa, sai idanunsa suka kafe suna kallon sama, sai A’isha ta fari jin wasu kalmomin suna fitowa daga bakinsa, sai ta ji yana cewa: "Ya Allah, ka gafarta mini, ka yi mini rahama, ka haɗa ni da abokan zama mafiya ɗaukaka). Ya maimaita haka sau uku.

Sai Allah Ya karɓi ransa, ya haɗa shi da abokan zama mafiya ɗaukaka, a lokacin yana ɗakin A’isha Allah Ya ƙara mata yarda, Annabi (SAW) ya rasu ne yana da shekaru sittin da uku.

Sai bala’i ya tsananta da rasuwar Annabi (SAW), masifar ta girmama al’amarin ya yi girma, kuma musulmi suka shiga cikin rikici da firgici, har sai da Abubakar Siddiƙ Allah Ya ƙara masa yarda ya zo, ya tara mutane, ya yi musu jawabi mai ɗorewa, ya ce: “Bayan haka; duk wanda ya ƙasance yana bautar Annabi Muhammadu, to lallai Annabi Muhammadu ya rasu, amma duk wanda ya ƙasance yana bautar Allah ne, to lallai Allah Mai cikakken rai ne da ba ya mutuwa".

Sannan ya ƙaranta musu faɗin Allah: ((Annabi Muhammadu ba kowa ba ne face Manzo da wasu manzanni suka gabace shi, shin idan ya mutu ko aka kashe shi, sai ku juya bisa dugaduganku? To, duk wanda ya juya baya to ba zai cutar da Allah da kome ba, kuma da sannu Allah Zai saka wa masu Godiya))[1].

Sai mutane suka ƙasance kamar ba su taɓa jin wannan aya ba kafin wannan lokaci. Babu wanda bai miƙe yana ƙaranta ta ba[2].

Daga nan musulmi suka nufi Rumfar Bani Sa‘ida, sai duka ra'ayinsu ya haɗu kan zaɓen Abubakar Allah Ya ƙara masa yarda a matsayin Halifa ga musulmi, kuma suka yi masa mubaya’a a wurin, sannan ya fito, gama-garin mutane suka yi masa mubaya’a a kan mimbar.

Daga nan sahabbai suka fara shirin jan'izar Manzon Allah (SAW), sai suka yi masa wanka cikin rigarsa[3], kuma waɗanda suka yi wannan aikin su ne Baffansa Abbas, da ɗansa Ƙutham, da Aliyu ɗan Abi Talib, da Usama ɗan Zaid, da Shukran Allah Ya ƙara musu yarda baki ɗaya[4].

---

[1] [Ali'Imran: 144].

[2] Bukhari ne ya rawaito shi (1242).

[3] Abu Dawud (3141).

[4] Al-Bidāya wan-Nihaya (8/201).

Kuma suka yi masa likafani a kan da mayafai guda uku na auduga farare, babu riga kuma babu rawani a cikinsu[1]. Daga nan Sahabbai suka yi masa salla kowa shi kaɗai ba tare da limami ba domin girmar darajarsa (SAW), yayin da maza suka gama yi masa salla, sai mata suka yi suma, sai aka binne shi a ranar Talata, a wurin da ya rasu, cikin ɗakin A'isha Allah Ya ƙara mata yarda[2].

Tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gare shi, da alayensa, da sahabbansa, Ya saka masa da mafi alherin abin da yake saka wa wani Annabi a kan al'ummarsa, ko wani Manzo a kan ɗa'awarsa da saƙonsa.

[1] Bukhari (1223), da Muslim (941) ne suka rawaito shi.
[2] Al-Bidāya wan-Nihaya (8/233).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SA‘AD ƊAN MU'AZU (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Sa‘ad ɗan Mu'azu ɗan Nu'man ɗan Imri’ul-Ƙais ɗan Zaid ɗan Abdul-Ashhal, ana kiransa da Abū Amr.

An haife shi ne a Madina shekaru goma sha biyu kafin a aiko Manzon Allah.

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Sa‘ad Allah Ya ƙara masa yarda yana da tsayi, fatarsa fara ce, kuma yana kyakkyawar fuska da gemu, shi ne shugaban kabilar Aus, mai matsayi ne a wajensu, a lokacin da ya musulunta, ya ya ɗau azamar yaɗa Musulunci a cikin kabilarsa, sai ya tafi wurinsu ya tsaya a gaban ya ce: Ya ku Banu Abdil-Ashhal, mene ne matsayi na a gare ku? Suka ce: Kai ne shugabanmu mafi daraja, kuma abin alfaharinmu. Sai ya ce: to, ba zan ƙara magana da ku ba, mazanku da matanku, har sai kun yi imani da Allah da Manzonsa, don haka, babu wanda ya rage a cikin Ƙabilar Banu Abdl-Ashhal, namiji ko mace, har sai da ya musulunta"[1].

Sa‘ad Allah Ya ƙara masa yarda ya halarci yaƙe-yaƙe masu yawa tare da Annabi (SAW) mafi shahara daga cikinsu shi ne Yaƙin Badar da Yaƙin Khandaƙ

Daga cikin mafi shaharar ayyukansa: Akwai hukuncinsa mai ƙarfi a kan Banu Ƙuraiza; saboda sun karya alƙawarinsu da musulmi, kuma suka yi haɗin guiwa da Ƙuraishawa a Yaƙin Khandaƙ, sai Allah Ya ba musulmi nasara a kansu, sai suka aiko suna neman sulhu, kuma sun yarda da hukuncin Sa‘ad ɗan Mu'azu a kansu, domin shi ne abokin huldarsu a lokacin jahiliyya, sai Annabi (SWA) ya aika a kira

[1] Siyaru A‘lamin-Nubala (1/280).

Sa‘ad, sai aka zo da shi a kan jaki, domin a lokacin yana Madina yana jinyar ciwon da aka ji masa a Yaƙin Khandaƙ, sai mutane suka ce masa: Ka kyautata wa abokan huldarka, domin Manzon Allah ya sanya ka kai ne mai hukunci a kansu.

Yayin da ya isa wajen Annabi (SAW) suka sauko da shi, sai ya ce: To, hukuncina a kansu shi ne a kashe maza mas yaƙi daga cikinsu, kuma a kama matansu da ‘ya’yansu a matsayin bayi, sai Annabi (SAW) ya ce: “Ka yi hukunci da hukuncin Sarki Allah)[1].

❖ **Rasuwarsa:**

Bayan hukuncinsa Allah Ya ƙara masa yarda a kan Banu Ƙuraiza, sai ya roƙi Allah Mai girma da ɗaukaka yana cewa: “Ya Allah! Lallai ina kyatata zaton Ka kawo ƙarshen yaƙin dake tsakaninmu da su, to idan har akwai sauran yaƙi tsakanimmu da Ƙuraishawa, to ka bar ni a raye har sai na yaƙe su domin ka, amma idan ka riga ka kawo ƙarshen yaƙin, to fasa ɗan yatsana, kuma Ka sanya shi sanadiyar mutuwata, To, sai ɗan yatsar ya fashe, sai ya rasu ta dalilin hakan Allah Ya ƙara masa yarda[2]. Wannan ya ƙasance ne a sheƙara ta biyar bayan Hijira.

Annabi (SAW) ya halarci wankan gawarsa, kuma ya ce: “Wannan shi ne bawan Allah nagari wanda da al’arshi ya motsa saboda shi, kuma aka buɗe masa ƙofofin sama, kuma Mala’iku dubu saba’in suka halarci ɗaukar ransa, waɗanda ba su taɓa sauko wa ƙasa ba kafin wannan lokaci)[3].

[1] Bukhari (4121), da Muslim (1768) ne suka rawaito shi.
[2] Bukhari (4122), da Muslim (1769) ne suka rawaito shi.
[3] Nasa’i (2055) ne ya rawaito shi.

Auna fahimtarka a cikin darussan mako na 40			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Menene ake nufi da kalmar “Al-Arā’ik”?**		c
	a. Matashin kai.	b. Tufafin hariri.	c. Gadoje da aka kawata da labule da mayafai.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Idan wani dabba ta ci daga abin da mutum ya shuka:**		c
	a. Ana rubuta masa amfanin ta da ladan ta.	b. Wanda ya taƙaita a kan mai shi da wanda ke kaiwa zuwa ga wani	c. Ta zama sadaka a gare shi.
Darasin Aƙida	**Tambaya: Asali a cikin ibadodi shi ne:**		a
	a. Haramci.	b. Halacci.	c. Makaruhi.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Dogaro wajen lissafin zagayowar sheƙara ta zakka yana ginuwa ne bisa:**		b
	a. Lissafin rana .	b. Lissafin wata.	c. Dukansu daidai ne.
Darasin Sira	**Tambaya: Farkon ciwon Annabi (SAW) ya faru a cikin ɗakin:**		c
	a. Hafsa Allah Ya ƙara mata yarda.	b. Ummu Salama Allah Ya ƙara mata yarda.	c. Maimuna Allah Ya ƙara mata yarda.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin shaharar ayyukan Sa‘ad ɗan Mu'azu Allah Ya ƙara masa yarda:**		a
	a. Hukuncinsa a kan Banu Ƙuraiza.	b. Kariya da ya yi wa Annabi (SWA) a Yaƙin Uhud.	c. Jaruntarsa a Yaƙin Ahzab.

MAKO NA ARBA'IN DA ƊAYA

LAHADI: DARASIN TAFSIRI
SURATUL-INFIDAR

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
إِذَا ٱلسَّمَآءُ ٱنفَطَرَتۡ ١ وَإِذَا ٱلۡكَوَاكِبُ ٱنتَثَرَتۡ ٢ وَإِذَا ٱلۡبِحَارُ فُجِّرَتۡ ٣ وَإِذَا ٱلۡقُبُورُ بُعۡثِرَتۡ ٤
عَلِمَتۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ وَأَخَّرَتۡ ٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡإِنسَٰنُ مَا غَرَّكَ بِرَبِّكَ ٱلۡكَرِيمِ ٦ ٱلَّذِي خَلَقَكَ
فَسَوَّىٰكَ فَعَدَلَكَ ٧ فِيٓ أَيِّ صُورَةٖ مَّا شَآءَ رَكَّبَكَ ٨ كَلَّا بَلۡ تُكَذِّبُونَ بِٱلدِّينِ ٩ وَإِنَّ عَلَيۡكُمۡ
لَحَٰفِظِينَ ١٠ كِرَامٗا كَٰتِبِينَ ١١ يَعۡلَمُونَ مَا تَفۡعَلُونَ ١٢ إِنَّ ٱلۡأَبۡرَارَ لَفِي نَعِيمٖ ١٣ وَإِنَّ ٱلۡفُجَّارَ لَفِي
جَحِيمٖ ١٤ يَصۡلَوۡنَهَا يَوۡمَ ٱلدِّينِ ١٥ وَمَا هُمۡ عَنۡهَا بِغَآئِبِينَ ١٦ وَمَآ أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ ١٧ ثُمَّ مَآ
أَدۡرَىٰكَ مَا يَوۡمُ ٱلدِّينِ ١٨ يَوۡمَ لَا تَمۡلِكُ نَفۡسٞ لِّنَفۡسٖ شَيۡـٔٗاۖ وَٱلۡأَمۡرُ يَوۡمَئِذٖ لِّلَّهِ ١٩﴾

❖ Fassara:

1. Idan sama ta tsattsage.
2. Idan kuma taurari suka farfaɗo suka tarwatse.
3. Idan kuma koguna aka harhaɗe su.
4. Idan kuma ƙaburbura aka fito da matattun da ke cikinsu.
5. Kowane rai ya san abin da ya gabatar da wanda ya jirkintar.
6. Ya kai mutum, me ya ruɗe ka ne game da Ubangijinka Mai ƙaramci?
7. Wanda Ya halicce ka Ya kuma daidaita ka Ya miƙar da kai?
8. Ya harhaɗa ka cikin irin surar da Ya ga dama?
9. A'a dai, kawai dai kuna ƙaryata sakamako ne.
10. Kuma lalle akwai masu kula da ku.
11. Masu daraja marubuta.
12. Suna sane da abin da kuke aikatawa.
13. Lalle mutanen kirki tabbas suna cikin ni’ima
14. Lalle kuma fajirai tabbas suna cikin wutar Jahima.

15. Za su ƙonu da ita sakamako.
16. Kuma su ba masu rabuwa ne da ita ba.
17. Kuma kai me ya sanar da kai mece ce sakamako?
18. Sannan me ya sanar da kai mece ce sakamako?
19. Ita ce da wani rai ba ya mallakar wani amfani ga wani rai; al'amari kuwa gaba ɗayansa a wannan yana ga Allah.

❖ Saƙon da Surar ke ɗauke da shi:

Gargaɗin mutum daga ruɗuwa da manta AlƘiyama.

❖ Baƙin Kalmomi:

اِنْفَطَرَتْ	**Infaɗarat**	ta tsage.
اِنْتَثَرَتْ	**Intasarat**	suka tarwatse.
فُجِّرَتْ	**Fujjirat**	suka cika, suka malala, suka farfashe, ruwansu ya gudana.
بُعْثِرَتْ	**Bu'sirat**	aka juya ta ta hanyar fito da abin da aka binne a cikinta.
ما غَرَّكَ	**Ma garraka**	menene ya ya ruɗe ka, ya kai ka zuwa ga kafirci da saɓa masa .
فَسَوَّاكَ	**Fasawwaka**	Ya halicce ka cikin daidaitacciyar sura, lafiyayyen sassa.

❖ Ma'anar Surar a Dunƙule:

Suratul-Infiɗar Sura ce Makiyya tana ƙunshe da bayani ne a kan Ranar Ƙiyama, da abubuwan firgici da ke cikinta, ta hanyar watsewar halittu da aka tsara gininsu, da sauyawar yanayinsu, da taɓarɓarewar hanyarsu; domin mutane su fito daga ƙaburbura, suna masu fuskantar tsayuwa a gaban Allah, a wannan lokacin ne za a

yaye labule, abin da ke ɓoye zai fito, kowane rai ya san abin da ke tattare da shi na riba ko asara.

Sannan ayoyin zargi da tsoratarwa ga mutum suka zo suna cewa: Mene ne ya ruɗe ka, ya ƙawa ta maka saɓa wa Ubangijinka? Wanda Ya halicce ka cikin kyakkyawar sura da mafi kyawun zubi, kuma Ubangijinka ya tsara halittarka tsari mai ƙarfi da daidaito, amma duk da haka mutane ba su gushe ba suna ci gaba da ƙaryatawa game da sakamako, sai dai Allah Ya sanya mala'iku masu girma a tare da su, suna rubuta maganganunsu da ayyukansu a cikin littattafai, domin su gabatar musu da su a Ranar Ƙiyama.

To, wanda ya ƙasance mai biyayya nagari, za a saka masa da Aljanna da ni'ima, wanda kuma ya ƙasance fajiri mai saɓa wa Allah, to zai hadu da sakamakonsa a cikin wuta, a da babu wani rai da zai mallaka wa wani rai komai, kuma ƙauna ko ceto ba za su yi amfani ba.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Girmamawar Allah ga mutum; inda Ya halicce shi cikin mafi kyawun sura da kyakkyawan da mafi ƙayatarwar zubi.

2) Gargadi game da gafala daga tashin kiyāma da sakamako; domin hakan shi ne babban sababbin shirka da ɓarna.

3) Gargadi game ruɗuwa da ƙaramcin Allah da jinkirirtawarsa.

4) Tunatar da bayin Allah kan cewa lallai ana kiɗanya musu ayyukansu, kuma za a bijiro da su ga kowane bawa a cikin littafinsa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR KYAKKYAWAR ɗABI'A

An karɓo daga A’isha Allah Ya ƙara mata yarda, ta ce: Na ji Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: (**Lallai mū’mini yana iya kaiwa matsayi irin na mai azumi mai tsayuwar dare saboda kyawun ɗabi'arsa**)[1].

❖ Sharhi

Ɗabi'antuwa da kyakkyawar daɓi'a yana daga cikin mafi girman ibadodi da suke sanya Allah Ya yarda da bawa, kuma ya sanya shi daga mafi kusa da Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a majalisarsa, haka kuma yana kai shi ga matsayi irin na wanda yake shafe darensa yana yin sallar nafila, kuma yake yin azumn nafila a yini, wannan kuwa saboda wanda yake kyautata daɓi'arsa da mutane ta hanyar hana kansa daga cutar da su, da yi musu magana mai daɗi, da tausasawa da sauƙaƙawa gare su, da yi musu murmushi da da sakin fuska, da bayar da kyauta gare su, da hakuri bisa cutarwarsu, tare da bambancin halayensu, lallai yana yin jihadi ne da rayuka masu yawa, kuma a tattare da shi akwai gajiya da wahala wadda ta yi daidai da ta mai azumi da mai tsayuwar dare cikin gajiyarsa da wahalarsa a kan biyayya ga Allah; saboda haka ne ya daidaita su a daraja da matsayi.

❖ Abubuwan za a koya daga Hadisin:

1) Dole ne Musulmi ya ɗabi'antu da ɗabi’u na ƙwarai kuma kyawawa; har Allah Ya sanya masa ƙauna da karɓuwa a wurin mutane, da kusanci da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a

[1] Abu Dawud ne ya ruwaito shi (4798).

gare shi a lahira, kuma da samun irin darajar mai azumi da mai tsayuwar dare.

2) Munanan ɗabi’u kamar mummunar magana, da ɗaure fuska, da kaushin mu'amala, suna jawo ƙiyayya daga mutane a duniya, da nisa daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a lahira.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

TABARRUKIN DA AKA HARAMTA

Tabarrukin da aka haramta: Shi ne wanda da babu wani dalili na shari'a da ya nuna halaccinsa.

Kuma yana da misalai masu yawa, daga cikinsu akwai:

Na farko: Tabarruki da zatin mutane ta hanyar shafa su da makamantan haka, irin wannan bai halatta ba saboda rashin izinin shari'a a akai, shari'a ba ta halatta tabarruki da kowa ba sai da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a lokacin da yake raye, domin haƙiƙa ya tabbata cewa lallai Sahabbai sun yi tabarruki da gashinsa da yawunsa, da ruwan alwalarsa, da zufarsa, da akushinsa da kuma tufafinsa, saboda abin da Allah Ya sanya a masa na albarka, wannan nau'i na tabarruki ya ƙare, domin babu wani abu da ya rage da cikin waɗannan abubuwa, kuma ba zai taɓa yiwuwa ba a iya tabbatar da samuwarsu ba bayan wucewar shekaru da zamuna masu yawa.

Amma wanin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi daga cikin salihai, ba ya halatta a yi tabarruki da zatinsu ko abubuwan da suka bari, saboda:

1. Rashin samun hujjar da ta nuna halaccin haka; sai hukunci ya tabbata a kan asali wato hani da haramci.
2. Lallai Sahabbai Allah ya yarda da su, ba su aikata irin wannan tabarruki ba ga wanin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi.
3. Don toshe kafar shirka, domin tabarruki da abin da salihai suka bari na iya kaiwa ga yin wuce gona da iri a kansu.

Sheikh Abdulaziz bin Baz Allah Ya masa rahama ya ce: "Tabarruki da abin da salihai suka bari ba ya halatta, abin sani kawai, haka yan

halatta ne da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi shi kaɗai, saboda abin da Allah Ya sanya a jikinsa da abin da ya shafe shi na daga albarka"[1].

Sai dai ya halatta a yi tabarruki da zama tare da salihai, inda ake samun nau'o'in albarka kamar amfana da iliminsu, da addu'arsu, da sauraron wa'azinsu, da kuma samun falalar zama a majasosin zikiri tare da su.

Na biyu: Tabarruki da wuraren da Annabi (SAW) ya taɓa tafiya a cikinsu, ko ya wuce ta cikinsu, ko ya zauna a cikinsu; kamar wanda yake hawa Dutsen Hira, ko Dutsen Thaur, ko Dutsen Uhud, ko wani makamancinsu. Tabbarruki da wuraren, ko yin salla a cikinsu, ko ziyartar su, bai tabbata ba zamanin Annabi (SWA) ba, haka kuma bai tabbata ba a zamanin Halifofi shiryayyu, har ma Umar ɗan Khaɗɗab Allah ya ƙara masa yarda ya sare bishiyar da ke Hudaibiyya wadda aka yi mubaya'a a ƙarƙashinta, lokacin da ya ga mutane suna tabarruki da ita[2].

Na uku: Tabarruki da ƙabarin Annabi (SAW), da niƙar gari zuwa ƙabarin, da abin da wasu suke aikatawa a wurin marasa kyau; kamar wanda yake roƙon sa ko neman addu'a daga gare shi, ko neman ceto, ko shafa bangon ƙabarinsa, ko sumbatar su, ko ya fuskanci ƙabarin da salla da gangan, ko ya gabatar da wasu ibadodi a wurin; kamar ƙaratun Alƙur'ani'ani, da azkar, da makamantansu, Manzon Allah (SAW), ya ce: "Ya Allah, kada Ka mai da ƙabarina gunki abin bauta"[3]. Kuma Annabi (SAW) ya ce: "Ba a niƙar gari sai zuwa masallatai uku: Masallaci mai alfarma, wannan masallacina, da Masallacin ƙudus)[4].

---

[1] Majmu'ul-Fatawa (7/454).

[2] Ibnu Abi Shaiba (7237) da Ibnu Sa'ad a cikin Aɗ-Ɗabaƙat (2/100) ne suka rawaito shi..

[3] Bukhari (435), da Muslim (530) ne suka rawaito shi.

[4] Bukhari (1189) da Muslim (1397) ne suka rawaito shi..

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

SADAƘA TA MUSTAHABBI

❖ Falalar sadaƙa:

Daga cikin kyawawan abubuwan addinin Musulunci: akwai cewa Allah Ya shar'anta sadaƙa ta Mustahabi tare da zakka ta wajiba da aka shar'anta ta a kowane lokaci, kuma tana in ganta ne ga dukkan masu hali, kuma akwai dalilai masu yawa game da falalarta da girman ladanta, daga ciki akwai:

Allah Maɗaukaki Ya ce: ((kuma in da za ku yi sadaƙa shi ya fi alheri a gare ku in kun ƙasance kuna da masaniya))[1].

Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Wane ne zai ba wa Allah kyakkyawan rance, sai Ya ninka masa shi ninki mai yawa? Kuma Allah ne Yake kame (dukiya), Yake kuma shimfiɗa ta, kuma zuwa gare Shi za a mayar da ku))[2].

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: (Sadaƙa tana goge zunubi kamar yadda ruwa yake kashe wuta)[3].

Kuma ya ce: (Babu wanda zai yi sadaƙa da ɗan ƙwayar dabino daga halaliyarsa face Allah Ya karɓe shi da hannun damansa, sannan Ya haɓaka ta ya ninka ladanta don ta nauyaya mimizani kamar yadda ɗayanku yake reno ɗan dokinsa, har sai ya zama kamar dutse mai girma)[4].

❖ Fifiko cikin Sadaka:

Sadaka a asirce ta fi falala fiye da ta bayyane; saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((In da za ku bayyanar da sadakoki a fili, to madalla da

---

[1] [Al-Baƙara: 280].
[2] [Al-Baƙara: 245].
[3] Tirmizi ne ya rawaito shi (2616).
[4] Bukhari (1410) da Muslim (1014) ne suka rawaito shi.

hakan, kuma idan kuka ɓoye sadaƙar, kuma kuka ba da ita ga talakawa, to hakan shi ya fi alheri a gare ku))[1].

kuma saboda hakan shi ya fi nesantawa daga riya, sai idan cikin bayyana sadakar akwai wata maslaha mai rinjaye, kuma mai bayar da sadakar bai tsron faɗa wa cikin riya.

Sadaka a lokacin ƙoshin lafiya tafi alheri fiye da ita a lokacin rashin lafiya, domin ya zo a Hadisi cewa lokacin da aka tambayi Annabi (SAW) cewa: “Wacce irin sadaka ce ta fi girman lada? Sai Annabi (SAW) ya ce: (Ka yi sadaka a lokacin da keke da lafiya, kake matuƙar bukatar abin sadakar, kana fatan arziki kuma kana tsoron talauci)[2].

Sadaka a lokutan da wurare masu falala tafi alheri; ya zo a Hadisi cewa: "Manzon Allah (SAW) ya ƙasance ya fi kowa yawan kyauta, kuma ya fi yawaita kyauta a watan Ramadana)[3].

Sadaka a lokutan buƙata tafi falala; Allah Maɗaukaki Ya ce (Ko kuma ciyarwa a wata rana ta yunwa () Ga maraya ma'abocin kusanci () Ko miskini ma'abocin talauci)[4].

Sadaka ga dangi da maƙwabta tafi falala fiye da sadaka ga waɗanda ba su ba; domin Allah Ya yi wasiyya game da dangi, kuma Ya sanya musu haƙƙi a kan danginsu a cikin ayoyi masu yawa; kamar faɗinsa cewa (Ka bai wa dangi makusanta haƙƙinsu)[5],

Kuma Annabi (SAW) ya ce: (Sadakarka ga miskini sadaka ce kawai, amma sadaka ga dangi makusanta abubuwa ne guda biyu: sadaka ce da kuma sada zumunci)[6].

---

[1] [Al-Baƙara: 271]

[2] Bukhari (1419), da Muslim (1032) ne suka rawaito shi.

[3] Bukhari (3220), da Muslim (2308) ne suka rawaito shi.

[4] [Al-Balad: 14-16].

[5] [Al-Isra: 26].

[6] Abu Dawud (1693) da Tirmizi (658) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTARSA (SAW)

Magana game da Alamomin Annabtarsa (SAW) za ta iya cika shafuka masu yawa da littattafai masu yalwa; domin sunnar Allah ga dukkan annabawa ita ce Ya ƙarfafa su da mu'ujizozi, ba Ya aiko wani Annabi face Ya ba shi daga cikin mu'ujizozi abin da zai tabbatar da gaskiyan saƙonsa su, kuma ya ƙalubalanci dukkan wanda ya saɓa masa da su, ya kuma nuna gaskiyarsa da su, kuma abin da malamai suka tattara cikin alamomin gaskiyar annabtar Annabinmu Muhammadu (SAW) ya haura dubu.

Kuma mafi girma daga cikinsu shi ne: (Al-ƙur'ani Mai girma), wanda ɓarna ba ba ta shiga cikinsa ta gabansa ko ta bayansa, saukakke ne daga Allah Mai hikima, Sha yabo; shi ne mafi girman mu'ujizozi, mafi banƙayen ayoyi, kuma mafi bayyanar hujjoji bayyanannu, Annabi (SAW) ya ce: (Babu wani Annabi daga cikin Annabawa face an ba shi wata mu'ujiza daga cikin mu'ujizozi da za ta sanya mutane su yi imani da ita, amma ni abin da aka ba ni shi ne wahayin da Allah Ya saukar mini, kuma ina fata in ƙasance na fi su yawan mabiya a Ƙiyama)[1].

Mu'ujizar Al-Kur'ani Mai girma ta fito ne daga ɓangaren lafazinsa, da kuma daga ɓangaren ma'anarsa:

Dangane da mu'ujizarsa daga ɓangaren ma'anarsa: Lallai ya kai maƙura wajen cika, da hikima, da rahama, da maslaha, da kyakkyawar ƙarshe, da cin m mafi ɗaukakar manufa, da rushe dukkan ɓarna, kuma yana ƙunshe da dukkan alheri da nagarta, kuma yana hani daga dukkan sharri da lalata, domin shi yana umarni ne da kaɗaita Allah, yana kuma hani daga shirka, yana umarni da gaskiya,

[1] Bukhari (7274) da Muslim (1052) ne suka rawaito shi.

yana hani daga ƙarya, yana umarni da adalci, yana hani daga zalunci, yana umarni da amana, yana hani daga ha'inci, yana umarni da cika alƙawari, yana hani daga yaudara, yana umarni da kyautata wa iyaye, yana hani daga rashin biyayya gare su, yana umarni da sada zumunci, yana hani daga yanke zumunci, yana umarni da kyautata wa maƙwabta, kuma yana hani daga munana musu.

Dangane da lafazinsa kuwa: Shi ne mafi fasahar zance, kuma dukkan wanda iliminsa ga harshen Larabci ya ƙaru, to ƙaunarsa da girmamawarsa ga Al-ƙur'ani za su ƙaru, kuma Annabi (SAW) ya ƙalubalanci dukkan masu fasahar zance a zamaninsa da wannan Al-ƙur'ani Mai girma duk da tsananin ƙiyayyarsu gare shi, da ƙoƙarinsu na ƙaryata shi ta hanyar zuwa da kwatankwacinsa, kuma ya faɗa musu cewa ba za su iya yin hakan ba har abada. Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ko kuwa suna cewa: "Ya ƙago shi?" A'a, su dai ba sa yin imani ne kawai () To su zo da wani zance irinsa idan sun ƙasance masu gaskiya))[1].

Bari dai, ya ƙalubalanci mutane da aljannu gaba ɗayansu da su kawo kwatankwacinsa, sai suka gaza, Allah Maɗaukaki Ya ce: (Ka ce da su: "Wallahi da mutane da aljannu sun haɗu kan su kawo irin wannan Alƙur'anin, to ba za su zo da irinsa ba, ko da kuwa wasu sun zamanto suna taimaka wa wasu)[2].

Sa'an nan kuma ya ƙalubalance su da su kawo surori goma makamancin nasa. Sai Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Bari dai, ko cewa suka yi: "Ya ƙirƙire shi ne?" Ka ce: "Ku kawo sura goma kamarsa ƙagaggu, kuma ku kira duk wanda za ku iya wanda ba Allah ba (ya taimake ku) in kun ƙasance masu gaskiya)[3], sai suka ƙasa yin hakan.

Sa'an nan kuma ya sake ƙalubalantar su da su zo da sura guda ɗaya

[1] [Aḍ-Ḍur: 33-34].
[2] [Al-Isra': 88].
[3] [Hud: 13].

kwatankwacin nasa, Allah Madaukaki Ya ce: (Ko kuma cewa suke yi: “Kagar sa ya yi ne?” Ka ce: “To ku kawo sura daya tal irinsa, kuma ku kirawo wanda duk za ku iya (ya taimaka muku) wanda ba Allah ba idan kun kasance masu gaskiya)[1].

Dukkan wadannan kalubalen sun faru ne a Makkah, sannan ya sake maimaita musu kalubalen a Madina, inda aka hada da kalmar «لَنْ» wadda take nufin korewa a nan gaba, domin bayyana musu cewa ba za su iya kalubalantar sa ba, a yanzu ko a gaba, sai Allah Madaukaki Ya ce a cikin Suratul-Bakara: (Kuma idan kun kasance cikin kokwanto game da abin da Muka saukar wa bawanmu, to ku zo da kwatankwacin sura daya kamarsa, kuma ku kirawo masu taimakonku ba Allah ba in kun kasance masu gaskiya () To idan har ba ku aikata hakan ba, kuma ba za ku taba iyawa ba, to ku kiyayi wata wuta wadda mutane ne da duwatsu makamashinta; an kuwa tanade ta domin kafirai)[2].

Kuma irin wannan kalubale ba ya fitowa sai daga wanda yake da tabbacin cewa abin da ya zo da shi Maganar Ubangijin Talikai ne, wanda kwata-kwata bai yi kama da maganar halittunsa ba ta kowace fuska[3].

[1] [Yunus: 38].

[2] [Al-Bakara: 23-24].

[3] Al-Bidāya wan-Nihaya (8/54).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

SALMANUL-FARISI (RA)

❖ SunanSa da Haihuwarsa:

Shi ne: Salmanul-Farisi, ana kiran sa da Abu Abdillah, asalinsa daga ƙasar Farisa yake, Sunansa kafin Musulunci shi ne: Ruzbah ɗan Buzakhshan.

❖ Rayuwarsa da Falalarsa:

Shi ne Salmanul-Khair, wanda ya fara shiga Musulunci daga cikin Farisawa, bawan Annabi (SAW) ne, sahabinsa ne kuma hadiminsa, kuma ya rawaici Hadisi daga gare shi.

Ya ƙasance Allah ya ƙara masa yarda mai tsawo ne, mai diri, mai basira, jajirtace, mai kaifin hankali, mai ra'ayi madaidaici, kuma mai yalwar ilimi game da shari'o'in litattafan da suka gabata.
Ya yi rayuwa irin ta zuhudu, yana mai gudun duniya, mai shagaltuwa da ibada, kuma ya ƙasance idan aka kawo masa rabonsa daga Baitul-mal – kimanin zinari dubu biyar – sai ya yi sadaka da shi gaba ɗaya, mutum ne mai sana'ar hannu, kuma ya kan ce: "Na kan sayi wani ƙaramin ɗaki da dirhami ɗaya, sai in gina shi, sai in sayar da shi da dirhami uku, sai in aje dirhami ɗaya don gyaransa, in kashe dirhami ɗaya ga iyalina, in kuma yi sadaka da dirhami ɗaya" [1].
Ya shahara -Allah ya ƙara masa yarda - da labarinsa na musamman wajen neman gaskiya, ta yadda ya bar addinin mutanensa na Majusanci, ya yi ta yawo a ƙasashe da dama yana neman addinin gaskiya, yana bibiyar malaman Ahlul-Kitab. Ya wahala sosai wajen tafiye-tafiye da faɗa wa hunnun mayaudara, har sai da wani ya bayyana masa cewa wani Annabi ya bayyana a ƙasar Larabawa, sai

[1] Usdul-Ghabah (2/420).

Salmanu ya nemi Banu Kalb da su kai shi ƙasar Larabawa a kan cewa zai ba su shanunsa da tumakinsa, sai suka yarda, amma suka yaudare shi, suka sayar da shi ga wani Bayahude ɗan wani gari mai sun Wadil-ƙura, sannan wani Bayahuden daga Banu Ƙuraiza ya sake sayensa, ya kuma kai shi zuwa garin Madina, yayin da Annabi (SAW) ya yi hijira zuwa gare ta, sai Salmanu ya ji labarinsa, sai ya tafi wurinsa da gaggawa, ya yi imani da shi[1].

Sa'annan bauta ta hana shi shiga yaƙin Badar da Uhud, daga baya kuwa ya ya fanshi kansa daga bauta da taimakon Annabi (SAW), sai ya samu ‘yanci.

Sai yaƙin Khandaƙ ya ƙasance shi ne yaƙin farko da ya yi tare da Annabi (SAW) inda ya shahara da ra’ayinsa na dabara kan shawarar haƙar gwalalo (Khandaƙ), daga nan ya ci gaba halartar sauran yaƙe-yaƙe tare da Annabi (SAW).

Kuma Manzon Allah (SAW) ya siffanta shi da gaskiyar imani da ƙarfinsa a lokacin da ya ɗora hannunsa wata rana a kans, ya ce: (Da imani wajen tauraron thurayya yake, da wasu mazaje daga cikin waɗannan sun same shi)[2].

Kuma a lokacin da ya kamu da rashin lafiya Allah - Ya ƙara masa yarda-, Sa‘ad ɗan Malik ya fito daga Kufa zuwa wurinsa don ya duba shi, sai ya zo ya tarar da shi cikin cutar ajali yana kuka, sai ya tambaye shi: Me ya sa kake kuka ya kai ɗan’uwana? Ashe ba ka tuna zama tare da Manzon Allah (SWA) ba? Ashe ba ka tuna ayyukan ƙwarai ba? Sai ya ce: Na rantse da Allah, ba don son duniya nake kuka ba, ko don ƙin haduwa da Allah ba, sai Sa‘ad ya ce: To, me yasa kake kuka bayan ka kai sheƙara tamanin? Sai ya ce: Abin da ya sa nake kuka shi ne, abokina kuma baɗayina ya yi mini alkawari, ya

[1] Ahmad ne ya rawaito shi (23237).
[2] Bukhari (4897), da Muslim (2546) ne suka rawaito shi

ce: “Guzurin ɗayanku a cikin wannan duniya ya ƙasance kamar guzurin matafiyi ne)) kuma muna tsoron a ce mun ƙetare iyaka)![1].

❖ Rasuwarsa:

Ya haɗu da Ubangijinsa a garin Mada’in, a lokacin halifancin Usman Allah Ya ƙara masa yarda, kuma ya kusa kai sheƙara tamanin.

[1] Ahmad ne ya rawaito shi (4385).

Auna fahimtarka a cikin darusaan Mako na 41 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma’anar "infatarat"?		a
	a. Ta tsattsage.	b. Ta zuzzube.	c. aka juyata ta
Darasin Hadisi	Tambaya: Annabi (SAW) ya bayyana cewa mumini mai kyakkyawan hali yana kai wa matsayin:		b
	a. Shahidi.	b. Mai azumi da tsayuwar dare.	c. Siddiƙai.
Darasin Aƙida	Tambaya: Daga cikin misalan tabarruki da aka haramta:		c
	a. tabarrukin Sahabbai da gashin Annabi (SAW).	b. Tabarruki da ƙaratun Alƙur’ani.	c. Tabarruki da jikin mutane ta hanyar shafa su.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin falalar sadaka akwai cewa tana:		c
	a. gogayya da laifi.	b. Rage ƙarfin laifi.	c. Kankare laifi.
Darasin Sira	Tambaya: Alamomin annabta da malaman suka tattara game da Annabinmu Muhammadu (SAW) sun haura:		c
	a. Hujjoji hamsin.	b. Hujjoji ɗari.	c. Hujjoji dubu.
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Farkon yaƙin da Salmanul-Farisi Allah Ya ƙara masa yarda ya halarta shi ne yaƙin:		b

MAKO NA ARBA'IN DA BIYU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI
SURATUT-TAKWIR (1)

﴿بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
إِذَا ٱلشَّمۡسُ كُوِّرَتۡ ١ وَإِذَا ٱلنُّجُومُ ٱنكَدَرَتۡ ٢ وَإِذَا ٱلۡجِبَالُ سُيِّرَتۡ ٣ وَإِذَا ٱلۡعِشَارُ
عُطِّلَتۡ ٤ وَإِذَا ٱلۡوُحُوشُ حُشِرَتۡ ٥ وَإِذَا ٱلۡبِحَارُ سُجِّرَتۡ ٦ وَإِذَا ٱلنُّفُوسُ زُوِّجَتۡ ٧ وَإِذَا
ٱلۡمَوۡءُۥدَةُ سُئِلَتۡ ٨ بِأَيِّ ذَنۢبٖ قُتِلَتۡ ٩ وَإِذَا ٱلصُّحُفُ نُشِرَتۡ ١٠ وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ كُشِطَتۡ ١١
وَإِذَا ٱلۡجَحِيمُ سُعِّرَتۡ ١٢ وَإِذَا ٱلۡجَنَّةُ أُزۡلِفَتۡ ١٣ عَلِمَتۡ نَفۡسٞ مَّآ أَحۡضَرَتۡ ١٤﴾

❖ **Fassara:**

1. Idan rana aka naɗe ta.
2. Idan kuma taurari suka farfaɗo.
3. Idan kuma duwatsu aka tafiyar da su.
4. Idan kuma raƙuma masu ciki aka bar su ba makiyayi.
5. Idan kuma namun daji aka tattara su.
6. Idan kuma koguna aka rura su (suka zama wuta).
7. Idan kuma rayuka aka haɗa su (da jinsinsu).
8. Idan kuma yarinyar da aka binne da rai aka tambaye ta.
9. Da wane laifi ne aka kashe ta?
10. Idan kuma takardun (ayyuka) aka baza su.
11. Idan kuma sama aka ɗaye ta.
12. Idan kuma wutar Jahimu aka hura ta.
13. Idan kuma Aljanna aka kusanto da ita.
14. To kowane rai ya san abin da ya halarto (da shi na ayyuka).

❖ Falalar Surar:

Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda yake so ya ga Ƙiyama kamar yana kallo da idonsa; to ya karanta wannan sura)[1].

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Tunatar da mutane game da tashin ƙiyama, da rikicewar halitta a cikinsa.

❖ Baƙin Kalmomi:

كُوِّرَت	Kuuwwirat	Aka nannade ta, haskenta ya dusashe.
انكدرت	Inkadarat	Ta lalace, haskenta ya ɓace.
العِشار	Al-‘ishaar	Raƙuma masu juna biyu (masu ciki).
زُوِّجَتْ	Zuwwijat	A ka haɗa su da makamantansu
المَوْؤُودَةُ	Al-Maw’ūdah	Jaririya da aka binne da ranta.
الصحف	Al-Muṣḥaf	Littafin ayyukan bayin Allah.
نُشِرَتْ	Nushirat	Aka buɗe su aka watsa su.
عُطِّلَت	Uɗɗilat	An yi watsi da su, aka wofintar da su.
حُشِرَت	Hushirat	Aka tattara su; domin a yi hisabi tsakaninsu.
سجرت	Sujjirat	Aka rura ta, ta koma wuta.
كشَطَتْ	Kushiɗat	An juyar da ita, aka cire.
سُعِّرَتْ	Su‘‘irat	Ak rura ta

[1] Tirmizi (3333) da Ahmad (4806) ne suka rawaito shi.

أُزْلِفَتْ	Uzlifat	An kusanto da ita.
أَحْضَرَتْ	Uhdirat	abin da ta gabatar na alheri ko sharri.

❖ Ma’anar Surar a Dunkule:

Suratul-Infidar tana daga cikin surori Makkiyya, ta kushi bayani game da Kiyama, da rushewar duniya bayan karfinta, da kuma abin da zai faru da sama da kasa da duwatsu da tekuna da dabbobi, domin mutane su bambanta da juna, sai a tashi mutum tare da wadanda suke aiki irin nasa: managarta tare da managarta, fajirai tare da fajirai, ta yadda kowa zai san abin da ya gabatar domin lahirarsa, da abin da ya zo da shi na alheri ko na sharri.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Tunatarwa game da Kiyama da firgicinta; domin masu hankali su wa’aztu, su kuma shirya da kyawawan ayyuka.

2) Tunatarwa game da kididdigar da Allah Madaukaki Zai yi ga ayyukan bayinsa, da rubutun mala’ikunsa ga ayyukan, da sanin kowa ga abin da ke cikin littafin sakamakon aikinsa.

3) Lallai wutar Jahannama za a kimtsa ta kuma a rura ta domin ma’abotanta, haka ita ma Aljanna za a kimtsa kuma a kusanto da ita ga ma’abotanta.

4) Lallai ratayuwar zukata da juna sababi ne na haduwarsu a lahira, kamar yadda Allah Madaukaki Ya ce: ((Idan rayuka aka hada su da jinsinsu)), kuma Annabi (SAW) ya ce: (Mutum yana tare da wanda yake so)[1].

[1] Bukhari (6168) da Muslim (2640) ne suka rawaito shi.

LITININ: DARASIN HADISI

KWAƊAITARWA GAME DA SADAKA DA MAGANA MAI DAƊI

An karɓo daga Adiyyu ɗan Hatim (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: “Babu wani daga cikinku face sai Ubangijinsa ya yi masa magana, babu wani mai fassara tsakaninsa da shi, sai ya dubi gefen damansa, ba zai ga komai ba sai abin da ya gabatar, ya dubi gefen hagunsa, ba zai ga komai ba sai abin da ya gabatar, ya dubi gabansa, ba zai ga komai ba sai wuta tana tana fuskanto shi, don haka ku tsare kanku daga wuta, ko da da rabin dabino ne, wanda kuwa bai samu hakan ba, to ya furta kyakkyawar kalma). Bukhari da Muslim suka rawaito shi[1].

❖ Sharhi

Wannan Hadisi ne mai girma wanda ya ƙunshi bayani game da girman Allah Maɗaukaki, abin da hankali ba zai iya kewayewa shi ba, kuma harsuna ba za su iya bayyana shi yadda ya kamata ba, domin haƙiƙa Annabi (SAW) ya ba da labari cewa dukkan halittu Allah Zai yi musu magana kai tsaye ba tare da fassara ko mai shiga tsakani ba, kuma Zai tambaye su game da dukkan ayyukansu, a wannan hali, bawa ba zai sami mataimaka ko masu kawo ɗauki ko dukiyoyi, ko ‘ya’ya ba, domin ya zo ne shi kaɗai kamar yadda aka halicce shi tun farko, kuma ayyukansa sun kewaye shi suna neman sakamako da alheri ko sharri, a gefensa na dama da hagu akwai ayyuka, a gabansa kuma akwai wuta da babu makawa sai ya shiga cikinta, kuma babu wata hanyar tsira daga gare ta sai da rahamar Allah, sannan da abin da hannayensa suka gabatar na ayyuka masu tseratarwa, saboda haka ne Annabi (SAW) ya umurci al’ummarsa

[1] Bukhari (6539), da Muslim (1016) ne suka rawaito shi.

da su tsare kansu daga wuta, ko da da ƙaramin abu ne; kamar mutum ya yi sadaka da rabin dabino, idan kuwa hakan bai samu ba, to ya furta kyakkyawar kalma.

❖ **Abubuwan da za a koya daga Hadisin:**

1) Tabbatar da tayar da halittu bayan mutuwa, da tsayuwar mutane a gaban Ubangijin halittu domin ya yi musu hisabi a kan ayyukansu.

2) Tabbatar da maganar da Allah Zai yi da bayinsa a ranar Alƙiyama domin titsiye da hisabi.

3) Lallai daga cikin mafiya girman abubuwan da suke tseratarwa daga wuta akwai kyautatawa ga halittu ko da da ƙaramin abu ne, kamar rabin dabino ko magana mai daɗi.

4) Lallai sadaka koda kaɗan ce tana tseratarwa daga wuta, saboda faɗin Annabi (SAW) cewa: (Ku tsare kanku daga shiga wuta ko da ta hanyar bayar da rabin dabino ne).

5) Magana mai daɗi ta ƙunshi duk wata kalma da za ta faranta rai kuma ta daɗaɗa zuciya.

6) Daga cikin magana mai daɗi akwai nasiha ga halittu ta hanyar sanar da su abin da suka jahilta, da nusantar da su ga abin da zai amfane su duniya da lahira.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

TABARRUKI DA AKA SHAR'ANTA

Tabarruki da aka shar'anta: shi ne tabarruki tabbatacce wanda aka yi umarni da shi cikin Alkur'ani da sunna.

Kuma yana da hanyoyi daban-daban masu yawa, masu tasiri da izinin Allah ga wanda ya yi riƙo da su, kuma masu amfanar sa cikin addini da arziki da lafiya da lokaci da 'ya'ya.

Shi wannan tabarruki da aka shar'anta yana da misalai masu yawa, daga ciki akwai:

Na farko: Tabarruki ta hanyar ambaton Allah Maɗaukaki, kamar yin bismillah yayin fara wasu maganganu da ayyuka, da yin salati ga Annabi (SAW), da zikirin safe da na dare, da makamantansu daga nau'ukan zikiri da suke cikin Alkur'ani da sunna, kuma suna daga cikin mafiya girman ababen da ake neman albarkarsu, kuma mai faɗarsu yake rabauta da kankare zunubai, da shiga aljanna da yaye damuwa da yawaitar arziki da zuri'a, da waraka daga cutattuka.

Na biyu: Tabarruki ta hanyar wuraren da albarkarsu ya tabbata cikin Alkur'ani da sunna cikin yanayi ingantacce, domin su wurare masu albarka, kamar masallacin Haramin Makka da masallacin Annabi (SAW) da masallacin Ƙudus sannan sauran masallatai, tabarruki da su yana kasancewa ne tahanyar salla a cikinsu, da halartar wuraren da ake karatu da karatun Alkur'ani da bitarsa da neman ilimin addini, ba wai shafar duwatsu ko ƙasa ko sinbatar tagogi da ƙofofi ba.

Tabarruki da ɗakin Ka'aba kuwa yana kasancewa ne ta hanyar ɗawafi, da fuskantar ta yayin salla da addu'a, ba wai shafar rigar da aka sanya mata ko waninsa, domin yadda abin yake shi ne ba a

shafar wani wuri wanda ba hajarul aswad da rukunul yamani ba, kamar yadda sunna ingantacciya ta tabbatar[1].

Ibnul Ƙayyim Allah ya masa rahama ya ce: "Babu wani wuri a doron ƙasa da aka shar'anta sunbatarsa da shafarsa kuma ake kankare laifuka da zunubai sai hajarul aswad da rukunul yamani"[2].

Kuma Sheikh Abdul'aziz bin Baz Allah ya masa rahama ya ce: "Neman tabarruki tahanyar shafar Muƙamu Ibrahim ko ginin Ka'aba ko rigarta duk waɗannan ababe ne da ba su halatta, kuma ba su da asali cikin shari'a kuma Annabi (SAW) bai aikata ba"[3].

Na uku: Daga cikin misalan tabarruki da aka shar'anta akwai: neman tabarruki da zamunna masu albarka waɗanda Allah Maɗaukaki ya keɓence su da wani ƙari na daraja da albarka, kamar watan Ramadana da daren lailatul ƙadari da ɗaya bisa ukun ƙarshe na dare da goman farko na watan Zulhijja, saboda haka duk wanda ya yi kirdadon aikin alheri da ibada cikinsu, to alkhairai da albarkoki masu girma za su same shi.

Na huɗu: Tabarruki da nau'ukan abinci da abin sha waɗanda dalilai na shari'a suka tabbatar da albarkarsu da amfaninsu, daga cikinsu akwai: man zaitun da zuma da ruwan zamzam da dabinon ajwa na garin Madina.

---

[1]. Bukhari (1606) da Muslim (1268) ne suka rawaito shi.
[2]. Zadul-Ma'ad (1/48).
[3]. Majm'ul-Fatawa (17/21).

LARABA: DARASIN FIƙIHU

LADUBBAN SADAKA

Sadaka tana da wasu ladubba waɗanda kiyaye su yake da muhimmanci, su ne kamar haka:

1. Sadakar ta kasance don neman yardar Allah Mai girma da buwaya, riya da son-asani bai shafe ta ba, domin ya samu ladarta mai girma, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Kuma misalin waɗanda suke ciyar da dukiyoyinsu don neman yardar Allah da tabbatar da imani a zukatansu, kamar misalin gona ce a kan jigawa sai ruwan sama mamako ya same ta, sai ta ba da amfaninta riɓi-biyu. To idan mamakon ruwan bai same ta ba, sai yayyafi ya wadatar da ita. Kuma Allah Mai ganin abin da kuke aikatawa ne)) [1].
2. Ya riƙa yawaita ciyarwa cikin fuskokin alheri da biyayya ga Allah, kuma hakan sababi ne na yawaitar dukiyarsa da ƙaruwarta, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wata rana da bayi za su wayi gari face mala'iku biyu sun sauko, sai ɗaya daga cikinsu ya ce: ya Allah ka mayar wa duk wanda ya ciyar gurbi, shi kuma ɗayan yana cewa: ya Allah ka gadar da asara ga wanda ya ƙi ciyarwa) [2].
3. Ya gaggauta yin sadakar kafin samuwar ababen da za su hana shi ba da ita, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Kuma ku ciyar daga abin da Muka arzuta ku tun kafin mutuwa ta zo wa ɗayanku sannan ya riƙa cewa: “Ya Ubangijina, me ya hana Ka saurara min zuwa wani ɗan lokaci na kusa sai in ba da gaskiya in kuma zama cikin bayi nagari)) [3].
4. Sadakar ta kasance daga dukiyar halal, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lallai Allah Maɗaukaki Mai tsarki ne ba ya karɓar aiki sai mai tsarki) [4].

---

[1]. [Al-Baƙara: 265].
[2]. Bukhari (1442) da Muslim (1010) ne suka rawaito shi
[3]. [Al-Munafiƙun: 10].
[4]. Muslim ne ya rawaito shi (1015).

5. Sadakar ta kasance daga dukiya mai kyau wacce yake so wa kansa; Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ba za ku taɓa samun Aljanna ba har sai kun ciyar daga abin da kuke so, kuma duk wani abu da za ku ciyar, to lallai Allah yana sane da shi))[1].

6. Ya nisanci girman-kai da jiji da kai, kuma kada ya riƙa ganin yawan sadakar da yake bayarwa, Allah Ya ce: ((Kada kuma ka goranta wa Ubangijinka da ganin yawan (ayyukanka na ƙwarai))[2].

7. Ya kiyayi abin da zai ɓata sadakar, kamar gori da cutarwa, Allah Ya ce: ((Ya ku waɗanda suka yi imani! Kada ku ɓata sadakokinku da gori da cutarwa, kamar wanda yake ciyar da dukiyarsa domin nuna wa mutane, kuma ba ya yin imani da Allah da Ranar Lahira))[3].

8. Ya sirranta sadakar, kuma kada ya bayyana ta sai idan akwai wata maslaha ta shari'a, Allah Maɗaukakin sarki Ya ce: (Idan kun nũna sadakõki to, yana da kyau ƙwarai kuma idan kuka ɓõye su kuma kuka je da su ga matalauta, to shi ne mafi alhẽri a gareku, kuma Yana kankarẽwa, daga barinku, daga miyãgun ayyukanku. Kuma Allah ga abin da kuke aikatawa Masani ne)[4], ya zo cikin hadisi, Annabi (SAW)ya ce: (Akwai wasu mutane bakwai da Allah zai lulluɓe su a inuwarsa a ranar da babu wata inuwa sai inuwar tasa.....) sai ya ambaci hadisin, a cikinsa akwai (Mutumin da ya yi sadaka sai ya ɓoye ta, ta yadda hannun hagunsa bai san abin da na dama ya bayar ba)[5].

---

[1]. [Alu-Imran: 92].
[2]. [Al-Muddassir: 6].
[3]. [Al-Baƙara: 264].
[4]. [Al-Baƙara: 271].
[5]. Bukhari (660), da Muslim (1031) ne suka rawaito shi

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Tashinsa da rayuwarsa (SAW)

Daga cikin alamomin gaskiyar Annabtarsa (SAW) akwai kyakkyawar tashinsa mai tsafta da tsaftataccen tarihinsa; domin haƙiƙa ya tashi a tsakanin mutanen da suka san asalinsa da rayuwarsa, da shige da fitarsa cikakken sani, bai gushe ba a wurinsu yana da shaidar gaskiya da amana, da kyautatawa da cika alkawari, da kyawawan ɗabi’u, da adalci, da kunya, da kuma zumunci, da wasu ɗabi'un na daban waɗanda ba su haɗu ga wani ba sai shi gare shi (SAW), kuma ba a taɓa saninsa da wani abu da za a iya aibanta shi da shi ba, cikin maganganunsa ko ayyukansa ko halayensa, kuma ba a taɓa samun shi da ƙarya ko zalunci ko alfasha ba.

Sannan Annabta ta ƙara masa kamala bisa kamalarsa, sai ya kasance cikin daraja mafi girma wanda masu hankali ba su taɓa ganin kamarta ba, kuma ya kasance cikin bauta ga Allah, da tsoronsa, da kira zuwa gare shi, da haƙuri kan cutarwar wanda ya saɓa masa da jure hakan, da gudun duniya, da nisantar ƙawarta, da kuma haƙuri kan jarrabawowinta.

Manzon Allah (SAW) yana cewa: (Haƙiƙa an tsoratar da ni saboda Allah, irin tsoratarwar da ba a taɓa irinsa ga wani ba, kuma haƙiƙa an cutar da ni saboda Allah irin cutarwar da ba a taɓa irinsa ga wani ba, kuma haƙiƙa kwanaki talatin sukan riske ni ban mallaki wani abinci wanda mai rai zai saka a bakinsa ba face abin da hammatar Bilal take iya ɓoyewa) [1].

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (2472).

Saboda mai hankali zai fahimci cewa wannan ba zai taɓa yin ƙarya ga mutane ba ko sau ɗaya, to ta yaya zai zo yana ɗan shekara arba'in ya yi ƙarya ga Ubangijin talikai?!

Ibnu Taymiyyah Allah ya masa rahama ya ce: "Tarihin rayuwar Manzon Allah (SAW) da ɗabi'unsa, da maganganunsa, da ayyukansa, na daga cikin alamomin annabtakarsa, wato daga cikin mu'ujizojinsa, kuma Shari'arsa na daga cikin mu'ujizojinsa, al'ummarsa daga na daga cikin mu'ujizojinsa, haka kuma ilimin al'ummarsa na daga cikin mu'ujizojinsa, kuma addininsu na daga cikin mu'ujizojinsa, kuma karamar salihan bayi cikin al'ummarsa na daga cikin mu'ujizojinsa, kuma hakan yana bayyana ne ta hanyar tuntuntini game da tarihin rayuwarsa tun daga lokacin da aka haife shi har zuwa lokacin da aka aiko shi, sannan kuma tun daga lokacin da aka aiko shi har zuwa lokacin rasuwarsa, da kuma tuntuntini game da nasabarsa da garinsa da asalinsa ƙabilarsa, domin shi ya fito ne daga mafi darajar nasaba a duniya, daga tsatson Annabi Ibrahim wanda Allah ya sanya annabta da littafi cikin zuriyarsa, babu wani Annabi da ya zo bayan Annabi Ibrahim face daga cikin zuriyarsa, kuma Allah ya ba shi 'ya'ya biyu: Isma'il da Ishaƙ, kuma an ambace wannan da wannan a cikin Attaura, kuma an yi bushara cikin Attaura game da abin da zai kasance na 'ya'yan Isma'il, amma babu wanda busharar annabta da aka yi ta bayyana a kansa sai shi kaɗai, kuma Annabi Ibrahim ya yi addu'a ga zuriyar Isma'il kan Allah ya aiko manzo daga cikinsu, sannan Manzon Allah daga Ƙuraishawa yake zaɓaɓɓun zuriyar Annabi Ibrahim, sannan daga Banu hashim zaɓaɓɓun Ƙuraishawa, kuma daga Makka uwar birane, kuma garin da ɗakin Ka'aba wanda Annabi Ibrahim ya gina shi, kuma ya kira mutane don su ziyarce shi, kuma bai gushe ba ana

ziyartarsa tun daga zamanin Annabi Ibrahim, abin da aka ambace shi cikin littafan Annabawa da mafi kyawun siffa"[1].

[1]. Al-Jawabus-Sahih li man Baddala Dinal-Masih (5/437).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI SALAMATU ɗAN AKWA'U (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Salamatu bin Amru bin Sinan Al-Aslami, ana yi masa alkunya da Baban Muslim.

An haife shi ne kafin Hijira da shekaru kaɗan.

❖ Tarihinsa da falalarsa:

Ya kasance (RA) mai yawan kyauta mai alheri mai falala, jarumi mai saurin gudu, mai iya harbi, ya yi bakancen kansa ga Musulunci, ya halarci Bai'atur ridwan, sunansa ya fito fili a yaƙin Ziƙarad, yayin da aka ɗauki raƙumin Annabi (SAW) shi kaɗai ya bayan mutanen, yana jifar su da duwatsu da kifiya har sai da ya gajiyar da su, yana mai cewa: Ni ne ɗan Ak'wa'u..... kuma yau ranar ce ta halakar da marasa albarka, sai ya kuɓutar da su daga gare su[1].

Kuma a ranar yaƙin Khaibar an yi masa rauni a ƙwabrinsa, sai ya zo wurin Annabi (SAW), sai ya masa tofi sau uku, tun daga lokacin wurin bai ƙara damun sa ba har ya koma ga Allah[2]..

Kuma ya nuna bajinta a ranar yaƙin Mu'uta, a ranar har sai da Annabi (SAW) ya faɗa game da shi cewa: (Mafi alherin mahayanmu shi ne Abu Ƙatada, mafi alherin masu yaƙi a kan ƙafafuwansu kuma shi ne Salamatu ibnul Ak'wa'u) kuma Manzon Allah (SAW) ya ba shi kason mai yaƙi a kan ƙafarsa da na mahayi[3].

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (3041).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (4206).
[3]. Ibnu Hibban ne ya rawaito shi (7175).

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu ne (RA) a garin Madina, a shekara ta 74 bayan Hijira, yana da shekara 80.

Auna fahimtarka a darussan Mako na 42			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar "Al'ishar?		b
	a. Alfadari	b. Taguwowi masu ciki	c. Doki
Darasin Hadisi	Tambaya: Duk wanda bai samu abin da zai yi sadaka da shi ba, to sai ya yi sadaka da?		c
	a. Abincin iyalansa	b. Bashi	c. Kyakkyawar magana
Darasin Aƙida	Tambaya: Neman tabarruki da abinci da ababen sha waɗanda amfaninsu ya tabbata cikin nassoshi?		a
	a. Tabarruki ne da aka shar'anta	b. Tabarruki ne da aka hana	c. Tabarruki ne makruhi
Darasin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin abin da ke ɓata sadaka akwai?		c
	a. ƙarancinta	b. Mutane su san da ita	c. Gori
Darasin Sira	Tambaya: Daga cikin alamomin annabcin Annabi Muhammad bin Abdullah (SAW) akwai:		c
	a. Musuluntar mafi kusancin Sahabbai	b. Gajartar shekarun al'ummarsa	c. Kyakkyawar tashinsa da tsaftataccen tarihinsa
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin yaƙoƙin da sunan Salamatu binul Ak'wa'u ya shahara?		b
	a. Yaƙin Zi-ƙarad	b. Ranar Zi-ƙar	c. Yaƙin Zallaƙati

MAKO NA ARBA'IN DA UKU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUT-TAKWIR (2)

﴿فَلَآ أُقۡسِمُ بِٱلۡخُنَّسِ ١٥ ٱلۡجَوَارِ ٱلۡكُنَّسِ ١٦ وَٱلَّيۡلِ إِذَا عَسۡعَسَ ١٧ وَٱلصُّبۡحِ إِذَا تَنَفَّسَ ١٨ إِنَّهُۥ لَقَوۡلُ رَسُولٖ كَرِيمٖ ١٩ ذِي قُوَّةٍ عِندَ ذِي ٱلۡعَرۡشِ مَكِينٖ ٢٠ مُّطَاعٖ ثَمَّ أَمِينٖ ٢١ وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجۡنُونٖ ٢٢ وَلَقَدۡ رَءَاهُ بِٱلۡأُفُقِ ٱلۡمُبِينِ ٢٣ وَمَا هُوَ عَلَى ٱلۡغَيۡبِ بِضَنِينٖ ٢٤ وَمَا هُوَ بِقَوۡلِ شَيۡطَٰنٖ رَّجِيمٖ ٢٥ فَأَيۡنَ تَذۡهَبُونَ ٢٦ إِنۡ هُوَ إِلَّا ذِكۡرٞ لِّلۡعَٰلَمِينَ ٢٧ لِمَن شَآءَ مِنكُمۡ أَن يَسۡتَقِيمَ ٢٨ وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٢٩﴾

❖ **Fassara:**

15. Ina rantsuwa da taurari masu ɓuya.

16. Masu gudu zuwa masaukansu.

17. Da kuma dare idan ya yi duhu.

18. Da kuma asuba idan ta keto.

19. Lalle shi Alƙur'ani magana ce ta Manzo mai karamci.

20. Ma'abocin ƙarfi a wurin Mai Al'arshi, kuma mai babban matsayi.

21. Wanda ake yi wa biyayya ne a can (sama), amintacce.

22. Mutumin naku kuma (watau Ma'aiki) ba mahaukaci ba ne.

23. Haƙiƙa kuma ya gan shi a sararin sama mabayyani.

24. Shi kuma ba mai rowa ba ne game da wahayi.

25. Kuma shi (Alƙur'ani) ba zancen Shaiɗan ne la'ananne ba.

26. To ina za ku dosa ne?

27. Shi ba wani abu ba ne sai wa’azi ga talikai.

28. Ga wanda ya ga dama daga cikinku ya bi hanya madaidaiciya.

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi

Griman Alƙur'ani Mai girma

❖ Baƙin Kalmomi

فَلَآ أُقۡسِمُ	Fala Uksimu	Ina rantsuwa/ lamun ɗin ta zo ne don ƙarfafawa
بِٱلۡخُنَّسِ	Bil-Khunnas	Taurari masu ɓoye haskensu da rana
ٱلۡجَوَارِ	Al-Jawari	Taurari masu gudu a duniyarsu
ٱلۡكُنَّسِ	Al-Kunnas	Taurari da suke ɓoye a cikin masauƙinsu
عَسۡعَسَ	As'as	Ya fuskanto da duhunsa kuma ya juya baya
تَنَفَّسَ	Tanaffas	Haskensa ya bayyana kuma ya faɗaɗa
رَسُولٍ كَرِيمٍ	Rasulin Karim	Shi ne Mala'ika Jibirilu
مَكِينٍ	Makin	Ma'aboci matsayi maɗaukaki a wurin Allah
وَلَقَدۡ رَءَاهُ	Wa laƙad Ra'ahu	Ya ga Annabinmu Muhammadu ya ga Jibirilu bisa siffarsa
ثَمَّ	Thamma	Can a sama
وَمَا صَاحِبُكُم	Wa ma Sahibukum	Shi ne Annabi Muhammadu (SAW)
بِضَنِينٍ	Bi dwanin	Marowaci game da isar da wahayi

رَّجِيمِ	Rajim	Jefaffe korarre daga rahamar Allah
فَأَيْنَ تَذْهَبُونَ	Fa aina Tazhabun	Ina hankulanku za su tafi da ku?

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule

A cikin waɗannan ayoyin Allah Maɗaukaki Yana rantsuwa da taurari yayin ɓuyarsu da gudunsu, da kuma dare yayin fuskantaowarsa, da safiya yayin hudowarta, game da cewa lallai wannan Alƙur'anin shi ne littafin Allah kuma wahayinsa, Jibirilu wanda ya siffantu da amana da ƙarfi da ɗaukakar daraja ne ya sauko da shi domin ya kasance tunatarwa ga talikai, sai Annabi Muhammadu (SAW) ya karɓe shi, kuma ya isar da shi kamar yadda aka sauke, bai kasance abin tuhuma game da hankalinsa ba kamar yadda maƙiyansa suke faɗi, bari dai, shi ne yafi kowa kaifin hankali cikin mutane, kuma bai kasance marowaci wurin isar da (Alƙur'anin) gare ku ba, tun da ba a taɓa samun wata rana da ya nemi lada ga kansa ba, kuma bai taɓa kawo wata magana da ta yi kama da maganar shaiɗanu da bokaye ba, domin daga cikin aikinsu akwai ɓarna da ɓatarwa, shi kuma ya zo ne da shiriya da haske da ayyukan alheri da kyawawan abubuwa.

Abin da za a koya daga Surar:

1) Girman Alƙur'ani mai girma, ta yadda ya kasance shi ne mafi darajar littafai, kuma mafi daraja daga cikin mala'iku ne ya sauko da shi zuwa ga mafi darajar Manzanni, a cikin mafi darajar lokuta.
2) Kuɓutar Manzo mai daraja (SAW) daga tuhume-tuhumen da mushrikai suke masa game da hankalinsa da amanarsa.
3) Falalar Jibirilu da ƙarfinsa da ɗaukakar darajarsa a kan sauran mala'iku.

4) Lallai bawa yana da zaɓi da nufi, sai dai suna bin bayan na Allah Maɗaukakin sarki ne.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

AMFANI DA DUKIYA BA TARE DA ALMUBAZZARANCI KO NUNA ƘASAITA BA

An karɓo daga Amru bin Shuaib, daga babansa daga kakansa ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: **(Ku ci kuma ku yi sadaka kuma ku sanya tufafi ba tare da almubazziranci da girman kai ba)** [1].

❖ Sharhi:

Annabi (SAW) ya kwaɗaitar a kan kiyaye dukiya, da amfani da ita, ta hanya mai kyau da Allah ya halatta, kamar ci da sanya tufafi da bayar da ita cikin ƙofofin alheri ta yadda sakamakonsa da alherinsa zai wanzu, kamar ba da sadaka ga mabuƙaci da makusanci, domin lallai Allah Maɗaukakin sarki ya sanya dukiya madogarar al'amarin bayi, da ita ne al'amuransu na musamman da na bai-ɗaya suke gudana, kuma amfaninta yana ƙanƙancewa kuma tasirinta yana gushewa idan almubazziranci da girman kai suka shiga cikinta, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Kuma ku ci ku sha kada ku almubazziranci, lallai shi ba ya son masu almubazziranci))[2], kuma Allah ya ce: (Su ne waɗanda idan suka ciyar ba sa almubazziranci kuma ba sa yin ƙwauro, ciyarwarsu kuwa ta kasance tsaka-tsaki ce))[3], kuma Allah ya ce: (Kuma kada ka yi tafiya a bayan ƙasa kana mai girman kai, lallai Allah ba ya son duk wani mai taƙama mai fariya))[4], saboda haka, wannan shi ne daidaito wurin gudanar da dukiya, domin lallai almubazziranci abu ne mai cutar da gangar jiki, ta yadda yake janyo cutuka da rashe-rashen lafiya, kuma abu ne dake lalata rayuwa, ta yadda yake gaggauto mata da talauci da fatara, shi

---

[1]. Ahmad (181) da Abu Dawuda (2559) ne suka rawaito shi.
[2]. [Al-A'raf: 31].
[3]. [Al-Furƙan: 67].
[4]. [Luƙman: 18].

kuma girman kai abu ne mai cutar da zuciya, ta yadda yake haifar mata gabar mutane, mai cutarwa ne ga lahirar mutum, ta yadda yake haifar da zunubi da uƙuba ga mutum.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) A cikin Hadisin akwai hani game da fariya da girman kai, da ɓarnata dukiya da almubazziranci.
2) Bayanin yalwar Musulunci da sauƙaƙawarsa ga mutane game da abubuwan da aka halatta.
3) Kwaɗaitarwa game da nusantar da rai da mallakar damar sarrafa sha'awarta.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

RANTSUWA DA WANIN ALLAH MAƊAUKAKI

Rantsuwa: Rantsuwa ita ce ƙarfafa wani hukunci ta hanyar ambaton abu mai girma.

Ita girmamawa hakkin Allah Maɗaukaki ce, malamai sun haɗu a kan cewa lallai rantsuwa ba ta kasancewa sai da Allah ko da sunayensa da siffofinsa, kuma sun haɗu kan cewa lallai rantsuwa da wanin Allah shirka ne, an karɓo daga ibnu Umar Allah ya ƙara musu yarda cewa lallai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya yi rantsuwa da wanin Allah, to haƙiƙa ya kafirta ko ya yi shirka)[1], kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lallai Allah ya hana ku rantsuwa da iyayenku)[2], kuma shi ɗin yana daga cikin ƙaramar shirka, sai dai idan ya kasance wanda aka rantse da shi abin girmamawa ne a wurin wanda ya yi rantsuwar ta yadda ya daidaita shi da Allah, to yin hakan babbar shirka ne, kuma wannan yana faruwa ne a wurin masu bautar ƙaburbura, domin lallai suna tsoron ma'abota ƙaburburan kuma suna girmama su fiye da tsoronsu ga Allah da girmamawrsu gare shi!

Kuma wajibi ne ga kowanne musulmi ya girmama rantsuwa da Allah da kiyaye ta, kuma kada ya yawaita yin ta, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Kuma ku kiyaye rantsuwarku))[3], kuma Allah ya ce: ((Kuma kada ka yi biyayya ga dukkan wani mai yawan rantsuwa kuma wulaƙantacce))[4], hakan ya kasance ne saboda lallai yawan rantsuwa yana nuni ne kan rena sha'anin Allah da rashin girmamawa ga sunayensa da siffofinsa, kuma hakan yana kore kamalar tauhidi, ya

---

[1]. Tirmizi (1535) da Abu Dawud (3251) ne suka rawaito shi.
[2]. Bukhari (1646) da Muslim (6647) ne suka rawaito shi.
[3]. [Al-Ma'ida: 89].
[4]. [Al-ƙalam: 10].

zo cikin hadisi cewa lallai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Mutane uku Allah ba zai yi musu magana ba, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma suna da azaba mai raɗaɗi.....) cikinsu akwai: (Mutumin da ya sanya Allah ya zamto jarinsa, ba ya saya sai da rantsuwarsa kuma ba ya sayarwa sai da rantsuwarsa) [1].

Kuma haramun ne a yi rantsuwa da Allah bisa ƙarya, kuma wannan ita ce rantsuwa mai dulmiyarwa, an kira ta da wannan suna ne saboda tana dulmiyar da ma'abocinta cikin zunubi sannan cikin wuta, kuma tana daga cikin manyan zunubai, saboda a lokacin da aka tambaya Annabi (SAW) cewa; mene ne manyan zunubai? Ya ce: (Haɗa Allah da wani cikin bauta) aka ce: sannan sai me? Ya ce: (Saɓa wa iyaye) aka ce: sannan sai me? Ya ce: (Rantsuwa mai dilmiyarwa) [2].

Kuma haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya sanya ta daga cikin siffofin munafukai, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Kuma suna yin rantsuwa a kan ƙarya alhali suna sane)) [3].

❖ **Za a iya taƙaita abin da ya gabata cikin abubuwa masu zuwa:**

1. Haramcin rantsuwa da wanin Allah Maɗaukaki, kamar rantsuwa da amana ko alƙawari ko Ka'aba ko Annabi, kuma lallai hakan yana daga cikin shirka.

2. Haramcin rantsuwa da Allah bisa ƙarya da ganganci, wato rantsuwa mai dulmiyarwa.
3. Ƙyamatar yawan rantsuwa da Allah ba tare da buƙata ba ko da a kan gaskiya ne.
4. Halascin rantsuwa da Allah bisa gaskiya yayin buƙata.

---

[1]. Ɗabarani ne ya rawaito shi (6111).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (6920).
[3]. [Al-Mujadila: 18].

LARABA: DARASI CIKIN FIƙIHU

AZUMI

Daga cikin hikimar Allah Maɗaukaki da rahamarsa ga bayinsa akwai cewa Ya farlanta musu wasu daga cikin ibadodi waɗanda akwai gyaruwarsu da maslaharsu na addininsu da duniyarsu a ciki, sannan Ya sanya musu nafilfili waɗanda suke kama da farillan, domin samun ƙarin lada a gare su, da kuma ɗinke ɓarakar da aka samu cikin farilla, domin lallai farillai na salla da zakka da azumi ana cika su ne da nafilfilunsu ranar Alƙiyama.

❖ Falalolin Azumi:

Falalolin azumi da girman ladansa ya tabbata cikin nassoshi masu yawa, daga cikin akwai:

- Faɗin Annabi (SAW) cewa: (A cikin Aljanna akwai ƙofofi guda takwas, cikinsu akwai ƙofar da ake kira Arrayyan, babu mai shigar ta sai masu azumi) [1].
- Da kuma faɗinsa (SAW) cewa: (Allah Maɗaukaki ya ce: Dukkan aikin ɗan-adam nasa ne ban da azumi, domin lallai shi nawa ne kuma ni ne zan ba da sakamakonsa, kuma warin bakin mai azumi ya fi turaren miski a wurin Allah) [2].

❖ Hikimar shar'anta Azumi:

Allah Mai girma da buyawa Ya shar'anta azumi saboda hikama mai girma wacce hankali ba zai iya kewaye ta ba, daga ciki akwai:

1. Lallai azumi tsani ne mai girma na samun tsoron Allah Mai girma da buwaya, wanda yana daga cikin mafi girman matakan

[1]. Bukhari (3257) da Muslim (1152) ne suka rawaito shi.
[2]. Bukhari (1894) da Muslim (1151) ne suka rawaito shi.

addini, da shi ne mumini yake samun rabautar duniya da lahira, Allah Maɗaukakin sarki yace: ((Ya ku waɗanda kuka yi imani, an wajabta muku azumi kamar yadda aka wajabta wa waɗanda suke gabaninku, don ku samu taƙawa))[1].

2. Lallai azumi babbar makaranta ce wacce mumini ke samun horo bisa kyawawan ɗabi'u, da tsarkake zuciya da tsarkake ta daga abin da ta rataya da shi na morewar rayuwa da laifukanta, domin neman yardar Allah Maɗaukaki.

3. Lallai cikinsa akwai hutu ga hanji mai narkar da abinci, yana samun hutu daga ƙoshi, da aiki akai-akai, da samun sukuni, sai ya sabunta aikinsa da ƙarfinsa, kuma ya fitar da abubuwa marasa amfani da abincin da bai narke ba.

4. Lallai azumi yana ƙara wa mutum tausayi da jinƙai, sai yunwar da yake ji ya riƙa sa shi kyautata wa 'yan-uwansa daga cikin talakawa da mabuƙata.

5. Lallai mumini yana tunawa da ni'imar halatta masa abincin tsawon shekara sakamakon kamewa daga cikin abinci da yake yi na lokaci ƙayyadajje, sai ya riƙa yawaita godiya ga Ubangijinsa.

6. Lallai azumi yana taƙure hanyoyin shaiɗan wanda yake kaikomo a jikin ɗan-adam irin yadda jini yake yi, kuma ya tunkuɗa shi cikin zunubai da saɓo.

7. Lallai azumi yana daga cikin nau'ukan yaƙar zuciya, domin yana taimakawa wurin tursasa ta da rage mata kaifin sha'awa, da daƙile ababen da suke haifar da son rai da yaƙar tunzirin shaiɗan.

[1]. [Al-Baƙara: 183].

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Amsa addu'arsa (SAW):

Karɓar addu'arsa yana daga cikin alamomin gaskiyar annabtakarsa (SAW), da hujjoji kan gaskiyarsa, saboda kasancewarsa dalili ƙara da ke nuni a kan ɗaukakar matsayinsa a wurin Ubangijinsa, da inganci abin da yake isarwa daga gare shi, kuma haƙiƙa hakan ya faru a wurare da ambatonsu zai ci lokaci kuma iyakance su zai yi wuya, daga cikin haka akwai:

- Abin da ya faru a kan hanyarsa ta hijira, an karɓo daga Abubakar (RA) ya ce: Suraƙa bin Malik ya bi sawunmu, sai na ce: An cimma mana ya ma'aikin Allah! Sai Manzon Allah (SAW) ya ce: kada ka yi baƙin-ciki, lallai Allah yana tare damu, sai Annabi (SAW) ya yi mummuman addu'a ga Suraƙan , sai dokinsa ya jefo shi ƙasa, sai ya ce: (Lallai ina ganin kun yi mini mummunar addu'a, don haka ku yi mini addu'a, ina muku alkawarin cewa zan mayar da duk wanda yake bin sawunku, sai Annabi ya masa addu'a ya kuɓuta, sai ya zamto duk wanda ya haɗu da shi yana mayar da shi, yana cewa: an riga an gama muku da wannan ɓangaren) [1].
- Shiriyar mahaifiyar Abu Huraira Allah ya ƙara musu yarda ta hanyar addu'arsa, an karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Na kasance ina kiran mahaifiyata zuwa ga Musulunci lokacin tana mushrika, wata rana na kira ta zuwa ga Musulunci, sai ta faɗi abin da ya ɓata min rai a kan Manzon Allah (SAW), sai na zo wurin Manzon Allah (SAW) ina kuka, sai na ce: ya Manzon Allah, lallai na kasance ina kiran mahaifiyata zuwa ga Musulunci tana ƙi, yau da na kira ta sai ta faɗa min abin da ya ɓata min rai a kanka, saboda haka ka roƙi Allah ya shiryar da mahaifiyar Abu Huraira, sai

[1]. Bukhari (3615) da Muslim (2009) ne suka rawaito shi.

Manzon Allah (SAW) ya ce: Ya Allah ka shiryar da mahaifiyar Abu Huraira. Sai na fita ina mai fatan alheri game da addu'ar Annabin Allah (SAW), yayin da isa ƙofa, sai mahaifiyar tawa ta ji ƙaran tafiyata sai ta ce: Tsaya a inda kake ya kai Abu Huraira, sai ta yi wanka kuma ta sanya rigarta, ta yi sauri ta sanya mayafinta, sai ta buɗe ƙofa, sannan ta ce: ya kai Abu Huraira, lallai ni ina shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, kuma Annabi Muhammadu bawansa ne kuma Manzonsa! Sai na dawo wurin Manzon Allah ina kuka saboda farin ciki, na ce: Ya Manzon Allah, albishirinka, haƙiƙa Allah ya karɓi addu'arka kuma ya shiryar da mahaifiyar Abu Huaraira! Sai ya gode wa Allah kuma ya yabe shi[1].

- Abin da Jabir (RA) ya rawaito inda ya ce: Na yi yaƙi tare da Manzon Allah (SAW), ina kan raƙumi wanda ya gaji, har ba ya iya tafiya, sai Manzon Allah ya ce da ni: Me ya samu raƙuminka? Sai na ce: gajiya ya yi, sai Manzon Allah ya sauka ya zaburar da shi kuma ya masa addu'a, sai ga shi ya shiga gaban sauran raƙuma, sai ya ce: Ya ka ga raƙumin naka? Na ce: Ya samu lafiya, haƙiƙa albarkar addu'arka ta shafe shi[2].
- Addu'arsa lokacin roƙon ruwa yayin da mutane suka shiga fari, sai suka zo wurinsa yana huɗuba ranar juma'a, suka ce: Ya Manzon Allah, ruwa ya yanke, bishiyoyi sun bushe kuma dabbobi sun halaka, saboda haka ka roƙa mana Allah ya shayar da mu, sain ya ce: Ya Allah ka shayar da mu! sau biyu yan faɗin haka, ina rantsuwa da Allah, a lokacin babu wani girgije a sama, sai girgije ya haɗu aka yi ruwa, sai ya sauka daga kan mimbarin ya yi salla, bayan ya idar, ruwa bai gushe ba yana sauka har sai da juma'a ta zagayo, yayin Annabi (SAW) ya tashi zai yi huɗuba, sai suka yi masa magana cewa: Gidaje sun rurrushe kuma hanyoyi sun yayyanke, don haka ka roƙi Allah ya tsayar da ruwan haka, sai Annabi (SAW) ya yi murmushi, sannan ya ce: Ya Allah a kai shi gefen gari ga ba a kanmu

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2491).
[2]. Bukhari (2967) da Muslim (715) ne suka rawaito shi.

ba, sai Madina ta bushe, sai aka fara ruwa gefenta amma cikin Madina babu ko ɗigon ruwa.

- Abul-Abbas Al-ƙurɗubiy ya ce: "Wannan yana daga cikin wani ɓangare na addu'o'in Annabi (SAW) waɗanda aka amsa su cikin gaggawa, kuma suna da yawan da sun wuce a ƙididdige su, idan ka ka haɗa su suna tabbatar da cewa lallai Allah Maɗaukaki ya karrama Annabi Muhammadu (SAW) ta hanyar amsa addu'arsa, kuma ya taimake shi cikin buƙatunsa masu yawa, kuma wannan dukkansa yana nuni ne game da matsayinsa da gaskiyar manzncinsa[1].

[1]. Al-Mufhim (6/68).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI – UBADATA ƊAN SAMIT (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Ubbadata ɗan Samit ɗan Ƙais Alkhazraji mutumin Madina.

An haife shi a Madina a shekara ta 37 kafin hijira.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Ya kasance daga cikin mafi darajar mutanen Madina, dogo mai jiki kyakkyawa, mai iya magana mai fasaha, mai tsayuwa kan gaskiya, ba ya tsoron zargin mai zargi game addini.

Ya halarci mubaya'ar Bai'atul-Aƙba ta farko da na biyu, kuma ya kasance ɗaya daga cikin jagorori a lokacin[1], kamar yadda ya halacci yaƙin Badar da Uhudu da sauran dukkanin yaƙoƙi tare da Manzon Allah (saw), kuma Annabi ya naɗa a matsayin tattara zakka sannan sai ya nemi uzuri saboda takatsantsan, sai Annabi (SAW) ya sauwaƙe masa[2].

Ya kasance daga cikin mahaddata Alƙur'ani, Muhammad bin Ka'ab alƙuraziy ya ce: "Mutum biyar da suka haddace Alƙur'ani daga cikin mutanen Madina a lokacin Annabi (SAW)su ne: "Mu'azu da Ubbadatu da Ubayyu da Abu Ayyuba da Abud-Darda'i"[3].

Kuma Yazidu bin Abu Sufyan wata rana ya rubuta zuwa ga Umar (RA) cewa: "Lallai mutanen Sham sun yawaita kuma sun cika garuruwa, kuma suna buƙatar wanda zai karantar da su Alƙur'ani kuma ya fahimtar da su, don haka ka taimaka min da wasu mutane da za su karantar da su" sai Umar ya aika masa Mu'azu bin Jabal da Ubbadatu binus Samit da Abud-Darda'i[4], sai Ubbadatu (RA) ya tafi

---

[1]. Bukhari (7056) da Muslim (1706) da Ahmad (22774) ne suka rawaito shi.
[2]. Ibnu Hibban ne ya rawaito shi (3270).
[3]. Siyaru A'lamin-Nubala (6/2).
[4]. Siyaru A'lamin-Nubala (6/2).

a matsayin malami mai bada fatawa kuma alƙali, kuma ya zauna baitul maƙadis, sai ya kasance alƙali na farko Falasɗinu.

Kamar yadda kuma ya kasance daga cikin waɗanda suka yi tarayya wurin buɗe Laziƙiyya da Jabala da Ƙuburus, kuma ɗaya ne daga cikin kwamandojin buɗe Iskandariya, kuma kwamandan tawagar da Amru binul Asi ya aika zuwa wurin Maƙauƙas, kuma ya tsorata saboda yanayinsa da ƙarfinsa.

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu a garin Ramla a shekara ta 34 bayan hijira, yana ɗan shekara 72, kuma aka birne shi baitul maƙadis.

Auna fahimtarka a darussan Mako na 43			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Me ake nufi da "Alkhunnas"?**		a
	a. Taurarin da haskensu yake ɓuya da rana	b. Masauƙin rana da wata	c. Kakar huɗa da shuka
Darasin Hadisi	**Tambaya: Me ake nufi "makhila" cikin hadisin?**		c
	a. Almubazziranci	b. Laifuka	c. Girman kai
Darasin Aƙida	**Tambaya: Rantsuwa da Allah a kan ƙarya ana kiransa?**		c
	a. Ƙage	b. Ƙirƙirar ƙarya	c. Rantsuwa mai dilmiyarwa
Darasin Fiƙihu	**Tambaya: Daga hikimomi masu girma da Allah ya shar'anta azumi saboda su akwai cewa:**		c
	a. Lallai yana ba da hutu ga hanji mai narkarwa	b. Yana horar da jiki a kan tsayuwar dare	c. Yana taimakawa a kan karatun Alkur'ani
Darasin Sira	**Tambaya: Sahabin da raƙumi ya samu albarkar Annabi (SAW) shi ne:**		b
	a. Anas bin Malik	b. Jabir bin Abdullah	c. Abu Ɗalha
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Ubadatu binus Samit (RA) ya kasance farkon alƙali a ƙasar?**		c
	a. Madina	b. Misra	c. Falasɗinu

MAKO NA ARBA'IN DA HUDU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATU ABASA (1)

﴿عَبَسَ وَتَوَلَّىٰٓ ۝١ أَن جَآءَهُ ٱلۡأَعۡمَىٰ ۝٢ وَمَا يُدۡرِيكَ لَعَلَّهُۥ يَزَّكَّىٰٓ ۝٣ أَوۡ يَذَّكَّرُ فَتَنفَعَهُ ٱلذِّكۡرَىٰٓ ۝٤ أَمَّا مَنِ ٱسۡتَغۡنَىٰ ۝٥ فَأَنتَ لَهُۥ تَصَدَّىٰ ۝٦ وَمَا عَلَيۡكَ أَلَّا يَزَّكَّىٰ ۝٧ وَأَمَّا مَن جَآءَكَ يَسۡعَىٰ ۝٨ وَهُوَ يَخۡشَىٰ ۝٩ فَأَنتَ عَنۡهُ تَلَهَّىٰ ۝١٠ كَلَّآ إِنَّهَا تَذۡكِرَةٞ ۝١١ فَمَن شَآءَ ذَكَرَهُۥ ۝١٢ فِي صُحُفٖ مُّكَرَّمَةٖ ۝١٣ مَّرۡفُوعَةٖ مُّطَهَّرَةِۭ ۝١٤ بِأَيۡدِي سَفَرَةٖ ۝١٥ كِرَامِۭ بَرَرَةٖ ۝١٦ قُتِلَ ٱلۡإِنسَٰنُ مَآ أَكۡفَرَهُۥ ۝١٧ مِنۡ أَيِّ شَيۡءٍ خَلَقَهُۥ ۝١٨ مِن نُّطۡفَةٍ خَلَقَهُۥ فَقَدَّرَهُۥ ۝١٩ ثُمَّ ٱلسَّبِيلَ يَسَّرَهُۥ ۝٢٠ ثُمَّ أَمَاتَهُۥ فَأَقۡبَرَهُۥ ۝٢١ ثُمَّ إِذَا شَآءَ أَنشَرَهُۥ ۝٢٢ كَلَّا لَمَّا يَقۡضِ مَآ أَمَرَهُۥ ۝٢٣﴾

❖ **Fassara:**

1. Ya ɗaure fuska, ya kuma ba da baya.
2. Don makaho ya zo masa.
3. Me kuma zai sanar da kai cewa watakila shi ne zai tsarkaka?
4. Ko ya wa’azantu, sai wa’azin ya amfane shi?
5. Amma wanda ya wadatu daga wa’azinka.
6. To kai shi kake fuskanta.
7. Babu kuwa komai a kanka don ya ki ya tsarkaka.
8. Amma kuma wanda ya zo maka yana sauri.
9. Alhali kuma shi yana tsoron Allah.
10. To kai shi kake kawar wa da kai.
11. Abin ba haka yake ba, lalle wannan da'awar wa’azi ne.
12. Don haka wanda ya ga dama ya wa’azantu.
13. Wannan Alkur'ani yana cikin takardu ababan girmamawa.
14. Maɗaukaka, tsarkaka.
15. A hannayen jakadu mala’iku.
16. Manya masu biyayya.
17. An la’anci mutum, me ya kai tsananin kafircinsa!
18. Shin daga wane abu ne Allah Ya halicce shi?

19. Daga maniyyi ne Ya halicce shi, sannan Ya ƙaddara shi matakai a halitta.
20. Sannan tafarki na rayuwa Ya hore masa shi.
21. Sannan Ya kashe shi, sai Ya sa shi cikin ƙabarinsa.
22. Sannan in Ya ga dama Ya tashe shi.
23. Fafau (zaton mutum) ba haka ne ba, har yanzu bai aikata abin da (Allah) Ya umarce shi ba.

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Tunatar da kafirai waɗanda suka wadata daga Ubangijinsu game da hujjojin tayar da matattu.

❖ Bakin kalmomi:

عَبَسَ	Abasa	Ya ɗaure fuska
وَتَوَلَّىٰٓ	Wa tawalla	Ya kawar da kai
يَزَّكَّىٰٓ	Yazzaka	Zai tsarkaka daga zunubansa
تَصَدَّىٰ	Tasadda	Kake fuskantarsa
تَلَهَّىٰ	Talahha	Kake shagaltuwa
كَلَّآ	Kalla	Al'amarin ba kamar yadda ka aikata ba ne
سَفَرَةٍ	Safarah	Mala'iku masu rubutu, suna kaikomo tsakanin Allah da halittunsa
بَرَرَةٍ	Bararah	Masu biyayya ga Allah ba sa saɓa masa
قُتِلَ ٱلْإِنسَٰنُ	Kutilal-Insanu	An wa kafiri kuma an azabtar da shi
مَآ أَكْفَرَهُۥ	Ma Akfarah	Yi mamakin tsananin kafircinsa!

نُّطۡفَةٍ	Nudfatin	Wani ruwa dan kadan wulakantacce, wato maniyyi
فَقَدَّرَهُۥ	Fa ƙaddarah	Ya halicce shi a matakai
ٱلسَّبِيلَ يَسَّرَهُۥ	As-Sabila yassarah	Ya bayyana masa hanyar alheri da na sharri.
كَلَّا لَمَّا يَقۡضِ مَآ أَمَرَهُۥ	Kalla lamma Yaƙdi ma amarah	Bai aikata abin da Allah Ya umarce shi ba

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

An budɗe wannan surar da gyara daga cikin tausasawa ga Manzon Allah (SAW) lokacin da ya kawar da kai daga Abdullahi ɗan Ummu maktum makaho, shi ɗaya ne daga cikin muhajirai, ya zo yana neman a yi masa nasiha da tunatarwa, sai ya katse zance Annabi (SAW) da da'awar da yake yi wa manyan ƙuraishawa, sai Allah ya ci gyaran Annabinsa (SAW) bisa shagaltuwarsa da mushrikan marasa buƙata, saboda shi wannan Alƙur'anin tunatarwa ne ga dukkan mutane, don haka bai dace a fifita wani a kan wani ba, sannan sai Allah ya ƙara razanar da mushrikai masu girman kai, da kuma tunatar da su asalin halittarsu, da yadda aka samar da kowannensu daga gudan maniyyi sannan gudan jini sannan gudan tsoka, sannan ya tanadar masa wanda zai birne shi bayan mutuwarsa saboda kada ya yi wari ya lalace, sannan ya tayar da shi domin yin hisabi da tashi bayan mutuwa, alhali bai aikata umarnin da Allah ya masa ba kuma bai ba da haƙƙoƙinsa ba!

Abin da za a koya daga Surar:

1) Amanar Manzon Allah (SAW) wurin isar da saƙo, da rashin ɓoyewa wani abu na wahayi, koda a cikinsa akwai zargi gare shi.
2) Wajibcin ba da muhimmanci ga mai neman ilimi da mai neman shiriya.
3) Cikin amfani da lafazin makaho a Alƙur'ani akwai tunatarwa game da kulawa da masu rauni da masu buƙata ta musamman.
4) Bayanin gazawar mutum game da sauke haƙƙi Ubangijinsa, koda ya bauta masa tsawon rayuwarsa.
5) Lallai talaka da mai rauni sun alheri sama da wasunsu, idan sun fi yawan taƙawa da kwaɗayi a kan Musulunci.
6) Kyautatawar Allah ga mamaci da darajta shi ta hanyar birne su, saɓanin sauran dabbobi waɗanda suke zama mushe a bayan ƙasa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

HAƘƘIN MUSULMI A KAN MUSULMI

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: **(Haƙƙin musulmi a kan musulmi guda shida ne: Idan ka haɗu da shi ka yi masa sallama, idan ya kira ka ka amsa, idan ya nemi ka yi masa nasiha, ka yi masa, idan ya yi atishawa ya gode wa Allah, to ka gaishe shi, idan ya yi rashin lafiya, ka yi masa dubiya, kuma idan ya mutu, ka raka gawarsa)** [1].

❖ Sharhi:

Musulunci addini ne soyayya da ƙauna da 'yan'uwantaka, yana kwaɗaitarwa game da su, kuma ya shar'anta sabubban da suke tabbatar da su, daga cikin mafiya muhimmancin waɗannan sabbuban akwai: Aikata wajiban haƙƙoƙin zamantakewa tsakanin musulmi, su ne kamar haka:

Na farko: (Idan ka haɗu da ka yi masa sallama), ita sallama tana daga cikin kyawawan ɗabi'u na Musulunci da ladubbansa masu kyau, domin kowanne ɗaya daga cikin mutum biyu da suka haɗu yana addu'ar kuɓuta daga sharrori ga ɗan-uwansa, da kuma samun rahama da albarkar da samar da dukkan alheri, sababi ne na soyayyar da take wajabta Imani, wanda sababi ne na shiga Aljanna.

Na biyu: (Idan ya kira ka, ka amsa masa), wato idan ya kira ka zuwa cin abinci ko shan abin sha, to ka daɗaɗa masa kuma ka amsa masa, matuƙar babu shan wahala cikin hakan, kamar ya kasance sai bulaguro mai nisa kafin a kai gare shi, ko akwai saɓon Allah a wurin, kamar ababen ƙi bayyanannu.

Na uku: (Idan ya nemi ka yi masa nasiha, to ka yi masa), domin lallai nasiha ga musulmi abu ne da aka shar'anta, kuma yana ƙara ƙarfi idan ya nemi ka yi masa nasiha da kansa kuma ya nema shawara mai amfani daga gare ka game da aikata wani aiki ko barin

[1]. Muslim (2162) ne ya rawaito shi.

wani aiki, ko mu'amala da wani daga cikin mutane, ko aurar masa ko aura daga gare shi, a irin wannan hali, dole ne ka yi masa nasiha da irin abin da kake so wa kanka, kuma ka ba shi shawara irin yadda za ka yi wa kanka.

Na huɗu: (Idan ya yi atishawa ya gode wa Allah, to ka gaishe shi), saboda lallai atishawa ni'ima ce daga Allah Maɗaukaki, ta yadda hayaƙin da ya toshe zai samu wurin fita don mai atishawar ya samu hutu, don haka sai aka shar'anta masa gode wa Allah bisa wannan ni'imar, kuma an shar'anta wa ɗan-uwansa ya ce da shi: "Yarhamukallah", kuma an umarce shi ya amsa masa da cewa: "Yahdikumu-llahu wa yuslihu balakum". Wanda kuma ya yi atishawa amma bai gode wa Allah ba, to bai cancanci a gaishe shi ba, kuma haƙiƙa ya sarayar wa kansa ni'imomi guda biyu: ni'imar godiyar Allah Maɗaukaki da ni'imar addu'ar ɗan-uwansa gare shi!

Na biyar: (Idan ya yi rashin lafiya, ka yi masa dubiya), ita dubiyar marar lafiya tana daga cikin haƙƙoƙin musulmi, musamman wanda yake da haƙƙi mai ƙarfi, kamar makusanci da aboki da makamantansu, domin ita dubiyar tana sanya nutsuwa a zuciyarsa kuma ta mantar da shi zafin ciwonsa, kuma mai aikata ta zai samu lada mai girma, Manzon Allah (SAW)ya ce: (Wanda ya je dubiyar marar lafiya ba zai gushe ba yana cikin kayan marmarin Aljanna)[1], kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wani mutum musulmi da zai je dubiyar musulmi da safe, face mala'iku dubu saba'in sun yi masa addu'a har sai ya wuni, idan kuma ya je duba shi da mareci, to mala'iku dubu saba'in za su yi masa addu'a har sai ya wayi gari) [2], kuma ya kamata ya yi wa marar lafiyar addu'a kuma ya yaɗebe masa kewa kuma ya yi masa albishir, kuma kada ya tsawaita zama a wurinsa.

Na shida: (kuma idan ya mutu, ka raka gawarsa), domin lallai cikin rakiyar gawa akwai tsayar da haƙƙin Allah Maɗaukaki, da haƙƙin mamaci da kuma haƙƙin makusantan mamacin, kuma haƙiƙa Allah

[1]. Muslim (2568) ne ya rawaito shi.
[2]. Tirmizi (969) ne ya rawaito shi.

Ya sanya lada mai girma a cikinsa, saboda darajar musulmi a wurin Allah Maɗaukaki, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya yi wa gawa salla, to yana da lada kwatankwacin ƙiraɗi ɗaya, idan ya halarci birne shi kuwa, to yana da lada kwatankwacin ƙiraɗi biyu, ƙiraɗi ɗaya ya kai girman dutsen Uhudu) [1].

[1]. Bukhari (47) da Muslim (946) suka rawaito shi.

TALATA: DARASI CIKIN AKIDA

HUKUNCIN YI WA ADDINI IZGILI

Izgili ga addini fita ne daga Musulunci, kuma fita ne daga addini gaba-ɗaya, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Idan da za ka tambaye su da sannu za su ce ai kawai mun kasance kutsawa ne kuma muna wasa, ka ce shin da Allah da ayoyinsa da manzonsa kuke izgili? To kada ku ba da hanzari haƙiƙa kun kafirta bayan imaninku))[1], kuma Allah Maɗaukaki ya faɗa dangane da mushrikai cewa: ((Idan suka gan ka ba komai suke ɗaukar ka ba face abin izgili (suna cewa) shin wannan shi ne wanda Allah ya aiko a matsayin manzo))[2].

Sa'adi Allah ya masa rahama ya ce: "lallai izgili ga Allah da Manzonsa (SAW) kafirci ne da yake fitar da mutum daga addini, domin tushen addini an gina shi ne a kan girmama Allah, da girmama addininsa da Manzonsa, izgili ga wani abu daga cikin waɗannan abubuwan kuwa yana kore wannan tushen kuma yana warware shi matuƙar warwarewa"[3].

Sai wannan ya yi nuni da cewa lallai kowane daga cikin izgili ga Allah ko ga Manzonsa ko da ayoyinsa kafirci ne, sawa'un izgilin ya kasance a zahiri ne ko ba a zahiri ba.

Shi izgili na zahiri: Shi ne cin fuska da aka bayyana, kamar aikin waɗanda ayar ta sauka a kansu a yaƙin Tabuka, yayin da sashensu suka ce: "Ba mu taɓa ganin irin waɗannan makarantar namu ba, masu haɗama da ƙarya kuma matsorata yayin karo da abokan gaba", suna nufin Manzon Allah (SAW) da sahabbansa makaranta, sai Auf bin Malik ya ce da shi: ƙarya kake yi, kawai dai kai munafiki ne! Kuma wallahi sai na ba da labari wa Manzon Allah (saw), sai Auf ya tafi wurin Manzon Allah (SAW) don ya ba shi labari, sai ya tarar Alƙur'ani ya riga shi, sai wannan mutumin ya zo wurin Manzon

---

1. [At-Taubah: 65-66].
2. [Al-Furkan: 41].
3. Taisirul-Karimir-Rahman (342).

Allah (SAW) bayan ya yi doguwar tafiya bisa taguwarsa, ya ce: ya Manzon Allah, mun kawai muna kutsawa cikin zance da tattaunawa irin ta wanda ya hau abin hawa ne, don rage wahalar hanya. Sai Manzon Allah (SAW) ya ce masa: (Shin yanzu ga Allah da ayoyinsa da Manzonsa kuka kasance kuna yin izgili?!), bai waiwaye shi ba kuma bai masa ƙari a kan haka ba[1].

Kuma daga cikin irin waɗannan akwai waɗanda suke cewa: Lallai Musulunci bai dace da wannan zamanin ba, kawai ya dace ne da zamunnan tsaka-tsakiya, ko kuma shi Musuluncin cibaya ne da komawa baya, ko kuma akwai tsanani da rashin tausayi a cikinsa, da makamantan waɗannan maganganu waɗanda dukkaninsu zagi ne ga addini da ma'abotanta, kuma izgili ne ga ingantacciyar aƙida.

Izgilin da ba na zahiri ba kuwa: Shi kamar kogi ne mara gaɓa, misalinsa kuwa shi ne kamar yin wata alama da ido, da fitar da harce da zunɓuro leɓe da yafice yayin karanta littafin Allah ko sunnar Manzon Allah (saw), ko yin izgili ga wanda ya yi riƙo da wata sunna daga cikin sunnonin Manzon Allah (saw), da izgili ga shigar da ya yi ko maganarsa ko nasiharsa, da makamantan haka daga cikin ayyukan masu izgili.

[1]. Tafsirud-Dabari (14/333).

LARABA: DARASI CIKIN FAIƘIHU

KWANAKIN DA AKE SO A RIƘA AZUMTARSU

Akwai wasu kwanaki masu daraja waɗanda shari'ah ta kwaɗaitar game da ribatarsu ta hanyar azumi, kuma akwai lada da sakamako mai yawa cikin haka, daga cikinsu akwai:

1. Azumin kwanaki shida na watan Shawwal, Manzon Allah (SAW)ya ce: (Duk wanda ya azumci watan Ramadana sannan ya bi bayansu da kwana shida na Shawwal, to ya kasance kamar azumin shekara ne) [1].
2. Azumin ranar Arfa, Manzon Allah (SAW)ya ce: (Azumin ranar Arfa ina sa ran Allah yana kankare zunubin shekarar da ta gabata da shekarar da ta biyo bayanta) [2].
3. Azumin ranar Ashura, Annabi (SAW) ya faɗa dangane da shi cewa: (Ina tsammanin cewa Allah yana kankare zunuban shekarar da ta gabace shi) [3], kuma mustahabbi ne azumtar kwana ɗaya gabaninsa ko kwana ɗaya bayansa, saboda faɗar Annabi (SAW) cewa: (Idan Allah ya kai rayuwata shekara mai zuwa, to lallai zan azumci ranar tara ga wata) [4], da faɗarsa: (Ku azumci kwana ɗaya gabaninsa ko kwana ɗaya bayansa, ku saɓa wa yahudawa) [5].
4. Azumin litinin da alhamis na kowane sati, saboda Hadisin A'isha Allah ya ƙara mata yarda cewa: "Annabi (SAW) ya kasance yana kirdadon azumin litinin da alhamis, kuma saboda faɗarsa cewa: (Ana bijiro da ayyuka ranar litinin da alhamis, don haka ina so a bijiro da aikina a halin azumi) [6].
5. Azumin kwana uku a kowane wata, saboda faɗar Annabi (SAW) cewa: (Ka azumci kwanaki uku a wat, domin aikin alheri guda ɗaya ana ninkashi sau goma, hakan sai ya kasance kamar

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (1162).
[2]. Muslim ne ya rawaito shi (1162).
[3]. Muslim ne ya rawaito shi (1162).
[4]. Muslim ne ya rawaito shi (1133).
[5]. Ahmad ne ya rawaito shi (1/241).
[6]. Ahmad (5/201) da Tirmizi (745) ne suka rawaito shi.

azumin shekara ne)[1], an karɓo daga Abu Huraira cewa: "Masoyina ya yi mini wasici da abubuwa uku: azumtar kwanaki uku a kowane wata da sallar walaha, kuma na riƙa yin wuturi kafin na kwanta bacci".

Abin da ya fi shi ne azumin ya kasance a cikin (kwanaki masu haske), wato: Ranar sha uku da sha huɗu da sha biyar, saboda faɗar Annabi (SAW)cewa: (Duk wanda yake son azumi cikin wata, to ya azumci kwanakin haske guda uku).

6. Azumin kwana ɗaya da shan ruwa kwana ɗaya, wannan shi ne mafi falala daga cikinsu saboda faɗar Annabi (SAW) cewa: (Mafi falalar azumi shi ne azumin Annabi Dauda aminci ya tabbata gare shi, ya kasance yana azumtar kwana ɗaya kuma yana shan ruwa kwana ɗaya), kuma an karɓo daga Abdullahi bin Amru cewa lallai Annabi(SAW)ya ce masa: (Ka azumci kwana ɗaya kuma ka sha ruwa kwana ɗaya, hakan shi ne irin azumin Annabi Dauda, kuma shi ne mafi dacewar azumi), Abdullahi ya ce: "Lallai ni zan iya fiye da haka, Manzon Allah (SAW)ya ce: (Babu wanda ya fi wannan falala).

7. Azumin watan Almuharram, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Mafi falalar azumi bayan Ramadana shi ne watan Allah Almuharram).

8. Azumin kwana tara na watan Zulhijja, Manzon Allah (SAW) ya ce: (Babu wasu kwanaki waɗanda aiki nagari a cikinsu ya fi soyuwa a wurin Allah sama da waɗannan kwanaki goman).

9. Azumi a cikin watan Sha'aban, A'isha Allah ya ƙara mata yarda tana cewa: "Ban taɓa ganin Annabi (SAW) yana yawaita azumi ba kamar yadda yake yi cikin watan Sha'aban ba).

[1]. Tirmizi (751) da Nasa'i (1/322) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASIN SIRA ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Tsagewar Wata:

Daga cikin alamomin gaskiyar annabtakarsa (SAW) akwai abin da Allah Maɗaukaki ya bayyana ta hannunsa na abubuwan da suka saɓa al'ada, daga cikin mafiya shahararsu da girmansu akwai: tsagewar wata, Allah Maɗaukaki ya ce: ((Alƙiyama ta kusanto wata kuma ya tsage () Idan kuma suka ga wata aya sai su kau da kai kuma su ce: wannan sihiri ne ƙaƙƙarfa () Suka kuma ƙaryata, suka bi soye-soyen zukatansu. Kowane al'amari kuwa (na alheri ko na sharri) mai tabbata ne () Haƙiƙa kuma wasu labarai waɗanda tsawatarwa take cikinsu sun zo musu () Hikima ce mai kaiwa matuƙa, sai dai kuma gargaɗin ba ya amfanarwa))[1].

Kuma kamar yadda bayyanannen Alkur'ani ya yi nuni a kan wannan ayar, haƙiƙa mutane masu yawa daga cikin sahabbai Allah ya ƙara musu yarda sun rawaito shi tahanyar tawaturi, daga cikinsu akwai: Abdullahi ɗan Mas'ud da Anas da ɗan Abbas da Ibnu Umar da Huzaifa da Aliyu da Jubairu ɗan Muɗ'im da wasunsu, kuma kwatankwacin waɗannan daga cikin tabi'ai sun rawaito daga sahabbai, sannan kamar haka har hadisin ya iso gare mu, don haka sai ilimi na yaƙini wanda babu wani mai hankali da zai yi shakka a kansa ya tabbata game da wannan mu'ujiza.

- An karɓo daga Anas (RA) ya ce: "Mutanen Makka sun tambayi Annabi cewa ya nuna musu aya, sai ya nuna musu tsagewar wata"[2].
- Kuma an karɓo daga Abdullahi bin Mas'ud (RA) ya ce: "Wata rana muna tare da Manzon Allah (SAW) a mina sai ga wata ta tsage gida biyu, sai tsagi ɗaya ya kasance a bayan dutse ɗaya tsagin kuma ƙasa da shi, sai Manzon Allah (SAW) ya ce da mu: (ku shaida)[3].

---

[1]. [Alƙamar: 1-5].
[2]. Bukhari (4867) da Muslim (2802) ne suka rawaito shi.
[3]. Bukhari (4867) da Muslim (2802) ne suka rawaito shi.

Sai Ibnu Mas'ud (RA) ya bayyana yanayin yadda wannan tsagewar ta kasance, kuma da cewa lallai hakan da gaske ne, sai yake cewa: " Sai tsagi ɗaya ya kasance a bayan dutse ɗaya tsagin kuma a ƙasa da shi, saboda kada ya bar wani da magana a ransa.

A wata riwayar ta daban kuma Ibnu Abbas yana bayani daki-daki dangane da abin da ya faru bayan wannan ayar, sai yake cewa: "Yayin da kafiran Ƙuraishawa suka gani sai suka ce: wannan sihiri ne da Ibnu Abi Kabsha ya sihirce ku da shi! Ku jira matafiya su dawo, idan sun ga irin abin da kuka gani, to haƙiƙa ya yi gaskiya, idan kuma ba su ga irin abin da kuka gani ba, to sihiri ne ya sihirce ku da shi, domin lallai Muhammadu bai isa ya sihirce dukkanin mutane ba, sai aka tambaya matafiyan da suka taho daga dukkan ɓangarori, sai suka ce: Haƙiƙa mun gani".[1]

[1]. Al-Bidaya Wan-Nihaya (8/562).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABBAS ƊAN ABDULMUƊƊALIB (RA)

❖ Sunansa da Haifuwarsa:

Shi ne Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib Alhashimi Alƙurashi, ana masa alkunya da Abul-Fadl.

An haife shi a Makka, kafin shekarar giwa da shekara uku.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Abbas (RA) ya kasance daga cikin mafiya tsawon mazaje, mafiya hasken halitta, mafiya kyawunsu, kuma mafiya girman murya cikinsu, tare da cikakke hankali, da maɗaukakin matsayi; Ya kasance a lokacin Jahiliyya shugaba kuma jagora a cikin Ƙuraishawa, kuma ya kasance mai yawan kyauta mai karamci, mai ƙetare iyaka wajen kyauta, mai sada zumunci, mai kaifin basira sosai, ya ci nasarar tunkuɗe cutarwa da muzgunawa mai yawa ga Annabi (SAW) saboda kaifin basirarsa.

Daga cikin mafiya mahimmancin ayyukansa (RA) akwai: Shayarwa, da raya masallaci mai alfarma, haka kuma yana daga cikin mafiya taimakon Manzon Allah (SAW) daga cikin makusantansa bayan baffansa Abu Ɗalib, kuma ya halarci mubaya'a ta Aƙaba ta biyu tare da Annabi (SAW) domin ya tabbatar da mubaya'a, kuma ya shardanta wa mutanen Madina kiyaye Manzon Allah (SAW) da taimakonsa, alhali a wannan lokaci yana kan addinin mutanensa[1].

Kuma ya kasance daga cikin waɗanda suka tsaya a lokacin da mutane suka gudu a yiƙin Hunaini, ya riƙe linzamin dokin Annabi

[1]. Al-Bidaya Wan-Nihaya (3/160).

(SAW) har aka samu nasara,[1] kuma da yake yana da babban murya, sai Annabi (SAW) ya umurce shi da ya yi yekuwa ga mutane ya ce: “Ya ku taron ansarawa, ya ma’abota suratul-Baƙara”, har sai da mutane suka juyo kuma suka taru.[2]

Manzon Allah (SAW) ya kasance yana girmama shi yana kuma karrama shi bayan ya musulunta, yana kuma cewa: (Lallai baffan mutum kamar babanshi yake),[3] kuma haƙiƙa Manzon Allah (SAW) ya keɓance shi da waɗannan addu’o’i: (Ya Allah Ka gafarta wa Abbas da ‘ya’yansa, gafara a zahiri da ɓoye, kada Ka bar wani zunubi, ya Allah Ka kiyaye shi cikin ‘ya’yansa).[4]

Haka kuma sahabbai, su ma sun kasance suna girmama shi, kuma suna roƙon shi da ya yi musu addu’a kuma ya roƙa musu ruwa idan aka yi fari; an karɓo daga Umar bin Khaɗɗab (RA) cewa ya kasane yana neman Abbas da ya roƙa musu Allah, sai ya ce: “Ya Allah! Lallai mu mun kasance muna tawassuli zuwa gare ka da addu’arAnnabinmu sai ka saukar mana da ruwa, to gamu yanzu muna tawassuli da addu’ar baffan Annabinmu, ya Allah Ka saukar mana da ruwa”, sai ko a saukar musu da ruwan[5].

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu a Madina, ranar Juma’a, sha huɗu ga watan Rajab, shekara ta talatin da biyu, a lokacin halifancin Usman, yana ɗan shekara tamanin da takwas, kuma ya ‘yanta bayi saba’in a lokacin mutuwarsa,[6] sai Aliyyu ɗan Abu Ɗalib da ‘ya’yansa Abdullahi da

[1]. Muslim ne ya rawaito (1775).
[2]. Abu Ya’ala (3606) da Ɗabarani (2758) ne suka rawaito shi.
[3]. Tirmizi ne ya rawaito (3760).
[4]. Tirmizi ne ya rawaito (3762).
[5]. Bukhari ne ya rawaito (1010).
[6]. Ibnu Sa’ad ne ya rawaito (4/30).

Ƙusam da Ubaidullahi suka masa wanka, sai aka binne shi a maƙabartar Baƙi’.

Auna fahimtarka darussan Mako na na 44			Amsa na ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Me ake nufi da “Assafara”?**		a
	a. Mala’iku	b. Salihai	c. Mujahidai.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Abubuwan aka ambata a hadisin haƙƙin musulmi a kan ɗan’uwansa su:**		b
	a. Biyar ne.	b. Shida ne.	c. Bakwai ne.
Darasin Aƙida	**Tambaya: Mene ne hukuncin izgili ga addini?**		c
	a. Munafurci ne na aiki.	b. Ƙaramin kafirci ne.	c. Ridda ne daga musulunci.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Mafi falalar azumi bayan Ramadan shi ne:**		c
	a. Na watan Rabi’ul Awwal	b. Na watan Zul-ƙa’ada.	c. Na watan Allah Almuharram
Darasin Sira	**Tambaya: Waɗanda Ƙuraishawa suka nemi shaidansu a kan ingancin tsagewar wata su ne:**		a
	a. Matafiya.	b. Ƙauyawa.	c. Rumawa.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin mafi muhimmanci ayyukan Abbas (RA) akwai:**		b
	a. Tona rijiyar Zamzam	b. Shayarwa	c. Ɗaukan tuta da ya yi ranar yaƙin Mu’uta.

MAKO NA ARBA’IN DA BIYAR

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATU ABASA (2)

فَلْيَنظُرِ ٱلْإِنسَٰنُ إِلَىٰ طَعَامِهِۦٓ ﴿٢٤﴾ أَنَّا صَبَبْنَا ٱلْمَآءَ صَبًّا ﴿٢٥﴾ ثُمَّ شَقَقْنَا ٱلْأَرْضَ شَقًّا ﴿٢٦﴾ فَأَنۢبَتْنَا
فِيهَا حَبًّا ﴿٢٧﴾ وَعِنَبًا وَقَضْبًا ﴿٢٨﴾ وَزَيْتُونًا وَنَخْلًا ﴿٢٩﴾ وَحَدَآئِقَ غُلْبًا ﴿٣٠﴾ وَفَٰكِهَةً وَأَبًّا ﴿٣١﴾ مَّتَٰعًا
لَّكُمْ وَلِأَنْعَٰمِكُمْ ﴿٣٢﴾ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلصَّآخَّةُ ﴿٣٣﴾ يَوْمَ يَفِرُّ ٱلْمَرْءُ مِنْ أَخِيهِ ﴿٣٤﴾ وَأُمِّهِۦ وَأَبِيهِ ﴿٣٥﴾
وَصَٰحِبَتِهِۦ وَبَنِيهِ ﴿٣٦﴾ لِكُلِّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُمْ يَوْمَئِذٍ شَأْنٌ يُغْنِيهِ ﴿٣٧﴾ وُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ مُّسْفِرَةٌ ﴿٣٨﴾ ضَاحِكَةٌ
تَرْهَقُهَا قَتَرَةٌ ﴿٤١﴾ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْكَفَرَةُ ٱلْفَجَرَةُ ﴿٤٢﴾ مُّسْتَبْشِرَةٌ ﴿٣٩﴾ وَوُجُوهٌ يَوْمَئِذٍ عَلَيْهَا غَبَرَةٌ ﴿٤٠﴾

❖ Fassara:

24. To mutum ya yi duba zuwa ga abincinsa mana?

25. Cewa lalle Mu Muka zubo da ruwan sama zubowa.

26. Sannan Muka tsaga ƙasa tsagawa.

27. Sai Muka tsiro da ƙwaya daga cikinta.

28. Da inabai da ciyayi.

29. Da zaitun da dabino.

30. Da gonaki cike da itatuwa.

31. Da kayan marmari da makiyaya.

32. Don jin dadinku da na dabbobinku.

33. Sannan idan mai sa kurunta ta zo (watau busa ta farko).

34. A ranar da mutum yake guje wa dan’uwansa.

35. Da uwarsa da ubansa.

36. Da matarsa da ‘ya’yansa.

37. Kowane mutum daga cikinsu a wannan ranar yana da lamarin da ya sha kansa.

38. Wasu fuskoki a wannan ranar masu haske ne.

39. Masu dariya, masu farin ciki.

40. Wasu fuskokin kuma a ranar akwai ƙura a kansu.

41. Baƙin ciki zai lulluɓe su.

42. Waɗannan su ne kafirai maɓarnata.

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Tunatar da kafirai, waɗanda suka wadatu daga Ubangijinsu, da hujjoji a kan tashi bayan mutuwa.

❖ Baƙin Kalmomi:

وقضبا	Wa Ƙadba	Abincin dabbobi
غلبا	Gulba	Mai manyan bishiyoyi
وأبّا	Wa abba	Ciyayin dabbobi
الصاخّة	Assaakkha	Ƙarar ranar alƙiyama, wacce take kurumta kunnuwa.
يغنيه	Yugnih	Wanda zai shagaltar da shi
مسفرة	Musfira	Mai haskakawa
مستبشرة	Mustabshira	Masu farin ciki.
غبرة	Gabara	Ƙura da dauɗa

ترهقها	Tarhaƙuha	Yana lilluɓe su
قترة	Ƙatara	Ƙasƙanci da duhu.
الكفرة	Alkafara	Masu musu a zukatansu
الفجرة	Alfajara	Masu saɓo a ayyukansu

❖ Ma’anar Ayoyin a Dunƙule:

Waɗannan ayoyin sun zo ne don su tunatar da mutum game da abin da ke kewaye da shi na ni’imomin Allah, sai suka tunatar a kan ni’imomin abinci da abin sha waɗanda Allah Ya azurta shi da shi ba tare da wata dabara daga gare shi ko ƙarfi ba, Allah shi ne yake zubar da ruwa daga sama zuwa ƙasa, kuma shi ne yake tsaga ƙasa don hatsi ya tsuro da inabi da zaitun da dabino da sauran tsirrai, waɗanda mutane suke riƙan sa a matsayin abin morewa ga kawunansu da dabbobinsu.

Wannan kuma gaba ɗayansa mai ƙarewa ne kuma mai gushewa a lokacin da ƙara mai kurumta kunnuwan halittu da tsananin ƙarfinta za ta zo, sai mutum ya gudu a wannan ranar saboda firgici, ya kuma shagala da sha’aninsa ya bar iyalansa da mafi kusancin mutane a gare shi, a wannan lokaci fuskoki za su kasu zuwa kashi biyu: Fuskoki masu farin ciki da dariya, waɗanda su ne ‘yan aljanna, da kuma fuskoki da baƙin ciki da damuwa za su dabaibaye su, waɗanda su ne kafirai fajirai.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Tunatarwar da Allah Maɗaukaki ga halittunsa game da baiwar da ya musu na abinci kala-kala wanda zai dace da ɗanɗanonsu da buƙatunsu.

2) Dukkan abin da ke ban ƙasa na dabbobi, haƙiƙa Allah Ya tanada musu abin da za su rayu a kansa na abinci da arziki.

3) Tunatarwa a kan tsananin firgicin ranar alƙiyama, da kwaɗaitarwa a kan yin shiri dominsa.

4) Yankewar alaƙoƙi da sanayya a ranar alƙiyama, da shagaltuwar mutum da kansa, da mancewarsa ga waninsa.

5) Bayyanar alamomin ma’abota imani da ma’abota taɓewa a fuskokinsu ranar alƙiyama.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

ADDINI NASIHA NE

An karɓo daga Tamim Addari (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: **(Addini nasiha ne, addini nasiha ne, addini nasiha ne).** Suka ce: Ga wa ya Manzon Allah? Ya ce: **(Ga Allah, da Manzonsa, da shugabannin musulmi, da gamagarinsu)**[1].

❖ Sharhi:

Addini na gaskiya ya zo da umurni da tsantsanta nasiha da yaɗa ta, a cikin wannan hadisi kuma Annabi (SAW) yana bayyana cewa lallai addini gaba ɗayansa, zahirinsa da baɗininsa nasiha ne, sannan ya fassara nasihar da cewa ita ce tsayuwa da waɗannan haƙƙoƙi guda biyar:

Na farko: Nasiha ga Allah, ta hanyar tabbatar da rububiyyarsa da ɗayantakarsa, da kaɗaituwarsa da siffofi na kamala a bisa yanayi da wani ba ya tarayya da shi cikinsa, da tsayuwa da bauta masa a fili da ɓoye, da komawa zuwa gare Shi a kowane lokaci, da tuba da istigifari daga kowane laifi.

Na biyu: Nasiha ga littafin Allah Maɗaukaki, ta hanyar koyon lafuzansa da ma'anoninsa, da haddace shi, da tadabburin shi, da ƙoƙari wurin aiki da shi.

Na uku: Nasiha ga Manzon Allah (SAW), ta hanyar imani da shi, da ƙaunar sa, da gabatar da shi a kan rai da dukiya da 'ya'ya, da gabatar da maganarsa a kan maganar kowa, da bin sa, da bin shiriyarsa a ginshiƙan addini da rassansa.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (55).

Na huɗu: Nasiha ga shugabannin musulmi, ta hanyar yarda da shugabancinsu, da ji da biyayya gare su, da tsayuwa da wajibinsu, da kwaɗaitar da mutane a kan haka, da ƙoƙarin nusar da su ga abin da zai amfane su kuma ya amfani mutane, da kuma yin nasiya ga duk wanda yake da shuganci babba ko ƙarami.

Na biyar: Nasiha ga gamagarin musulmi, ta hanyar so musu abin da yake so wa kansa, da ƙin abin da yake ƙi wa kansa gare su, ya kuma faɗakar da su zuwa ga gaskiya don su bi ta, kuma ya ja kunnensu game da ɓarna don su guje ta.

❖ **Abubuwan da ake koya daga Hadisin:**

1) Fassarar Annabi (SAW) ga nasiha, yana daga cikin dunƙulallun kalmomi; haƙiƙa ya ƙunshi addini gaba ɗayansa, kuma bai bar komi daga cikinsa ba.

2) Fassarar Annabi (SAW) ga wannan kalma, wato: (Addini nasiha ne), don ƙarfafa ta, da girmama sha'aninta, da ba da muhimmanci gare ta.

3) Tsayuwa da waɗannan haƙƙoƙi guda biyar na tabbatar da tsayuwa da addinin Allah da shari'arsa.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

RAYA SANIN ILIMIN GAIBU

Abin da ke nufi da gaibu shi ne: Abin da ya ɓuya daga sanin mutane cikin al'amura da na yanzu, da waɗanda za su zo, da waɗanda suka shuɗe.

Allah Maɗaukaki kuma Shi ne Wanda Ya kaɗaitu da sanin ilimin gaibu, babu wanda ya san gaibu sai Shi; Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce: ((Ka ce waɗanda suke cikin sammai da waɗanda suke ƙasa, ba sa sanin gaibu sai Allah kaɗai)),[1] don haka, duk wanda ya raya cewa ya san gaibu ta hanyar bokanci, ko tsafi, ko duba, ko karanta tafukan hannu, ko kifa kofuna, ko ta hanyar taurari manya ko ƙanana, ko wani abu makamancin haka, to shi maƙaryaci ne kuma mai kafirce wa Allah!

Kuma bokanci ba ya kasancewa sai ta hanyar kusantar shedanu waɗanda suke sato ji daga sama; Allah Maɗaukaki ya ce: ((Shin ba Na ba ku labari ba game da wanda shedanu suke sauka masa? () Suna sauka ne a kan duk wani maƙaryaci mai yawan laifi () Suna jefa wa (bokaye) abin da suka sato jinsa, yawancinsu kuwa maƙaryata ne))[2].

Haka ya kasance ne saboda shedan yana sato jin kalma daga maganar mala'iku, sai ya jefa ta a kan harshen matsafi ko boka, sai ya yi ƙarya ɗari tare da ita, sai a ce: Ashe bai ce kaza a rana kaza ba? Sai a gaskata shi da wannan kalmar da aka ji daga sama.[3]

Wasu daga cikinsu suna riya cewa sun san abin da ya faru a ban ƙasa da abin da zai faru, wasu kuma suna riya cewa za su iya ba da labarin

---

[1]. [An-Naml: 65].
[2]. Ash-Shu'ara (221-223).
[3]. Bukhari ne ya rawaito (4800).

wajen wani abu da ya ɓata, wasu kuma suna alaƙanta tsakanin abubuwan da suke faruwa a ban ƙasa da kaikomon taurari, sai ya ce: Duk wanda ya yi aure a lokacin da tauraro kaza ya yi kaza, duk wanda ya yi tafiya a lokacin da tauraro kaza ya yi kaza, duk wanda aka haife shi a lokacin da tauraro kaza ya yi kaza; To waɗannan gaba ɗaya shirka ne babba cikin Rububiyya da Uluhiyya.

Shirka ne a rububiyya saboda riya tarayya da Allah cikin iliminsa da aka yi, kuma shirka ne a uluhiyya saboda kusantar sheɗanu da wani abu na bauta.

Haka kuma halin wanda ya gaskata su yake, hukuncinsa shi ne: Kafirci mai fitar da mutum daga addini; saboda haƙiƙa shi ya sanya wa Allah abokin tarayya cikin abin da Allah Ya keɓanta da shi; Annabi (SAW) ya ce: (Duk wanda ya je wajen boka, sai ya gaskata shi a kan abin da yake faɗi; to haƙiƙa ya kafirce wa abin da aka saukar wa Muhammadu (SAW)[1].

[1]. Abu Dawud (3904) da Nasa'i (9017) ne suka rawaito shi

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

ABUBUWAN DA SUKE LALATA AZUMI

Allah Maɗaukaki Ya shar'anta wa mai azumi ya yi azumi daidaitacce, wanda ba zai cutar da shi ko ya raunana shi ba, kuma kada ya yi sakaci ko wasa da shi; Ya yi hakan ne don Ya isa zuwa ga wata hikima da aka nufa da yin sa.

Kuma haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya ambaci ginshiƙan abubuwan da suke karya azumi a cikin faɗinsa: ((To a yanzu ku sadu da su da (daddare), kuma ku nemi abin da Allah Ya rubuta muku, kuma ku ci, kuma ku sha har farin zare ya bayyana a gare ku daga baƙin zare na alfijir (wato ketowar rana), sannan kuma ku cika azumi zuwa dare)).[1] Sai wannan ayar ta tattare ginshiƙan abubuwa masu karya azumi gaba ɗaya, waɗanda su ne: Ci, da sha, da jima'i. Amman sauran abubuwan haƙiƙa Annabi (SAW) ya bayyana su a sunnarsa.

❖ **Saboda haka, lallai abubuwa masu lalata azumi a dunƙule su bakwai ne:**

Na farko: Jima'i:

Kuma shi yana daga cikin mafi girman abubuwa masu lalata azumi, kuma laifukan masu girma, kuma kaffara ba ta wajaba da wani abu daga cikin abubuwa masu lalata azumi sai jima'i.

Na biyu: Istimna'i (Auren hannu);

Dalili a kan haka kuwa shi ne faɗin Allah Maɗaukakin Sarki a Hadisi Ƙudusi a kan mai azumi: (Yana barin abincinsa, da abin shansa, da sha'awarsa saboda ni).[2]

---

[1]. [Al-Baƙara: 187].
[2]. Bukhari (1894) da Muslim (1101) ne suka rawaito shi.

Na uku: Ci da sha:

Haka kuma idan ya shigar da wani abu a cikinsa ta hanyar hanci, to shi ma kamar ci da sha yake; don haka ne ma Annabi (SAW) ya ce: (Kuma ka zurfafa wujen shaƙan ruwa, sai dai idan kana da azumi).[1]

Na huɗu: Abin da za a iya ɗaukan shi a matsayin ci da sha, wannan kuma ya ƙunshi abubuwa guda biyu:

- Sanya wa mai azumi jini; saboda lallai jini shi ne maƙuran abinci da abin sha.
- Allura mai ƙosarwa, wacce ake wadatuwa da ita daga abinci da abin sha; saboda lallai ita ma a matsayin abinci da abin sha take.

Amma ka ga allura da ba a ɗaukan ta a maimakon abinci da abin sha, sai dai ana aiki da ita ne don magani; kamar allurar binsilin da insolin ko kuma allurar riga kafi; to ba za ta cutar da azumi ba.

Na biyar: Fitar da jini ta hanyar ƘAho:

Saboda faɗin Annabi (SAW): (Mai ƙaho da wanda aka yi wa ƙaho azuminsu ya karye gaba ɗayansu.[2]

Daga cikin abubuwan da za a iya ɗaukan su a matsayi ƙaho akwai: Sadaukar da jini; saboda shi ma yana tasiri wa jiki irin tasirin ƙaho. Amma wanda zubar jini ta same shi, to lallai azuminsa ba zai lalace ba; saboda ba da sonsa ba ne hakan ya faru.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito (788).
[2]. Abu Dawud ne ya rawaito (2367).

Na shida: Tsokano amai da gangan:

Saboda fiɗin Annabi (SAW): (Duk wanda amai ya rinjaye shi, to babu ramako a kansa, wanda kuwa ya tsokano shi da gangan, to ya rama).[1]

Na bakwai: Fitar jinin haila da na nifasi (wato jinin haifuwa).

Saboda faɗin Annabi (SAW): (Ashe idan haila ta zo mata ba tana barin salla da azumi ba)[2].

[1]. Tirmizi ne ya rawaito (720).
[2]. Bukhari ne ya rawaito (304).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Saukar albarka a Madina saboda addu'arsa (SAW):

An karɓo daga A'isha (RA) ta ce: Mun taho Madina a lokacin da take ɗauka da annoba, sai Abubakar ya yi rashin lafiya, sai Bilal da Amir ɗan Fuhaira ma suka kamu da rashin lafiya, Abubakar ya kasance idan zazzaɓi ya buge shi yana cewa: "Kowane mutum ana gai da shi da safiya a cikin iyalansa ... Mutuwa kuwa tafi kusa da shi sama da igiyar takalminsa".

Shi kuma Bilal ya kasance idan zazzaɓi ya sake shi yana cewa – yana mai begen Makka -: "Kaitona, ina ma a ce zan kwana wani dare a wajen wani kwari da yake ɗauke da itacen ƙirya da itacen jalil. Shin akwai ranar da zan tuzga wa ƙoramun Majanna ... Shin dutsen Shama da Ɗafilu za su sake bayyana a gare ni".

Yayin da Manzon Allah (SAW) ya ga irin fama da sahabbansa suke yi, sai ya ce: (Ya Allah Ka sanya mana ƙaunar Madina kamar yadda Ka sanya mana ƙaunar Makka ko ma sama da haka, kuma Ka gyara ta, kuma Ka albarkace mu a cikin kwanonta da mudunta, kuma Ka mayar da annobarta ta zazzaɓi zuwa Juhfa).[1]

- Kuma abin da ake nufi da faɗinsa "Ka gyara to" shi ne: Ka raba ta da annoba, kuma Ka sanya iskarta da ruwanta su zama masu kyawu kuma lafiyayyu.
- Az-Zurƙani ya ce: "Sai Allah Maɗaukaki Ya amsa addu'arsa, sai ya daidaita iskarta, da ƙasarta, da gidajenta, da kuma rayuwa a cikinta"[2].

[1]. Bukhari (304) da Ahmad (24405) ne suka rawaito shi.
[2]. Sharhuz-Zurƙani (5/50).

- Annawawi ya ce: “Cikin wannan hadisi akwai alama daga cikin alamomin annabtakar Muhammadu (SAW); saboda lallai Juhfa tun daga wannan ranar ta zama abar nisanta, babu wanda zai sha ruwanta face sai ya kamu da zazzaɓi; wato sai zazzaɓi ya kama shi”.[1]

[1]. Sharhun-Nawawi ala Sahihi Muslim (9/150).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABDULLAHI ƊAN ABBAS (RA)

❖ Sunansa da Haifuwarsa:

Shi ne Abdullahi ɗan Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib ɗan Hashim ɗan Abdu Manaf, ana masa alkunya da Abul-Abbas.

An haife shi a Shi'ib, wato wajen da Banu Hashim suka koma lokacin da aka sa musu takunkumi a Makka, hakan ya faru ne kafin hijra da shekara uku.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Ya kasance (RA) mutum ne mai tsawo, mai farin fata, mai karkata zuwa fatsi-fatsi, mai hasken fuska, mai kaifin basira, mai ƙarfin ƙwaƙwalwa, mai ƙarfin hadda, mai yawan ilimi, ana masa laƙabi da "Habrul Umma" da kuma "Turjumanul-Ƙur'an" saboda albarkacin addu'ar Manzon Allah (SAW); Abin da ya faru shi ne: Abdullahi ya kwana wata rana a ɗakin goggonsa Maimuna (RA), sai ya zuba wa Annabi ruwan alwalansa da daddare ya ajiye masa, sai Manzon Allah (SAW) ya yi tambaya a kan wanda ya ajiye, sai Maimuna (RA) ta sanar da shi cewa Ibnu Abbas ne ya aikata hakan, sai Annabi (SAW) ya ce: (Ya Allah Ka fahimtar da shi addini, kuma Ka sanar da shi fassarar Alƙur'ani).[1]

Ya haddace Alƙur'ani tun yana yaro, kuma ya ba da himma wurin neman ilimi da lazimtar ma'abotansa, sai ya samu kaso mai gwaɓi a cikin ilimi, yana cewa (RA): "Na haddace alƙur'ani a zamanin Annabi (SAW), kuma ya yi wafati ina ɗan shekara goma".[2] Kuma yana cewa: "Labari ya kan zo mun cewa akwai wani mutum da yake

[1]. Bukhari (143) da Muslim (2645) ne suka rawaito shi.
[2]. Ɗabarani ne ya rawaito (10577).

ɗauke da wani hadisi, sai na je wajensa na tarar da shi yana bacci, sai na kwanta a kan riga ta a ƙofar gidansa, sai iska ta watso mun ƙasa, sai mutumin ya fito, sai ya ce: Ya kai ɗan baffan Manzon Allah, Me ya hana ka aiko ni naje wajenka?! Sai na ce: Kai kafi cancanta na zo wajenka na tambaye ka”.[1]

Sai ya zama babban malamin zamaninsa a ilimin tafsiri, kuma masanin fiƙihun zamaninsa, har ma Umar da Usman suka kasance suna kiran sa ya halarci zaman shura tare da ma’abota Badar, kuma ya kasance yana fatawa a zamaninsu; kuma yana cewa: “Umar ya kasance yana shiga da ni tare da dattijan ma’abota Badar, sai wasu daga cikinsu suka nuna cewa ba su ji daɗin hakan ba, har ma wani ya ce: Don me za ka shigo mana da wannan alhali muma muna da ‘ya’ya sa’anninsa?! Sai Umar ya ce: Lallai shi ai kun san matsayinsa, sai wata rana Umar ya kira shi, sai ya shiga da shi wajensu, sai ya ce: Me za ku ce game da faɗin Allah Maɗaukakin Sarki: ((Idan nasarar Allah da buɗi suka zo)?[2] Sai wani daga cikinsu ya ce: An umurce mu ne da mu gode wa Allah kuma mu nemi gafararsa idan nasarar Allah ta zo kuma aka mana buɗi. Sai ya ce da ni: Kai ma wannan shi ne ra’ayinka ya kai ɗan Abbas? Sai na ce: A’a. Sai ya ce: To me za ka ce: Sai na ce: Magana ake a kan ajalin Manzon Allah (SAW), Allah Ya sanar da shi. Sai Umar ya ce: Ni ma ban san wani abu ba koma bayan abin da ka faɗa.[3]

Kuma Abu Wa’il yana cewa: Ibnu Abbas ya yi mana huɗuba a wani lokacin da aka ɗaura shi a matsayin Amirul Hajji, sai ya buɗe suratun-nur, sai riƙa karantarwa yana fassarawa, sai ni kuma na riƙa cewa: Ban taɓa gani ko jin maganar wani mutum kamar wannan ba, da a ce Farisawa da Rumawa da Turkawa za su saurare shi da sun

[1]. Ɗabarani ne ya rawaito (20592).
[2]. [An-Nasr: 1].
[3]. Bukhari ne ya rawaito (4970).

musulunta.[1] Haka kuma an san shi da yawan ibada; Abu Mulaika yana cewa: “Na aboci Ibnu Abbas daga Makka zuwa Madina, ya kasance yana sallatar farilla raka’a biyu, idan kuma ya sauka, sai ya tashi a tsakiyar dare, sai ya riƙa karanta Alƙur’ani harafi harafi, yana kuma yawaita kuka sosai a cikin karatun nasa”.[2]

Ɗawus ma yana cewa: “Ina rantsuwa da Allah ban ga wani mutum da ya kai Ibnu Abbas tsananin girmama alfarmar Allah ba”.[3]

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu a shekara ta 68 bayan hijira, a garin Ɗa’if, a lokacin yana ɗan shekara saba’in, sai Muhammadu bin Hanafiyya ya sallace shi.

[1]. Hilyatul-Auliya (1/324).
[2]. Siyaru A’alamin-Nubala’ (3/352).
[3]. Hilyatul-Auliya’ (1/329).

Auna fahimtarka a darussan Mako na 45			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Me ake nufi da “Alƙadbu”?**		c
	a. ‘Ya’yan itatuwan lokacin zafi.	b. Abincin ‘yan wuta.	c. Abincin dabbobi.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Koyon lafuzan Alƙur’ani da ma’anoninsa, da haddace shi, da tadabburin shi, da ƙoƙari wurin aiki da shi, dukkan waɗannan suna daga cikin nasiha ga:**		b
	a. Allah Maɗaukaki.	b. Littafinsa.	c. Gamagarin musulmi.
Darasin Aƙida	**Tambaya: Mene ne hukuncin alaƙanta ababen da ke faruwa a ban ƙasa da yanayin kaikoman taurari?**		a
	a. Shirka ce babba.	b. Ƙaramar shirka ce.	c. Halal ce babu laifi.
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Daga cikin abubuwan da ba sa karya azumi akwai:**		b
	a. Yin ƙaho.	b. Alluran rigakafi.	c. Tsokano amai da gangan
Darasin Sira	**Tambaya: Annabi (SAW) ya roƙi Ubangijinsa Ya mayar da annobar Madina zuwa:**		c
	a. Yaman.	b. Dimaska.	c. Juhfa.
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Ana yi wa Abdullahi ɗan Abbas (RA) laƙabi da:**		a
	a. Turjumanul-Ƙur’an	b. Zush-shahadatain	c. Aminul-umma.

MAKO NA ARBA'IN DA SHIDA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUN-NAZI'AT (1)

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلنَّٰزِعَٰتِ غَرۡقٗا ١ وَٱلنَّٰشِطَٰتِ نَشۡطٗا ٢ وَٱلسَّٰبِحَٰتِ سَبۡحٗا ٣ فَٱلسَّٰبِقَٰتِ سَبۡقٗا ٤
فَٱلۡمُدَبِّرَٰتِ أَمۡرٗا ٥ يَوۡمَ تَرۡجُفُ ٱلرَّاجِفَةُ ٦ تَتۡبَعُهَا ٱلرَّادِفَةُ ٧ قُلُوبٞ يَوۡمَئِذٖ وَاجِفَةٌ ٨
أَبۡصَٰرُهَا خَٰشِعَةٞ ٩ يَقُولُونَ أَءِنَّا لَمَرۡدُودُونَ فِي ٱلۡحَافِرَةِ ١٠ أَءِذَا كُنَّا عِظَٰمٗا نَّخِرَةٗ ١١ قَالُواْ تِلۡكَ
إِذٗا كَرَّةٌ خَاسِرَةٞ ١٢ فَإِنَّمَا هِيَ زَجۡرَةٞ وَٰحِدَةٞ ١٣ فَإِذَا هُم بِٱلسَّاهِرَةِ ١٤ هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ مُوسَىٰٓ
﴿إِذۡ نَادَىٰهُ رَبُّهُۥ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ١٦
إِلَىٰٓ أَن تَزَكَّىٰ ١٨ وَأَهۡدِيَكَ إِلَىٰ رَبِّكَ فَتَخۡشَىٰ ١٩ فَأَرَىٰهُ ٱلۡأٓيَةَ ٱلۡكُبۡرَىٰ ٢٠ فَكَذَّبَ وَعَصَىٰ ٢١ ثُمَّ
أَدۡبَرَ يَسۡعَىٰ ٢٢ فَحَشَرَ فَنَادَىٰ ٢٣ فَقَالَ أَنَا۠ رَبُّكُمُ ٱلۡأَعۡلَىٰ ٢٤ فَأَخَذَهُ ٱللَّهُ نَكَالَ ٱلۡأٓخِرَةِ وَٱلۡأُولَىٰٓ
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰٓ ٢٦﴾

❖ Fassara:

Da sunan Allah Mai Rahama, Mai Jin ƙai.

1. Na rantse da (mala'iku) masu cizgar (ran kafiri) mummunar cizga.
2. Da kuma (mala'iku) masu zare (ran mumini) sassauƙar zarewa.
3. Da kuma (mala'iku) masu ninƙaya (a sama don sauko da umarni) ninƙaya mai tsananin sauri.
4. Sannan da (mala'iku) masu matuƙar rigegeniya (don zartar da umarnin Allah).
5. Sannan da (mala'iku) masu tsara al'amura.

6. Ranar da mai girgizawa za ta yi girgiza (watau busar ƙaho ta farko).
7. Mai bin ta kuma za ta biyo ta (watau busa ta biyu).
8. Wasu zukata a wannan ranar a tsorace suke.
9. Idanuwansu kuma a ƙasƙance suke.
10. (A duniya) suna cewa: “Yanzu zai yiwu a dawo da mu a raye (bayan mutuwa)?
11. “Yanzu ko bayan mun zama ƙasusuwa rududdugaggu?
12. Suka ce: “Idan ko ya yiwu, to wannan komawa ce mai cike da asara.
13. To lalle ita kawai tsawa ce guda ɗaya tal!
14. Sai ga su a bayan ƙasa.
15. Shin labarin Musa ya zo maka?
16. Lokacin da Ubangijinsa Ya kirawo shi a kwari mai tsarki, (watau) Ɗuwa?
17. (Aka ce da shi): Ka tafi zuwa ga Fir’auna, haƙiƙa shi ya yi ɗagawa.
18. Sai ka ce: “Shin zai yiwu gare ka kuwa ka tsarkaka?
19. In kuma shiryar da kai zuwa ga Ubangijinka, sai ka ji tsoron Sa?
20. Sai ya nuna masa babbar aya.
21. Sai ya ƙaryata ya kuma kangare.
22. Sannan ya ba da baya yana ta gaggawa.
23. Sai ya tattara (jama’arsa) sai ya yi shela.
24. Sai ya ce, “Ni ne ubangijinku mafi girma!”
25. Saboda haka Allah Ya kama shi da azabar lahira (watau Jahannama) da ta duniya (watau nutse wa a ruwa).
26. Lalle a game da wannan tabbas akwai izina ga wanda yake tsoron (Allah).

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Tunatarwa game da Allah da mala’ikunsa da ranar lahira.

❖ Baƙin Kalmomi

تتبعها الرادفة	Tattba'uhar-radifa	Wata busa ta daban na biye da ita don tashin alƙiyama.
واجفة	Wajifa	A tsorace, a rikici.
خاشعة	Khashi'a	A ƙasƙance saboda girman abin da take gani.
الحافرة	Alhafira	Halin da muka kasance a cikinsa a ban ƙasa.
نخِرة	Nakhira	Rududdugaggu
كرة	Karratun	Dawowa
زجرة	Zajaratun	Busa
بالساحرة	Bis-sahira	A doron ƙasa
الآية الكبرى	Al'ayatul-kubra	Mu'ujizar sanda da farin hannu
نكال	Nakal	Uƙuba.

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

Suratun-Nazi'at sura ce Makkiyya, tana bayani ne a kan wasu ginshiƙai guda uku daga cikin ginshiƙan aƙida, waɗanda su ne: Imani da Allah Maɗaukakin Sarki, da mala'ikunsa, da ranar alƙiyama, sai aka buɗe ta da rantsuwa da mala'iku masu daraja, da ayyukansu da suke nuni a kan cikar miƙa wuyansu ga umurnin Allah da gaggawansu wurin zartar da shi, da bayanin ɓangaren da mala'iku suke jiɓinta a lokacin mutuwa, sai su zari ran kafiri da tsanani da ƙarfi, su kuma zare ran mumini da taushi da sannu-sannu,

sannan sai tunatarwa game da alƙiyama da firgicinta ta zo, da makomar masu taƙawa, da kuma makomar maɓarnata.

Bayan wannan kuma sai aka koro labarin Annabi Musa, saboda rarrashin Annabi (SAW); saboda shi Fir'auna yafi ƙarfi da mugunta sama da Ƙuraishawa, sai kuma Allah Ya damƙe shi, tare da haka bai kuɓuta daga uƙubarsa ba.

❖ **Abubuwan da za a koya daga Surar:**

1) Tuna firgice-firgicen alƙiyama abu ne mai sa tsoron Allah da aikata ayyukan nagartattu.
2) Girman sha'anin mai kira zuwa ga Allah Maɗaukakin Sarki.
3) Wajibcin taushi wurin magana da waɗanda ake kira, da haƙuri wurin kiran su.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

FALALAR TASBIHI DA HAMDALA

An karɓo daga Abu Malik Al'ash'ari (RA) ya ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: **(Tsarki rabin imani ne, kuma faɗin "Alhamdu lillahi" yana cika mizani, kuma "Subhanallahi da Alhamdu lillahi suna cika – ko yana cika – abin da ke tsakanin sama da ƙasa, kuma salla haske ce, sadaka dalili ce, haƙuri haske ne, Alƙur'ani kuma hujja ne gare ka ko kuma hujja a kanka, dukkan mutane suna sammako, wani ya sayar da ransa, wani ya 'yantar da shi ko kuma ya halakar da shi).**[1]

❖ Sharhi:

Ubangijinmu Maɗaukakin Sarki Mai karamci ne kuma Mai girma, Ya shar'anta wa bayinsa ayyuka 'yan kaɗan, sai kuma ya sanya wa aikata su lada mai girma, a cikin wannan hadisi akwai bayani a kan wani abu game da hakan:

(**Tsarki rabin imani ne**): Tsarki shi ne alwala, Annabi (SAW) ya siffanta ta da cewa ita ce rabin imani, wato rabin salla; saboda salla ba a karɓar ta ba tare da tsarki ba, wannan kuma ƙara tabbatar da kulawa da alwala ne a bisa siffar da Allah da Manzonsa suka yi umurni da ita.

(**Alhamdu lillahi yana ciki mizani**), ma'anar "Alhamdu" shi ne jinjina ga Allah da yabon sa da siffofin kamalarsa da siffofin buwayarsa, tare da son sa da girmama sa, kuma Allah Maɗaukaki Yana son yabo da jinjinawa, kuma Yana sakayya a kansa da lada mai girma, kuma wannan kalma 'yar gajera tana nauyaya mizanin bawa kuma tana cika shi.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito (223).

(**Subhallahi da Alhamdu lillahi**), tasbihi shi ne girmama Allah da tsarkake Shi daga kowane aibi, ladansa tare da hamdala kuma shi ne cewa suna ciki abin da ke tsakanin sama da ƙasa da kyawawan ladaddaki; saboda sun haɗa siffanta Allah da cikakkiyar kamala tare da tabbatarwa da tsarkakewa.

(**Salla haske ce**): Wato haske ne ga bawa a duniya da lahira; ita haske ce gare shi a zuciyarsa, wacce za ta hana shi aikata saɓo, kuma ta hana shi zakke wa alfasha da munanan ayyuka, kuma ta shirayar da shi zuwa ga daidai, kuma ita haske ce a fuskarsa, kuma haske a gare shi a ƙabarinsa, kuma haske a gare shi ranar alƙiyama.

(**Sadaka dalili ce**), wato bayyanannen dalili a kan gaskiyar imanin ma'abocinta da nisantar shi daga munafurci; saboda rayuka an halicce su a kan son dukiya, saboda haka, kasancewar mutum yana ciyarwa daga wannan dukiya a bisa radin kansa, wannan dalili ne bayyananne a kan gaskiyar imaninsa.

(**Haƙuri haske ne**), wannan ya ƙunshi haƙuri da nau'ukansa guda uku, wato: Haƙuri a kan aikin ɗa'a, da haƙuri a kan barin saɓo, da kuma haƙuri a kan ƙaddarorin Allah masu ɗaci, siffantuwa da haƙuri haske ne a duniya, yana haskaka zukata, kuma yana haskaka hanya, kuma yana shiryarwa zuwa ga tafarki miƙaƙƙe; Allah Yana shiryar da masu haƙuri zuwa ga mafiya kyawun halaye, kuma yana taimakon su a kan aikata mafiya kyawun ayyuka, kuma duk wanda ya yi haƙuri, to Allah zai haƙurtar da shi, amma a lahira, to shi haske ne ga ma'abotansa a ƙaburbura, kuma haske ga ma'abotansa a ranar tashi daga ƙaburbura, kuma haske a gare su a ranar da za su haɗu da Ubangijinsu Mabuwayi Mai gafara.

(**Alƙur'ani hujja ne gare ka ko kuma a kanka**), duk wanda ya kasance mumini mai gaskata shi, mai aiki da umurninshi, mai

nisantar hane-hanenshi; Alƙur'ani zai zama hujja gare shi ranar alƙiyama, idan kuwa ya kawar da kanshi daga gare shi, ya kuma saɓa wa umurninshi da hane-hanenshi; to a wannan ranar zai zama hujja a kansa.

(**Dukkan mutane suna sammako**), wato: Idan suka wayi gari sai su yaɗu a bayan ƙasa, wani sammakonsa don abin da zai amfane shi ne, wani kuma sammakonsa masifa ce a kansa, kuma kowannensu yana sayar da ransa ne, ko dai ya sayar da shi ga Allah Maɗaukaki sai ya kuɓutar da shi daga wuta, ko kuma ya sayar da shi ga sheɗan, sai ya jefa shi wuta!

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1. Mahimmancin cika alwala a bisa siffar da Allah Ya yi umurni da ita, kuma Manzon Allah (SAW) ya bayyana ta.
2. Falalar ambaton Allah Maɗaukakin Sarki, da salla da sadaka.

TALATA: DARASI CIKIN AƙIDA

SIHIRI

Sihiri: Shi ne surƙulle, da tofi, da zane-zane, da magunguna, da hayaƙi, wanda yake tasiri a zukata da ganganjiki, sai ya jinyatar, ko ya kashe, ko ya raba tsakanin mutum da matarsa, da izinin Allah.

Sihiri kafirci ne, kuma yana daga cikin ayyukan shedanu wadanda suke warware aƙida; saboda ba ya samuwa sai da wasu abubuwa na shirka; Allah Madaukaki Ya ce: ((Sai dai shedanu ne suka kafirce, suna koya wa mutane sihiri)),[1] kuma Allah subhanahu Ya bayyana cewa duk wanda ya yarda da shi kuma ya neme shi to ba shi da rabo a lahira; Allah Madaukaki Ya ce: ((Kuma haƙiƙa sun san cewa tabbas duk wanda ya fanshe shi to ba shi da rabo a lahira)).[2]

Kuma Annabi (SAW) ya ambaci sihiri cikin zunubai masu halakarwa, ya kuma hada shi da shirka, sai Annabi (SAW) ya ce: (Ku nisanci laifuka guda bakwai masu halakarwa). Suka ce: Mene ne su? Ya ce: (Shirka ga Allah, da sihiri ...).[3]

Sa'adi Allah ya rahamce shi ya ce: "Sihiri na shiga cikin shirka ta fuska biyu: Ta ɓangaren abin da ke cikinsa na amfani da shaidanu, da ratayuwa da su, ko ma neman kusunci gare su da bin abin da suke so don su masa hidima kuma su biya masa buƙatarsa, da kuma ta ɓangaren abin da ke cikinsa na riya sanin gaibu, da riya tarayya da Allah cikin iliminsa, da bin hanyoyi masu kaiwa zuwa ga hakan, wannan kuma na daga cikin rassan shirka da kafirci".[4]

---

[1]. [Al-Baƙarah: 102].
[2]. [Al-Baƙarah: 102].
[3]. Bukhari (2766) da Muslim (89) ne suka rawaito shi.
[4]. Alƙaulus-sadid (97).

Haka kuma hukuncin wanda ya je wajen matsafi don neman magani da makamantansa, hukuncinsa shi ne kafirci mai fitarwa daga addini.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

HAJJI DA UMRA

❖ Falalar Hajji da Umra:

Annabi (SAW) ya ce: (Duk wanda ya yi Hajji saboda Allah, bai yi alfasha ba, bai yi fisƙanci ba; zai dawo kamar ranar da mahaifiyarsa ta haife shi) [1].

Annabi (SAW)ya ce: (Umrah zuwa Umrah kaffara ce ga abin da ke tsakaninsu, kuma Hajji barrantacce ba shi da sakamako sai Aljanna)[2]..

❖ Hukuncin Haji da Umra:

Hajj da Umrah wajibi ne ga wanda ya samu iko sau ɗaya a rayuwa, dalilin hakan shi ne:

Faɗin Allah Maɗaukaki cewa: ((Kuma Allah Ya wajabta wa mutane ziyarar wannan ɗakin ga wanda ya sami iko. Wanda kuwa ya kafirce, to lalle Allah Mawadaci ne ga barin talikai) [3].

Da faɗinsa cewa: ((Ku cika Hajji da Umrah saboda Allah)) [4].

Da faɗin Annabi (SAW) ga A'isha lokacin da ta tambaye shi: Shin akwai jihadi a kan mata? Sai Annabi (SAW) ya ce: "Eh, akwai jihadi ba tare da yaƙi ba shi ne: Hajji da Umra) [5].

---

[1]. Bukhari (1521) da Muslim (1350) ne suka rawaito shi.
[2]. Bukhari (1773) da Muslim (1349) Muslim ne suka rawaito.
[3]. [Alu Imran: 97].
[4]. [Al-Baƙara: 196].
[5]. Ahmad (26565), da Ibnu Majah (2901) ne suka rawaito shi.

Da faɗin Annabi (SAW) ga wanda ya ambata masa cewa mahaifinsa ba zai iya yin Hajj ko Umrah ba, sai ya ce: (Ka yi wa mahaifinka Hajji da Umra) [1].

❖ Hikimar shar'anta Hajji da Umra:

Allah Ya shar’anta Hajji da Umrah ne saboda hikimomi da sirrori masu yawa, daga cikinsu akwai:

1. Bayyana ƙasƙanci da bauta ga Allah Maɗaukaki a cikin aiwatar da dukkan ayyukan Hajji kamar Ɗawafi da Sa’ayi da sauransu.
2. Cewa lallai a cikinsu akwai godiya ga Allah Maɗaukaki bisa ni’imar lafiya da dukiya, waɗanda suke daga cikin manyan ni’imomin Allah ga mutum.
3. Cewa lallai a cikinsu akwai horo ga rai domin kaiwa ga mafi girman darajojin imani da haƙuri da jihadi na rai da na sha’awa.
4. Cewa lallai a cikinsu akwai alama daga cikin alamomin haɗuwar kan Musulmi a wuri guda, cikin tufafi guda, domin gudanar da ibada guda, kuma wannan babbar manufa ce wadda take kai su ga haɗuwar zukata.

[1]. Abu Dawud (1810) da Nasa'i (1115) ne suka rawaito shi.

AL-HAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ **Yawaitar abinci ɗan kaɗan da iznin Allah Mai girma da ɗaukaka:**

- An karɓo daga Anas (RA) cewa Abu Ɗalḥa ya ce wa Ummu Sulaim: “Haƙiƙa na ji muryar Manzon Allah (SAW) ta yi ƙasa-ƙasa kuma na fahimci cewa lallai akwai yuwuwar a tattare da shi, shin akwai wani abu a wrinki?” sai Ta ce: “Eh.” Sai ta fito da ƙwayoyin burodi da aka yi da sha’ir, sai ta fito da wani mayafi nata, ta naɗe buredin da wani da shu, sannan ta saka shi ƙarƙashin hannuna. Anas ya ce: Sai ta aike ni zuwa wurin Manzon Allah (SAW), sai na tafu, sai na tarar da Manzon Allah (SAW) yana cikin Masallaci tare da mutane, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: “Shin Abu Ɗalha ne ya aiko ka?sai Na ce: “Eh sai Ya ce: “Da abinci?” Na ce: “Eh.” Sai Manzon Allah (SAW) ya ce wa waɗanda suke tare da shi: “Ku miƙe mu tafi"? Sai suka tafi, sai na shiga gabansu, har sai da na zo wurin Abu Ɗalha na faɗa masa, sai Abu Ɗalha ya ce: “Ya Ummu Sulaim, haƙiƙa Manzon Allah (SAW) ya zo da mutane, kuma ba mu da abin da za mu ciyar da su! Sai Ta ce: “Allah da Manzonsa ne suka fi sani.” Sai Manzon Allah (SAW) ya ce, ya Ummu Sulaim me kika tanada mana, sai ta kawo wannan biredin, sai Manzon Allah (SAW) ya umarcni da a gutsuttsura shi, sai aka gutsuttsura shi, sannan Ummu Sulaim ta yi masa miyan romo, sai Manzon Allah (SAW) ya yi addu’a a cikinsa gwargwadon yadda Allah Ya so ya yi, sannan ya ce: “Ku ba mutum goma izini su shigo”, sai aka ba su izini, sai suka shigo suka ci har suka ƙoshi sannan suka fita, sai ya sake cewa: “Ku ba mutum goma izini su shigo", sai aka ba su izni, suka ci har suka ƙoshi sannan suka fita, sai ya kuma cewa: "Ku ba mutane goma izini su shigo", sai dukkan mutanen suka ci, suka ƙoshi, kuma da ma mutanen su saba’in ne[1].

[1]. Bukhari (3578) da Muslim (2040) ne suka rawaito shi.

- Kuma an karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Na rantse da Wanda babu abin bauta da gaskiya sai Shi, lallai na kan kwanta a kan cikina saboda yunwa, kuma lallai na kan ɗaure dutse a kan cikina saboda tsananin yunwa, kuma haƙiƙa wata rana na taɓa zama a kan hanyar da mutane ke fitowa, sai Abubakar ya wuce, sai na tambaye shi game da wata aya daga cikin Littafin Allah, ban tambaye shi ba face sai don ya ciyar da ni, sannan Umar ya wuce, sai na tambaye shi game da wata aya daga cikin Littafin Allah, shi ma ban tambaye shi ba face saboda ya ciyar da ni, sai Abul-ƙasim Annabi (SAW) ya zo wurina, ya yi murmushi lokacin da ya gan ni, ya san abin da ke cikin raina da abin da ke bayyana a fuskata, sai ya ce: "Ya kai Abu Huraira", sai na ce: "Na amsa maka ya Manzon Allah", sai ya ce: "Ka biyo ni", sai ya wuce, ni kuma na bi shi, sai ya shiga gida ya tarar da nono a cikin wata ƙwarya, sai ya ce: “Ya Aba Hirrin! Na ce: “Na'am ya Manzon Allah! Sai ya ce: “Je ka ka kira min Ahlus-Suffa", Ya ce: kuma da ma Ahlus-Suffa baƙin musulunci ne, ba su da iyali, ko dukiya wani ɗan'uwa, sai hakan ya dame ni, sai na ce: “Ta ya ya ɗan wannan madarar za ta ishi Ahlus-Suffa!? Ni na fi cancantar in sha ɗan wannan madara ko zan samu kuzari, kuma ni ma ba in da zai kai min” kuma babu makawa wurin biyayya ga Allah da Manzonsa (SAW), sai na tafi na kira su, sai suka zo suka nemi izinin shigowa, sai aka yi musu izini, sai suka samu wuri suka zauna a cikin gidan, sai ya ce: “Ya Aba Hirrin” Na ce: “Na'am ya Manzon Allah, sai ya ce: “Ka ɗauka ka raba musu", sai na ɗauki ƙwaryar, na fara zuba wa wani mutum, sai ya sha har sai da ya ƙoshi, sai ya miƙa wa wani, shi ma ya sha har sai da ya ƙoshi, har na gama da su gaba ɗaya, sai na juya wurin Annabi (SAW), kowa ya sha ya ƙoshi, sai ya karɓi ƙwaryar, ya ɗora ta a kan hannunsa, sai ya kalle ni ya yi murmushi, sai ya ce: “Ya Aba Hirrin” Na ce: “Na'am ya Manzon Allah", sai ya ce: “saura ni da kai", sai na ce: “Ka faɗi gaskiya ya Manzon Allah", sai ya ce: “Zauna ka sha", sai na zauna na sha, bai gushe ba yana cewa: Ka Sha!", har sai da na

ce: “Na rantse da Wanda Ya aiko ka da gaskiya, ba in da zan shigar da shi!”, sai ya ce: “To, bani in gani.” Sai na miƙa masa ƙwaryar, sai ya yi godiya ga Allah, ya ambaci sunansa, kuma ya sha"[1].

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (6452).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

ABDULLAHI ƊAN UMAR (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne: Abdullah ɗan Umar ɗan Khaɗɗab, inkiyarsa: Abu Abdirrahman, An haife shi ne a Makka shekara goma kafin Hijira.

❖ Tarihnsa da Falalarsa:

Ya kasance (RA) mutumin kirki, mai kyakkyawan mu'amala, ya musulunta tun yana ƙarami tare da mahaifinsa Umar ɗan Khaɗɗab, kuma ya yi Hijira tare da shi zuwa Madīna yana ɗan shekara goma, yaƙin farko da ya halarta shi ne yaƙin Khandaƙ, domin an gabatar da shi ga Annabi (SAW) a ranar Uhud yana ɗan shekara goma sha huɗu amma Annabi bai ba shi dama ba, sai aka sake gabatar da shi a ranar Khandaƙ yana ɗan shekara goma sha biyar, sai Annabi (SAW) ya ba shi dama[1].

Bayan haka bai taɓa fasin wani yaƙi daga cikin yaƙe-yaƙe a zamanin Manzon Allah (SAW) ba, haka kuma a zamanin halifofi shiyayyu, domin da shi aka buɗe Makka, da yaƙin Mu'ta, da Yarmuk, da Yamama, da ƙadisiyya, da Jalula', kuma da shi aka buɗe ƙasar Masar da ƙasashen Afirka.

Ya kasance (RA) daga cikin sahabbai mafiya ilimi, kuma daga cikin mafi yawan rawaitar hadisi, ya zauna a Madina kimanin shekaru sittin yana ba da fatawa.

Kuma ya kasance mai gudun duniya, mai tsoro Allah, mai yawan tsayuwar dare da tahajjudi, mai tsananin tasirantuwa da Alƙur'ani'ani, hadiminsa Nafi'u ya ce: Ibnu Umar bai taɓa karanta

[1]. Bukhari ne suka rawaito shi (4097)

wadannan ayoyin biyu dake karshen Suratul-Bakara ba: ((Kuma in har kuka bayyana abin da yake cikin zukatanku ko kuka boye shi, Allah zai yi muku hisabi a kansa)) [1], face ya yi kuka, ya ce: “Lallai wannan lissafi mai tsanani ne"[2].

Kuma idan ya karanta: ((Ashe lokaci bai yi ba ga wadanda suka yi imani zukatansu su yi taushi da zikirin Allah)) [3], sai ya yi ta kuka har ya rinjaye shi[4].

Ya kasance yana da wata randa dake dauke da ruwa, idan dare ya yi, sai ya yi salla gwargwadon abin da ya saukaka, sannan ya kwanta ya yi barci kadan kamar barcin tsuntsu, sai ya tashi ya yi alwala ya yi salla, ya kan yi haka sau hudu ko biyar a cikin dare[5].

Kuma hakika Annabi (SAW) ya yabe shi ya kuma siffanta shi da nagarta, wannan kuwa ya tabbata a cikin fassarar mafarkin Annabi (SAW) lokacin da ya ga Abdullah kamar a hannusa akwai wani yanki na alhariri, wanda ba ya nuna wani wuri a aljanna, ba face ta tashi da shi zuwa wurin, sai Hafsa ta fada wa Annabi (SAW), sai ya ce: " Lallai dan'uwanki mutumin kirki ne"[6].

Haka kuma (RA) kasance mai karamci ne, mai yawan ciyarwa, mai tausayin talakawa. Yana cewa (RA): “Wata rana na tuna da wannan aya: ((Ba za ku taba dacewa da aiki na alheri ba har sai kun ciyar daga abin da kuke so))[7], sai na tuna abin da Allah Ya ba ni, sai ban

---

1. [Al-Bakara: 284].
2. Ḥilyatul-Auliyā (11061).
3. [Al-Hadid: 16].
4. Ḥilyatul-Auliya (1/305).
5. Siyaru Alāmin-Nubalā’ (3/215).
6. Bukhāri (7015), da Muslim (2478) ne suka rawaito shi.
7. [Ālu Imrān: 92].

samu wani abu da na fi so ba fiye da wata baiwa tawa ba mai suna Rumaisa, sai na ce: ‘Wannan na 'yanta ta saboda Allah"[1].

Wani lokaci Mu'awiya (RA) ya aika masa da dinari dubu ɗari, amma shekara ba ta zagayo ba face babu abin da ya rage masa a ciki [2].

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu a shekara ta 73H, yana da shekara 87 a duniya, kuma an birne shi a Makka a wani wuri da ake kira Wadī Fakh.

[1]. Ḥilyatul-Auliya (103).
[2]. Ḥilyatul-Auliya (103).

Auna fahimtarka a darussan Mako na 46			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma’anar fadinSa Madaukaki: "Nakhirah"?		b
	a. Mara lafiya	b. Rududdugagga	c. Mai ƙarfi
Darasin Hadisi	Tambaya: Menene ake nufi da imani a fadin Annabi (SAW)Tsarki rabin imani ne?		b
	a. Taƙawa	b. Sallah	c. Ingantacciyar aƙida
Darasin Aƙida	Tambaya: Menene hukuncin wanda ya e wajen boka kuma ya gaskata shi akan abin da yake faɗi?		a
	a. Kafurci babba	b. Kafurci ƙarami	c. Shirka ƙarama
Darasin Fiƙihu	Tambaya: Menene jihadin da aka halatta wa mata?		c
	a. Sallah da azumi	b. Yawan karatun Alkur'ani	c. Hajji da Umra
Darasin Sira	Tambaya: Waɗanne mutane ne Manzon Allah (SAW)ya umarci Abu Huraira da ya kira su don shan madara?		a
	a. Ahlus-Suffa	b. Ahlu Badar	c. Ahlu-ƙhandak
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Tambaya: Farkon yaƙin da Ibnu Umar Allah ya ƙara yarda a gare su ya fara halarta ita ce?		b
	a. Yaƙin Uhud	b. Yaƙin Khandaƙ	c. Bude Makka

MAKO NA ARBA'IN DA BAKWAI

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUN-NAZI'AT (2)

﴿ءَأَنتُمۡ أَشَدُّ خَلۡقًا أَمِ ٱلسَّمَآءُۚ بَنَىٰهَا ٢٧ رَفَعَ سَمۡكَهَا فَسَوَّىٰهَا ٢٨ وَأَغۡطَشَ لَيۡلَهَا وَأَخۡرَجَ ضُحَىٰهَا ٢٩ وَٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ دَحَىٰهَآ ٣٠ أَخۡرَجَ مِنۡهَا مَآءَهَا وَمَرۡعَىٰهَا ٣١ وَٱلۡجِبَالَ أَرۡسَىٰهَا ٣٢ مَتَٰعًا لَّكُمۡ وَلِأَنۡعَٰمِكُمۡ ٣٣ فَإِذَا جَآءَتِ ٱلطَّآمَّةُ ٱلۡكُبۡرَىٰ ٣٤ يَوۡمَ يَتَذَكَّرُ ٱلۡإِنسَٰنُ مَا سَعَىٰ ٣٥ وَبُرِّزَتِ ٱلۡجَحِيمُ لِمَن يَرَىٰ ٣٦ فَأَمَّا مَن طَغَىٰ ٣٧ وَءَاثَرَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا ٣٨ فَإِنَّ ٱلۡجَحِيمَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ٣٩ وَأَمَّا مَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ وَنَهَى ٱلنَّفۡسَ عَنِ ٱلۡهَوَىٰ ٤٠ فَإِنَّ ٱلۡجَنَّةَ هِيَ ٱلۡمَأۡوَىٰ ٤١ يَسۡـَٔلُونَكَ عَنِ ٱلسَّاعَةِ أَيَّانَ مُرۡسَىٰهَا ٤٢ فِيمَ أَنتَ مِن ذِكۡرَىٰهَآ ٤٣ إِلَىٰ رَبِّكَ مُنتَهَىٰهَآ ٤٤ إِنَّمَآ أَنتَ مُنذِرُ مَن يَخۡشَىٰهَا ٤٥ كَأَنَّهُمۡ يَوۡمَ يَرَوۡنَهَا لَمۡ يَلۡبَثُوٓاْ إِلَّا عَشِيَّةً أَوۡ ضُحَىٰهَا ٤٦﴾

❖ Fassara

27.Yanzu ku ne halittarku ta fi tsanani ko kuwa sama wadda Shi ne Ya gina ta?

28 .Ya ɗaukaka rufinta Ya kuma daidaita ta.

29 .Ya lulluɓe darenta da duhu Ya kuma fitar da hasken hantsinta.

30 .Ƙasa kuma bayan haka Ya shimfiɗa ta.

31 .Ya fitar da ruwanta da makiyayarta daga gare ta.

32 .Duwatsu kuma Ya kafa su.

33 .Don jin daɗinku da na dabbobinku.

34. Sannan idan mafi girman busar ƙaho ta zo (watau busa ta biyu).

35 .A ranar da mutum zai tuna abin da ya aikata.

36 .Aka kuma bayyana (wutar) Jahimu ga kowane mai gani.

37 .To a wannan ranar duk wanda ya yi ɗagawa.

38 .Ya kuma fifita rayuwar duniya.

39 .To lalle (wutar) Jahimu ita ce makoma.

40 .Duk wanda kuma ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa, ya kuma hana zuciya bin abin da take so.

41 .To lallai Aljanna ita ce makoma.

42. Suna tambayar ka game da alƙiyama, yaushe ne lokacinta?

43 .Me ya gama ka da ambaton lokacinta?

44 .Zuwa ga Ubangijinka ne iyakacin saninta yake.

45 .Kai dai kawai mai gargaɗin wanda yake tsoron ta ne.

46 .Kai ka ce su ranar da za su gan ta ba su zauna ba (a duniya) face wani yammaci ko kuma hantsinta

❖ Saƙon da Surar take ɗauke da shi:

Magana game da Allah da Ranar Lahira.

❖ Ma’anar Baƙin Kalmomi:

رَفَعَ سَمْكَها	Rafa'a samkaha	Ya ɗaukaka rufinta
وَأَغْطَشَ لَيْلَها	Wa Aghɗasha Lailaha	Ya lulluɓe darenta da duhu da faduwar rana

وَأَخْرَجَ ضُحاها	Wa Akhraja Duhaha	Ya kuma fitar da hasken hantsinta da hudowar rana
دَحاها	Dahaha	Ya shimfiɗa ta kuma Ya fitar da abubuwa masu amfani dake cikinta
وَمَرْعاها	Wa Mar'aha	Makiyayarta na daga tsirrai
أَرْساها	Arsaha	Ya kafa su cikin ƙasa kamar turaku
الطّامَّة	Adɗamma	Al'ƙiyama (watau busa ta biyu).
وَبُرِّزَت	Wa Burrizati	Aka bayyana ta matuƙar bayyanawa
المَأْوَى	Al-Ma'wa	Makoma
مقام ربه	Makama Rabbihi	Tsayuwa a gaban Ubangijinsa domin hisbai
أيانَ مُرْسَاهَا	Ayyana Mursaha	Yaushe ne lokacin faruwarta?
فِيمَ أنتَ مِن ذِكْرَاهَا	Fi ma Anta Min Zikraha	Me ya gama ka da ambaton lokacinta?
عشِيَة	Ashiyyatan	Daga tsakanin lokacin azahar zuwa faduwar rana
ضُحاها	Duhaha	Lokacin daga fitowar rana zuwa rabin yini

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

Allah Maɗaukaki Ya'ana mayar da martani ga masu ƙaryata tashin ƙiyama da hujja bayyananna ƙwarai, wato halittar manyan sammai, masu inganci da ƙarfi, da tsayi mai ban mamaki, da abin da ke cikinsu na duhun dare da hasken rana, da ƙasa mai yalwa da faɗi, da abin da ke kanta na duwatsu kafaffu, da abubuwa masu amfanoni da aka adana a cikinta, don haka, idan wannan babbar ƙiyama ta zo, da tsanani ta mafi girma, a lokacin ne kowane mutum zai tuna da abin da ya aikata a duniya na alheri ko sharri, kuma zai san cewa aikinsa shi ne sinadarin ribarsa da asararsa a wannan ranar, don haka, duk wanda ya kyautata to zai samu kyakkyawan sakamako, kuma duk wanda ya mummuna aiki to kada ya zargi kowa sai kansa, sannan Allah Maɗaukaki Ya ambaci tambayar masu taurin kai, masu ƙaryatawa, game da lokacin da tashin ƙiyama zai zo, sai Ya amsa musu da cewa babu wani amfani cikin saninsu ga hakan, kuma babu wata maslaha ta addini ko ta duniya, bari dai, maslaha tana cikin ɓoyuwarsa gare su, don wanda ke tsoron zuwanta ya amfana da gargaɗi, sai ya shirya kuma ya yi aiki, amma mai ƙaryatawa, da ma taurin kansa ya samo asali ne daga ƙin gaskiya, don haka amsa tambayarsa wargi ne da Allah ke tsarkaka daga shi.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Lallai halittar sammai da ƙasa da abin da ke cikinsu hujja ce a kan girman Allah, da ikonsa na dawo da abin da ya shuɗe daga cikinsu.

2) Sanin lokacin tashin ƙiyama yana daga cikin ɓoyayyun al’amura wanda ba wanda ya san su sai Allah Maɗaukaki.

3) Lallai tsoron Allah Maɗaukaki da hana rai bin son zuciya yana daga cikin manyan sababban shiga Aljanna.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

DAGA CIKIN ZIKIRORIN DA SUKE KARE BAWA

An karɓo daga Abu Huraira (RA) ya ce: Wani mutum ya zo wurin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, ya ce: "Ya Manzon Allah, maciji ya sare ni jiya da daddare, sai Annabi ya ce: **(Da da yamma ka fadi cewa: A'uzu bi kalimatillahit-Tammati min Sharri Ma Khalak, da bai cutar da kai ba)[1].**

❖ Sharhi:

Sabubban da suke kare musulmi daga sharri da cuta nau'i ne biyu:

Na farko: Sababba na zahiri: Misali: shan magani yayin cuta, da kariya ta hanyar sanya tufafi masu kauri a lokacin sanyi.

Na biyu: Sababba na shari'a: Misali: kula da zikirin safe da na yamma, yin sallar asubahi, da yin sallar isha'i a cikin jam'i.

A cikin wannan hadisin Annabi (SAW) ya bayyana ɗaya daga cikin sababba na shari'a da suke kare musulmi -da izinin Allah- daga sharruka da cutarwa, shi ne ya ce: "Ina neman tsari da cikakkun kalmomin Allah daga sharrin abin da Ya halitta", ma'anarsa: Ina neman tsari kuma ina fakewa da cikakkun kalmomin Allah waɗanda ba su da wata tawaya ko aibi, daga kowanne sharri cikin abin da Ya halitta, idan ya faɗe hakan, wannan zikiri zai zama sababin da Allah zai tsare shi daga saraar maciji da sauran sharrori, saboda haka ya kamata musulmi ya haddace wannan zikiri ya riƙa yawan faɗinsa a ko da yaushe a safiyarsa da yammansa.

Lokacin zikirin safe yana farawa ne daga bayan sallar asuba har zuwa fitowar rana, lokacin zikirin yamma kuma yana farawa ne

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2709).

daga bayan sallar la’asar har zuwa faɗuwar rana, idan kuwa ya manta da su a lokacinsu, to zai iya yi duk lokacin da ya tuna.

❖ Abubuwan da z a koya daga Hadisin:

1) Ƙarfin dogaron Annabi (SAW) ga Ubangijinsa, da ambatonsa gare shi.
2) Bayanin kwaɗayin Annabi (SAW) wajen koyar da al’ummarsa abin da zai amfanar da su.
3) An shar'anta wa musulmi ya kula da dukkan sababba na shari’a da na zahiri, kuma ya riƙa aiki da su duka.
4) Muhimmancin zikirorin safe da na yamma; domin suna kare musulmi da izinin Allah daga sharruka da shaiɗanu.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

RUƘIYYA

Kalmar "Ar-Ruƙa": Jam'in kalmar ruƙya ce, ma'anarta ita ce karatu ga mara lafiya.

Kuma ta kasu zuwa nau'i biyu:

Nau'i na farko: Shi ne wanda babu shirka a cikinsa, wato a karanta wani ɓangare na Alƙur'ani ga mai mara lafiya, ko a nemi tsari da sunayen Allah da sifofinsa, ko da wasu addu'o'in da suka halatta, wannan ya halatta, domin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya taɓa yin ruƙiya, kuma ya umurni da ita, an karɓo daga Auf ɗan Malik ya ce: "A zamanin jahiliyya mu kasance muna yin ruƙiya, sai muka ce: Ya Manzon Allah! Ya ya kake ganin hakan?" Sai Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: (Ku bijiro mini da ruƙiyarku, babu laifi cikin ruƙiya muddin ba ta ƙunshi shirka ba) [1].

Ibnu Hajar ya ce: "Malamai sun yi ijma'i kan cewa ruƙiyya tana halatta idan aka cika sharuɗɗa uku:

- Ta kasance da maganar Allah, ko da sunayensa da sifofinsa.
- Kuma ta kasance da harshen Larabci da abin da ake iya fahimtar ma'anarsa.
- Kuma a ƙudurta cewa lallai ruƙiyya ba ta warkarwa da kanta, sai da ƙaddarar Allah Maɗaukaki [2].

❖ **Yadda ake yin ta shi ne kamar haka:**

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2200).
[2]. Fathul-Bari (10/195).

A karanta, a busa a tofa ga mara lafiya; ko a karanta cikin ruwa, sai a ba shi ya sha; ko kuma a karanta a ƙasa sai a shafa a inda ciwon yake, A’isha Allah ya ƙara mata yarda tana cewa:

“Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya kasance idan zai kwanta a gadonsa, sai ya yi tofi a tafukan hannuwansa, ya karanta "Ƙul huwallahu Ahad", da falaƙi da Nasi a tare, sannan ya shafi fuskarsa da inda da hannuwansa suka iya isa daga jikinsa, A’isha ta ce: “Lokacin da Manzon Allah ya kamu da ciwo, ya kasance yana umarta na da in yi masa haka"[1].

Kuma ya zo a cikin hadisin Sabit bin Ƙais an cewa lallai: Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ɗibi ƙasar Budhan, ya sanya ta cikin wata ƙwarya, sannan ya yi togi a cikinta, ya zuba a kan mai ciwo[2].

Nau’i na biyu daga cikin nau'ukan Ruƙiyya: Shi ne wanda akwai shirka a cikinsa, ita ce wacce ake neman taimako da wanin Allah a cikinta, ko a kira waninsa, kamar ruƙiyya da sunayen aljannu, ko Mala’iku, ko Annabawa, ko Mutanen kirki, ko wasu makamantansu, wannan shirka ce babba, kuma ba ta amfanarwa da komai, kuma ita ce wadda Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya nufe ta da faɗarsa: (Lallai ruƙiyya, da layu, da sihirin jawo ƙauna — dukkansu shirka ne[3].

Kuma an karɓo daga Ibnu Mas‘ud (RA) ya ce: "Lallai Allah bai sanya waraka cikin abin da Ya haramta muku ba"[4].

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (5748).
[2]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (3885).
[3]. Ahmad (3615) da Abu Dawuda (3883) ne suka rawaito shi.
[4]. Bukhari ne ya rawaito shi (5614).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

WURAREN DA AKE ƊAUKAR HARAMAR HAJJI DA UMRA

Wuraren ɗaukar haramar Hajji da Umra: Su ne iyakokin da ba ya halatta ga mai mahajjaci ko mai Umrah ya ƙetare su ba tare da ɗaukar niyya ba.

Kuma haƙiƙa Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya bayyana su cikin hadisin Ibnu Abbas Allah ya ƙara musu yarda inda ya ce: "Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya iyakance wa Mutanen Madīna – Zhul-Hulaifa, Juhfa ga mutanen Sham, Ƙarnuk-Manaziil ga mutanen Najd, Yalamlam ga mutanen Yaman, ya ce: Waɗannan wuraren ɗaukar niyya ne g mutanen dake zaune a wurin, da waɗanda suke bi ta wurin waɗanda ba wurin suke zaune ba, daga cikin maniyyata Hajji ko Umrah, waɗanda ke zaune a garuruwan dake tsakanin waɗannan wurare da Makkah, to zai ɗauki harama ne daga inda yake, har su ma mutanen Makka, daga Makka za su ɗauki harama) [1].

❖ **Hikimar hakan:** Yayin da Ɗakin Allah mai alfarma ya kasance wuri ne mai girma da daraja, sai Allah Ya sanya masa kariya – wato alfarma ,

Kuma Ya sanya wa wannan alfarmar yana da wani kariya na daban, wanda shi ne wuraren ɗaukar harama, wato waɗanda ba ya halatta a ƙetare su ba tare da ɗaukar niyya ba– domin girmama Ɗakin Allah mai alfarma.

[1]. Bukhari (1524), da Muslim (1181) ne suka rawaito shi.

Ga cikakken bayani game da su kamar haka:

Miƙatin Zhul-Hulaifa: Wannan shi ne wurin da mutanen Madīna suke ɗaukar harama, a yanzu yana cikin iyakar birnin Madīna ne, kuma ana kiransa “Masjidul-Miƙat.”

Miƙatin Juhfa: Wannan shi ne wurin da mutanen Sham, da Misra, da Maghrib suke ɗaukar harama, a zamanin yanzu daga Rabigh suke ɗaukar harama, saboda kafin Juhfa take, kuma tana kusa be da ita, kuma nisan wannan miƙati daga Makka kusan kilomita 200 ne.

Miƙatin ƘararnuI-Manazil: Wannan shi ne wurin da mutanen Najd suke ɗaukar harama, kuma ana kiransa a yanzu da As-Sail, kuma daga wurin akwai hanyoyi biyu zuwa Makka: ɗaya ta hanyar As-Sail, ɗaya kuma ta hanyar Jabalu Kara, kuma nisan wannan miƙati daga Makka kusan kilomita 70 ne.

Miƙatin Yalamlam: Wannan shi ne wurin da mutanen Yaman suke ɗaukar harama, kuma yana da nisan kilomita 70 ne daga Makka.

Miƙatin Zhatu Irƙin: Wannan shi ne wurin da mutanen Iraƙi da na ƙasashen gabashin duniya ke ɗaukar harama, kuma yana da nisan kilomita 70 daga Makka.

Saboda haka, waɗannan su ne Miƙatoti da aka ambata daga nan ne mazauna wurin ke ɗaukar harama, haka kuma wanɗanda suke ratsa wa ta cikinsu daga wasu yankuna, da nufin Hajji ko Umrah, dole ne su ɗauki harama daga wurin, idan kuwa suka ƙetare su ba tare da ɗaukar harama ba ihrami ba, ti wajibi ne su koma wurin idan hakan zai yiwu, idan kuma hakan bai yiwu ba, to fidiya ta wajaba a kansa, wato yanka akuya a garin Makka ga talakawan harami, wanda kuma hanyarsa ba ta ratsawa ta wurin da miƙati yake, to zai ɗauki harama

ne idan ya iso wuri mafi kusa da miƙatin; saboda faɗin Umar (RA) cewa: "Ku duba wurin da yake setin miƙati daga hanyarku"[1].

Haka ma wanda yake cikin jirgi, zai ɗauki harama ne idan jirgin ya kai setin ɗaya daga cikin miƙatotin daga sama, saboda haka, yana da kyau ya shirya kafin jirgin ya tashi: ya yi wanka, ya sanya ihrami, idan jirgin ya kai setin Miƙatin, sai ya ɗauki harama, yana cikin jirgin, kuma ba ya halatta ya jinkirta ɗaukar harama har sai ya sauka a filin jirgin Jidda, domin Jidda ba Miƙati ba ce sai dai ga mazaunanta.

Miƙatin mutanen Makka: Waɗanda suke zaune a Makka, suna ɗaukar haraman Hajji ne daga gidajensu, amma idan za su yi Umrah, sai su fita zuwa wajen harami, kamar At-Tan‘im da Al-Ji‘irrana.

Mutanen dake zaune a wajen Harami: Waɗanda gidajensu ke tsakanin Makka da sauran Miƙatoti, za su ɗauki haramar Hajji da Umra ne daga gidajensu.

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (1531).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Ba shi kariya daga maƙiya:

Daga cikin alamomin Annabtar Annabi A tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi akwai cewa Allah Maɗaukaki Ya kare shi tun daga lokacin da aka aiko shi da saƙo har zuwa lokacin da ya bar duniya zuwa matsayi mafi ɗaukaka, Allah Ya kare shi daga makirce-makircen mushrikai, Ya tsare shi daga izgilancin masu izgili, Ya kuma kare addininsa har zuwa Ranar Ƙiyama, Allah Madaukaki Ya ce: ((Lalle Mu Mun isar maka (sharrin) masu izgili () Su ne waɗanda suke sanya wani abin bauta tare da Allah. Ba ko da daɗewa ba za su sani)) [1]. kuma Ya ce: ((Lalle mai ƙin ka shi ne mai yankakken alheri)) [2]. Ya kuma cewa: ((To da sannu lAllah zai isar maka da su, kuma Shi Mai ji ne, Mai gani)) [3]. Ya sake cewa: ((Allah kuwa Shi ne Yake kare ka daga sharrin mutane)) [4].

Kuma da Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare ba da gaske shi Manzon Allah bane, da Allah Bai tabbatar da shi ba, kuma da Bai taimake shi ba, ku da Bai ƙarfafe shi Ya ɗaukaka shi ba, Kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Kuma da ya ƙaga Mana wasu maganganu () Tabbas da Mun kama shi da ƙarfi () Sannan da Mun yanke masa jijiyar zuciyarsa () Sannan kuma ba wani ɗaya daga cikinku da zai kare shi))[5].

Daga cikin kariyar da Allah Ya yi masa akwai abin da Abu Huraira (RA) ya rawaito cewa: Abu Jahl ya ce: "Shin Muhammadu yana

---

[1]. [Al-Hijr: 94–96].
[2]. [Al-Kauthar: 3].
[3]. [Al-Baƙara: 137].
[4]. [Al-Ma'ida: 67]
[5]. [Al-Haƙƙa: 44–47].

sanya fuskarsa a ƙasa a gabanku, wato yana sallah-" Sai aka ce masa: "Eh". Sai ya ce: "Ina rantsuwa da Lata da Uzza, idan na ganshi yana yin haka, sai na taka wuyansa, sai ya tafi ya tarar da Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana salla, amma sai suka ga yana ja da baya, yana kakkare kansa da hannayensa, sai aka ce masa: Me ya same ka ne? Sai ya ce: "Lallai na tarar da wani rami cike da wuta tsakanin ni da shi, da abubuwan ban tsoro, da fuka-fukai, sai Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: (Da ya matso kusa da ni, da Mala'iku sun cafke shi sun yi gunduwa gunduwa da shi) [1].

Kuma daga cikin haka akwai abin da Jabir ɗan Abdullah Allah ya ƙara musu yarda ya ruwaito cewa: Ya fita yaƙi tare da Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi zuwa wani wuri dake gaban Najd, yayin da Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yake hanyarsa ta dawowa, sai ya sauka ƙarƙashin wata bishiya mai suna (Samura), ya rataye takobinsa a kanta, mutane suka watse suna neman inwanta ƙarƙashin bishiyoyin dake wurin, yayin da suka yi barci, sai wani mutum daga cikin mushrikai ya zo, takobin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana rataye a kan bishiyar, sai ya zare takobin, ya ce: Shin kana jin tsorana?" Sai Annabi (SAW) ya ce: "A'a ". Sai ya ce: "To wa zai hana ni in kashe ka?" Sai Annabi (SAW) ya ce: "Allah", sai mutumin ya mayar da takobin cikin gidansa, kuma Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi bai yi masa uƙuba ba[2], sai Allah Maɗaukaki Ya saukar da faɗinsa cewa: (Allah kuwa Shi ne Yake kare ka daga sharrin mutane) [3].[4].

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2797).
[2]. Bukhari (2910) da Muslim (843) ne suka rawaito shi.
[3]. [Al-Ma'ida: 67]
[4]. Sahihu Asbabin-Nuzul (6/273)

ASABAR: DARASI CIKIN SAHABBAI

SAFWAN ƊAN MU'AƊƊAL (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Safwan ɗan Mu'aɗɗal As-Sulamī, ana inkiya da Abu Amr.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Ṣafwan (RA) yana daga cikin salihan sahabban Annabi Muhammad (SAW)kuma ya kasance mawaƙi ne, jarumi kuma gwarzo.

Ya halarci yaƙin Gwalalo, kuma bai taɓa fashin wani yaƙi tare da Manzon Allah (SAW)ba bayan haka.

Ya fi shahara a lokacin labarin (Ifk) wato ƙage da aka yi wa A'isha Allah Ya ƙara mata yarda, inda Annabi (SAW) ya yabe shi yana mai cewa: (Ban san komai game da shi ba sai alheri).[1]

Wannan ya faru ne a lokacin yaƙin Muraisi shekara ta biyar bayan hijira, Safwan Allah Ya yarda da shi yana tafiya a bayan rundunar sojoji yana tattara abubuwan da suka faɗi a baya, sai ya ga wani mutum, ya kusanto, sai ya ga A'isha ce Allah ya ƙara mata yarda ta tsaya domin neman abin wuya da ya ɓace, sai ya ce: "Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un", daga nan bai ƙara magana ba, sai ya kwantar mata da raƙuminsa ta hau, shi kuma ya ja raƙumin har suka isa wajen mutane, daga nan sai masu ƙage suka fara yaɗa labarin ƙaryar da aka yi game da ita, sai Annabi (SAW) ya miƙe tsaye, Ya yi godiya ga Allah kuma ya yabe Shi da abin da Ya cancanta, sai ya ce: (Ya ku jama'ar Musulmi! Wane ne zai taimake ni daga wasu mutanen da suke cutar da ni game da iyalina?! Na rantse da Allah, ban taɓa sanin wani mummunan abu game da iyalina ba, kuma suna zargin wani

[1]. Bukhari (2637), da Muslim (2770) ne suka rawaito shi.

mutum daga cikin sahabbaina, kuma ni ban taɓa sanin wani mummunan abu game da shi ba, kuma ban taɓa fita wani yaƙi ba face ya fita tare da ni).[1]

Sai Allah Maɗaukaki Ya saukar da ayoyin da suka tabbatar da tsarkakarta .

❖ Rasuwarsa:

Ya rasu ne Sumaisaɗ, wani ƙauye dake yammacin kogin Furat a shekara ta 60 bayan Hijira, a ƙarshen mulkin Mu’awiya (RA).

[1]. Bukhari (2637), da Muslim (2770) ne suka rawaito shi.

Auna fahimtarka a darussan Mako na 47			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ma'anar faɗin Allah Maɗaukaki: "Dahaha?**		b
	a. Ya naɗeta	b. Ya shimfiɗa ta, kuma ya sanya abubuwa masu amfani a cikinta	c. Ya kyakketa ta
Darasin Hadisi	**Tambaya: Yaushe ake fara lokacin zikirin na yamma yake farawa?**		a
	a. Bayan sallar la'asar har zuwa faɗuwar rana	b. Bayan sallar isha'i har zuwa fitowar rana	c. Bayan Sallar Duha har zuwa kiran sallar La'asar
Darasin Aƙida	**Tambaya: Ruƙiyyar da ta halatta ita ce:**		a
	a. Wadda take daga Alƙur'ani	b. Wacce ta tabbata daga Sahabbai	c. Wacce ta kuɓuta daga shirka
Darasin Fiƙihu	**Tambaya: Mutanen da ke zaune a cikin harami (Makka), daga ina suke ɗaukar harama don aikin Hajji?**		a
	a. Daga gidajensu	b. Daga Tan'im	c. Daga Ji'irrana
Darasin Sira	**Tambaya: Wanda ya yaga wasikar Annabi (SAW) shi ne?**		b
	a. Hiraƙil	b. Kisra	c. Muƙauƙis
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin shahararrun abubuwa da suka faru a rayuwar Ṣafwan (RA) akwai:**		a
	a. Lamarin Al-Ifk (Labarin ƙage)	b. Rushe Al-Uzza	c. Hijira zuwa Habasha

MAKO NA ARBA'IN DA TAKWAS

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUN-NABA'I (1)

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

عَمَّ يَتَسَآءَلُونَ ١ عَنِ ٱلنَّبَإِ ٱلۡعَظِيمِ ٢ ٱلَّذِي هُمۡ فِيهِ مُخۡتَلِفُونَ ٣ كَلَّا سَيَعۡلَمُونَ ٤
ثُمَّ كَلَّا سَيَعۡلَمُونَ ٥ أَلَمۡ نَجۡعَلِ ٱلۡأَرۡضَ مِهَٰدٗا ٦ وَٱلۡجِبَالَ أَوۡتَادٗا ٧ وَخَلَقۡنَٰكُمۡ أَزۡوَاجٗا
٨ وَجَعَلۡنَا نَوۡمَكُمۡ سُبَاتٗا ٩ وَجَعَلۡنَا ٱلَّيۡلَ لِبَاسٗا ١٠ وَجَعَلۡنَا ٱلنَّهَارَ مَعَاشٗا ١١ وَبَنَيۡنَا
فَوۡقَكُمۡ سَبۡعٗا شِدَادٗا ١٢ وَجَعَلۡنَا سِرَاجٗا وَهَّاجٗا ١٣ وَأَنزَلۡنَا مِنَ ٱلۡمُعۡصِرَٰتِ مَآءٗ ثَجَّاجٗا
١٤ لِّنُخۡرِجَ بِهِۦ حَبّٗا وَنَبَاتٗا ١٥ وَجَنَّٰتٍ أَلۡفَافًا ١٦

❖ **Fassara:**

Da sunan Allah Mai rahama Mai jin ƙai

1. Akan me suke tambayar juna?
2. Akan wani labari mai girma.
3. Wanda suke sabani a cikinsa.
4. A'aha! Za su sani nan gaba.
5. Sa'an nan a'aha! Za su sani nan gaba.
6. Ashe ba Mu sanya ƙasa shimfiɗa ba.
7. Kuma duwatsu turaku.
8. Kuma Mun halicce ku maza da mata.
9. Kuma Mun sanya barcinku hutawa gare ku.
10. Kuma Mun sanya dare sutura gare ku.
11. Kuma Mun sanya yini lokacin neman arziki.
12. Kuma Mun gina a saman ku sammai bakwai masu ƙarfi?
13. Kuma Mun sanya rana fitila mai tsananin haske.
14. Kuma Mun saukar daga da ruwa ruwa mai yawan kwarara daga gajimare.

15. Domin mu fitar da shi da hatsi da tsirrai.
16. Da kuma lambuna masu yalwa da cike da bishiyoyi.

❖ Sakon da Surar take ɗauke da shi:

Bayani kan dalilan dake nuna ikon Allah wajen tayar da matattu, da tsoratar da masu ƙaryata shi.

❖ Bakin Kalmomi

عَمَّ	Amma	A kan me?
النبأ العظيم	Annaba'il-Azeem	Labari mai girma, wato Alƙur'ani da ke ɗauke da labarin tashin kiyama
مِهَادًا	Mihada	Shimfiɗa tamkar tabarma
أوتادًا	Autada	Turaku da ke riƙe da ƙasa
أزواجًا	Azwaja	Maza da mata
سُبَاتًا	Subata	Hutu ga jikinku
لِبَاسًا	Libasa	Sutura gare ku daga duhun dare.
مَعَاشًا	Ma'asha	Lokacin neman rayuwa.
سِرَاجًا وَهَّاجًا	Sirajan Wahhaja	Fitila mai haske sosai, mai haskakawa
المُعصِرَات	Al-Mu'sirat	Giza-gizai dake ɗauke da ruwan sama.
ثَجَّاجًا	Sajjaja	Mai kwarara
جَنَّاتٍ أَلْفَافًا	Alfafa	Lambuna waɗanda ke cike da bishiyoyi

❖ Ma’anar Ayoyin a Dunƙule:

Wannan surar ta fara ne da tambaya mai girma, wanda ake nufin kambamawa da shi: A kan me ne ne mushrikai suke shakka, kuma sashinsu ke tambayar sashe? Sai amsa ta zo kan cewa shakkarsu a kan wani labari ne mai girma, kuma shi labarin ba ya karbar shakka, wato Alƙur’ani da abin da ya ƙunsa na labaran tashin Ƙiyama da tayarwa, domin haƙiƙa jayayyarsu da shakkunsu ya yawaita a cikinsa, wani lokaci su kira shi sihiri, wani lokaci su kira shi da waƙa, wani lokaci kuma su ce tatsuniyoyin mutan farko ne, kuma lamarin ba kamar yadda suke zato ba ne, kuma da sannu za su san sakamakon ƙaryatawarsu.

Sa’an nan Allah Maɗaukaki Ya lissafo dalilan dake tabbatar gaskiyar da wannan labari mai girma, wato ni’imominsa da Ya watsa a cikin duniyarsa; ga ƙasa nan an shimfiɗe ta domin mutane, kuma an tanade ta domin amfaninsu, kuma ga duwatsu nan an kafa su a matsayin turaku don su hana ta girgiza, kuma ga halittu nan an halicce su maza da mata domin kowannensu ya sami nutsuwa da ɗayan, sai a samu soyayya da jinƙai da kuma zuriyya, kuma ga dare nan yana lullube mutane da kwanciyar hankali, kuma barci yana samar musu da hutu, sammai kuma, suna ɗauke da cikakken ƙarfi, rana kuwa tana dauke da haskenta da zafinta da amfaninta ga mutum da dabba da tsirrai, ruwan sama kuwa yana sauka da yawa, kuma bayan saukarsa sai a samu tsiron hatsi da gonaki masu yalwa dake cike da bishiyoyi. To, wanda Ya yi baiwa da waɗannan ni’imomi masu girma, ta ya ya za a kafirce masa, kuma a ƙaryata labarinsa?!

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Tabbatar da gaskiyar labari mai girma (Al-ƙur’ani), ta hanyar bayyana alamominsa da hujjojinsa.
2) Kyakkyawan tsari da Allah Ya yi wa halitta dalili ne na ikonsa kan sake dawo da shi bayan mutuwa.
3) Falalar Allah ga mutane, da abin da Ya halitta kuma Ya hore musu su don sauƙaƙa musu more rayuwa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

YALWAR RAHAMAR ALLAH DA TSANANIN AZABARSA

An karbo daga Abu Huraira (RA), cewa Manzon Allah (SAW) ya ce: **(Da mumini ya san abin da Allah Ya tanda na uƙuba, babu wanda zai yi kwaɗayin samun Aljannarsa; kuma da kafiri ya san abin da Allah Ya tanada na rahama, to da babu wanda zai yanke ƙauna daga Aljannarsa)**[1].

❖ Sharhi:

Ya kamata Musulmi a hanyarsa ta komawa zuwa ga Allah ya haɗa tsakanin tsoron azabar Allah da kuma fatan rahamarsa; domin kada ya yanke ƙauna daga rahamarsa ya tsananta wa kansa, kuma kada ya ruɗu da girman afuwarsa ya yi sakaci wurin aikata zunubi, kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ka faɗa wa bayina cewa lallai Ni ne Mai gafara Mai jin ƙai () Kuma lallai azabata ita ce azaba mai tsananin zafi))[2], saboda haka, idan duka biyun suka haɗu a cikin zuciyar mumini, Allah zai ba shi abin da yake fata, kuma Ya tsare shi daga abin da yake tsoro.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) Tsoron Allah na gaskiya shi ne yake hana ma'abocinsa aikata haram, don haka ba zai bar salla ba, ba zai yi ha'inci ba, ba zai yi sata ba, domin shi yana jin tsoron Allah.
2) Fata ta gaskiya ga Allah ita ce wacce take haɗe da aiki; sai ya aikata kyawawan ayyuka don neman falalar Allah da ladansa, kuma ya tuba daga miyagun ayyuka don neman gafarar Allah da rahamarsa.
3) Daga cikin ribar tsoron Allah ta gaskiya, akwai cewa bawa kada ya dogara da aikinsa sai ya ruɗu da shi.

---

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2755).
[2]. [Al-Hijr 49 -50].

4) Daga cikin ribar fata na gaskiya, akwai cewa bawa ba ya rena wani aiki na alheri; domin ta yiwu ƙaramin aiki ya jawo rahamar Allah.

5) Fatan samun rahama ba tare da tuba ko aikin alheri ba, rudi ne da talala daga shaiɗan.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

LAYU

Kalmar "Tama'im": Jam'i ne kalmar *(Tamīma*), wato laya, abin da ake ratayawa ga marasa lafiya ko yara ko dabbobi na don kariya daga cuta ko dauke ta, kuma tana ƙasancewa ne a siffar awarwaro, sarƙoƙi, da abubuwan da ake ratayawa a wuya, da makamantansu.

❖ Layu nu'i biyu ne:

Nau'i na farko: **Layun da ake yi daga Alƙur'ani, wannan nau'in malamai sun yi saɓani a kan hukuncin rataya shi zuwa ga maganganu biyu**:

Magana ta farko: Halalasci, kuma wannan shi ne ra'ayin Abdullah bin Amr Allah ya ƙara musu yarda.

Magana ta biyu: Haramci, kuma wannan shi ne ra'ayin Ibnu Mas'ud, da Ibnu Abbas, da Hudhaifa bin Al-Yaman, da Uƙba bin Amir, da Ibnu Hakim Allah ya ƙara musu yarda, kuma wannan shi ne ra'ayin wasu daga cikin Tabi'ai, ciki har da daliban Ibnu Mas'ud.

Wannan magana ta biyu ita ce ta fi inganci ta fuskoki guda uku:

- Ta farko: Gamammen hani dake cikin hadisai masu zuwa, kuma babu abin da ya keɓe wannan gamewar.
- Ta biyu: Toshe kafar fitina (Saddul-Zari'a), domin halatta shi hanya ce da za ta kai ga rataya abin da bai halatta ba.
- Ta uku: Cikin rataya Alƙur'ani akwai raina darajarsa, saboda mutum zai iya shiga bayan gida da makamantansa da shi.

Nau'i na biyu na Layu: Shi ne wanda ba da Alƙur'ani aka yi shi ba; kamar waɗanda aka yi da ƙwayoyin tagulla, da na zare, da na fata, da na ƙyalle, da sauransu, wannan haramun ne bisa ijma'i,

kuma yana daga cikin shirka, domin dogaro ne da wanin Allah Maɗaukaki.

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: (Duk wanda ya rataya laya to lallai ya yi shirka)[1], kuma ya ce (SAW): (Duk wanda ya rataya wani abu, to an bar shi da abin da ya rataya)[2]. Ma'ana: Allah zai bar shi da abin da ya rataya, don haka, duk wanda ya dogara da halittu, da layu, da ƙaburbura, to, Allah zai taɓar da shi, ya bar shi da su, kuma ba za su amfane shi da komai ba, ko su tunkude masa wata cuta, sai aƙidarsa ta lalace saboda hakan, alakarsa da Ubangijinsa ta yanke, amma wanda ya dogara ga Allah, kuma ya nemi mafaka a wurinsa, ya miƙa al'amarinsa gare shi, to Allah zai wadatar da shi, ya kare shi, ya kusanto masa dukkan wani abu mai nisa, ya sauƙaƙa masa dukkan abu mai wuya.

[1]. Ahmad ne ya rawaito shi (4/154).
[2]. Tirmizi ne ya rawaito shi (2072).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

ƊAUKAR HARAMAR HAJJI KO UMRA

❖ Sunnonin Ɗaukar Harama:

Ana so wanda yake son yin Hajji ko Umarah ya shirya kafin ɗaukar Harama ta hanyar yin wasu abubuwan da ake so, domin ya fara wannan ibada cikin mafi kyawun hali, daga cikin waɗannan abubuwan akwai:

1. Wanka, (SAW) ya yi wanka saboda daukar Harama[1].
2. Tsaftace jiki, ta hanyar cire abin da shari'a ta yarda a cire; kamar aske gashin baki, aske gashin hamata, da na mara idan akwai buƙata, idan babu buƙata, ba zai cire ba, domin ana aikata hakan ne idan akwai buƙata, kuma ba ya daga cikin abubuwan da suka keɓanci ɗaukar Harama.
3. Shafa turare a jiki, saboda maganar A'isha (RA) cewa: "Na kan shafa wa Manzon Allah (SAW) turare a ihraminsa kafin ya ɗauki Harama, da lokacin da ya gama aikin Hajji kafin ya yi ɗawafin Ɗakin Allah[2]".
4. Zabar farin gyauto da kwarjalle masu tsafta ga maza, saboda maganar Annabi (SAW): "Mafi alherin tufafinku su ne farare, saboda haka, ku sanya su kuna raye, kuma ku yi mamatanku likkafani da shi"[3].
5. Ɗaukar Harama bayan yin salla, saboda abin da Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya yi[4].
6. Yawaita yin Talbiya tun daga lokacin Ɗaukar Harama, yana cewa: "Labbaika-llahumma labbayk, labbaika la sharika laka labbaik, innal-hamda wa-n-ni'mata laka wal-mulk, la sharika lak[5]".

---

1. Tirmizi ne ya rawaito shi (830).
2. Bukhari da (1539) da Muslim ne suka rawaito shi.
3. Abu Dawud (1970, Tirmizi (949) suka rawaito shi.
4. Bukhari (1550) ne ya rawaito shi.
5. Bukhari: (1549) da Muslim (1184) ne suka rawaito shi

❖ Yadda ake Ɗaukar Harama:

Aikin farko shi ne "Iḥram" wato ɗaukar Harama, kuma ma'anar Iḥram ita ce: **niyyar shiga cikin ibadar Hajji ko Umarah.**

An kira shi (Ihrami) ne wato ɗaukar Harama saboda musulmi yana haramta wa kansa abin da a baya yake halatta gare shi; kamar aure, shafa turare, aske gashi da makamantansu.

Idan ya yi nufn shiga cikin ibada, zai yi niyya da furuci, yana cewa: "Labbaika-llahumma hajjan" ko "Labbaika-llahumma umratan".

Idan kuma yana tsoron wani abu da zai iya hana shi cika ibadar saboda wani uzuri ko rashin lafiya, ana so ya yi sharadi bayan ya ɗauki Haramar, ya ce: "Allahumma mahilli haythu habastani", Ya Allah, wurin da ka tsayar da ni shi ne wurin fita daga haramata"[1].

[1]. Bukhari: (5089) da Muslim (1207) ne suka rawaito shi

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTKARSA (SAW)

❖ Warkar da marasa lafiya:

- **Daga cikin haka akwai**: Warkar da idanun Aliyu ɗan Abi Ɗalib (RA) — da izinin Allah —; an karɓo daga Sahl ɗan Sa'ad (RA) cewa Manzon Allah (SAW) ya ce a ranar Yaƙin Khaibar ya faɗi cewa: "Zan ba wani mutum mai ƙaunar Allah da Manzonsa wannan tutar, kuma Allah zai ba da nasara ta hannunsa", Sai mutane suka shafe dare su suna tattaunawa, wane ne za ba. Da gari ya waye, suka zo wurin Manzon Allah (SAW), kowanne yana fatan a ba shi, sai ya ce: Da gari ya waye, suka zo wurin Manzon Allah (SAW), kowanne yana fatan a ba shi, sai ya ce: "Ina Aliyu ɗan Abi Ɗalib?" Aka ce: Yana fama da ciwon ido, sai aka aika a kira shi, sai aka zo da shi, sai Manzon Allah (SAW) ya yi masa tofi a idanuwansa, ya yi masa addu'a, sai ya warke tamkar bai taɓa ciwo ba. "Ka tafi, kada ka Daga cikin hujjojin Annabcinsa: Warkar da idanun Ali bn Abi Ɗalib (RA) — da izinin Allah —; daga Sahl ɗan Sa'ad (RA) cewa Manzon Allah (SAW) ya ce a ranar Yaƙin Khaibar: "Zan ba tutar gobe ga wani mutum wanda Allah zai ba nasara a hannunsa, yana son Allah da Manzonsa, kuma Allah da Manzonsa suna son shi, sai mutane suka shafe daren su suna tattaunawa, wane ne zai samu a ba shi. Da gari ya waye, suka zo wurin (SAW), kowanne yana fatan a ba shi, sai ya ce: "Ina Ali bn Abi Talib?" Aka ce: yana fama da ciwon ido. Sai aka aika masa, Manzon Allah (SAW) ya tofa masa a idanuwansa, ya yi masa addu'a, sai ya warke tamkar bai taɓa yin ciwo ba, kuma ya ba shi tutar, ya ce masa: "Ka tafi a hankali har ka isa cikinsu, sai ka kira su zuwa Musulunci, ka gaya musu abin da ya wajaba a kansu na hakkin Allah a cikinsa. Na rantse da Allah, Allah Ya shiryar da mutum ɗaya ta hannunka, ya fi maka alheri fiye da ka mallaki ja-jayan raƙuma masu daraja"[1].

[1]. Bukhari (4210) da Muslim (2406) ne suka rawaito shi.

- Daga cikin haka har-wa-yau akwai: Warkar da ƙafar Salama bin Al-Akwa'u (RA) — da izinin Allah —; An karbo daga Yazid bin Abi Ubaid ya ce: Na ga alamun rauni a ƙafar Salama, sai na ce: *"Ya Aba Muslim, mene ya ji maka rauni?"* Sai ya ce*: "Wan bugu ne da aka yi min a ranar Khaibar."* Sai mutane suka ce: "An ji wa Salama rauni" Sai na je wurin Annabi (SAW), ya yi tofi sau uku a wurin raunin, daga nan bai ƙara jin zafi ba har zuwa wannan lokaci[1].
- Daga cikin haka har-wa-yau: Akwai warkar da ƙafar Abdullah ɗan Atīk (RA) — da izinin Allah —; Wannan ya faru ne a lokacin da Manzon Allah (SAW) ya aiki wasu mutane daga cikin Ansar zuwa wurin wani bayahude Abu Rafi'u, sai ya sanya shugabancinsu a hannun Abdullah ɗan Atik, kuma da ma Abu Rafi'u ya ƙasance yana cutar da Manzon Allah (SAW), yana kuma taimakawa a cutar da shi, yana zaune a cikin wata ganuwa a ƙasar Hijaz. Yayin da suka kusa zuwa gare shi, rana ta fadi, mutane kuma suka dawo da dabbobinsu, sai Abdullah ya ce wa abokansa*: "Ku zauna a nan, zan tafi in roki mai gadin, watakila in samu in shiga, y*a ce: Sai na tafi har sai da na yi galaba a kan Abu Rafi'u, na tabbatar na kashe shi, sai na fara buɗe ƙofofi, ƙofa bayan ƙofa, sai dai duka a kulle suke, har na kai ga wata matakala, sai na ɗora ƙafata a kai, sai na faɗo, ƙafata ta karye, sai na ɗaure ta da rawanina, na tafi na zauna a ƙofar, na ce: *"Ba zan fita a wannan daren ba sai na tabbatar: shin na kashe shi ko ban kashe shi ba?"* Da zaƙara ya yi cara, sai mai shela a saman ganuwar ya shelanta cewa: *"Ina sanar da mutuwar Abu Rafi'u, ɗan kasuwar mutanen Hijaz"*, Sai na koma wurin abokaina na ce: *" ku bar nan da sauri, Allah Ya kashe Abu Rafi'u",* da na isa wurin Annabi (SAW), na ba shi labari, sai ya ce: "Miƙar da ƙafarka" Sai na miƙar da ƙafata, sai ya shafa ta, sai ta warke tamkar ban taɓa jin wani ciwo ba[2].

---

[1]. Bukhari ne ya rawaito shi (4206).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (4039).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

AMMAR ƊAN YASIR

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Ammar ɗan Yasir Amir ɗan Malik ɗan Kinana, kuma inkiyarsa ita ce Abul-Yaƙazan.

An haife shi ne a Madina sheƙara ta 56 kafin Hijira, saboda haka shi sa'an Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ne a shekaru[1].

❖ Tarihinsa da Falalrsa:

Ammar (RA), ya ƙasance mutum ne mai tsawo, mai faɗin kafadu, mai ƙudan gashi, ya iya rubutu da ƙaratu, ba ya yawan magana, shiru shiru ne[2].

Ya Musulunta tun farkon kira, (RA), kuma yana daga cikin waɗanda aka zalunta a Makka, saboda haka shi da mahaifinsa da mahaifiyarsa sun sha azaba mai tsanani domin Allah, har Manzon Allah (SAW) ya ce musu: "Ku yi haƙuri ya iyalan Yasir, domin lallai makomarku ita ce Aljanna[3]".

Abdullah ɗan Masʿud (RA) yana cewa: ‘‘Mutanen da suka fara bayyana Musuluncinsu su bakwai ne: Manzon (SAW), Abubakar, Ammar, mahaifiyarsa Sumayya, Suhaib, Bilal, da Miƙdad, amma Manzon Allah (SAW) Allah Ya tsare shi ta dalilin baffansa Abu Ɗalib, Abubakar kuwa Allah Ya tsare shi ta dalilin danginsa, amma sauran su kuwa mushrikai sun kama su, suka sanya musu sulken ƙarfe, suka bar su a rana"[4].

---

1. Ḥākim ne ya rawaito (3/232).
2. Ḥilyatul-Auliya’ (1/145).
3. Al-Ṭabarānī (8/208) da Al-Ḥākim (3/232).
4. Musnad Aḥmad (3223) da Ibnu Mājah (150).

Annabi (SAW0 ya yabe shi, ya kuma yi jinjina a kan imaninsa a cikin Hadisai masu yawa, daga ciki akwai faɗinsa cewa: (Lallai Ammar cike yake da imani har ƙasusuwansa)[1]. Kuma wani lokaci ya zo neman izinin shiga wurin Annabi (SAW), sai Annabi ya ce: “Barka da zuwa, nagartacce kuma tsarkakke[2]".

Ammar (RA) ya yi hijira zuwa ƙasar Habasha, sannan kuma ya yi hijira zuwa Madina, Ya halarci yaƙin Badar, kuma babu wanda ya halarta daga cikin waɗanda iyayensu maza da mata Musulmai ne sai shi, kuma ya halarci yaƙin Uhud da sauran yaƙe-yaƙe duka tare da Manzon Allah (SAW). A ranar yaƙin Yamama kuwa, ya nuna jarumta matuƙa a lokacin da Musulmi suka samu kansu a wani matsanancin hali, ta yadda ya hau kan wani dutse, kunnensa na zubar da jini saboda an sare shi, yana kiran mutane: “Ya ku al’ummar Musulmi! Shin Aljanna kuke gujemawa?! Ni ne Ammar ɗan Yasir, ku taho zuwa gare ni!”. Yana faɗin haka kuma yana ci gaba da gwabza yaƙi[3]".

❖ Rasuwarsa:

Ya yi shahada a sheƙara ta 37H, yana da shekaru casa’in da ɗaya, sai Alyyu ɗan Abi Ɗalib ya ɗauke shi bisa kirjinsa, ya yi masa sallar jana’iza tare da sauran Musulmi, sannan aka birne shi cikin tufafinsa.

---

1. Al-Ḥākim (5680).
2. Bukhari ya rawaito shi a Adabul-Mufrad (1031).
3. Siyaru A'lamin-Nubala' (1/224).

Auna fahimtarka - a darussan Mako na 48 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ake nufi da "Al-Mu'sirat?**		a
	a. Gazagizai masu ɗauke da ruwan sama	b. Duwayen masu girma.	c. Manyan Jiragen ruwa.
Darasin Hadisi	**Tambaya: Daga cikin ribar fata na gaskiya akwai cewa:**		a
	a. Kada bawan Allah ya raina wani abu mai kyau	b. Kada bawan Allah ya dogara ga aikinsa kuma ya rudu da shi	c. Kada bawan Allah ya tsananta wa kanasa ya bar wasu abubuwa suka halatta
Darasin Aƙida	**Tambaya: Abin da ake rataya wa marasa lafiya ko yara ko dabbobi domin tunkude bala'i ko dauke shi, wannan shi ake kira da:**		c
	a. Rukuya	b. Dan manne	c. Laya
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Daga cikin abin da ake so a aikata kafin dauakar hrama akwai:**		b
	a. Niyya	b. Wanka	c. Daura harama daga miƙati
Darasin Sira	**Tambaya: Wanene ya kashe Abu Rafi'ul-Yahudi:**		b
	a. Salama ɗan Al-Akwaʿ	b. Abdallah ɗan Atik	c. Sa'ad ɗan Mu'az
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Daga cikin falalar Ammar (RA), faɗin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi cewa:**		c
	a. Lallai kai mutum ne salihi	b. Lallai Ruhu Mai tsarki (Mala'ika Jibrilu) yana goyon ƙarfafarka	c. "Barka da zuwa, nagartacce kuma tsarkakke

MAKO NA ARBA'IN DA TARA

LAHADI: DARASIN TAFSIRI

SURUTUN-NABA'I (2)

إِنَّ يَوْمَ ٱلْفَصْلِ كَانَ مِيقَٰتًا ﴿١٧﴾ يَوْمَ يُنفَخُ فِى ٱلصُّورِ فَتَأْتُونَ أَفْوَاجًا ﴿١٨﴾ وَفُتِحَتِ ٱلسَّمَآءُ
فَكَانَتْ أَبْوَٰبًا ﴿١٩﴾ وَسُيِّرَتِ ٱلْجِبَالُ فَكَانَتْ سَرَابًا ﴿٢٠﴾ إِنَّ جَهَنَّمَ كَانَتْ مِرْصَادًا ﴿٢١﴾ لِّلطَّٰغِينَ
مَـَٔابًا ﴿٢٢﴾ لَّٰبِثِينَ فِيهَآ أَحْقَابًا ﴿٢٣﴾ لَّا يَذُوقُونَ فِيهَا بَرْدًا وَلَا شَرَابًا ﴿٢٤﴾ إِلَّا حَمِيمًا
وَغَسَّاقًا ﴿٢٥﴾ جَزَآءً وِفَاقًا ﴿٢٦﴾ إِنَّهُمْ كَانُوا۟ لَا يَرْجُونَ حِسَابًا ﴿٢٧﴾ وَكَذَّبُوا۟ بِـَٔايَٰتِنَا كِذَّابًا ﴿٢٨﴾ وَكُلَّ
شَىْءٍ أَحْصَيْنَٰهُ كِتَٰبًا ﴿٢٩﴾ فَذُوقُوا۟ فَلَن نَّزِيدَكُمْ إِلَّا عَذَابًا ﴿٣٠﴾

❖ Fassara:

17. Lalle ranar hukunci ta ƙasance (rana ce) mai tsayayyen lokaci.
18. Ranar da za a busa ƙaho sai ku zo jama’a-jama’a.
19. Aka kuma buɗe sama sai ta zama ƙofofi.
20. Aka kuma tafiyar da duwatsu sai suka zama kawalwalniya.
21. Lalle Jahannama ta ƙasance madakata ce.
22. Makoma ce ga masu ɗagawa.
23. Masu zama ne a cikinta shekaru aru-aru.
24. Ba sa ɗandanar wani sanyi a cikinta ko wani abin sha.
25. Sai tafasasshen ruwa da ruwan mugunya.
26. Don sakayya da ta dace.
27. Lalle su sun ƙasance ba sa tsoron hisabi
28. Suka kuma ƙaryata ayoyinmu iyakar ƙaryatawa.
29. Kuma kowane abu Mun ƙididdige shi a rubuce.
30. Sai a ce da su: To ku ɗandana, don ba za Mu ƙara muku ba sai dai wata azaba

❖ Baƙin Kalmomi:

ميقاتًا	Mīƙata	Lokaci da wa'adi na rarrabẽwa tsakanin halittu
الصور	As-Ṣur	Ƙahon da Israfīl zai yi busa a cikinsa
أبوابًا	Abwaba	Ma'abociya ƙofofi masu yawa domin saukar mala'iku.
سُيِّرت	Suyyirat	tafiyar da su bayan kafuwarsu
مرصادًا	Mirsada	Tana jiran ma'abotanta kuma tana dakonsu
أحقابا	Ahkaba	Shekaru marasa yankewa
بَرْدًا	Bardan	Sanyi
حَمِيمًا	Hamiman	Ruwa mai tsanani zafi
وَغَسَّاقًا	Ghassaƙa	Ruwan mugunya
وِفَاقًا	Wifaƙa	Daidai da ayyukansu
لَا يَرْجُونَ	La yarjuna	Ba sa tsoro
أَحْصَيْنَاهُ	Ahsainahu	Mun ƙididdige shi

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

Allah Maɗaukaki ya ambaci girman ranar Alƙiyama, wadda ya sanya ta zama wa'adi ga halittu, kuma abin da zai faru a cikinta na tashin da rikicewa, duwatsu za a jijjiga su sai su zama kamar ƙura,

kuma sama za ta tsage har ta zama ma'abociya ƙofofi, sannan Allah Zai raba tsakanin halittu da hukuncinsa wanda babu zalunci a cikinsa, sai a gabatar da wutar Jahannama wadda aka tanada ta domin masu girman kai masu ƙetare iyaka, ta zama makomarsu, za su zauna a cikinta shekaru masu tsawo ba tare da sun samu sanyi ba ko kuma abin sha ba, sai dai ruwa mai tsananin zafi da zai riƙa ƙona musu fuska da 'ya'yan hanjinsu da kuma ruwan mugunya dake fita daga al'auran 'yan wuta wanda yake da tsananin wari da ƙazanta, wannan shi ne sakamakon abin da ya dace da ayyukansu, domin sun cancanci waɗannan azabbobi masu girma saboda ayyukansu, kuma Allah Bai zalunce su ba, sai dai su ne suka zalunci kansu, domin sun ƙasance ba su yi imani da hisabi ba, sai suka ƙaryata ayoyin Allah ƙaryatawa ta ƙwarai, kuma dukkan wannan Allah Ya ƙididdige shi, kuma Ya rubuta shi cikin littattafan ayyukansu, domi Ya saka musu da azaba mai tsanani wacee a ko da yaushe take daɗa ƙaruwa da girmama.

❖ Abubuwan da za koya daga Surar:

1. Tunatarwa game da ranar ƙiyama, da abin da ke cikinta na wahalhalu masu tsanani.
2. Lallai tuna wahalhalun ranar ƙiyama magani ne ga gafalar zuciya, kuma abu ne dake ƙarfafa guiwa wurin aikata alheri.
3. Gargadi game da zalunci, da bayyana sakamakon ma'abotansa.
4. Cewa lallai mutum ba a halicce shi don wasa ba, bari dai, Allah Ya halicce shi ne domin wata hikima mai girma, kuma da sannu Zai yi masa hisabi a kanta a wani yini mai girma.
5. Rubutun Mala'iku ga ayyukan bayin Allah, ƙanana da manyansu, na alheri da na sharri.
6. Bayani game da abin da Allah Ya tanada wa kafirai na azaba domin su tsorata.
7. Lallai azabar kafirai a cikin wuta mai ƙaruwa ce da ninkuwa.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

UMURNI DA KYAUTATA ZATO GA ALLAH MAƊAUKAKI

An karɓo daaga Jabir ɗan Abdullah Allah Ya ƙara musu yarda ya ce: Na ji Manzon Allah (SAW) yana cewa kwanaki uku kafin rasuwarsa: **(Kada wani daga cikinku ya mutu face yana kyautata zatoga Allah Mai girma kuma da ɗaukaka)** [1]**.**

❖ Sharhi:

Ya kamata mumini a rayuwarsa ya kasance yana kyautata zato ga Ubangijinsa, musamman a lokacin tsanani, da bala'i, da jarabawa, ko rashin lafiya, da lokacin da mutuwa ta kusanto; sai ya tuna karamcin Allah da tausasawarsa, kuma ya yi fatan samun rahamarsa da afuwarsa, wannan zai taimaka masa wajen tsallake wannan ƙunci da dacewa da kyakkyawan ƙarshe da cikawa da kyawawan maganganu, kuma duk lokacin da bawa ya kasance mai kyautata zato ga Allah, mai kyakkyawan fata game da abin da ke wurin Allah; to Allah ba zai tozarta fatansa ba, kuma ba zai ɓata aikinsa ba, amma munana zato ga Allah alama ne na rashin sanin Allah, kuma sababi ne na dulmiyewa cikin zunubai da tsananta wa kai.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) Kwaɗayin Manzon Allah (SAW) wajen shiryar da al'ummarsa, da tsananin tausayi da jinƙansa a gare su har a cikin rashin lafiyar rasuwarsa.

2) Gargaɗi game da ɗebe tsammani da yanke ƙauna, da kuma kwaɗaitar wa a kan kyautata zato da fata ga Allah.

3) Ya kamata kyautata zaton musulmi ga Allah ya sanya shi aikata ayyuka nagari, ba ya sanya shi sakaci da aikata zunubai ba, domin hakan ruɗi ne.

4) Daga cikin kyautata zato ga Allah akwai cewa: Idan bawa ya yi addu'a, ya yi zaton cewa Allah zai karɓa; kuma idan ya aikata

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2877).

zunubi ya nemi gafara, ya yi zaton cewa Allah zai karɓi tuba da neman gafararsa; idan kuma ya aikata aiki nagari, ya yi zaton cewa Allah zai karɓi aikinsa.

5) Daga cikin munana zato ga Allah akwai cewa: Bawa ya yi ayyukan ɗa'a amma ya yi zaton cewa Allah ba zai karɓa daga gare shi ba; idan kuma ya yi zunubi ya tuba, ya zaci cewa Allah ba zai karɓi tubarsa ba.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

BIYAYYA GA SHUGABA

Lallai daga cikin ginshiƙan aƙidar Ahlus-Sunna wal-Jama’a, kuma daga asalin addininsu, akwai: wajibcin biyayya da ɗa'a ga shugaba, domin nassoshi daga littafin Allah Maɗaukaki da sahihin sunnan Manzonsa tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, da kuma ijma’in malaman Musulmi daga magabata da waɗanda suka biyo bayansu da sun yi mana nuni kan wajabcin biyayya ga mai shugaba Musulmi da haramcin fito-na-fito da shi, wannan wajibi ne na shari’a da ake bauta wa Allah da shi, kuma aƙida ce da ake bautar Allah da ita, kuma kusanci ne da ake fatan samun ladansa da sakamakonsa.

Allah Maɗaukaki Shi ne wanda Ya halicci halittu, kuma shi ne mafi sani game da ɗabi’unsu, mafi sani game da bukatunsu, kuma mafi sani game da abin da zai gyara al’amuransu, don haka, alheri dukkansa yana cikin bin umarninsa da bin shari’arsa.
Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ya ku waɗanda suka yi imani, ku yi ɗa’a ga Allah, kuma ku yi ɗa’a ga Manzo da kuma majiɓinta lamarinku. Idan kun yi jayayya a kan wani abu, to ku mayar da shi zuwa ga Allah da Manzonsa in kun ƙasance kun yi imani da Allah da ranar ƙarshe. Wannan shi ne mafi alheri, kuma mafi kyan makoma)) [1].
Ya zo a cikin Hadisin Ubadah ɗan Samit (RA) ya ce: “Mun yi mubaya’a a kan biyayya da ɗa'a ga shugaba cikin sauƙi da tsanani, da wahala da yalwa, kuma ko da ya fifita kansa a kanmu, kuma kada mu yi fito-na-fito da da masu mulki sai dai idan kuka ga kafirci bayyane da kuka da hujja daga Allah a kansa[2]".
Kuma Manzon Allah (SAW), mai tsananin tausayi ga al’ummarsa, ya ƙwadaitar kan cewa kada mutum ya ware daga jama’a ko da kuwa a cikin ƙaramin abu ne, kuma ya tsananta bayani game da mummunan sakamakon haka, sai ya ce (SAW): (Wanda ya ga wani abu da yake ƙi daga shugabansa, to ya yi haƙuri a da shi, domin lallai

---

1. [An-Nisa'i’: 59].
2. Bukhari (7055), da Muslim (1709) suka rawaito shi

wanda ya ware kansa daga jama’a daidai da girman ɗani, sai ya mutu a haka, ya yi mutuwa irin mutuwar jahiliyya)[1].

Kuma Manzon Allah (SAW) ya ce: (Wanda ya cire hannu daga biyayya, zai haɗu da Allah a ranar kiyama ba tare da wata hujja ba, kuma wanda ya mutu alhali babu mubaya’a a wuyarsa har ya mutu, ya yi mutuwa irin mutuwar jahiliyya)[2].

Bari dai hankali cikakke yana nuni game da wannan; domin alheri da hikima su ne kowace al’umma ta ƙasance tana da jagora da ake biyayya gare shi, domin ya rika tafiyar da al’amuransu, ya kula da maslaharsu, sai su ƙasance cikin aminci a rayuwarsu da dukiyoyinsu da mutuncinsu, kuma su samu damar yin ibadunsu da ayyukansu na ɗa'a, su sauƙaƙa musu rayuwarsu da bukatunsu, kalmarsu ta haɗu waje guda, ƙarfinsu da darajarsu su ɗaukaka, kuma abokan gabansa kuma su rushe.

[1]. Bukhari (7054), da Muslim (1849) ne suka rawaito shi.
[2]. Muslim (1851) ne ya rawaito shi.

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

ABUBUWAN DA SUKA HARAMTA GA WANDA YA ƊAUKI HARAMA

Abubuwan da suka haramta ga wanda ya ɗau harama: Su ne abubuwan da ya wajaba ga wanda ya ɗau harama ya nisance su.

Kuma abubuwa ne guda takwas:

Na farko: Aske gashin kansa ko na jikinsa; saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((Kuma kada ku aske kawunanku har sai hadaya ta isa wurin yankanta))[1]. Kuma ana yarda ya wanke gashinsa, domin Annabi (SAW) ya wanke kansa alhali yana cikin harama[2].

Na biyu: Yanke farcen hannunsa ko na ƙafarsa, amma idan ya karye ne sai ya cire shi, babu komai a kansa.

Na uku: Rufe kansa da abin da yake mannewa da shi; domin Annabi (SAW) ya hana sanya rawani da alkyabba mai hula[3]. Amma an yarda ya inuwanta da tanti ko bishiya, ko lema daga rana; domin Annabi (SAW), an kafa masa tanti ya shiga ciki alhali yana cikin harama[4].

Na huɗu: Namiji ya sanya ɗinkakken tufafi, wato tufafin da aka ɗinka a gabobin jiki, kamar riga, wando, ko safar hannu, domin an tambayi Annabi (SAW): Menene wanda ya ɗau harama zai sanya? Sai ya ce: “Kada ya sanya riga, ko rawani, ko alkyabba, ko wando, ko wani kaya da aka shafe shi da turare ko za’faran, ko huffi” [5], amma mace, za ta iya sanya tufafin da ta ga dama domin buƙatarta ta rufe jikinta, sai dai za ta guji abubuwa guda biyu, su ne: Niƙabi

---

1. [Al-Baƙara: 196].
2. Bukhari (1846) da Muslim (1205) ne suka rawaito shi.
3. Bukhari (1838) da Muslim (1177) ne suka rawaito shi.
4. Muslim ne ya rawaito shi (1177).
5. Bukhari (1838) da Muslim (1177) ne suka rawaito shi.

da safar hannu; saboda faɗin Annabi (SAW): (Mace ba ta sanya niƙabi, kuma ba ta sanya safar hannu)[1].

Kuma wajibi ne ta rufe fuskarta da mayafi ko makamancinsa idan maza za su ratsa; saboda faɗin A'isha Allah ya ƙara mata yarda: "Matafiya sun ƙasance suna wucewa ta wurinmu alhali mu cikin harma tare da Manzon Allah (SAW), idan suka kusantomu sai kowace daga cikinmu sai ta rufe fuskarta da mayafinta, idan suka wuce sai mu buɗe fuskar"[2].

Na biyar: Sanya turare, a jiki ko a tufa; domin Annabi (SAW)ya umarci wani daga cikin msau harama da ya wanke turare daga jikinsa[3]. kuma ya ce game da maniyyacin da rakumarsa ta faɗo da shi wuyansa ya karye: (kada ku sanya masa turare) [4].

Na shida: Farautar namun daji; saboda faɗin Allah Maɗaukaki: (Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kashe abin farauta alhali kuna cikin harama)[5], da faɗinsa: (amma an haramta muku farautar naman daji matuƙar kuna cikin Harami)[6], saboda haka, wanda ya ɗau harama ba ya halatta ya farauci naman daji, ko ya taimaka wajen farautarsa, kuma ba ya halatta ya ci abin da aka farauto ko ya taimaka wajen farauto shi, ko abin da aka farauto masa, amma farautar naman ruwa ya halatta a gare shi; saboda faɗinsa: (An halatta muku farautar naman ruwa da abincin cikinsa)[7], haka kuma dabbobin gida waɗanda ba na farauta ba, irin su kaji da tumaki.

Na bakwai: Daura aure, wanda ya ɗau harama ba zai ɗaura wa kansa aure ba kuma ba zai ɗaura wa waninsa ba, Usman (RA) ya

---

1. Bukhari ne ya rawaito shi (1838).
2. Abu Dawud ne ya rawaito shi (1833).
3. Muslim ne ya rawaito shi (1180).
4. Muslim ne ya rawaito shi (1206).
5. [Al-Ma'ida: 95].
6. [Al-Ma'ida: 96].
7. [Al-Ma'ida: 96].

ce: (Wanda ya ɗau harama ba zai ɗaura wa kansa aure ba kuma ba zai ɗaura wa waninsa ba, kuma ba zai nemi aure ba) [1].

Na takwas: Saduwa da mace, da abubuwan da suke kai wa gare ga hakan, kamar runguma da sha'awa; saboda faɗin Allah Maɗaukaki: ((Duk wanda ya wajabta wa kansa aikin Hajji cikin waɗannan watanni, to, babu maganar saduwa da mace)) [2].

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (1409).
[2]. [Al-Baƙara: 197].

ALHAMIS: DARASIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Ba da Labarin Al'amura na Ghaibu:

Daga cikin alamomin gaskiyar annabtakarsa (SAW): Akwai abin da ya sanar daga ɓoyayyun abubuwan da za su faru a gaba waɗanda suka faru daidai da yadda ya faɗa kwabo da kwabo, domin Allah Maɗaukaki Ya yi wahayi ne zuwa ga Manzonsa Annabi ummiyyi wanda bai iya rubutu ba, kuma bai san komai daga ilimin mutanen farko ba da labaran waɗanda suka gabata ba, sai Ya ba shi labarin da abin da ya gabata da abin da zai faru a gaba daidai da daidai, kamar yadda Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Waɗannan suna daga labaran gaibu da muke yi maka wahayinsu, don kai da mutanenka ba ku san su ba kafin wannan labarin; sai ka yi haƙuri; haƙiƙa kyakkyawan ƙarshe yana ga masu taƙawa))[1].

Don haka, a cikin wannan Alƙur'ani akwai labaran gaskiya game da Allah da mala'ikunsa, da Al'arshinsa, da halittunsa na sama da na ƙasa, kamar sammai da ƙassi da abin da ke tsakaninsu da abin da ke cikinsu; al'amura masu girma da yawa, tabbatattu da yankakkun hujjoji, kuma akwai labaran al'ummomi da annabawansu, da yadda Allah Ya tsaratar da muminai, Ya kuma halaka kafirai, cikin wani salo na magana da babu wani ɗan'adam da zai iya yin irinsa, za ka samu a wani wuri labarin ya zo taƙaice cikin mafi kyawun salo da fasaha, a wani wuri kuma an faɗaɗa shi, babu abin da ya kai wannan tsari na magana kyawu da haske da daraja, har sai mai sauraro yana jin kamar a gabansa abubuwan da ake faɗa suka faru, kamar yadda Allah Ya ce: ((Kuma ba ka ƙasance a gefen dutsen Ɗuri ba, lokacin da Muka kirawo Annabi Musa, sai dai wata rahama daga Ubangijinka))[2].

---

1. [Hud: 49].
2. [Al-ƙasas 46].

Kuma Allah ya ce: ((Wancan abin da ya gabata a baya yana cikin labaru na gaibi da Muke yi maka wahayinsa, kuma kai ba ka wurinsu lokacin da suka jefa alƙalumansu don tantance wane ne cikinsu zai karɓi renon Maryamu, kuma kai ba ka nan tare da su yayin da suke jayayya da juna)) [1]. Kuma Allah ya ce: ((Wannan yana daga labaran gaibu da Muke yi maka wahayinsa; ba ka kuma tare da su lokacin da suka haɗa al'amarinsu suna ƙulle-ƙullen makirci)) [2].

❖ **Kuma daga cikin waɗannan labaran na gaibu da suka faru kamar yadda ya ba da labari:**

- Akwai abin da Allah Maɗaukaki Ya ambata a cikin Suratul-Muzzammil, wacce tana daga cikin surori na farko da aka saukar a Makkah: (Ya san cewa daga cikinku akwai waɗanda za su ƙasance marasa lafiya, waɗansu kuma suna tafiya a bayan ƙasa don fatauci suna neman falala daga Allah, waɗansu kuma suna yin yaƙi saboda Allah)[3]. Kuma abu ne sananne cewa lallai jihadi bai shar'anta shi ba sai a Madina bayan Hijira.
- Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce a cikin Suratul-ƙamar, wacce Makkiyya ce: (A'a, suna dai cewa ne: "Mu jama'a ce wadda za ta ci nasara () To ba da daɗewa ba za a karya jama'ar tasu, su kuma su ba da baya) [4]. Wannan ya faru ne a ranar Badar, kuma Annabi (SAW) ya ƙaranta ta ne a lokacin yana fitowa daga wani wuri mai suna Arish.
- Kuma Allah Maɗaukaki ya ce a cikin Suratun-Fath: ((Haƙiƙa Allah Ya tabbatar wa Manzonsa gaskiyar mafarkin cewa, lalle za ku shiga Masallaci mai alfarma insha Allahu, kuna cikin aminci kuna masu aske kawunanku da masu yin saisaye, ba tare da kuna jin tsoron (komai) ba, to Ya san abin da ba ku sani ba, sai Ya sanya buɗi na kusa kafin wannan)) [5], wannan alƙawari ya sauka ne a sheƙara ta

---

1. [Al-Imran: 44].
2. [Yusuf: 102].
3. [Al-Muzzammil: 20].
4. [Al-ƙamar: 44-45].
5. [Al-Fath: 27].

shida a Hudaybiyya, kuma ya tabbata a Umratul-ƙada a sheƙara ta bakwai.

- Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((ALIF LAM MIM () An yi galaba a kan Rumawa () A ƙasa mafi kusa (da su), su kuma da sannu za su yi galaba (a kan Farisa) bayan galabar da aka yi a kansu () A cikin ‘yan tsirarun shekarun))[1]. Wannan ya faru ne lokacin da Farisawa suka ci Rumawa da yaƙi, sai mushrikai suka yi farin ciki, muminai kuwa suka yi baƙin ciki; domin Nasara sun fi kusa da Musulmi fiye da Majusawa, sai Allah Ya sanar da Manzonsa (SAW) cewa su ma Rumawa za su yi galaba a kan Farisawa a cikin wasu ‘yan tsirarun shekarun, sai kuma hakan ya tabbata kamar yadda ya faɗa.
- Kuma Allah Maɗaukaki ya ce: ((Allah Ya yi wa waɗanda suka yi imani daga cikinku suka kuma yi aiki na gari alƙawarin lalle zai sanya su halifofi a bayan ƙasa)) [2]. Sai Allah Ya tabbatar da addininsa, ya ɗaukaka shi a dukkanin sasannin duniya a zamanin Halifofi shiryayyu.

[1]. [Ar-Rum: 2-3].
[2]. [An-Nur: 55].

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

IMRAN ƊAN HUSAIN (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Imran ɗan Husain ɗan Ubaid, daga kabilar Khuza‘a.

Ya musulunta shi da mahaifinsa da Abu Huraira Allah Ya ƙara musu yarda a sheƙara guda, sheƙara ta 7 bayan hijira.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Ya ƙasance daga cikin fitattun sahabbai masu falala kuma masu ilimi, (RA), kuma shi mai gaskiya ne, mai tsantseni ne mai nagarta, mai himma wajen ɗa'a ga Allah da Manzonsa (SAW). Haka kuma yana daga cikin waɗanda ake karɓar addu’arsu, kuma ya ƙasance mai yawan kuka ne da tsoron Allah.

Kuma Shi (RA) mutum ne mai kyawun sutura da shiga, an karɓo daga Abu Raja’ ya ce: Wata rana Imran ya fito wurinmu yana sanye da wata riga ta alfarma da ba mu taɓa ganin irinta ba, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Lalle idan Allah Ya yi wa bawansa ni’ima, yana son Ya ga tasirin wannan ni’ima a tare da shi) [1].

Umar ɗan Khaɗɗab (RA) ya aika shi zuwa Basra domin ya koyar da mutanenta al’amuran addininsu, sai mutanen Basra suka ƙaunace shi ƙauna mai yawa, suka kuma riƙa ɗaukar ilimi daga wurinsa, Hasanul-Basri da Ibnu Sirin suna cewa: (Babu wani daga cikin sahabban Manzon Allah (SAW) da ya zo Basra da ya fi Imran ɗan Husain falala) [2].

Ya yi fama da cuta tsawon shekaru talatin kafin rasuwarsa, amma a haka ya yi ta haƙuri haƙuri mai kyau a kan jarabtar da Allah Ya yi masa, sai hakan ya ƙasance baiwa da ƙarama gare shi, daga ciki

---

[1]. Aḥmad (4/438) ne ya rawaito shi.
[2]. Siyaru A‘lāmin-Nubalā’ (3/322).

akwai cewa Mala’iku suna yi masa sallama daga kowane bangaren gidansa[1].

❖ Rasuwarsa:

Allah Ya karɓi ransa a gidansa a Basra, yana kwance ba lafiya, a sheƙara ta 52 bayan Hijira.

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2502).

Auna fahimtarka – a cikin darussan Mako na 49			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Mene ne ma'anar "Al-Ghassaƙ?**		a
	a. Ruwan mugunya	b. Ruwan zafi.	c. itace mai ƙaya
Darasin Hadisi	**Tambaya: Ya kamata kyakkyawan zaton Musulmi ga Allah ya sanya shi ya riƙa yin:**		a
	a. Aikikin ƙwarai	b. Hutu da ɗa'awa	c. ƙaranta nafilfili
Darasin Aƙida	**Tambaya: Wane ne ya ce: "Mun yi mubaya'a a kan ji da biyayya a lokacin farin ciki da a lokacin ƙunci, a lokacin sauƙi da a lokacin wuya, kuma ko da shugaba ya fifita kansa a kanmu, kuma ba za mu yi fito-na-fito da masu mulki ba?**		b
	a. Abu Huraira	b. Ubadah ɗan Ṣamit	c. Mu'azu ɗan Jabal
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Abubuwa nawa ne aka haramta yayin harama?**		c
	a. Abubuwa huɗu ne	b. Abubuwa shida ne	c. Abubuwa takwas ne
Darasin Sira	**Tambaya: Daga cikin labaran gaibu da suka faru kamar yadda Annabi (SAW)ya faɗa akwai:**		b
	a. Shahadar Ḥamza ɗan Abdulmuɗɗalib	b. Samun galaba a kan musrikai a ranar Badar	c. Musuluntar Salmanul-Farisi
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Umar ɗan Khaɗɗab (RA) ya aika Imran ɗan Ḥuṣain a matsayin malami zuwa:**		a
	a. Basra	b. Dimashƙ	c. Misra

MAKO NA HAMSIN

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

SURATUN-NABA'I (3)

إِنَّ لِلْمُتَّقِينَ مَفَازًا ﴿٣١﴾ حَدَآئِقَ وَأَعْنَٰبًا ﴿٣٢﴾ وَكَوَاعِبَ أَتْرَابًا ﴿٣٣﴾ وَكَأْسًا دِهَاقًا ﴿٣٤﴾ لَّا يَسْمَعُونَ
فِيهَا لَغْوًا وَلَا كِذَّٰبًا ﴿٣٥﴾ جَزَآءً مِّن رَّبِّكَ عَطَآءً حِسَابًا ﴿٣٦﴾ رَّبِّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا
ٱلرَّحْمَٰنِ ۖ لَا يَمْلِكُونَ مِنْهُ خِطَابًا ﴿٣٧﴾ يَوْمَ يَقُومُ ٱلرُّوحُ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ صَفًّا ۖ لَّا يَتَكَلَّمُونَ إِلَّا مَنْ أَذِنَ
لَهُ ٱلرَّحْمَٰنُ وَقَالَ صَوَابًا ﴿٣٨﴾ ذَٰلِكَ ٱلْيَوْمُ ٱلْحَقُّ ۖ فَمَن شَآءَ ٱتَّخَذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ مَـَٔابًا ﴿٣٩﴾ إِنَّآ
أَنذَرْنَٰكُمْ عَذَابًا قَرِيبًا يَوْمَ يَنظُرُ ٱلْمَرْءُ مَا قَدَّمَتْ يَدَاهُ وَيَقُولُ ٱلْكَافِرُ يَٰلَيْتَنِى كُنتُ تُرَٰبًا ﴿٤٠﴾

❖ Fassara

31. Lalle masu taƙawa suna da babban rabo.
32. Su ne gonaki da inabai.
33. Da ‘yan mata tsaraiku.
34. Da kofin giya cikakke.
35. Ba sa jin maganar banza a cikinta ko kuma ƙarya.
36. Sakamako ne daga Ubangijinka, kyauta ce a lissafe gwargwadon aikin kowa.
37. Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake tsakaninsu (watau Allah) Mai rahama; (halittu) ba sa samun ikon yi masa magana daga gare Shi.
38. Ranar da Jibrilu da mala’iku za su tsaya sahu-sahu; (halittu) ba sa iya magana sai fa wanda (Allah) Mai rahama Ya yi wa izini, ya kuma faɗi abin da ya dace.
39. Wannan rana ce tabbatacciya; saboda haka wanda ya ga dama sai ya riƙi kyakkyawar makoma zuwa ga Ubangijinsa.
40. Lallai Mun yi muku gargaɗin azaba ta kurkusa, a ranar da mutum zai ga abin da hannayensa suka gabatar (na alheri ko na sharri), kafiri kuma ya riƙa cewa: “Ina ma da na zama turɓaya!

❖ Bakin Kalmomi:

مَفَازًا	Mafazan	Rabauta da shiga Aljanna.
كَوَاعِبَ	Kawa‘ib	'Yan mata, masu tsayayyen nono
أَتْرَابًا	Atraba	Tsaraiku
دِهَاقًا	Dihaƙa	Cikakke kofin giya
لَغْوًا	Laghwan	Maganar banza, marar amfani
حِسَابًا	Hisaban	Mai yawa, mai isarwa gare su
ٱلرُّوحُ	Ar-ruh	Mala’ika Jibrilu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi
مَـَٔابًا	Ma’aban	kyakkyawar makoma zuwa ga Ubangijin

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule

Bayan Allah Madaukaki Ya ambaci halin masu laifi, sai Ya biyo shi da bayanin halin masu tsoron Allah, da abin da za su samu na rabo da tsira, da kuma abin da wannan ni'ima ta ƙunsa na daga lambuna masu girma, wadanda ke tattare da kowane irin bishiyoyi da kyawawan ’ya’yan itatuwa wadanda ƙoramu ke gudana a ƙarƙashinsu, kuma suna da matan aure kyawawa, sa'anni ta fuskar shekaru da samartaka da kyawu, kuma suna da kofuna cike da ruwan giya mai dadi ga masu sha, kuma su ababen tsarkakewa ne daga jin maganar banza da hayaniya marar amfani, dukkan wadannan abubuwa masu girma Allah Ya ba su ne don falalarsa da kyautatawarsa, a matsayin sakamako bisa ayyukansu, wadanda Allah Ya sanya su a matsayin farashin Aljannarsa da ni'imarta.

Sa'an nan Allah Maɗaukaki Ya ambaci ribubiyyarsa, da girmansa, da Mulkinsa a wannan rana, da kuma cewa dukkan halittu – har da mala'iku – za su kasance masu tawali'u ne kuma za su yi shiru, ba za su yi magana ba sai idan Ya ba su izini, sai su faɗi magana ta gaskiya, domin wannan rana ita ce ranar gaskiyar da ba a yaɗa ƙarya a cikinta, kuma ƙarya ba ta amfani a cikinta, ta yadda kowane mutum zai ga abin da hannuwansa suka gabatar a wannan rana, idan ya tarar da alheri sai ya yi farin ciki kuma ya yi bushara, idan kuma ya tarar da akasin haka, sai ya yi nadama, amma lokacin ba lokacin nadama ba ne, ya yi fatan halaka saboda tsananin nadamar.

❖ Abubuwan da ake Fahimta daga Surar:

1) Bushara da ni'imomin da Allah Ya tanadar wa masu tsoronsa domin su yi farin ciki kuma su yi bushara.
2) Cewa tsoron Allah Maɗaukaki shi ne sanadiyyar shiga Aljanna.
3) Cewa tsarkake kunnuwa daga sauraron maganar banza wani ɓangare ne na ni'imar da ake fatan samu.
4) Cewa duniya ita ce gidan aiki da yi da gaske.
5) Cewa dukkan halittu bayi ne ga Allah, raunana ne a gabansa, masu ƙasƙanta ne ga umarninsa, masu bin hukuncinsa ne.
6) Nadama mai tsanani ta tabbata ga wanda ya yi wasa kuma ya ɓata rayuwarsa cikin wasa da wargi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

MASIFU MASU KANKARE ZUNUBAI

An karɓo daga A'isha Allah ya ƙara mata yarda ta ce: Manzon Allah (SAW) ya ce: (**Babu wani musulmi da ƙaya za ta soke shi ko wani abu da ya fi ƙayar cutarwa, face an rubuta masa lada saboda hakan, kuma a shafe masa laifi)** [1].

❖ Sharhi:

Daya daga cikin nu'ukan ƙaunar Allah ga bawansa mumini: Akwai jarabtarsa da masifa, kamar ciwo, ko damuwa, ko ƙunci, ko baƙin ciki, don haka, babu wata masifa da za ta same shi face ta ƙasance alheri gare shi idan ya yi haƙuri kuma ya nemi lada, saboda haƙuri a kan masifa yana haifar da waɗannan alherai masu zuwa:

- Mumini ya bautawa da haƙuri, kuma ya bayyana ƙankantarsa da bukatuwrsa ga Allah.
- Ana kankare zunubansa da kura-kuransa da shi.
- Ana ɗaga darajarsa zuwa matsayin da da aikinsa bai isa ya kai shi ba.

❖ Abubuwan da za a koya daga Hadisin:

1) Falalar Allah ga bayinsa muminai, da rahamarsa gare su, ta yadda yake gafarta musu zunubansu da mafi ƙankantar cutar dake samun su.

2) Ya kamata musulmi ya tarbi masifu da haƙuri da yarda da Allah, har sai ya samu lada da sakamako daga Allah Maɗaukaki.

3) Fushi da rashin yarda da masifu zunubi ne da ke haifar da laifi, ya hana samun lada, kuma ya jefa mutum cikin jayayya da ƙaddara.

---

[1]. Bukhari (5646) da Muslim (2572) ne suka rawaito shi.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

FALALAR AHLUL-BAITI DA ABIN DA YA WAJABA GAME DA SU

❖ Su waye Ahlul Baiti?

Ahlul Baiti: su ne dangin Annabi (SAW) waɗanda aka haramta musu karɓar sadaka, kuma su ne iyalan gidan Ali, da na Ja'afar, da na Aƙil, da na Abbas, da zuriyar Haris ɗan Abdulmuɗɗalib, tare da matan Annabi (SAW) da zuriyarsa.

❖ Falalar Ahlul-Baiti:

Nassoshi masu yawa sun zo game da falalar Ahlul-Baiti, daga cikinsu akwai:

- Faɗin Allah Maɗaukaki: ((Abin sani kawai, Allah Yana nufin Ya kawar muku da duk wata ƙazanta, ya ku iyalin gidan Annabi, Ya kuma tsarkake ku tsarkakewa))[1].
- Da Faɗin Annabi (SAW) cewa: (Lallai Allah Ya zaɓi Kinanah daga zuriyar Isma'il, Ya zaɓi Ƙuraishawa daga Kinanah, Ya zaɓi Banu Hashim daga Ƙuraishawa, kuma Ya zaɓe ni daga Banu Hashim)[2].
- Da Faɗin Annabi (SAW) cewa: (Kuma iyalan gidana, ina tuna muku Allah game da iyalan gidana, ina tuna muku Allah game da iyalan gidana)[3].

❖ Haƙƙinsu da Abin da ya wajaba game da su:

Ahlus-Sunnah wal-Jama'ah cikin abin da ya shafi haƙƙin Ahlul-Baiti, suna bisa wani tafarki ne madaidaici, da tsari na tsaka-tsaki,

---

1. [Al-Ahzab: 33].
2. Muslim ne ya rawaito shi (2276).
3. Muslim ne ya rawaito shi (2408).

wanda babu wuce gona da iri a cikinsa kuma babu sakaci, babu tauyewa a cikinsa kuma babu ƙetare iyaka.

Saboda haka, Ahlus-Sunnah suna son iyalan gidan Manzon Allah (SAW), kuma suna jiɓintarsu, kuma suna girmama su, kuma suna kiyaye wasiyyar Manzon Allah (SAW) game da su; domin ƙaunarsu na daga cikin ƙaunar Annabi (SAW) da girmama shi. Amma wannan bisa sharaɗin ƙasancewarsu masu bin Sunnah, masu tsayuwa a kan addini, amma wanda ya saɓa wa Sunnah, bai tsayu a kan addini ba, to ba ya halatta a jiɓince shi, ko da kuwa yana daga cikin Ahlul-Baiti, kuma ya zo a cikin Hadisi Annabi (SAW) ya ce: (Wanda aikinsa ya jinkirta shi, to nasabarsa ba za ta gaggautar da shi ba)[1].

Kuma Ahlus-Sunnah suna barranta kansu daga hanyar nawasib waɗanda suke ƙin Ahlul-Baiti, kuma suke sukarsu, haka kuma suna barranta daga hanyar waɗanda suke wuce gona da iri game da su, suke yi musu iƙirarin tsarkaka daga zunubi, suke neman tsani da su, kuma suke bauta musu, domin lallai Ahlul-Baiti su kansu suna ƙin wuce gona da iri cikin lamarinsu, suna kuma barranta kansu daga wanda ya ƙetare iyaka game da su, domin haƙiƙa Amirul-Mu'minin Ali ɗan Abi Ɗalib (RA), ya ƙona waɗanda suka ƙetare iyaka game da shi, kuma Ibnu Abbas ya goyi bayansa a kan kashe su, amma ya saɓa masa a kan ƙonasu da wuta) [2].

Haka kuma Aliyu (RA), ya nemi Abdullah ɗan Saba, shugaban masu ƙetare iyaka, domin ya kashe shi, amma sai ya gudu[3].

---

1. Muslim ne ya rawaito shi (2699).
2. Bukhari ne ya rawaito shi (2854).
3. Tarikhu Dimashƙ na Ibnu Asakir (7/295).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

FIDIYAR AIKATA ABUBUWAN DA AKA HARAMTA WA MANIYYACI

Idan maniyyaci ya aikata abin da aka hana yayin hrama yana sane, kuma da gangan, ba cikin mantuwa ba; to ya zama wajibi a gare shi ya bayar da fidiya.

❖ **Kuma fidiyar abubuwan da aka hana ta kasu kashi huɗu:**

Kashi na farko: Fidiyar kashe abin farauta, wadda ake da zaɓi tsakanin abubuwa uku a kanta:

Ko dai ya yanka dabbar gida kwatankwacin abin da ya kashe, ko kuma ya sayi abinci na ƙimar abin da ya kashe ya ciyar da talakawa, ko kuma ya yi azumi gwargwadon abincin kowane miskini guda ɗaya, Allah Maɗaukakin Sarki ya ce: ((Ya ku waɗanda suka yi imani, kada ku kashe abin farauta alhali kuna cikin Harami. Duk kuwa wanda ya kashe shi daga cikinku da gangan, to sakamakonsa shi ne (ya bayar) da kwatankwacin abin da ya kashe cikin dabbobin gida; waɗanda za su yi hukunci da wannan su ne mutum biyu adalai a cikinku, a matsayin hadaya wadda za ta isa Ka'aba, ko kuma ya yi kaffarar ciyar da miskinai, ko kuma ya yi azumi na kwatankwacin haka))[1].

Kashi na biyu: Shi ne Jima'i, yana ɓata aikin Hajji da Umra, kuma duk wanda ya aikata shi akwai ramuwa a kansa, kuma sai ya bayar da fidiya, wacce ita ce: Raƙuma idan ya yi jima'i a Hajji, ko tunkiya idan ya yi jima'i a Umara.

Kashi na uku: Shi ne ɗaura aure, ba ya inganta idan ya yi shi alhali yana cikin harama, kuma dole ya yi ramuwa, amma fidiya ba ta wajaba a kanshi ba.

---

[1]. [Al-Ma'ida: 95].

Kashi na huɗu: Sauran abubuwan da aka hana, kuma guda shida ne: Aske gashi, yanke farata, sanya ɗinkakken tufafi, sanya turare, rufe kai, runguma, fidiya a cikinsu zaɓi ne tsakanin abubuwa uku:

1- Yin azumin kwana uku.
2- Ko ciyar da miskinai shida.
3- Ko yanka rago.

Domin faɗin Annabi (SAW) ga Ka'ab ɗan Ujrah, lokacin da ƙwarƙwata da dame shi a kansa: (Ka yi azumin kwana uku, ko ka ciyar da miskinai shida, ko ka yanka rago) [1].

[1]. Bukhari (1815) da Muslim (1201) ne suka rawaito shi.

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Kukan kututture:

Ya tabbata a Sahihul-Bukhari[1] cewa lallai Manzon Allah (SAW) ya ƙasance yana hawa kan wani kututturen dabinon a ranar Jumu'a domin ya yi Huɗuba a kansa, a wata rana sai wata mata daga cikin mutanen Madina ta zo wurin Manzon Allah (SAW) ta ce masa: Ashe ba za ka bari mu yi maka mimbari ka riƙa yin huduba a kansa ba? Sai ya ce: "Idan kun ga dama za ku iya yi, sai wannan mata ta umurci ɗanta, wanda shi kafinta ne, sai ya yi masa mimbarin katako, sai suka sanya shi a cikin Masallaci, sai suka matsar da kututturen dabinon gefe, da ranar Jumu'a ta zo, kuma Manzon Allah (SAW) ya hau kan mimbarin domin ya fara huɗuba, sai aka ji kututturen dabinon na kuka da ƙarfi kamar kukan ɗan rakumi, sai Annabi (SAW) ya sauko daga mimbarin, ya zo wurin kututturen dabinon, ya ɗora hannunsa a kansa har sai da ya yi shiru.

- Kuma Hasanul-Basri ya kasance idan yana ba da wannan labari yana cewa: "Abin mamaki gare ku! Kututture na kuka saboda Manzon Allah (SAW), amma ku ba ku kuka dominsa)[2].

❖ Kawo masa koke da Rakumi ya yi:

An karɓo daga Abdullah ɗan Ja'afar (RA), cewa Manzon Allah (SAW) ya shiga gonar wani daga cikin Mutanen Madina, kwatsam sai ga rakumi a ciki, da ya ga Annabi (SAW) sai ya fara kuka, idanunsa suka yi ta zubo da hawaye, sai Annabi (SAW) ya zo ya shafa bayan kunnuwansa, sai ya yi shiru, sai ya ce: "Wanene mai wannan rakumin? Wannan rakƙumi na wane ne? Sai wani saurayi daga cikin Mutanen Madina ya zo, sai Manzon Allah (SAW) ya ce: "Ashe ba za ka ji tsoron Allah game da lamarin wannan dabba wacce

---

1. Sahihul-Bukhari (3585).
2. Fada'ilul-Madina (1/327).

Allah Ya mallaka maka ba?! Domin lallai ya kawo min ƙara cewa lallai kana barinsa da yunwa kuma kana wahalar da shi[1].

Ma’anar (ذِفراه – zifrah): wurin da ke fitar da zufa daga bayan kunnen rakumi. Kuma (تُدئبه – tud’hibuhu): Kana wahalar da shi.

[1]. Abu Dawud (2549), da Ahmad (1745) ne suka rawaito shi.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

AMRU ƊAN JAMUH (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Amru ɗan Jamuh ɗan Zaid ɗan ḤarAm Al-Khazraji Al-Ansari As-Sulami.

An haife shi a Madina, kuma ana yi masa inkiya da ɗan fari mai kudan gashi Mai farar fata mai ƙudan gashi.

Yana da ‘ya’ya maza huɗu: Mu'az, Mu'awwiz, Khallad, da Abdurrahman, kuma sun ƙasance suna halartar yaƙe-yaƙe tare da Annabi (SAW).

❖ Tarihinsa da falalara:

Ya ƙasance - (RA) - shugaba ne daga cikin manyan shugabannin Banu salima kuma daya daga cikin jagororinsu, ya shahara da ƙaramci, da kyauta da ladabi, da sauran kyawawan ɗabi’u na shugabanni da manyan mutane, don haka, mutanensa Banu Salima sun san darajarsa da kimarsa, kuma suna mutunta shi irin mutuntawar da ta dace da shi, kuma ya cancanci hakan

Yana da matsananciyar gurguntaka a ƙafarsa, amma hakan bai hana shi ƙarfin zuciya da tsayuwa ba, bari ma dai, hakan ya ƙara masa azama ne da ƙarfin guiwa.

Daga cikin labarinsa: akwai lokacin da ya ji yekuwar yaƙi a ranar Yaƙin Uhud, sai ya yi nufin fita don jihadi, sai ’ya’yansa suka so su hana shi, suka ce masa: “Ya kai babanmu! Lallai Allah Ya riga Ya ɗauke maka wajabcin halartar jihadi, kuma mu za mu wakilceka kamar yadda Allah Ya ce: ((Babu wani laifi a kan makaho, babu kuma wani laifi a kan gurgu, kuma babu wani laifi a kan marar lafiya

game da rashin fita yaƙi) [1], sai Amru ɗan Jumuh ya tafi wurin Manzon Allah (SAW) sai ya ce masa: "'Ya'yana suna so su hana ni fita tare da kai, na rantse da Allah ina fatan in taka Aljanna da wannan ƙafar tawa mai naƙasa", sai Annabi (SAW), Ya ce (Ai kai Allah maka uzuri, don haka jihadi bai wajaba a kanka ba), kuma ya ce wa 'ya'yansa: (Kada ku hana shi fita, ta yiwu Allah Ya azurta shi da shahada)[2], sai ya ɗauki makaminsa ya fita, ya yi ta yaƙi har sai da aka kashe shi.

❖ Rasuwarsa:

Ya yi shahada - (RA) - a yaƙin Uhud, a shekara ta 3 bayan Hijira. Annabi (SAW)ya ratsa a kusa da gawarsa ya ce: “Na rantse da Allah! Lallai ina ganin ka kana tafiya da wannan ƙafar taka mai naƙasa a cikin Aljanna, tana cikin koshinta) [3].

[1]. [Al-Fatḥ: 17].
[2]. Siratu Ibni Hisham (2/90) Dala'ilun-Nubuwwa na Baihaƙi (3/246).
[3]. As-Sunanul-Kubra na Baihaƙi (9/42).

Auna fahimtarka - a cikin darussan Mako na 50 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Mene ne ma'anar "Atraban?		b
	a. Masu tsawon jiki.	b. Tsararraki	c. 'Yan mata
Darasin Hadisi	Tambaya: Daga cikin abubuwan dake hana bawa amun lada, kuma ya sa ya ki yarda da ƙaddara?		c
	a. Raɗaɗi	b. Addu'ar neman mafita	c. Fushi da raki
Darasin Akida	Tambaya: Su wane ne An-Nawasib?		a
	a. Su ne waɗanda ke sukar Ahlul-Baiti	b. Su ne waɗanda ke ƙaunar Ahlul-Baiti	c. Su ne waɗanda ke wuce iyaka game da Ahlul-Baiti
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Mene ne fidiyar jima'i a cikin Umrah?		b
	a. Raƙuma	b. Akuya	c. Ciyar da miskinai shida
Darasin Sira	Tambaya: Rakumi ya yi ƙorafi ga Annabi (SAW)cewa maigidansa:		b
	a. Yana bugunsa	b. Yana barinsa da yunwa	c. Zai yanka shi
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Nakasar da aka jarrabci Amru ɗan Jamuh (RA)- da ita ita ce?		a
	a. Makanta	b. Kurumta	c. Gurguntaka mai tsanani

MAKO NA HAMSIN DA DAYA

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

AYATUL-KURSI

﴿ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُۚ لَا تَأۡخُذُهُۥ سِنَةٞ وَلَا نَوۡمٞۚ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ مَن ذَا ٱلَّذِي يَشۡفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦۚ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَيۡءٖ مِّنۡ عِلۡمِهِۦٓ إِلَّا بِمَا شَآءَۚ وَسِعَ كُرۡسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفۡظُهُمَاۚ وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡعَظِيمُ ٢٥٥﴾

❖ Fassara:

(Allah, babu wani abin bauta wa da cancanta sai Shi, Rayayye, Tsayayye da zatinsa; gyangyad ba ya kama Shi, ballantana barci, abin da yake cikin sammai da abin da yake cikin ƙasa nashi ne kaɗai, wane ne ya isa ya yi ceto a wurinsa in ba da izininsa ba? ya san abin da yake tare da su a yanzu da kuma abin da zai biyo bayansu; kuma ba sa iya sanin wani abu cikin iliminsa sai abin da ya ga dama. Kursiyunsa ya yalwaci sammai da ƙasa, kuma kiyaye su ba ya masa nauyi, kuma Shi ne Madaukaki Mai gima).

Falalarta:

Hadisai sun yawaita game da falalar ayatul kursiyu da ƙwadaitar wa game da ƙaranta ta, da kuma sanya ta ta zama wuridin safe da na yamma da lokacin barci, da kuma bayan sallar farilla, daga cikin waɗannan Hadisan akwai:

- An karɓo daga Ubayyu ɗan Ka'ab (RA) cewa lallai Manzon Allah (SAW)ya ce: ((Ya kai Baban Munzir, shin ko ƙasan wace aya ce mafi girma a littafin Allah take tareda kai?)) sai ya ce: na ce: (Allahu lailaha illahuwal hayyul-ƙayyum), ya ce: Sai ya dake ni a

kan ƙirjina, ya ce (Wallah ilimi ya zama abin daɗaɗuwa a gare ka ya kai Aba Munzir) [1].

- Kuma ya zo a cikin Sahihul-Bukhari daga Hadisin Abu Huraira (RA) cewa akwai abin da yake nuni game da cewa lallai duk wanda ya ƙaranta ta lokacin da ya hau shinfiɗarsa wani mai tsar daga Allah ba zai gushe ya tare da shi ba, kuma shaiɗan ba zai kusance shi ba har sai ya wayi gari[2].

❖ Baƙin Kalmomi

ٱلْقَيُّومُ	Alƙayyum	Tsayayye akan sha'anonin halittunsa
سِنَةٌ	Sinatun	Gyangyaɗi
كُرْسِيُّهُ	Kursiyyuhu	Wurin ƙafar Ubangiji
يَـُٔودُهُۥ	Ya'uduhu	Ya yi masa nauyi, Ya masa wahahla

❖ Ma'anar Ayoyin a Dunƙule:

Ayatul kursiyu ita ce mafi girma da falala da daukakar ayoyin Alƙur'ani, saboda abin da ta ƙunsa na tabbatar da halitta da bauta ga Allah shi kaɗai, da kuma bayanin sunayensa da siffofinsa da girmansa da buwayarsa da kuma gamewar mulkinsa da kuma gamewar iliminsa da yalwar mulkinsa da ɗaukakarsa akan halittunsa.

Allah Yana ba da labari cewa Shi ne abin bautawa da gaskiya babu abin bauta bisa cancanta sai Shi, Shi ke da rayuwa cikakkiya wacce rashi bai gabace ta ba kuma mutuwa ba za ta riske ta ba, kuma Shi ke da cikakkiyar tsayuwar zati da tsayuwarsa ga sha'anonin dukkan

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (810).
[2]. Bukhari ne ya rawaito shi (2311)

halittunsa, yana daga cikin kamalar rayuwarsa da cikar tsayuwar zatinsa: cewa Shi ba ya bacci kuma bacci ba ya ɗaukarsa, kuma Shi ne Mamallakin dukkan abin da ke cikin sammai da ƙasa, Shi ne Mamallakinsu ta fuskar halitta da mulki da azurtawa da kuma guɗanarwa, kuma duk wanda ba Shi ba to abin halitta ne kuma abin mallaka ne, abin azurtawa ne kuma abin guɗanarwa ne, ba ya mallaka ma kansa ko waninsa ko da kwatan-kwacin kwayar zarra, shi ya sa babu wanda zai samu ceto a wurinsa sai da izininsa, tsarki ya tabbata gare Shi, Shi ke da cikakken ilimi wanda ya ƙaraɗe komi da sanin ɗaiɗaikun halittunsa kuma Ya game da sanin abin da ya gabata na al-amura, da abin da ake fuskanta na alamarinsu, kuma bayi ba su da wani ilimi sai abin da Ya sanar da su, kursiyyunsa ta yalwaci sammai da ƙasa duk da girmansu da girman ababen da ke cikin su, ina kuma ga abin da ya fi kursiyyu girma wanda shi ne Al-Arshi, to ya kuma girman shi da girman Mahaliccinsu kuma makaginsu, Wanda ya halicci sammai da ƙasa kuma ya riƙe su don kada su zame daga inda suke ba tare da gajiyawa ko kagara ba cikin kiyayesu? Maɗaukaki a zatinsa a saman Al-Arshi Mai daukaka da rinjaya kan dukkan halittunsa, Maɗaukaki a ƙudurarsa saboda cikar kamalarsa cikin mulkinsa da girmansa da sarautarsa.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Ƙunsar Ayatul kursiyu ga sunayen Allah guda goma sha takwas tsakanin suna bayyanannne da kuma ɓoyayyaye.

2) Yalwar ilimin Allah da girman gudurarsa da kuma ƙaraɗewarsa da saninsa game da sha'anin halittunsa, da kuma cewa kiyaye su da kula da sa ba ya gajiyar da Shi.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WAJABCIN RINTSA IDO

An karɓo daga Jarir ɗan Abdullahi Allah Ya ƙara musu yarda ya ce: Na tambayi Manzon Allah (SAW) game da kallo na gaggawa sai, ya ce: **(Ka kame ganin ka)** [1].

❖ Sharhi:

Bawa yan yana bijirowa zuwaga fitintinu mawusu yawa a wannan duniyar, tsakanin fitintinun shubuha da fitintinun sha'awa, kuma daga cikin mafi girman fitintinun sha'awa akwai: fitnuwar maza da mata da kuma fitinuwar mata da maza.

Kuma kofar fadawa a cikin waɗannan fitinu shi ne sakin gani, saboda haka ne Allah Yayiwa muminai maza da mata umarni da kare gani, da kuma sanya shi cikin ya zama hanyar tsarkake zuciya da kuma tsaftace ta Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Ka ce da muminai maza su kame iɗanunsu kuma su kiyaye farjinsu, wannan shi ne yafi tsarki a gare su () Kuma ka ce da muminai mata su kame iɗanunsu kuma su kiyaye farjinsu)) [2].

Kuma kallo ya kan iya aukuwa ba tare da nufatar zuciya ba, shi ne abin da Hadisin ya kira shi da kallo na kaggawa, sai Annabi Ya umarci mumum da ya kame ganinsa da gaggawa da barin tsawaita ganin

❖ Ababuwan da za a Fahimta daga Hadisin:

1) Muhimmancin komawa ga malamai da kuma tambayarsu game da abin da ba'a gane ba.

---

1. Muslim ne ya rawaito shi (2159).
2. [An-Nur: 30-31].

2) Lallai haramcin kallo a sake abu ne tabbatacce a wajan Sahabbai, shi ya sa Jarir ya yi tambaya game da aukuwar kallo ba tare da mutum ya nufata ba.
3) Zunubi yana girmama iɗan gani ya ƙasan ce ta hanyar bincike da kuma satar gani.
4) Rintse gani ibada ce mai girma, za a ba ma'abocinta lada saboda ya myi ɗa'a ga umarniin shari'a.
5) Rintse gani alama ce ta tsarkin zuciya, da kuma hankali, da amanar ma'abocinsa.
6) Kallo zuwa ga abin da Allah Ya haramta ba tare da nufi ba bu laifi a cikin sa, sai dai ya wajaba a kame kallon nan take ba tare da cigaba ba.
7) Umarni da rintse gani ya shafi rintse ganin daga kallon hotuna haramtattu a TV ko waya ko jarida ko waninsu.
8) Aiki da ƙa'idar toshe kofofin da za su iya kaiwa ga ɓarna domin kallo da keɓewa haramcinsu ya zo ne ɗan toshe kofar zina.

TALATA: DARASI CIKIN AƙIDA

FALALAR SAHABBAI DA ABIN DA YA WAJABA A ƙUDURCE GAME DA SU

❖ Aƙidar Ahlis-Sunnah Wal-Jama'a game da Sahabbbai:

Sahabi: shi ne wanda ya haɗu da Annabi (SAW) yana mai imani da shi, kuma ya mutu akan haka.

Kuma Aƙidar Ahlissunnah wal -jama'a game da Sahabbai: shi cewa lallai su ne mafifitan Al-umma, kuma zamaninsu ne mafi alherin zamani, saboda rigayarsu da imani da kuma keɓantarsu da abotar Annabi (SAW), da jihadi tare da shi, da kuma ɗaukar shari'a daga gare shi da isar da ita ga waɗanda suka zo bayansu.

Su Ahlisunna suna son Sahabbai kuma suna girmama su, kuma suna komawa zuwa ga zantuttukansu da fahimtarsu wajen fahimtar nassoshin addini, domin su ne mafi alherin mutane, kuma su ne mafi kusancin mutane zuwa ga mashayar Annabta mai tsafta, kuma su ne mafiya sanin mutane da abin da Allah Ya ke nufi da kuma abin da Manzonsa (SAW) ya ke nufi.

❖ Falalar Sahabbai

Allah Maɗaukaki Ya yabi Sahabbai a cikin kyutataccen littafinsa Ya ke cewa: ((Muhammadu Manzon Allah ne. Waɗanda kuma suke tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, kuma masu tausayin junansu ne; za ka gan su suna ruku’i suna sujjada suna neman falala daga Allah da yardarsa; alamominsu na gurbin sujjada suna bayyana a fuskokinsu. Wannan shi ne misalinsu a cikin Attaura. Misalinsu kuwa a cikin Linjila kamar shuka ce da ta fitar da reshenta sai ya ƙarfafe ta, sannan ta yi kauri sai ta daidaita a kan tushiyarta ta riƙa ƙayatar da manoma, don Ya cusa wa kafirai haushi. Allah Ya yi wa

waɗanda suka yi imani suka kuma yi ayyuka nagari daga cikinsu alƙawarin gafara da lada mai girma))[1].

Kuma Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Magabata kuwa na farko daga cikin masu hijira da Ansaru da kuma waɗanda suka biyo bayansu da kyautatawa, (duka) Allah Ya yarda da su, su ma sun yarda da Shi, Ya kuma tanadar musu gidajen Aljanna da ƙoramu suke guɗana ta ƙarƙashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wannan shi ne rabo mai girma))[2].

A cikin waɗannan Ayoyi akwai jumloli na nau'ikan yabo ga Sahabbai da kuma siffanta su da jinkai a tsakaninsu da tsanani ga kafirai da kuma siffanta su da yawan ruku'u da sujuda da kyutatuwar niyoyi da zuciya, da cewa lallai su ana sanin su ne da alama ta ɗa'a da Imani, da kuma cewa lallai Allah Ya zabe su ne domin don abota da Annabinsa saboda ya sanya ma kafirai baƙin ciki da su, kuma Allah Ya keɓance Muhajirai da Ansar da ƙarin falala da daraja, sai Ya siffantasu da rigaye zuwa ga alkhairai, kuma ya ba da labari cewa Ya yarda da su, kuma Ya tanada musu gonaki na dawwama a lahira.

Ya zo a cikin Sunnah ya tabbata cewa Manzon Alllah (SAW) ya yabi Sahabbai da kuma fifitasu akan sauran mutane, kuma lallai Allah Zai saka musu da bisa kyutatawarsu da irin abin da ba Zai ba da shi ga waninsu ba, Manzon Allah (SAW) ya ce :(Mafi alherin mutane su ne mutanen zamani na)[3]. Kuma ya ce: (Kada ku zagi Sahabbaina, na rantse da wanda raina ke hannunsa, da ɗayanku zai ciyar da kwatankwacin dotsen Uhudu na zinari, ba zai kai mudun ɗayansu ba ko rabin shi)[4].

Kuma a lokacin da Annabi (SAW) ya ambaci karkasuwar Al-umma zuwa kashi saba'in da uku, kuma lallai su na cikin wuta sai guda

---

1. [Al-Fath 26].
2. [At-Tauba: 100].
3. Bukhari ne ya rawaito shi (6429).
4. Bukhari (3673) da Muslim (2540) ne suka rawaito shi.

ɗaya, sai suka tambaye shi game da wannan ɗayan, sai ya ce: (Su ne waɗanda suke kan abin da nake kansa a yau ni da Shabbaina) [1].

Wannan su ne wasu daga acikin falalolinsu gamammu kuma akwai wasu fololin na daban wanda wasunsu suke keɓanta da su da gwargwadon rigayarsu zuwa musulunci da jihadi da hijirah, kamar misalin falalar halifofi guda huɗu sannan sauran goman da aka yi musu bushara da Aljanna, sannan waɗanda suka halarci yaƙin Badar sannan waɗanda suka halarci Bai'atur-Ridwan.

[1]. Tirmizi ne ya rawaito shi (2641).

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

AYYUKANA HAJJI DA NA UMRA

Ayyukan Hajji da na Umra sun kasu zuwa: Rukunnai, Wajibbai, da Sunnoni.

Rukunnai yana wajaba a aikata su dukkansu, kuma ibadar mutun ba ta inganta idan ya bar wani abu daga cikinsu, kuma wajibabbun abubuwa idan aka bar wani abu daga cikinsu, to ana iya gyara shi ta hanyar yanka.

❖ **Rukunan Umra gudu uku ne:**

Harama, Dawafi, Sa'ayi.

Kuma abubuwan da suka wajaba a umrah guda biyu ne:

Ɗaukar harama daga miƙati, da kuma aski ko saisaye.

❖ **Rukunnan Hajji kuwa guda huɗu ne:**

1. Ɗaukar harama: shi ne niyyar shiga aiki saboda fadin Annabi (SAW): (Abin sani kawai, ayyuka bas u inganta sai da niyyoyi, kuma abin sani kawai, kowane mutum yana da ladar abin da ya yi niyyah) [1].
2. Tsayuwar Arfa ranar tara ga watan zulhijjah, saboda fadin Annabi (SAW): (Hajji shi ne Arfa) [2].
3. Ɗawafin ifada a ranar goma ga wata, Allah Maɗaukaki Ya ce : (kuma su yi ɗawafi a ƴantaccen Ɗakin ka'aba) [3].
4. Sa'ayi saboda fadin Annabi (SAW): (Ku yi sa'ayi domin Allah Ya wajabta muku sa'ayi) [4].

❖ **Amma abubuwan da suka wajaba a Hajji su ne kamar haka:**

1- Ɗaukar harama: daga migati.

---

[1]. Bukhari (1) da Muslim (1907) ne suka rawaito shi.
[2]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (1949).
[3]. Al-Hajj [29].
[4]. Ahmad ne ya rawaito shi (27407).

2- Zama a arafa har zuwa magriba.
3- Kwana a muzdalifa a daren goma wata.
4- Kawana a mina dararrakin ayyamu-ttashriƙ.
5- Jifan jamrori: jamratul aƙabah ranar idi, da kuma jamrori uku ayyamu-ttashriƙ.
6- Aski ko saisaye, sai dai mace za ta yanke gashinta ne ƙwarƙwaɗon saman ɗan yatsa.
7- Ɗawafin ban-kwana.

Duk wanda ya bar wani abu daga cikin abubuwan da suka wajaba, to dole ya gyara shi ta hanyar yanka ƙaramar dabba ko kuma manyan dabbobi guda baƙwai ko kuma saniya baƙwai, za'a yanka ne a Makka, za a ba wa talakawan Harami, saboda faɗin ibnu Abbas Allah Ya ƙara masu yarda cewa:(Wanda ya manta wani abu daga cikin ayyukan Hajji to ko ya bar shi, to ya zubar da jini)[1].

❖ Amma abin ba waɗannan rukunnan abubuwan da suka wajaba ba, to sunnoni ne da mustahabbai, laɗan hajji yana cika da su ne saboda koyi da Annabi (SAW), kamar misalin kwana a Mina a ranar taƙwas ga wata, da ɗawafin isowa, da kuma azkar da addu'oin da aka rawaito, da talbiyya tun daga ɗaukar haramar Hajji har zuwa lokacin jifan jamratul aƙaba, da kuma lokacin Umra har zuwa lokacin ɗawafi.

[1]. Malik ne ya rawaito shi (1258).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA

❖ Rusinawar bishiya gare shi:

An karɓo daga Jabir ɗan Abdullahi Allah Ya ƙara musu yarda ya ce: Mun yi tafiya da Manzon Allah (SAW) har sai da muka sauka kwarin Afyaha, sai Manzon Allah (SAW) ya tafi ɗon biyan bukatarsa, sai na bi shi da salkar ruwa, sai Manzon Allah (SAW) ya duba bai ga abin da zai yi sutura da shi ba, sai ga bishiyoyi biyu a gefen wannan kwari sai Manzon Allah (SAW) ya tafi wajen ɗaya daga cikinsu, sai ya riƙe ɗaya daga cikin rassanta, sai ya ce: (Ki taho zuwa gare ni da izinin Allah), sai ta taho gare shi kamar raƙumi mai linzami da yake bin mai janye da shi, har sai da ya je wajan dayar bishiyar, sai ya riƙe ɗaya daga cikin rassanta sai ya ce: kitaho zuwa gare ni da izinin Allah, sai ta bi shi ita ma, har sai da ya ƙasance a tsakiyansu, sai ya haɗa tsakaninsu, sai ya ce: ku yi min rumfa sai suka haɗe suka masa rumfa, sai na zauna ina zancen zuci, sai na waiga kwatsam sai ga Manzon Allah (SAW) ya dumfaro, sai ga bishiyoyin nan biyu sun rabu da juna, kowacce sai ta tsayu akan kafarta)[1].

❖ Sallamar Dutse gare shi:

An karɓo daga jabir ɗan Samurata (RA) ya ce: Manzon (SAW) ya ce: (lallai na san wani dutse a Makka da ya ƙasance yana min sallama kafin a aiko ni kuma lallai ni a yanzu haka na san shi)[2].

Imamun-Nawawi ya ce: kamar yadda Allah Ya ce: ((Babu wani abu face yana tasbihi tare da yabonsa, sai dai ku ba ku fahimtar tasbihin nasu))[3], kuma kamar yadda kututturen dabino ya yi kuka gare shi, da yadda tsakuwa ta yi tasbihi da yadda dutse ya gudu da tufafin

---

1. Muslim ne ya rawaito shi (3012).
2. Muslim ne ya rawaito shi (2277).
3. [Al-Isra: 44].

Annabi Musa amincin Allah Ya tabbata a gare shi, to ko wani abu yana tasbihi a haƙiƙa gwargwadon halinsa, sai dai ba ma iya fahimta[1].

[1]. Sharhin Nawawi ga muslim (9/140).

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

AMRU ƊAN AS (RA)

❖ Sunansa da Haihuwarsa:

Shi ne Amru ɗan As ɗan Wa'il ɗan Hisham ɗan ƙabilar saham.

An haife shi a Makka sheƙara ta 47 kafin Hijira.

❖ Tarihinsa da Falalarsa:

Ya kasance (RA) mai dara-daran iɗanu ne, mai hasken fuska, mai cikar gemu, mai faɗin kafaɗa, mai yalwar tafukan hannu da kafafu, yana yi wa gashinsa lalle, ya ƙasance daga cikin jaruman ƙuraishawa, a zamanin jahiliyya su na ƙirga shi daga cikin ɗai-ɗaikun masu kaifin ƙwaƙwalwa na wancen zamani gami da basira da fasaha da jajircewa da azama da sani salon yaƙi, ya ƙasance bajimin mawaƙi, an rawaito waƙoƙi masu yawa daga gare shi[1].

Ya yi hijira zuwa ga Manzon Allah (SAW) yana musulmi a farkon sheƙara ta takwas, tare da Kalid ɗan Walid da Usman ɗan Ɗalha, sai Manzon Allah ya yi farin ciki da isowarsu da kuma musuluntar su[2], tun da ya musulunta zuciyarsa ta cika da ƙauna da girmama Annabi tsira da amincin Allha su tabbata a gare shi.

(RA) yana cewa: "ina rantsuwa da Allah lallai ina daga cikin mafi jin kunyar Manzon Allah tsira da amincin Allha su tabbata a gare shi, ban taɓa cika idauna da Manzon ba kuma ban taba zuwa na tambaye shi wani abin da nake so ba har ya haɗu da Allah, saboda jin ƙunyarsa"[3].

Kuma haƙiƙa Annabi tsira da amincin Allha su tabbata a gare shi ya yabe shi kuma ya shaida masa da Imani, ya ce, sai Manzon Allah

---

1. Siyaru A'alamin-Nubala (3/55).
2. Siyaru A'alamin-Nubala (3/55.
3. Muslim ne ya rawaito shi (121).

tsira da amincin Allha su tabbata a gare shi ya ce: ('Ya'yan As muminai ne Amru da hisham)[1].

Annabi sira da amincin Allha su tabbata a gare shi ya nada shi jagorancin rundunar Zatus-Salasil, kuma a cikin su akwai Abubakar da Umar[2], wannan ya faru ne a Jumadal-Akhir shekara ta takwas bayan Hijira, (RA) yana cewa: Annabi tsira da amincin Allha su tabbata a gare shi ya aiko min da cewa ka dauki tufafinka da makaminka ka zo wurina, sai na je na samu yana alwala, sai ya kura min ido, sannan ya dawo cikin hayyacinsa, sai ya ce : lallai ina so na nada ka jagorancin wata runduna, Allah Ya amintar da kai, kuma ya ba ka ganima, kuma ina maka kyakkyawar fatan samun dukiya, sai na ce: Ya Manzon ba don kudi na Musulunta ba, sai dai ni na musulunta ne ina mai kwadayin musulunci, kuma don na kasance tare da Manzon Allah (SAW), sai Manzon Allah Ya ce: Ya Amru madalla da dukiya ta gari ga mutum na gari[3].

kuma a Ramadan Annabi (SAW) ya aike shi cikin wata rundunar kwantar bauna domin su rusa gunkin Suwa'a.

Kuma a watan Zul-Hjja Annabi (SAW) ya aika shi da wata wasika zuwa ga sarakunnan Uman su biyu yana kiransu zuwa ga musulunci, kuma bayan sun musulunta sai Annabi (SAW) ya sanya shi ya zama mai karbar zakka a wannan gari, sai ya zauna a wannan gari har tsawon shekaru biyu har sai da Annabi (SAW) ya yi wafati.

A zamanin halifancin Abubakar Amru ya kasance shi ne jagoran yakar wadan da suka yi ridda, kuma shi ne kwamandan yakin bude Falasdinu yana jagorantar mayaka dubu shida, kuma shi ne kwamandar rundunar bangaren dama na yakin Yarmuk.

A zamanin halifancin Umar Allah Ya kara musa yarda da Amru aka bude garin Dimashka da Baitul Makdis, kuma ya hadu da Khalid

[1]. Nasa'i ne ya rawaito shi a Sunanul-Kubra (8300).
[2]. Bukhari (3662) da Muslim (2384) ne suka rawaito shi.
[3]. Bukhari ne ya rwaito shi a cikin Adabul-mufrad (299).

ɗan Walid a yaƙin Ajnadin, kuma Abu Ubaida ya tura shi don sulhu da mutanen Halab da na Anɗakiya.

Kuma a lokacin da aka jarabci Abu Ubaida da annobar Amwas ya sanya Amru a matsayin shugaban Falasɗinu da Urdun da sauran garurruwan Sham.

Kuma a shekara ta 20 bayan Hijira Amru ya bijiro wa Umar (RA) da shawarar buɗe Misra, sai Amru ya buɗe ta sai ya zama Gomnan musulmi na farko a garin, kuma ya samar da garin Gosɗandiniyya ya kuma gina masallaci na farko da aka san shi da sunan Amur daga baya.

A zamanin halifancin Usman Amru ya buɗe garin Iskandariya a shekara ta 21 bayan Hijira sannan ya buɗe Ɗarabulus a shekara ta 24 bayan Hijira.

❖ Rasuwarsa:

(RA) ya rasu a daren ƙaramar sallah shekara ta 43H a Misra yana da shekara 88.

Auna fahimtarka - a cikin darussan Mako na 51 -			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	Tambaya: Menene ma'anar "Ya'uduhu?		a
	a. yana masa nauyi da tsanani	b.yana cutar da shi	c. yana mantar da shi.
Darasin Hadisi	Tambaya: Ƙofar faɗawa cikin fitinar sha'awa ita ce ?		b
	a.Yawaita cin abinci	b. Yawaita yin bacci	c. Rashin kame gani
Darasin Aƙida	Tambaya: Su wanene mafi falalar alumma kuma mafi kyawun ƙarni?		b
	a. masu jihadi	b. sahabbai	c. malamai.
Darashin Fiƙihu	Tambaya: Daga cikin abubuwan da suka wajaba a Hajji akwai:		a
	a. Ɗaukar harama daga miƙati	b. Ɗaukar ihrami a mina ranar takwas ga wata	c. Ɗawafin isowa
Darasin Sira	Tambaya: Daga cikin alamomin Annabtar Annabinmu Muhammadu akwai:		c
	a. Maganar duwatsu gare shi	b. Hura masa iska da akayi	c. Sallamar duwatsu gare shi
Darasin Tarihin Sahabbai	Tambaya: Daga cikin garurrukan da Amru ɗan As ya buɗe akwai?		b
	a. Roma	b. Misra	c. Ƙusdandiniyya

MAKO NA HAMSIN DA BIYU

LAHADI: DARASI CIKIN TAFSIRI

AYOYIN ƘARSHEN SURATUL-BAƘARA

﴿ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ وَقَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ غُفۡرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيۡكَ ٱلۡمَصِيرُ ٢٨٥ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِلَّا وُسۡعَهَاۚ لَهَا مَا كَسَبَتۡ وَعَلَيۡهَا مَا ٱكۡتَسَبَتۡۗ رَبَّنَا لَا تُؤَاخِذۡنَآ إِن نَّسِينَآ أَوۡ أَخۡطَأۡنَاۚ رَبَّنَا وَلَا تَحۡمِلۡ عَلَيۡنَآ إِصۡرٗا كَمَا حَمَلۡتَهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِنَاۚ رَبَّنَا وَلَا تُحَمِّلۡنَا مَا لَا طَاقَةَ لَنَا بِهِۦۖ وَٱعۡفُ عَنَّا وَٱغۡفِرۡ لَنَا وَٱرۡحَمۡنَآۚ أَنتَ﴾

❖ **Fassara:**

1. Manzon ya yi imani da abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa, muminai ma haka, kowanne ya yi imani da Allah da mala'ikunsa da littattafansa da manzanninsa, suna cewa: "Ba ma nuna bambanci tsakanin ɗaya daga cikin manzanninsa." Kuma suka ce: "Mun ji kuma mun bi; muna neman gafararka ya Ubangijinmu, kuma zuwa gare Ka ne makoma take)).
2. Allah ba Ya kallafa wa rai sai abin da zai iya. Abin da ya aikata na alheri) nasa ne, hakanan sakamakon abin da ya aikata (na sharri) shi ma nasa ne. Ya Ubangijinmu, kada Ka riƙe mu da laifi iɗan mun yi mantuwa ko mun yi kuskure. Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana wani nauyi irin wanda ka ɗora wa waɗanda suke gabaninmu. Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana abin da ba mu da iko a kansa, kuma Ka yi mana afuwa, kuma Ka yi mana gafara, kuma Ka ji ƙan mu; Kai ne Majiɓincin lamarinmu, don haka Ka taimake mu a kan mutane kafirai.

❖ Sababin saukar Ayoyin:

Lokacin da faɗin Allah Maɗaukaki ((Kuma in har kuka bayyana abin da yake cikin zukatanku ko kuka ɓoye shi, Allah zai yi muku hisabi a kansa)[1], ya sauka, sai hakan ya tsananta ga sahabbai suka ce: Ya Manzon Allah, an wajabta mana abin da zamu iya na aiki kamar salla, azumi, jihadi, sadaka, kuma haƙiƙa an saukar maka da wannan aya kuma ba za mu iya aiwatar da ita ba, sai Manzon Allah (SAW) ya ce:(Shin kuna son ku faɗi irin abin da ma'abota littafi gabaninku suka faɗa: Mun ji kuma mun saɓa!? A'a cewa za ku yi: "Mun ji mun yi ɗa'a gafararka muke nema ya Ubangijinmu kuma zuwa gare ka makoma take", sai suka faɗi hakan, kuma yayin da mutane suka yi ta ƙaranta ta, harsunansu suka saba furta ta, sai Allah Ya saukar a bayanta cewa: (Manzon ya yi imani da abin da aka saukar masa daga Ubangijinsa, da muminai) lokacin da suka aiwatar sai Allah Ya saukar da ((Allah ba Ya kallafa wa rai sai abin da zai iya. Abin da ya aikata (na alheri) nasa ne, hakanan sakamakon abin da ya aikata (na sharri) shi ma nasa ne. Ya Ubangijinmu, kada Ka riƙe mu da laifi idan mun yi mantuwa ko mun yi kuskure)) sai Allah Ya ce: Haƙiƙa na yi muku[2].

❖ Falalar Ayoyin:

- An karɓo daga Abdullahi ɗan Abbas Allah Ya ƙara musu yarda ya ce :Wata rana Jibril yana zaune a wajan Annabi (SAW)kwatsam sai ya ji wani sauti daga samansa, sai ya ɗaga kansa ya ce: Wannan wata koface ta Aljannah da aka buɗe ta yau, ba a taɓa buɗe ta ba sai a yau, sai wani Mala'ika ya sauko ya ce: Wannan wani mala'ika ne ya sauko ƙasa bai taɓa saukowa ba sai yau, ina maka bushara da haske guda biyu da ba a bai wa wani Annabi ba kafinka, suratul-fatiha da kuma ƙarshen suratul-Baƙara ba za ka ƙaranta ɗaya daga cikinsu ba face sai an ba ka laɗansa[3].

---

1. [Al-Baƙara: 284].
2. Muslim ne ya rawaito shi (125).
3. Muslim ne ya rawaito shi (806).

- Kuma an karɓo daga Abu Mas'ud Albadri (RA) cewa lallai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Duk wanda ya ƙaranta ayoyi biyu na ƙarshen suratul baƙara a cikin dare to sun isar masa) [1].

❖ **Ma’anar Ayoyin a dunƙule:**

A cikin wannan ayoyi Allah Yana ba mu labari game da imanin Manzon Allah (SAW) da imanin muminai tare da shi Manzon Allah da Mala'kunsa da littattafansa da da Manzaninsa da kuma irin miƙa wuyarsu da ɗa'arsu cikin haka, da irin roƙonsu na yafiya da gafarar Allah.

Kuma imani da Allah Ya ƙunshi imani da dukkan abin da Ya ba da labari game a kanshi, da kuma abin da Manzanninsa suka ba da labari na siffofin kamalarsa da ɗaukakarsa.

Kuma imani da mala'iku ya ƙunshi imani da sunayensu da siffofinsu da ayyukansu a dunƙule da fayyace, kuma imani da manzanni da littattafai ya ƙunshi imani da dukkan abin da Manzanni suka ba da labari a kai, da abin da littattafai suka ƙunsa na umarni da hani.

Sannan Allah Ya ba da labari cewa lallai muminai ba sa nuna bambanci tsakanin wani daga cikin Mazanni, bari dai su na yin imani da su ne dukkanin su domin saƙonsu ɗaya ne, kuma shi ne kaɗaita Allah da aiki da sharia'arsa, domin kafirci da wani sashed aga cikinsu kafircine ga dukkaninsu, muminai su ka ce mun ji kuma munyi Imani, gafararka muke nema ya Ubangijinmu kuma zuwa gare ka makoma take ranar ƙiyama.

Sannan Allah Mai girma da ɗaukaka Ya bayyana a aya ta biyu cewa lallai addininsa sauƙi ne babu tsananini a cikinsa, da kuma cewa ba ya neman daga bayinsa su aikata abin da ba za su iya ba, don haka duk wanda ya aikata alheri to yana da laɗan abin da ya aikata, kuma ba za a tauye masa komai ba, kuma duk wanda ya aikata sharri to

[1]. Bukhari (4008) da Muslim (807) ne suka rawaito shi.

zai tarar da sakamakon abin da ya aikata kuma babu wanda zai ɗauke masa nauyin zunubinsa.

Sannan ya bayyana cewa lallai addu'ar Manzon Allah (SAW) da muminai ita ce: Ya ubangijinmu kada Ka kama mu iɗan muka aikata wani abu da mantuwa ko kuskure, kuma kada ka ɗaura mana wani nauyi ko tsanani da ba za mu iya ɗauka ba kamar yadda ka ɗaura wa waɗanda Ka yi musu uƙuba gabaninmu saboda zaluncinsu kamar Yahudawa, Ka yi mana afuwa ka gafarta mana kuma Ka yi mana rahama, kai ne Majiɓincinmu masoyinmu kuma mai ba mu nasara, Ka ba mu nasara akan mutane azzalimai.

❖ Abubuwan da za a koya daga Surar:

1) Dukkan Tabbatar da rukunnan imani da kuma bayanin ginshiƙansa.
2) Cewa lallai imani shi ne mabuɗin miƙa wuya, domin a farkon ayar an siffanta su da imani a ƙarshen ayar kuma an siffantasu da amsa kira.
3) Rahamar Allah ga bayi, saboda bai ɗaura musu abin da ba za su iya ba, kuma ba zai yi musu hisabi ba sai a kan abin da suke iyawa.
4) Cewa lallai samuwar gajiyawa da tawaya abu ne da babu makawa ga ɗan'adam, saboda haka ne aka rufe ayoyin da neman afuwa da gafara da rahama.

LITININ: DARASI CIKIN HADISI

WASU DAGA CIKIN ADDU'O'I MASU AMFANI

An karɓo daga Abdullahi ɗan Umar Allah Ya ƙara musu yarda ya ce Annabi (SAW) bai kasance yana barin ƙaranta waɗannan kalmomi ba iɗan ya wayi gari ko iɗan ya yammata ba

(اللَّهُمَّ إِنِّي أَسْأَلُكَ الْعَافِيَةَ فِي الدُّنْيَا وَالْآخِرَةِ، اللَّهُمَّ إِنِّي أَسْأَلُكَ الْعَفْوَ وَالْعَافِيَةَ فِي دِينِي وَدُنْيَايَ وَأَهْلِي وَمَالِي، اللَّهُمَّ اسْتُرْ عَوْرَاتِي وَآمِنْ رَوْعَاتِي، اللَّهُمَّ احْفَظْنِي مِنْ بَيْنِ يَدَيَّ وَمِنْ خَلْفِي، وَعَنْ يَمِينِي وَعَنْ شِمَالِي وَمِنْ فَوْقِي، وَأَعُوذُ بِعَظَمَتِكَ من أَنْ أُغْتَالَ مِنْ تَحْتِي).[1]

(Ya Allah lallai ni ina roƙon ka lafiya a duniya da lahira, ya Allah lallai ni ina roƙon ka yafiya da lafiya cikin addinina da duniyata da iyalaina da dukiyata, ya Allah ka suturtamin alaurata ka amintar da tsorona, ya Allah ka kiyaye min gabana da bayana, ka tsare damata da haguna, ka tsare samata da ƙasata, ina neman tsari da girmanka ka tsare ni kada a hallaka ni ta ƙasata.

❖ Sharhi:

Annabi (SAW)ya kasance mai yawan addu'a ne ga Ubangijinsa Mai gairma da ɗaukaka, kuma mai yawan ƙanƙan da kai ne gare shi tsarki ya tabbata gare shi, a cikin wannan Hadisi akwai ba da labari cewa Annabi (SAW)ya kasance yana da wasu addu'oi da ba ya barin su har abada, ma'anar **(وَحِينَ يُصْبِحُ):** wato iɗan ya wayi gari **(وحِينَ يُمْسِي)** iɗan ya yammata (الْعَافِيَةَ) aminci da tsira **(الْعَفْوَ)** yafiya **(فِي دِينِي وَدُنْيَايَ)** a duniyata da lahirata **(وَأَهْلِي)** matana, ƴaƴana da ma ƙusantana **(وَمَالِي)** dukiyata da abin da zai shiga cikin wannan ma'ana na daga aiki da kasuwanci da wanin wannan.

(اللَّهُمَّ اسْتُرْ) ka suturta **(عَوْرَاتِي)** alaurata, da duk abin da bayyanarsa zai baƙanta min **(رَوْعَاتِي)** ka amintar ɗa ni daga duk abin da zai razanar

[1]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (5074).

da ni ya samin tsoro sai ya ambaci **(الرَوْعَات)** da sigar jam'i saboda yawan abubuwan tsoro dake kewaye da ɗan'adam.

(اللَّهُمَّ احْفَظْنِي مِنْ بَيْنِ يَدَيَّ وَمِنْ خَلْفِي، وَعَنْ يَمِينِي وَعَنْ شِمَالِي وَمِنْ فَوْقِي) m'ana ka tsare ni ta ko wani ɓangare kada wani mummunan abu ya same ni, **(وَأَعُوذُ بِعَظَمَتِكَ)** ina neman kariya kuma ina fakewa da girmanka da ƙarfinka da ƙudurarka **(أُغْتَالَ مِنْ تَحْتِي)** kada dulmiyar da ni ko a halakar da ni.

❖ Abin da za a koya daga Hadisin

1) Muhimmancin zikirin safe da na yamma domin - da izinin Allah – suna tsare musulmi daga sharruka da shaiɗanu.
2) Wajibcin dogaro ga Allah da mayar da al'amura gare shi cikin dukkan abin da ya damu musulmi na neman alkhairi ko guje ma sharri.
3) Muhimmancin ƙoƙari wajen suturta alaura da aibobi, da kuma roƙon Allah akan ya jiɓinci hakan don kada bawa ya tozarta.
4) Lallai cikin ambaton Allah aƙwai waraka mai amfani ga abin da mutum yake tsoro da abin da yake razana sa da baƙanta masa.

TALATA: DARASI CIKIN AƘIDA

MATSAYAR AHLUS-SUNNA GAME DA SAƁANIN SAHABBAI

Ahlisunnah Wal-Jama'a suna da tsakatsakiyar matafiyar game da abin da ya auku na saƁani a tsakanin sahabbai, wanda za mu iya taƙaita shi cikin wasu al'amura:

Al'amari na farko: Cewa lallai su suna kamewa game da abin da ya faru a tsakanin sahabbai, kuma suna kamewa game da ba da labarinsa da kutsawa cikinsa, domin yin shiru cikin irin wannan abu shi ne hanyar tsira aiki da faɗin Allah Maɗaukaki: ((Waɗanda suka zo bayansu cewa suke ya Ubangijinmu ka gafarta mana mu da yan'uwanmu da suka rigaye mu ga imani, kuma kada Ka sanya wata ƙullata a zukatanmu game da waɗanda sukayi imani ya Ubangijinmu, lallai kai Mai tausayi ne, Mai jin ƙai)) [1].

Alamari na biyu: Tace labaran da aka rawaita game da haka domin a cikinsu a akwai ƙarerayi da maƙiyansu suka ƙaga domin su ɓata musu suna, kuma a ciki aƙwai ƙari da ragi, kuma akwai wanda aka juyar da shi daga fuskarsa ta gaskiya.

Alamari na uku: Sanin cewa abin da ya inganta daga cikin wannan labarai kaɗan ne, kuma su sahabbai abin bai wa uzuru ne a cikinsa, domin su sahabbai cikin wannan abu ko dai masu ijtadi ne da suka dace da daidai, ko kuma masu ijtihadi ne da suka yi kuskure, kuma haƙiƙa Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce:(Idan shugaba ya yi yayi hukunci ya kuma dace da daidai to yana da lada biyu, idan kuwa ya yi kuskure to, yana da lada ɗaya) [2].

Alamari na hudu: A sani cewa lallai sahabbai mutane ne ba ma'asumai ba, ɗayansu na iya faɗawa cikin laifi, kuma kurakuransu akwai abubuwa masu yawa da za su kankare su, daga cikin akwai:

---

1. [Al-Hashr 20].
2. Bukhari (7352) da |Muslim (1716) suka rawaito shi.

Tuba, jihadi, rigayar mu zuwa ayyuka masu falala da na alheri, kuma haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya ce: ((Lallai kyawawa ayyuka suna tafiyar da mumunana) [1].

Saboda haka bai halarta ba a riƙi kurakuransu a matsayin tsani zuwa ga cin mutuncinsu ko taɓa ƙimarsu, alhali haƙiƙa Manzon Allah ya ce: (Kada ku zagi sahabbaina, na rantse da wanda raina ke hannunsa da ɗayanku zai ciyar da kwatankwacin dutsan uhudu na zinari, ba zai taɓa kai mudun ɗayansu ba, ko rabinsa) [2].

[1]. [Hud:114].
[2]. Bukhari (3673) da Muslim (2540) ne suka rawaito shi

LARABA: DARASI CIKIN FIƘIHU

HUKUNCE-HUKUNCEN ƊAWAFI DA DA SA'AYI

❖ Sharuɗɗan ɗawafi:

1. Tsarki daga hadasi da najasa.
2. Suturta al'aura, domin da mutum zai yi ɗawafi ba tare da suturta al'aura ba, to ɗawafinsa ya ɓaci.
3. Ya fara ɗawafi daga wurin Hajarul-aswad ya ƙare a wurin.
4. Ɗakin Ka'aba ya kasance a hagunsa lokacin ɗawafi.
5. Ɗawafin ya ƙasance daga wajan ka'aba. domin da zai yi ɗawafi a cikin Ka'aba ko a Hijiru Ismail to bai inganta ba domin Hijiru Isma'il yanki ne na Ka'aba.
6. Ɗawafi ya ƙasance kewaye baƙwai cikakku, domin ƙasa da haka bai inganta ba.
7. Da jerantawa da yi ɗaya bayan ɗaya tsakanin adadin dawafi, dakatawa 'yar kaɗan ba ya tasiri wuri ɓacin ɗawafin kamar sallah da makamantanta.
8. Tafi yayin ɗawafi iɗan zai iya.

❖ Sunnunin Ɗawafi:

1. Shafar Hajarul-aswad da sunbatar shi a farkon kowani zagaye iɗan hakan ya samu, iɗan kuwa bai samu ba, to ya shafa shi sai ya sumbaci hannunsa, idan haka bai samu ba, to ya yi nuni da hannunsa ya yi kabbara.
2. Ya ce (Bismillahi Allahu Akbar, Allahumma imanan bika wa tasdiƙan bi kitabika, wa wafa'an bi ahdika, wattiba'an lisunnati nabiyyika, Muhammadin Sallalahu alaihi wa sallam) [1].
3. Ya ce a tsakanin Ruknul-yamani da Hajarul-aswad: "Rabbana Atina fidduniya Hasanatan wa Filakirati Hasanatan waƙina Azabannar"[2].
4. Iɗɗiba'i, wato buɗe kafaɗa ta dama, ta yadda zai sanya gefen gyauto akan kafadarsa ta hagu, ya sanya tsakiyarsa ƙarƙashin

---

[1]. Ɗabrani (1/157) da Baihaƙi (5/79) ne suka rawaito shi.
[2]. Abu Dawuda ne ya rawaito shi (1892).

hammatarsa ta dama, wannan ya keɓanta ne kawai ga ɗawafin isowa da Umrah ban da ɗawafin Ifada daga muzdalifa da na banƙwana.
5. Sassarfa ya yin zagaye ukun farko na ɗawafin isowa da na Umra, wannan sassarfa sunna ce ga maza ban da mata bisa cewa kada ya cutar da kowa yayi sassarfar.
6. Shafan Ruknul-yamani: Wannan kuwa ta hanyar shafa shi da hannu ba tare da sumbatar shi ba, kuma idan bai samu damar sumbatar shi ba, to ba sai ya yi nuni gare shi ba.
7. Salla raka'a biyu bayan gama ɗawafi a bayan maƙamu Ibrahim idan hakan ya samu, idan hakan bai samu ba to ya yi salla a ko'ina cikin Masallaci.
8. Komawa zuwa Hajarul-aswadi da sumbatarsa idan hakan ya yiwu.

❖ Sharuɗɗan Sa'ayi:

1. Sa'ayin ya ƙasance bayan gama ɗawafi.
2. Jerantawa ta yyada zai fara da Safa ya gama a Marwa.
3. Sa'ayin ya kasance zagaye baƙwai.
4. Ya karaɗe tazarar dake tsakanin Safa da Marwa, kuma kada ya yi kasa da haka.
5. Yin Sa'ayin ɗaya bayan ɗaya, kuma tazara 'yar kaɗan ba zai cutar ba.
6. Tafiya yayin Sa'ayi idan zai iya.

❖ Sunnonin Sa'ayi:

1. Fita zuwa safa ta kofarsa.
2. Yin Sa'ayi bayan dawafi kai tsaye.
3. Tsarkakuwa daga kari da najasa.
4. Ya hau kan Safa da Marwa duk sanda ya isa zuwa gare su.
5. Fuskantar alƙibla duk sanda ya isa Safa da Marwa tare da kabbara da hailala da faɗin abin da ya zo cikin nassi.
6. Sassarfa cikin gaggawa tsakanin koriyar wuta kuma wannan ya keɓanta ne da maza ban da mata, saboda abin da ake nema ga mata shi ne suturta kansu.

Kuma dalilan dukkan ababen da suka gabata shi ne aikin Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, domin haƙiƙa ya tabbata daga gare shi ya ce: (Ku koyi ayyukanku na Hajji daga gareni)[1].

[1]. Muslim ne ya rawaito shi (2/943).

ALHAMIS: DARASI CIKIN SIRA

ALAMOMIN ANNABTAKARSA (SAW)

❖ Zantawar abinci gare shi:

An karɓo daga Amru daga Abu salamat ya ce: Annabi (SAW) ya kasance yana amsar kyauta amma ba ya cin sadaka, sai wata bayahudiya ta aiko masa da naman aƙwuya soyayye wanda ta sanya guba a cikinsa, sai Annabi ya ci naman, mutane ma suka ci sannan ya ce: (Ku cire hannunku domin naman ya ba ni labarin cewa an sanya guba a cikinsa), sai Bisru ɗan Bara'u ɗan Ma'arur Alansari ya rasu, sai Annabi (SAW) ya aika zuwa bayahudiyar ya ce: (Me ya sa kikayi haka?) sai ta ce: iɗan kai Annabi ne to wannan guba ba za ta cutar da kaiba, iɗan kuma kai sarki ne to na hutar da mutane daga kai, sai Manzon Allah (SAW) ya ba da umarni aka kashe ta, sannan ya riƙa fada a rashin lafiyar da ya rasu a cikinsa cewa: (Ban gushe ba ina jin tasowar gubar da naci a Khaibar) [1].

❖ Ɓuɓɓugowar Ruwa daga Yatsunsa:

An karɓo daga Jabir (RA) ya ce mutane sun ji ƙishi ranar yaƙin Hudaibiya, kuma Annabi (SAW) ya kasance akwai salkar ruwa a gabansa sai ya yi alwala da ruwan cikinta, sannan mutane suka nufato shi sai Manzon Allah (SAW) ya ce: (Me ya same ku?) sai suka ce: Ya Manzon Allah ba mu da ruwan da zamu yi alwala shi ba, da wanda za mu sha, sai wanda yake wurinka, sai Annabi ya sanya hannunsa a cikin wannan salka, sai ruwa ya riƙa kwararowa ta tsakankanin yatsunsa, kai kace iɗanun ruwane, sai ya ce: Sai mutane suka yi ta sha, kuma suka yi alwala, sai na ce wa Jabir, ku nawane a wannan rana? Sai ya ce: Idan da mun kai mu dubu ɗari da ruwnnan ya ishe mu, mun kasance mu dubu ɗaya da dari biyar ne[2].

---

[1]. Abu Dawud ne ya rawaito shi (4512).
[2]. Bukhari (415) da Muslim (1856) ne suka rawaito shi.

Ma'anar (Salka) wata 'yar ƙaramar buta ce ta fata da ake shan ruwa daga gare ta.

ASABAR: DARASI CIKIN TARIHIN SAHABBAI

MUS'AB ƊAN UMAIR (RA)

❖ Sunansa da haihuwarsa:

Shi ne Musaba ɗan Umair ɗan Hashim da Abdumanafin Alƙurashi Albadri, ana yi masa inkiya da Abu Abdullahi, an haife shi ne a Makka a sheƙara ta 42 kafin Hijrah, ya kuma taso ne a cikin ta.

❖ Tarihinsa da falalarsa:

Mus'ab (RA) ya taso ne ƙarƙashin kulawar iyayansa biyu masu hali masu dukiya, sai ya yi rayuwa ta masu sarauta a farkon rayuwarsa, yana bushsaha da jindaɗi, yana sanya mafi taushin kuma mafi tsaɗansa, yana sanya mafi ƙamshin turare kuma mafi kyawunsa, babu wani matashi a Makka da ya fi kyau da gayu da arziki da kula.

Kuma lokacin da ya ji da'awar Annabi (SAW) ni'imar da yake cikin ba ta hana shi karɓar gaskiya ba da yarda da ita, kuma ni'imar duniya ba ta hana masa neman ni'imar lahira ba, sai ya yi gaggawa ya musulunta a gidan Arƙam, 'Yan'uwansa na jin cewa ya musulunta suka kama shi suka tsare shi, kuma suka cutar da shi, Sa'ad ɗan Malik yana cewa: "Haƙiƙa na gan fatar shi tana saɓa kamar sabɓar maciji, kuma haƙiƙa na gan shi lokacin da aka ƙyale shi ko tafiya ba ya iya yi, sai muka ba shi 'yar sanda muka ɗauke shi a kafaɗarmu"[1].

Kuma bai gushe ba yana a tsare har sai da ya gudun Hijira tare da sahabbai Allah Ya ƙara musu yarda zuwa Habasha, sannan ya sake hijira zuwa Madina bayan da akayi Bai'ar aƙaba ta farko, saboda Annabi (SAW) ya aika shi tare da jagororin Madina guda sha biyu don ya koya wa mutanen Madina Alƙur'ani da ilimin addinin Musulunci, sai ya ƙasance shi ne jakada na farko a Musulunci, sannan ya dawo Makka a lokacin Bai'ar aƙaba ta biyu,

[1]. Siyaru A'alamin-Nubala (1/148).

kuma haƙiƙa Sa'ad ɗan Mu'azu da Usaidu ɗan Hudair a hannunsa suka musulunta.

(RA) ya halarci yaƙin Uhudu, kuma ya yi matuƙar ƙoƙari saboda ya kasance shi ke ɗauke da tutar musulmi, ya kutsa gaba da wannnan tuta ya kuma bai wa Manzon Allah kariya yayin da Ubayyu ɗan Khalaf ya kawo msa farmaki, ya tare sarar da Ubayyu ya kaima Manzon Allah saboda ya ba da kanshi fansa ga Manzon Allah (SAW), haka ya yi ta yaƙi da wannan rauni da aka yi masa yana ɗauke da tutarsa har sai da ɗan Ƙami'ata Al-laisi ya sare shi da takobinsa har ya cire masa hannun dama, sai ya riƙe tutar da hannun hagu, sai ɗan Ƙami'ata kafiri ya ƙara saransa ya cire masa hannun, sai Mus'ab (RA) ya ƙankame tutar da damatsensa a girjinsa, sai wannan kafuri ya sokeshi da mashi a kirjinsa, sai yayi shahada (RA).

A lokacin da Annabi (SAW) ya juyo daga Uhudu, ya tsaya a kan gawar Mus'ab, ya yi misa addu'a, sannan ya ƙaranta ((Daga cikin muminai akwai wasu mazaje da suka cika abin da suka yi ma Allah alƙawarinsa, daga cikinsu akwai wanda ya hadu da ajalinsa akwai kuma daga cikinsu wanda yake sauraron ajalin, kuma ba su su sauya daga alƙawarin ba)) [1].[2].

Mus'ab bai bar gadon dukiya kowani abu ba sai riga ƙwara ɗaya, ko da aka zo birne shi da ita iɗan suka rufe kansa da ita sai ƙafafunsa su bayyana, kuma iɗan suka rufe kafafunsa sai kansa ya bayyana, sai Annabi (SAW) ya ce: (Ku rufe kansa sai kusanya ciyawaR izkir a ƙafafunsa) [3].

Khabbab (RA) yana ce wa: "Mun yi hijra da Monzon Allah (SAW) don neman yardar Allah, sai ladanmu ya tabbata ga Allah daga

[1]. [Ahzab 23].
[2]. Tarikul-Islam (2/207).
[3]. Bukhari (4047) ne ya rawaito shi.

cikinmu a kwai wanda ya tafi cikin hanyarsa baici komai cikin ladɗansa ba, kuma daga cikinsu akwai Mus'ab ɗan Umair"[1].

❖ Rasuwarsa:

(RA) ya yi shahada a yaƙin Uhudu a shekara ta uku bayan Hijira yana ɗan sheƙara arba'in.

[1]. Bukhari (1682) da Muslim (940) ne suka rawaito shi.

Auna fahimtarka a daraussan Mako na 52			Amsa ta ƙwarai
Darasin Tafsiri	**Tambaya: Lokacin da aka saukar da ayar: (Kuma in har kuka bayyana abin da yake cikin zukatanku ko kuka ɓoye shi, Allah zai yi muku hisabi a kansa) Annabi (SAW) ya umurci sahabbansa su ce:**		b
	a. Mun yi imani da Allah shi kaɗai	b. Mun ji kuma mun yi biyayya	c. Mun dogara ga Allah
Darasin Hadisi	**Tambaya: Annabi (SAW) yana yawan cewa: " Allahumma inni as'alukal-afiyata fid-dunya wal-akhirah, Allahumma inni as'aluka al-'afwa wal-'afiyata fī dīnī wa dunyaya?**		a
	a. Idan ya wayi gari kuma idan ya yammata	b. Bayan kowace salla	c. Idan zai tafi tafiya
Darasin Aƙida	**Tambaya: Menene matafiyar Ahlus-Sunnah game da saɓanin da ya faru tsakanin sahabbai?**		b
	a. Suna karantar lamarin ba tare da son kai ba	b. Suna kamewa daga magana cikin abin da ya faru tsakaninsu.	c. Suna tattauna lamarin a wuraren tarurruka domin fadakar da mutane
Darashin Fiƙihu	**Tambaya: Daga cikin Sunnonin Sa'yi akwai:**		c
	a. Yin sa'ayi zagayen bakwai	b. Jerantawa tsakanin zagayen	c. Yin sa'ayi kai tsaye ba Ɗawafi
Darasin Sira	**Tambaya: Nawa ne adadin sahabban da suka sha kuma suka yi alwala daga ruwan da ya fito daga yatsun Annabi (SAW)?**		b
	a. Ɗari tara	b. Dubu ɗaya da ɗari biyar	c. Dubu uku
Darasin Tarihin Sahabbai	**Tambaya: Mus'ab bin ʿUmair Allah Ya kara masa yarda ya yi shahada ne a hannun?**		a
	a. Ɗan Ƙami'ata Al-laisi	b. Wahshiyyi ɗan Harb	c. Ikrimata ɗan Abi Jahl

MANAZARTA

1. Taysirul-Karimir-Raḥman fi Tafsiri Kalamir-Raḥman na Shaikh Abdur-Rahman bin Nasir as-Saʿdi.
2. Aisarut-Tafasir li-Kalamil-Aliyyil-Kabir na Shaikh Abu Bakr al-Jaza'iri.
3. Al-Mukhtasar fit-Tafsir wanda Cibiyar Tafsir ta fitar don nazarin Ƙur'ani.
4. Bahjatu Ƙulubil-Abrar wa Ƙurratu Uyunil-Akhbar na Shaikh Abdur-Rahman bin Nasir as-Saʿdi.
5. Shafin Ad-Durarus-Saniyya na Shaikh Alawi As-Saƙƙaf.
6. Shafin yanar gizo na Mawsu'atul-Ahadithin-Nabawiyya.
7. Nubzatun fil-Aqidatil-Islamiyyah na Shaikh Muhammad bin Salih Al-Uthaimin.
8. Nurat-Tawhid wa Zulamatush-Shirk fi Daw'il-Kitab was-Sunnah na Shaikh Dr. Sa'id bin Ali bin Wahf Al-Ƙahṭani.
9. Kitabut-Tawhid na Shaikh Dr. Salih bin Fawzan Al-Fawzan.
10. Al-MulakhkhaSul-Fiƙhi na Shaikh Dr. Salih bin Fawzan al-Fawzan.
11. Al-Fiƙhul-Muyassar wanda suka shirya: Prof. Abdullah bin Muhammad Aɗ-Ɗayyar, Prof. Abdullah bin Muḥammad Al-Muɗlaƙ, da Dr. Muhammad bin Ibrahim Al-Musa.
12. MawsuAt al-Fiƙhil-Islami na Shaikh Muhammad bin Ibrahim bin Abdullah At-Tuwajiri.
13. Al-Fiƙhul-Muyassar fi Daw'il-Kitab was-Sunnah wanda Majma'in Malik Fahd na buga Mushaf Mai Tsarki ya fitar.
14. As-Siratun-Nabawiyyah na Shaikh Abdul-Malik bin Hisham Al-Himyari.
15. Al-Fusul fi Siratir-Rasul (SAW) na Abul-Fida' Ismaʿil bin Umar bin Kathir Ad-Dimashƙi.
16. Ad-Durus wal-Ibar fi Sirati Khairil-Bashar na marubuci Aḥmad Al-Imran.
17. Al-Isabah fi Tamyizis-Sahabah na hafiz Aḥmad bin Ali bin Hajar Al-Asƙalani.

18. Siyar Alamin-Nubala’ na Shamsuddin Muḥammad bin Aḥmad bin Uthman Azzhahabi.
19. Al-Bidayah wan-Nihayah na Abul-Fida’ Ismaʿil bin Umar bin Kathir ad-Dimashƙi.
20. Sifatus-Safwah na Abul-Faraj Abdur-Rahman bin Ali Ibnul-Jawzi.
21. Tarajim Sayyidat Baytin-Nubuwwah na Dr. A’ishah Abdur-Rahman.

Abubuwan da ke cikin darusan yau da kullum			
Mako na farko			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Fatiha	4
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar Rukunen Musulunci	7
Talata	Darasi cikin Aƙida	Bayyanar karkace a cikin aƙidar mutane	9
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Tsarki	11
Alhamis	Darasi cikin Sira	Sunan Annabi (SAW) da haifuwarsa	13
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abubakar Siddiƙ (RA)	15
Mako na biyu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Ikhlas	20
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wajibcin imani da falalar tsayuwa a kansa	23
Talata	Darasi cikin Aƙida	Taƙaitaccen tunani game da rayuwa	25
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Hukunce-hukuncen ruwa	27
Alhamis	Darasi cikin Sira	Shayar da shi da tasowarsa (SAW)	29
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Umar ɗa Khaɗɗab (RA)	31
Mako na uku			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Falaƙ	35
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wajibcin kiyaye harshe da hannu	37

Talata	Darasi cikin Aƙida	Abubuwan da addinin musulunci ya keɓanta da su	39
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Ladubban biyan buƙata	41
Alhamis	Darasi cikin Sira	Samartakarsa (SAW)	44
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Usman ɗan Affan (RA)	46
Mako na huɗu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratun-Nas	51
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Daga cikin ɗabi'un munafurci	54
Talata	Darasi cikin Aƙida	Matsayin ilimin aƙida	56
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Abubuwan da aka haramta yayin biyan buƙata da abubuwan da ake ƙi	58
Alhamis	Darasi cikin Sira	Auren Annabi (SAW)	61
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Aliyyu ɗan Abu Ɗalib (RA)	62
Mako na biyar			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-kafirun	67
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitarwa game da lazimtar tsoron Allah Maɗaukakin Sarki	70
Talata	Darasi cikin Aƙida	Amfanin ingantacciyar aƙida	72
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sunnonin Fiɗira	74
Alhamis	Darasi cikin Sira	Labarin abin da ya faru game da dutsen Hajarul-Aswad	77

Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abdurrahman ɗan Auf (RA)	78
Mako na shida			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratun-Nasr	82
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar kira zuwa ga shiriya, da hatsarin kira zuwaga ɓata	85
Talata	Darasi cikin Aƙida	Shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah	86
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Asuwaki	88
Alhamis	Darasi cikin Sira	Ibadar Manzon Allah (SAW) a cikin kogo	90
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Ɗalha ɗan Ubaidullahi	91
Mako na bakwai			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Masad	95
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar fahimtar addini	97
Talata	Darasi cikin Aƙida	Sharuɗan shaidawa babu abin bauta bisa cancanta sai Allah	99
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Alwala	102
Alhamis	Darasi cikin Sira	Farkon saukar wahayi	105
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Zubairu ɗan Awwam (RA)	107
Mako na takwas			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratu Ƙuraish	111

Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wasiyoyin Annabi masu amfani	113
Talata	Darasi cikin Aƙida	Shaidawa cewa Annabi Muhammadu Manzon Allah ne	115
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Farillan alwala	117
Alhamis	Darasi cikin Sira	Da'awa a sirrance	120
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Sa'ad ɗan Abu Waƙƙas (RA)	122
Mako na tara			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Ma'un	126
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Tsoratarwa game da cutar da musulmi	129
Talata	Darasi cikin Aƙida	Wajibcin son Manzon Allah (SAW) da girmama shi	131
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sunnonin Alwala	132
Alhamis	Darasi cikin Sira	Da'awa a bayyane	135
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Sa'idu ɗan Zaid (RA)	137
Mako na goma			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Kausar	141
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Fifikon mumini mai ƙarfi	144
Talata	Darasi cikin Aƙida	Wajibcin yin biyayya ga Manzon Allah (SAW)	146
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Kurakurai da suke yawan faruwa a cikin alwala	148

Alhamis	Darasi cikin Sira	Cutarwar Ƙuraishawa ga musulmi	150
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abu Ubaida ɗan Jarrah (RA)	152
Mako na goma sha ɗaya			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Asr	156
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar salloli biyar da kankarewarsu ga ƙananan zunubai	158
Talata	Darasi cikin Aƙida	Hani game ƙetare iyaka da wuce gona da iri wurin yabon Annabi (SAW)	159
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Abubuwan dake warware alwala	161
Alhamis	Darasi cikin Sira	Hijira ta farko zuwa Habasha	163
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Khadija ‘yar Khuwailid (RA)	165
Mako na goma sha biyu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Humaza	169
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Ayyukan da amfaninsu ke cigaba da gudana bayan mutuwa	171
Talata	Darasi cikin Aƙida	Ginshiƙa da ake cirato addini daga cikinsu	173
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Shafa a kan huffi	175
Alhamis	Darasi cikin Sira	Musuluntar Hamza da Umar (RA)	177
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Saudatu ‘yar Zam’a (RA)	179

Mako na goma sha uku			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Fili	183
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitarwa a kan yafiya da ƙanƙan da kai	186
Talata	Darasi cikin Aƙida	Ginshiƙan Aƙidar musulunci	188
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Wankan tsarki	190
Alhamis	Darasi cikin Sira	Takunkumin Ƙuraishawa ga Banu Hashim da Banul-Muɗɗalib	192
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	A'isha (RA)	194
Mako na goma sha huɗu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Ƙari'a	198
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Tsoratarwa a kan zalunci	201
Talata	Darasi cikin Aƙida	Rukunin farko daga cikin Rukunan imani guda shida: Imani da Allah Maɗaukaki	203
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Siffar wanka da shafa a kan bandeji	205
Alhamis	Darasi cikin Sira	Hijira ta biyu zuwa Habasha	207
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Hafsa (RA)	209
Mako na goma sha biyar			
Lahadi	Darasin cikin Tafsiri	Suratut-Takasur	203
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Lazimtar gode wa Allah Maɗaukaki a akan ni'imominsa	216

Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da Rububiyyar Allah Maɗaukaki	218
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Taimama	221
Alhamis	Darasi cikin Sira	Shekarar baƙin cikin	224
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Zainabu ‘yar Khuzaima (RA)	226
Mako na goma sha shida			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratuz-Zalzala	230
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Abin da Allah Yake la’akari da shi game da bayinsa	233
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da Uluhiyyar Allah Maɗaukaki	235
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Salloli biyar	238
Alhamis	Darasi cikin Sira	Tafiyar Annabi (SAW) zuwa Ɗa’if	240
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Ummu Salama (RA)	242
Mako na goma sha bakwai			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Adiyat	247
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wajibcin neman yardar iyaye da jan kunne a kan fusata su	250
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da sunayen Allah da siffofinsa	252
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Lokutan salla	255
Alhamis	Darasi cikin Sira	Isra’i da Mi’iraji	258

Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Zainab ‘yar Jahshu (RA)	261
Mako na goma sha takwas			
Lahadi	Darasin cikin Tafsiri	Suratul-Ƙadar	265
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Ɗabi’un da suke gyara zukata	268
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da mala’iku	270
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Ludubban tafiya zuwa salla	272
Alhamis	Darasi cikin Sira	Mubaya’ar Aƙaba ta farko	275
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Juwairiyya ‘yar Haris (RA)	278
Mako na goma sha tara			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Bayyina (1)	282
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar azumtar Litinin da Alhamis	285
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da littattafai	287
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Rukunan salla	290
Alhamis	Darasi cikin Sira	Mubaya’ar Aƙaba ta biyu	293
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Maimuna ‘yar Haris (RA)	296
Mako na ashirin			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suaratul-Bayyina (2)	300

Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar sallar wutiri	302
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da Manzanni	304
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Wajiban salla da sunnoninta	307
Alhamis	Darasi cikin Sira	Shiri domin hijirar Annabi	309
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Safiyya ‘yar Huyayyu (RA)	311
Mako na ashirin da ɗaya			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratut-Tin	315
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Tsoratarwa a kan ƙauracewa da gaba da juna	318
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da Ranar lahira	320
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Abubuwan da ba a so a yi su a salla	322
Alhamis	Darasi cikin Sira	Hijira	324
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Ummu Habiba (RA)	327
Mako na ashirin da biyu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Alaƙ (1)	332
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wajibcin tuba zuwa ga Allah	335
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da ƙaddara	337
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Kurakurai da ake yawaita yin su a salla	340

Alhamis	Darasi cikin Sira	Ɗabi’ar rayuwa a Madina	343
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abu Ayyub Al-Ansari (RA)	345
Mako na ashirin da uku			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Alaƙ (2)	349
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar Yawaita karatun Alƙur’ani	352
Talata	Darasi cikin Aƙida	Mas’alolin da suke da alaƙa da ƙaddara	354
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sujjadar rafkanuwa	357
Alhamis	Darasi cikin Sira	Shigar Annabi (SAW) Madina	360
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abu Zarrin Alghifari (RA)	362
Mako na ashirin da huɗu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suaratud-Duha	366
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Daga cikin sabuban amsa addu’a	369
Talata	Darasi cikin Aƙida	Imani da gaibu	370
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sujjadar tilawa da ta Godiya	372
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Badar Babba	375
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abu Musa Al-Asha’ari (RA)	378
Mako na ashirin da biyar			

Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratush-Sharh	382
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Barin shagaltuwa da abin da bai shafi musulmi ba	385
Talata	Darasi cikin Aƙida	Ma’anar shirka da karkasuwarta	386
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sallar Jam’i	388
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Banu Ƙainuƙa	391
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abu Huraira (RA)	393
Mako na ashirin da shida			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratus-Shams	398
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Karhancin yawaita magana da tambaya da lalata dukiya	401
Talata	Darasi cikin Aƙida	Misalan shirka ƙarama	403
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Hukunce-hukuncen limanci da sallar jam’i	405
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Uhudu	407
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Usama ɗan Zaidu (RA)	410
Mako na ashirin da bakwai			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Lail	401
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Roƙon Allah alkhairan duniya da na lahira	417
Talata	Darasi cikin Aƙida	Dalilai da hujjoji a kan ɓacin shirka	419

Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sunnonin yau da kullum (Rawatib)	422
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Banun-Nadir	424
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Usaidu ɗan Khudair (RA)	427
Mako na ashirin da takwas			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Balad	431
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar imani, da sakamakon wanda ya mutu a kansa	435
Talata	Darasi cikin Aƙida	Illolin shirka da tasirinta	437
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sallar wutiri	439
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Gwalalo (Ahzab)	442
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Bilalu ɗan Rabah	445
Mako na ashirin da tara			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Fajr (1)	450
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitarwa a kan khushu'i a cikin salla	452
Talata	Darasi cikin Aƙida	Sababban shirka da hanyoyinta	454
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sallar walaha	456
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Banu Ƙuraiza	458

Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Ja’afar ɗan Abu Ɗalib	461
Mako na talatin			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Fajr (2)	466
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Hani game da fatan mutuwa yayin saukar cuta	470
Talata	Darasi cikin Aƙida	Kafirci, ma’anarsa da nau’ukansa	472
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Lokatan da aka hana yin salla a cikinsu	475
Alhamis	Darasi cikin Sira	Mubaya’a ta Ridwan	477
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib	479
Mako na talatin da ɗaya			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Ghashiya (1)	484
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar ambaton Allah	485
Talata	Darasi cikin Aƙida	Munafurci, ma’anarsa da nau’ukansa	490
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sallar Juma’a	492
Alhamis	Darasi cikin Sira	Sulhun Hudaibiyya	495
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Khalid ɗan Walid (RA)	498
Mako na talatin da biyu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Gashiya (2)	502

Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar sada zumunci	505
Talata	Darasi cikin Aƙida	Bidi'a a cikin addini	507
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sunnonin ranar Juma'a	509
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Khaibar	512
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Suhaibur-Rrumi (RA)	514
Mako na talatin da uku			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-A'la	518
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Mutum yana tare da wanda yake so	522
Talata	Darasi cikin Aƙida	Matsayar magabata game da bidi'a	524
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sallar jana'iza	526
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Mu'uta	530
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Julaibib (RA)	533
Mako na talatin da huɗu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratuɗ-Ɗariƙ (1)	537
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Tsoratarwa a kan fushi	540
Talata	Darasi cikin Aƙida	Misalan bidi'a	542
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Zikirorin bayan salla	544

Alhamis	Darasi cikin Sira	Buɗe Makka	546
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Zaidu ɗan Sabit (RA)	549
Mako na talatin da biyar			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratuɗ-Ɗariƙ (2)	553
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Haramcin girman kai	555
Talata	Darasi cikin Aƙida	Nau'ukan ziyarar ƙaburbura	557
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Zakka	559
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Hunain	562
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Khabbab ɗan Aratt	565
Mako na talatin shida			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Buruj	569
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitawa a kan Kamewa da wadatar zuci	573
Talata	Darasi cikin Aƙida	Ceto	575
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Zakkar kuɗaɗen takarda	578
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Ɗa'if	580
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Khubaibu ɗan Adiyyu (RA)	582
Mako na talatin da bakwai			

Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Inshiƙaƙ (1)	587
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitarwa a kan tausayin mutane	591
Talata	Darasi cikin Aƙida	Tawassuli	593
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Waɗanda ake bai wa zaka	596
Alhamis	Darasi cikin Sira	Yaƙin Tabuka	599
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Zaidu ɗan Harisa (RA)	602
Mako na talatin da takwas			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Inshiƙaƙ (2)	606
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Hassadar fata a cikin lamarin ilimi da ciyarwa	609
Talata	Darasi cikin Aƙida	Tawassuli (2)	611
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Zakkar bashi	614
Alhamis	Darasi cikin Sira	Shekarar Jakadu	616
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abdullahi ɗan Mas’ud (RA)	618
Mako na talatin da tara			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Muɗaffifin (1)	623
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Hani game da bincikin aibukan mutane da ƙkiyayya da juna	627
Talata	Darasi cikin Aƙida	Neman taimako da neman agaji	629

Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Zakkar hannayen jari da da ta filaye da gidaje	631
Alhamis	Darasi cikin Sira	Hajjin bankwana	633
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Sa’ad ɗan Ubada (RA)	636
Mako na arba’in			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Muɗaffifin (2)	640
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitarwa a kan dashe da shuka itatuwa	643
Talata	Darasi cikin Aƙida	Tabarruki	645
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Kurakurai dake yawan faruwa wajen fitar a zaka	647
Alhamis	Darasi cikin Sira	Rasuwar Annabi (SAW)	650
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Sa’ad ɗan Mu’azu (RA)	653
Mako na arba’in da ɗaya			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratul-Infiɗar	657
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar kyakkyawan ɗabi'a	660
Talata	Darasi cikin Aƙida	Tabarruki da aka haramta	662
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Sadaka ta mustahabbi	664
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Alƙur’ani mai girma)	666

Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Salmaunl-Farisi (RA)	669
Mako na arba'in da biyu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratut-Takwir (1)	674
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Kwaɗaitarwa game sadaka da magana mai daɗi	677
Talata	Darasi cikin Aƙida	Tabarruki da aka shar'anta	679
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Ladubban sadaka	681
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamonin annabtakarsa (SAW) (Tasowarsa da rayuwarsa)	683
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Salamatu ɗan Akwa'u (RA)	686
Mako na arba'in da uku			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratut-Takwir (2)	690
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Amfani da dukiya ba tare da almubazzanci da nuna ƙasaita ba	694
Talata	Darasi cikin Aƙida	Rantsuwa da wanin Allah Maɗaukaki	696
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Azumi	698
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Amsa addu'arsa)	700
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Ubada ɗan Samit (RA)	703
Mako na arba'in da huɗu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratu Abasa (1)	701

Litinin	Darasi cikin Hadisi	Haƙƙin musulmi a kan musulmi	711
Talata	Darasi cikin Aƙida	Hukuncin yi wa addini izgili	714
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Kwanakin da ake so a rika azumtar su	716
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Tsagewar wata)	718
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib	720
Mako na arba'in da biyar			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratu Abasa (2)	725
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Addini nasiha ne	729
Talata	Darasi cikin Aƙida	Raya sanin ilimin gaibu	731
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Abubuwan da suke lalata azumi	733
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Saukar albarka a Madina ta dalilin addu'arsa)	736
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abdullahi ɗan Abbas (RA)	738
Mako na arba'in da shida			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratun-Nazi'at (1)	743
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Falalar tasbihi da hamdala	747
Talata	Darasi cikin Aƙida	Sihiri	750

Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Hajji da Umara	752
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Yawaita abinci ɗan kaɗan da izinin Allah Mai girma da ɗaukaka)	754
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Abdullahi ɗan Umar (RA)	757
Mako na arba'in bakwai			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratun-Nazi'at (2)	762
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Daga cikin zikirori dake kare bawa	766
Talata	Darasi cikin Aƙida	Ruƙiyya	768
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Wuraren ɗaukar haramar hajji da umara	770
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Kamewar maƙiya daga cutar da shi)	773
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Safwan ɗan Mu'aɗɗal (RA)	775
Mako na arba'in da takwas			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratun-Naba'I (1)	779
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Yalwar rahamar Allah da tsananin azabarsa	782
Talata	Darasi cikin Aƙida	Layu	784
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Ɗaukar haramar hajji da umara	786
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Warkar da marasa lafiya)	788

Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Ammar ɗan Yasir	790
Mako na arba'in da tara			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratun-Naba'I (2)	794
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Umurni da kyautata zato ga Allah Maɗaukaki	797
Talata	Darasi cikin Aƙida	Biyayya ga shugaba	799
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Abubuwan da suka haramta ga wanda ya ɗauki harama	801
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Bayar da labarin al'amura na gaibu)	804
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Imran ɗan Hussain (RA)	807
Mako na Hamsin			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Suratn-Naba'I (3)	811
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Masifu suna kankare zunubai	814
Talata	Darasi cikin Aƙida	Falalar Ahlul-Baiti, da abin da ya wajaba game da su	815
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Fidiyar aikata abubuwan da aka wa haramta wa maniyyaci	817
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Shasshekar kututturen dabino, da kokawar rakumi)	819
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Amru ɗan Jamuh (RA)	821
Mako na hamsin da ɗaya			

Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Ayatul-Kursiyyu	825
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wajibcin rintsa ido	828
Talata	Darasi cikin Aƙida	Falalar sahabbai, da abin da ya wajaba a ƙudurce game da su	830
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Ayyukan Hajji da na umra	833
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Rusunawar bishiya, da sallamar dutse)	835
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Amru ɗan As (RA)	837
Mako na hamsin da biyu			
Lahadi	Darasi cikin Tafsiri	Ayoyin ƙarshen suratul-Baƙara	842
Litinin	Darasi cikin Hadisi	Wasu daga cikin addu'o'i masu amfani	846
Talata	Darasi cikin Aƙida	Matsayar Ahlus-sunna game da saɓanin sahabbai	848
Laraba	Darasi cikin Fiƙihu	Hukunce-hukuncen ɗawafi da sa'ayi	850
Alhamis	Darasi cikin Sira	Alamomin annabtakarsa (SAW) (Zantawar abinci gare shi, da ɓuɓɓugowar ruwa daga yatsunshi)	853
Asabar	Darasi cikin Tarihin Sahabbai	Mus'ab ɗan Umair (RA)	855